🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*

_{United we stand and succeed; Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}_

*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

*(💗SPECIAL THANKS TO HAJIYA FATIMA MOMYN NIGER💗)*

*BISMILLAHIR RAHAMANIR RAHIM*

*CHAPTER 1*

*SOORAJ*

Tsugune yake akan ƙafafunsa, kansa na kallon ƙasa, yayinda kyawawan idanunsa suke alumshe, jama'a ne cike awajen, sai hayaniya suke, fuskar kowa ɗauke take da farinciki, banda wani mutum ɗaya, shima ɗin baƙin ciki da damuwarsa basu bayyana akan fuskarsa ba, amma tabbas zuciyarsa nacikin matsanancin damuwa.

Sake matse ƴan saffa saffan idanunsa yayi da ƙarfi, jiyake kansa na juyawa, zuciyarsa nayi masa wani irin tuƙuƙi, sosai hayaniyar jama'an dake wajen ke hautsina masa ƙwaƙwalwa, sam shiba mutum bane mai son yawan hayaniya, aduk sanda hayaniya yayi yawa awajen da yake, to ciwon kai ne ke kamasa mai tsanani, yanzu haka shikaɗai yasan abunda yakeji, jiyake kamar ya buɗe bakinsa ya kwarara ihu, koda zaiji sauƙin abun da yakeji.

"ALHAMDULILLAH AURE YA ƊAURU YAU ASABAR AN ƊAURA AUREN SOORAJ MAI NASARA DA AMARYARSA AISHATU KABEER MUNA TAYA ANGO MURNA!!!" abunda wani maroƙi keta faɗa kenan cikin ɗaga murya.

Wannan maganan da maroƙin keyi shiyayi sanadiyar dawo da SOORAJ dake tsugune cikin hayyacinsa,   wani yawu mai ɗaci ya haɗiya, lokaci guda idanunsa suka rikiɗe suka zama jajaye, ƙoƙarin tashi tsaye yasomayi. Da sauri wani kyakkywan matashi dake gefensa yariƙe hanunsa, cikin murya ƙasa ƙasa yace "Please SOORAJ karkayi haka mana, acikin jama'a fa muke, kuma kasan tunda mukazo nan idanun jama'a akan mu yake"

Tsuka wanda aka ƙira da Sooraj yayi, tare da fusge hanunsa daga riƙon da wannan ɗin yayi masa, kallonsa yamayar ga Abbansa, karab idanunsu suka sauƙa akan najuna, da sauri Sooraj yayi ƙasa da kansa.

A hankali Tururuwan jama'ar da suka taru a ƙofar gidan Alhaji Kabeer suka soma raguwa, kowa na ƙoƙarin kama gabansa,    ganin haka yasa Sooraj miƙewa tsaye yasoma nufar inda motarsa take, ko ɗaga kansa baiyiba balle har wasu daga cikin mutanen da sukayi ragowa su fahimci wani irin yanayi yake ciki.   Hanunsa yaɗaura akan murfin motar zai buɗe, yaji muryar  MAS'UD ta daki dodon kunnensa.

"Inazakaje?" abunda Mas'ud yatambaya kenan.

Juyowa Sooraj yayi ya watsawa Mas'ud harara, ransa amatuƙar ɓace yake, wani irin haushin Mas'ud ɗin yakeji, gani yake komai daya faru hadda sa hanun Mas'ud ɗin aciki,  takaici ne yasake turnuƙe zuciyarsa,  sai kawai yasaki tsuka yabuɗe motarsa yashige, Mas'ud na ƙoƙarin zagayawa gefen mai zaman banza yashiga, Sooraj yayiwa motar key, aguje yafigeta haɗe da turbuɗawa Mas'ud dakuma sauran jama'an dake kusa dasu ƙura.  Hakan yasa kowa yabisa da kallo, ciki kuwa hadda Abbansa dake can gefe suna ganawa da Baban Amarya.

Sheshsheƙan kuka ne ketashi acikin ɗan madaidaicin ɗakin, wata yarinyace rakuɓe ajikin bango, ta takure kanta waje ɗaya, daga yanda take sauƙe ajiyar zuciya akai akai zai tabbatar maka da cewa kuka taci ta ƙoshi son ranta,   idanunta da suka kaɗa sukai jajur ta buɗe haɗe da kai kallonta sama.   "YA ALLAH!" abun da ta ambata kenan cikin wata irin raunanniyar murya, dake cikin halin matsanancin naiman taimako,   tabbas ta yarda cewa idan Ƴa Mace tarasa Uwa to tarasa babban gata aduniya, Uwa itace komai itace ginshiƙin rayuwa, kamar yanda ruwa keda matuƙar amfani aduniya, haka uwa take awajen kowani ƴa/ɗa, ayanda take da ƙananun shekaru, tunaninta da hankalinta basukai ɗaukar wasu matsalolinba, amma saboda halin rayuwa duk tazama wani iri, rayuwarta duhu ne, rayuwarta ƙunci ne, HASKE take nema akoda yaushe, da fata dakuma burin wani wanda zai taimaka mata.

"Dan Ubanki wai maikikeyi acikin ɗakinnan ne? baƙar munafuƙa, Allah dai yayi wadaranki ZIYADA natsani waƴannan halayyartaki, muguwa mai baƙar zuciya, zaki fitone kosai nashigo cikin ɗakin nayi ƙasa ƙasa dake!?"   faɗan wata mata dake tsaye abakin ƙofar ɗakin da yarinyar ke ciki, matar tacika fam sai jijjiga ƙugu take.

Jinmuryan Inna Ma'u acikin dodon kunnuwanta baƙaramin tsoritata yayiba, jikinta na rawa tanufi hanyar fita daga ɗakin.

Tana fitowa Inna Ma'u ta bita da wani irin kallo.
"Wallahi natsaneki Ziyada, natsani koda jin sunanki ne, adole nake rayuwa dake acikin gidannan, keda uwarki kun riga da kunzamemin JARABA, ƴan iska masu fararen fuska!" Inna Ma'u tafaɗi haka cike da takaicin Ziyada.

Itadai Yarinyar da ake ƙira da sunan ZIYADA shiru tayi tare da sunne kanta ƙasa, ƙirjinta kuwa jitake kamar zaiyo tsalle yafito waje sarai tasan wacece Inna Ma'u, yanzu zata kuma sake jibganta fiye da wanda tayi mata ɗazu.

"Ungo wannan naira ishirin ɗin kije maza ki ɗauko min niƙa na, kuma wallahi idan kika sake baki dawo da wuri ba, yau saina ƙona wannan ɗan iskan fuskan naki, mai zubin mayu" Inna Ma'u tafaɗi haka tana mai sanya hanunta ta mangare Ziyada harsai dakanta ya bugu da bango, sosai taji zafin bugewa dakuma mangareta da Inna Ma'u tayi, amma babu halin tayi kuka, naira ishirin ɗin ta amsa, cikin yanayinta mai sanyi tanufi hanyar ficewa daga gidan.
Tana ficewa Inna Ma'u tayi ƙwafa haɗe da cewa.
"Wallahi bazaki ƙara min cikakken sati biyu agidannan ba, ko kasheki ne ma gwamma nayi na huta, komai na mayyar uwarki kin kwashe"....

Gudu sosai yake tsalawa akan babban titin, saida yayi tafiya mai nisa kafun yayi parking motar agefen titi, hanunsa yasanya ya bugi steering motar, tare da furzar da iska daga bakinsa, wata drawer dake jikin motar yajawo haɗe da ciro goran ruwa, ɓalle murfin goran yayi haɗe da kafa goran abakinsa, saida yasha ruwan fiye da rabin goran kafun ya ɗauke bakin goran daga kan nasa bakin, numfashi yake fitarwa ahankali, jiyayi ƙirjinsa yayi masa nauyi, ɗaga kansa yayi ya kalli madubin dake cikin motar, da sauri ya kauda kansa gefe, wani irin tsananin tausayin kansa ne ya kamasa, jiyayi zuciyarsa tayi wani irin karyewa, kifa kansa yayi ajikin steering motar, baisan yazaiyi da rayuwarsa ba, baikuma san taya zai fahimtar da iyayensa lalura da damuwarsa ba, akodayaushe su kansu kawai suka sani, koda sau ɗayane basu bashi dama yasanar dasu matsalarsa ba, ako da yaushe basu da wata magana saita Aure, burinsu ɗaya shine yayi aure, baruwansu su basu wani damu da sanin shiɗin yayakeba, ɗago kansa yayi daga jikin steering motar, idanunsa ne suka sakeyin ja, kamar anwatsamusu garin barkono, bayajin cewa zai iya zama da kowace mace aduniyarnan, yanaji ajikinsa cewa shi ba'ayisa don yayi aure ba, rayuwarsa cike take da DUHU baisan wani HASKE ba, "Sai yaushene zasu fahimci hakan?" yatambayi kansa. Shiru yayi naɗan wasu mintuna kafun yatada motarsa, yanzu kam ahankali yake tuƙin motar bakamar ɗazu ba, saidai kuma zuciyarsa cike take da tarin tunani kala kala lallai dolene zaiyi abun da ya saba, duk da yasan hakan ba daidai bane kuma ALLAH Ma bayaso, amma baida wani zaɓi da ya wuce haka...

*(Sunan labarinnan SOORAJ shima ƙirƙiransa nayi kamar yanda na ƙirƙiri sauran, kamar yanda kukasani labarina ina ginashine akan mutum biyu, to wannan labarin ma hakanne, domin akan SOORAJ da kuma ZIYADA na ginashi, kamar yanda nagina SHU'UMIN NAMIJI akan ZAID da

ZAHRAH,  nakan tsayawa nayi komaina akan daidai, ina iyaka ƙoƙarina wajen ganin nabaku nishaɗi, nasamu ƙalubale sosai akan Labarin dana gama wato SHU'UMIN NAMIJI duk da nasan matakin nasara yana tarene da ƙalubale, amma wasu sunta faɗamin maganganu son ransu so please kuna kiyayewa, bakowacce magana yakamata ace wasunku na furtawa ba, karku manta magana mai daɗi sadaka ce.)*

*VOTE and COMMENT yawan vote da comment yawan typing...😝*     *Friday/13 March/2020*

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*

_{United we stand and succeed; Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}_

*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

*CHAPTER 2*

Agaban wani tankamemen gate yayi parking motarsa, fitowa yayi daga cikin motar ya nufi ƴar ƙaraman ƙofar dake jikin gate ɗin, ahankali yatura ƙofar yashiga, Manu mai gadi naganinsa ya kwaso aguje cike da girmamawa yace.
"Ranka ya daɗe barka da zuwa, Ango, Ango kasha ƙamshi...."

Kallon da yayiwa Manu mai gadine yasa yaja bakinsa yayi shiru, batare daya ƙarasa maganar dayakeyi ba.

Direct wani dogon gini dake tsakiyan compound ɗin gidan yanufa.

Wata ƴar dattijuwar mata ce ke zaune acikin katafaren falon, kayane zube agabanta tare da wasu manyan akwatuna masu kyau da tsada.

Da sallama ɗauke abakinsa yashigo cikin falon, amsa masa sallaman matar tayi fuskarta babu yabo ba fallasa. Baidamu da yanayin yanda yaga fuskarta ba, don yasan dalilin daya sanya tayi kicin kicin da fuska damace batason bashi, kuma amma duk da haka baijin zaiƙi furta abundake cikin ranshi.

"Barka da gida Ummu"
Sooraj yafaɗi haka bayan yayiwa kansa mazauni akan lallausan carpet ɗin da ya mamaye ƙasan falon.

"Yauwa sannu" Ummu tafaɗa tana mai ƙoƙarin tattare kayan dake gabanta. Shirune yashiga tsakaninsu, dama shi haka yake idan yayi magana saiyaja wasu mintuna baisake cewa wani abu ba, bakuma don baida abun cewa ba, a'a haka ya sabarwa kansa. Ummu kuwa afakaice ta ɗan saci kallonsa, yanda taga fuskarsa ya tabbatar mata da cewa akwai magana abakinsa, itakuwa bazata so taji komai daga bakinsa ba. Miƙewa tayi daga zaunen da take, wayarta taɗauka kana ta nufi hanyar da zai sadata da ɗakinta.

Ganin da yayi cewa idan yabari tatafi yarasa damansa ne, yasanyashi gyara zama haɗe da cewa. "Ummu dama inaso...."

"Banason kacemin komai, ya isa haka, munriga da mungaji da halinka SOORAJ, wallahi kaji na rantsema awannan karon kasaki matar da muka aura ma, ranka saiyayi mummunan ɓaci, zakuma kaga fushinmu irin wanda baka taɓa gani ba!" Ummu takatseshi ta hanyar faɗan haka cikin ɓacin rai.

Jajayen idanunsa yaɗago ya watsawa Ummun, itakuwa ko waiwayosa batayiba ta wuce ɗakinta.

Wani irin tsannin baƙinciki ne yasake kawo masa ziyara, babban abun takaicin shine yanda akaƙi basa dama, jiyayi kansa na sarawa kamar zai rabe gida biyu, tashi yayi ya fice daga cikin falon, ko iya kallon gabansa bayayi haka yakoma motarsa, kafa kansa yayi ajikin steering motar, yana fidda numfashi mai zafi, "Wannan wace irin rayuwace yakeyi? sai yaushene zai samu sauƙi daga raɗaɗin da yakeji?" tambayar dayaketa yiwa kansa kenan acikin zuciyarsa. Ya kusan mintuna 10 a wajen, kafun ya iya tada motarsa yabar unguwartasu gaba ɗaya, kaitsaye gidansa ya nufa.

Koda ya isa bedroom ɗinsa kayan dake jikinsa ya cire tare da shigewa cikin bathroom, wanka yayi tare da ɗauro alwala kana yafito, dogon wando na jeans yasanya tare da wata farar T-shirt, kallon agogo yayi yaga da sauran time kafun aƙira sallan Azahar, kwanciya yayi akan makeken gadonsa tare da lumshe gajiyayyun idanunsa.....

***

Idan hankalin Ziyada yayi dubu to atashe yake, domin kuwa tana zuwa injin niƙan tasamu ba'a niƙawa Inna Ma'u niƙan garin kunun tsamiyanta na gobe ba, hawayene suka cika idanunta,

yayinda tashiga haɗa mai injin da Allah akan yaniƙa mata sauri take, da ƙyardai tasamu ya yarda ya niƙa mata.   Tunda ta shawo kwanan ƙofar gidannasu take  hango wata yagalgalalliyar mota, wanda taji tsufa harta gode Allah,  cikin yanayinta na sanyi taƙaraso ƙofar gidannasu.

Wani dattijone wanda aƙalla shekarunsa zasukai 60 tsaye ajikin wata ragwaɓaɓɓiyar mota dagani motar taci wahala, mutumin irin baƙaƙen tsofinnan ne, sannan kuma ko wani gashi najikinsa yatashi daga baƙi yakoma fari,  kai tsaye zaku iya ƙiransa da tsohon najadu, domin daganin idanunsa zakasan cewa baƙaramin ɗan duniya bane, yanayin yanda yake kallon Ziyada kamar wani tsohon maye ne yasanya tayi ƙasa da kanta,  tashige cikin gida,  Murmushi Tsohon  yayi haɗe da jijjiga kansa, wani irin daɗi yaji aransa alokacin dayaga Ziyada'n.

"La'anatu sai yanzu kikaga daman dawowa? halin asaran dai shine bazaki fasa ba?" Inna Ma'u ta tambayeta.

"Kiyi haƙuri Inna Ma'u, wallahi ba ayi miki niƙan da wuri bane, shine kuma....."

"Da Allah rufemin baki shine kuma me? waye baisan  fetsarancinki ba, shashasha kawai, yanzu da kika ebo ƙafa kika shigo cikin gida, shin bakiga  Tsoho ɗan dashe  natsaye a waje yana jiranki bane?"

Wani irin bugawa ƙirjin Ziyada yakumayi, a tsorace tace
"Tsoho ɗan dashe kuma?"

"Ƙwarai kuwa, zakije kisamesane ko kuwa saina ɓaɓɓallaki yanzu anan wajen!" Inna Ma'u tafaɗi haka a hasale.

Jikin Ziyada ne yasoma ɓari amma bata da wani zaɓi daya wuce zuwa tasamu tsohon najadun dake tsaye a waje yana zaman jiranta.

Tana fitowa daga gida Tsoho ɗan dashe yasaki dariya irinta tsofaffin ƴan duniya.  Kallonsa yamayar kan ƙirjinta, saida ya haɗiyi wani yawu,    "Ƙaraso mana Amaryata" yafaɗa yana washe wawagegen bakinsa.

Kallon tsananin tsana Ziyada tabisa dashi haɗe da soma ƙare masa kallo,  idanunta ta sauƙe akan jajayen haƙoransa dayaketa washewa, gaba ɗaya bakinsa cike yake da tsakin goro, komai nasa dagajaja ba kyaun gani, duk da itama acikin dauɗa da ƙazanta take, sannan kuma bata da wani suturun kirki, amma duk da hakan ƙazancin Tsoho ɗan dashe daban take dana kowa, duk garin babu wanda baisan wanene Tsoho ɗan dashe ba, tsohone da bai riƙe mutumcin kansa ba, bashida wani aiki sai lalata yaran jama'a, matansa huɗu, kuma acikin garinnasu sosai akeji dashi, kasancewar yana da shanaye dakuma dabbobi, saboda tsabar duniyanci irin nasa har mota yake dashi, irin ko ohon motocinnan, nanma ƙaryan raine kawai irin nasa, ko iya tuƙata baiyiba, akwai wani ɗan ƙullinsa Ɗan liti shike tuƙasa yakaisa duk inda zashi, yanzuma tare

suke.

Saida tagama ƙare masa kallo kafun ta kawar dakanta gefe, wani sabon tsanarsa taji acikin ranta,  ganin da yayi cewa yarinyar nada taurin kai bazata ƙaraso garesaba yasanyasa soma takowa zuwa inda take, da sauri taja da baya.

"Wai Amaryata badai tsorona kikeji ba? ai gwamma kisaki jikinki dani domin ina tabbatar miki da cewa mako mai zuwa za'a ɗaura mana aure dake" Tsoho ɗan dashe yafaɗi haka yana mai sake washe ƙaton bakinsa.

Jin ya ambaci kalmar aure yasanya taƙara ja da baya, ganin da tayi kamar baya cikin hayyacinsa ne yasanya ta juya ta koma gida yana ƙiranta amma ko waiwayosa batayiba, ashe Inna Ma'u na laɓe tanajinsu, Ziyada nashigowa cikin gida Inna Ma'u ta ɗauketa da wani irin faskareren mari, cike da takaici tace.   "Amma kedai anyi yarinyar banza, ke inbanda hauka har Tsoho ɗan dashe zaizo miki da maganan aure kinemi wulaƙantasa, to kijini da kyau, ninan nabada aurenki ga Ɗan dashe, ko kinaso ko bakyaso, munafuka kawai, mai baƙar zuciya da aniya!"

Kai Ziyada tashiga jijjigawa lokaci guda kuka ya ƙwace mata, durƙushewa tayi aƙasa haɗe da kama ƙafan Inna Ma'u cikin muryan kuka tace.

 "Dan Allah Inna Ma'u kimin rai, karki haɗani da Tsoho ɗan dashe, kowa dake garinnan yasan halinsa ɗan iska ne, kuma ba tsohon kirki bane dan Allah kiyi haƙuri !!"

Ƙafa Inna Ma'u tasanya ta shure Ziyada cike da tsanarta tace "Idan kinga baki auri Ɗan dashe ba to saidai in mutuwa kikayi, ke ko mutuwa kikayi sai ankai masa gawarki" tanafaɗin haka tazari mayafinta da koyaushe ke akan igiya ta fita zuwa waje.

Kuka Ziyada tasanya haɗe da tashi ta nufi ɗan ƙaramin ɗakinta.  Zama tayi akan tabarma tare da cusa kanta tsakankanun cinyoyinta kuka tashiga rerawa mai taɓa zuciya, tasan tunda Inna Ma'u tafaɗi haka to sai ta aikata.

Inna Ma'u kuwa koda taje tasamu  tsoho ɗan dashe sosai suka tattauna akan Ziyada, inda yatada hankalinsa akan cewa shi lallai bayason aja lokacin auren, idan da ta sonsa ne ma shi koda yau abasa ita, idan yaso daga baya sai a ɗaura auren sosai yarinyar tashiga ransa, musamman daya lura cewa komai nata ɗanyene shakaf, da'alama zai kwashi garaɓasa mai romo,  kuɗi sosai ya dumbulawa Inna Ma'u ita kuwa sai washe baki take da haka sukayi sallama..

Saida tayi kuka mai isarta kafun ta fito daga cikin ɗakin takama aikace aikacenta daya zame mata  dole.

Sallaman Babanta da tajine yasanya taji gabanta ya tsananta bugawa,  muryarta na rawa ta

amsa sallaman nasa.

"Baba Sannu da dawowa!" tafaɗa murya a sanyaye.

"Daban dawoba ai da bazaki ganni ba!"  Fari kyakkyawan dattijon da taƙira da sunan Baba yafaɗi haka ahasale.

Cikin sanyi ta sunkuyar da kanta ƙasa, wannan halin shi kullum Babanta ke nuna mata, tun tana ƙarama harkawo yanzu bata taɓa sanin ya soyayyar mahaifi yake ba, babanta ko kusa dashi bayaso tazo, tsanar dayake nuna mata haryafi wanda Inna Ma'u ke nuna mata, cigaba tayi da aikinta, shikuma kai tsaye ya wuce ɗakin Inna Ma'u jikinsa na rawa, gudun kada ta leƙo ta fara zazzaga masa masifa, don kamar yaron cikinta haka tamaida shi.

***

Bayan yadawo daga sallan Azahar bacci mai nauyine ya ɗaukesa, kusan awa uku ya share yana bacci, kasancewar yau weekend babu aiki.  Ahankali yake buɗe kyawawan idanunsa masu ɗauke da zara zaran gashi asamansu (Eye lashes)   akan agogon dake saƙale jikin bangon ɗakin ya sauƙe idanunsa.  3:00 pm daidai yagani, cikin nutsuwa ya zuro ƙafafunsa ƙasa daga kan gadon,   bathroom yashiga yakumayin wanka tare da ɗauro alwala.

Tsab yagama shirya kansa cikin riga da wando na jeans masu kyaun gaske,  ya feshe jikinsa da turarukansa masu ƙamshi da kama jiki, combat shoe yasanya aƙafarsa haɗe da ɗaura agogon Apple a hanunsa na dama, sosai yayi kyau,  ɗago kyawawan idanunsa yayi ya kalli kansa acikin madubi, shikansa yasan cewa shi cikakken kyakkyawan Namiji  ne mai aji dakuma ɗaukar hankali, amma kuma saidai yana da tarin matsaloli.   SOORAJ  namijine kyakkyawa, komai nasa abun burgewa ne,  Yana da cikar halitta sosai, jikinsa amurɗe yake kasancewarsa ma'abocin yin gym,  farine shi tas banda lallausan sajen dake kwance akan ƙuncinsa babu wani abu dayake ɓaƙi ajikinsa. Yana da wasu irin idanuwa  ƴan madaidaita masu kyaun gaske, kamar yanda gashin idanunsa suke zara-zara haka gashin giransa ma suke, yana da dogon hanci, dakuma ɗan ƙaramin baki mai ɗauke da pink colour lips.

 Ya ɗauki sama da 3 minute yana ƙarewa kyakkyawan fuska da jikinsa kallo,  ahankali ya  sauƙe idanunsa ƙasa cike da raunin zuciya,   yasani ahaka idan kowa ya kallesa zaiyi masa kallon Cikakken Namiji Mai lafiya da kuma jin daɗi, amma shiyafi kowa sanin kansa yana da RAUNI sosai.       Wayarsa ƙirar Galaxy S20 ne tasoma ƙara alamar shigowar ƙira, ko kallon wayan baiyiba yasakai yafice daga cikin ɗakin, yayarda da abun da zuciyarsa tagama yanke masa, bazai bari awannan karon yasake faɗawa cikin irin halin daya faɗa abaya ba, ɗaukar ƙaddara yazame masa dole, don hakane ya yankewa kansa hukuncin nesantar duk wata ƴa mace, mahaifiyarsa ce  kawai bazai iya nesanta kansa da'ita ba, amma sauran mata kam hakan yazame masa dole, kodan rufewar sirrinsa.

***

"Nagama yanke shawara Aure zamuyiwa Ziyada"   Inna Ma'u tafaɗi haka ga Malam Garba bayan takai loman tuwo bakinta.

Malam Garba dake zaune akan ƴar tabarma ya ɗago kansa ya kalleta, cikin murya mai sanyi, yace...   "Aure kuma Ma'u?"

"Ƙwarai kuwa Aure, ko so kake muzaba mata idanu tacigaba da yawon bin maza? to idan kuwa haka kakeso wallahi saina cire hanuna akan lamuranku!" Inna Ma'u tafaɗi haka cikin ɓacin rai.

"A'a bawai nace bazatayi aure bane Ma'u, duk hukuncin da kika yanke akan Ziyada aini bazance a'a ba, amma kinsan banda kuɗin aurenta a yanzu!"  ya ƙare maganar cike da tsoron Inna Ma'un.

"Kai dai kawai kazubamin ido, domin nariga dana gama yanke shawara, gobe   Tsoho ɗan dashe yace zai kawo kuɗin aurenta, kuma kadai san yanda tsoho ɗan dashe yake, idan yace zai auri yarinya, to baya buƙatar komai daga wajen iyayenta, hakanan zamu kaita mu wurgar "

Da sauri Malam Garba yasake ɗagowa ya kalli Inna Ma'u bakinsa na rawa yace
 "Tsoho ɗan dashe kuma? ɗansa zaki aurawa Ziyada'n?"

Harara Inna Ma'u ta watsa masa cike da takaici tace  "Atunaninka akwai wani matashin saurayin da zai jajiɓawa kansa wannan maƴƴar ƴartaka? Ɗan dashe ne ke nemanta kuma nariga dana basa, ko kana da maganane?"

Kansa yagirgiza alamar "A'a" amma kuma har acikin zuciyarsa baiji daɗin hakan ba,  kowa yasan Tsoho ɗan dashe ba mutumin kirki bane, tsohon banzane dabai riƙe mutumcin kansa ba, sannan kuma sam baisan darajan aure ba, ya auri mata sama da 15, daya auri mace tana samun ciki, zai koreta tare da takardan sakinta.  To amma mai zaice, shi awajensa komai Inna Ma'u tayi dai dai ne...

*(A wannan littafin zan buga muku wasa mai zafi, kudai kucigaba da bina, sannan kada ku manta comment ɗinku shizai ƙaramin ƙarfin guiwa)*

*14/March/2020*
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*

_{United we stand and succeed; Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}_

*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

*CHAPTER 3*

Tunda yafita baidawo gidannasa ba har sai ƙarfe goma da rabi na dare, saida yagama daidaita tsayuwar motar tasa, kafun ya cire sit velt ɗin dake saƙale ajikinsa, aƙalla yakusan 7 minute acikin motar baifito ba, ahankali ya zuro ƙafafunsa waje cike da isa irin nasa, dama shi gwanine wajen jin kai da kuma miskilanci, baka gane gabansa baka gane bayansa. Sam yamanta da cewa wai yau aka ɗaura masa aure, saboda haka baiyi tunani ko tsammanin samun wata halitta acikin gidan nasa ba, kamar koda yaushe idan yashiga falon gidan direct bedroom ɗinsa yake wucewa, yauma hakance takasance. Wanka yasoma yi kafun yadawo yayiwa kansa mazauni akan gado, laptop ɗinsa yajawo yasoma latsawa, long jeans ne ajikinsa sai kuma wata farar riga wacce aka jere aninaye agabanta, saidai bai maƙala aninayen duka ba, hakan yasanya faffaɗan ƙirjinsa bayyana, kusan koda yaushe irin wannan shigar shine shigansa, duk da kasancewarsa farin mutum amma kuma yanason kalan fari, shiyasa yawancin kayansa suka kasance farare, duk da cewa idanu da nutsuwarsa suna ga abun dayakeyi acikin laptop ɗinsa, amma hakan baihanasa jiyo motsi a ɗakin dake kusa danasa ba, mamakine yakamasa don baiyi tunanin akwai wani agidan bayan shiba, sai alokacin auren da aka ɗaura nasa yau ya faɗo masa, jiyayi gabansa yafaɗi, yayinda bugun zuciyarsa ta tsananta, da sauri yakawar da ruɗun dayake ƙoƙarin shiga, tare da miƙewa tsaye, ƙirjinsa na bugawa haka yafice daga cikin ɗakin nasa.

7 minute yaɗauka yana tsaye yayinda yaɗaura hanunsa akan handle ɗin ƙofar, kokonto yake akan shigarsa cikin ɗakin, ganin baida wata mafita da ta wuce ya shiga yasanya yaturo ƙofar ahankali bakinsa ɗauke da sallama.

Daidai lokacin wata matashiyar budurwa da bazata wuce 21 years ba tafito daga bathroom jikinta duk ruwa da'alama wanka tayi, idanunsu ne yasauƙa acikin na juna, da sauri ya ɗauke kansa daga kallonta, itama akunyace tayi ƙasa da kanta, durƙusawa tayi har ƙasa cikin sanyin murya tace "Ina wuni" shiru yaɗanyi nawasu sakanni kamar bazai amsa mata ba. "Lafiya" yafaɗa ataƙaice haɗe da juyawa yafice daga cikin ɗakin, bayansa tabi da kallo tare da lumshe idanunta, wani irin sanyi taji na ratsata, ahankali tace. "Lallai samun cikakken Namiji mai kyau da aji kamar ka Sooraj babban sa'ane ga kowacce ƴa mace"

Yana fita daga cikin ɗakinnata yaji kansa dake tsananin yi masa ciwo, yayi masa nauyi.  haka yaji gaba ɗaya duniyar na juya masa, ƙirjinsa ne keta luguden duka,  da ƙyar ya iya dafe kansa yakoma ɗakinsa, faɗawa kan gado yayi tare da rumtse idanunsa, shikaɗai yasan abunda yakeji, Ƙunci, Raɗaɗi, sune suka mamaye zuciyarsa, haƙoransa yasanya ya datse laɓɓansa, acikin zuciyarsa yaketa karanto addu'o'i'n samun nutsuwa,,   ahankali kuwa yaji nutsuwa tasoma sauƙar masa,  yayinda yaji ransa nayi masa sanyi, bai tsagaita dayin addu'anba har  bacci ɓarawo ya ɗaukesa.

Ɓangaren amarya kuwa kwalliya ta tsantsara tanajiran dawowan ango, saidai kuma ko motsinsa bata sakejiba, shiru shiru har 12 hakan yasa ta rakuɓe jikinta ajikin gado tasoma kuka, tun tana kukan har bacci itama ya saceta.

*** Kamar koda yaushe kuma kamar kowacce rana, ƙiran sallan asuban fari akan kunnuwanta, duk da cewa bacci bai isheta ba amma kuma tashi yazame mata dole, kodan aikin gida dake kanta, tashi tayi daga kan ƴar tabarmar da take kwana akai ta zauna, hanunta takai kan wuyanta tashiga sosawa, daren jiya saurayene sukayi lugude ajikinta, suncijeta son ransu, dama ɗakinnata bawani wadataccen rufi yake dashi ba, gashi ko ƙofa babu, labulene kawai da aka sakaya ajikin ƙofar, ako wani dare sauro cizonta suke sosai, tun bata saba da cizon nasuba harta saba, kuma sosai cizon dasukeyi mata ke illatata, saboda kusan kullum fama take da zazzaɓi da kuma ciwon kai, amma dayake bata da wani gata haka take yawo cikin ciwo, saidai idan wahala tayi wahala tasamu ruwa akofi ta tofa Fatiha ƙafa uku tasha, da yardan Allah shike yaye mata ciwon kai.

Ruwa ta samu tayi alwala haɗe da kabbara salla tana idarwa kuwa ta ɗauki tulu tawuce rafin da suke ebo ruwa. Sanyi ake busawa sosai amma haka take tafiya babu ko mayafin kirki ajikinta, tunda tafito daga gida harta isa rafi bata haɗu da kowa ba, kowa nagida yana bacci banda ita wahalalliya marar gata. Zama tayi agaban wawakeken kogin haɗe da ƙurawa ruwan dake gudana acikin kogin idanu, wasu hawayene masu ɗumi suka gangaro daga cikin idanunta. akullum kuma ako da yaushe, addu'a take Allah yakawo mata ɗauki,   tana buƙatar farinciki acikin rayuwarta,  Kwantar da kanta tayi akan guiwowinta, hawaye nacigaba da tsiyaya daga cikin idanunta.   Tajima sosai tana zubda ƙwalla kafun daga bisani ta  ɗauki ruwan da ta iba tabar wajen, lokacin har gari yasomayin haske.    Gaba ɗaya ayyukan gidan ita tayisu tundaga kan shara da wanke wanke harzuwa ɗumamen tuwo, tana tsugune agaban murhu tana ta kiciniyar iza wutan murhu,  Inna Ma'u tafito daga ɗaki hanunta ɗauke da tulin kayan wanki, watsawa Ziyada kayan tayi, ayatsine tace.

"Nanda mintuna 20 nakeson nagansu awanke"

Idan da sabo Ziyada ta saba da wannan wahalan, saboda haka bataji komaiba taɗauki kayan tasomawa wankewa.

***

Yafi mintuna 20 yana juya biron dake riƙe ahanunsa, gabansa kuwa wata ƴar ƙaramar farar takarda ne aje,  so yake ya rubuta abun da shine mafita agaresa amma kuma yana fargaban abun da zaije yadawo,  maganganun Mahaifiyarsa ne suka shiga yi masa yawon acikin kunnuwansa, inda take cewa.....  "Wallahi kaji na rantse ma awannan karon kasaki matar da muka aurama, ranka saiyayi mummunan ɓaci, zakuma kaga fushinmu irin wanda baka taɓa gani ba!"
Tun ɗazu kalamannata keyawo acikin kansa, lumshe idanunsa da suka soma sauya kala daga farare zuwa jajaye yayi, tare da sanya haƙoransa ya datse lips ɗinsa,    tsikar jikinsa ne yasoma tashi yayinda gashin jikinsa suka soma mimmiƙewa tsaye, jiyayi kansa yasoma juyawa, yayinda  tunanin wasu abubuwa ke son hautsina masa ƙwaƙwlwa, da sauri yaɗaura alƙalami akan farar yakardan yasoma rubutu, bawani rubutu mai tsayi yayi ajikin takardan ba, ya nannaɗeta tare da sanya ta acikin wani envelop.
Tashi yayi daga zaunen dayake yashige cikin bathroom. Wanka yayi kana yafito sanye da rigan wanka ajikinsa.

Kayan training ɗinsa da sukeyi masa matuƙar kyau yasanya, tare da ɗaukan wata ƴar doguwar jaka,  ɗaukan takardan dayayi rubutu acikinta ɗazu yayi haɗe da sakai yafice daga cikin ɗakin.

Yana murɗa ƙofar ɗakin ta buɗe hakan yasa ya kutsa kansa ciki.

Tanaganinsa tatashi zaune daga kwancen da take, kallo ɗaya yayi mata ya ɗauke idanunsa akanta,  a kuma wannan kallon dayayi matane ya gane cewa taci kuka ta ƙoshi.

Cikin takunsa na isa yaƙaraso har wajen da take zaune.

Miƙa mata takardan hanunnasa yayi batare dayace da ita komai ba.
Karɓan takardan tayi tana mai kafesa da idanunta,   juyawa yayi yanufi hanyar fita daga ɗakin, har yakai bakin ƙofa saikuma ya tsaya cak, murya ashaƙe yace.

 "Kada kiga laifina, haka tawa ƙaddaran take"
yana gama faɗin haka yafice daga ɗakin, ko waiwayowa gareta baiyiba.

Kallon mamaki tabisa dashi
"Kenan miye maganganunsa suke nufi?"   tatambayi kanta tambayar da babu amsa.   Buɗe envelop ɗin daya bata tayi tare da zaro ƴar ƙaramar takardan dake ciki.

Wani irin bugawa zuciyarta tayi yayinda gaba ɗaya jikinta yaɗauki rawa,  sake waro idanunta tayi tana karanta abun dake rubuce ajikin takardan.  Kukane yaƙwace mata, lokaci guda ta shiga Jijjiga kanta, azabure tatashi daga kan gadon tafice daga cikin ɗakin.

Tana ƙarasawa compound ɗin gidan shikuma motarsa na ƙarisa ficewa daga cikin gidan.  Wani

irin ƙara tasaka haɗe da zubewa aƙasa tashiga rera kuka, ganin kukan bazai mata maganin komaiba yasa ta koma cikin gida, mayafinta kawai taɗauka saikuma envelop ɗin dake riƙe ahanunta.

Tazo fita daga gidan maigadi yatsareta da tambayar lafiya take kuka.  Ko kallonsa batayiba tafice tana ƙara volume ɗin kukanta..

Shikuwa Tanimu mai gadi komawa yayi kan benci ya zauna, aransa kuwa yana tsananin mamakin hali irin na SOORAJ, ko tantama bayayi abun da yafaru da sauran matanne itama yafaru da ita,  shiyasa tatafi tana kuka...

Yana tsaye agaban madubi, wani ɗan madaidaicin towel ne riƙe ahanunsa, yana goge gumin dake tsastsafowa ta goshinsa, kasancewar yanzu gama training ɗinsa.

Wayarsace  tasoma ƙara alaman shigowan ƙira,    saida yaji gabansa yafaɗi alokacin dayaga sunan dake yawo akan screen ɗin wayartasa, maganganun Ummu ne suka shiga dawowa kunnuwansa filla filla.   Jiki a sanyaye ya ɗauki wayar tasa ya kara akan kunnensa.

Ko sallaman da Sooraj ɗin keyi masa bai amsa ba, cike da ɓacin rai yasoma cewa.....   " Yau katabbatarmin da cewa kacika ishashshe Sooraj, yau kuma kaƙara tabbatar min da cewa kai mutumin banza ne, wanda baida tunani, ashe har abada bazaka daina kunyatamu ba? shikenan kaci gaba duniyace, ita kuma yarinyar da kayiwa saki har uku kasani wallahi Allah bazai barkaba, sai ya saka mata, Shashasha kawai!!!"

Jikin Sooraj ne yaɗauki rawa cikin inda inda yace "Dan Allah Abba ka sau....."

"Bazan taɓa sauraranka ba Sooraj, wallahi ko ganinka banasonyi,  gargaɗi na ƙarshe kada kasake ka zomin gida, tunda haka kazaɓa kaci gaba, mukam munzare hannuwan mu daga cikin al'amuranka!!!"

Abba yafaɗa murya a kausashe.

Baibawa Sooraj damar sake cewa komaiba yakatse wayar.

Zamewa Sooraj yayi daga tsayen da yake yazauna daɓas, hannayensa duka yasanya ya tallafi kansa, idanunsa ne suka kaɗa sukai jajur, take jijiyoyin dake kwance akan goshinsa suka fito raɗa raɗa,  saurin rumtse idanunsa yayi, domin idan yace zai barsu a buɗe, to tabbas ruwan hawayene zasu fito daga cikinsu...

*ZIYADA*

Tun safe take ta faman jibgan aiki kamar wata jaka, har zuwa yanzu kuwa bata huta ba. Shigowarta gidan kenan tasamu Inna' Ma'u tsaye sai rangaɗa guɗa take, hanunta riƙe da kuɗaɗe masu yawa, gefenta kuwa Malam Garba ne zaune yayi jigum, shidai baida tacewa, komai Inna Ma'u ne keyi, tamaidashi kamar wani yaronta, shikuwa biyayya yakeyi mata kamar raƙumi da akala duk hanyar da ta jasa nan yake bi.

Harara Inna Ma'u ta aikawa Ziyada da ta tsaya tana kallonta.

"Mayyar banza miye kika tsaya kina kallona?"

Da sauri Ziyada tayi ƙasa da kanta,  sumu sumu ta wuce cikin ɗakinta, hakanan taji gabanta na faɗuwa, jitake ajikinta kamar wani babban al'amari na kusantota, wanda kuma da dukkan alama ba abubane mai daɗi.
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*

_{United we stand and succeed; Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}_

*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

*CHAPTER 4*

Tunda ya zauna ya tallafe kansa da duka hannayensa biyu  baisake wani ƙwaƙƙwaran motsiba, numfashi kawai yake fitarwa a hankali..

Mas'oud dake tsaye akansa tuntuni yasanya hanu ya dafa kafaɗansa.

Jin sauƙar hanu akan kafaɗansa ya tabbatar masa da cewa Mas'oud ne, ɗago kansa yayi ya kalli  Mas'oud da rinannun idonsa.

Yanayin yanda Mas'oud yaga cikin idanun SOORAJ saida ya tsorita,  saboda bai taɓa ganin

abokinnasa acikin matsananciyar damuwa irin wannan ba.  Zagayowa yayi ya zauna akusa da SOORAJ ɗin. Cike da kulawa yace.
"Basai na tambayeka ba RAJ nasan kana cikin damuwa, amma kuma bantaɓa ganinka acikin irin wannan yanayin ba, ina fata dai ba halinnaka kasake gwadawa ba?"

Sauƙe hannayensa dake kansa  yayi ƙasa, haɗe da furzar da wani irin iska mai zafi daga bakinsa, kallon Mas'oud ɗin yayi kamar zaice dashi wani abu saikuma ya fasa, kawai ya kawar da kansa gefe.

Murmushi Mas'oud yayi  tare da girgiza kansa, tun suna ƙanana suke tare shida SOORAJ saboda haka kusan gaba ɗaya halayyar SOORAJ ɗin Mas'oud yasani,  idan SOORAJ bayason yin magana, akwai wani irin kallo dayakeyi, dazaran Mas'oud yaga SOORAJ yayi irin wannan kallon, to yasan mene kallon ke nufi.

"Bazan tilastaka kacemin wani abuba RAJ amma kuma kada kamanta cewa nidakai tamkar ƴan uwan juna ne, har sai yaushene zaka tsaya kana ɓoye damuwarka? yanada kyau ko bazaka faɗa duniya tasani ba, muda muke tare dakai, muncancanci musan damuwarka, amma maiyasa ako da yaushe kake ware kanka? idan har bazaka iya faɗamin damuwarka ba RAJ banda wani amfani awajenka, haka tarayyata dakaima bata da wani amfani!"  Mas'oud yafaɗi haka cikin ƙunan zuciya, saboda shi kansa al'amarin SOORAJ yasoma basa haushi, koda yaushe SOORAJ acikin damuwa yake, abune mawuyaci kaga dariyan SOORAJ, gaba ɗaya yasamo wani banzan hali ya arawa kansa, baida aiki sai zaman ƙunci.

Kallon takaici Mas'oud yashiga bin SOORAJ ɗindashi, ganin ko alamar ɗaukar maganarsa baiyi ba, azuciye yatashi zaibar wajen.  Riƙo hanunsa SOORAJ yayi, cikin wata irin murya mai sanyi yace.

"Bazan iyaba Mas'oud, niba namiji bane dazai iya riƙe mace, itama Nasaketa!"

Idanu Mas'oud yazaro waje cike da mamakin jin kalaman dake fita abakin SOORAJ ɗin.

"Kasaketa fa kace?" Mas'oud yatambaya cike da mamaki.

Kai kawai SOORAJ ya kaɗa masa alamar "Eh"

Wani irin tuƙuƙin baƙinciki da takaicin SOORAJ ɗinne suka turnuƙe Mas'oud, yanzu kam ya yarda cewa  akwai matsala a ƙwaƙwalwar SOORAJ domin maihankali bazai aikata irin abun da SOORAJ ke aikatawa ba.

"Anya kuwa kana cikin hankalinka RAJ? kodai asiri akayi maka ne? shin kakuwa san abunda kake aikatawa? kasaketafa itama kace? mata huɗu fa kenan yanzu ana aurama kana sakinsu, daga ankai maka mace yau washe gari kake sakota,  wai kodai aljanune dakai ??"  Mas'oud yatambayesa cike da tsananin mamaki, saboda duk wani maihankali dole ya tsoraci lamarin

SOORAJ.

Kallon Mas'oud ɗin SOORAJ yayi da jajayen idanunsa, araunane yace "Inada hankali Mas'oud kamar yanda kaima kake dashi, abu ɗaya kawai nasani shine wannan itace ƘADDARATA!" yana kaiwa ƙarshen zancennasa ya miƙe tsaye tare da soma tattara kayan training ɗinsa, Mas'oud na kallonsa ya tattara komai nasa yafice daga cikin ɗakin training ɗin. Mas'oud kam kasa tashi yayi yazauna daɓas, sosai al'ajabi da kuma mamakin abokinnasa RAJ ke ƙara kamasa, shikam yanzu yayarda cewa aljana ce tashafi Abokinnasa.

SOORAJ kuwa yana fita daga wajen training ɗin direct motarsa yanufa, yana shiga yayi mata key tare da cillata kan titi..

Yana komawa gidansa yayi wanka, dakansa yashiga cikin makeken kitchine ɗinsa, wanda yazuba masa kayan amfani, babu abun da babu na amfani acikin kitchine ɗin. Ruwan tea yadafa kana ya juye a flask, kan dinning area yadawo yazauna tare da haɗa tea, ahankali yake sipping tea ɗin yayinda ɗayan hanunsa ke riƙe da wayarsa yana latsawa. Safiya rana dare SOORAJ bayida wani abinci sama da ruwan tea, arana sai yasha tea sama da sau uku, abune mawuyaci yazauna yaci abinci kamar yanda kowa yakeci. Yana shanye tea ɗin ya miƙe tsaye, mug ɗin da ya haɗa tea ɗin aciki ya ɗauka ya wuce kitchine, wankewa yayi yamaida shi mazauninsa.

Falo yadawo yazauna akan ɗaya daga cikin lallausan kujerun falon, remote ɗin receiver yaɗauka, ya sanja tasha. Knocking ƙofar falon akasomayi, cikin gajiyawa yace "Yes come in"

Piter ne yashigo hanunsa riƙe da wasu zabga zabgan tsintsiyaye dakuma moper, ɗurƙusawa yayi cike da ladabi yace "Good Morning Sir"

"Morning" kawai yace tare da tashi yatattare wayoyinsa ya nufi bedroom, don bawa piter daman yin aikinsa da kyau.

Yana shiga ɗaki yafaɗa saman gado haɗe da jawo pillow yaɗaura kansa akai. Shiru yayi yana mai lumshe idanunsa, tun ɗazu kalaman Abbansa ketayi masa yawo acikin kunnuwansa, tabbas yasan dolene iyayensa suyi fushi dashi, amma shima bayin kansa bane, ƘADDARA ce baikuma isa kauce mata ba, amma yanda iyayen nasa suka ɗauki zafi sosai shine abun dayasanya yaji gaba ɗaƴa duniyar tayi masa ɗumi, shi kaɗai yasan kansa, shikaɗai yasan wanene shi, shine wanda yasan matsalarsa, taya ayanda yake zai iya zama da mace? sai yaushene iyayensa zasu fahimci matsalarsa? sama da shekaru 7 kenan yana fama da matsala guda ɗaya, shiɗin namijine, baida wani wanda zaije yafaɗawa damuwarsa, dole shine zai nemi maganin matsalarsa, haryau kuma akan neman maganin matsalannasa yake amma baidace ba, shikansa bazai iya fitowa fili yafaɗi abun dake damunsa ba, yabarwa kansa cewa matsalansa itace sirrinsa, zama da mace kamar mafarin tonuwar asirin sa ne, yajima yana tunanin cewa shi ba'ayisa don yazauna kuma yasan wata ƴa mace ba, amma dazaran yafara wannan tunanin yake saurin furta astagfirullah domin yasan saɓone yakeyi, to amma yazaiyi

shima bayida zaɓi ne, akullum akuma koda yaushe da Allah kawai ya dogara....

*** Tana zaune aɗaki tayi jigum abubuwane suka haɗe mata, aƴan kwanakinnan sosai take mamakin sauyan da Inna Ma'u tayi, tarage sata yawan aikace aikace, sannan kuma koda aikanta ne yanzu andainayi bakamar daba da kullum ƙafarta na waje tana yawon zuwa aika, yanzuma tana zaune ne aɗakinta tana sauraran hayaniyar ƙawayen Inna Ma'u dake tashi a tsakar gidan, itadai batasan meke gudana acikin gidannasu ba amma tabbas tasan cewa akwai wani abu da za'ayi acikin gidan. Zulai ƙawar Inna Ma'u ce ta yaye yagalgalellen labulen dake ƙofar ɗakin nata. Ayatsine ta watsowa Ziyada dake zaune harara, "Uwar munafurci saiki fito ae" cewar Zulai, tana gama faɗan haka kuwa tasake labulen tayi tafiyarta.

Jiki asaɓule Ziyada tafito daga cikin ɗakin nata, Gani tayi su Inna Ma'u sun baje akan tabarma yayinda suka kwaɓa lalle awani babban fanteka.

"Zo maza ki zauna" ɗaya daga cikin ƙawayen Inna Ma'u tace da Ziyada.

Cikin sanyin daya zame mata sabo taƙaraso ta durƙusa agabansu, ƙirjinta sai bugawa da sauri yake saboda tsabar tsoronsu da take.

Zaunar da ita sukayi agabansu, yayinda suka sanya ta kwaye musu cinyoyinta, da ƙarfin gaske suka shiga durza mata ƙwaɓeɓɓen lallen ajikinta, hatta fuskarta saida suka mulke mata shi da lalle, itadai ganin abun take awani baƙon yanayi, saboda tasan agarin nasu idan za'awa mace aurene kawai ake yi mata haka, suna gama shafa mata lallen sukace taje ta wanke, wani irin daɗine yaziyarci zuciyarta, domin albarkacin wannan lallen da suka shafa mata yasa zatayi wanka, bata mantawa rabonta da wanka yau sati guda kenan, dokace mai zaman kanta Inna Ma'u takafa mata akan cewa duk randa tayi wanka, bazata sake yi ba sai bayan wani satin, ruwa takandama abaho tayi bayinsu, alokacin da tacire kayanta tasoma watsawa jikinta ruwa, saida ta sauƙe wasu lafiyayyun ajiyar zuciya harsau uku, saboda wani irin sanyin daɗi daya ratsata, dama ita tuncan haka nan Allah yayita, tanada tsananin sonyin wanka, amma kuma bata samu tanayi saboda uƙubar Inna Ma'u.

Inna Ma'u kuwa masifa ta rufe ƙawayennata dashi wai akan mai zasu kwaɓa lalle su shafawa Ziyada. Zulai ce tagyara zama haɗe da turo ɗaurin ɗankwalinta gaba. "Wallahi yanzu na tabbatar baki da wayo Ma'u, kinga wannan lallen damuka shafa mata, shizai sanya jikinta yaƙara kyau, hasken fatarta yasake fitowa, kinsan yarinyar shegiya ɗanbanzan kyaune da ita, to kinga yanzu zata ƙara kyau akan nada, idan Tsoho Ɗan Dashe kuwa yaganta, saiya ƙara susucewa akanta, kinga ke kuwa kinsamu hanyar da zaki amshe masa ƴan kuɗaɗe kice kuɗin gyaran jiki, ai abirni haka akeyi kinsan nifa nayi zaman birni"

Shewa Inna Ma'u tasanya haɗe da bawa Zulai hanu suka tafa, cike dajin daɗi tace "Wallahi shiyasa nake mugun sonki Zulai, kinsan kan duniya, aikuwa ayau yau saina karɓi wani abu daga wajensa" sake tafawa Inna Ma'u da Zulai sukayi daidai lokacin Ziyada tafito daga wanka, zanine ɗaure aƙirjinta kanta gaba ɗaya yajiƙe yake da ruwa, tana shigewa ɗakinta, Zulai

tadawo da kallonta ga Inna Ma'u cike da mamaki tace "Wai Ma'u dama haka wannan yarinyar keda diri da kyau? nikuwa anya basu haɗa iri da larabawa ba?"

Taɓe baki Inna Ma'u tayi, domin ita aduniyarta babu abun datafi tsana kamar taji anyabi Ziyada, "To wama yasanine tsinannu, ai tunda nasamu nagama da uwarta itama yarinyar bawuya zata bani ba, wannan shegen idanun nasu masu kama dana aljanu yana ɗaya daga cikin abun dayasa na mugun tsanarsu, gashi komai na halittar uwarta ta kwashe!" Inna Ma'u tafaɗi haka cike da baƙin ciki.

"Aikuwa Ma'u kinyi farar dabara da kika haɗa auren ta da Ɗan Dashe, kinga zata ƙare rayuwarta cikin ƙasƙanci, kinsansa baya riƙe aure, duk da yagama tsofewa, amma baijirayi kansa ba,  dakin tsaya kuwa kina nan zakiga wani sarki ko senata sunzo neman aurenta" cewar wata daga cikin ƙawayen Inna Ma'un, wato Lantana.

"Cab iye bakinki Lantana, ina darai kam ƙaryane wani mai arziki ya raɓi Ziyada, sam hakan bamai yiwuwa bane, koda kuwa zanyi yawone tsirara na gwammace nayi, dana bar jinin Maryama ta auri wani mai kuɗi, nama kashe maciji bansare kansaba kenan" Faɗar Inna Ma'u. Dariya suka sanya sudukansu, yayinda ƙawayennata sukacigaba da fonfata....

Ziyada kuwa tsabar taji daɗin jikinta da tayi wanka tana kwanciya kawai sai bacci ɓarawo ya saceta...

Washe Gari.

*** Tun tashinta yau takejin faɗuwar gaba, babban abun daya ɗaure kanta shine, ƴan uwan mahaifinta da tagani sun cika gidan, da'alama dai kamar biki za'ayi agidannasu bata kuma san bikin waye za'ayi  ba.   Tazo wucewa zata shiga banɗaki  wata ƴar addar babanta  ke cewa "Amarya Amarya bakya laifi Amarya agidan Tsohon najadu"

Jitayi gabanta yafaɗi cike da mamaki tajuyo tana kallon Hajara wacce tafaɗi maganar, bakinta na rawa tace.   "Yaya Hajara wacece amaryan?"

Harara Hajara ta watsa mata domin dama tun can su bawani sonta suke ba.   "Wace amarya kuwa inbanda ke, ko baki da labarin cewa gobe za'a ɗaura miki aure da tsohon najadu?" Dariya Hajara tasanya haɗe dacigaba dacewa "Abun yayifa yarinya ta auri wanda yagirmi ubanta" sai takuma sake bushewa da dariya.

Jikin Ziyada ne yasoma rawa, lokaci guda taji cikinta yayi wani irin murɗawa atsorace ta ƙaraso gaban Hajara tazube aƙasa, murya na rawa tace  "Dan Allah Adda Hajara kifaɗamin gaskiya, auren waye za'ayi?"

Kallon kinma rainamin wayo Hajara tashiga yiwa Ziyada  ahasale tace..   "Bansaniba munafuka, waye baisan cewa kema son auren kikeba? dama ai kowa yasancewa ke tsohuwar hanuce,

wayasanima koshima Tsohon najadun ya ɗana"

Kuka Ziyada ta fashe dashi da gudu ta tashi tanufi ɗakin Inna Ma'u, tana shiga ta zube agaban Inna Ma'u dake tsaye, cikin kuka tace.
"Dan Allah Inna Ma'u kimin rai, kifaɗamin cewa maganar da Adda Hajara kefaɗi bagaskiya bane, wai dagaske aurena za'ayi, kuma ɗan dashe zan aura?"

Wata uwar tsuka Inna Ma'u taja haɗe da ɗauko ashar ta bankawa Ziyada cike da takaici tace

"To idan bakiyi aure ba kwaɗaki zamuyi mucinye?   inbanda ƙaddarama me Ɗan Dashe zaiyi dake, shima dai dayake tsohon maye ne shiyasa, amma bacin haka banga maiyagani awannan busheshshen jikinnaki ba, da Allah nitashi kibani waje, kuma aurenki da ɗan dashe babu fashi, gobe iwar haka kinzama matarsa"

Kuka Ziyada tashiga rerawa hadda majina tana roƙon Inna Ma'u, amma Ina Inna Ma'u haka ta murje idanunta.

Komawa cikin ɗakinta tayi hankalinta amatuƙar tashe, zama tayi daɓas aƙasa haɗe da ɗauko wani mayafin mamanta ta rungumeshi ƙam acikin ƙirjinta, kuka take tamkar zurarriya...

"Wayyo Mamana kinga rashinki abundaya jawomin, Ya Allah kataimakeni kakawomin ɗauki!" Ziyada tafaɗi haka cikin matsanancin kuka.  Tsabar kukan da Ziyada tayi harsaida muryarta ta dashe.     Tana zaune aɗaki taji muryan Babanta, a tsakar gidan nasu, da sauri ta ɗaga labulen ɗakin tana leƙensa, sosai takejin tsananin tausayin mahaifinnata, duk da cewa tana da ƙananun shekaru amma hakan baisa takasa fahimtan cewa wasu abubuwan dayake aikatawa ba acikin hayyacinsa yakeyinsu ba,    ganin yafice daga cikin gidanne, yasa tafaki idon mutane tarufa masa baya, zaune ta iskeshi akan ɗan dakalin dake ƙofar gidannasu.  Tsugunnawa tayi agabansa  Cikin da shashshiyar muryarta da ta ƙoshi da kuka tace

"Baba!"

ɗagowa yayi ya kalleta, batare da ya amsa mata ba.

"Dan Allah Baba kataimakeni, wallahi banason ɗan dashe!"  tafaɗi haka hawaye suna mai kwaranya daga cikin idanunta.

Shiru Malam Garba yayi cike da tausayin ƴartasa, lokaci guda kuwa ya zabura kamar anjona masa shocking.

"Uban maikikeyi anan?" yatambayeta atsawace.

Jikintane yasoma rawa, yayinda kuka yasakecin ƙarfinta,  cikin kukan tace.  "Dan Allah Baba kaceci rayuwata, katunafa ni amana ce Allah yabaka, dan Allah Karka bari acutar da rayuwata!!"

Wata uwar tsawa yakuma doka mata, haɗe da rufe idanunsa yakorata gida.

Haka takoma gida tana kuka maicin rai, lallai tasake tabbatarwa da kanta cewa ita cikakkiyar marar gata ce, zama tayi akan tabarmarta haɗe da sanya hanu ta share hawayenta, lokaci guda taji zuciyarta tayi wani irin bushewa, yayinda wani tunani yaɗarsu acikin ranta...

(Menene ra'ayinku akan auren ZIYADA da Tsoho Ɗan Dashe? Bazan cigaba ba harsai naga ruwan comment da vote ɗinku, dama nace yawan comment yawan typing.)

*✅OTE ME ON WATTPAD*
@fatymasardauna
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*

_{United we stand and succeed; Our ambition is to entertain and motivate the mind of readers}_

*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

*CHAPTER 5*

Wanene SOORAJ?

Alhaji Mansur Mai Nasara shi ne yakasance uba ga SOORAJ, Alhaji Mansur Mai Nasara wani hamshaƙin mai arziki ne dake zaune acikin garin Kaduna, Alhaji Mansur tsohon commissioner'n Ilimi ne dake zaune a cikin garin Kaduna, cikakken ɗan boko ne shi, wanda yatara dukiya, sannan mutum ne dayake jure gwagwar mayar rayuwa, wannan yasa mutane suka masa laƙabi da suna MAI NASARA, saboda duk wani abu daya sanya agaba saiyayi nasara akai. Hajiya Sulaimiya itace matarsa kuma mahaifiya ga SOORAJ, Hajiya Sulaimiya dai irin wayayyun matan nan ne, don asalinta yar ƙasar Sudan
ce, tana da kyau sosai, tsananin kyawunta yana ɗaya daga cikin abun daya sanya Alhaji Mansur, narka maƙudan kuɗaɗe wajen ganin ya aurota, zama sukeyi cike da so da kuma

ƙaunar juna, koda yaushe cikin farinciki suke, shekaransu uku da aure Allah ya azurtasu da samun ƙaruwan yaro namiji, tun daga randa aka haifi SOORAJ Alhaji Mansur yaƙara ganin buɗi acikin arzikinsa, soyayyar duniya suka ɗauka suka ɗaura ta akan yaron nasu, komai Na SOORAJ irin na Mahaifiyarsa ne domin kyawunta ya ɗauko. sosai SOORAJ ke zuba tashen kyau da burgewa tun yana ƙarami, saidai yataso da wani irin hali, miskiline na ƙarshe, sannan sam baida yawan magana, komai nasa atsare yakeyinsa, tun yanada shekara 12 mahaifinsa ya turasa England acan yayi gaba ɗaya karatunsa, tundaga kan secondary school har zuwa Masters ɗinsa, P.H.D ɗinsa ne kawai yayi aƙasar America. Sosai SOORAJ yake da ƙwazo akan dukkan komai, babu ruwansa da kowa, rayuwarsa kawai yake, bashida wani aboki aduniya sama da Mas'oud, sosai abotarsu tayi ƙarfi da Mas'oud, kasancewar sun fara abotanne tun suna ƙanana, gaba ɗaya sirrin Mas'oud SOORAJ yasani, haka shima Mas'oud ɗin yasan wasu sirrukan SOORAJ, saidai akwai wani sirri da SOORAJ ɗin yaɓoyewa kowa, shikaɗai yasan matsalarsa. Tun daga kan SOORAJ Alhaji Mansur baisake haihuwa ba, amma hakan baisa sun tashi hankalinsu ba, kasancewarsu wayayyun ƴan boko, dama ba wani son tara ƴaƴa suke ba, ayanzu dai SOORAJ yana da shekara 30 aduniya, cikekken matashine mai tsananin ji da kansa, rayuwarsa yakeyi maicike da burgewa baruwansa da kowa, abune mawuyaci kaga dariyansa, duk yanda Ƴan Mata keson samun daman kai kansu garesa, hakan baya yiwuwa, domin SOORAJ wani irin mutum ne, da akomai nasa baya sanya mata aciki, duk wata mu'amalarsa baya sanya mace aciki, mace duk kyau da haɗuwarta sam bata gabansa, batama burgesa, duk wani irin karairaya da mace mai lafiya zata zo tayi agabansa bazata taɓa burgesaba, duk tsananin kyawun mace, SOORAJ bata burgesa, shi yariga daya sanya aransa cewa mace bata cikin tsarinsa. Ayanzu yana akine a babban bankin Nigeria dake cikin garin Abuja wato Central Bank Of Nigeria (CBN) yanzuma hutu ya ɗauka shiyasa ya zo Kaduna wajen iyaye da danginsa. A rayuwarsa yana tsananin son iyayensa, sai gashi kuma daga zuwansa sun laƙaba masa auren dole. Wannan shine taƙaitaccen tarihin SOORAJ MAI NASARA.

Kamar koda yaushe idan yana acikin damuwa yakan fita yazaga gari, wani lokaci har ƙauyukan dake kusa dasu yake zuwa, sosai yakejin daɗi idan yaziyarci ƙauyuka musamman irin ƙauyukan da fulani ke rayuwa acikinsu, yauma hakance takasance dashi, hakanan yaji yanason fita daga cikin gari, bayaso yakoma Abuja baije yaɗan zaga gari ba...

Tsab yashirya kansa cikin long pencil jeans black colour,and Black t-shirt, agaban t-shirt ɗinnasa anrubuta ( THE MAN) da farin fenti. white denim jacket fara irinta maza yaɗaura akan rigar dake jikinsa, sosai kayan suka amshi jikinsa kasancewarsa mai farin fata, wasu fararen takalma combat wanda aƙalla kuɗinsu zasu haura sama da 30k yasanya aƙafarsa, hmmm SOORAJ yanason gayu sosai, hakan yasa koda yaushe cikin ɗaukar hankali yake. Da turarukansa masu tsada ya feshe jikinsa, take ko ina naɗakinnasa ya gauraye da ƙamshi. Wayoyinsa haɗe da key ɗin Range Rover ɗinsa ya ɗauka, kana yafice daga cikin ɗakin.

Yanashiga cikin motarsa ya kunnata, maigadi ne ya wangale masa gate, yana cilla motar tasa kan titi yasoma murza steering motar ahankali cike da salo..

*ZIYADA*

Gaba ɗaya ko ina acikin garin yaɗauki shiru, babu wani abu dake kai kawo, kowa yana gida akillace, adai dai irin wannan lokacin mafi yawancin mutane suna kwance ne aɗaki suna bacci, duhun dare ne sosai, babu wani abu dake motsi, sai ɗan abun da baza'a rasa ba, kamar yanda ko ina yaɗauki shiru haka gidannasu ma yake shiru, babu motsin kowa, gaba ɗaya jama'ar gidan suna bacci, amma banda ita, idanunta sun ƙeƙashe sun bushe, babu wani alamun bacci acikinsu, tun tana kuka da iyaka ƙarfinta, harta koma sauƙe ajiyar zuciya akai akai, babu wani abu dake ɗaga mata hankali, kamar idan tatuna cewa gobe za'a ɗaura mata aure da Tsoho Ɗan Dashe, tsohon dakowa yasan cewa ba mutumin kirki bane, shiru tayi tana mai sake nazartan abun da zuciyarta ke raya ma ta. Tabbas awani ɓangaren tunanin dake kwance cikin zuciyarta awajenta shine daidai, amma kuma tawani wajen tanaga kamar hakan ba daidai bane, duk duniya bata da kowa sai mahaifinta da kuma danginsa da suka ɗauki karan tsana suka ɗaura mata. Tana zaune awajen taji ansoma ƙiraye ƙirayen sallan asuba, jitayi gabanta ya tsananta bugawa, lokaci ɗaya taji zuciyarta na ingizata, ɗan dangwalin kayanta taɗauka, haɗe da yaye labulen ɗakinnata tasako kanta kaɗan tana leƙa tsakar gidannasu, ganin bakowa yasa tafito saɗaf saɗaf ta nufi hanyar fita daga gidan, saida takai bakin ƙofa kafun ta tsaya tare da juyowa tana mai kallon ƙofar ɗakin Babanta, wata irin karyewa zuciyarta tayi, take sai ga hawaye nasauƙa akan kumatunta, sosai takeson Babanta, tasan duk wani abu dayakeyi mata balaifinsa bane, amma bata da yanda zatayi, dole ko duniya ne ma tashiga, dole tanesanta kanta ga faɗawa halakar auren tsoho ɗan dashe. Juyawa tayi aɗari tabar cikin gidannasu, gudu takeyi sosai harta yi nisa da gidajen dake cikin ƙauyen tasoma shiga jejin dazai sadata da bakin hanya, komai tanayinshine acikin ƙarfin hali, amma har aƙasan zuciyarta tsorone shimfuɗe..

Bai kwana acikin garin Kaduna ba, kasancewar dare yayi masa, sam shi ba mutum bane mai son tafiyar dare, hakan yasa ya gangara gefen hanya, anan ya kwana cikin motarsa. Asuban fari yakamo hanyar dawowa cikin gari, saboda yau ɗin yakeso ya koma Abuja. Gudu sosai yaketa shararawa akan titi kasancewar babu wasu yalwan motoci dake tafiya akan titin.

Ba ƙaramin tafiya bane daga cikin ƙauyen nasu zuwa bakin titi saboda haka sosai tagalabaita, ganin takusa kawo bakin titi ne yasa ta rage sauri tasoma tafiya ahankali, dama ƙarfinta yasoma ƙarewa. Jitayi kamar anabin bayanta, da sauri tawaiwaya aikuwa wasu maza tagani su biyu abayanta, waro manya manyan idanunta tayi cike da tsoro tana kallonsu, dariya suka bushe dashi, ɗayanne ya sanya harshe yalashi laɓɓansa, cikin yanayi irin na ƴan iska yace.
"Baaba yau fa munyi babban samuwa, ɗanyen kaya ce"

Dariya wanda aka ƙira da suna Baaba yayi, ya karkace tsayuwarsa tare da kai hanunsa kan belt ɗin wandonsa. "Ay gaye yau zamu more" yafaɗi haka yana me zare belt ɗin wandonsa. Ganin haka yasa Ziyada shiga cikin wani irin matsanancin firgici, aruɗe tasoma ja baya, da ƙarfin gaske ɗayan ya fusgota, ihu tashiga yi tare da yunƙurin ƙwace kanta amma riƙon da yayi mata bana wasa bane, ɗan kwalin dake kanta ya fusge ya yi cilli dashi gefe, ganin haka yasa taƙara fasa ihu haɗe da turjewa, amma takasa ƙwacewa, hanunsa yasanya da iyaka ƙarfinsa ya

ja rigan koɗaɗɗiyar atamfan dake jikinta, ɓesss kakeji rigar ta yage, dama tuni kayan sunyi laushi.  Ganin saman ƙirjinta ya bayyana afili, yasa samarin suka bushe da dariya, kowanne acikinsu jikinsa yaɗauki mazari, burinsu kawai shine suga sun farketa.    Wani irin ihu Ziyada tasa tare da kafa bakinta akan hanun wanda ke riƙe da ita ta sakarmasa cizo, awahalce yasaketa yana fidda wani irin ƙaran azaba, itakuwa aguje ta lula cikin jejin.   Ganin haka yasa suka rufa mata baya, gudu take sosai  suna biye da ita, sam batasan cewa takawo bakin titi ba, aguje ta zo zata bi takan titin tasake faɗawa wani jejin... Kafun ƙiftawan ido wata mota da tataho aguje tayi sama da ita, tim haka ta faɗo ƙasa.   Amatuƙar razane yafito daga cikin motar yayo kanta,  waro kyawawan idanunsa waje yayi tare dasa hanu ya toshe bakinsa, lokaci guda jikinsa yaɗauki rawa ganin irin ɓarnar da yayi,  kwance take cikin jini ba ako iya gane kamanninta, wani irin rawa jikinsa keyi kamar anjona masa shocking, hannayensa duka yasanya yaɗagota, buɗe motar yayi yasata agidan baya, yanashiga wajen driver ko gama rufe murfin motar baiyiba, ya figi motar da gudun gaske.   Samarinnan naganin abun daya faru sukayi saɗaf saɗaf suka bar wajen, cike da haushin rashin samun nasara da basuyi ba.

Gudun da yakeyi har ya wuce hankali, tamkar zaitashi sama, gaba ɗaya ya ruɗe, ganin yanda jini ke fita ajikinta.  Alokacin daya shigo cikin garin Kaduna, gani yake kamar motar tasa bata gudu, hakanne yasanya yaƙara gudun motar mintuna kaɗan saigashi a cikin asibiti,   amatuƙar ruɗe yaje yaƙira likitoti suka zo suka ɗauketa aka wuce da ita emergency room.   Ganin yanda kanta ke zubda jini yasa likitoti suka duƙufa akanta wajen bata taimakon gaggawa.

Shikuwa SOORAJ yana nan awaje yakasa zaune yakasa tsaye, hankalinsa amatuƙar tashe yake, tsoronsa ɗaya kar ace masa ta mutu,  wani irin gumi ne ke fesowa ta goshinsa, kowa yagansa yasan cewa yana cikin tashin hankali.

Aƙalla sama da awa ɗaya da rabi likitoti suka ɗauka suna bata taimakon gaggawa,  cikin ikon Allah Kuwa sun shawo kan lamarin, saidai bata farfaɗo ba, amma sun tsaida jinin dake fita daga goshinta dakuma gefen kanta da ya fashe.

Yana tsaye likitotin suka fito daga Emergency room ɗin.  Da sauri yataho wajen  Dr.Salees, baikai ga cewa komaiba Dr.Salees yasakar masa murmushi tare da sanya hanu ya dafa kafaɗan SOORAJ ɗin.
"Karka damu SOORAJ munshawo kan matsalan, sai dai mujira farkawanta, muje office saina ƙarasama sauran bayanin"

Babu musu SOORAJ yabi bayan Dr.Salees zuwa office ɗinsa.

Suna shiga cikin office ɗin Dr.Salees ya nunawa SOORAJ wajen zama, kana shima ya zauna.

Sakeyin musabaha sukayi kafun Dr.Salees yacigaba da cewa.

"Ka kwantar da hankalinka ba wani babban damuwa bane, buguwane  kawai, tabugu sosai gaskiya, amma dayardan Allah munshawo kan komai, saidai kuma bamusan awani irin yanayi

zata buɗe idanuba, amma muna kyautata zato, Insha Allahu ma zata tashi lafiya, Allah dai yatsare na gaba"

Da "Ameen" Kawai SOORAJ ya amsa yana mai sauƙe ajiyar zuciya akai akai.

Bisa umarnin SOORAJ aka maidata wani special room,,,, ahankali yaturo ƙofar ɗakin yashigo, sauƙe idanunsa yayi akanta, tana kwance flat kanta na kallon sama, gaba ɗaya rigar dake jikinta ta ɓaci da jini, kanta kuwa a ɗaure yake da farin bandeji (bandage) yayinda tulin gashin kanta ke watse akan pillow, ɗauke kansa yayi daga kallonta tare da ƙarasowa cikin ɗakin, kan wata kujera yaje ya zauna haɗe da kai dubansa kan ledan ruwan da aka saƙalashi ajikin wani dogon ƙarfe, yana shiga cikin jikinta ahankali, kallonsa yakuma dawowa dashi kan agogon kamfanin Gucci dake ɗaure a tsintsiyar hanunsa. Ƙarfe goma na safe daidai haka agogon yanuna masa, hanunsa yaɗaura akan haɓansa haɗe da furzar da iska daga bakinsa, miƙewa yayi tsaye tare da nufar ƙofar fita, haryaje bakin ƙofar kuma sai ya tsaya juyowa yayi ya kalleta, idanunsa ne suka sauƙa akan ƙirjinta da kusan rabin breast ɗinta suke a bayyane, da sauri yakawar da kansa, wani irin bugawa yaji kansa yayi, kamar andoka masa guduma, jacket ɗin dake jikinsa ya cire tare da nufar inda take kwance, saidai koda wasa baisake barin idanunsa sun kalli ƙirjinnata ba, jacket ɗin nasa yarufa mata ajikinta, kana yafice daga cikin ɗakin. Office ɗin Dr.Salees yaje ya biya kuɗi, aka tura nurses guda biyu wanda zasu tsaya akanta don bata kulawa, shikuwa motarsa yashiga yabar asibitin. Direct gidansa ya nufa ransa ajagule, sam baiso haka takasance ba, yau yatsara tafiya Abuja, amma ga abun daya faru, zaman cikin Kaduna yakamashi dole harzuwa farfaɗowar yarinyar.

Wanka yayi kana yazo ya kwanta akan gado, lamo yayi yana tunanin yanda accident ɗin ya kasance, sai alokacinne ma mamaki ya kamasa, ƙaramar yarinya irinta mai zai fito da ita awannan lokacin? da dukkan alamu kuma ba acikin hayyacinta take ba. "To kodai mahaukaciya ce?" ya raya hakan azuciyarsa, da sauri ya kawar da wannan tunanin acikin ransa, wayarsa yaɗauka ya kunna karatun Al'Qur'ani mai girma, yana cikin jin karatun bacci ɓarawo ya sace shi.....

(More Comment nd Vote more typing😝 kuyi haƙuri yau banyi editing ba... Zan fara halina fa readers idan nayi update yau sai jibi kuma🤣😝 Allah yasa bazaku takura ba. )

*🍇SOORAJ FANS GROUP🍇*

Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/HFwwNXNTaW6HUbrbHjBHVM

*Idan kinsan Bazakina Comment ba kada kishiga, ONLY NOVELS kawai mukeso, bayan haka bamason kowani irin post.... Bamason Talla kona menene, idan kinyi zaki ganki a waje*

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*

_{United we stand ans succeed; Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}_

*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

*CHAPTER 6*

Tunda ya kwanta bacci bashi ya tashi ba sai da aka soma ƙiraye ƙirayen sallan Azahar.  Toilet yashiga yayo wanka.  Still riga da wando na jeans yasanya ajikinsa. Masallacin dake kusa da gidansa ya nufa donyin sallah.   Tun da yafita yin sallah baidawo ba sai ƙarfe huɗu na yamma, wanka yasakeyi.   Combat jeans ne ajikinsa baƙi sai kuma wata farar riga mai ɓakaƙen aninaye.    Yana tsaye agaban dressing mirror yana taje tulin sumar kansa, wanda yasha aski irin na zamani, screen ɗin wayarsa ya soma kawo haske, ɗan matsawa kusa da yawartasa yayi.   Sunan  Mas'oud ne ke yawo akan screen ɗin wayar, kasancewar ya sata a silent shiyasa batayi ƙara ba, ɗan ɓata fuska yayi haɗe da ɗaukan wayar yakara akan kunnensa.

"Ina falo" Inji cewar Mas'oud.

"Okay"  kawai Sooraj yafaɗa akasalance tare da aje wayartasa,   bai fita falon ba yaci gaba da taje sumar kanshi, saida ya kammala duk wani abu dazaiyi kana ya ɗauki wayarsa dakuma car key ɗinsa yafita zuwa falo.

Cike da takaici  Mas'oud ke kallonsa,  duk da yasan cewa halin Sooraj ne shanya mutane, amma kuma abun da yayi masa yauɗin yayi masa ciwo.

"Inakuma zakaje?" Mas'oud yatambayesa yana me ƙare masa kallo.

"Asibiti"
SOORAJ yabashi amsa ataƙaice.

"Abiti kuma? Baka da lafiya ne?" Mas'oud yajero masa duk waƴannan tambayoyin alokaci guda.

Ɗan ya mutsa fuska yayi haɗe da sanya hanu ya shafi kwantaccen sajen dake shumfuɗe akan fuskarsa.
"Accident mukayi, zanje na duba yarinyar dana bugene kota farfaɗo" ya faɗi haka yana me nufar hanyar fita daga falon, kai kawai Mas'oud ya girgiza haɗe da miƙewa tsaye yabi bayan SOORAJ ɗin. SOORAJ ne ke tuƙa motar yayinda Mas'oud ke zaune agefen mai zaman banza. Tafiya suke babu wani wanda yace da ɗan uwansa wani abu, ahaka har suka kawo asibitin, sam Mas'oud baiwani damu da shirun da SOORAJ ɗin yayi ba, because yasan hakan halinsa ne, bakoda yaushe yacika yawan magana ba, amma idan kafahimcesa yana da daɗin zama, dan bayashiga abun da babu ruwansa...

Atare suka jera suka shiga cikin asibitin. Office ɗin Dr.Salees suka nufa, shiyayi musu jagora zuwa ɗakin... dama yana shirin zuwa dubata kenan suka shigo.

Tananan har yanzu bata farfaɗo ba, wasu allurai Dr.Salees yayi mata, juyawa yayi ya kalli SOORAJ dake zaune akan wata plastic chair.... "Zata iya farfaɗowa akowani lokaci da yardan Allah, Yana da kyau katsaya atare da ita." Inji cewar Dr.Salees.

Kai kawai ya iya jinjina wa Dr.Salees alaman yaji, fita Dr.Salees yayi daga cikin ɗakin.

Kallon Mas'oud daya kafe yarinyar da idanu SOORAJ yayi, tsayawa yayi yana kallon yanda idanun Mas'oud ke yawo ajikin yarinyar ko ƙyaftawa ba yayi, takaicin Mas'oud ɗinne yakamashi, sam shi kam baiga wata mace aduniya dazai tsaya ɓata lokacinsa wajen kallonta ba, yaga manyan mata da suka amsa sunansu mata baiji komai gamedasu ba balle wannan ta tsitsiyar yarinyar, inbanda ƙaddara ma maizai haɗashi da ita, sam shi baya shiga sha'anin mata, saboda yasan menene matsalarsa, wannan ma don dolene kawai, amma dazaran ta farfaɗo zaisa amaidata inda ya ɗaukota.

"Tunda kana nan ni inaga kawai zantafi yau nakeso nakoma Abuja, please kakula da ita, idan tafarfaɗo tagayama garinsu saika maida ita!" SOORAJ yafaɗi haka yana me miƙewa tsaye.

Da sauri Mas'oud ya kallesa cikin mamaki yace "Zaka koma Abuja kuma?"

Kai SOORAJ ya jinjina masa alamar "Eh"

"Hmmm lallai SOORAJ baka da imani, kabuge yarinya kuma katafi kabarta? wato nine marainin wayonka shine kakeso katafi kabarni da ita ko?"

Murmushin gefen baki SOORAJ yayi wanda yayi masifar ƙarawa fuskarsa kyau.

"Mene matsalarka Mas'oud idan kakula da ita? Kasan inada abubuwan yi da yawa, banjin kuma zan iya ɓata lokacina akan mace" SOORAJ yafaɗi haka yana me kai dubansa ga agogon dake ɗaure a tsintsiyar hanunsa.

"Nima ai bazaman banza ne sana'ata ba, kai kabugeta kuma kai kake da alhakin tsayawa akanta kakuma bata kulawa harsai ta warke, saboda haka ni kaga tafiyata" Mas'oud yafaɗi haka aƙufule, don ya lura tsagwaran iskanci ne ke damun SOORAJ ɗin.

Still murmushin gefen baki yayi haɗe da bin Mas'oud ɗin da kallo harya fice daga cikin ɗakin. Kan kujera yakoma ya zauna, yayinda ya juyawa gadonnata baya, wayarsa yaciro ya soma latsawa..

Ahankali take ware manya manyan oily eyes ɗinta masu kyau da burgewa, dishi dishi tasoma gani, kafun daga bisani idanun nata suka soma washewa, ɗakin tasoma ƙarewa kallo, yayinda ƙwaƙwalwarta ke tunano mata abubuwan da suka faru, amatuƙar razane ta ƙwalla ƙara..
"Wayyo Allah Nashiga Uku dan Allah karku cutar dani!!"

Azabure yajuyo jin ihunta abayansa, yunƙurin tashi zaune tasomayi amma ina jin kanta take yayi mata wani irin nauyi, ga wani raɗaɗin azaba dake ratsata...

Tsuka yayi ƙasa ƙasa tare da maida kansa ga wayarsa yacigaba da latsawa, yatsani mutumin da baida nutsuwa.

Babu yanda ta iya haka takoma ta kwanta tana gunjin kuka, saboda kotafi kowa ƙoƙari ayanzu bazata iya tashiba. Idanunta ne suka sauƙa akan bayansa, domin dama yabata baya. Ganin namiji na zaune ya bata baya yasa taƙara volume ɗin kukanta, jikinta na rawa tace "Dan Allah kuyi haƙuri ku ƙyaleni, nakoma inda nafito, wallahi nayarda ma ni Zan auri tsoho ɗan dashe'n, nidai kada ku cutar dani, wallahi ni marainiya ce, dan Allah ku ƙyaleni natafi!" kuka take tsakaninta da Allah tana zabga magiya da roƙo, amma ko motsi baiyiba balle tasaran zai juyo gareta, duk atunaninta shiɗin ɗaya daga cikin mazan da suka ka mata ɗazu ne.

Ganin baijuyo gareta ba yasa tacigaba da kukanta, yana zaunene kawai amma jiyake kamar ana hautsina ƙwaƙwalwarsa, kuka yana ɗaya daga cikin abun daya tsana, wata tsuka yaja me ƙarfi haɗe da juyowa ya watsa mata wani irin kallo, idanunsu ne suka sarƙe acikin na juna, wani irin shock Ziyada taji acikin jikinta, lokaci guda ta haɗiye kukanta, ɗauke idanunsa yayi daga cikin nata yaci gaba da latsa wayarsa.

Ajiyar zuciya tashiga sauƙewa akai akai, neman kukannata tayi ta rasa, sai jikinta daya ɗauki wani irin zazzaɓi mai zafi. Idanunta na kallon bayansa, cikin wata irin murya mai sanyi tace....
"Kamaidani gidanmu kaji!"

Tsayawa yayi daga latsa wayar da yake yayi shiru... Bugun zuciyarsa ne ke ƙara tsananta, lumshe kyawawan idanunsa yayi, tare da sauƙe wata irin ajiyar zuciya. Tashi yayi ya fice daga cikin ɗakin batare daya kalli koda ɓangaren da take ba.

Ganin yafita daga cikin ɗakin yasa Ziyada fashewa da kuka.

"Shikenan na mutu yatafi ƙiran sauran ƴan uwannasa, shikenan zasu zo su lalatamin rayuwa!" Cikin gunjin kuka take maganar.

Jin anbuɗe ƙofar ɗakinne yasa, tayi saurin kallon bakin ƙofar,  murmushi Dr.Salees yasakar mata haɗe da cewa
"Yauwa Patient kintashi ko? sannu, yanzu inane ke miki ciwo ?"

Kasa amsa masa tayi saima kafesa da idanunta dake ɗigan ruwan hawaye da tayi,  kamar yasan tunanin da take acikin ranta, murmushi yakumayi akaro nabiyu haɗe da cewa "Ki kwantar da hankalinki nan asibiti ne, ba wai wajen da za'a cutar dake ba."

Rumtse idanunta tayi da ƙarfi sai alokacin tatuna da cewa tana cikin gudu taji wani abu ya doketa har saida ta ɗagu sama, to daga wannan lokacin bata sake sanin maiya faru ba sai yanzu data ganta cikin wani ɗaki.

Hanu Dr.Salees yakai jikinta ya taɓa, zafi zau yaji ajikinnata,   alluran daya shigo dasu yasoma ɓarewa,  ganin allura ahanunsa yasa Ziyada sake fashewa da sabon kuka, murya adashe tace "Don Allah kayi haƙuri karkamin, wallahi bazan sake guduwa ba!"

Mamakine yakama Dr.Salees sai kawai yatsaya yana kallonta.  Dai dai lokacin SOORAJ yashigo cikin ɗakin.

Kallonsa Dr.Salees yayi haɗe da cewa. "Yauwa SOORAJ gwamma daka shigo ai, kaga wannan ƙanwartaka tsoron allura takeyi, kuma akwai zazzaɓi ajikinta dole sai anyi mata allura sannan zata samu relief, bayan haka kuma yakamata kanemo mata ko tea ne tasha, akwai yunwa ajikinta sosai"

"Okay, kayi abun daya dace kawai!" SOORAJ yafaɗa a gajarce, domin baison yawan surutu.

Kai kawai Dr.Salees yagirgiza aransa yana mamakin miskilanci'n SOORAJ.

Ziyada na kuka haka Dr.Salees yayi mata allura, SOORAJ kuwa yana zaune ko kallon inda suke baiyi ba, earpiece ma yasa akunnensa yana saurararan cool music.   Dr.Salees nagama aikinsa yafita daga cikin ɗakin.

Cusa kanta tayi acikin pillow tana kuka, hakanan taji haushin  mugun mutumin daya sanya akayi mata allura, dama ance mata turawa mugayene to gashi yau ta tabbatarwa kanta, domin kuwa tana da tabbacin  cewa shiɗin idan ba bature bane to kuwa balarabe ne, don wannan farinnasa ba'a banza ba.

Yana zaune aka soma knocking ɗin ƙofar ɗakin.

"Come in" yafaɗa da ɗan ƙarfi.  Wani matashin saurayine ya turo ƙofar ɗakin yashigo, jikinsa sanye da wata jar riga  wacce agaba da bayanta aka rubuta MUZAFAS HOTEL da manyan harufa.   Manyan ledodin dake hanunsa ya miƙawa SOORAJ cike da girmamawa,   kuɗi SOORAJ yaciro daga cikin wallet ɗinsa ya miƙawa matashin saurayin.     Kallon SOORAJ saurayin yayi zaiyi magana, SOORAJ yaɗaga masa hanu, haɗe da cewa
"No badamuwa jeka kawai"

Godiya Matashin saurayin yashiga yiwa SOORAJ cike da murna yafice daga cikin ɗakin.

Ɗaukan leda ɗaya daga cikin ledodin SOORAJ yayi, cikin Unigue Voice ɗinsa yace
"Tashi kici abinci!"  yanayin yanda yayi maganar ne yasata saurin juyowa takalleshi, saidai kuma yanda ya fusge, yasa tashiga raba idanu kozataga wanda yayi maganar, domin ayanda yasha mur bazaka taɓa cewa shine yayi maganan ba.   Aje mata ledan akan ɗan ƙaramin drawern dake kusa da gadon yayi,  juyawa yayi cikin takunsa na isa yafice daga cikin ɗakin.

Tana ganin fitansa ta sauƙe wata irin ƙaƙƙarfan ajiyar zuciya, har acikin zuciyarta tsoronsa takeji.

Shiru yayi bayan yagama sauraran jawabin  dake fita daga bakin Dr.Salees.

Hanu yasa yashafi sajensa,  sam bayajin yiwuwar abunda Dr.Salees ɗin ke faɗi,  daransa da lafiyansa bayajin zai iya kwanan asibiti.  Tashi yayi tsaye yabawa Dr.Salees hanu suka sakeyin musabaha kana yafice daga cikin office ɗin bayan yasanya hanu acikin wata takarda.   Ɗakin datake kwance ya nufa, bayajin abunda zai aikata akanta daidai ne, amma kuma hakan shikaɗai ne mafita.   Yasan abun da zuciyarsa ke raya masa ba abu bane mai kyau, amma kuma baida wata hanyar dazai samawa kansa hutu sama da wannan, idan kuwa har maganar da Dr.Salees yafaɗa masa gaskiya ne, to yazama lallai ya aikata abun da zuciyarsa ke umartansa daya aikata, a wani ɓangaren baidamu da wani irin kallo mutanen duniya zasuyi masa ba, yasan kansa yasan ba irin sa mata ke ɓuƙata ba, kyawunsa da haɗuwarsa afili kawai suke, amma abaɗininsa yafi kowani irin namiji rauni....

*(My Wattpadians Vote ɗinkufa yana ƙasa😥 I swear ku ƙara yawan vote kokuma nata baku gajeren pages)* 🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*

_{United we stand and succeed; Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}_

*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

*CHAPTER 7*

A ƙalla yaɗauki kusan mintuna 4 ajikin ƙofar, yayinda hanunsa ke kan handle ɗin ƙofar. Cije laɓɓansa yayi kana yatura ƙofar ahankali yashiga.

Duka hannayensa ya zuba acikin aljihun wandonsa yana kallonta cike da takaici. Kallonsa yakuma maidawa ga ledan daya aje mata, yananan ayanda ya aje, don ko taɓa ledan batayi ba.

Ƴar ƙaraman tsuka yaja, haɗe da sanya hanu ya ɗan bugi kansa. "Wannan yarinyar da'alama itace ƙaddarata ta biyu!" yafaɗi haka cikin wata silent voice, sam bayason damuwa, gashi yafahimci cewa ita kanta Yarinyar Damuwa ce mai zaman kanta agaresa. "Yanzu da tayi bacci, shine takeso ya ɗauketa ko kuma me?" yatambayi kansa cike da takaicinta.
Tsuka ya kuma ja kana yafice daga cikin ɗakin.

Mintuna kaɗan wasu nurses su biyu suka shigo cikin ɗakin, kasancewar alluran da Dr.Salees ya mata nada matuƙar ƙarfi bazata iya farkawa nan kusa ba, yasa Nurses ɗin suka ɗaurata akan wani gado wanda keda ƙafafun taya, haka suka turota akan gadon har bakin motarsa, buɗe musu gidan baya yayi suka sanyata aciki. Da wani irin gudu ya figi motartasa yafice daga cikin asibitin, shikaɗai yaketa zuba tsuka, har ya iso makeken gidansa dake cikin unguwar Malali, yana gama daidaita parking ɗin motar tasa, yaɗauki goran ruwan dake gefensa, ɓalle murfin yayi haɗe da kai goran bakinsa, gaba ɗaya ruwan dake cikin goran yashanye tas, ko kaɗan bai rageba, yanaganin wayarsa na ƙara amma yaƙi ɗagawa, duk da bai duba sunan dake yawo akan screen ɗin wayarba, amma yasan wake ƙiransa, tunda yatafi yabarsa kuwa to shima bazai ɗaga ƙiransa ba, idan wulaƙancine shima ya'iya salo salo.

Direct ɓangaren da zai sada sa da part ɗinsa ya nufa. Yana shiga cikin bedroom ɗinsa yasoma rage kayan dake jikinsa. Wani farin towel ya ciro acikin drawer'nsa ya ɗaura, bathroom yashiga tare da kwanciya acikin haɗaɗɗen jakuzzie'n da ruwan cikinsa ke ta tashin ƙamshi. lumshe gajiyayyun idanunsa yayi, Sosai yakejin sanyin ruwan na ratsa sa. Aƙalla yakusan 30 minute yana kwance acikin jakuzzie'n. Da ƙyar ya samu ya iyayin wanka, jinsa yake amugun gajiye. Koda yafito a wanka sama sama yashafa mai, da body spray ɗinsa mai matuƙar ƙamshi, ya feshe duka jikinsa, take ɗakin yasake gaurayewa da wani ni'imtaccen ƙamshi. 3 guater combat jeans yasanya, sai kuma wata riga da bata da nauyi. Ƙara gudun AC'n ɗakin yayi, haɗe da faɗawa kan gado, pillow ya jawo ya ɗaura kansa, tare da lumshe idanunsa.

Ƙarar wayarsane takaraɗe kunnuwansa, tsuka yayi cikin baƙin ciki yajawo wayar ya kara akan kunnensa,  shiru yayi batare da yace komaiba, baiduba wake ƙiransaba alokacin daya ɗaga wayar, amma tabbas yasan cewa bawani wanda zai ƙirasa adaidai wannan lokacin in banda Mas'oud.

Jin yayi shiru baice komaiba yasa Mas'oud buga tsuka cike da haushin SOORAJ ɗin yace...
"Karkayi tunanin nawani damu da kaine, tausayin yarinyar mutane kawai nake, yanzu yajikinnata? inafata dai ta farfaɗo ba wata matsala?"

Ƙirjinsa ne ya buga, da sauri ya buɗe idanunsa da suke a lumshe, haɗe da tashi zaune, hanu yasa ya ɗan doki kansa, harga Allah shi ya ma manta da batun wata yarinya, sam yamanta da tana cikin motarsa, da sauri ya kashe wayar, tare da sauƙowa daga kan gadon. Bedroom slipper ɗinsa yazura aƙafafunsa kana yafice daga cikin ɗakin.

Key yasa ya buɗe murfin motar, tananan kwance tana sheƙa baccinta cikin kwanciyar hankali.

Hararanta yayi kafun ya tura kansa cikin motar, ɗaukota yayi kamar wata ƴar baby yayi cikin gidan da ita.  Ɗakin dake gefen nasa yashiga da ita, komai na ɗakin neat kamar akwai wani wanda ke rayuwa acikinsa. Yana zuwa daidai gadon ya saketa, ji kake tim tafaɗi akan lallausan katifan dake kan gadon.  Tabbas da badon alluran da aika mata mai ƙarfi bace, da ayanda ya wurgatan nan dole saita farka.  Juyawa yayi yafice daga cikin ɗakin.  Ɗakinsa ya koma, rigar jikinsa ya cire, komawa kan gado yayi ya kwanta. Shi kaɗai yake ƙunƙuni acikin zuciyarsa har bacci yaɗaukesa.....

1:30 am

Tsananin yunwan dake damunta, shiyayi sanadiyar farkawanta daga bacci..  Buɗe gajiyayyun idanunta tayi tana jujjuyasu ahankali. Azabure tatashi tana ƙarewa ɗakin data ganta aciki kallo, tabbas idan zata tuna, wannan bashine ɗakin da ta ganta ɗazu aciki ba, da sauri tashiga waige waige, dirowa tayi ƙasa tana ƙarewa royal bed ɗin data ganta kwance akansa kallo, jingina tayi da bangon ɗakin zuciyarta cike da tarin tsoro da kuma tambayoyi, hanu tasa ta dafe cikinta, da takejinsa kamar babu ƴaƴan hanji acikinsa, tsabar yunwan dake nuƙurƙusanta, wani irin juwa ne ke ibanta, durƙusawa tayi aƙasa haɗe da fashewa da kuka,  da duka hannayenta ta kama cikinta, tunda take adunia bata taɓa jin yunwa irin wanda takeji ayanzu ba, jitake kamar wani abu na tsakalan cikinta. Miƙewa tayi ta buɗe wata ƙofa dake cikin ɗakin, atunaninta ko wani ɗakine da zata iya samun abinci taci,  gani tayi ɗakin ba komai sai fanfo da kuma wasu fararen abubuwa, saikuma wani abu da tagani asama kamar famfo, duk da cewa bata taɓa zuwa birni ba, amma jikinta yabata cewa nan ɗin banɗaki ne, jan ƙofar tayi ta rufe haɗe da nufar wata ƙofar, tana jan ƙofan kuwa ya buɗe, ahankali ta buɗe ƙofar ta fita, ganinta tayi acikin wani katafaren falo wanda yagaji da haɗuwa, duk da cewa babu yalwataccen haske acikin falon, amma hakan baihanata ganin kyawun falon ba, wurga idanunta dake ɗigar da ruwan hawaye tasomayi tako ta ina, tsorone yasake kamata, kawai saita sulale awajen tashiga rera kuka.

Bayida nauyin bacci ko kaɗan, sama sama yakejiyo gunjin kuka acikin kunnuwansa, ɗan ya mutsa fuskarsa yayi, haɗe da buɗe idanunsa. Shiru yayi yana maijin sautin kukan naƙara ratsa kunnuwansa, Ahankali yace "Najidowa kaina masifa!"

Gyara kwanciyarsa yayi cike da takaicin tashinsa daga daddaɗan baccinsa da tayi, hanu yasanya ya toshe kunnuwansa, sosai yatsani jin kukan mace arayuwarsa, so yayi ya shareta amma kukan da takeyi masa yakasa barinsa yayi hakan. Sauƙowa yayi daga kan gadon, batare daya sanya riga ajikinsa ba ya fice zuwa falo.

Hanunsa ya ɗaura akan makunnin wutan dake falon haɗe da ɗan matsawa, take haske ya gauraye cikin falon, saurin ɗago kanta da ta cusa acikin cinyoyinta tayi, idanunsu ya sauƙa acikin na juna, wani irin bugawa kirjinta yayi kamar zai faɗo waje, take jikinta yaɗauki rawa, da sauri ta rumtse idanunta, ganinsa a haka babu riga da tayi, ya mafi yunwar da takeji ɗaga mata hankali.

"Wai Uban me kikewa kuka?" ya tambayeta a tsawace.

Bakinta ne ya ɗauki rawa, ƙanƙame jikinta tayi guri guda, ahankali ta shiga jijjiga masa kanta alaman "Babu"

"Mcheeww" yaja tsuka cike da takaicinta.

Kallonta yayi a ƙufule sakamakon yanda yaga gaba ɗaya jikinta na rawa. Harara ya wurgamata haɗe da nufar inda zai sadashi da kitchine ɗin dake cikin falon.

Tana ganin tafiyarsa, ta saki wani irin marayan kuka, aranta tana cewa, inane takawo kanta, wataƙila ma saida ita zaiyi, shikenan itakam ga abun da guduwa yajawo mata.

Mintuna kaɗan yadawo cikin falon, hanunsa ɗauke da wani cup, ƙarasowa gabanta yayi haɗe da miƙa mata cup ɗin. Jikinta na rawa haka tasanya hanu ta karɓi kofin, ruwan tea ne aciki, hanunta har ɓari yake alokacin da takai kofin bakinta, abun da batasani ba shine Tea ɗin da zafi sosai, da sauri ta furzar da wanda ta kurɓa, sakamakon ƙona mata harshe da yayi, ta gefen ido yakalleta, haɗe da yin wata muguwar murmushi, yana sane ya haɗa mata tea ɗin da tafasheshshen ruwa.

Hawayene suka gangaro daga cikin idanunta, harshenta ya ƙone sosai, amma Allah yasani bazata iya haƙura da shan tea ɗin ba, saboda yunwa takeji sosai. Haka ta daure ta cigaba da shan tea ɗin tun tanajin zafinsa har ta daina ji, tas ta shanye tea ɗin ta aje kofin, lokaci guda jikinta ya soma tsatstsafo da gumi, sake jin gina bayanta tayi da jikin bango tana sauƙe ajiyar zuciya akai akai.

Fitowa yayi daga kitchine ɗin haɗe da sanya key ya rufe ƙofar, plate ne ahanunsa, wanda ke ɗauke da yankakkun kayan fruit, miƙa mata plate ɗin yayi cike da haushinta yace

"Gargaɗi na ƙarshe kada ki sake tashina idan ina bacci!"

Itadai kanta na ƙasa bata sake ɗagowa ta kallesaba tun ganin farko da tayi masa,  jin ƙaran rufe ƙofarsa ne, yasa ta sauƙe ajiyar zuciya, da bibbiyu take tura yankakkun kayan fruit ɗin abakinta,  fruit ɗin nada yawa, amma saida taci fiye da rabinsa sannan taji ta dawo cikin hayyacinta, hamma tayi haɗe da tashi tsaye tanufi wajen da fridge ke aje, bata iya buɗe fridge ɗin ba, hakan yasa tasoma kiciniyar ɓalle murfin, da ƙyar dai tasamu ta buɗe dayake murfin na glass ne, kana iya hango komai dake cikin fridge ɗin, goran ruwa ta ɗauka tasha, mayarda sauran ruwan tayi cikin fridge ɗin,  saɗaf saɗaf haka ta koma ɗakin da ta ganta aciki tun farko, jingina tayi da jikin ƙofar tana mai ƙarewa ɗakin kallo,   tsananin tausayin kantane ya kamata, yau gata a wata duniya wacce batasan ina bane,  gata acikin gida tare da wani, wanda batasan ko shiɗin waye bane, ahalin yanzu batasan menene makomarta ba, zamewa tayi akan yalwataccen carpet ɗin dake malale a tsakar ɗakin, kuka tashiga rerawa marar sauti, sosai tayi kuka harsaida taji kanta yayi mata nauyi, sannan ta tsagaita ajiyar zuciya tashiga sauƙewa akai akai, tana jingine ajikin bango, wani wahalallen bacci ya ɗauketa.....

Tunda kukanta ya tashesa yakasa komawa bacci, toilet yashiga ya ɗauro alwala,  dardumansa ya shumfiɗa yatada sallah.... Yajima yana salla kafun ya idar, laptop ɗinsa yajawo ya soma gudanar da wasu ayyuka, yananan har aka ƙira sallan asuba,   rufe laptop ɗin yayi yafita zuwa masallaci...

Sauri Sauri yake shirya kansa kasancewar angayyacesa meeting ɗin gaggawa anan branch ɗinsu dake cikin Kaduna.

Sanye yake da riga da wando na suit masu mugun tsada da kyau, navy blue colour,  takalmin ƙafarsa kuwa toms ne mai kyau shima navy blue colour,  sosai yayi kyau acikin kayan, nikaina bansan haɗuwarsa takai hakaba, sai yau dana gansa acikin shigar suit. Lol.
Agogon Rolex yake ƙoƙarin ɗaurawa a tsintsiyar hanunsa, babu abun dake tashi ajikinsa sai daddaɗan ƙamshin turarensa mai sauƙar da nutsuwa, gashin kansa kuwa sai ƙyalli yake fitarwa, sosai yasha gyara da mayuka kala kala,    wayarsa mai tambarin Apple abaya ya ɗauka, tare da key ɗin motarsa, kana yafice daga cikin ɗakin..

Haɗaɗɗiyar sabuwar motarsa BMW ya hau,  mai gadi na buɗe masa ƙofa ya cillata kan titi ahankali yake murza steering motar cike da nutsuwa..

Tun ƙarfe 7 tatashi zama tayi jigum acikin ɗakin,  kallon kayan jikinta tashigayi gaba ɗaya sunɓaci da jini, gashi sunyi bala'in yin dotti, banda ɓarkewan da saman rigarta yayi.

Tun tana zaune tana nazari harta kwanta, juyi kawai take tayi, amma gaba ɗaya bata da nutsuwa,  jin ana knocking ƙofar ɗakinnata  yasa taji ƴaƴan cikinta sun sake hautsinawa saboda tsoro,  cigaba akayi da knocking ƙofar, yayinda itakuma ta matse jikinta waje ɗaya,  mugun tsoronsa takeji.

"Good Morning Madam" taji muryan mai knocking ƙofar na faɗan haka.

Tsorone yasake kamata,  raba idanu tashiga yi tana neman wajen ɓuya don batasan meyake cewa ba, tasan dai wani yare kawai yake yi.

Peter dake tsaye jikin ƙofa hanunsa riƙe da leda ɗin abinci, yaji yasoma gajiya saboda haka, yaciro wayarsa yaƙira ogansa,    bansan mai SOORAJ yafaɗa masa ba, sai gani nayi ya aje ledan  abakin ƙofa yajuya yayi tafiyarsa.

Jin shiru andaina ƙwanƙwasa ƙofarne bakuma alamar motsin mutum, yasata sauƙo daga kan gadon ahankali.  Saɗaf saɗaf take tafiya harta buɗe ƙofar ɗakin, bugewa tayi da ledan da Peter ya ajiye.  ko kallon ledan batayi ba tashiga takawa harzuwa tsakiyan katafaren falon.   Gaba ɗaya bata cikin nutsuwarta sai waige waige take, ƙirjintane keta bugawa da sauri sauri fatanta ɗaya Allah yasa kada wani yakamata.   Wata ƙofa dake cikin falon tanufa, tana buɗe ƙofar kuwa ta buɗu,  wani irin ƙaƙƙarfan ajiyar zuciya tasauƙe sakamakon ganinta a waje da tayi.   Da sauri sauri ta nufi  inda ta hango wani ƙaton gate, burinta ɗaya shine ta ganta awaje, sam batajin zata iya zama agidan ƙattin maza, wataƙilama da wata manufa suka ajiyeta.      Taci sa'a kuwa babu kowa abakin gate ɗin saboda haka gadan gadan tanufi ƴar ƙaramar ƙofan dake jikin gate ɗin ɗaura hanunta tayi ajikin ƙofan tare da buɗewa....

*(Niba cikakkiyar bahaushiya bace dole sai kunyi haƙuri da hausana, nasan wasunku bakomai suke ganewa acikin rubutuna ba😥)*

*21/March/2020*

*✅OTE ME ON WATTPAD*
@fatymasardauna

#hearttouching
#truelove

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

*(Banso cigaba da rubutunnan ba amma yazanyi daku😥 My Wattpadians sun sakoni gaba, waƴand sukace aci gaba sunfi waƴanda sukace a dakata yawa... Nagode da nunawa littafina ƙauna. Inayinku hundred percent My Wattpadians Allah yabar Ƙauna!!)*

*Chapter 9*

Sake lumshe gajiyayyun idanunsa yayi, aransa yanaso yaje yasanar da mahaifiyarsa matsalan dake damunsa, saidai kuma sosai wata zuciyar ke gaya masa hakan badai dai bane. Jikinsa asanyaye ya nufi wajen da yayi parking motarsa.
***
Bacci tasha sosai ba ita tafarka ba sai lokacin da aketa ƙiraye ƙirayen sallan la'asar. Banɗaki tashiga ta ɗauro alwala, kan lallausan carpet ɗin dake malale a gefen gadon ta hau haɗe da tada Sallah, bayan ta idar da sallan ta zauna jigum haɗe da sanya hannayenta ta tallafi kyakkyawar fuskarta. Jitayi ruwan hawaye sun cika idanunta, tausayin kanta take, musamman ma yanzu da take cikin rayuwa irin ta BULAYI.
***
Kallon Mamaki Mas'oud ke yiwa SOORAJ, da ƙyar ya iya cewa. "Me hakan yake nufi kenan SOORAJ? kakuwa san illan abun da kake shirin aikatawa? ajiye mace'n da ba muharramanka ba acikin gidan ka fa abune da baidaceba sannan kuma hatsarine babba"

Murmushin gefen baki SOORAJ yayi, haɗe da ɗaukan cup ɗin fresh milk ɗin dake aje agabansa yaɗanyi sipping kaɗan, miƙewa tsaye yayi tare da kai dubansa ga agogon dake ɗaure a tsintsiyar hanunsa.

"Ni zan wuce" yace da Mas'oud ataƙaice.

Kallonsa kawai Mas'oud yayi haɗe da girgiza kansa.
"Nasani dama SOORAJ ba zaka taɓa sanjawa ba" Mas'oud yafaɗi haka acikin zuciyarsa.
SOORAJ baisake bi takan Mas'oud ba yanufi wajen da motarsa take.

Yana shiga cikin motar ya murza mata key haɗe da cillata kan titi. Direct babban asibitin dake cikin Garin Kaduna ya nufa.

Ajiyar zuciya mai ƙarfi Dr.Waleey yayi haɗe da gyara zamansa, kallon SOORAJ yayi cike da tausayawa.... "Ka kwantar da hankalinka SOORAJ, akwai wani sabon magani idan na ɗauraka akai wata ƙila adace"

Kallon Dr.Waleey Sooraj yayi da shanyayyun idanunsa.

"Banatunanin akwai wani maganin da zan ƙarasha Dr.Waleey, zan haƙura kawai, zamana ahaka wata ƙila shine abu mafi alkhairi!" yafaɗi maganar cike da raunin zuciya.

"Karkace Haka SOORAJ, kada ka karaya, sauƙi zai iya samuwa ako da yaushe, kasan Allah

Babu yanda baya ikonsa, amma nikaina al'amarinka yana matuƙar girgizani, nasha samun case ire iren  wannan, amma naka yayi worse."  Ɗan tsagaitawa daga maganan Dr.Waleey yayi, haɗe da sauƙe ajiyar zuciya, cigaba yayi da cewa.
"Kada kadamu Sooraj Insha Allah watarana sai labari." ya ƙare maganar cike da son ƙarfafawa Sooraj guiwa.

Murmushi Sooraj yayi haɗe da cije lips ɗinsa,   jin Dr.Waleey kawai yake, amma ji yake ajikinsa kamar shikam ahaka zai mutu, ahaka zai ƙare rayuwarsa babu wata ingantacciyar farinciki. Sunan wasu magunguna Dr.Waleey ya rubutawa Sooraj a ƴar wata farar takarda.  Hanu Sooraj yabasa sukayi musabaha, kafun ya fice daga cikin office ɗin.

Direct Pharmacy yaje yasaya maganin, sannan yabar cikin asibitin.
***
Idar da salla'n isha ɗinta kenan ta zauna akan gado, haɗe da kama cikinta daketa yi mata kukan yunwa, gawani tsoro daya lulluɓeta, ayanda tafahimta shine ita kaɗaice ke rayuwa acikin gidan, domin kuwa tunda ta zauna bataji motsin kowa ba.  Sam bata saba irin wannan zamanba, tasaba gaba ɗaya rayuwarta cikin aiki take, sam bata da hutu, yi wancan ɗauko wancan, da haka ta saba, shiyasa gaba ɗaya takejinta amatuƙar takure.

Ƙarfe takwas na dare daidai motarsa ta kunno kai cikin gidan.     Yana gama daidaita parking ɗin motar tasa ya tattaro ledodin dake cikin  motar yafito.

Sake matse jikinta tayi haɗe da soma ƙif ƙifta oily eyes ɗinta, jin motsi acikin falon yasa taɗanji gabanta ya faɗi.

Direct bedroom ɗinsa ya wuce, kayan jikinsa ya cire kana ya wuce toilet.

Fitowa yayi ɗaure da towel aƙugunsa, jikinsa duk danshin ruwa.   Agaban dressing mirror ya tsaya, tare da ɗaukan ɗan ƙaramin towel yashiga goge ruwan dake jikinsa. sama sama yashafa body lotion ɗinsa mai daɗin ƙamshi,   3 guater jeans yasanya haɗe da saka wata riga marar nauyi, da turarensa mai sanya nutsuwa ya feshe jikinsa. aje comb ɗin dake hanunsa yayi, haɗe da sanya hanu ya shafi lallausan sajen dake kwance akan fuskarsa, wayarsa ya ɗauka yafice daga cikin ɗakin.

Tsayawa yayi ajikin ƙofar ɗakin, haɗe da ɗaura hanunsa akan handle ɗin ƙofar, kamar zai tura ƙofar ciki kuma sai ya fasa, hanunsa yakai jikin ƙofar yayi knocking.

Da sauri takalli ƙofar jin ana ƙwanƙwasawa,  shiru tayi haɗe da ƙurawa ƙofar ido.    Sooraj dake tsaye ajikin ƙofar yasake ƙwanƙwasawa.

Saɗaf saɗaf ta sauƙo daga kan gado, zuwa tayi ta buɗe ƙofar, karab idanunsu ya sauƙa acikin na juna, wani irin bugawa taji ƙirjinta yayi, abubuwa biyune suka haɗe mata, ganin kyawawan eyeballs ɗinsa da kuma daddaɗan ƙamshinsa mai sanyaya zuciya.

"Biyoni!" yace da ita atakaice haɗe da juyawa ya koma cikin falon,  sumu sumu haka ta bi bayansa tana matse jikinta domin kuwa mayafin rigar dake jikinta iya ƙirjinta kawai ya tsaya.

Zama yayi akan lallausan carfet ɗin dake malale tsakiyan falon, tare da tanƙwashe ƙafafunsa. Cikin sanyi ta ƙaraso cikin falon, durƙusawa tayi aƙasa haɗe da sunne kanta ƙasa.
"Gani"
tace dashi in a silent voice.

"Kinci abinci?" yatambayeta batare daya kula sashin da take ba.

Mamakin tambayar da yayi matane ya kamata,  ta ina zata samu taci abinci bayan babu abincin.

"Bakiji bane?" yasake tambayarta cike da ƙosawa.

"A'a banci ba" tafaɗa masa haka a sanyaye.

Ledan dake aje agefensa ya jawo.  "Ɗauko min plate" yafaɗa still batare daya kalleta ba.

Inda take tunanin nanne kitchine ta nufa,  sum sum ta dawo riƙe da plate a hanunta.

Durƙusawa tayi haɗe da miƙa masa plate ɗin.

Ledar ya buɗe ya ciro take away guda ɗaya, haɗe da tura mata gabanta,  ɗaukan ɗaya yayi ya juye abun dake ciki acikin plate ɗin da ta kawo masa.

Spoon yasa acikin plate ɗin yasoma tsakalan jalop rice ɗin da yaji busashshen kifi.

Shiru  tayi ta kasa cin abincin, tsoron tashi take, sannan kuma bazata iya sakewa taci abinci a gabansa ba.

Tunda yafara tsakalan abincin bai ko da ɗago kansa ya kalleta ba, abincinsa kawai ya ke cusawa,   fiye da rabi yaci sannan ya ture plate ɗin gefe, goran peach ɗin dake gefensa ya ɗauka, haɗe da tsiyayawa acikin wani ɗan ƙaramin glass cup, ahankali yake sipping peach drink ɗin,   yana kammalawa ya miƙe ya wuce ɗakinsa.

Tanajin rufe ƙofarsa ta saki wata ajiyar zuciya mai ƙarfi, take away ɗin ta jawo gabanta, buɗewa tayi, amma amaimakon taga shinkafa kamar yanda taga nasa, sai taga ferfesun naman kaza ne aciki, wani yawu ta haɗiya haɗe da soma ci ahankali, bata wani ci sosai ba taji gaba ɗaya cikinta ya cushe, rufewa tayi tare da ɗaukan goran ruwan dake gefenta tasha.  Ɗauke plate da take away ɗin tayi tamayar kitchine, zama tayi afalon tana daɗa ƙarewa falon kallo, idanunta ta sauƙe akan makeken tv plasma'n dake cikin falon,  kasancewar ba akunne yakeba yasa ta

ɗauke idanunta daga kansa, kanta ta jingina ahanun kujeran da take zaune aƙasanta,  shiru tayi haɗe da lumshe idanunta da suka kawo ƙwalla, tunanin babanta ne ya faɗo mata arai, take taji zuciyarta ta ƙara karaya,, tana cikin wannan tunanin bacci ya ɗauketa ahaka.

Tsab ya gama shirin kwanciyarsa,  bayan ya gama latsa laptop ɗinsa.   Kwanciya yayi flat akan gadon haɗe da lumshe idanunsa,  sosai yakejin daɗin sanyin Ac'n dake hurasa,   wani abune yazo ya toshe masa maƙoshi,  akowacce dare baya samun wata gamsashshiyar nutsuwa, yanaji ajikinsa akwai wani gibi a tattare dashi,  haƙoransa yasa ya datse laɓɓansa,  sakamakon tunowa da korar da Ummu tayi masa ɗazu da yayi,  sam baya ganin laifin iyayennasa, saboda kowa tunani yake cewa  ason ransa yake sakan matan da ake aura masa, tunowa da magungunansa da yasayo yau yayi, miƙewa yayi jiki a sanyaye ya ɗauko magungunan,  ruwa ya ɗauka ya sha.

Luf yayi akan tattausan katifarsa,  duk yanda yaso bacci ya ɗaukesa ya kasa shikaɗai yaketa juyi akan gado,  saƙƙowa yayi daga kan gadon haɗe da zura slippers ɗinsa, falo ya nufa hanunsa riƙe da wayarsa.

Bai lura da itaba sam saida ya zauna akun kujeran dake facing ɗin wanda ta ɗaura kanta akai.

Shiru yayi haɗe da ƙura mata idanu,  kallon yanda tayi kwanciyar nata yasoma yi, duka jikinta na ƙasa yayinda kanta kuwa ke kan hanun kujera, dagani kasan baccinne ya ɗauketa batare da ta shiryawa hakan ba,  kallon ɗan ƙaramin bakinta dake ɗan buɗe yayi, tare da kawar da kansa gefe.

Ɗan zamewa yayi ya jingina bayansa da jikin kujera, lumshe idanunsa yayi haɗe da soma sauƙe numfashi ahankali.

*** *** ***

4:50 am  dai dai ya shiga buɗe idanunsa ahankali, azabure ya tashi zaune yana bin inda ya gansa akwance da kallo,  yana jingine akan kujera bacci ya ɗaukesa batare daya sani ba, hanu yasa ya dafe goshinsa haɗe da furzar da wani iska mai zafi daga bakinsa.  Kallon gefensa yayi tananan kamar ɗazu saidai yanzu tadawo da kanta ƙasa, yayinda ta takure jikinta waje ɗaya da alama sanyin AC ne ke damunta.

Miƙewa yayi ya wuce ɗakinsa yana me mamakin kansa, tunda yake bai taɓa kwana afalo ba sai yau, sam baisan yaushe bacci ya ɗaukesa ba.

Toilet yashiga haɗe da sakarwa kansa ruwa.  Yana fitowa ya zura maroon jallabiya tare da ɗaukar sallayansa ya fice daga cikin ɗakin.

Haka ya wuceta afalon tana ta bacci ko kallon inda take baiyi ba ya fice.

Ahankali ta ware idanunta akan haɗaɗɗen zanen POP'n dake mamaye saman falon, fuskarta ta ɗan yatsuna haɗe da sanya hanunta akan wuyanta, jitayi wuyannata ya ƙage waje ɗaya sosai yakeyi mata ciwo, ahankali ta miƙe tsaye, kallon falon tayi sannan ta wuce ɗaki, banɗaki tashiga ta ɗauro alwala, tana idar da sallan ta zauna akan sallayan haɗe da sake lumshe idanunta, ciwo wuyanta keyi mata sosai hakan yasa ko motsa kanta batason yi.

Tunda yafita daga gidan baidawo ba sai Ƙarfe 9 na safiya, yana shiga bedroom direct toilet ya nufa, kwanciya yayi luf acikin jakuzzien daya ji ruwan wanka wanda aka cakuɗasa da daddaɗan turaren wanka mai ƙamshin gaske, lumshe idanunsa yayi, kansa ne ke ɗanyi masa ciwo kaɗan kaɗan, ajiyar zuciya yayi, sakamakon tunawa da yayi cewa gobe zai wuce Abuja, sai dai kuma baisan ina zai saka wannan kayan daya ɗaukowa kansa ba.

***

Acan Ƙauye kuwa, Inna Ma'u sun wayi gari anata shirye shiryen ɗaurin aure, basu farga da cewa Ziyada bata gidan ba saida jama'a suka hallara don ɗaurin auren, tashin hankali kam Inna Ma'u ta shigesa, babu inda ba su bazama ba wajen nemanta amma babu ko wani wanda yace ya ganta. Sosai hankalin Mahaifinta ya tashi, har baisan sanda wasu ƙwalla suka gangaro daga cikin idanunsa ba, Inna Ma'u kuwa bala'i tashigayi haɗe da tsinewa Ziyada tana cewa wai ta cucesu ta kunyatasu, shikuwa Tsoho Ɗan Dashe ai masifa yadingayi kamar zai tashi sama, take rashin mutumcinsa ya tashi, nan yakafe kaida fata lallai sai Inna Ma'u ta biyasa kuɗaɗen daya dinga narka mata, idanu Inna Ma'u tashiga zarewa kamar munafuka.....
***

Riga da wandone ajikinsa wanda suka matuƙar yi masa kyau, cike da ƙosawa ya ture laptop ɗin dake gabansa, kusan awansa biyu yana aiki da ita, gaba ɗaya jinsa yake agajiye, kitchine ya wuce ya haɗa tea ɗinsa, dawowa cikin falon yayi ya zauna, kallon ƙofar ɗakin da take ciki yayi, kana ya dawo da kallonsa ga agogon dake saƙale ajikin bangon ɗakin 2:00pm dai dai yagani, sake kallon ƙofar ɗakin yayi, sai alokacin ya tuno da cewa ko break bai bata ba, kallon tea ɗinsa yayi haɗe da sake kallon ƙofar nata, yakan manta da cikinsa ma balle na wani, shi dama sam abinci bai dameshi ba, sannan ba ɗawainiyar kowane akansa ba, shiyasa baiwani damu da wani yaci ko karyaci ba, baisan ya ake kula da wani ba, saboda shikaɗai yake rayuwarsa bawani a ƙasansa, Saida yagama shanye tea ɗinsa kafun ya tashi daga zaunen da yake. Wayarsa ya ɗauka ya turawa wata number text message, yanaganin alamar saƙon yatafi ya ajiye wayartasa. Kwanciya yayi akan kujera haɗe da lumshe idanunsa.

(Readers anya Sooraj bazai kashe Ziyada da yunwa ba kuwa? My Wattpadians karku taɓa mantawa saboda ku kawai wallahi nayi typing, saboda haka kuma ku ɗaga darajata tahanyar bani comment da Vote, sannan kuma ba kullum zakuna samun Update ba.)
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*

*Wattpad*
@fatymasardauna

*Chapter 11*

Tunda jirgin su ya ɗaga bai buɗe idanunsa ba har jirgin nasu ya sauƙa a NNAMDI AZIKWE Internation airport. Buɗe idanunsa yayi a hankali tare da zare sit belt ɗin dake jikinsa, dubansa ya kai zuwa gareta, wani babban abun mamaki ganinta yayi tana bacci, fuskarta ɗauke da wani bushashshen hawaye, takaicinta ne ya sake kamashi, shi sam baisan ita wace irin bagidajiya bace ba, yanzu aɗan tafiyan da bai wuce 30 minute ba har ace tayi bacci ?

Hanunsa yasa ya zunguri kanta, da yake baccin nata baiyi nisa ba, hakan yasa ta buɗe idanunta, ta sauƙe ƙwayar idanunta a kansa.

Nuni yayi mata da ta cire sit belt ɗin dake jikinta, cire sit belt ɗin tayi tana mai mutsutstsuka idanunta da suke cike da bacci.
Gudun kada tayi masa halinnata na ƙauyanci ta ba da shi agaban mutane yasa ya tusa ƙeyarta gaba suka nufi hanyar fita daga cikin jirgin.

Cikin takunsa na isa yake sauƙowa daga kan matattakalan jirgin, sanye yake da riga da wando na jeans baƙaƙe sai kuma facing cap white colour daya sanya akansa, kalan takalman dake ƙafansa.
Kallo ɗaya zakayi masa kafahimci cewa shiɗin cikakken ɗan gaye ne wanda yake murza naira. babu wani makusa atattare dashi, komai nasa yayi hundred percent, sam a halittarsa ta bayyane bazaka taɓa kawo cewa yana ɗauke da wata damuwa ba, saboda shiɗin irin mazan nanne masu aji da wayewa, sannan yanada cikar halitta, komai nasa abun so ne ga ƴa macen da tasan kanta. yanada kyawun jiki data fuska, ajikinsa dai kam baida wata makusa, amma kuma saidai shikaɗai yasan menene aibunsa, wanda idan da zai bayyana rauninsa a fili, to tabbas da sai kowacce mace ta gujesa, saboda aibun dayake ɗauke dashi, yafi tsananin kyawu da dukiyarsa tasiri wajen rugujewar farincikinsa. idan akayi dubi da lalurar dake damunsa shekara da shekaru to tabbas kyawunsa da haɗuwarsa ba zasu amfana masa komaiba, dama kuma hakane yawanci kowani bawa da irin tasa tawayan.

Yana gama sauƙowa daga kan matattakalan ya gyara zaman facing cap ɗin dake kansa. Wani

matashin saurayi ne ya ƙaraso wajen da suke da sauri. Cike da girmamawa ya ce.

"Barka da zuwa Oga"
yaƙare maganar yana mai karɓan jakan dake hanun Sooraj ɗin...

"Yauwa!" Sooraj ya amsa ataƙaice.

Juyowa yayi ya kalli Ziyada dake ta faman murje gajiyayyun idanunta, tana kuma ƙarewa haɗaɗɗen wajen kallo, domin kuwa wannan airport ɗin ya ɗarawa wanda suka baro.

"Kuje mota ina zuwa" yafaɗi haka yana mai ƙoƙarin shiga wata babbar ƙofa ta glass dake cikin airport ɗin.

"Ranki yadaɗe muje ko" wannan saurayin yace da Ziyada, da haryanzu take ta kalle kalle.
Babu musu tabi bayansa, sai dai a ƙasan zuciyarta shumfuɗe take da tsoro, zuwa yanzu wata zuciyar na sanar da ita cewa "Sai da ita Sooraj zaiyi"  hakanan zuciyarta tasa mata cewa ba banza yake ɗawainiya da ita ba, saidai kuma ta wata fuskar sam baiyi kama da mugayen mutane ba, duk da bayi da sakewa, amma baiyi kamanni da mugaye ba.

Direct wajen wata dan ƙareriyar mota taga sun nufa,  buɗe mata gidan gaba ɓangaren mai zaman banza matashin saurayin da ake ƙira da Kamalu yayi,  yana mai satan kallon fuskarta, mamakine cike azuciyarsa, yana mamakin a ina ogansa ya samota, yasan Sooraj yakuma san baida wata ƙanwa mace balle yace itaɗin ko ƙanwarsa ce, ya kuma san halin ogan nasa baya neman mata, balle ko yace  wata ya ɗauko zasuyi zaman haramci,  da wannan tunanin yashiga ɓangaren driver ya zauna.

Fuskarta ta manna ajikin glass ɗin window'n motar tana mai kallon mutanen dake ta hada hada a wajen.
Kallonta ta mayar ga ƙofar da taga ya shiga, daidai lokacinne kuma ta hangoshi ya fito, fuskarsa ɗauke da wata ƴar guntun murmushi da iyakanta kan leɓe,    tunda take arayuwarta bata taɓa ganin mutum irinsa ba,  haka kawai take ganinsa wani daban acikin mutane, komai nasa special ne.    Gani tayi wani ya biyosa abaya yana dariya, atare suka jero da Sooraj ɗin fuskar wannan ɗin ɗauke take da fari'a saɓanin Sooraj da fuskarsa ke ɗauke da yanayi irin na ba yabo ba fallasa.  Har wajen motar Ma'arouf ya rako Sooraj. (Ma'arouf abokin Sooraj ne sannan babban matuƙin jirgin sama ne)

Buɗe gidan baya Sooraj yayi ya shiga,  ɗan ranƙwafowa Ma'arouf yayi haɗe dayin knocking glass ɗin window'n motar ta inda Ziyada ke zaune,  a hankali Kamalu yayi ƙasa da glass ɗin window'n, atunaninsa gaisawa Ma'arouf ɗin keso suyi dashi, don yasan halin Ma'arouf akwai kirki, baruwansa komin ƙasƙancinka zai sake kuyi mu'amala dashi.

Waro idanunsa yayi haɗe da sanya hanu ya shafi fuskarsa,  "Masha Allah!" yafaɗa acikin zuciyarsa bayan yayi tozali da kyakkyawar fuskar Ziyada.

"Wow!! Raj ina kasamo mana wannan haɗaɗɗiyar baby'n haka?     i hope dai ba kayan ka bace?"    Ma'arouf yatambayi Sooraj yana mai sake ƙarewa fuskar Ziyada kallo, saboda yarinyar tayi matuƙar tafiya da imaninsa musamman ma Innocent face ɗinta.

"Kaya na?" Sooraj ya maimaita tambayar da  Ma'arouf yayi masa abakinsa cike da mamaki.

Dariya Ma'arouf yayi haɗe da dawo da kallonsa ga Sooraj.  Gira ɗaya ya ɗage masa haɗe da cewa

"To ya kagani idan da ace zata zama MALLAKINA?"

Murmushin gefen baki Sooraj yayi haɗe da cewa " ko zaka jarraba hakan ?" yanayin yanda yayi maganar cikin halin ko inkula,  shiya sanya  Ma'arouf yin murmushi haɗe da kallon Ziyada wacce idan da za'a kasheta bata fahimci inda kalaman nasu suka dosa ba, ita hankalinta ma ba akansu yake ba.

"Zan jarraba idan kabani dama, amma bayanzuba zaifi kyau nayi kiwonta" Ma'arouf yafaɗi haka cike da shauƙi.

"Banda enough time zaka iya jan motar mutafi?" Sooraj yafaɗi haka ga Kamalu cike da halin ko inkula da zancen da Ma'arouf ɗin keyi.

Jin kalaman Sooraj yasa Kamalu saurin tada motar.

Ma'arouf dake tsaye yana kallon Sooraj yasaki murmushi haɗe da maida kallonsa ga kyakkyawar yarinyar dako sanin sunanta baiyi ba.   Maida Glass ɗin window'n Kamalu yayi ya rufe, haɗe da yin reverse.   Juyawa Ma'arouf yayi yakoma inda ya fito yana sakin wani murmushi.

Tunda suka hau titi ta sake baza idanunta wajen kalle kallen shukokin dake jere gefe da gefen titi, dogin gine gine masu kyau suketa  wucewa, komai gwanin burgewa.
Shikuwa tunda ya ɗauki jarida yamai da hankalinsa akai, ko ɗago kansa baiyi ba, sai dai har aƙasan zuciyarsa yanata juya kalaman Ma'arouf da yake tambayarsa "wai itaɗin kayansa ce?" Hmmm lallai yasake yarda babu wani wanda yasan sirrinsa, inbanda ma rashin aiki irin na Ma'arouf mai zaiyi da wannan ƴar mitsilan yarinyar? shi bayaji idan ma akwai wani abu acikin iskanci to zai samu atattare da ita, duka dukanta bata wuce 18 to 19 years ba to me zai ɗauka ajikinta? balle ma shikam mace kodaga wacce duniya tafito bazata amfanesa ta fannin mu'amala ba, saidai ko tawani ɓangare kamar aiki da sauransu.

Asokoro.

Gaban  wani tangamemen gate mai kyau da tsari Kamalu driver ya tsaya haɗe da soma danna

horn ɗin motar,  da sauri wani daga cikin gidan ya wangale musu makeken gate ɗin, shikuwa Kamalu driver ya shigar da motan ciki.

Yana gama daidaita parking ɗin motar ya juyo ga Sooraj cike da ladabi yace "Ranka ya daɗe mun ƙaraso"

Batare daya ɗago kansa daga karatun jaridan dayake ba yace "Okay!"
Fita daga cikin motar Kamalu driver yayi bayan ya ɗauki jakar Ogannasa ya yi cikin gida da ita.

Ganin yana ƙoƙarin fita daga cikin motar yasa itama ta buɗe murfin motar ta fito,  compound ɗin gidan take ta kallo.

Kamar jela haka take biye dashi a baya, kafun yaƙaraso ma tuni Kamalu yasa key ya buɗe ƙofar da zata sadasu da cikin katafaren falon gidan.

Ganin ya buɗe ƙofar yashiga yasa itama ta bi bayansa Tana jefa ƙafafunta acikin falon suka soma nutsewa acikin wani lallausan carpet dake malale aƙofar shigowa falon, wani sanyin AC ne ya ratsata.   Kamalu driver na ajiye jakan hanunsa ya fita daga cikin falon haɗe da rufo musu ƙofar,  sam tamanta ma tare suke dashi, falon tashiga ƙarewa kallo, komai na cikin falon milk colour ne daga kan kujeru har zuwa kan labulaye, falo ne haɗɗaɗɗe mai ɗauke da tsari irin na mazan da suka san kansu.

Sooraj kuwa kota kanta baibi ba direct ɗakinsa ya wuce,  yana shiga yarage kayan dake jikinsa haɗe da shigewa cikin bathroom.    Al'adansane idan yaje wanka kafun yayi wanka sai ya kunna shower ruwa ya dakesa sosai, yau ma hakance ta kasance, sosai ruwan shower yadaki jikinsa, sannan yayi wanka.

Fitowa yayi daga cikin bathroom ɗin sanye da rigan wanka ajikinsa.

Akan kujeran dressing mirror ya zauna haɗe da ɗaukan comb yashiga taje sumar dake kansa wacce take a jiƙe da ruwa.
Yana kammalawa yayi amfani da handryer wajen busar da gashin kansa,  hakanan yake shi mutum ne maison tara suma akansa, sannan kuma koda yaushe, askin kansa irin na turawa ne, shiyasa always yake yanayi dasu,  sosai kuma askin keyi masa kyau, saboda gashin nasa yana da laushi, ga kuma gyaran da yakesha na mayuka masu tsadan gaske.

Sosai yake son combat trouser saboda hakanema yawancin wandunansa suka kasance Combat.    Yanzu madai Combat jeans yasanya a jikinsa.   kwanciya yayi akan makeken gadonsa,  lumshe idanunsa yayi haɗe da jawo wayarsa ya saƙala earpiece akunnensa,  waƙa yakeji mai sanyin sauti, hakan yasa  duk yaji jikinsa yayi weak.

Jin ansoma ƙiraye ƙirayen sallan Isha ne yasashi miƙewa,  jallabia ya sanya ajikinsa, haɗe da zura flat shoe aƙafafunsa ya fice daga cikin ɗakin.

*** *** ***

Biro ya ɗauka ya cike wata farar takarda dake aje kan babban table ɗin dake gabansa.  Ɗaukar takardan yayi yashiga jujjuyata acikin hanunsa, kamar wani maiyin nazari,  kallon katafaren office ɗinsa yayi haɗe da fitar da wani dogon numfashi ta bakinsa.

Hanu yasa ya shafi tarin sumar dake kansa,  ware idanunsa da suka soma rikiɗa daga farare zuwa kalan ja yayi, wani zafi zafi ya keji aƙasan ƙirjinsa, ga wani zazzaɓi dake shirin dirar masa lokaci guda,  haka yake  aduk sanda yayi yunƙurin tuna wani abu da ya danganci sha'awa sai yayi wani zazzaɓi mai zafin gaske, abun yakan fin ƙarfin brain ɗinsa, duk yanda yaso yayi wani tunani mai ƙarfi abun ya faskara.       Tashi yayi yanufi wata ƴar ƙaraman drawer dake cikin office ɗinnasa,     buɗe drawer'n yayi haɗe da ciro wata allura, tun ɗazu ya haɗata amma hatsarin dake cikinta yasa yaɗan jinkirta yinta, shikansa baisan mai zai biyo baya ba idan yayi alluran, amma bashi da wani zaɓi wanda ya wuce yayi ta.
akan jijiyar dake hanunsa  na dama ya saita alluran, rumtse idanunsa yayi haɗe da soma matse ruwan alluran acikin jikinsa,  yana gama yiwa kansa alluran ya buɗe durstbin ya jefa alluran aciki,     suit ɗin sa dake rataye kan kujera ya ɗauka yariƙe ahanunsa, haɗe da ɗaukan wayoyinsa.    Fitowa yayi daga cikin office ɗin haɗe da sa key  ya rufe ƙofar office ɗin.      Ta ƙofar baya yabi   direct inda zai sadasa da parking space ya nufa,   yana zuwa ya faɗa cikin motarsa, haɗe da kunnata yafice acikin Bank ɗin baki ɗaya....

Yanayin yanda yake murza steering motar kaɗai ya isa tabbatar maka da cewa ba ƙalau yake ba, saboda a slow yake tuƙa motar kamar wani wanda baida ishashshen ƙarfi ajikinsa, ahalin yanzu yakai wani stage da ko iya kallon gabansa bayayi sosai,  idanunsa sun yi jajur dasu yayinda suka ƙanƙance alokaci guda, yanayin yanda yake danna horn ɗin motar ne yasa mai gadi ya yi saurin wangale masa gate,  kashe motar yayi haɗe da kifa kansa akan steering motar.  Jiyake gaba ɗaya duniyar na juya masa, gawani zazzaɓi da ya rufesa, hatta numfashinsa saida ya sauya.  Da ƙyar ya iya buɗe murfin motar ya fito. Direct babban falon gidan ya nufa.

Tana zaune akan sofa ta ƙurawa TV plasma'n daketa aiki idanu, sosai kallon ya ɗauki hankalinta. Ahankali ya tura ƙofar falon ya shiga, idanunsa a lumshe haka yasoma takawa zuwa cikin falon,   ɗago da manya manyan idanunta tayi ta kalleshi, kasa ɗauke idanunta tayi akansa ganin yanda yake tsaye kamar ma baya cikin hayyacinsa.     Yana ɗaga ƙafansa yaji gaba ɗaya jikinsa yayi sanyi komai nasa ya tsaya cak, take numfashinsa ya ƙwace mai, yanke jiki yayi ya faɗi a wajen baya ko numfashi.

*Vote me on Wattpad*
@fatymasardauna

#heartouching
#truelove

*Vote me on Wattpad*
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

#romance

*Chapter 12*

Arazane ta tashi daga zaunen da take haɗe da waro manya manyan idanunta.   Lokaci guda jikinta ya ɗauki rawa,  ƙafafunta na rawa haka ta nufi inda yake a yashe baya numfashi.

Hanunta dake rawa ta ɗaga haɗe da kaiwa kan fuskarsa, hanunta tasa adai dai saitin hancinsa, saidai bataji abun da takeson jiba, wato numfashi.

Tsorone yasake kamata, hanunta ta ɗaura akan kafaɗunsa ta shiga jijjigasa, cikin wata irin murya mai ɗauke da tsantsar tsoro haɗe da ruɗewa tace.   "Katashi ka buɗe idanunka Don Allah!"        wasu hawaye masu zafi ne suka soma sulalowa daga cikin idanunta suna sauƙa akan fuskarta.     Ganin jijjigashi da takeyi bazai kawo mata wata mafita ba, yasa aguje ta fice daga cikin falon,  wajen mutumin dake zaune a bakin tankamemen gate ɗin gidan ta nufa.   Yanayin yanda yaganta abirkice har yaso yaɗan tsoratashi.    Kafun yace wani abu ta rigashi cikin haki tasoma cewa....     "Baya numfashi kataimakeni kada ya mutu!"

Zaro idanunsa waje Sammani mai gadi yayi cike da tsoro. Yana ƙoƙarin tambayarta meke faruwa, yaga ta sake rugawa aguje ta koma ciki.  Cikin hanzari shima ya rufa mata baya.

Sake zube guiwowinta tayi  a ƙasa haɗe da cigaba da jijjigashi,   Dai dai lokacin Sammani mai gadi ya shigo,   ganin Ogan sa kwance aƙasa baya motsi yasanyashi ƙarasowa cikin falon da

sauri har yana jin tuntuɓe.

"Meke faruwa mekikayi masa?" Sammani dake a ruɗe ya tambayi Ziyada wacce gaba ɗaya hawaye sun gama wanke mata fuska.

Cikin tsoro tashiga girgiza kanta cikin sarƙewar murya tace.

"Wallahi banyi masa komai ba, bani bace, kawai nima gani nayi ya faɗi, Allah banyi masa komai ba!" Taƙare maganar tana mai fashewa da wani irin kuka mai sauti.

Da gudu Sammani yafita daga cikin falon, Kamalu driver yaje ya ƙira suka dawo falon a tare, hankalinsu amatuƙar tashe.

Da ƙƴar Kamalu driver da Sammani suka iya ɗaga Sooraj suka yi waje dashi, ganin haka yasa itama ta rufa musu baya, mota Kamalu ya buɗe suka sanyashi agidan baya.

"Kajira gidan, mu zamu kaishi asibiti" Kamalu driver yace da Sammani mai gadi. Kallon Ziyada da har yanzu idanunta ke fitar da ƙwalla yayi. "Muje" yace da ita yana mai buɗe mata murfin motar, da saurinta ta faɗa cikin motar shima Kamalun yashiga. Sammani ya buɗe musu gate suka fice daga cikin gidan, gudu sosai Kamalu keyi hakan yasa basu wani jima ba suka isa asibitin da yasan Sooraj ɗin nazuwa.

Da taimakon wasu likitoti aka ɗaura Sooraj akan wani gado mai ƙafafun taya, sannan aka gungurasa zuwa Emergency Room..

Kai Ziyada ta cusa acikin cinyoyinta, haɗe da sakin wani sabon kuka, addu'a take aranta Allah Yasa ba mutuwa yayi ba, hakanan takejinsa acikin wani ɓangare na jikinta, ko ba komai yayi mata hallacci, ya killace rayuwarta daga gurɓacewa, bazata taɓa son wani abu ya sameshi ba.

A Emergency Room kuwa sosai likitoti suka duƙufa akansa wajen basa taimakon gaggawa, da ƙyar suka samu suka shawo kan al'amuran, alokacin da suka gano matsalar kuwa baƙaramin mamaki sukayi ba, domin sun gano cewa allura akai masa ko yayiwa kansa, wacce take da mugun haɗari sannan tana da ƙarfin gaske, aƙalla idan a kayiwa mutum ita zai iya kaiwa sati ɗaya batare daya san inda hankalinsa yake ba, koda kuwa ya farfaɗo ba zai dawo cikin hayyacinsa da wuri ba, sai dai ma shi Sooraj ɗin yaci sa'a jininsa na da ƙarfi sosai, amma duk da haka ƙarfin alluran yayi tasiri acikin jikinsa. Drip suka ɗaura masa sannan suka wuce dashi wani ɗaki na musamman, kasancewar kusan duka likitotin asibitin sun sansa, don yana zuwa lokaci zuwa lokaci yana dubawa koda akwai waƴanda suke da buƙatar taimako shi yakan zuba dukiyarsa ya taimaka musu.

Dr.Haisam wanda yake ɗaya daga cikin manya manyan likitotin asibitin ya kalli Kamalu driver, dawo da kallonsa ya kuma yi ga Ziyada wacce har yanzu kuka take....

"Tare kuke ne?" Dr.Haisam ya tambayi Kamalu yana maiyi masa nuni da gefen da Ziyada'n ke zaune.

"Eh ƙanwar Oga ce" Kamalu driver yafaɗi haka, don ya rasa ma mai zai ce.

Kai Dr.Haisam yajinjina alaman gamsuwa,   kallon Ziyada ya kumayi wanda itama a yanzu kallonsa takeyi.

"Biyoni Office"  yace da ita yana mai nufar hanyar office ɗinsa.

Kallon Kamalu driver Ziyada tayi,  kansa ya jinjina mata alamar ta bi Dr. Haisam ɗin, jiki a sanyaye tabi bayanshi.

Zama Dr.Haisam yayi akan kujera haɗe da yi mata nuni da wata kujera dage aje gabansa yace "Ta zauna"

A ɗaɗare ta zauna akan kujeran tana mai murje ƴan yatsun hanunta.

"Ya Sunanki?" Dr.Haisam ya tambayeta.

Murya araunane tace "ZIYADA"

Kansa yajinjina haɗe da maimaita sunan ZIYADA acikin ransa.

"Ki kwantar da hankalinki Ziyada, ki daina kuka kinji, yayanki zai warke insha Allah, Ina iyayenku suke? don yana da kyau na tattauna matsalan dake damunsa dasu"

Ɗago jajayen idanunta tayi ta kallesa,  murya asanyaye tace.
"Basanan sunyi tafiya!"   ita kanta batasan ya akayi taji ta furta wannan ƙaryan ba, sai dai kuma bata da wani abun da zata ce masa ne wanda ya wuce hakan.

Ajiyar zuciya Dr.Haisam yayi haɗe da cewa.

"Shikenan ba damuwa, amma a wannan yanayin yayanki yana tsananin buƙatar kulawarki, bazance miki zai farfaɗo a yau ko gobe ba, wannan na Allah Ne, amma ki zauna atare dashi ki basa kulawa har zuwa farfaɗowansa,  idan drip ɗin da aka sanya masa ya ƙare kizo ki ƙirani saina cire masa ko"

Kanta kawai ta kaɗa masa alamar    "To"

"Tashi kije"  yace da ita yana mai ƙoƙarin haɗa wasu takardun dake kan table ɗin gabansa.

Tana fitowa Kamalu driver ya tambayeta wai me Dr.Haisam ɗin yace mata.

"Babu"  kawai ta basa amsa ataƙaice, wata Nurse ce tazo garesu, kallon Kamalu driver tayi haɗe da cewa "Oga yace katafi ƙanwartasa sai ta kula dashi"  kai Kamalu driver ya jinjina alaman gansuwa, sannan nurse ɗin ta wuce gaba Ziyada ta rufa mata baya.

Nurse ɗin na nuna mata ɗakin da yake kwance ta juya tayi tafiyarta. Ahankali tatura ƙofar ɗakin ta shiga.

Yana kwance akan gadon asibitin, kansa da jikinsa duk suna fuskantar sama, yayinda idanunsa kuwa suke a rufe ruf, wata na'ura ne mai kamar computer agefensa, yayinda aka saƙala masa wata ƴar waya da tafito daga jikin na'urar a ƙirjinsa.  Wasu hawayene taji sun taru sun cika idanunta, wani irin tausayinsa ne mai ƙarfi ya ɗarsu acikin zuciyarta.

Ahankali ta taka har zuwa jikin gadon, kan kujeran dake kusa da gadonnasa ta zauna, a kusa da inda hanunsa yake ta ƙifa kanta. Kusan 30 minute ta ɗauka tana zaune a wajen, a hankali ta ɗago kanta haɗe da duban ledan ruwan da aka ɗaura masa, gani tayi saura kaɗan ruwan ya ƙare.  Dawo da kallonta tayi zuwa jikinta, kwata kwata ta manta da shigan dake jikinta, baƙar doguwar riga ce ajikinta mai dogon hannu, sai kuma mayafin rigan dake ɗaure akanta, warware mayafin rigan tayi da yake yana da girma ta rufe jikinta dashi, fita daga cikin ɗakin tayi, da ƙyar ta iya gane office ɗin Dr.Haisam, yana zaune tashigo tasanar masa cewa ruwan yakusa ƙarewa..

Cire masa ledan ruwan Dr.Haisam yayi kana ya barsa sai zuwa anjima asake sa wani.

Dr. Haisam na fita daga cikin ɗakin tasoma jin ƙiran sallan Magriba, wanda yake fitowa daga cikin masallacin dake gefen asibitin.

Kallon ƙofar da Dr.Haisam yace mata nanne banɗaki tayi, ahankali tatura ƙofar tashiga, banɗaki ne mai kyau da tsafta, gaban sink taje ta ɗauro alwala sannan ta fito.

Tsayawa tayi tana nazarin yanda za'ayi tayi sallah babu sallaya, duk da cewa rayuwar rashin ƴanci da kuma ƙauyanci tayi, hakan baisa ta zamo mace mai wasa da sallah ba, duk da bawani ilimi take dashi akan addini ba, amma tana kyautata zaton wajen bazaiyi sallah ba idan har ba a shumfuɗa sallaya ba,  kallonsa tayi yananan dai a yanda yake, ahankali ta ƙarasa jikin gadon, aƙalla ta ɗauki sama da 7 minute tana kallonsa, jitayi duk ƙwalla suncika idanunta,  buɗe ƙofar ɗakin tayi ta fice.  Tana fita daga ɗakin taga wata nurse zata wuce, da sauri ta ƙarasa gareta haɗe da gaisheta.

Amsa mata gaisuwar nurse ɗin tayi tana mai ƙare mata kallo.

"dama Sallah zanyi shine kuma banda sallaya ko zaki ɗan aramin" Ziyada ta tambayi nurse ɗin tana mai sanya mata fuskar tausayi.

"Biyoni muje ki amsa" nurse ɗin tafaɗi haka tana mai ci gaba da tafiyarta.   Sallaya hadda Hijab nurse ɗin ta bata, ta kumace ta riƙe a wajenta zuwa gobe,  godia Ziyada tayi mata sannan tadawo ɗaki, shumfuɗa sallayan tayi  haɗe da tada Sallah.   Sosai ta jima a sujjadanta na raka'an ƙarshe, addu'a tayi sosai akan Allah yabawa Mai taimakonta lafiya.   "Mai Taimako" shine sunan da Ziyada ta raɗawa Sooraj acikin zuciyarta.  Tananan zaune akan sallayan har aka ƙira sallan Isha..   Shima a sujjadan ƙarshe saida tajima tana addu'a kafun ta ɗago.  Shiru haka ta zauna akan sallayan haɗe da jingina bayanta ajikin bango.  Har ƙarfe 9 Ziyada na zaune agefen gadon,  sannu ahankali yunwa ke ƙwaƙulan cikinta,  gyan gyaɗi ta fara mintuna kaɗan bacci ya ɗauketa.  Cikin dare     Sanyin AC ya dameta, tashi tayi ta lulluɓe jikinta sannan ta koma bacci.

Washe Gari.

Tunda ta tashi da asuba tayi sallah, wani bacci yasake ɗaukanta, ba ita ta farka ba sai wajen ƙarfe 8 na safiya. Ban ɗaki ta wuce taje  ta wanko fuskarta, tana zama akan kujera Dr.Haisam ya turo ƙofar ɗakin ya shigo, gaishesa tayi cike da girmamaw,   fuskarsa ɗauke da murmushi ya amsa mata.

Checking ɗin Sooraj ya sakeyi, yaji daɗin ganin komai Normal kuma zai iya farfaɗowa ako wani lokaci.

Hannayenta ta ɗaura akan kumatun ta haɗe da kafesa da manyan manyan idanunta, kyakkyawar fuskarsa take kallo, babu wani abu dayafi saurin ɗaukar hankali akan fuskarsa kamar yalwataccen sajen sa, wanda yake baƙi siɗik, ga zara zaran eye lashes ɗinsa da suke a mimmiƙe, sosai suka ƙarawa fuskartasa kyau, hakan yasa bata taɓa gajiyawa da kallonsa...

Wasa Wasa har ƙarfe 5 na yamma Sooraj bai farfaɗo ba, haka Ziyada ke zaune awajensa, batare da ta ci wani abu wai sunansa abinci ba, ruwa kawai take ta zubawa cikinta.  Tun yunwar na damunta har tazo ta daina ji, yanzu bata da wani buri daya wuce taga Mai Taimakonta ya buɗe idanunsa.

9:30 pm  Babbar yatsan ƙafarsa ta dama ne ta soma motsawa  sai kuma yatsun hanunsa, sannu sannu bugun zuciyarsa ta dai dai ta, yayinda cikin sakannin da basu wuce huɗu ba brain ɗinsa ta soma aikin.

Ahankali ya soma buɗe idanunsa,  da kaɗan kaɗan yake ware idanun nasa hakan yasa ya soma ganin komai dishi dishi. Sannu ahankali idanun nasa suka washe, kallon saman ɗakin daya gansa aciki ya soma yi.  Sake ɗan lumshe idanunsa yayi, komai daya faru ya dawo cikin kansa,  ɗan yunƙurawa yayi ya tashi zaune haɗe da jingina bayansa da pillow,    juyo da kansa yayi zuwa gefen damansa,  idanunsa suka sauƙa akanta, tana zaune akan sallaya ta jingina bayanta da kanta a  jikin gadon da yake, bacci takeyi cikin yanayi na takura, da dukkan alamu bata shiryawa baccin ba ya ɗauketa, domin kuwa hadda goran ruwa riƙe ahanunta, ƙurawa

fuskarta idanu yayi,  hango wasu  zanen busassun  hawaye  yayi  kwance akan fuskarta, kallon yanda ɗan ƙaramin bakinta ke ɗan buɗe yayi.  Janye idanunsa yayi daga kanta, haɗe da ɗan tattaro ragowan ƙarfin daya rage masa ya sauƙo daga kan gadon.

Ƙofar da yake tunanin nanne toilet ya nufa, yana shiga ya soma rage kayan jikinsa.  Kunna shower yayi ya tsaya ruwa ya dake shi sosai.   Dogon wandonsa kawai ya maida batare da ya sanya rigar shi ba ya fito daga cikin toilet ɗin.

Zama yayi abakin gadon haɗe da sanya hanu ya dafe kanshi dake yi masa ciwo sosai, hakanan yakejin shi  wani iri,  gaba ɗaya babu wani isashshen kuzari ajikinsa, yasan hakan kuma duk yana daga cikin sharrin Alluran da yayiwa kan shi ne.

Kallon shi  ya kuma maidawa zuwa gareta, har yanzu tananan tana wahalallen baccin daya ɗauketa,  gaba ɗaya jikinta a tukuikuye yake da Hijab,  tashi yayi ya ƙarasa jikin window'n ɗakin, hanu yasa yaɗan buɗe labulen window'n kaɗan, gani yayi gaba ɗaya duhu ya mamaye sararin samaniya,  hanu yakai yashafi aljihun wandon dake jikin shi,  atunanin shi wayar shi na tare da shi.  sai dai kuma saɓanin haka yaji shi  wayam, ɗan kalle kalle yasomayi acikin ɗakin ko zai hangota amma baiganta ba,  komawa yayi ya zauna akan gadon yana mai lumshe idanunsa, saboda wani juwa da yaji yana neman ka da shi.   Aƙalla yakusan mintuna goma idanunshi suna  lumshe, jin da yayi juwan yasoma lafawa ne yasanya ya tashi tsaye, inda take zaune ya nufa, tsayawa yayi akanta ya kasa ta ɓuka komai.  Ɗan ranƙwafowa yayi ya ɗagota caɗak,  kan gadon da aka ajiye musamman don taya majinyaci kwana ya ɗaurata,   a hankali ya zare hijab ɗin dake jikinta ya ajiye mata shi agefe.  Ziyada da baccinta yayi nisa sam batasan meke faruwa ba, saima ƙara gyara kwanciarta  da tayi, sakamakon jin ta samu sauyin makwanci.     Komawa kan nashi gadon yayi ya kwanta,  lumshe idanunsa yayi bawai kuma don yanajin bacci ba saidan kawai babu wadataccen ƙarfi ajikinshi..

Yatsun ƙafanta ya ƙurawa ido, azahirin gaskiya yatsunnata yake kallo, amma kuma hankali da tunaninsa ba agareta suke ba, yayi nisa acikin wani tunanin daban, baiso ace ya biyewa zuciyarsa ba, baiso ace ya kasa haƙurin ɗaukar ƙaddaransa ba,  duk da cewa shiɗin mai raunine amma yana fatan dacewa anan gaba, saidai aduk sanda yayi wannan tunanin sai wata zuciyar ta gargaɗesa da kada ya yaudari kansa, dolensa haka yake haƙura  ya watsar da tunnin acikin ransa.

Buɗe gajiyayyun idanunta tayi, ganin haske tarwal acikin ɗakin yasa ta tashi aɗan zabure, kallonta takai wajen window gani tayi har hasken rana yasoma bayyana ta jikin window'n.  Da sauri ta zuro ƙafafunta daga kan gadon,   dai dai lokacinne kuma idanunta suka sauƙa akansa, yana kwance ya bata baya.

Sake waro idanunta tayi haɗe da mutsutstsukasu  atunaninta ko gigin bacci takeyi ganinsa da tayi babu riga, bayan koda zata kwanta tabarshine sanye da riga ajikinsa.        "Kodai likita ne yazo ya cire masa riga'n tana bacci bata sani ba?" tambayar da tayiwa kanta kenan.

Ahankali ta sauƙo daga kan gadon, cikin sanɗa tataka harzuwa inda yake kwance.

Kanta ta ɗaura ajin gadonnasa, lokaci guda idanunta suka kawo hawaye murya araunane tace.

"Mai Taimakona Allah yabaka lafiya, tausayinka nakeji sosai, banso wani abu ya sameka!" taƙare maganar daidai lokacin da hawayen dake cikin idanunta suka samu daman gangaro zuwa kan fuskarta,  daidai lokacinne kuma shima da tun tashinta zuwa yanzu yanajin abun da takeyi ya ɗan buɗe idanunsa kaɗan....

*Vote Me On Wattpad*
@fatymasardauna
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

#romance

*Chapter 13*

Wani numfashi mai ɗumi ya fesar daga bakinsa, haɗe da maida idanunsa ya rufe,  kalamanta ne suka shiga yi masa yawo acikin kunnuwansa, ji yayi tsikar jikinsa na tashi, hakanne ma yasa ya kasa yin koda kyakkyawan motsi ne.

Ban ɗaki ta wuce ta je ta ɗauro alwala, sam bata san ya akayi bacci ya ɗauketa ba, taso ace bata makara ba, kasancewar yanzu har hasken rana ya bayyana.   Tana idar da sallan ta gyara zamanta akan sallayan,  sai alokacinne ta tuno da cewa aƙasa ta kwanta ba akan gado ba,  "To kenan ya akayi ta koma kan gado?" tambayar da tayiwa kanta kenan, ƙaran buɗe ƙofar ɗakin da akayi ne ya katse mata tunaninta.   Dr.Haisam ne yashigo cikin ɗakin bakinsa ɗauke da sallama, amsa masa tayi haɗe da gaidashi.  Fuska asake shima ya amsa mata gaisuwar. Ƙarasawa gaban gadon da Sooraj ɗin ke kwance yayi.    "Ya jikinna ka dai?" Dr.Haisam ya tambayi Sooraj wanda har yanzu bai sauya kwancia daga juya bayan da yayi ba.

Ziyada nashirin ce da Dr.Haisam bai farfaɗo ba, taji muryarsa ta doki dodon kunnenta.

"Da sauƙi!" Sooraj ya bashi amsa ataƙaice, sai alokacin ya juyo ya fuskanci Dr.Haisam ɗin.

"Masha Allah dama kullum haka mukeso, yanzu babu wani inda yake maka ciwo?" Dr.Haisam yatambayeshi cike da kulawa.

"Babu" ya bashi amsa ataƙaice.

"Masha Allah zamu baka sallama zuwa anjima, amma yana da kyau ka riƙa kulawa da lafiyarka, kasan fa lafiya itace komai arayuwa, sai da itane mutum yake sanin daɗin rayuwa, saboda haka kakiyaye abun da zai cutar dakai!"

Kai kawai Sooraj ya jinjina alamar yaji, sam baison magana mai tsawo.

Kallon Ziyada dake zaune tana kallonsu Dr.Haisam yayi. Fuskarsa ɗauke da murmushi yace. "Congrat ƴar ƙaramar ƙanwa, da alama brother ɗinki ya samu lafiya"

Murmushin daya bayyana kyawun fuskarta tayi haɗe da sunkuyar da kanta ƙasa, hakanan taji wani irin sanyi acikin ƙirjinta. Dr.Haisam na fita ta ɗago da kanta takai dubanta ga Sooraj wanda yake ta murza fatan hanunsa, kallon yanda jijiyoyin jikinsa suka fito sukayi raɗa raɗa tayi, gani tayi ya sanya haƙoransa ya danne lip ɗinsa na ƙasa, tamkar wani wanda yakejin wata azaba ta daban, tashi tayi daga kan sallayan cikin sanɗa tashiga takowa zuwa inda yake.

Muryarta na rawa tace "YAH...YAH!!" ita kanta batasan ya akayi ta ƙirasa da wannan sunan ba.

Cak ya tsaya daga murza hanunnasa da ya keyi haɗe da buɗe idanunsa da suka zama jajur dasu, ɗago da kansa yayi ya kalleta.

Sai da taji gabanta ya faɗi alokacin da idanunsa suka sauƙa acikin nata idanun, bakomai ya tsorata ta ba kamar yanda taga idanunsa sun rikiɗe daga farare zuwa jajaye.

Ko second biyu bai ɗauka ya na kallonta ba ya sauƙe idanunsa ƙasa.

Ƙwalla ne suka cika idanunta, murya araunane tace "Dama.... dama.. Bansani ba ne ko kanajin yunwa" tafaɗi haka tana mai murza ƴan yatsun hanunta.

"Miƙomin rigana" yafaɗi haka batare daya ɗago kansa ko ya tanka mata maganan da takeyi ba, babu musu ta ɗauko rigan nasa tazo ta miƙa masa, tashi tsaye yayi daga kan gadon haɗe da sanya rigarsa, Kallon ƙafansa ƴayi yaga ko takalmi baida shi. Hanu yasa ya dafe goshinsa.

"Ina wayata?"
yayi mata tambayar yana mai tsareta da idanunsa.

"Wayanka?" tafaɗa tana mai rarraba idanunta.

Yanayin yanda tayi maganar ne yasashi ƙanƙance idanunsa haɗe da ware su alokaci guda.

"Wa ya kowani nan?" ya tambayeta yana mai ƙoƙarin maƙala aninayen dake gaban rigarsa.

"Ni da Kamalu driver ne" tabashi amsa tana mai wasa da yan yatsun hanunta.

Ɗauke kansa kawai yayi daga kallonta, dai dai lokacin Dr.Haisam yashigo cikin ɗakin.

Sooraj na ganinsa yace "Ko zan iya samun aron waya?"

Murmushi Dr.Haisam yayi haɗe da cewa "Eh" ciro wayarsa yayi ya miƙawa Sooraj ɗin.

Number'n Khalid yasanya acikin wayan Dr.Haisam haɗe dayin dialing. Ringing biyu Khalid yaɗauki ƙiran, "Ina Mahfuz Specialist Hospital, kazo kayi dropping ɗina a gida" Baijira mai Khalid ɗin zaice ba ya kashe wayan, miƙawa Dr.Haisam wayar yayi. Takardan sallamansa Dr.Haisam ya miƙa masa.

Mintuna kaɗan Khalid ya iso cikin asibitin. Yana shigowa ɗakin, cikin tashin hankali ya kalli Sooraj cike da kulawa yace "Raj maiyasa meka haka, harda zuwa asibiti?"

Murmushin gefen baki Sooraj yayi haɗe da cewa " stress ne kawai, muje ko" yaƙare maganar cikin yanayi na ƙosawa.

Motar Khalid suka shiga, suna zaune agaba ita kuma tana zaune agidan baya, Khalid ne ke ta tambayar Sooraj jikin nasa cike da kulawa, amma kuma shi Sooraj ɗin cikin halin ƙosawa yake mayar masa da amsa.

Suna isowa gida Khaleed yayi musu sallama ya koma, dama aiki yabari a office ɗinsa ya zo.

Wanka yayi haɗe dayin brush sai alokacin yaji wani ɗan iskan yunwa na ƙwaƙulan cikinsa, dogon wando yasanya da wata riga marar nauyi, kana ya zura slippers ɗinsa ya fita zuwa falo.

Direct kitchine ya wuce, ruwan zafi ya tafasa haɗe da juyewa acikin flask. Cup ya ɗauka ya haɗa tea, hannayensa ya sanya akan waist ɗinsa, yana ƙarewa kitchine ɗin kallo. itace ta faɗo masa arai, yasan gaba ɗaya zaman yunwa tayi acikin a asibitin.

Ruwan zafi ya ɗaura akan gas, mintuna ƙalilan ruwan ya tafasa indomie ya jefa acikin ruwan haɗe da sanya spiece. yana tsaye acikin kitchine ɗin, har Indomie ɗin ya nuna, acikin wani plate na tangaran mai kyau ya juye indomie'n. hanunsa riƙe da plate da kuma cup ɗin tea ɗin ya fita zuwa falo.

Zaune  take akan gado, tayi jigum fitowanta daga wanka kenan, ta sanya wani riga da sket ƴan kanti.  Zuwa yanzu idanunta har sun soma rufewa sbd yunwa, gaba ɗaya ƙarfin jikinta ya gudu, duk da zama da yunwa ba sabon abu bane a wajenta..
 Wani irin murɗawa taji cikinta nayi.   Hanu yasa ajikin ƙofar ya ƙwanƙwasa, batare daya jira anbuɗe ƙofar ba ya juya ya koma cikin falon. Zama yayi akan kujera haɗe da ɗaukan cup ɗin tea ɗinsa ya soma sipping da kaɗan kaɗan.

Cikin rashin ƙarfi ta buɗe ƙofar ɗakin ta fito, ganinsa zaune a falon yasa ta nufo cikin falon.

Durƙusawa tayi agabansa, kafun tace wani abu, ya turo mata plate ɗin imdomie ɗin gabanta.

Ɗago da kanta tayi ta kallesa, gani tayi kwata kwata idanunsa ba'akanta suke ba.  Ɗaukan plate ɗin tayi ta ɗaura akan cinyarta, loman farko da tayi ta lumshe idanunta, wanda suke cike da gajiya da kuma bacci,  sosai takecin indomie'n harta manta ma da cewa agabansa take.
Duk abun da takeyi yana lure da ita, duk wani motsin da tayi yana kallonta ta gefen idanunsa.
Bata gama cin indomie'n  ba har ya kammala shan tea ɗinsa yatashi yabar wajen, tana kammala cin indomie ɗin taji wata nutsuwa ta sauƙar mata, ɗaki ta koma tana kwanciya bacci yaɗauketa.

*** *** ***

Tun tashinta yau ta riga da ta gyara ɗakin da take kwana tsab, hakanan taji sha'awar shiga kitchine ɗin gidan, gani take kamar wahala take bashi don kullum saiya saya mata abun da zata ci, duk da cewa baya wuni agidan amma yana turowa ana kawo mata. Yanzu rabonma da ta sanya shi acikin idanunta kusan kwana biyu kenan.

Tsayawa tayi a kitchine ɗin tana ƙarewa ko ina da ina kallo, ita sam bata wani iya girkin zamani ba, shinƙafa kawai ta iya dafawa,   wata drawer dake cikin kitchine  ɗin ta buɗe, kayan abinci ta gani shaƙe acikin drawer'n,   ruwa ta ɗaura akan gas, wanda da ƙyar ta iya kunnasa, saura ma kaɗan wuta ya kama hanunta.   neman inda zata samu kayan miya tashiga yi, saidai neman duniya tayi bataga wani abu mai kama da kayan miya a kitchine ɗin ba, dolenta haka ta kashe gas ɗin ta fito daga kitchine ɗin.

Fitowarta yayi daidai da shigowarsa cikin falon. Sanye yake da suit coffee colour, ya yinda ƴar cikin rigan ta kasance milk colour, Sosai yayi kyau. Har batasan sanda tasake baki tana kallonsa ba.

Kallonta yayi tare da kawar da kansa gefe.  "Ɗauko mayafinki" yace da ita ataƙaice.

Babu musu ta koma ɗaki ta ɗauko mayafinta.

Tafiya suke kowannensu da abun dayake saƙawa acikin zuciyarsa.  Gaban wani tangamemen

gate taga sun tsaya yayinda yasoma danna horn ɗin motar. Wangale musu gate ɗin akayi ya tura hancin motar ciki.      adai dai wani ƙaton parking space ya yi parking motar.    "Muje" yafaɗa yana mai ƙoƙarin buɗe murfin motar,  yana gaba tana biye dashi abaya, gaba ɗaya hankalinta naga tsirarun mutanen da tagani suna shawagi a tafkeken farfajiyan wajen, daga mata har mazan dake wajen sanye suke da uniform maroon and milk colour.     Direct office ɗin Mr. Isyaka Nuhu suka nufa, har cikin office ɗin akayi musu iso.   Cike da mutuntawa Sooraj yabawa  Mr. Isyaka Nuhu hanu suka gaisa.  Fuska cike da fari'a Mr.Isyaka Nuhu ya dubi  Ziyada haɗe da dawo da kallonsa ga Sooraj.   "Wannan itace yarinyar?" Ya tambaya.

"Eh" Sooraj yabasa amsa.

Wayarsa ya ɗauka haɗe da danna ƙiran wata number,  yanajin an ɗaga ƙiran yace "Kasameni a office ɗina" yana aje wayar bawani jimawa saiga wani mutumi yashigo cikin office ɗin.

Kallonsa Mr.Isyaka Nuhu yayi haɗe da cewa.

"Kuje da yarinyarnan kayi mata interview"

"Okay Sir!" mutumin daya shigo ya faɗi haka haɗe da kallon Ziyada yace "Muje ko"

Kallon Sooraj tayi saidai kuma taga sam idanunsa ba akanta yake ba, wayarsace ma ahanunsa yana dannawa..

(manage)

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written by*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

#romance

*Chapter 14*

Basu wani jima ba suka fito daga ɗakin da akeyiwa duk wani ɗalibi da yakasance sabon zuwa interview.  Direct office ɗin principal ɗin suka koma zuciyar Ziyada cike take da farinciki da kuma jin daɗi, addu'anta ɗaya Allah yasa hasashen da takeyi yazamanto gaskia.

"Har kun gama interview ɗin?" Mr. Isyaka Nuhu ya tambayi Sir. Yusuf wanda shine ke yiwa duk wani sabon ɗalibi dazai shigo makarantar interview.

"A'a Sir ai ma bata taɓa zuwa makaranta ba, inaga kawai sai dai afarayi mata lesson" Sir.Yusuf yafaɗi haka cikin siga irinta bada shawara.

Jinjina kai Mr. Isyaka Nuhu yayi haɗe da dawo da kallonsa ga Sooraj wanda har yanzu wayarsace riƙe ahanunsa yana latsawa.

"To kaji abun da yace, ya kagani ko za'a fara yi mata lesson ɗin, idan ta ɗan soma iya wasu abubuwan sai abata ko s.s.one ne"

Sai alokacin ya ɗago kansa, wannan murmushin nasa da baya wuce kan laɓɓansa yayi haɗe da cewa.
"Bakomai hakan yayi, yaushe za'a fara lesson ɗin?"

"Ai tunda kusan munkammala komai ko yau ma idan kun shirya sai afara yi mata" Inji cewar Mr. Isyaka Nubu (Principal).

"Okay ba damuwa, ni zan wuce"  Sooraj yafaɗi haka yana me miƙewa tsaye, hanu yabawa Principal ɗin sukayi musabaha, kana yabawa Sir. Yusuf ma suka gaisa,  ko kallon gefen da take baiyiba ya fice daga cikin office ɗin.

Principal ne yace da Sir.Yusuf  suje ya samo mata malamin lesson su fara tun yau, hakan kuwa akayi,   Wani Teacher Abdallah Sir.Yusuf ya samo mata, wanda shine zaina koyar da ita lesson everyday, hatta ranan saturday da sunday zai na zuwa koya mata gida, domin biyanshi za'ana yi.

abubuwa masu sauƙi Teacher Abdallah yafara koya mata, sam babu wani abu da ta fahimta tana dai jinsane kawai, duk kuwa yanda taso ta fahimci abubuwan sam ƙwaƙwalwarta takasa ɗauka.
***
Zaune yake atamfatsetsen office ɗinsa, dagashi sai dogon wandon suit da kuma rigan parking shirt dake sanye ajikinsa, laptop ɗinsa ne agabansa yana shigar da wasu bayanai gaba ɗaya hankalinsa nakan laptop ɗin, turo ƙofar office ɗin akayi tare da shigowa, yaji motsin buɗe ƙofar amma sam baiɗago kansa ya kalli wanene ya shigo cikin office ɗin ba, yau sosai ƴan miskilancin nasa suke kusa.

Jingina bayanta tayi da jikin ƙofar tana kallonsa, wani irin murmushine ya bayyana akan fuskarta, kallonsa kaɗai idan tayi yakan sanya mata nutsuwa, sosai take jin son sa acikin ranta, komai nasa yana burgeta tana son duk wani abu nasa, musamman yanayin yanda yakeyin adonsa, uwa uba kuma kyau da kwarjininsa dake tafiya da imanin duk wata mace da zatayi tozali dashi,  cikin takunta nason ɗaukar hankalinsa tasoma takowa zuwa cikin office ɗin. Ƙaran takalman dake ƙafanta shiya fara sanar dashi wacce ta shigo cikin office ɗin nasa,  jiyayi wani abu ya toshe masa maƙoshi,  sam yatsani ganinta ko kaɗan bayaso tana raɓarsa, baisan ita wace irin mace bace wacce bata da zuciya ko kaɗan.    Harta ƙaraso gaf da inda yake bai ɗago dakansa ya kalleta ba,  cikin muryar shagwaɓa tace.

"Barka da hutawa ranka ya daɗe"

Kamar ma baisan da mutum a wajenba haka yayi banza da ita,  bakinta da yaji pink lips stick taturo gaba.   "Maiyasa kakemin hakane wai Raj? at least dai ko kallona yakamata ace kayi wajenka fa nazo" taƙare maganar tana ɗan bubbuga ƙafafunta, alaman shagwaɓa.

Sai alokacin Sooraj ya ya ɗago kansa, saidai bai kalli inda take ba.    "Kina da buƙatar wani abu ne?" yatambayeta ata ƙaice.

"Kainake da buƙata Raj, wallahi kainake da buƙata, kafi kowa sanin yanda na damu dakai, maiyasa kake min haka ne? kadubeni Raj nacika mace irin wanda take girgiza zuciyoyin maza amma maiyasa bazaka dubeni ba? na amince ma kayi duk wani abun da kakeso dani amma maiyasa bazaka amince min ba!" taƙare maganar kamar zatayi kuka.

Murmushin gefen baki Sooraj yayi haɗe da tashi ya ƙarasa gaban fridge, buɗewa yayi ya ɗauko ruwa mai sanyi, saida yasha sosai kafun  ya sauƙe goran ƙasa,  inda suit ɗinsa ke aje ya nufa, ɗaukan suit ɗin yayi ya saƙala ahanunsa,  touch watch ɗin dake hanunsa ya duba,  gani yayi akwai sauran time sosai kafun lokacin tashinsa ya cika, amma a yanda  Aneesa tashigo masa office baya jin zai ƙara mintuna biyu acikin office ɗin.

Wayarsa ya ɗauka haɗe da rufe laptop ɗinsa,   juyawa yayi ya nufi ƙofar fita yana mai karkaɗa key ɗin motarsa dake riƙe a hanunsa.

Da sauri Aneesa tasha gabansa, idanunta cike da ƙwalla tace "Please Raj ka tsaya atare dani, kasani kaine burina da kuma fatana, maiyasa kakemin haka ne?"   hawayene suka gangaro daga cikin idanunta.

Sai alokacin Sooraj ya ɗaura idanunsa akanta, kallonta yayi tun daga samanta har zuwa ƙasa. sannan yasaki wani killer smile.

"Bani hanya na wuce"  ya faɗa mata haka cikin halin ko inkula.

"Bazan baka hanya ba Raj, harsai kamin abinda nakeso, please Raj kasani akullum da

buƙatarka nake kwana, please kabani dama ko sau ɗaya ne."

Ƙanƙance idanunsa yayi haɗe da tamke fuskarsa alokaci guda, cikin takaici yasanya hanunsa ya turata gefe, harsai da kanta ya bugu da bango, ƙofar office ɗin ya buɗe ya fice abunsa.

Kuka Aneesa tasanya mai ɗauke da tsananin ɓakin ciki da takaici,  takardun dake kan table ɗin office ɗin ta soma watsarwa a ƙasa tana kuka, ta tsani wannan banzan halin na Sooraj,  a kullum baida wani buri da ya wuce ya wulaƙantata, mai tarasa wanda har zai tsaneta haka? alƙawari tayiwa kanta matuƙar ta rasa Sooraj to kowacce mace aduniya ma tarasashi domin bazata taɓa ɓari ya auri wata mace ba idan ba ita ba.

Yana fita ya wuce wajen da yayi parking motarsa, sama sama yake amsa gaisuwar  ma'aikatan dake gaidasa.  Yana shiga cikin motar yayi mata key haɗe da ficewa daga cikin bank ɗin, direct wani hotel ya nufa......

Sosai Teacher Abdallah ya dage ya zuba mata lesson,  lokacin da aka kaɗa ƙararrawan tashi ga duka ƴan makarantan dai dai lokacin shima ya dakata daga koyar da ita english lesson ɗin da ya keyi.    Tana fitowa ƙofar ajin taga cincirondon ɗalibai maza da mata kowa na ƙoƙarin kama gabansa, ko ta ina acikin makarantar ɗalibaine, yayinda parking space ɗin makarantar kuwa ke cike da tarin motoci, har waje motoci ne a fake, duk wani ɗan makarantan dazaka kalla, kallo ɗaya zakayi masa ka hango alamun zaman naira ajikinsa, domin daga mata har mazan gaba ɗayansu ƴan gayu ne, da alama kuma kowa yanaji da kansa.

Kamalu driver ta hango ya nufo inda take, wata ajiyar zuciya ta sauƙe, domin kuwa da har tafara tunanin yanda za ayi ta koma gida ita kaɗai.

Gaba ɗaya yau tsananin farincikinta ya kasa ɓoyuwa, jinta take cikin farinciki. Haka ta koma gida zuciarta cike da jin daɗi.  Wunin ranan gaba ɗaya haka tayishi cikin jin daɗi, duk yanda taso ganinsa tayi masa godiya abun yaci tura, domin kuwa ko motsinsa bata jiba

*** *** ***

Kullum sai Ziyada taje Lesson Kamalu driver ne ke kaita shine kuma ke dawo da ita, sosai ta kejin daɗin lesson ɗin nata, yanayin yanda ta dage tasanya son karatun acikin ranta shi ya ƙara sanya teacher Abdallah dagewa wajen ganin ya koyar da ita yanda zata fahimta,  zuwa yanzu dai tana ɗan fahimtan abubuwa da kaɗan kaɗan, musamman ma wajen karatun Hausa da kuma rubuta shi,  ta ɗan ƙware ta wajen wannan fanni, har ma idan taga abu zata iya karantashi, English ɗinne dai sai a hankali.

Tun ɗazu aka tashe su saidai ga mamakinta yau Kamalu driver baizo ɗaukanta ba, gashi ɗaliban da suka rage acikin makarantar basu wuce ƴan tsiraru ba sam basu da wani yawa. Kalle kalle take tayi ko zata hango Kamalu driver amma babu shi babu alamarsa.  Tsaye take a harabar makarantar, sanye take da doguwar riga da kuma Hijab, hannayenta nannaɗe suke

akan ƙirjinta.

Tun daga nesa yayi parking ɗin motar, jingina bayansa yayi da jikin kujeran motar haɗe da lumshe idanunsa, ahankali ya ware idanunsa haɗe da sauƙesu akanta, hakanan ya tsinci kansa da tsaida idanunsa akanta, kusan 2 minute ya ɗauka yana kallonta, mai da idanunsa yayi ya rufe, wani irin gajiya haɗe da kasala ne yaji sun sauƙar masa alokaci guda. Buɗe murfin motar yayi haɗe da zuro ƙafafunsa waje. Tun fitowarsa daga cikin motar idanun ɗaliban da ke wajen ya dawo kansa. Yanayin yanda yake taku cike da nutsuwa shine abun daya burgeta, har batasan sanda ta saki wani murmushi ba. Yana ƙarasowa inda take yace.

"Kijirani a mota" baijirayi mai zata ce ba, yayi gaba abunsa, tana kallonsa ya shige cikin office ɗin principal. Juyawa ita tayi ta nufi inda ya aje motar tasa, jingina tayi da jikin motar tana jiran zuwansa. Baiwani jima ba ya dawo hanunsa riƙe da wata leda.

Tunda suka ɗauki hanya babu wanda yace da ɗan uwansa wani abu kowa da irin tunanin da yake saƙawa acikin zuciyarsa, yarda da abun da zuciarta ke gaya mata da tayi yasanya ta gyara zama cikin wata murya mai sanyi tace. "Nagode Yaya"

Bai kalli inda take ba, bai kuma tanka mata ba, jin yayi shiru bai ce da ita komai ba yasa taji jikinta yayi sanyi. Saidai kuma kamar daga sama ta tsinkayi muryarsa. .

"Waye yayan naki?" yafaɗa cikin tsare gida, batare daya kula sashin da take ba.

Jin tambayar nasa yasa ta ɗago da kanta ta kallesa, tsintar kanta tayi da kasa ɗauke idanunta akansa, musamman ma data ga hankali da idanunshi ba akanta suke ba.

"Kallon kuma fa?" yafaɗa adaidai sanda yake shiga wata kwana, da zata sadasu da gida.

Da sauri ta janye idanunta daga kan nasa azuciyarta tanajin wani iri.....

Monday.

Yau ne zata fara shiga Class itama tayi karatu kamar yadda ko wanni ɗalibi keyi. Fitowarta daga wanka kenan. Ledan daya bata jiya da dare ta ɗauko, kayan shafa ne aciki sai kuma uniform da takalman makarantar ta. gefe kuwa wasu biscuit ne manya manya.

Sama sama ta shafa mai ajikinta, babu powder bare wata uwa kwalli haka tabar fuskarta, uniform ɗinta wanda suke riga da wando ta sanya, wandon irin mai tsukakken ƙafannan ne amma ba har canba, yayinda tsawon rigan ta kasance har zuwa guiwarta, rigan milk colour ce, wandon kuwa shike da kalan maroon. Warware hijab ɗin makarantar tayi tana ƙare masa kallo, bashi da wani girma da kaɗan tsawonsa ya wuce cikinta. Tana sanya hijabin taje gaban makeken mirror'n dake ɗakin ta tsaya tana mai kallon kanta aciki, duk da cewa uniform ne

amma sosai tayi kyau, white skin ɗinta yasake fitowa acikin maroon colour hijab ɗin,   jinta tayi awani ta kure, sam batajin zata iya sakewa acikin mutane da irin wannan shigartata,  sam bata saba ba,hakan yasa take ganinta wata daban.  Zama tayi akan gado haɗe da ɗaukan safanta ta sanya, tana kammala sa safa ta zura takalminta me kama da toms, sosai takalmin yayi mata kyau gashi milk colour kalan riganta.     Tunowa da maganan teacher Abdallah tayi inda yake ce mata "tazo da wuri kada ta sake ta makara"  tashi tayi da sauri tafice daga cikin ɗakin.

Tana fitowa falo daddaɗan ƙamshin turarensa da daɗinsa ke sanya taji wani bacci ya daki hancinta, hakan ya tabbatar mata da cewa bai jima da fita daga falon ba.  Da saurinta itama ta fita daga cikin falon, tana fita ta hango ficewar motarsa daga gidan.  Ajiyar zuciya ta sauƙe haɗe da nufan inda Kamalu ke tsaye, ba wani ɓata lokaci ta shiga suka ɗauki hanyar makarantar...

Suna zuwa direct office ɗin teacher Abdallah ta nufa, don dama anan yace ta sameshi.

Teacher Abdallah yana ganinta yasaki murmushi..
 "Student!" yace da ita yana mai faɗaɗa fari'arsa. Murmushi kawai tayi masa haɗe dayin ƙasa da kanta. Yana kammala abubuwan da yakeyi ya ce suje ya nuna mata ajin da zata zauna, yana gaba tana biye dashi a baya.

S.S 1 A  shine abun da aka rubuta asaman ajin daɗan manyan baƙi,   ɗalibaine  wayanda aƙalla zasu kai su 25 acikin ajin maza da mata, wasu suna zazzaune, yayinda wasu kuwa ke tsaye, wasu kamma akan desk suke zaune,   suna ganin shigowar Teacher Abdallah ko wanne daga cikinsu ya shiga cikin nutsuwarsa, cike da girmamawa suka tashi  tsaye dukansu suka gaidashi, amsa musu yayi haɗe da basu izinin zama.    Gyara tsayuwarsa yayi haɗe da  cewa

"Ga sabuwar ɗaliba nan nakawo muku, ina fata zaku karɓeta hanu bibbiyu, sannan idan bata gane abuba, inaso kuyi mata ƙarin haske" cikin harshen turanci yake maganan.   Kallon Ziyada dake tsaye tama kasa ɗago kai ta kalli mutanen ajin yayi.

"Ga wajen zamanki nan daga yau" yafaɗi haka yana maiyi mata nuni da wata kujera wacce take tsakiyan wasu ƴan mata...

(Kuɗan ƙara haƙuri show ɗin yana gaba.)

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*
{United we stand and succeed our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}
*https://ww.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

#romance

*Chapter 15*

Cikin sanyinta ta nufi inda teacher Abdallah ya nuna mata. Ɗaya daga cikin ƴan matanne ta bita da wani irin kallo. teacher Abdallah yana ganin ta zauna ya fice daga cikin class ɗin bayan ya bata jakar makarantarta mai kyau.

Gaba ɗaya jinta take atakure, kasancewar kusan gaba ɗaya rabin ƴan ajin idanunsu na kanta.

"Sannu!" matashiyar budurwan dake gefenta ta faɗa, wacce aƙalla bazata wuce sa'an Ziyada'n ba.

Sai alokacin Ziyada ta ɗago da kanta ta kalli wacce tayi mata maganan. murmushi tayi mata haɗe da cewa "Yauwa!"

Murmushi itama yarinyar tayi tare da sake cewa.
"Sunana Nasmah, kefa?"

"Sunana Ziyada" Ziyada ta bata amsa tana mai ɗan faɗaɗa fari'an dake kan fuskarta.

"Nice name!" Nasmah tafaɗa tana mai ɗaukan wani text book dake gabanta.

Ɗan satan kallonta Ziyada tayi haɗe da yin murmushi, duk da cewa bata fahimci me Nasmah'n take nufi ba.

Shiru Ziyada tayi bata sake cewa komai ba, yayinda suma ƴan matan sukayi shiru, Nasmah gaba ɗaya hankalinta nakan littafin dake hanunta, yayinda wacce ke gefen Ziyada ta ɓangaren damanta kuwa ko ƙala bata ce ba, sai dai time to time tana yawan kallon Ziyadan, maganane abakinta amma saboda halin jin kai irin na Shukhra ta kasa cewa komai.

Wani malami ne ya shigo cikin ajin, dukansu ɗaliban suka tashi tsaye haɗe da gaidashi, sai da ya ɗan yi rubutu kaɗan akan white board ɗin da ke cikin ajin sannan ya basu izinin zama.

Darasin Maths yake koyar musu cike da ƙwarewa, yayinda gaba ɗaya ƴan ajin suka bada attention ɗinsu gareshi, ciki kuwa hadda Ziyada, wacce ɗigo ɗaya na daga cikin abun da yake koyarwa bata fahimta ba, jinsa kawai take, tana kuma kallon yanda yake solving guestions. Tambaya yayi da sauri wacce ke gefen hagunta, wato Shukhra kenan ta ɗaga hanu, ya ta da ita ta bashi amsa, ƴan ajine suka hau yi mata tafi. Haka dai ya gama yi musu karatun ya fita abunsa. Yana fita baifi da mintuna 5 ba wani Malamin Biology ya kuma shigowa. Tunda malamin yafara darasi'n ta kafe allon da idanu, turanci yakeyi musu cike da ƙwarewa, sannan gaba ɗaya explanation ɗin da yayi musu da turanci yayi su, tunda ya shigo babu wani wanda yayi Hausa haka kuma shima ko A akalmar hausa bai ambata ba, kamar dai yanda wancan malamin maths ɗin yayi haka shima wannan ɗin, hakanne ma yasa sam bata fahimtan komai, domin kuwa turanci zalla suke basa ko ɗan surkawa da yaren da zata gane wato Hausa, lokacin da taga kowa ya ciro littafinsa yana rubutu itama sai ta buɗe jakarta wanda Teacher Abdallah ya bata, bayan littatafai dake cikin jakan hadda wasu tarin kayan snacks. Wani littafi ta ciro haɗe da pen. Dayake Teacher Abdallah ya ɗan koya mata rubutu a lesson ɗin da sukayi, hakan yasa rubutun bai wani bata wahala ba, sai dai kuma bata wani ƙware sosai ba. Gani tayi shima kafun ya fita saida yayiwa ƴan ajin tambayoyi, amma inda Allah Ya taimaketa ita bai tambayeta ba, kuma ko dama ya tambayeta saidai ta bashi amsar shiru. Yana fita wani malamin yakuma shigowa shima dai yaɗan jima yana musu darasi kafun ya fita. Yana fita aka buga ƙararrawan fita break, gani tayi da ɗai ɗai ɗaliban ajin ke ficewa zuwa waje, Shukra ce ta miƙe tafice daga cikin ajin.

"Bazaki fita break bane?" Nasmah dake ƙoƙarin tashi tsaye ta tambayeta.

Samun kanta tayi dayin murmushi haɗe da cewa.

"Zan fita"

Ganin kowa yana fita da jakarsa rataye akafaɗarsa ne, yasa itama ta ɗauki ƙatuwar jakarta ta rataya akafaɗanta, sai da ajin ya zama babu kowa acikinsa sannan ta miƙe ta nufi hanyar fita, awani babban barandan dake gaban ajin ta tsaya tana mai bin ɗaliban dake ta hada hadarsu a harabar makarantar da ido, kowani ɗalibi ka gani yana tare da abokinsa, yayinda wasu kuwa sukaiwa kansu mazauni akan kujerun da akayi da siminti wanda ke ƙarƙashin wasu bishiyoyi dake harabar makarantar, zama tayi akan makeken dakalin dake ƙofar ajinsu, yayinda ta zuro da ƙafafunta ƙasa, aranta wani daɗi takeji wai yau itace acikin makaranta makarantar ma ta boko, yunwa takeji na ƙwaƙulan cikinta don haka ta buɗe zip ɗin jakarta, wani cake dake cikin wani haɗaɗɗen leda ta ciro, tare da fito da goran peach ɗin dake cikin jakar, ɓare ledan cake ɗin tayi ta soma gutsura ahankali, gani take kamar idanun gaba ɗaya ƴan makarantar akanta suke, musamman ma da taga duk wanda yazo gilmawa ta inda take sai ya kalleta, tana cikin cin cake ɗinne, ta hango Nasmah da Shukrah na tahowa zasu dawo aji. Suna ƙarasowa gareta Shukra ta wuce yayinda Nasmah ta tsaya akusa da ita, cike da kulawa tace.
"Me kikeyi ke ɗaya anan?"

"Babu" Ziyada ta bata amsa tana karkaɗe Hijabinta da burbuɗin cake ya ɗan zuba akai.

"Tashi muje Class, ko kin gane lecture's ɗin da akayi mana yau?" inji cewar Nasmah.

Ɗago kanta tayi ta kalli Nasmah'n,  samun kanta kawai tayi da girgiza mata kai alaman "A'a"

"Okay to muje Class" Nasmah tafaɗa tana mai ƙoƙarin haura dakalin ƙofar ajin nasu.

Tare suka shigo ajin ita da Nasmah,  Nasmah  ne ta ciro littafin Maths ɗinta, ahankali ta shiga yiwa Ziyada bayani dalla dalla da Hausa yanda zata fahimta, abun mamaki kuma sai gashi ta ɗan gane wasu abubuwan,  tana kammala koya mata Maths ɗin ta ɗauko Biology shima ta koya mata, aikuwa harma tafi gane Biology'n akan Maths ɗin, kasancewar shi baida  lissafi, bakamar Maths ba, har subject ɗin da akayi musu na ƙarshe kafun break wato Agric science saida Nasmah ta koyawa Ziyada, Alhamdulillah kuma ta fahimta sosai, akuma ɗan lokaci ƙanƙani wata ƴar shaƙuwa ta shigo tsakaninsu da  Nasmah, duk abun da sukeyi Shukrah na jinsu, amma ƙala bata ce musu ba, saima wata fakekiyar wayarta data ciro ta soma latsawa.  Suna kammala karatun aka dawo break.

Sosai suke shan karatu basu suka samu kansu ba sai  ƙarfe 1 na rana nan ma sallah aka fito dasu.  Nasmah ne ta jata suka nufi masallacin dake cikin school ɗin, Nasmah saida ta jirata tayi alwala sannan itama tayi, atare suka shiga cikin masallacin nan suka iske Shukrah tana sallah, gefe suma suka samu suka tada nasu sallan, suna idarwa Nasmah ta sake kama hanun Ziyada suka fito daga cikin masallacin.   Aji suka koma kowa yaciro abincinsa yafara ci,  ita dai da bata da wani abinci sai snacks shi ta ciro ta ɗanci kaɗan, Nasmah ce tayi mata tayi'n  soyayyen doya da naman kaza wanda tazo da shi, amma sam taƙi ci babu yanda Nasmah batayiba akan taci amma taƙi dolenta ta haƙura.

5:00  pm daidai shine lokacin tashinsu akowacce rana, yauma biyar na cika dai dai aka kaɗa ƙararrawan tashi.  Tare da Nasmah suka fito tana fitowa ta hango Kamalu driver tsaye ajikin mota, sallama tayiwa Nasmah da Shukrah sannan tanufi inda yake tsaye.
Tana shiga yaja motar suka bar haraban makarantar.

Tana shiga cikin falon, daddaɗan ƙamshin turare ya daki hancinta, ko ina na falon a gyare yake tsab.  Ƙofar ɗakinsa ta kalla, sannan ta wuce ɗakinta. Tana shiga ta soma cire kayan uniform ɗinta,  ban ɗaki ta shiga ta yi wanka, yanzu babu abun da bata iya amfani dashi ba na cikin banɗakin.

Tana fitowa awanka ta sanya kaya haɗe da faɗawa kan gado, ajiyar zuciya tashiga sauƙewa akai akai, wani irin gajiya haɗi da bacci takeji, basaban ba, idanunta ne suka sauƙa akan wani ƙaton akwati dake aje cikin ɗakin. Tashi tayi ta nufi inda akwatin yake tana buɗewa taga kayane shaƙe acikin akwatin, kama daga kan dogin riguna riga da sket ƴan kanti, da kuma dogin wanduna,  murmushi tayi haɗe da lumshe idanunta, batasan da wani baki zata gode masa ba, amma tabbas Ya Zama MADUBI acikin rayuwarta, da sannu itama zata haskaka ta zama kamar wata TAURARUWA. Komawa tayi ta kwanta cike da ɗokin sababbin kayan da tayi masu yawa.

Jin anata ƙiraye ƙirayen sallan Magriba ne yasa tatashi ta shiga toilet ta ɗauro alwala bata tashi akan sallayan ba saida ta yi sallan Isha, tana gama naɗe sallayan da tayi sallah akai, ta faɗa kan gado, wani irin baccine ke fusganta, tana kwanciya kuwa bacci ya ɗauketa ko lufayan dake jikinta bata cire ba.

Duk yanda yaso bacci ya ɗaukesa abun yaci tura, kwance yake akan makeken Royal bed ɗinsa wanda yaji lallausan bedsheet. Idanunsa dake alumshe ya buɗe haɗe da sanya hanu ya dafe kansa dake wani irin sara masa kamar zai faɗo ƙasa haka yakeji. Gaba ɗaya duniyar bata yi mashi daɗi, ƙuna yakeji acikin zuciyarsa abubuwa da yawa ne suka haɗe masa, hanunsa na dama ya sanya akan cikinsa wanda ke ɗauke da manya manyan 6 packs, ahankali ya ke murza fatan cikinsa, idanunsa gaba ɗaya sun kaɗa sunyi jajur dasu. Cigaba yayi da murza fatar cikinsa da ɗan ƙarfi haɗe da cije laɓɓansa. "Sai yaushe ne zai zama mutum me cikakken lafiya? sai yaushene zai san cewa shima Namiji ne? yaushe ne damuwarsa zata gushe? yaushe ne zaiyi bacci acikin farinciki da nishaɗi? yaushene zaiji abun da yake buri da fatan ji watarana? Abun tambayar aransa shine yaushe ne yazama haka? yaushe ne kuma zaici wannan jarabawar tasa mai wahala?" waƴannan tambayoyin su yakeyiwa kansa akullum, sau tari yakan cire rai amma yasan Allah na sane dashi idan yana darai watarana zai dace, amma kuma yaushene wannan ranan zata zo? shine abun da baisani ba, tashi yayi ya zauna still hanunsa nakan fatar cikinsa yana murzawa. Ƙafafunsa ya zuro ƙasa tare da sauƙowa daga kan gadon, gaban window ɗinsa ya nufa, tsayawa yayi ajikin window'n haɗe da sanya hanu ya yaye labulen window'n, buɗe glass ɗin window'n yayi take wata iska mai daɗi ta bugi fuskarsa, lumshe idanunsa yayi haɗe da buɗesu alokaci guda, ɗaga kansa yayi yana kallon sararin samaniya, farin wata ne ya haske ko ina da ina. Ahankali ya kejin nutsuwa na sauƙar masa, sosai yakejin daɗin ni'imar dake hurawa, yajima tsaye ajikin window'n kafun ya dawo cikin ɗakin. Kwanciya yayi akan gado yayinda ƙafafunsa ke ƙasa, ahaka wani bacci ya ɗaukesa, dagani kasan bajin daɗin baccin yake ba.

** **

Tun 7 ta kammala duk wani shirinta, saboda ta fahimci ba aso azo late a makarantar, duk yanda ta buga sammako wajen fita, amma bata iske shi afalo ba, saidai ta iske daddaɗan ƙamshinsa mai sanya nutsuwa, haka tashiga mota Kamalu driver yaja motar suka tafi batare da tayi tozali dashi ba.

Kamalu driver na tsaida motar ta ɗauki jakanta haɗe da soma ƙoƙarin buɗe murfin motar.
"Ga wannan Oga yace abaki" Kamalu driver ya tsaidata tahanyar faɗan haka, yana mai ciro kuɗi acikin aljihunsa.

Kallon kuɗin tayi sannan ta kalli Kamalu driver. "Ni kuma mai zanyi dasu to?" ta tambaya cike da mamaki.

"Haka dai yace abaki, hala ko kuɗin taran ki ne" Kamalu driver yafaɗi haka yana me ƙara miƙo mata kuɗin.

Cikin sanyin jiki tasa hannu ta amshi kuɗin, sannan tafice daga cikin motar aranta tana mai cewa da zaran takoma gida zata tambayeshi, hala ko wani abu ya keso tasayomasa da kuɗin.

Yau ta riga Shukra da Nasmah zuwa saboda haka ita kaɗai ta zauna tayi jigum,  ba wani jimawa sosai sai gasu sunzo atare, ga mamakinta yau fuskar Shukra asake take babu tsumewa kamar na jiya,  Nasmah na ganinta ta saki murmushi haɗe da ƙarasowa ta zauna akusa da ita.   "Yau munyi late kin rigamu zuwa" Inji cewar Nasmah dake ƙoƙarin sauƙe jakarta dake kafaɗarta.

Ta buɗe baki zatayiwa Nasmah magana kenan malami ya shigo ajin. Sai bayan yafita ne suka ɗanyi taɗi da Nasmah.. Yau dai sosai Nasmah tasake jawota jikinta ko ina zasu tare suke zuwa kuma Shukra na biye dasu saidai bata cika yawan magana ba. Hatta sallah yau atare sukayi su duka ukun.   Ko da suka idar da sallan ma tare sukaci abinci wanda Shukrah ce tazo musu da jallop rice wacce taji ɗanyen kifi.

Yauma agajiye ta dawo daga school ɗin tana idar da sallah ta soma bacci.

*** ***
Yau kimanin sati guda kenan tana zuwa makaranta, Alhamdulillah yanzu kam tana ɗan fahimtan wasu abubuwa musamman da Nasmah ta dage da koya mata,  acikin waƴannan kwanaki tayi sabo da Nasmah sosai, duk da cewa Shukra na shiga sha'aninta yanzu amma sunfi sabo da Nasmah,  aduk tsawon kwanakinnan bata taɓa ganinsa ba koda sau ɗaya ne,  saidai idan ta fito falo tana samun tsaraban ƙamshinsa dayake barmata akowacce rana.

(Wallahi yau ina busy sosai, tun jiya nagama typing amma bansamu daman yin update ba sai yanzu, . please kuyi manage da wannan banyi editing ba. Love you all and Son So.
Ku ƙaramin yawan Vote na ƙara muku yawan typing👌)
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈KAINUWA WRITERS ASSOCIATION*
_{United we stand and succeed; Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}_
*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

#romance

*Chapter 16*

Saturday!

Kamar dai yanda kowa ya sani saturday ranar hutuce ga yawancin ɗaliban makarantar boko. To haka ranar yau ta kasance saturday wato (Asabar). Zaune take aƙasa ta tanƙwashe ƙafafunta, jakar makarantarta ne agabanta, sai kuma wani littafin English ɗin dake riƙe a hanunta, lecture'n da akayi musu jiya take dubawa, so take karatun ya zauna akanta sosai, don taji malamin nacewa wani sati zai basu Assignment. Tunda tayi sallah ta ke riƙe da littafi, gaba ɗaya hankali da nutsuwarta naga littafinta so take ta iya duk wani abu da aka koya musu, a yanda ta ba da himma ne yasa ta fahimci wasu abubuwa da dama, wato shi karatu ɗan naci ne idan kanace masa da yardan Allah Zaka iya, sannan zaka gane komai sannu ahankali, yarda da wannan da tayi ne yasa abubuwa da yawa dake cikin karatun da take suka zauna akanta. Yunwar da ta soma ƙwaƙulan cikinta ne yasa ta aje littafin haɗe da jingina bayanta da jikin gado, ajiyar zuciya ta sauƙe, tare da lumshe idanunta da suke cike da bacci, kasancewar daren jiya bata wani samu isashshen bacci ba, domin kuwa jiya ba tayi bacci da wuri ba, har sai wajen ƙarfe 12:30 na dare sannan ta kwanta, karatu tayi sosai, sannan gashi kuma yau tayi tashin sassafe sakamakon wani irin zazzaɓi dake ta sanɗanta tun jiya da rana, amma dayake zazzaɓin baiyi ƙarfi ajikinta ba hakan yasa bata jikkata ba.

***

Duk da cewa yau Asabar amma bayajin zai iya zaman gida, shi kansa yasan yana da buƙatar hutu amma kuma yasan ko ya zauna agida hutun nasa bazai samu yanda yakeso ba. Fitowarsa awanka kenan yana ɗaure da towel a ƙugunsa, sannan kuma ga wani ɗan ƙaramin towel still dake riƙe a hanunsa, yana tsane ruwan dake kansa. Yana gamawa ya ɗauko handryer, da shi yayi amfani wajen busar da gashin kansa, mayinsa mai ƙamshi ya shafa, sannan ya ɗauki comb ya shiga taje sumar dake kansa, mayukan gashi har kala uku ya shafawa kansa, take gashin kannasa ya ƙara bayyana sheƙi da kuma walwali. Dogon wandon jeans wanda ke ɗauke da zane irin na kayan sojoji ya sanya, wandon irin mai yawan aljihunnan ne sannan ƙasan wandon atsuke yake da rubber, wata farar t-shirt ya sanya ajikinsa, take kyawunsa ya sake bayyana sosai kayan suka amshi jikinshi, kasancewarsa namiji mai murɗaɗɗiyar surar jiki, gun ƴar ƙaramar drawer'n da yake aje drugs ɗinsa ya nufa, wani magani dake cikin sachet ya ciro, tare da ɓallan guda biyu ya watsa abakinsa, sannan yakora da ruwan swan. Hanunsa riƙe da goran swan ɗin ya nufi falo.

Yana shiga cikin falon ya soma bin ko ina dake cikin falon da kallo, ko alaman datti babu acikin falon, hakanne ya tabbatar masa da cewa tabbas gyara falon akayi, duk da cewa dama babu wani datti acikin falon, amma dai kallo ɗaya zakayi kasan an gyara falon.

Kitchine ya wuce ya tafasa ruwan zafi acikin heater cup, yana gamawa ya juye a flask. Zama

yayi akan dinning tare da haɗa tea ɗinsa.  Sanya kofin tea ɗin yayi agaba ya kasa koda  ɗauka ne yakai bakinsa, sai jujjuya spoon ɗin dake  hanunsa yake acikin cup ɗin, yanayin yanda ya nutsu yayi shiru shine abun da zai baka tabbacin cewa tunani yakeyi.   Tabbas kuwa tunanin yake, maganganun da mahaifinshi yayi mishi masu tsauri su suke damunshi, bai ɗauka fushin da mahaifannashi keyi dashi har yakai haka ba, bai taɓa tunanin suma zasuƙi fahimtarshi ba, maganan da Abbanshi yayi mishi akan cewa  wai ya nemo matar aure ya aura, acikin ƴan ƙanƙanin lokaci idan ba haka ba kuma kada ya sake ƙiran wayanshi shine abun dake damunsa, tabbas hukuncin da Abbansa yayi mishi yayi tsauri da yawa, koda wasa baitaɓa tunanin zasu sake kawo mishi maganar aure nan kusa ba,  ya ɗauka zasu fahimceshi a wuce wannan stage ɗin,  ashe abun ba haka yake ba.  Wayarsa dake gefensa ne tasoma ƙara alaman shigowan ƙira,  jikinsa a sanyaye ya ɗaga ƙiran tare da kara wayar akan kunnensa.

Mas'oud dake zaune acikin motarsa yace
 "Gaye na shigo Abuja fa yanzu"

Cike da ɗan mamaki Sooraj yace

"Da gaske?"

"Bakayarda ba?"  murayar dake cikin wayar Sooraj ne ta bayyana raɗau acikin falon, da sauri Sooraj dake zaune akan dinning ya kalli ƙofar falon.

Mas'oud yagani yana murmushi.

Murmushin da iya kansa leɓe Sooraj yayi tare da kashe wayarsa.
"Kai ɗan rainin hankaline Mas'oud" Sooraj yafaɗi haka yana me kallon Mas'oud dake takowa zuwa garesa.

"Ni ne ɗan rainin hankali, ko kuma nida kai ne dukanmu ƴan rainin hankali?" Mas'oud ya faɗi haka yana mai ƙoƙarin jawo wata kujera dake fuskantar wacce Sooraj ke kai ya zauna.

Still ɗan guntun murmushinsa yayi,  haɗe da ɗaukan kofin  tea ɗinsa ya ɗanyi sipping kaɗan.

 "Sauƙar yaushe?"
ya tambayi Mas'oud.

"Banwuce 30 minute da sauƙa ba"  Mas'oud yafaɗi haka yana mai ƙoƙarin ɗaukan wani cup zai haɗawa kanshi tea, duk da cewa bawani damuwa da tea din yayiba kawai don yanajin yunwa ne ya sanya zai sha.

Ɗan sipping tea ɗin kaɗan yayi, tare da kallon Sooraj da yaketa aikin juya tea da spoon ɗin dake hanunsa,  ya ɗan karanci damuwa akan fuskar Sooraj ɗin, amma da yake yasan kwanan zancen sai kawai ya share haɗe da cewa..

"Ya maganan waƴannan kayanne? kasanfa yanzu babu kaya aƙasa"

Ajiyar zuciya Sooraj ya sauƙe haɗe da cewa "Next week zanje USA zan taho dasu"

Kai Mas'oud ya jinjina cike da gamsuwa sannan yace.
"Amma baka karɓi ribanka na wannan month ɗin bafa"

Shiru yayi baice komai ba, aƙalla yaɗauki kusan 4 minute bai tankawa Mas'oud ba, ganin haka yasa Mas'oud yin murmushi kawai ya cigaba da shan tea ɗinsa.

Ganin bazai iya shan tea din bane yasanya shi miƙewa tsaye, yana ƙoƙarin barin wajen Mas'oud yace.
"Inason muyi magana dakai"

Komawa yayi ya zauna tare da ɗaukan wayarsa ya soma latsawa "Inaji!" yace ataƙaice.

"Aure nakeso nayi" Mas'oud yafaɗi haka yana wata ƴar dariya.

Ajiye wayan Sooraj yayi tare da dawo da duk wani attention ɗinsa ga Mas'oud.

"Aure kuma?" ya tambaya da ɗan mamaki.

"Eh Aure mana, gaskia Raj na gaji, shekaru 29 fa ba wasa ba, ko so kake na zauna sha'awa ta kasheni bansamu na kawar da ita ba?" Mas'oud yafaɗi haka yana mai kafe Sooraj din da idanu.

Sunkuyar da kai ƙasa Sooraj yayi tare da cije laɓɓansa, wani irin abu mai ƙuna yaji acikin ƙirjinsa, ahankali ya ɗago kansa ya kalli Mas'oud ɗin cikin wata irin murya kamar mai koyon magana yace. "Sha'awa!"

"Eh sha'awa, banason na faɗa halaka Raj, amma seriously ina da buƙatar mace akusa dani, ina da buƙatar zama cikakken mutum nima, inaga kawai zan tura su Baba gidansu Aisha, su tambayomin izinin aurenta, inaga hakan shine mafita, amma kai maikagani?" Mas'oud ya tambayi Sooraj.

Wani murmushi Sooraj yayi, wanda shi kaɗai yasan menene meaning ɗin murmushin nasa, leɓensa na ƙasa ya sake ɗan ciza, tare da fesar da iska ta bakinsa.

"Allah Ya sanya Alkhairi!" yafaɗa ataƙaice.

"Ameen" Mas'oud ya amsa yana maison karantar yanayin da Sooraj ɗin ke ciki, sai dai kuma sam ya kasa gano wani irin yanayi Sooraj ɗin ke ciki, saboda Sooraj murɗaɗɗen mutum ne, zai maka wahala gane gabansa da bayansa.

"Abba ya faɗamin yanda kukayi dashi,  ina fata dai zakayi abun da ya keso?" Mas'oud ya tambayi Sooraj.

Miƙewa Sooraj yayi daga kan dinning ɗin, tare da  ɗaukar wayarsa ya bar wajen.  Da kallo Mas'oud ya bisa har ya shige ɗakinsa,  kai kawai  Mas'oud ya girgiza, sannan yadawo cikin falon ya zauna.

Yana shiga cikin ɗakinsa ya rufo ƙofar gam, jingina bayanshi yayi da jikin ƙofar tare da lumshe idanunshi,  wani iri ya keji acikin jikinsa, baijin ayau zai iya ɓoye rauninsa.  "Inama da ace zai iyayin kuka, inama da ace akwai wani wanda zaiyi sharing ɗin damuwarsa dashi, inama da ace zaiji abun da Mas'oud ya keji."   Abun da yake faɗa acikin ransa kenan.   Hanu yasa ya dafe saitin ƙirjinsa da keyi masa zafi.  Aƙalla ya ɗau kusan sama da mintuna 10 tsaye ahaka, da ƙyar ya iya jan ƙafafunsa ya zauna akan gado, har yanzu idanunsa a rufe suke,  jin kansa yake nayi masa ciwo, kwanciya yayi akan  gadon tare da buɗe idanunsa, numfashi yake fitarwa a hankali.... Saida yaji yaɗan dawo normal sannan yatashi ya fita falo, can ya samu Mas'oud, sake ɗan tattaunawa sukayi kafun daga bisani suka bar gidan baki ɗaya.

Gumi ne keta fitowa daga jikinta, zaune take agefen gado ta takure jikinta waje ɗaya, wani irin ciwo mararta da cikinta keyi mata, sake matse ƙafafunta tayi, laɓɓanta kuwa sai rawa suke kamar wata wacce  take jin sanyi,   ahankali sautin kukanta ke tashi acikin ɗakin,  jin mararta take kamar zata ɓalle ga zazzaɓi mai zafin gaske da ya rufeta.    Jin bazata iya daure ciwon ita kaɗai bane, yasa ta tashi a daddafe ta nufi falo.   Tana kaiwa tsakiyan falon ta faɗi a wajen tare da sakin wani ƙara, ciwonne ya ta so mata gadan gadan, kwanciya tayi aƙasa tanata mutsu mutsu da ƙafafunta yayinda ciwon ke ci gaba da nuƙurƙusanta.  Kuka take sosai hatta numfashinta saida ya soma seizing.

Dawowarsu kenan daga Sheraton  hotel inda sukaje suka gudanar da wani business ɗinsu, atare suka shigo cikin falon. Akuma daidai lokacinne kukanta ya dira acikin kunnuwansu, a ɗan razane Mas'oud ya kalli Sooraj, shima kallonsa yayi amma sai ya share ya ƙarasa cikin falon, idanunsa yaɗan waro ganin yanda take yashe aƙasa gaba ɗaya ta fita acikin hayyacinta, ɗan kwalin dake kanta ya zame gefe yayinda gashin kanta ya watse akan carpet ɗin dake malale a tsakiyar falon,  yanayin yanda yaga takeyi shine abun daya ɗan tsoratashi, domin kuwa ta shiɗe sosai da alama ma bata cikin hayyacinta,  amatuƙar tsorace Mas'oud ke kallon Yarinyar yana kuma kallon Sooraj, koda wasa bai taɓa tunanin Sooraj yana tare da yarinyar ba, a iya tunaninsa Sooraj yajima da sallamanta ta kama gabanta,  wani irin bahagon tunani ne ya ɗarsu acikin ran Mas'oud, bakinsa cike suke da tarin tambayoyi amma dole ya adana tambayoyinsa.

Ƙarasawa inda take yayi haɗe da ɗan durƙusawa hanunsa yakai yaɗan bugi fuskanta  "Ke!" ya faɗa yana mai sake ɗan tattaɓa fuskarta.

Wani irin nishi tayi take kuma gaba ɗaya jikinta ya sake komai nata ya daina motsi.  Ya ɗan razana kaɗan da al'amarin nata, ɗaukarta yayi caɗak ajikinsa ya nufi ƙofar fita daga falon. Tsananin mamaki shiya hana Mas'oud rufa musu baya, tsayawa yayi ya kasayin komai kamar

wani statue,  ganin tsayuwar baza ta kai mishi ba, yasanya shima ya rufa musu baya, lokacin da ya fita waje har Sooraj ya sanyata acikin mota yana ƙoƙarin shiga gidan driver, da sauri Mas'oud yaje ya shiga motar ɓangaren mai zaman banza.     Gudu sosai Sooraj keyi akan titi mintuna kaɗan suka isa asibiti, likitoti ne suka karɓeta sukayi ciki da ita.

Zama yayi akan wata kujera tare da sanya hannayensa ya rufe fuskarsa da tafukan hannunsa. Agefen Sooraj Mas'oud shima ya zauna, shiru yayi ko wanne daga cikinsu da irin nazarin da yakeyi acikin ransa,   tambayoyi ne cike azuciyar Mas'oud, shi kuwa Sooraj ya marasa wani tunani zaiyi, abubuwa sunyi masa yawa,   ahankali idanunsa suka kaɗa sukayi jajur dasu, tananne kawai zaka iya fahimtar tarin damuwan da yake ciki.   Wani likita ne ya fito daga cikin ɗakin da aka kwantar da Ziyada, ce wa yayi su Sooraj ɗin su sameshi a office ɗinsa, babu musu suka tashi suka rufa masa baya.

Ajiyar zuciya Sooraj ya sauƙe abayyane tare dayin ƙasa da kansa.
Mas'oud ne yayi ƙarfin halin cewa "Yanzu likita wani hali take ciki?"

Gyara zama Likitan yayi tare da cewa.
 "Kamar yanda na faɗa muku a farko, ba wani babban matsala bane, yawancin mata sukan samun irin wannan matsalolin idan zasu fara period, to itama tana ɗaya daga cikin irin waɗannan matan, amma babu wani damuwa zata warke insha Allah, Yanzu haka ta samu bacci, da ta farka kuma zamu baku Sallama, ga wannan saiku sayo shine magungunan da za tana sha"  likitan ya faɗi haka yana me miƙowa Mas'oud wata ƴar farar takarda da yayi rubutu ajiki, amsa Mas'oud yayi tare da ɗan satan kallon Sooraj wanda har yanzu kansa ke ƙasa bai ɗago ba.    Hanu dukansu suka miƙawa likitan suka sakeyin musabaha daga haka suka fice daga cikin office ɗin, direct wajen da ake biyan kuɗi Sooraj ya nufa,  kuɗin gadon da aka kwantar da ita ya biya, sannan suka nufi pharmacy. Bayan sun karɓi maganin Sooraj ya sake biyan kuɗi,  direct motarsa ya nufa,  ganin haka yasa Mas'oud ya bi bayansa. Ƙoƙarin buɗe murfin motar yake, muryar Mas'oud ta dakatar dashi.  ɗan tsayawa da abun da yakeyi yayi tare da juyowa ya fuskanci Mas'oud ɗin.

Shima Mas'oud fuskantar Sooraj ɗin yayi haɗeme da cewa..  "Wacece ita awajenka? Sannan mai yasa ka ajiyeta agidanka? Me wannan rayuwar da kukeyi take nufi SOORAJ ?"  Mas'oud yayi masa duka waɗannan tambayoyin alokaci ɗaya.

(Sorry🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈KAINUWA WRITERS ASSOCIATION*
_{United we stand and succeed; Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}_
*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

#romance

*Chapter 17*

Buɗe murfin motar yayi ya shiga, batare da yace wa Mas'oud dake tsaye ƙala ba, zai rufe murfin motar ne, Mas'oud yayi saurin riƙe murfin ransa aɗan ɓace yace.
"Wai hakan da ka keyi me yake nufi ne Sooraj? me kake tunani idan su Abba sukaji abun da ka aikata? menene amfanin hakan!!"

Wani iska ya fesar daga bakinsa, tare da jingina bayanshi da jikin kujeran motar.
"Mai kakeson ji daga gareni Mas'oud?" yafaɗi haka cikin wata murya mai sanyi.

A ƙufule Mas'oud yace.
"Bansani ba" Juyawa Mas'oud yayi afusace yabar wajen, da ƙafansa ya nufi hanyar fita daga cikin asibitin, Sooraj na kallonsa ya tari taxi ya shiga, yana ganin tashin taxi ɗin ya jawo murfin motarsa ya rufe, kifa kansa yayi akan steering motar, tare da sauƙe wata ƙaƙƙarfan ajiyar zuciya, ya ɗauki kusan mintuna 6 ahaka, kafun daga bisani ya ta da motarsa ya fice daga cikin asibitin. Direct wani super market ya nufa, zama yayi akan wata kujera, tare da umartan wata ma aikaciyar wajen da ta haɗa masa duk wani abu da tasan mace na da buƙata, kama daga kan suturun sawa da dai sauransu, take ita kuwa tashiga aikinta, kaya masu kyau ta jidar masa hadda su pants, kasancewar tasan duk wata mace indai ta girma to tana da buƙatarsu, bai da mu da yawan kuɗin kayan ba haka ya cire ya biya, yaran dake aiki a wajen su suka kwashe kayan suka kai mishi cikin mota.

Kafun ya koma asibitin saida ya biya ta wani hotel yayi take away, sannan ya ɗauki hanyar komawa asibitin. Yana shiga asibitin direct ɗakin da aka kwantar da ita ya nufa.
Tana kwance tana baccinta cikin kwanciyar hankali.
Zama yayi akan wata kujera dake gefen gadon tare da lumshe idanunsa. Kamar jiran zuwansa take ahankali ta ɗan soma motsawa, jin motsinta da yanda numfashinta ke fita ne, ya san yashi buɗe idanunsa, haɗe da maida kallonshi gareta.

Ahankali ta soma ɗan ware manyan idanunta harta buɗesu tarwai, saidai kuma kallo ɗaya zakayi mata kasan taji jiki, domin kuwa hatta ƙwayan idanunta saida suka sauya kala, sunyi wani fari fat dasu.
Tashi tayi ta zauna tana mai ɗan cije laɓɓanta, sam batasan da cewa yana cikin ɗakin ba.

"Aushhh" taɗan saki wani ƙara, saka makon murɗawan da taji maranta yayi,  ɗan yarfe hannuwanta ta somayi,  tare da soma yunƙurin sauƙa daga kan gadon,   Idanunsu ne ya sarƙe acikin na juna, ji tayi gabanta ya wani irin faɗuwa, da sauri tayi ƙasa da kanta,  tare da haɗiyan wani yawu dake maƙale a maƙoshinta.
Aƙalla yaɗauki kusan 50 second yana kallonta,  abun da bai taɓa yi ba kenan, ahankali ya janye idanunsa daga kanta tare da kawar da kanshi gefe.

Shiru ne ya shiga tsakaninsu na kusan mintuna 2,  jin wani abu  me ɗumi tayi ya fito daga jikinta, hakan yasa ta ƙosa ta je banɗaki ta duba ko menene,    ganin zaman bazai kaita ba yasa ta sauƙa daga kan gadon, banɗaki'n dake cikin ɗakin ta shiga tare da rufo ƙofar,   tashi shima yayi ya fita daga cikin ɗakin.

Bugun zuciyarta ne ya tsananta,  duk da kasancewar tasan abun da ta gani ajikinta mai yake nufi,  amma sai da ta ɗan tsorita.
"Yanzu yazatayi kenan? wa zata faɗawa ya taimaketa?" Tambayar da tayiwa kanta kenan.  Ji tayi ana knocking ƙofar banɗakin, ai saura ƙiris ta zame awajen da take tsaye saboda tsoro, atunaninta Sooraj ne ke buga ƙofar,   ƙafafunta ne suka soma rawa.    "Taya zata fara faɗa masa matsalanta?"  still ta kuma sake tambayar kanta,  jin anata buga ƙofar ba a tsaya ba,  ya sa ta taho cikin sanɗa ta buɗe ƙofar,  wata ƙatuwar ajiyar zuciya ta sauƙe,  sakamakon ganin wata likita mace da tayi tsaye abakin ƙofar, ashe ma ita ke buga ƙofar ba Mai taimako ba, saɓanin tunaninta.

"Sannu ya jikinnaki?" nurse ɗin ta tambayeta.

"Da sauƙi" Ziyada ta bata amsa tana ɗan ƙaƙalo murmushin dole.

"Masha Allah haka ake so ae, ga wannan saiki kimtsa kanki ko" nurse ɗin ta faɗi haka tana me miƙo mata wata baƙar leda dake hanunta.
Karɓan ledan tayi tare da komawa cikin ban ɗakin,  tana buɗe ledan taga pad's da kuma pant's ne aciki, wani ƙaton ajiyar zuciya ta sauƙe, gefe guda kuwa tsananin mamaki haɗi da kunya ne ke ɗawainiya da ita, da farko dai mamakin yanda akayi nurse ɗin tasan halin da take ciki take, na biyu kuma tsantsar kunyar nurse ɗin ne ya kamata,  wani pant ta ɗauko wanda anriga da an maƙala pad ɗin ajikinsa, kallon yanda aka maƙala pad ɗin tayi da kyau, sai da ta ciro wani pant ɗin ta gwada maƙalawa taga yayi sannan ta sauƙe ajiyar zuciya, kasancewar dama bata san ya ake amfani dashi ba.    Aɗaɗare ta fito daga banɗakin sai dai rashin ganin kowa da tayi acikin ɗakin hakan sosai yayi mata daɗi.  Tana zama akan gado, akaturo ƙofar ɗakin, wannan nurse ɗin ce dai ta kuma dawowa,  bayani tayi mata sosai akan yanda zata kula da kanta, da kuma yanda za tana tsabtace jikinta, sannan tace mata taje yayanta na jiranta a mota.  Ɗaukan ledan da nurse ɗin ta bata tayi,  sannan suka fito atare da nurse ɗin, har bakin motar Sooraj nurse ɗin ta rakota sannan sukayi sallama.

Tana shiga cikin motar ko gama gyara zamanta batayi ba ya yiwa motar key.  Saida suka hau titi sannan ta ɗan saci kallonsa ta gefen idanunta,  maganane abakinta, amma yanda fuskarsa take

babu alaman wargi, yasa taja bakinta tayi gum,  ita ayanda ta fuskanta ma shine, shi ko da yaushe ahaka fuskarsa take.

Basu yi wani tafiya sosai ba, ta ga  ya gangara gefen titi tare da tsaida motar cak,  juyawa yayi ya ɗauko wata leda dake  aje a sit ɗin baya, miƙo mata ledan yayi  tare da cewa.
 "Kici yanzu yanzun nan sai kisha magani"

 Baijirayi mai zata ceba ya buɗe murfin motar ya fita, tana kallonsa ya shige cikin wani waje mai kama da kamfani, wanda yake gaba kaɗan da inda ya aje motar tasa,  ledan ta buɗe ta ciro take away ɗin, rubber spoon ɗin dake jikin  take away ɗin, ta zare haɗe da sanyawa acikin abincin.   ahankali take tsakalan abincin, gaba ɗaya bata wani jin daɗin bakinta, duk da cewa tana jin yunwa amma batajin abinci zai wani samu shiga cikinta sosai,  bata wani ci abincin sosai ba,  ta rufe take away ɗin tare da maidashi cikin ledan, goran ruwan da tagani a inda ya tashi tasanya hanu ta ɗauka,  buɗewa tayi tare da kai bakin  goran bakinta,  lumshe idanunta tayi, tare da sauƙe wani irin ajiyar zuciya, tayi imani duk wani abu da zai fito daga gareshi to ƙamshi yake, hatta goran ƙamshinsa take, tana son wannan ƙamshin nashi har acikin ranta, bama ita kaɗai ba ta tabbatar duk wanda yaji ƙamshin nashi dole zai so sa.  Bata fargaba sai kawai jin motsinsa  tayi a gefenta, da sauri ta kalleshi don sam batasan da zuwanshi ba,    buɗe wani waje mai kama da ɗan ƙaramin drawer dake cikin motar yayi, magungunanta ya ciro, da kansa ya ɓare magungunan ya miƙa mata, aƙoƙarinsa na ya zuba mata magungunan acikin hanunta ne hannayensu suka haɗe waje guda,  da sauri ya zuba mata magungunan acikin tafin hanunta, tare da zare nashi hanun,  ba don taso ba haka tasha magungunan kasancewar suna da ɗan ɗaci, tana sha ta jingina bayanta ajikin kujera tare da lumshe idanunta.    Tuƙi yake amma gaba ɗaya hankalinshi na ga wayarsa yana duba wani saƙo da aka turo masa, ahaka har suka isa gida.
Yana danna horn mai gadi ya wangale masa gate ya tura hancin motar ciki.

Jin sun tsaya ne yasa ta buɗe idanunta ahankali,   ganin yana ƙoƙarin fita daga cikin motar ne, yasa itama ta buɗe murfin motar ta fita.  Sawa yayi Kamalu driver ya shigar masa da kayan da ya sayo ciki.

 Yana shiga cikin ɗakinsa ya kwanta flat akan gado tare da lumshe idanunsa,  kamar an tsikareshi haka ya buɗe idanunsa da sauri, bakomai yasa hakan ba face, ganin oily eyes ɗinta da ya keyi  suna yi  masa yawo acikin nasa idanun, hakan kuwa na sawa yaji wani iri ajikinsa. Ban ɗaki ya wuce ya haɗawa kansa ruwan wanka..

Itama tana shiga cikin ɗakinta,  gado ta hau ta kwanta, tare da cusa kanta acikin pillow, abu kamar wasa sai ga wani sabon bacci ya sake ɗaukanta...

***   Tsakanin  jiya da yau Alhamdulillah ciwon ya ɗanyi mata sauƙi,  kwana biyunnan jinta take atakure, zuwa yanzu ta saba da makaranta,  shiyasa takejin zaman gidan gaba ɗaya bayayi mata daɗi, gashi shima Ogan gidan ba ganinshi take ba, ita kaɗai take rayuwarta,  jakar

makaramtarta ta ɗauko ta shiga haɗa littatafanta, tana gamawa ta jawo ledan abincin da aka kawo mata ta soma ci, bata wani ci mai yawa ba ta ture abincin gefe, jin gidan ya ɗauki shiru babu alaman motsin kowa acikinsa ne yasa ta fita zuwa falo, kusan kullum TV plasma'n dake cikin falon a kashe yake, amma yau ga mamakinta akunne ta sa meshi, zama tayi akan sofa tare da maida hankalinta ga TV'n, tana nan zaune acikin falon har aka ƙira sallan Isha sai alokacin ta tashi ta koma ɗaki, tana shiga tayi kwanciyarta, kasancewar ba sallah takeyi ba.

1:30 na dare, ƙaran taɓa gate ɗin gidan da ake, shine yayi sanadiyar tashinta daga bacci, ahankali ta sauƙo daga kan gadon, bakin window ta nufa don ganin wake taɓa gate ɗin, duk da babu wadataccen haske aharabar gidan, amma inuwarsa kaɗai yasanya tagane wanene, domin akaf gidan babu wani mai irin yanayin jikinsa shi kaɗai ne, tana ganinsa da kansa ya buɗe gate ɗin gidan, sannan ya koma ya shigo da motarsa ciki, tana ganin ya mai da gate ɗin ya rufe ta ɗan saki wata ajiyar zuciya, mamaki da wani kokonto ne suka ɗarsu acikin zuciyarta, don son sake tabbatarwa da kanta cewa shiɗinne ko ba shi bane, yasa ta ɗan buɗe ƙofarta ahankali fitowa tayi ta tsaya abakin ƙofar, dai dai lokacin shi kuma ya buɗe ƙofar falon ya shigo, key ya murza ajikin ƙofar sannan yabar key ɗin ajiki, Yana maiƙoƙarin cire rigar dake jikinsa ya ƙarasa gaban fridge. Buɗewa yayi ya ɗauko goran Fearless. Wuceta yayi tamkar baiganta ba, alhali kuma tunshigowarsa idanunsa suka gane masa ita, harya ɗaura hanunsa akan handle ɗin ƙofar ɗakin nasa, sai kuma ya dakata batare da ya juyo ba yace.

"Me kikeyi anan?"

Ziyada dake ƙoƙarin komawa ɗaki, taji sauƙar muryartasa tamkar rugugi acikin kunnuwanta, da sauri ta juyo garesa saidai bata iya kallonsa ba, duk da cewa ya bata baya.
"Babu"
Tace murya asanyaye.

"Wani abu ya faru ne?" Yasake tambayarta still batare daya juyo ya kalleta ba.

"A'a" Ta bashi amsa muryarta naɗan rawa, hakanan idan yana gabanta sai taji wani irin tsoronsa ya kamata.

Murɗa ƙofarsa yayi ya shige ciki
tare da rufo ƙofar, tana tsaye taji ya murzawa ƙofar key ta ciki, ajiyar zuciya ta sauƙe haɗe da komawa nata ɗakin itama, da ƙyar ta samu bacci yasake ɗaukanta.

Shikuwa bai iya samu bacci ya ɗaukesa ba, har sai da yasha maganin da ke taimaka masa wajen sanyashi bacci, duk da haka dai baccin baiyishi cikin daɗin rai ba.

7:00
Daidai ta gama shiryawanta, tayi kyau acikin uniform ɗinta kamar kullum, tana kammala saka white socks ɗinta, tasoma jin ana knocking ƙofar falon, school bag ɗinta ta rataya bisa

kafaɗanta sannan tafi ta zuwa falon,  dama bata saba ganinshiba don haka batasa aranta zata ganshi ba. Tana buɗe ƙofar wanda ke kawo mata abinci kullum yaɗan yi mata murmushi, itama murmushin tayi masa tana ƙoƙarin gaidashi ne ya miƙo mata wata kula mai kyau wacce take da ɗan mariƙi a samanta.
 "Madam ga saƙonki inji Oga"  yace da ita.
Karɓa tayi, shikuma ya juya yayi tafiyarsa,  komawa cikin falon tayi tare da buɗe kulan. Kulan irin mai hawa ukunnanne wato (3pieces) hawan farko da ta buɗe soyayyen dankali ne aciki wato chips da kuma ƙwai, sai hawa na biyun dake ɗauke da gasashshen nama mai albasa, hawan ƙarshe shine ke ɗauke da shinkafa fried rice wacce taji liver,  ɗaukan kulan tayi ta riƙe ahanunta, tana fita waje ta samu Kamalu yana tsaye ajikin mota yana jiranta.    Tunda suka ɗauki hanyar makarantar yau Kamalu keta mata zuba, ita dai ba gadon magana bace hakan yasa take amsa masa kaɗan kaɗan, shikuwa sai labarai yaketa bata, ganin yanda take amsa masa ne, yasa aranshi yace "Duk yanda akayi itaɗin jinsin Oga ce, da'alama duka zuri'arsu haka suke basason magana"

Yau kam Su Nasmah sun rigata zuwa, tana zama Nasmah ta ce "Ki koma kinyi late"

Dariya ta yi tare da ɗan satan kallon Shukrah,  matsawa kusa da Nasmah tayi sosai cikin ƙasa da murya tace.
 "Yau maiyasamu Shukrah na sake ganin fuskarta babu walwala?"

Baki Nasmah ta taɓe haɗe da cewa.  "Hmm barta kawai kekam wahalane bai ishetaba, wai fa soyayya take kullum kuma sai sunyi faɗa da saurayin"
Idanu Ziyada taɗan zaro waje cike da mamaki tace.  "Soyayya!"

"Eh Soyyayya" Nasmah ta faɗa tana ɗan kallonta.

Shiru Ziyada tayi tare da jin wani abu acikin ranta. "Kenan dama Soyayya gaskia ce?" tambayar da tayiwa kanta kenan sannan ta kuma sake tambayar kanta "Menene alamomin soyayya?"

"Yanaga kamar kina tunani" Cewar Nasmah da ta shiga mamakin yanayin da taga Ziyada ta shiga.

"Babu" Ziyada tafaɗi haka tana ɗan yin murmushi, Malamin English ne ya shigo cikin ajin hakan yasa suka bada gaba ɗaya hankalinsu gareshi.

Yau a wajen da aka tanadar musamman dan cin abincin ɗalibai sukaci abincinsu,   ita dai Shukrah gaba ɗaya bata da wani walwala, Ziyada da Nasmah ne kawai suketa sha'aninsu. Shaƙuwar da ke tsakanin Ziyada da Nasmah shine ke ƙarawa Ziyada jin daɗin rayuwar makarantar.   Yau ba atashesu ba har sai biyar da rabi kasancewar anshiga dasu meeting akan jarabawan da zasu fara next month.    Agajiye ta dawo gida ga ciwon cikin dake  sanɗanta, da ruwan zafi tayi wanka sannan ta kwanta.

11:00 ta farka daga ɗan baccin daya ɗauketa, wani irin ciwon da cikinta keyi mata shine abun daya ɗaga mata hankali, Kuka take hanunta dafe da saman mararta wanda takejinta kamar zata ɓalle.

Yana zaune akan gado yana danna laptop ɗinsa, ahankali ƙaran kukanta ya shiga kawowa kunnensa ziyara. Ɗauke hanunsa yayi daga kan laptop ɗin tare da yin shiru yana mai sauraran yanda kukan nata ke tashi. Kallon agogo yayi yaga ƙarfe 11:10 na dare, wata ƴar ƙaramar tsuka yaja tare da sanya hanu ya dafe goshinsa. "Me na ɗaukowa kaina ne?" tambayar da yayiwa kansa kenan.

Jin kukannata na daɗa ƙaruwa ne yasan yashi miƙewa, ƙofar ɗakin ya buɗe ya fita, tsayawa yayi ajikin ƙofar ɗakin da take yana mai tunanin shiga cikin ɗakin. Jin taƙi daina kukan ne yasashi murɗa handle ɗin kofar ya shiga. Yashe ya ganta aƙasa tanata birgima gaba ɗaya gashinta ya watse akan tiles, kuka take irin na fitar hayyaci. Ƙarasawa yayi inda take yashe aƙasan tana ta mutsu mutsu, hannayensa yasanya ya kama kafaɗunta, jin sauƙar hanun mutum akan kafaɗunta yasanya ta kama hunun nasa ta damƙe da ƙarfi, da ɗayan hanunnasa da bata kama ba yayi amfani wajen ɗago haɓarta, gaba ɗaya fuskarta ta ɓaci da hawaye, zara zaran eye lashes ɗinta sun jiƙe da hawaye sun manne akan fatarta. Hanunsa dake cikin hanunta ta ƙara matsewa tare da sakin wani ƙara, ji take kamar taita buga kanta ajikin gini ko zata samu salama, ganin yanda take shiɗewa ne yasanya shi ɗagata caɗak ya nufi kan gado da ita, kwantar da ita yayi, tare da ɗauko magungunanta ya bata.
***
After 30 minute har yanzu gunjin kukanta ne ke tashi acikin ɗakin, sama da mintuna talatin kenan da bata magani amma har yanzu ciwon bai lafa ba, tun tanayin kukan da duka jarumtarta har takai tanayin kukan acikin yanayi na galabaita, hankalinsa ne yasoma tashi, wayarsa ya ɗauka ya ƙira Number'n Dr.Waleey, shaida masa abun dake faruwa Sooraj yayi, shiru yayi yana maijin amsar da Dr.Waleey ke bashi, cikin rashin ƙarfin guiwa ya aje wayartasa bayan sunyi sallama da Dr.Waleey'n, shiru yayi haɗe da zuba mata mayun idanunsa, sosai zuciyarshi ta karaya akanta, wani irin tausayinta yaji ya daki zuciyarsa, duk wanda yaganta acikin irin wannan halin sai ya tausaya mata, musamman yanda tayi buji buji da gashin kanta, ga numfashinta dake ƙoƙarin sarƙewa tsabar kukan da tayi, maganganun Dr.Waleey ne suke dawowa cikin kunnensa. Bayajin zai iya aikata abun da Dr.Waleey yace yayi, sannan kuma bayajin zai iya jure ganinta acikin halin wahala, baisan maiyasa yake jin son taimakonta ba tun farko, ayanzu yanaji inama da ace tun farko bai taimaketa ba, rumtse idanunsa yayi da ƙarfi sakamakon yanda yaga takeyi, baida wani zaɓi wanda ya wuce ya taimaketa, tashi yayi ya nufi gadon, sautin bugawar zuciyarshi ne ya tsananta yayinda ƙirjinsa ke tsalle kamar zai faɗo ƙasa, da ƙarfi bugun zuciyarsa ke harbawa...

(Na yau dana gobe duka na haɗa muku😝 kuji daɗinku ku more, idan ku naga kamar naso kaina, sai ku karanta rabi yau gobe ku ƙarisa karanta rabi😂)

[12/April/2020]

*Vote Me On Wattpad*
@fatymasardauna kwana biu bana baku update da wuri🙏🏼   Fans ɗina na Facebook ina gaisuwa)

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈KAINUWA WRITERS ASSOCIATION*
_{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}_
*https://facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

#romance

*Chapter 18*

Ƙirjinsa ne ke ta dokawa kamar zai fito waje. Yana ƙarasawa gaban gadon yaja ya tsaya tare da kafeta da idanunsa, jin kukanta yake har acikin ransa,  hannayen rigansa ya ɗan naɗe tare da nufar  toilet ɗin ɗake cikin ɗakin,     heater ya kunna ya tari ruwan zafi acikin wani ɗan madaidaicin bucket,  towel ya ɗauko sannan ya fito daga cikin toilet ɗin.   Kafansa ɗaya yasanya ya taka kan gadon, baisan tayaya kuma ta ina zai fara ba, hakan baikamacesa ba, sannan kuma sam hakan ba aikinsa bane, saidai kuma sosai yake tausayin halin da take ciki. Aƙalla yaɗau kusan mintuna 10 a haka ya kasa aikata komai, yayinda ita kuwa har yanzu take aikin kuka gaba ɗaya tasake fita  hayyacinta,    zama yayi akan gadon tare da sanya towel ɗin acikin ruwan zafi,  hannayensa ne suka ɗauki rawa, ya kasa  koda kai hanunsa jikinta, zuciyarsa bugawa take,  hanunsa yakai kan wuyanta ya ɗan taɓa, ji yayi babu wani zazzaɓi sosai ajikinnata,   rumtse idanunshi yayi tare da kai hanunsa kan lafeffen cikinta,  tamkar wanda aka jonawa shocking haka hannayensa ke rawa, da ƙyar ya iya ɗan ɗage rigan dake jikinta yayi sama dashi,   still hannayensa na rawa yasanya hanu ya ɗanyi ƙasa da sket ɗinta, towel ɗin yaciro daga cikin ruwan zafin tare da ɗan matsawa ya rage ruwan dake jiki,   sake rumtse idanunshi yayi tare da ɗaura towel ɗin adai dai kan cikinta, wani ƙara tasanya tare da ɗan soma yunƙurin tashi zaune, baisan sanda yasanya ɗayan hanunsa ya maida ita ta kwanta ba,  sai

alokacin ya samu damar buɗe idanunshi ya sauƙesu akan fuskarta, hawaye ne kawai ke gangarowa ta gefen idanun ta, gaba ɗaya ta galabaita. Sake danna towel ɗin yayi akan cikinta, gani yayi ta sake rumtse idanunta, ahankali yake ɗan matsa towel ɗin akan cikinta, ƙasa ya somayi da towel ɗin daidai kan mararta ya tsaya, Yanayin yanda yake matsa towel ɗin akan maranta ne, yasanya ta jin wani ɗumi na ratsa gaba ɗaya ilahirin jikinta, sake maida towel ɗin cikin ruwa yayi tare da ɗan matsewa, sake manna mata yayi akan maranta, haka yadinga yi mata har tsawon wasu lokuta, ahankali kukanta ya tsaya cak, wani irin ajiyar zuciya take sauƙewa akai akai, fitar numfashinta ne ya soma sanja sauti, ya zama na yana fita slowly, duk wannan abun da yake mata, bai bari idanunshi sun kaishi ga kallon jikinta ba. Cikin wani irin yanayi na wahala ta kamo hanunsa na hagu ta riƙe acikin nata hanun, ganin haka yasa ya aje towel ɗin agefe, ɗan ranƙwafowa yayi tare da kawo bakinshi dai dai saitin kunnenta, ahankali ya soma hura mata iskan dake bakinsa acikin kunnenta. Daddaɗan ƙamshin turarensa ne ke ziyartan hancinta, yayinda iskan bakinsa dake hura mata ya kasance garkuwa wajen samun nutsuwarta, ahankali taji wani irin salama na sauƙar mata, cikin wani irin yanayi hucin numfashinsu ke gauraya waje guda, jin yanda sautin numfashinta ya sauya ne, yasanyashi ɗan ɗago da kansa ya dube ta, gani yayi tana fitar da numfashi ahankali da alama bacci ne ya ɗauketa, wata ƙatuwar ajiyar zuciya ya sauƙe, tare da ɗago kansa daga ranƙwafon da yayi, hanunsa dake cikin nata ya kalla wanda ta damƙeshi gam. Ƙoƙarin cire hanunsa daga cikin nata yayi, amma yaji ta sake riƙe shi gam, cikin ɗan dabara ya samu ya zare hanunshi, hannayensa ya ɗaura akan kafaɗunta tare da gyara mata kwanciya, blanket ya rufa mata, sannan ya rage mata hasken ƙwan wutan dake cikin ɗakin, tashi yayi ya fita tare da jawo mata ƙofar. Ɗakinshi ya koma yayi kwanciyarsa, ya jima kafun bacci ɓarawo ya samu damar ɗaukarsa.

Tunda ta kwanta ba itace ta farka ba sai ƙarfe 8:00 daidai na safiya, ahankali take buɗe gajiyayyun idanunta da suka kumbura sukayi luhu luhu dasu, kasancewar daren jiya tasha kuka sosai, tashi tayi ta zauna akan gadon tare da sanya hanu ta shafi saman mararta, ko ɗigon ciwo bataji ajikinta saidai kasala kawai dake damunta, lumshe idanunta tayi tana mai ƙoƙarin son tunano abun da ya faru da'ita a daren jiya, ita dai bazata iya cewa ga abun daya wakana ba, amma tabbas tasan ta ganshi acikin idanunta, sannan kuma taji daddaɗan ƙamshinsa acikin hancinta, amma wata zuciyar ta na faɗa mata cewa ba shi bane. Zuro ƙafafunta ƙasa tayi daga kan gadon tare da tashi tsaye, banɗaki ta wuce ta haɗawa kanta ruwan wanka mai ɗan ɗumi, sosai taji daɗin wankan da tayi domin ya ƙara taimakawa wajen warware mata gajiyan dake jikinta.

Cikin sauri sauri ta zura kayan uniform ɗinta, safa'nta ta sanya tare da ɗaukan school bag ɗinta, duk da batasan ƙarfe nawa bane yanzun, amma tabbas da dukkan alama yanda taga rana ta bayyana raɗau tasan tayi latti, fitowa falon tayi tana mai ƙoƙarin cusa wani littafi dake hanunta acikin jaka, sam bata lura dashi ba kasancewar bata kawo ma aranta cewa zata ganshi ba.

"Ina zakije?" muryarsa ya doki dodon kunnenta, cak ta tsaya daga tafiyar da takeyi, tare da dawo da kallonta zuwa inda taji sautin muryar ta fito.
Zaune yake akan dinning table yasha kyau cikin riga da wando na suit amma baisanya suit ɗin ba, sai dai tana aje agefensa, parking shirt ne ajikinsa Navy blue colour wanda ta ƙara masa

kyau. Cup ɗin tea ne ahanunsa yana sha da kaɗan kaɗan.

Bazata iya jure kallonshi ba, saboda sosai yake mata kwarjini. "Dama zanje makaranta ne!" tabashi amsa cikin muryarta mai sanyi.

Shiru yayi kamar bazai amsa mata ba, sai kuma ya ɗago kansa yaɗan kalleta. "Zokici abinci!" yace da ita ataƙaice.

Duk da tasan cewa tayi latti, amma bazata taɓa iya faɗa masa hakan ba, batasan tayaya zata iya fara zama tare dashi ba, amma ya zatayi? Karasawa gaban dinning ɗin tayi tare daɗan durƙusawa. "Ina kwana!" tace dashi cikin sassanyar murya.

Kansa kawai ya kaɗa mata batare da ya amsa ba, aɗaɗare ta zauna akan ɗaya daga cikin kujerun dake dinning table ɗin. Food flask da kuma plate ɗin dake gabanshi ya turo mata, kana ya cigaba dashan tea ɗinsa, wayarsa ya ɗauka yasoma latsawa. Buɗe food flask ɗin tayi ta ɗan ɗibi abincin kaɗan, gaba ɗaya ta kasa sakewa taci abincin, jin kanta take atakure, duk abun da takeyi yana lure da ida ta gefen idanunshi, miƙewa tsaye yayi tare da ɗaukan suit ɗinsa ya sanya.

Saida ya ɗanyi tafiya kaɗan sannan ya tsaya, batare da ya juyo ya kalleta ba yace.
"Yau bazakije school ba kizauna agida" Baijira abun da zata ce ba yayi gaba abunsa.

Bata ɗauke idanu akanshi ba har saida yafice daga cikin falon.

"Yau bazakije school ba ki zauna agida"
Tamaimaita abun daya faɗa cikin ɗan nazari, kenan yana nufin tazauna agida kada taje makaranta? Babu mai amsa mata, hakan yasa ta ci gaba da tsakalan abincin. Bata wani ci abincin sosaiba tatashi ta koma ɗaki, uniform ɗinta ta cire sannan ta dawo falo ta zauna, ƙurawa tv idanu tayi tana kallon yanda ake koyar da girki.

***

Shikuwa yana fita daga falon direct wajen lafiyayyar motarsa ƙirar Range Rover Blue colour ya nufa, yana shiga Kamalu driver yaja suka fice daga cikin gidan. Yau meeting suke dashi a Transcop hilton saboda haka direct can suka wuce. Tun ƙarfe 9 da suka shiga meeting ɗin basu suka fito ba sai 11 daganan yawuce office.

Ziyada kuwa dake zaune agaban tv, duk wani abu da ake koyarwa na girki taɗaukeshi tsab akanta, hatta abun da tagani jiya a kitchine wani mai kamar kofi,(Blender) yau taga yanda ake amfani dashi, ashe abun markaɗe ne ita bata sani ba, suna gama koyar da girkin, suka sako wani film shine abun daya ƙara ɗauke mata hankali. Ba itane ta tashi agaban tv'n ba harsai bayan sallan Azahar. Kitchine ta shiga cike da karambaninta yau taci alwashin sai tayi girki.

Ruwa ta zuba atukunya cike da karambani ta kunna gas, duk abun da taga sunyi acikin tv'n ta riƙeshi yana kanta, ruwan na tafasa ta wanke shinkafa ta zuba, fridge ɗin dake cikin kitchine ɗin ta buɗe ta ɗibi kayan miya, saida ta wankesu sannan ta ɗauko irin abun da taga sunyi markaɗe aciki gaba ɗaya kayan miyan ta juye acikin blender tare da ɗaukanshi can ca ɗak takaishi gaban socket, kamar yanda taga sunyi haka itama tayi ta jona sa ajikin socket, ƙaran da taji yayi kaɗai saida ya kusa fasa mata ƙirji, don baka ɗan ba ta tsorata, can gefe ta koma tana ganin ya markaɗu ta siɗaɗo da ƙyar ta iya kashe socket ɗin, duba shinkafarta tayi taga ta nuna, haka ta sauke shinkafar batare da ta kashe gas ɗin ba, da sauri sauri ta juye markaɗen acikin wata tukunya sannan tasanya mangyaɗa akan markaɗen don ita agarinsu haka suke miyansu.
Baƙaramin jimawa tayi ba kafun ta samu miyan ya soyu mata, hmmm nan akeyinta sam batasan me zata sanyawa miyan don kashe mata tsami ba, haka ta zuba kayan haɗi ta rufe miyar, mintuna kaɗan ta kashe gas ɗin lokacin miyar tayi, komawa ɗakinta tayi tayi wanka, wata doguwar riga blue colour ta sanya mai kyau, rigan irin arebian gown ɗinnan ce, sosai ta amshi jikinta, zuciyarta fara tas ta nufi kitchine ɗin, daɗi takeji yau zataci abincinta, bata taɓa mantawa awasu lokuta da dama a ƙauye idan tayi girki babanta yaci yakan yaba girkin sosai, sannan ita kanta Inna Ma'u idan tanacin girkin har santi take, hakanne ma yasa aka sallama mata gaba ɗaya girkin gidan. Food flask ta ɗauka ta juye shinkafan aciki, sannan ta ɗauki plate ta zuba nata, miyan ma juyeshi tayi acikin wata kula gaba ɗaya kulolin takaisu kan dinning table ta ajiye..

Akan sofa ta zauna tare da ɗan ƙwashe ƙafafunta, cikin ɗari ɗari takai loman farko na abincin bakinta, saboda atunaninta miyan tayi tsami sosai, sai dai kuma koda taci abincin, ga mamakinta sai taji miyar batayi wani tsami sosai ba, hasalima mutum zai iyaci hankalinsa kwance. Sosai taci abincin tana kammalawa ta je kitchine ta wanke plate ɗin. Dawowa falon tayi ta zauna, tana zama tajiyo ƙarar horn ɗin motarshi, tashi tayi da sauri ta tafi jikin window ta ɗan leƙashi, yatsun hanunta tashiga murzawa aranta tana cewa.

"Allah yasa ya yarda yaci abincinnata"

(😆Lallai Sooraj zaici daɗi shinkafa da miya available, please waye zaizo aci shinkafarnan dashi😝.... Then saiku sani gobe fa babu update. Seriously i'am tired editing kaɗai yana bani headache)
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈KAINUWA WRITERS ASSOCIATION*

_{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}_
*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

#romance

*Chapter 19*

Tsaye take ajikin window tana mai jiran shigowanshi,  amma kuma sai dai ga mamakinta har anshare sama da mintuna 10 baishigo cikin faƙon ba, sake gyara tsayuwanta tayi,  tare da soma murza ƴan yatsun hanunta.    Buɗe ƙofar falon yayi ya shigo, yana mai ƙoƙarin cire suit ɗin dake jikinshi,  idanunsa ne suka sauƙa akanta, amma saiyayi saurin kawar da kanshi gefe, tare da ƙarasawa cikin falon,  aje suit ɗinnasa yayi akan kujera tare da cire agogon dake ɗaure atsintsiyar hanunshi,  gaban fridge yaje tare da buɗewa ya ɗauko goran ruwa, ɓalle murfin yayi tare da kaiwa bakinsa, saida ya tabbatar da cewa babu komai acikin goran,  sannan yayi wurgi da goran cikin dustbin, dawowa cikin falon yayi ya ɗauki suit ɗinshi kana ya nufi hanyar bedroom ɗinsa, gaba ɗaya ma yi yayi kamar baisan da zamanta acikin falon ba,  tana ganin shigewarsa cikin ɗaki.  Ta saki wani gauron  numfashi, sam bazata iya yi masa magana ba, kwarjininsa ya wuce gaba ɗaya tunaninta, sumu sumu haka ta wuce tayi ɗakinta.

Kwance yake acikin jakuzzie ɗinsa, wanda yasha haɗaɗɗen ruwan wanka,  daga kan ƙafafunsa zuwa ƙirjinsa, gaba ɗaya lume suke acikin ruwa, kansa da hannayensa ne kawai suke waje, yayinda kyawawan idanunsa suke alumshe, kana ya ɗan jingina bayan kanshi da jikin jakuzzie'n,  gaba ɗaya hankali da tunaninsa baya tare dashi,  sam kwana biyunnan baya cikin wata gamsashshiyar nutsuwa, tunani da damuwa sune abun da suka sakoshi gaba,  akullum kuma ako wacce rana jin kansa yake tamkar wani baƙon halitta, ya sani acikin rayuwarshi akwai tawaya sosai, amma kuma baison ya zamanto mai rauni saboda hakan,  baiso yazama ɗaya daga cikin irin mutanennan da basa iya riƙe damuwarsu,   shikansa ya sani da ace lafiyarshi ƙalau, to da bazai taɓa iya kai wannan lokaci mai tsawo haka, batare da mace akusa dashi ba, "Menene matsalarsa? mecece damuwarsa? meyasa baya iya zama da mace?" yasan duk waƴannan abubuwan iyayensa suna da buƙatar sani,  "Amma mai yasa basa tambayarsa?" wannan tambayar shi ne abun da yake tambayar kanshi akullum, baikamata don ya kasance Namiji su sakar masa ragamar rayuwarsa ba, duk da cewa ya girma amma tabbas yana da buƙatar kulawan Iyaye atare dashi.
Wani numfashi yaja tare da fesarwa alokaci guda,    wani irin tausayin kanshi yakeji, sosai yake tausayawa al'amuranshi,  baisan taya zai dubi wata mace yace yana sonta ba, haka kuma baisan wace macece zata iya zama ta jure lalurar shi ba,  bazai taɓa yaudaran kanshi ba, saboda yasan babu wata mace da zata iya jure zama dashi ayanda yake, musamman ma idan tasan ƙatuwar matsalan dake tare dashi, yasani  shi me raunine ako da yaushe, safe, dare, rana, babu wani lokaci da zaizo masa yana cikin farinciki da walwala,  sau da dama yakanji kamar yayita kuka, ko da zai samu salaman rage ƙuncin dake cikin zuciyarshi, saidai hakan

baya samuwa ayanzu, sakamakon zuciyarsa da tayi tauri, haƙoransa yasa ya ɗan ciji laɓɓansa da ƙarfi, shi kaɗai yasan me yake ji, haka kuma shi kaɗai yasan kalan ƙunci da yake ciki, sama da shekara 10 kenan da haske ya gujewa rayuwarsa, azahiri acikin haske yake rayuwa, amma kuma idan aka duba bayansa duhune dulum mai wuyar kalluwa. Cikin rashin kuzari haka yayi wanka, tare da ɗauro towel akan waist ɗinsa ya fito daga cikin toilet ɗin.
Zama yayi akan gado tare da ɗauko mayinsa ya soma shafawa, yana kammalawa ya feshe jikinsa da body spray mai daɗin ƙamshi. 3 guater jeans and white t-shirt ya sanya, laptop ɗinsa mai ɗauke da tambarin apple asaman murfin ya ɗauka, tare da ficewa daga cikin ɗakin. Aje laptop ɗin yayi akan rug tare da buɗe fridge ya ɗauko goran pepsi mai matuƙar sanyi. Zama yayi akan rug ɗin, tare da tanƙwashe ƙafafunsa, buɗe laptop ɗinshi yayi ya soma gudanar da aikinsa kamar yanda ya sabayi akowacce rana.
**
Ziyada kuwa komawa ɗaki tayi, tayi kwanciarta, harta fara bacci ta tuno cewa wulaƙanta abinci ba kyau, hakan yasa ta fito saɗaf saɗaf kan dinning ɗin ta nufa, abincin yana nan kamar yanda ta ajiye sa, ɗaukan kulan tayi ta fice daga cikin falon, direct wajen maigadi ta nufa nan ta sameshi zaune shida Kamalu driver suna hira, kulan abincin ta basu, duk da basusan menene aciki ba saida sukayi mata godiya, ita kuwa ta juya ta koma ciki. Zama Kamalu driver da maigadi sukayi, suka ci shinkafa da miyan, sam basuji wani abu na'alamar rashin daɗi acikin abincin ba, haka suka ci abincin sukayi nak.

*** ***

Washe Gari.

Tun kafun 7 yau ta kammala shirinta bayan tayi wankan tsarki, saboda tun jia da yamma bata ga komaiba, hakan yasa taji ajikinta cewa ta samu tsarki. 7 nayi suka bar gidan.
Zuwanta yayi daidai da zuwan Nasmah, nan suka zauna suka soma taɓa hira kafun Shukra tazo....

*** ***
Bayan sati biyu.

Alhamdulillah. Ayanzu sosai Ziyada take gane karatun da ake koyar musu, duk da cewa turanci har yanzu yana bata wahala, sannan kuma bata iya wani abu sosai daga cikinsa ba, amma duk da haka sosai take gane karatun, saboda kullum idan malami yazo yayi musu lecture yana fita Nasmah zata ƙara fahimtar da ita, yau suke shirye shiryen farayin test don haka daren jia, kusan kwana tayi tana biye karatun Maths ɗin da akayi musu, tun daga zuwanta har kama daga wanda akayi batanan, duk Nasmah tayi ƙoƙari wajen ganin ta koya mata.

Sunyi test ɗinsu lafiya, inda ko wanne ɗalibi dake cikin ajin yake sa ran cinyewa, ita ma Ziyada tayi ƙoƙari ƙwarai, domin kuwa acikin guestions huɗu da akace su amsa, ta samu ta amsa uku, kuma aranta tana sa ran cewa zataci duka ukun. Koda aka raba musu paper'n test ɗinnasu, ta samu six ɗayan da batayi ba kuwa tasamu zero, domin dama shine keda yawan

maki har 4 mark yake dashi, duk da haka ma taji daɗi sosai.

Kwana biyunnan gaba ɗaya basu da wani hutu ko acikin school, kullum cikin karatun test suke ga exams ɗinsu dake ta gaba towa, kasancewar exam ɗin third term ne, shi zai kaisu s.s 2, hakanne yasa gaba ɗaya hankalin ɗaliban dake cikin school ɗin atashe yake, domin kuwa matuƙar bakaci exam ɗin ba, to fa repeat ɗinka za ayi babu ruwansu dakai ɗan waye. Ɓangaren Ziyada kuwa abun ya haɗe mata sosai, domin kuwa ta dage tana koyan karatun da akayi baya kafun ta shigo, ga kuma wanda akeyi musu yanzu hakanne yasa gaba ɗaya brain ɗinta ta ɗauki charge, saidai kuma cikin ikon Allah da kuma tsananin nacin da tasanya aranta karatun yana zama akanta. Ayanzu kwata kwata ta daina haɗuwa da Sooraj, bata sanin fitarsa bata kuma sanin dawowarsa, duk da kuwa tsananin son ganinsa da take, amma hakan baya samuwa agareta. Agajiye ta ɗaura kanta akan kafaɗan Shukra wacce take ta faman latsa babbar wayarta. Ɗan kallonta Nasmah tayi tare da cewa.
"Badai kin gaji da karatun ba?"

"Nagaji mana Nasmah, zan bari sainaje gida kawai naci gaba!"

"Amma kinsan fa Monday zamu fara exam ko?" Shukrah tafaɗa tana me maida wayarta cikin jaka.

Murmushi Ziyada tayi tare da cewa "Har kingama shan soyayyan?"

Hararanta Shukrah tayi tare da cewa "Nifa wallahi kunsamin ido, hmm kawai don bakusan daɗin soyayya bane ba shiyasa"

"Daɗi? hmmm ina daɗi acikin wannan abar da kullum sai anbata miki rai? wallahi Shukra inaganin kawai wahalar dakanki kikeyi, s.s one kaɗai fa muke, amma wai ace ke har soyayya kike hmmm Allah ya kyauta!" Nasmah tafaɗi haka tana ɗan taɓe bakinta, ita sam wannan tsarin na soyayya baiyi mata ba, saboda ita atsarinta idan zatayi soyayya tafiso sai taje irin 2 hundred level ɗinnan.

"Hmm kwata kwata bazaki gane ba Nasmah, amma kema watarana nasan zakiji abun da nakeji!" Shukrah tafaɗi haka tana mai ƙoƙarin tashi tsaye daga zaunen da take.

"Ba abun da zan gane!" Nasmah tafaɗi haka cike da jin haushi.

Murmushi Ziyada tayi tare da sunkuyar da kanta ƙasa, haka nan tunaninsa ya faɗo mata arai, jitayi gaba ɗaya jikinta yayi sanyi, kallonta Shukrah tayi tare da cewa. "Muje ki rakani kinji share wannan abar" Still murmushi kawai tayi sannan tabi Shukrah suka tafi, Nasmah ma binsu tayi tace bazata zauna ita kaɗai ba, direct ɓangaren da ake koyar da girke girke dake cikin makarantar suka nufa, ƴan department ne dayawa awajen kowa yana baje basirarsa, gani tayi Nasmah tashiga itama ansoma bugawa da ita, tsayawa tayi daga gefe tana kallonsu, dukkan abun da sukeyi tana haddace shi akanta, sunjima awajen kafun suka koma class.

Koda ta koma gida gaba ɗaya bata wani samu sukuniba karatu ta dinga yi, har wayewar gari ta shirya tatafi makaranta, acikin ƴan kwanakinnan wani abu da ta fara fuskanta shine sauyawar da jikinta yasomayi, hips ɗinta ne taga sun ƙara faɗi, yayinda ƴan saffa saffan breast ɗinta suka ɗan ƙara girma, skin ɗinta ta sauya tayi wani fresh, ga kyawun da fuskarta take ƙarawa ako da yaushe, ita kanta sau da dama idan ta kalli kanta takanyi mamakin yanda kamanninta ke ƙara sauyawa. Tun ɗazu su Nasmah suka fita break suka barta, kasancewar bata ƙarasa note ɗinta da wuri ba, miƙewa tsaye tayi bayan ta kammala note ɗin, maida littafinta tayi cikin jaka tare da ficewa daga cikin ajin.

Wata haɗaɗɗiyar mota ƙirar benz ce ta kunno kai cikin makarantar. Adai dai kusa da parking space ɗin makarantar yayi parking motar, buɗe murfin motar yayi tare da zuro ƙafafunsa waje, cikin yanayinsa na nutsuwa yafito daga cikin motar, haɗaɗɗen saurayine mai kyau da gayu, ba fari irin tas ɗinnan bane, amma yana da nasa irin salon hasken, direct idan ka ganshi zaka ƙirasa da mai kyau, kasancewar babu laifi shima yana da nashi kyau'n, irin Handsome guy ɗinnan ne mai son ado da gayu, dogone amma basosai ba sannan yana da ɗan faffaɗan jiki, yana da wani kwantaccen sajen da yaƙarawa fuskarsa kyau, sanye yake da riga da wando na jeans masu kyau, yayinda ya rufe gashin kansa da facing cap blue colour. Cikin isa yake takunsa yana mai ɗan kaɗa key ɗin motarsa dake riƙe a hanunsa, direct office ɗin principal ya nufa. Ta baya baya take tafiya tana dariya yayinda Nasmah ke biyota da ɗan sauri sauri, ɗan juyawa tayi sam bata ankara ba, saiji tayi ta bugu da mutum yayinda kanta ya daki ƙirjin mutumin da ta buge, da sauri ta juyo tare da sanya hanu ta dafe goshinta cikin yanayi naɗan jin zafi tace. "Auchhh!!" Shima hanu yasanya ya dafe ƙirjinsa, daidai saitin inda kanta ya buga.

Ɗan zame hanunta tayi daga kan fuskarta, idanunsune ya sarƙe cikin na juna, ɗan matsawa baya tayi tare da sake kallonsa.
"Kayi haƙuri dan Allah bankula bane!" tace dashi cikin murya mai sanyi.

Murmushin daya bayyana dimples ɗinsa yayi mata tare da cewa. "Babu damuwa!" shima cikin sanyi yayi maganar, yana mai ɗan ƙara faɗaɗa murmushin dake kan fuskarsa. Raɓawa tayi taɗan gefensa ta wuce, Shukrah da Nasmah suka bita abaya. Kafeta da sexy eyes ɗinsa yayi har saida yaga shigarta class sannan ya ɗauke idanunsa, sannan ya juya ya nufi inda zashi.

Har ta zauna akan sit ɗinta tana dafe da goshinta, don taji zafin buguwar da tayi baɗan kaɗan ba.

Dariya Shukrah tayi tare da cewa "Wai miye hakan kike dafe da goshi sai kace wanda kika bugi dutse?"

"Ai inajin da dutse da shiɗin basu da maraba!" Ziyada tafaɗi haka tana mai ɗan mulmula goshinta.
Dariya su Nasmah suka sanya. "Dole zakiji zafi mana, daganinsa ai zaki san ma'abocin yin

gym" Shukrah ta faɗi haka tana mai ƙoƙarin murzawa Ziyada goshinta.  Malami ne ya shigo cikin ajin hakan yasa suka nutsu, tare da maida hankalinsu kansa. Kwana biyunnan duk ba atashinsu da wuri yau har 5:30 sannan aka tashesu.
**
Tana shiga cikin ɗakinta ta soma rage kayan jikinta, banɗaki ta shiga tayo wanka.  Riga da sket ƴan kanti ta sanya sannan taɗan yafa wani ɗan ƙaramin ɗan kwali akanta.   Direct kitchine ta wuce, duk wasu ƴan ƙananan girki yanzu babu abun da bata iyaba.    Indomie ta dafa bawai don tanaso ba saidon yunwan dake damun cikinta.    Gaba ɗaya kwanukan da suka ɗan yi ƙura a kitchine ɗin ta kwashe ta kai gaban sink wankesu tayi tas, sannan tayi mopping kitchine ɗin. Acikin kitchine ɗin ta zauna taci abincinta,  tana gamawa ta wanke plate ɗin data ɓata.    Zame ɗan kwalinta tayi ta ƙarasa gaban sink, hanu tasa ta tari ruwa ta wanke fuskarta,  tana maiƙoƙarin ɗaura ɗan kwalin tanufi hanyar fita daga kitchine ɗin, harta jefe ƙafarta na hagu acikin falon, da wani irin ƙarfi taji an jawota cikin kitchine ɗin tare da sanya hanu aka rufe mata baki gam.

(Kucigaba da haƙuri kuna manage lokacin dazan ƙara yawan typing yananan zuwa.
Vote da Comment ɗinku kawai nake buƙata please karkuna bani kunya seriously ina da buƙatar vote ɗinku sosai, because tananne kaɗai zangane kuna enjoying story'n.)

*VOTE Me On Wattpad*
@fatymasardauna
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈KAINUWA WRITERS ASSOCIATION*
_{United we stand and succeed; Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}_
*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

#romance

*Chapter 20*

Numfashinta ne yasoma ƙoƙarin ƙwacewa, saboda tsabar tsananin tsoron da ta samu kanta aciki, ƙasa tayi da idanunta, tana me kallon hanun da aka rufe mata bakinta dashi, hanun namiji ta gani, wanda ke ɗauke da kwantattun gargasa da sukayi luf akan farar fatarsa, jikinta ne ya ɗauki tsuma, wani irin tsoro mai ƙarfi ya ziyarceta, wani ɗan corridor dake cikin kitchine ɗin ya shiga da ita, ɗan sassauta riƙon da yayi mata yayi, ba tare da ya sake mata bakinta ba, ya juyo da ita suka zama suna fuskantar juna, idanunta ta zaro waje tana me sake kallonsa. Sake mata bakinta yayi, tare da ɗaura hanunsa akan laɓɓansa cikin ƙasa ƙasa da murya yace.
"Shiii!! kada kimin ihu, ina da baƙi a falo ki zauna anan kada ki fito" yana gama faɗan haka ya saketa, tare da juyawa ya nufi hanyar fita daga cikin kitchine ɗin, bakinta a wangale haka ta bisa da kallo har ya fice, wata irin ƙatuwar ajiyar zuciya ta sauƙe, tare da jingina bayanta da jikin bango, har acikin zuciyarta tayi bala'in tsorata, duk atunaninta wanine daban yazo saceta, hanunta ta ɗaura adaidai kan chest ɗinta dake ta bugawa da ƙarfi, aƙalla takusan mintuna 9 ahaka, kafun tasamu ta iya daidaita nutsuwarta, kan wani plastic chair dake cikin kitchine ɗin ta zauna, tare da kifa kanta akan cinyoyinta.

Shikuwa Sooraj yana barin kitchine ɗin, komawa cikin falo yayi, wajen abokan business ɗinsa, da suka kawo masa Ziyara, yana zaunene amma gaba ɗaya hankalinsa naga ƙofar kitchine, sam bayaso tayi gangancin fitowa, ba tsoronsa ganinta da zasuyiba, tsoronsa shine wani irin bahagon kallo za suyi masa? tabbas ba lallai suyi mishi kyakkyawan zato ba, shikuwa ko kaɗan bayason ayi masa irin wannan kallon. Sunjima suna tattaunawa akan business ɗinsu, kafun daga bisani sukayi masa sallama, har bakin motarsu ya rakasu, shima daga rakiyarsu bai dawo cikin gidanba, motarsa ya shiga ya fice daga gidan gaba ɗaya.

Jin anata ƙiraye ƙirayen sallan ne yasata takowa saɗaf saɗaf taɗan leƙa cikin falon, ganin ba kowa acikin falon yasa ta sauƙe ajiyar zuciya. Fitowa daga cikin kitchine ɗin tayi ta wuce ɗakinta.

*MONDAY*

Yau yakasance ranar da zasu fara exam, 8:00 am daidai zasu shiga exam ɗin inda zasu fara da Biology. Zaune suke akan wani bench su dukansu ukun, kallon Shukra da Nasmah Ziyada tayi murya asanyaye tace.
"Tun safe ƙirjina yaketa bugawa, wani irin tsoro nakeji, anya zan iya zana exam ɗinnan kuwa?"

Kallonta Shukra tayi tare da ɗanyin murmushi.
"Zaki iya mana, ki daure ki ƙarawa kanki confidence, amma ai babu wani wahala" Shukra tace haka cikin son ƙarawa Ziyada ƙarfin guiwa, shiru sukayi daganan basu sake cewa komai ba. Takwas na cika dai dai suka shiga jarabawa, 1 hour suka ɗauka suna rubuta exam ɗin, cike da jin daɗi Ziyada ta miƙa booklet ɗinta, sannan tafito daga cikin exams hall ɗin, tsayawa tayi ajikin wata bishiya tare da lumshe kyawawan idanunta, wani nishaɗi takeji acikin ranta saboda tana da yaƙinin cewa zata ci duka tambayoyin da ta amsa. Su Nasmah ne suka fito nan suka haɗe suka ci gada da hiransu, kasancewar yau paper biu zasuyi ƙarfe 10 daidai suka sake shiga wata jarabawan na Islamic. Suna kammala jarabawan kowa ya fara haramar komawa

gida, tsayawa tayi tare da dafe goshinta,  gaba ɗaya ta manta batace da Kamalu driver yazo ɗaukarta da wuri ba,  gashi yanzu sun gama exam kowa na ƙoƙarin ko mawa gida.   Kai tsaye ta nufi babban ƙofar gate ɗin makarantar.   Tana fita daga cikin gate ɗin ta soma kalle kalle, batasan ya zatayi ba don bata da wata mafita, gashi su Shukra sun tafi.  Wata baƙar motace tazo ta tsaya agabanta, hakan yasa ta ɗan ja baya.   Ahankali ya sauƙe glass ɗin windo'wn motar,  kyakkyawar fuskarsa ta bayyana wacce ke ɗauke da murmushi.

Kallonshi tayi tare da sauƙe idanunta ƙasa, tabbas bazata manta shiba shine wanda ta buge kwanaki.

Murmushi yakumayi tare da buɗe murfin motar ya fito, takowa yayi har zuwa inda take, murmushine akan fuskarsa wanda suka bayyana dimples ɗinsa.  "Tsayuwa acikin rana bai kamaceki bafa ƴan mata" yafaɗi haka yana me ɗan ɗaga kansa ya kalli sararin samaniya.  Ɗago manya manyan eyes ɗinta tayi, tare da sauƙesu akan fuskarsa.  Idanunsu ne suka sarƙe acikin na juna, murmushi yaƙara yi mata tare da cewa.
 "Mai kikeyi anan? ba'azo ɗaukarki bane?"

Samun kanta tayi ta kaɗa masa kai alamar "Eh"

"Okay muje na sauƙeƙi agida" yafaɗi haka yana me ƙoƙarin buɗe mata murfin motar, ɓangaren mai zaman banza.

Saurin kallonsa tayi tare da ɗan matsawa can gefe, sam batajin zata iya shiga motar, ita da batasan kowa ba banda MR. HANDSOME (Sooraj)  yaza ayi ta yarda ta shiga motar wani, kalan ma yaje ya sayar da ita. Abunda tafaɗa acikin ranta kenan.

Ganin alaman cewa bata yarda dashi bane yasanyashi sake ɗanyin murmushi cike da son ya gamsar da ita yace.  "Calm down dear, i will not hurt you, trust me!"

Yanzu kam salon kallon da tayi masa, yana ɗauke ne da ma'anoni masu yawa. Horn ɗin motar da taji abayanta ne yasata waigawa, ai kuwa Kamalu driver ta hango acikin mota, da sauri ta juya ta nufeshi, buɗe murfin motar tayi ta shiga,  ƙarasowa yayi har jikin motar,  sannan yayi knocking glass ɗin window, Kamalu driver ne yayi ƙasa da glass ɗin tare da ɗan dubansa, shikuwa idanunsa akan kyakkyawar fuskarta yake, cikin ƙasa da murya yace. "Yace kin ƙi yarda dani ko? ba damuwa ki kulamin da kanki!" yana gama faɗan haka ya juya ya nufi wajen motarsa.

Tafiya suke amma gaba ɗaya tunaninta yana ga maganan da ya gaya mata "Kikulamin da kanki!" mai hakan yake nufi kenan? tambayar da take ta yiwa kanta kenan gaba ɗaya kanta ya kulle, ahaka har suka isa gida.

Tsaye yake agaban drawer, dagashi sai dogon wando fari dake sanye ajikinsa, yayinda murɗaɗɗiyar surar jikinsa ta bayyana, gaba ɗaya shape ɗin bayansa abun burgewa ne.

Kayansa yake cirowa daga cikin drawer'n yana shiryawa acikin trolly bag ɗin dake aje kan gadonsa. yana gama shirya kayannasa ya ɗauki wata rubber t-shirt yasanya ajikinsa. Wata jaka ya ɗauko irin wacce ake goyawa a baya, buɗe jakan yayi ya zuba wasu takardu aciki, saida ya tabbatar daya haɗa komai nasa wanda yasan zai buƙata, sannan ya ɗauki wayarsa ya sanya acikin aljihunsa, direct falo ya nufa. Direct dinning area ya nufa, haɗa tea ɗinsa yayi, tare da dawowa cikin falon ya zauna. Sipping tea ɗin yake ahankali, yayinda lokuta zuwa lokuta ya ke kai dubansa ga agogon bangon dake cikin falon. 6 pm daidai jirginsu zai tashi. 5:40 ya kammala gaba ɗaya abubuwan da zaiyi, ɗaukan troly ɗinsa yayi tare da rataya jakarsa akafaɗansa, yana fitowa daga cikin ɗaki, dai dai lokacin ita kuma tana fitowa daga kitchine, sanye take da riga da wando na pakistan sai kuma hijab dake jikinta. Idanunsu ne ya sarƙe acikin na juna. Da sauri ya ɗauke kansa, ya nufi hanyar fita daga cikin falon, bin bayansa tayi da kallo harya fice daga cikin falon. Samun kanta tayi da kasa ɗauke idanunta daga bakin ƙofar fita daga falon, komai nasa abun burgewane, wasu irin hawayene suka cika idanunta, sannan suka samu daman fitowa alokaci guda. Jingina bayanta tayi da jikin bango, tare da ɗan cije laɓɓanta, akullum rayuwarta ta baya, ta zame mata abun tunawa, tunanin babanta ne akullum yake damun zuciyarta, tayi rayuwa cike da rashin gata da kuma ƴanci, ta taso cikin maraici, sam bata wani san menene daɗin mahaifiya ba, tun tana ƙarama mahaifiyarta ta rasu, har i'yanzu tana buƙatar sanin wacece ita, gaba ɗaya rayuwar da tayi abaya cike take da duhu, Maraici, Kaɗaici, da kuma Ƙunci su suka cika rayuwarta ta baya, babu wani wanda ya damu da ita, itake shanye damuwarta komai girmansa, ɗan zamewa tayi ta zauna daɓas akan tiles ɗin dake malale a wajen, lumshe kyawawan idanunta tayi, tare da soma murza ƴan yatsun hanunta. Ƙamshin turarensa da taji yana shiga hancinta ne, yasanya ta buɗe idanunta da suke cike tab da ƙwalla, ganinshi tayi tsaye akanta ya zuba mata idanunsa masu matuƙar rikitata.

Saurin ɗauke idanunsa yayi daga kanta, domin bazai taɓa iya juran kallon yanda ƙwayan idanunta ke cike da ƙwalla ba, envelop ɗin dake hanunsa ya miƙo mata, hanunta na rawa haka ta amshi envelop ɗin, shikuma ya juya ya fita, samun kanta tayi da kasa buɗe envelop ɗin jiki asanyaye ta koma ɗaki.

6:00 pm daidai jirginsu ya ɗaga zuwa sararin samaniya. Jingina bayanshi yayi da jikin kujeran da yake zaune, tare da lumshe idanunsa, wani tunani da yazo ranshi ne yasanyashi sakin murmushi, lokaci guda kuma ya haɗe fuskarsa tare da buɗe idanunsa da sukayi jajur dasu.

*** ***

Wasa wasa har sunyi sati ɗaya da fara exam, a ɓangaren Ziyada kuwa sai dai muce Alhamdulillah, domin kuwa tana amsa tambayoyin jarabawan da iyakayi mata, da duka iya ƙoƙarinta.

Zaune take a inda aka tanadar musu don cin abinci, kasancewar yau ta riga su Nasmah fitowa daga ɗakin jarabawan, yasa take zaune ita kaɗai, kanta ta kifa akan ɗan madaidaicin table ɗin dake gabanta wanda yake zagaye da kujeru.

Wani irin ƙamshin turarene yashiga kawowa hancinta Ziyara,    lumshe idanunta tayi tana mai shaƙan ƙamshin turaren batare da ta ɗago kannata ba.

Ahankali ya jawo kujeran dake fuskantar nata ya zauna.  Sexy eyes ɗinsa ya zuba wa ƴan yatsunta dake aje kan table ɗin.  Hakanan taji kamar akwai mutum akusa da ita, saboda hakane yasa  ta ɗan ɗago kanta, waro idanunta tayi cike da mamaki, duk da cewa aƴan kwanakinnan yaɗan matsa mata, amma kuma sam bata tsammaci ganinsa a wannan lokacinba.  Murmushi yayi mata tare da ɗage giransa sama.   "Surprise!"  yafaɗa yana me sake ƙarewa kyakkyawar fuskarta kallo.   Kawar da kanta gefe tayi tare da turo ɗan ƙaramin bakinta gaba.

"Idan kina cikin yanayi na damuwa kinfi kyau, but even at that, i don't want to seeing you in this situation, ki ɗan saki fuskarki kinji ƴan mata na!"  Ya faɗi maganar yana mai langwaɓar da kansa gefe tamkar wani ƙaramin yaro.  Yanayin yanda yayi maganar shine abun daya sanya ta ɗan juyo ta kalleshi,  irin kallon daya keyi mata ne ya sanya taji jikinta yayi sanyi.    Yana shirin sake yi mata magana ne wayarsa ta soma ringing alaman shigowan ƙira.  Ɗaga wayan yayi tare da karawa akan kunnensa,  baiwani jima yana wayanba ya kashe, tare da maida wayar cikin aljihunsa.  Miƙewa tsaye yayi, tare da ɗan ranƙwafowa dai dai fuskarta.  in a silent voice yace.  "Kina da kyau sosai, komai naki me kyau ne, zanyi baƙin ciki idan kika kasance saɓanin tunani na!!"  yana gama faɗin haka ya juya ya soma  tafiya, binsa tayi da kallo har ya ɓacewa ganinta.  Dai dai lokacin su Nasmah suka ƙaraso.  Shukrah na zama ta kwashe da dariya.  "Har angama shan love ɗin?" Nasmah tafaɗi haka tana mai ƙoƙarin gumtse dariyarta.
"Love kuma?" Ziyada ta tambaya.
Dariya Shukrah da Nasmah suka sanya tare da tafawa, ganin haka yasa Ziyada ci gaba da sabgoginta, domin ta sansu abu mai sauƙi ne su fassarata da wata manufar.

*** ***
LAGOS NIGERIA.

SOORAJ!!!

1:00 am, ƙarfe ɗaya na dare, kwance yake akan makeken gadonsa, wanda yaji zanin gado na alfarma.  Sanye yake da white pencil jeans ajikinsa,  bai sanya riga ba hakan yasa  gaba ɗaya surar jikinsa take abayyane, musamman ma sick packs ɗinsa, wanda suka samu daman kwantawa raɗau akan fatar cikinsa,  sama sama yake jiyo motsin mutane acikin kunnuwansa, ahankali ya buɗe idanunsa,  aikuwa nan ya tabbatar da cewa ba karya kunnuwannasa keyi masa ba, tabbas motsin mutanene acikin gidansa,  saƙƙowa yayi daga kan gadon tare da nufar ƙofan fita daga cikin ɗakin, ahankali ya murza handle ɗin ƙofar ya fita, taku uku kacal yayi ya samu kanshi a babban falon dake gidan,  hanu yasanya akan makunnin ƙwan wutan dake falon ya kunna, kunnawansa yayi daidai da sakar masa bullet  da akayi akan ƙirjinsa, wani ƙara yasanya sakamakon wani irin zafi da raɗaɗi da suka ratsa shi, tun daga ƙasan ƙafarsa harzuwa tsakiyar kansa,  kafun yayi wani yunƙuri ansake sakar masa wani bullet ɗin akan hannunsa, wani irin azabane yaji yana huda jijiyoyin jikinsa, yana ratsawa ta ƙwaƙwalwarsa,  take idanunsa suka soma rufewa,  wani irin abu yaji acikin jikinsa wanda bai taɓa jin irinsa ba, take yafaɗi

awajen baya ko motsi.

*(Kuyi haƙuri saida na gama typing ya goge gaba ɗaya, da ƙyar nasamu nayi wannan, nasan kuna fushi dani amma dan Allah kuyi haƙuri🙏🏻🙏🏻🙏🏻)*

*Vote Me On Wattpad*🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*
_{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain and motivate he mind of readers}_
*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

#romance

*Chapter 21*

Jini ne ke fitowa daga jikinsa yana malala akan white tiles ɗin da ya mamaye gaba ɗaya falon. Wasu ƙattin maza guda biyune suka fito daga maboyarsu, wato bayan labule kenan inda suka ɓoye, ko wannensu fuskarsa sanye take da mask, dukansu suna sanye da baƙaƙen kaya, sannan kuma kowannensu ahanunsa ɗauke take da bindiga, ɗan ranƙwafowa  ɗayan yayi tare da ɗaura hannunsa adai dai saitin hancin Sooraj, jin baya numfashine yasa ya kalli ɗayan ɗan uwannasa.  Alama yayi masa da ido akan su tafi aiki ya kammala,  babu wani ɓata lokaci, aƙagauce suka fice daga gidan..   10 minute da tafiyarsu saiga ƴan sanda har mota biyu.  Alhaji Ilyass (maƙocin Sooraj)  dake laɓe jikin gate ɗin gidansa, yana ganin ƴan sanda ya ƙaraso garesu haryana jin tuntuɓe, aruɗe yace.   "Yauwa ranka ya daɗe kun ƙaraso? Ni ne nan naƙiraku, tabbas naji ƙaran harbin bindiga awannan gidan har sau biyu, saboda haka duk yanda akayi babu lafiya!" yafaɗi haka yana me sharce gumin dake yankowa ta gaban goshinsa, gaba ɗaya atsorace yake, ƙiran ƴan sandan ma da yayi baƙaramin Jahadi yake ganin yayi ba, saboda tsorone cike fal aransa.

Cike da rashin tsoro haka ƴan sandannan suka rarrabu, kowanne daga cikinsu ya saita

kunamar bindigarsa, ƙiris sukejira su saki harsasai, haka sukayi cikin gidan Sooraj, ahankali suka tura ƙofar falon suka shiga, ganin bakowa acikin falon yasa suka shiga ƴan dube dube, yayinda wasu daga cikinsu suka nufi bedrooms ɗin dake cikin falon, ɗaya bayan ɗaya haka suka shiga suna dubawa, ɗaya daga cikin ƴan sandan ne idanunsa suka sauƙa akan jinin dake kwance ya daskare akan tiles, jawo ogansu yayi ya nuna masa jinin, aikuwa suna leƙa bayan kujera sukaga mutum yashe aƙasa, gaba ɗaya jini ya ɓata jikinsa, aɗan razane sukayi kanshi, daidai lokacin sauran ƴan sandan suka dawo cikin falon. "Sir gaba ɗaya fa mungama duba gidannan bakowa acikinsa" suka faɗa suna mai kallon Sooraj dake yashe aƙasa. Shiru ogannasu yayi tare da ciro wayarshi acikin aljihunsa ya danna ƙiran asibiti. Kallon sauran ƴan sandan yayi yace subi hanya duk wanda suka gani sukamashi. hakan kuwa akayi duk suka watse yazama saura mutane ƴan ƙalilan. Karar jiniyan ambulance ne yacika gidan. Ɗaukan Sooraj akayi aka sanyashi acikin ambulance ɗin, suka wuce asibiti.
Babban asibitin dake cikin garin Lagos suka wuce dashi, direct ɗakin bada taimakon gaggawa aka nufa dashi, duk da cewa basu da tabbacin cewa yana da rai ko bayidashi. Dr. Femus shine mutumin daya fara cire handglobes ɗin dake hanunshi, kallon sauran abokan aikinnasa yayi yace. "He is dead!" Jikinsune gaba ɗaya yayi sanyi, saboda haka suma suka soma ƙoƙarin cire handglobes ɗin dake hanunsu.

Dr. Fawwaz da bai yarda da abunda Dr.Femus yace ba, yaɗan matso gaf da Sooraj ɗin tare da kama hanunsa ya riƙe, sannan ya ɗaura kansa adai dai saitin ƙirjinsa inda zuciarsa ta ke. Da sauri ya ɗago da kansa tare da cewa "Bai mutu ba, zuciyarsa na bugawa, muyi sauri mucire masa bullet ɗin dake jikinsa!" nan suka duƙufa aikin cire bullet ɗin dake jikinsa. Sunyi masa gwaje gwaje sosai, inda suka tabbatar da cewa bai mutu ba, amma kuma su kansu basu san awani condition yake ba, abu ɗaya suka sani shine, zai iya wucewa tacan zai kuma iya tashi, duk wannan na Allah Ne. Duk abun daya kamata suyi mishi sun masa, sannan suka killaceshi awani ɗaki na musamman.
***
Gaba ɗaya ta hargitsa gadon, sai juye juye take, ta ya mutsa ko ina, gashin kanta gaba ɗaya ya watse akan gadon, yayinda ta sanya hanunta ta damƙi zanin gadon da iya ka ƙarfinta, duk da cewa sanyin ac na tashi acikin ɗakin, amma ita wani irin gumine ke fitowa daga jikinta. Arazane ta ware manya manyan idanunta da sukayi jajur dasu, tashi tayi ta zauna tare da dafe ƙirjinta dake bugawa da sauri. "Innalillahi wa'inna ilaihirraju'un!!" tafaɗa cikin wata murya me rauni, kawai saita samu kanta da fashewa da kuka, kuka tayi sosai wanda itakanta batasan na menene ba, aƙalla taɗauki kusan 40 minute tana kuka harsaida muryarta ta dashe, idanunta ne suka sakeyin jajur dasu, jin ana ƙiran sallan asuba ne yasata miƙewa ta nufi toilet, doguwar rigan dake jikinta ta cire tare da tsayawa agaban shower ruwa yashiga dukan ta, bazata iya tuna mafarkin me tayi ba, amma tabbas tasan taga wani abu wanda yake shirin taɓa rayuwarta, wani irin bacci tayi wanda adunia bata taɓa bacci marar ɗaɗinsa ba, MR. HANDSOME shine wanda tunaninsa ya kutso cikin rai da zuciarta, aƙalla ta ɗauki kusan sama da 15 minute tana tsaye ruwa na dukanta, da ƙyar ta iya ɗauro alwala tafito, domin gaba ɗaya bata jin ƙarfin jikinta.

Tsayawa tayi agaban madubi tare da kallon kanta, hanu tasanya ta shafi jajayen idanunta

wanda suke cike tab da ƙwalla,  ai kuwa take hawayen suka gangaro kan ƙuncinta, ita kanta batasan kukan metakeyi ba, kawai dai tasan tanajin ƙunci acikin zuciyarta, tanajin wani irin babu daɗi acikin ranta, tanajin wani ƙaton rauni ya rataya awuyanta,  gaba ɗaya tuna nin mai taimakone ga cika ranta,  gefe guda kuwa sosai takejin faɗuwar gaba, tana fatan kada wata mummunar ƙaddara tasake
samunta.     Sosai ta jima a raka'an ƙarshe tana kai kukanta ga mai duka, addu'a take kome zai sameta Allah Ya kawo mata shi da sauƙi.  Haka ta zauna akan sallaya har gari yayi haske, ko samun daman sake duba takardan jarabawanta ma batayi ba, gaba ɗaya jin kanta take acikin ƙunci.    Akullum cikin kuzari da ƙarfin jiki ta ke shirya kanta zuwa makaranta, amma yau hakanan take sanya uniform tunani fal ranta.  Jakarta ta saɓa akafaɗa tare da fitowa cikin falon, akullum ta saba haɗawa kanta break fast amma yau batajin zata iyacin komai.     Ba irin tambayan dasu Shukrah basuyi mata ba,  akan tasanar dasu abun dake damunta, amma  tace dasu sam batasan meke damunta ba.    Suna fitowa a exam ta tsaya ajikin wata bishiya,  tare da tsaida idanunta akan hanyar shigowa makarantar, hakanan tasamu kanta da son ganinsa, duk da cewa bawai ta wani damu dashi bane, amma yau da takejin kanta wani iri sai taji tanason ganinsa, tasan ko ma yaya zai iya cireta acikin ƙuncin da take ciki.  Har Kamalu driver yazo tana tsaye ajikin wannan bishian, Saidai kuma har zuwa lokacin  bata ganshiba kamar yanda taso, haka ta koma gida zuciarta ba daɗi.   Indomie ta dafa amma haka ta kasa ci, dole ta zauna jigum tana kallon TV....

LAGOS NIGERIA....

Ƴan sanda da kansu suka koma gidan Sooraj sukayi bincike, inda suka gano cewa shiɗin cikakken  ma'aikacin CBN ne, don haka direct branch ɗinsu dake Lagos suka nufa, BM ɗin wajen wanda yakasance tamkar aboki ga Sooraj,  shi suka samu suka sanar dashi gaba ɗaya abundake faruwa,  aikuwa baƙaramin tashi hankalinsa yayi ba,  koda yaje yaga halin da Sooraj yake ciki tamkar gawa, saida ya zubda ƙwalla, nan yaƙira wayan Mas'oud yasanar masa komai da komai, ai Mas'oud tamkar wani zararre haka yazama, wani irin mugun tashin hankali yasamu kanshi aciki, batare daya sanar dasu Abban Sooraj ba ya hawo jirgi yataho Lagos.

Kallon Mas'oud Babban likitan asibitin yayi tare daɗan gyara zamansa yace.  "Inaga basai anfita dashi waje ba ae, amma tunda ka matsa zaku iya fitar dashi, saidai kuma dole muna buƙatar ku ƙara mana sati ɗaya, idan baidawo cikin hayyacinsa ba shikenan sai ku fita dashi"

Shiru Mas'oud yayi tare da sanya hanu ya kama kanshi, adunia ayanzu babu wani mutum dayake tausayi sama da SOORAJ.  Cikin cushashshiyar muryarsa yace.  "Shikenan Dr. Babu damuwa Allah dai ya bashi lafiya!"     da "Ameen" doctor ɗin ya amsa nan sukayi musabaha, Mas'oud ya nufi ɗakin da Sooraj yake kwance, duk da ba abarin kowa ya shiga, amma zaka iya hangoshi ta glass ɗin window'n ɗakin.  Tsayawa yayi ajikin window tare da sauƙe idanunsa akan Sooraj wanda yake kwance flat, bazaka taɓa cewa akwai rai ajikinsaba, saidai na urar dake jikinsa  kawai dake aiki,  wani irin hawayene suka cika idanun Mas'oud, har baisan sanda suka silalo kan ƙuncinsa ba.  "Wani irin ƙaddarori masu girma ne haka suke ɗawainiya da RAJ? yaushe RAJ zai huta? yaushe RAJ zaiyi dariya yayi farinciki kamar kowa? yaushe damuwar

RAJ zata yaye?" abun da Mas'oud yake ta tambayar kansa kenan, tausayin SOORAJ yakeji mai tsanani, ayanzu baisan da wani baki zai iya furtawa iyayen Sooraj wannan mummunar labarinba, yace musu ɗansu yana cikin halin rayuwa ko mutuwa, ko kuwa yace musu ɗansu yazama marar amfani, ya zamanto tamkar gawa. Hanu yasanya ya share hawayen dake kan fuskarsa, aransa yaci alwashin nemo duk wani wanda yake da hanu akan harbin SOORAJ, wayarsa dake ƙara ya ciro ya duba, ganin commisioner'n ƴan sanda ne ke ƙiranshi, yasanyashi fita daga cikin asibitin baki ɗaya bayan ya ɗaga wayar ya kara akan kunnensa.
***
Zaune take akan wani ɗan dakali, yayinda shi kuma yake tsaye abayanta, ɗan ranƙwafo da kansa yayi daidai saitin kunnenta ahankali yace.
"Sau ba adadi na faɗa miki banaso ina ganin damuwa akan fuskarki" yaƙare maganar yana mai zagayowa ya zauna aɗan kusa da ita.

Raunannun idanunta ta ɗago ta kalleshi, ga mamakinsa sai kawai yaga hawaye sun gangaro daga cikin idanunta. Jiyayi wani abu ya soki zuciarsa, lumshe sexy eyes ɗinsa yayi tare da buɗesu alokaci guda.
"Menene?" yatambayeta cike da kulawa. Samun kanta tayi da cusa kanta acikin cinyoyinta ta fashe da kuka. Hankalinsa ne yaji ya tashi, cikin yanayi na rashin jin daɗin kukannata yace.
"Meke damunkine Baby? wani abu ya samekine? ko wanine ya taɓaki? ko kuma anɓata ranki ne? please dear na faɗamin meke damunki!!" yayi maganar cike da tsantsar nuna kulawarsa gareta.

Ɗago kanta tayi tare da turo ɗan ƙaramin bakinta gaba, ita kanta batasan awani yanayi take ciki ba, batasan meke damunta ba, hakan kawai tasamu kanta da cewa "Yayana ne, yau kusan kwana 10 banganshiba, kuma sannan inayawan jin faɗuwar gaba, inaso naganshi, bansan ina zanganshi ba!" wasu sabbin hawayene suka sake gangarowa daga cikin idanunta.

Ɗan kafeta da idanunsa yayi tare da ɗan yin murmushi, hakanan yanayin yanda tayi maganar ya burgeshi, yanason mace mai shagwaɓa sosai. "Kiyi haƙuri kinji Baby na, very soon yayanki zai dawo gareki"

Ɗago idanunta dake cike da ƙwalla tayi ta kalleshi, shima kallon nata yake, cikin wani irin yanayi dayake matuƙar kashe jikin mace, janye idanunta tayi daga kansa, tare da sunkuyar da kanta ƙasa, wasa ta shigayi da yatsun hanunta, aranta tunanin mai taimako ne kawai ke yawo, duk bayan kowani bugun zuciarta ɗaya da tunaninsa take tafiya. "Ziyadah!!!" yaƙira sunanta cikin wata cool voice. Da sauri ta kalleshi cike da mamaki haɗi da yarinta tace.
"A ina kasan sunana?"

Murmushi yayi tare da cewa "Kamar yanda shaƙan numfashi da fitarsa keda matuƙar mahimmanci haka sanin sunanki yake da mahimmanci a wajena, saidai kuma ke ko sau ɗaya baki taɓa tambayar nawa sunan ba why?"

Wani murmushi tayi tare da cewa "To meye sunanka?"

Dariya yayi harsaida fararen haƙwaransa suka bayyana, sosai tambayar tata ta basa daria. "Sunana FAROUK YUNUS HAMMA ni haifaffen ɗan garin Kano ne, domin har yanzu iyayena acan suke, aiki ne ya kawoni Abuja, ina zaune a unguwar Wuse zone 2, ke kuma sunanki Ziyadah kina zaune a unguwar Asokoro, iya abunda nasani akanki kenan"

Dariya Ziyada tayi tare da kallonsa. Shima kallonnata yayi, miƙewa tayi ta soma tafiya batare da tace dashi komai ba, da kallo ya bita harta ɓacewa ganinsa, ajiyar zucia ya sauƙe tare da lumshe idanunsa, yanason komai nata, musamman ƴan saffa saffan cute lips ɗinta masu kyau, ya ɗan jima awajen kafun ya tashi ya shiga motarsa ya tafi......
***
Mas'oud ne keta kai kawo atangamemen falon Alhaji Mai Nasara, gaba ɗaya baya cikin nutsuwarsa, baisan ta ina zai fara ba, baisan taya Alhaji Mai Nasara zai ɗauki maganarsa ba. "Mas'oud yana ganka a atsaye? Bismillah kazauna mana" Inji cewar Alh. Mainasara, da fitowarsa kenan daga cikin ɗaki. Jikin Mas'oud na rawa haka ya zauna akan kujeran tare da sanya hanu ya dafe kanshi.

⚠️NOT EDITED

(Kuyi manage banda enough charge)

*VOTE AND COMMENT*
@fatymasardauna🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*
_{United we stand and succeed; Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}_
*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

#romance

*Chapter 22*

Jikin Mas'oud na rawa haka ya zauna akan kujeran, tare da sanya hanu ya dafe kanshi.

Kallonsa Alhaji Mansur Mai Nasara yayi tare da cewa.  "Yanayin ka kaɗai ya tabbatarmin da cewa ba lafiya ba Mas'oud, meke faruwa? wani abu yasamu SOORAJ ne?" Alhaji Mansur Mai Nasara ya tambayi Mas'oud, fuskarsa cike da  damuwa.

Shiru Mas'oud yayi ya kasa cewa komai.   "Tabbas akwai matsala kenan" Inji cewar Alhaji Mansur.

Kai Mas'oud ya kaɗa alamar "Eh"

"Sooraj ne?" ya kuma tambaya.

Kai Mas'oud yasake kaɗawa alamar "Eh"

Hanu Alh.Mansur Mai Nasara yasanya ya dafe daidai saitin zuciyarsa, da ke ɗanyi masa zafi, gaba ɗaya acikin kwanakinnan haka yakejin faɗuwar gaba na ruskarsa, sannan gefe ga Ummu (Hajiya Sulaimiya) ta sameshi da zancen cewa tana yawan mugayen mafarkai akan ɗanta Sooraj.  Lallai tun da yaga Mas'oud a birkice haka, yasan matsalan babbace.   Hular kansa ya cire tare da ajeta agefe, har fargaban tambayar Mas'oud ɗin yake wani hali Sooraj din ke ciki, Sooraj shi kaɗaine ɗansa, sannan kuma yana matuƙar sonsa, sam bayason wani abu ya samu Sooraj, baisan yazaiyi ba, shi ya haifi Sooraj amma baisan Sooraj wani irin mutum bane, komai nasa aɓoye yake,baya bayyana duk wani sirrinsa. kullum cikin ƙunci da damuwa zaka ganshi, ada suna tunanin rashin zama da mace shine  matsalarsa, amma da sukayi masa aure, sai suka ga ashe wannan bashine matsalarsa ba.

"Abba akwai matsala, Sooraj yana asibitin Lagos baida lafiya,  hari aka kai masa a gidansa dake Lagos!" Mas'oud ya faɗi haka idanunsa suna mai cikowa da ƙwalla.

Arazane Abba yatashi daga zaunen dayake, tare da rumtse idanunsa. Muryarsa amatuƙar raunane yace.  "Kada kacemin wasu sun cutarmin da Sooraj, Mas'oud, zan iya jure komai, amma banda labari mummuna akan Sooraj, sun kashemin shi ko? " idanun Alhaji Mansur tuni sun ciko da ƙwalla.

"Ka kwantar da hankalinka Abba, Sooraj bai mutu ba kawai dai yana da buƙatar kulawarku ne ayanzu" Mas'oud yafaɗi haka yana mai ɗan share ƙwallan daya zubo daga cikin idanunsa.

"Kayi mana booking flight Mas'oud, amma banaso Ummu ta sani, yau zamu tafi Lagos" Alh. Mansur yafaɗi haka cike da damuwa.

Gaba ɗaya Alh. Mansur baya cikin nutsuwarsa, hankalinsa atashe yake sosai, baisan awani hali zaije ya taradda tilon ɗansa ba.  Babban damuwarsa ma itace Ummu, tabbas yasan idan Ummu taji to dole sai ciwonta ya tashi.
***
Yau aɗan acikin nishaɗi ta dawo gida, domin kuwa kwana biyunnan sosai Farouk ke ɗan ɗebe

mata kewa, babban abun dayasanya ta shaƙu dashi, shine irin yanda yake kawar mata da damuwarta, yana sakewa da ita sosai, sannan kuma yana bata dukkan kulawansa, ako da yaushe yakan kashe ayyukansa yazo gareta, hakan yasa tayi sabo dashi.
Gobe zasu kammala jarabawansu, sannan kuma agoben za'a basu hutu. Fitowarta awanka kenan ta sanya wata doguwar riga ja, kitchine ta wuce, tsaye tayi agaban gas tare dayin shiru, damuwarta ne ta dawo sabuwa fil. Motsinsa takeson ji acikin gidan, rashin jinsa da kuma rashin ganinsa yana damunta sosai, tanason koda ƙamshinsa ne taji, hakanan takeji ajikinta cewa baya lafiya. Cikin rashin daɗin rai haka ta soya indomie taci sama sama. Tunda tayi sallah take aikin duba littafin Physics da zasuyi gobe. Kamar kullum idan ta kwanta mafarkinsa kawai take, yauma hakance ta kasance domin kuwa gaba ɗaya shitake ta gani acikin mafarkinta, yanayin halin da take ganinsa acikin mafarkin sam baya mata daɗi.

Ƙarfe goma daidai suka fito a exams, direct wajen assembly suka nufa. Hutun 3 weeks kawai aka basu, duk da haka ɗaliban sunji daɗi sosai.

Cikin sanyin jiki ta ɗago idanunta ta kalli Farouk wanda shima kallonta yake, gaba ɗaya idanunsa sunyi wasu narai narai dasu, harshensa yasanya ya ɗan lashi kan lips ɗinsa. "Banason wannan hutun, kwata kwata banason duk wani abu da zai nesantani da ganinki pretty na, da gaske nake inasonki har acikin zuciyata!!" jin sauƙar kalaman nasa acikin kunnuwanta, ya sata jin tamkar aradu ce ta sauƙa, idanunta dake kan fuskarsa ne suka kawo ƙwalla, "So......na!!" tafaɗa murya asarƙe..

Kallonta shima yayi cikin wani irin yanayi, ɗan matsowa kusa da ita yayi, tare da kai hanunsa ya kama nata hanun. "Nasan ke ƙaramar yarinyace, sannan kuma bakisan menene so ba, dan inasonki bawai yana nufin zan cutar dake bane, ban taɓa jin soyayyar wata mace azuciyata kamar yanda nakejin taki soyayyarba, Inasonki Ziyadah, dan Allah Kada ki ƙini, tun ran da naganki nakamu da Sonki, har abada kuma zan ci gaba da sonki, namiki alƙawari bazan taɓa rabuwa dake ba!!" Yaƙare maganar cikin wata murya mai sanyi, yayinda gaba ɗaya yanayin idanunsa suka sauya. Hawayene suka gangaro daga idanun Ziyada, karo na farko arayuwarta da wani yafurta mata kalmar SO, karo na farko arayuwarta da wani namiji ya tsaya yayi mata magana cikin kulawa har haka, saidai kuma sam bata fahimci kalamansa ba. Ganin yanda hawaye yake fita daga idanunta ne ya sanyashi, kai hanunsa fuskarta da niyyar share mata hawayen, da sauri taja da baya, tare da ƙwace hanunta dake cikin nasa. Juyawa tayi cikin yanayi na gudu gudu sauri sauri tabar wajen, ƙiran sunanta Farouk yake amma ko waiwayosa batayi ba, balle yasa ran tsayuwarta, ajiyar zuciya mai ƙarfi ya sauƙe, tare da lumshe idanunsa da suka soma sauya kala, har acikin jininsa yana jin son yarinyar, komai nata me kyau ne, kallonta, tafiyarta, nutsuwarta, sau babu adadi yakan samun kansa cikin wani irin yanayi idan yana tare da ita, da ƙyar ya iya shiga motarsa yabar cikin makarantar.

Ziyada kuwa direct inda su Nasmah ke zaune ta nufa, tana zuwa ta faɗa kan cinyar Shukrah, tare da rumtse idanunta.

Kallon kallo Nasmah da Shukra suka shiga yiwa juna, cike da tsantsar kulawa suka haɗa baki

wajen tambaryarta.  "Lafiya Ziyada? meke damunki?"  duk waƴannan tambayoyin sunyi mata shine alokaci guda.

Ɗago kanta dake kan cinyar Shukrah tayi, gaba ɗaya hawaye ya ɓata mata fuska.     Ganin haka yasa suka ƙara ruɗewa.

"Kuka Ziyada, meke faruwane?" Inji cewar Shukra dake ƙoƙarin share mata hawaye.

Kanta taɗan girgiza cikin muryarta mai ɗauke da rauni tace.  "Bansan me yake nufi ba Shukra, bansan menene So ba, bansan ya akeyinsa ba, gaba ɗaya ya juyarmin da tunanina, dan Allah Shukra ki faɗamin menene SO?" taƙare maganar tana mai sakin ɗan guntun hawayen dake maƙale cikin idanunta.

Ajiyar zuciya Shukra tayi tare da ɗanyin murmushi.   "Dama nasan haka zata faru Ziyada, saboda tun randa yasake dawowa nasan ya kamu da sonki ne,  So ba ƙarya bane ba Ziyada, akwaita azuciyar kowa, kuma sannan Allah Ne ke halittarta aduk inda yaso akuma lokacin da ya so, zaki gane kin kamu da son mutum ne kaɗai,  ta hanyar yawan tunaninsa,  yawan damuwa dashi, zai dinga faɗo miki arai aduk wani halin da kike ciki, ƙunci, ko daɗi, amma ni aganina Farouk baida aibu, domin irin Farouk ko wacce mace zataso yin soyayya dashi, gayen yayi tako ina" Shukra taƙare maganar tana sakin murmushi.

Jin kalaman Shukra yasanya jikin Ziyada yin sanyi, hakan yasa ta juyar da kanta gefe, gaba ɗaya kalaman Shukra sun ɗaure mata kai, musamman ma inda tace wai "Idan kanason mutum zakana yawan tunaninsa, sannan zaina faɗowa ranka ako da yaushe"       "Me taimako" shine sunan data fara ambata acikin rai da zuciyarta.  Da sauri ta girgiza kanta,  sam bazata taɓa sakewa tasoma wannan banzan wasan dashi ba,  shi cikekken namiji ne, wanda haɗuwa da kyawunsa har sun wuce gaban kwatance,  tayama za'ayi tasoma wannan banzan wasan akansa, kawai dai saboda ya taimaketa ne, yasa takejinsa har acikin jikinta,  amma idan ba haka ba ita wacece  da har tunaninsa zaina damunta? duk wuya duk daɗi bazata taɓa manta wacece ita ba, Ƙasƙantacciya, wacce bata da wani gata, wacce tataso cikin talauci da maraici. Lumshe gajiyayyun idanunta tayi, tare da sanya hanu ta tallafi ƙuncinta.  Tanajin su Nasmah da Shukra suna hira, amma takasa sa musu baki, ahaka har Kamalu driver yazo ɗaukarta, cike da kewar juna tayi sallama da su Nasmah. Ko acikin mota jigum tayi gaba ɗaya damuwowi sun cika zuciyarta.

Lagos Nigeria.

Kuka sosai Alh.Mansur yayi alokacin dayaga yanda ɗansa Sooraj ya dawo,  gaba ɗaya ba abanbanceshi da gawa, domin kuwa har yanzu baisan inda kansa yake ba.  Gaba ɗaya yashiga damuwa, duk da cewa sosai likitotin suka dage wajen ganin sun bawa Sooraj ɗin kulawa.  Waya Alh. Mansur yayiwa babban abokinsa Dr.Mohd  dake aiki ababban asibitin Abuja, Dr.Mohd ƙwararren likitane wanda yasan aikinsa, domin kuwa aduk Abuja shine babban likita,   maganar da sukayi da Dr. Mohd ne yasanya Alh.Mansur yi musu booking flight,  ƙarfe 6 na yammaci

daidai jirginsu ya ɗaga zuwa sararin samaniya.
Koda suka isa Abuja Kamar gawa haka aka shiga da Sooraj Intensive Care Unit.

Jigum haka Abba ya zauna, tare da sanya hanu ya dafe kansa.  Gefensa Ummu ce wanda tabiyo flight daga Kaduna tazo, kuka take sosai, Abba yayi rarrashin duniya amma sam taƙiyin shiru.

Tafe yake yana tuƙa mota, amma gaba ɗaya hankalinsa baya tare dashi, tunani yake akan abunda zuciyarsa ke raya masa, har azahiri yana ganin hakan shine daidai.

Zaune take akan rug ta nannaɗe ƙafafunta, farcen ƙafanta take yankewa, amma azahiri hankali da tunaninta yana wani waje.  Jin ana ƙoƙarin buɗe ƙofar falonne yasa ta ɗago kanta da sauri, Dai dai lokacin Mas'oud ya buɗe ƙofar ya shigo bakinsa ɗauke da sallama.  Ganin Mas'oud yasata tashi tsaye da sauri, murya asanyaye ta amsa sallaman nashi.  Zama yayi akan ɗaya daga cikin kujerun falon, yana mai ɗan ƙare mata kallo

Gaisheshi tayi cikin murya me sanyi,  fuskarsa aɗan sake ya amsa mata, kitchine ta shiga ta ɗauko cup, sannan ta buɗe fridge ta ɗauko masa ruwa,  akan glass stull ɗin dake gabansa ta ajiye ruwan. Tana shirin komawa ɗaki taji yaƙira sunanta "Ziyadah!"

Tsayawa tayi cak tare da ɗan juyowa takalleshi "Na'am" ta amsa masa murya asanyaye.

"Ɗauko mayafinki kizo akwai inda zamuje" Yafaɗa yana mai ɗan kurɓan ruwan da ta kawo mai.

"To" tace murya asanyaye. Sannan ta wuce ɗaki, jigum tayi tana mai tunanin ina zasu, wata zuciyarne tasoma ƙoƙarin kawo mata wani mummunan tunani, hakan yasa tayi saurin ɗaukar lufayanta tasanya, tare da ɗaukan takalmi flat shoe ta zura aƙafafunta, lokacin da tafito falon a tsaye ta sameshi yana ta kaikawo da alama yana cikin damuwa.

Yanaganinta yace "Yauwa muje ko"  haka suka fito yana gaba tana biye dashi abaya,  gani tayi ya tsaya yanawa me gadi magana , hakan yasa taɗan tsaya itama agefe.

Tafiya suke babu wani wanda yace da ɗan uwansa wani abu.   Har saida sukayi nisa da gidan kafun yaɗan rage gudun motar, kallonta yayi tare da cewa.  "Inaso daga yanzu ki fara amsa sunan ƙanwata,  SOORAJ baida lafiya yana asibiti yanzu haka, nasan yana da buƙatar kulawanki adaidai wannan lokacin, please Dan Allah  Ziyada ki kula da Sooraj, shiɗin mai rauni ne akowani ɓangare, kulawarki kaɗai yake da buƙata"

Ji tayi gaba ɗaya jikinta yayi sanyi, yayinda idanunta suka cicciko da ƙwalla, damuwa ƙarara ta bayyana akan fuskarta, duk da batasan asalin sunansa ba , amma jikinta ya bata cewa SOORAJ shine me taimakonta. Har suka isa babban asibitin bata sake cewa komai ba, saidai gaba ɗaya bata da natsuwa.  Haka suka shiga cikin asibitin jiki asanyaye, direct wani ɗan ɗaki suka nufa,  suna shiga Mas'oud ya durƙusa tare da  sake gaishe da su Abba da Umma, Abba

ne kaɗai ya iya ƙarfin halin amsawa domin Ummu kam Kuka take har yanzu, cike da ladabi Ziyada ta durƙusa har ƙasa ta gaidasu,   Abba ya amsa yana me kallonta, sai alokacin Ummu dake kuka ta ɗago kanta ta kalli Ziyada.    Ganin irin kallon da Ummu keyiwa Ziyada yasa Mas'oud cewa.
"Amm Abba dama wannan ƙanwatace ƴar Baffana ne dake Sokoto, tana karatune anan, sannan kuma suna da kyakkyawan alaƙa tsakaninta da Sooraj, shine nace mai zaihana tazo tana tayaku kula dashi tunda yanzu sunyi hutun makaranta"  Yaƙare maganar yana ɗan sosa bayan kanshi, domin shi kansa yasan ya shiryota.

Ajiyar zuciya Abba ya sauƙe tare da cewa "Tabbas hakan da kayi ka kyauta Mas'oud, domin dama kaga zaman Ummu'nku anan bazai yi wuba, saboda tunda tazo kuka take, nikuma banason kukannan!" Abba yafaɗi haka cike da damuwa.

Ɗan ɗagowa Ziyada tayi ta kalli wacce ake ƙira da Ummu, tsananin kaman da tagani na me taimako akan fuskar matar shiya sanya tayi tunanin ko mahaifiyarsa ce, to amma idan da yana da iyaye aida tasan bazai zauna agidansa shi kaɗai ba,  dole ne zai zamana iyayensa suna tare dashi.

Kallon Ziyada Ummu tayi sosai, wani tunanine yake ɗarsuwa  acikin ranta,  bazatace bata yarda da maganganun da Mas'oud ya faɗa ba, amma ita ta haifi Sooraj tasan kusan gaba ɗaya halayyarsa, mutumin da bayason mu'amala dako wacce irin mace yau shine za'ace wai akwai kyakkyawar alaƙa atsakaninshi da wata?.

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*
_{United we stand and succeed; Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}_
*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

#romance

*Chapter 23*

Abba da Mas'oud ne suka tashi suka fice daga cikin ɗakin, kasancewar alokacin har ansoma ƙiraye ƙirayen sallan Magriba. Ummu ne tafito daga toilet ɗin dayake cikin ɗakin, fuska da hannayenta duk ruwa da'alama alwala tayi.

Kallon Ziyada dake zaune jigum tayi. "Jekiyi alwala" Ummu tafaɗa tana mai ƙoƙarin shimfuɗa darduma akan tiles. Sumu sumu haka ta wuce toilet ɗin ta ɗauro alwala, hanu tasanya acikin hijab ɗin dake jikinta, ta zaro ɗan kwalin dake kanta, shimfiɗawa tayi akan tiles, sannan ta hau tare da daidaita tsayuwarta, akan ɗan kwalin ta gabatar da sallan Magriba, ko da ta idar da sallan, samun kanta tayi dayin shiru, tare da jingina kanta da jikin bango, gaba ɗaya jin zuciyarta take babu daɗi, babu wani abu da takeson gani sama da Helper ɗinta, sosai hankalinta yake atashe, sannan gefe guda kuma, ga kukan da taga mahaifiyar Sooraj ɗin nayi yasake ɗaga mata hankali.

Dukansu daga ita har Ummu babu wacce tatashi daga kan abun sallanta, har aka ƙira sallan isha, baga Ummu kaɗai ba hatta Ziyada saida tasanya Sooraj cikin addu'anta. Ƙoƙarin ɗaura ɗan kwalin kanta take, aka turo ƙofar ɗakin aka shigo. Alh.Mansur ne dakuma Mas'oud, Mas'oud ne ya aje basket ɗin dake hanunsa, tare da kai dubansa gareta.

"Ziyada ki zubawa Ummu abinci taci, kema ki ɗebi naki kici, zuwa anjima likitotin sun tabbatar mana da cewa zamu samu ganinsa!" Mas'oud yaƙare maganar cike da ɗan yanayi na damuwa. Alh.Mansur kuwa kasa ma cewa komai yayi, zama kawai yayi akusa da Ummu tare dayin shiru.

Ɗaukan basket ɗin Ziyada tayi tare da zaro wasu plate, kulan dake cikin basket ɗin ta buɗe tare da sanya spoon ta zuba lafiyayyar jalop rice wacce taji bushashshen kifi acikin plate ɗin. Cike da ladabi ta ƙarasa gaban Ummu, cikin muryarta dake rawa tace. "Ummu ga abinci"

Kai Ummu tagirgiza cike da damuwa tace.
"Banajin zan iya cin abinci batare da na sanya ɗana a idanuna ba, kici kawai!" gaba ɗaya muryar Ummu rauni kawai take bayyanawa.

Hanun Ummu Alh.Mansur ya kamo, cike da tsananin so da kuma nuna kulawa ga matartasa yace. "Ki kwantar da hankalinki Sulaimiyya, Isha ALLAH Sooraj zai samu lafiya, addu'an mu kawai yake da buƙata bakomaiba, kibar kukannan haka kuka banaki bane." Kallon Ziyada yayi tare da cewa.

"Miƙomin abincin nan na bata" karɓan plate ɗin abincin Abba yayi yashiga lallaɓa Hajiya Sulaimiyya akan taci, amma gaba ɗaya ta daburce taƙi ci, hawayene kawai ke silalowa daga cikin idanunta, shima kanshi Abban ƙarfin hali kawai yake amma damuwane ninke aƙasan ranshi.

Gaba ɗaya itama Ziyada kasa cin abincin tayi, lomanta uku ta ture plate ɗin abincin gefe, ji tayi ko kallon abincin batasonyi, hawayene suka ziraro daga cikin idanunta, da sauri tasanya gefen

hijabinta ta share,  tausayin halin da taga Iyayensa aciki take, musamman yanda taga hawayen mahaifiyarsa ya kasa daina zuba,  jitayi gaba ɗaya zuciyarta ta karye..
Da ƙyar Abba yasamu Ummu taci 4 spoon na abincin.   Dr.Mohd ne dakanshi  turo ƙofar ɗakin ya shigo.   Cike da tausayawa ya dubi dukkaninsu, da sauri Alh.Mansur yataso daga zaunen da yake yana cewa.

"Dr.Mohd ya dai, akwai wani cigaba ko kanaga kawai gobe mu wuce Germany ɗin?"    Yanayin yanda Alh.Mansur yayi maganan kaɗai ya isa sanya zuciyar mai sauraro karyewa, domin kuwa kallo ɗaya zakayi masa kasan baya cikin wata nutsuwa, sosai rashin lafiyar Sooraj ɗin ke damunshi.

Ajiyar Zuciya Dr.Mohd yayi tare da kama hanun Alh. Mansur suka fice daga cikin ɗakin, ganin haka yasa Ummu fashewa da kuka, domin atunaninta wani abunne ya kuma sake faruwa, Mas'oud ne yayi ƙarfin halin fara rarrashinta.

"Calm down Alh.Mansur kazauna!" Dr.Mohd yafaɗi haka akaro na uku kenan, domin kuwa tun ɗazu yaketa yiwa Alh.Mansur ɗin tayin wajen zama, amma saboda ruɗun da Alhajin ke ciki, sam ya kasa zama.

"Bazan iya zama ba Dr.Mohd, hankalina amatuƙar tashe yake, kafaɗamin maiyasa ka kawoni office ɗinka? Shin wani abu yasake faruwa da SOORAJ ɗinne?"

"Na faɗama ka kwantar da hankalinka Alhaji, Insha Allah Sooraj zai farfaɗo nan bada jimawa ba, sai dai kawai akwai wata matsalane da sai yanzu, da mukayi masa gwaji muka san da ita!" Dr.Mohd yafaɗi haka yana mai shakkan abun da zai faɗawa Alh.Mansur, kasancewar baisan tayaya Alhaji'n zai ɗauki maganartasa ba.

"Innalillahi wa'inna ilaihirraju'n!! Doctor mai kuma yasake faruwa?" Alhaji Mansur ya tambaya cike da damuwa.

"Amm bawata matsalabace Alhaji matuƙar za akula,  nace dama tuncan kunsan cewa yana ɗauke da ciwon zuciya ne?"

Ai tamkar rugugin aradu haka Alhaji Mansur yaji sauƙan kalaman Dr.Mohd acikin kunnuwansa.

Daɓas haka Alhaji Mansur ya zauna tare da sanya hanu ya dafe kansa.  "Innalillahi wa'inna ilaihirraju'un!!" kawai yaketa ambata acikin rai da zuciyarsa.  "Shikenan kuma lokacin dazai rasa ɗansa mafi soyuwa agaresa yazo, haƙiƙa  wannan ƙaddaran tana da girma agaresu baki ɗaya, Allah yabasu ikon cinyeta!" yafaɗi haka acikin zuciyarsa.

Aƙalla yaɗauki kusan sama da 12 minute ahaka,
Idanunsa da sukai jajur dasu ya ɗago ya kalli Dr.Mohd.

"Idan nafahimci kalamanka Doctor kanaso kace dani Sooraj ɗana yana ɗauke da ciwon zuciya ko?"

"Ƙwarai kuwa haka nake nufi Alhaji, amma ciwon batayi tsanani sosaiba, idan har ya riƙe magani da yardan Allah Zai iya warkewa ako da yaushe, kada ka tashi hankalinka Alhaji, Insha Allah komai zaizo da sauƙi!!"
Inji cewar Dr.Mohd wanda yake cike da buri da kuma fatan ƙarfafawa Alhaji Mansur ɗin guiwa.

Ajiyar zuciya Alhaji Mansur ya sauƙe tare da cewa.

"Ni musulmi ne kuma nayarda da ƙaddaran da Allah Ya aikomin mai kyau ko marar kyau, kowani cuta aduniya tana da maganinta, cutar mutuwa ce kaɗai bata da magani, haƙiƙa komai da komai na Allah Ne, samun cuta da kuma sauƙi duk waƴannan ikonsa ne, kafun ka tsara naka shi yajima da tsara nashi, idan Allah Ya ƙadarta maka ƙaddara mummuna babu wani mahaluƙi daya isa sauya maka ita, haka idan ya nufeka da kyakkyawa babu wanda ya isa sauya maka ita, babu wani abu aduniya da yafi ƙarfin ikon Allah da kuma Addu'a, zamuyita addu'a Insha Allah komai zai zamo tarihi watarana!!" handkerchief ɗin dake cikin aljihunsa ya ciro tare da sanyawa yaɗan share ƙwallan da suka cika idanunsa.

Murmushi Dr.Mohd yayi tare da cewa "Haƙiƙa duk wani musulmin ƙwarai irinka akeso yakasance Alhaji Mansur, Allah yayi mana jagora"

Da "Ameen" kawai Alhj Mansur ya iya amsawa, sannan suka tashi suka fice daga cikin office ɗin.

Direct ɗakin da su Ummu suke suka nufa.

"Hajiya zaku iya ganinsa yanzu" faɗar Dr.Mohd.

Dukansu suka ɗunguma sukabi bayan Dr.Mohd ciki kuwa harda Ziyada. Wani waje suka nufa daganin wajen kasan na musammanne sannan kuma secret waje ne, wani ɗan corridor suka shiga sannan suka samu kansu a gaban wani ɗaki. Dr.Mohd ne ya tura ƙofar ɗakin ahankali, sannan suma suka rufa masa baya, Ziyada ce tayi na ƙarshen shiga. Tana shiga ɗakin idanunta suka hasko mata shi, kwance yake akan wani gado mai ɗan faɗi, fuskarsa na kallon sama, sanye yake da dogon wando babuko riga ajikinsa, sai bandage ɗin da aka lilliƙa awajen da akayi masa aikin cire bullet. Wata ƴar wayane aka sanya masa atacikin hancinsa, sosai ya ƙara haske, gashin kansa kuwa sun kwanta luf, sam batasan lokacin da hawaye suka gangaro daga cikin idanunta ba, jitayi ƙafafunta gaba ɗaya bazasu iya ɗaukarta ba. Hakan yasa ta jingina bayanta da wani dogon ƙarfe dake kusa da ita. Ummu kuwa sai aikin share hawaye kawai take da handkerchief ɗinta, shi kansa Alh.Mansur baƙaramin dauriya yayi ba da baiyi kuka ba, musamman ma da yanzu yasan cewa ciwukan ɗan nasa sun zame masa biyu. Mas'oud ma saida ya share ƙwallan tausayin abokinsa, domin kuwa duk wanda yaga Sooraj ahaka sai ya tausaya masa. Hannu Ummu takai ta shafi kansa, wasu sabbin hawayene suka

sake fitowa daga cikin idanunta. Bazata iya jurewa ba, hakanne yasanya ta juya da sauri ta fice daga cijin ɗakin, koda ta fita waje tsayawa tayi ajikin wata rumfa tasaki kukan tausayin Sooraj, ganin Ummu tafita yasa Alh.Mansur binta saboda yasan aikin kuka zataje tai tayi, bayan kuma tana da Hawan jini, sam bayason ciwonta ya tashi.

Mas'oud ne ya kalli Ziyada dake ta zubar hawaye ta kafe Sooraj ɗin da kyawawan idanunta, duk abun da ke wakana ma sam ita batasan anayinsa ba, gaba ɗaya hankali da tunaninta suna ga Mr.Helper ɗinta, har batasan sanda hawaye ke zuba daga cikin idanunta ba.

"Ziyadah!" Mas'oud yaƙira sunanta murya asanyaye. Sai alokacin ta dawo daga duniyar tunanin da take, bata iya amsa ƙirannasa ba, saidai ɗago kai da tayi ta kalleshi.

"Ki share hawayenki ba komai kuka ke magancewa ba, kiyi masa addu'a kawai, yafi buƙatar hakan agareki" Mas'oud yafaɗi haka yana mai cusa hannayensa acikin aljihun wandonsa.

Kai kawai ta iya jinjina masa alaman "To" domin bazata iya cewa dashi komaiba ayanzu, gaba ɗaya jikinta ya mutu, zuciyarta tayi rauni, duk wani tunaninta ya tsaya cak.

Dr.Mohd ne yace sutafi hakanan saboda ba aso hayaniya tayi yawa a inda yake.

Alh. Mansur ne ya kalli Mas'oud tare da cewa. "Mas'oud kakaisu gida, nikuma zan zauna anan"

"Banajin zan iya komawa gida Alhaji, nikam nafiso na zauna anan" Ummu tafaɗi haka cikin muryarta da ta soma dashewa saboda kuka.

"Zaman asibiti banaki bane Sulaimiyya kuje kawai gobe da safe sai kuzo!" Alh.Mansur ya faɗi haka aƙagauce saboda sam bayason musu.

"Abba me zai hana kabiyomu na sauƙeku idan yaso ni sai nadawo na kwana anan ɗin"

"A'a Mas'oud baza ayi haka ba, nine nan zan kwana, kuje kawai saida safe idan Allah Ya kaimu, sannan kuma banyarda kabarsu su kaɗai agidaba, ka kwana agidan kaima" Alhaji Mansur yana gama faɗan haka ya juya ya koma cikin asibitin. Babu yanda Ummu ta iya haka ta shiga cikin motar Mas'oud ya ɗauki hanyar Maitaima dasu inda anan gidan Abba dake Abuja yake. Wani irin tamfatsetsen gida Ziyada taga sunshiga, gaba ɗaya ginin gidan, gidan sama ne, gida ne mai kyau da girma, komai na gidan gwanin ban sha'awa ne, ko ina dake cikin gidan awadace yake da hasken ƙwan wuta, Mas'oud ne yasanya key ajikin ƙofar ya murza. take babban ƙofar falon ta buɗu. haka suka kutsa kai cikin babban falon dake cike da kayan more rayuwa, kayan ƙyale ƙyale dana ado. Komai na cikin falon tsab tsab yake, Mas'oud ne ya buɗe gaba ɗaya bedrooms ɗin dake cikin falon, acan sama bedroom ɗin Ummu yake hakan yasa ya wuce sama direct ya buɗe mata nata ɗakin. Ɗakin dake kusa dana Ummu yace da Ziyada ta shiga, gobe zai kawo mata kaɗan daga cikin kayanta. Saida ya tabbatar da cewa dukansu sunshiga ɗakunansu, kafun ya dawo ƙasa shima ya shiga wani ɗaki.

Ayɗan kwanakinnan tasaba duk dare saitayi wanka kafun ta kwanta saboda yanayin zafi da ake ciki, amma yau hakanan tasamu kanta da rashin duk wani kuzarinta, damuwar dake kwance aranta ma bazata bari tayi wani baccin kirkiba balle har aje ga yin wanka.   Hijabin jikinta ta cire tare da ɗalewa kan gadon ta kwanta jigum, yayinda ta sanya hannayenta ta tallafe ƙuncinta. Tunanin Mr. Helper ne ya tsaya acikin rai da zuciyarta, ganinsa da tayi acikin ciwo yau yasanya hankalinta gaba ɗaya ya tashi, wani abu takeji agame dashi, wanda takasa tantance menene amma ta ta allaƙa abun da sunan TAUSAYI,  juyin duniya tayi amma bacci yaƙi ɗaukarta, haka tayita saƙe saƙe har kusan asuba sannan tatashi ta ɗauro alwala.

Kamar yanda bacci ya guji Ziyada haka ya gujewa Ummu, haka Ummu ta kusan kwana tana sallah, sauƙi kawai take nemawa ɗanta awajen ALLAH, kuka kam tayishi, domin tun  tanayinshi da iyaka ƙarfinta, har hawayen suka daina fita.

7:30 daidai taji anayi mata knocking ƙofar ɗakin da take ciki, dama tana zaunene akusa da ƙofar hakan yasa ta miƙe taƙarasa jikin ƙofar. Koda ta buɗe Mas'oud tagani tsaye.   kafun yace wani abu tayi saurin cewa "Ina Kwana"

"Lafiya lau" ya amsa yana me miƙo mata wata leda dake hanunsa.

"Kayankine kishirya, saiki fito kiyi breakfast, anjima zamu koma asibiti"

Amsar kayan tayi tare dayi masa godiya, ta koma cikin ɗaki, shima juyawa yayi ya koma wajen Ummu dake zaune afalo, tun ɗazu ba abun da yake sai aikin rarrashi.

Wanka tayi sannan ta ɗauki doguwar rigan material blue wanda yakawo mata tasanya, ɗinkin rigan irin rapper gown ɗinnan ne, sannan tana da ɗan guntun hanu, kallon kanta tayi acikin madubi, tare da kallon rigan azahiri,  mamakin inda yasamo rigan take, domin kuwa tasan baya ɗaya daga cikin kayanta nacan gidan, gaba ɗaya ma kayan daya kawo mata sabbi ne, kuma duk daga ɗinkin materials sai wasu atamfa guda biyu wanda aka musu ɗinkin riga da sket. Jihabin data gani haɗe da rigan material ɗin ta ɗauka tasanya ajikinta, kasancewar white skin gareta saigashi kayan sunyi mata kyau sosai.   Afalo ta iskesu duka suna zaune, cike da ladabi ta rusuna ta gaishe da Ummu,  amsa mata gaisuwan nata Ummu tayi tanaɗan  dubanta.

Akan sofa ta zauna tare da tanƙwashe ƙafafunta, Mas'oud ne ya turo mata plate ɗin soyayyen chips gabanta tare da kofin tea.

Bata wani iyacin abincin sosaiba, tea ɗinnema ta ɗansha da yawa.   Mas'oud ma sama sama yaci abincin, Ummu kam adole takecin abincin, hakan ma saboda umarnin da Alh.Mansur ya bata ne, da yace "Idan tasan bataci abinci ba karta sake tazo asibitin, idan bahaka ba kuwa zata gamu da fushinsa." banda haka babu abun dazai sanya tasanya wani abu na abinci acikinta.

Yauma dai aɗakin jiya suka zauna, gaba ɗaya zuciyoyinsu babu dadɗi. Sai ƙarfe uku sannan

Dr.Mohd yayi musu jagora zuwa ɗakin da Sooraj ɗin yake.

kamar jiya haka Ummu tayita aikin ƙwalla, Ziyada ma idanunta sunyi tab da hawaye, ɗan matsawa kusa dashi tayi tare da kafesa da idanunta, gani takeyi kamar zai buɗe idanunsa, gani take kamar bacci yake idan katasheshi zai tashi, gani take kamar duk abun da suke yana jinsu, dubanta takai kan ƴan yatsun ƙafarsa, ƙurawa babbar yatsar ƙafansa ta dama idanu tayi, gani tayi kamar yatsar nasa tana motsawa, gefen hijab ɗinta ta sanya ta share ƙwallan dake cikin idanunta, wanda suka sa take ganin komai dishi dishi, sake kallon yatsar ƙafannasa tayi, sai kuma taga bata motsi, da alama gizone idanunta keyi mata.

Kallon Alh.Mansur Dr.Mohd yayi tare da nuna Ziyada yace.

"Matarsa ce?"

"A'a ƙanwarsace" Alh.Mansur yabashi amsa shima yana mai kallon Ziyada wanda idanunta ke cike da ƙwalla.

Kai Dr.Mohd ya jinjina tare da cewa "Inaganin ka ɗauki Hajiya ku koma gida kawai, ita sai kubarta anan, naga kamar yarinyar bata da hayaniya zamanta awajensa bazai kawo wata matsala ba, amma idan Hajiya ce zata zauna kasan dole saita ƙara ta da hankalinta"

Cike da gamtsuwa da kalaman Dr.Mohd, Alh.Mansur ya jinjina kansa. "Tabbas maganarka haka take doctor, yanzu kuwa zamu tafi insha Allah"

Da ƙyar da dabara Abba yasanya Ummu agaba yana rarrashinta sukabar cikin asibitin, tare da Mas'oud wanda shine ke tuƙasu.

Ziyada ita kaɗai akabari acikin ɗakin daga ita sai SOORAJ wanda bashida maraba da gawa. Akan kujeran dake gefen gadon ta zauna, tare da kifa kanta ajikin gadon. Tananan zaune har aka ƙira sallan Magriba, Sallah tayi sannan ta dawo ta zauna. Kallon kyakkyawar fuskarsa tayi, zara zaran eye lashes ɗinsa ne suka kwanta aƙasan idanunsa, sukayi luf dasu gwanin burgewa, gani tayi gumi nata fesowa akan goshinsa, mamakine ya kamata domin kuwa sanyin AC har yaso yin yawa acikin ɗakin. ɗan kwalinta ta ɗauka tashiga goge masa gumin. Atunaninta ko sanyin AC'n ne yayi masa kaɗan hakan yasa taɗan ranƙwafo da kanta zuwa daidai fuskarsa, ahankali tashiga hura masa iskan bakinta akan fuskarsa. hannunta takai kan nasa hanun tashiga goga masa taushin tafin hanunta akan fatar hanunsa, tanayin hakane cikin wani irin yanayi mai ɗauke da nutsuwa. Aƙalla taɗauki kusan sama da mintuna goma tana yi masa haka. Jin ana ƙiraye ƙirayen sallan isha ne yasata miƙewa daga zaunen da take, ta juya kenan kamar amafarki haka taji ya damƙi hanunta.

*(Alhamdulillah! This is to inform all my lovely fans that this will be my last update and i will insha Allah continue after ramadan. Thank you🙏🏼.)*

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ!!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*
_{United we stand and succeed; Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}_
*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*Wattpad*
fatymasardauna

#romance

*Taƙabbalullaha Minna Wa Minkum. May Allah make us stead fast on the path of the righteous,elevate our iman, forgive our sins and bless us abundantly.   Ameen Ya Rab!!!*
*🥀EID MUBARAK My Lovely Fans🥀*

*Chapter 24*

Kamar amafarki haka taji sauƙan hanunsa acikin nata.

Da sauri ta waiwaya zuwa gareshi, amma sai taga ko motsi baiyi ba, hasalima idanuwansa akulle suke da'alama bai dawo cikin hayyacinsa ba.  Ahankali ta koma ta zauna tare da kafe sa da ido,  zara zaran eye lashes ɗinsa da suka kwanta luf luf take kallo, ahankali tayi ƙasa da idanunta tana kallon ɗan ƙaramin pink lips ɗinsa wanda suka ɗan bushe. Idanunta ta sake mayarwa kan lallausan sajen dake kwance akan fuskarsa, baƙaƙen hairs ne kwance luf akan fatarsa, komai nasa me kyaune kuma gwanin burgewa.  Kanta ta mayar jikin gadon tare da lumshe idanunta.  Wani irin tausayinshi takeji,  daga wani ɓangare na zuciarta kuwa tunanin Farouk ne yazo yayi tsaye.  Bazata  iya faɗin me takeji game da shi ba, amma tabbas akansa tanajin wasu baƙin al'amura suna ziyartan ta.  Zare hanunta dake cikin nasa hanun tayi tare da miƙewa tsaye, toilet tashiga ta ɗauro alwalan sallan isha'i.

Tajima tana zaune akan sallayan. Wasu siraran hawayene suka silalo daga cikin idanunta, kallonta takai zuwa garesa,  wasu sabin hawayene suka sake fitowa daga cikin idanunta, hakanan batasan me yasa ba aduk sanda ta ɗaura idanunta akansa takanji zuciarta ta karye, tasan da cewa ita mai raunice tun tuni, amma akansa raunin da takeji na dabanne.  Tajima zaune akan sallayan har kusan 9 pm sannan ta tashi ta koma bakin gadon ta zauna.  Kanta ta

ɗaura adaidai saitin kanshi tare da lumshe idanunta. Mintuna goma tsakani bacci ya ɗauketa batare da ta shiryawa hakan ba.

Ahankali breath ɗinta ke fita, yayinda hucinsa ke sauƙa adaidai saitin kunnensa, ahankali yasoma buɗe idanunsa har ya waresu gaba ɗaya, akan zanen pop'n dake cikin ɗakin ya tsayar da idanunsa, sosai idanun nasa suka sauya kala daga farare zuwa kalan ja, sannan lokaci guda suka ƙanƙance sai tarin eye lashes dake samansu wanda yayi wara wara, wani irin ciwo yakejin kansa nayi masa, yayinda yakejin wani zogi na musamman adai dai chest ɗinsa. Lumshe gajiyayyun idanunsa yayi tare da sauƙe wata gajiyayyar ajiyar zucia. Ahankali ya ɗan yunƙura tare da ɗan jingina bayanshi ajikin pillow, saida ya ɗan cije pink lips ɗinsa sakamakon wani irin zogi dayaji ƙirjinsa nayi, hanunsa yakai kan wani ɗan madanni dake gefen gadonnasa ya ɗan danna da ƙarfi har saida yayi ƙara. 3 minute tsakani saiga wata Nurse tashigo cikin ɗakin da gaggawa. Ganinsa azaune yasa tashiga tambayarsa jikinnasa. Da kai kawai ya iya amasa mata, ganin haka yasa tafita da hanzari don ƙiran Dr.Moh'd.

Baƙaramin daɗi Dr. Moh'd yaji ba sakamakon jin cewa wai Sooraj ya farfaɗo, da ƙwarin guiwarsa haka ya nufo ɗakin da Sooraj ɗin ke kwance.

Checking ɗinsa yayi sosai sannan ya tambayesa ko akwai wani abu dake damunsa. Kai kawai Sooraj ya iya girgizawa, sannan yayi masa nuni da chest ɗinsa daidai inda aka ɗaure da bandage. Alaman nanne kawai ke masa zafi.
Wasu magungunan kashe zogi Dr. Moh'd ya basa ya sha, sannan yace masa yaɗan kwanta zuwa da safe. Har Dr.Mohd yagama abun da zaiyi yafita Ziyada na bacci bata sani ba. Shiru haka Sooraj ya koma ya kwanta tare da lumshe idanunsa, tunanine cunkushe acikin ransa, _KADDARA_ itace abun dake ɗawainiya da rayuwarsa, sau da yawa yakansamun kansa acikin ƙuncin rayuwa, sai dai dole ayanzu zai daure don yaga yayi faɗa da zuciyar da take ƙoƙarin hanasa ɗaukar ƙaddaransa.

6:00 am dai dai Ziyada ta buɗe idanunta, awahalce tayi miƙa saboda wani irin ciwo da taji duka jikinta nayi mata, gaba ɗaya duk wani gaɓa dake jikinta yayi tsami. Kallonta tamayar ga Sooraj wanda yake kwance luf acikin gadon idanunsa a rufe da'alama bacci yake, kallon small lips ɗinsa tayi tare da ɗan murza idanunta, A hankali ta buɗe ƙofar toilet ta shiga, gaban sink ta tsaya tare da ɗauro alwala, koda ta fito sallaya ta shumfuɗa tare da tada Sallah, koda ta sallame sallan bata tashi akan sallayan ba, sai dai lokaci zuwa lokaci tana kae dubanta zuwa gareshi.

7:00 am dae dae acikin asibitin tayiwa su Alhaji Ma'arouf da Mas'oud. Koda Dr.Moh'd yabasu kyakkyawan labarin farfaɗowan Sooraj baƙaramin farinciki sukayi ba, har suna rige rigen shiga ɗakin da Sooraj ɗin yake.

Da farinciki ɗauke afuskokinsu duka suka shigo cikin ɗakin, cike da ladabi Ziyada ta gaidasu, kowa fuskarsa ɗauke da annuri ya amsa mata, Ummu kam tuni tayi kan Sooraj, hawayene suka cika idanunta tab, hannunta ta ɗaura akan fuskarsa murya araunane tace. "SOORAJ!"

jin muryan Ummunsa acikin kunnuwansa yasanyashi buɗe idanunsa ahankali domin dama ba bacci yakeba kwana yayi idanunsa biyu batare da ya runtsaba.  Kuka ne ya ƙwacewa Ummu domin kuwa wani ƙaunar ɗannatane ya sake shiga zuciyarta, sosai takejin tausayinsa duk da ya kasance me laifine agaresu,    Hanunsa Abba yakama cike da ƙarfin guiwa haɗe da farinciki yace.

"Alhamdulillah! Yajikin naka, meke maka ciwo yanzu?"

Ɗan yunƙurawa yayi zai tashi Mas'oud yataimaka masa wajen sanya masa pillow a bayansa. Breath me ɗumi yafitar sannan ya kalli Abba cikin wata irin murya yace "Banajin komai Abba, kawai inaso na koma gidane, nagaji da zaman nan!"  yaƙare maganar yana ɗan ɓata fuska.

Farincikine yasake cika zuciyarsu jin cewa bayajin komai.  Murmushi Abba yayi tare da dafa kafaɗan sa yace.
"Ka kwantar da hankalinka, zannema maka sallama awajen Dr."

Ɗan ya mutsa fuska yayi tare da kawar da kansa gefe, idanunsu ne suka sauƙa acikin na juna, dai dai lokacinne kuma ƙwallan da suka cika idanunta suka samu daman gangarowa kan ƙuncinta, da sauri yajanye idanunsa tare da ɗan cizan lips ɗinsa.  Ƙoƙarin sauƙa daga kan gadon ya somayi, Mas'oud yace "Ina kuma zaka?"

"Wanka!" Sooraj yabashi amsa ataƙaice. Bathroom ɗin dake cikin ɗakin ya shiga, long pencil jeans ɗin dake jikinsa ya cire tare da tsayawa agaban shower ruwa na dukan jikinsa,  Sai da ya soma jin sanyi na ratsa cikin jikinsa sannan yakashe shower'n, dai dai lokacinne kuma aka soma knocking ƙofar toilet ɗin, yana buɗewa Mas'oud ya miƙo masa wani Blue pencil crazy jeans, tare da sabon brush da maclean, karɓa kawai yayi  yakoma cikin bathroom ɗin,  saida yasanya trouser'n kafun yayi brush, ruwa ya sanya yasake wanke fuskarsa.  Sannan yafito daga cikin toilet ɗin.  Zama yayi akan gado, lokacin har Ummu tagama haɗa masa tea. Miƙa masa cup ɗin tayi,  amaimakon ya karɓa sai ya ɓata fuska tare da kawar da kansa gefe, alaman bazai shaba.

"Kayi haƙuri kasha kaji, Dr. Moh'd  yace akwai maganin da zakasha kuma dole saika ci abinci!" Abba yafaɗi haka cikin rarrashi.

Karɓan cup ɗin yayi tare da kaiwa bakinsa, da kaɗan kaɗan yake sipping tea ɗin, hakanan yakejin bakinsa babu wani ɗanɗano, bai wuce rabin cup  yasha ba ya aje kofin, dai dai lokacin Dr.Moh'd ya dawo hanunsa ɗauke da magunguna.

Ita dai Ziyada tana daga zaune akan sallaya tana ganin ikon Allah, mamakin yanda ake shagwaɓasa kamar ƙaramin yaro take, daga cikin zuciarta kuwa wani irin sanyin daɗi takeji na ganin ya buɗe idanunsa har ma ya tashi,  Mas'oud ne ya dawo gefenta tare da jawo wata farar kujera ya zauna akai, plate ɗin dake hanunsa ya miƙa mata, abincine aciki Chips and onion soup wanda yaji ƙwai,  karɓa kawai tayi ta ajiye batare da takai koda loma ɗaya bakinta ba.

"Ziyadah!" Mas'oud yaƙira sunanta cikin ƙasa ƙasa da murya.

Bata amsa masa ba sai dai ɗago kanta da tayi ta kalleshi.

"Kukan na menene?" yatambayeta yana me ɗan satan kallonta.
Hanu tasanya ta shafi gefen kumatunta, sai alokacin ta tuna da cewa hawaye sun sauƙo daga idanunta kuma bata share ba, hannunta tasanya ta goge hawayen tare da yin ƙasa da kanta, tasoma wasa da yatsunta.

Murmushi kawai yayi tare da cewa. "Kici abinci, Sooraj ne damuwan kuma yatashi, saboda haka baikamata kina sa kanki adamuwa ba!"

Ɗan mareraice fuska tayi tare da cewa "Banajin yunwa ne fa!"

"Kici ko ba yawa" yafaɗa ataƙaice domin shima bawai yana da yawan magana sosai bane, saidai har aransa yana tsoron kada Ummu ta ranfo cewa babu wata alaƙa atsakaninsu.

Dole take kai abincin bakinta bawai don tanajin wani daɗinsa ba, duk da cewa abincin babu laifi amma hakanan takejinta wani iri. Duk abunda sukeyi Sooraj wanda ke zaune gaban Dr. Moh'd ana naɗa masa sabon bandage yana lure dasu.

Koda Alhaji Ma'arouf yanemi da Dr.Moh'd abasu sallama, cewa yayi subari sai zuwa yamma kafunnan da yardan Allah Sooraj ɗin yasake samun ƙarfin jiki. Abba ne ya dubi Mas'oud wanda suke ɗan taɗi sama sama da Sooraj yace.

"Inaga yakamata kakai su Ummunku Gida idan yaso anjima sai su dawo"

Badon Ummu tasoba haka Mas'oud ya dawo dasu gida.

Ziyada.

Banɗaki tashiga tare da rage kayan jikinta, wanka tayi haɗe dayin brush, koda ta fito sama sama ta shafa wani body lotion ajikinta, riga da sket na wani swiss material sky blue and pink colour tasanya, ahankali ta ƙarasa gaban window'n dake cikin ɗakin ta tsaya, hanunta tasanya taɗan yaye labulen tare da jan glass ɗin window'n gefe, lumshe idanunta tayi sakamakon wani daddaɗan iska daya ratsata, Dayake ɗakin da aka bata yana sama, hakan yasa daga bakin window'n tana iya hango ƴan tsirarun motocin dake ta shawagi akan babban titin dake malale agaban gidan, tunanin Farouk ne yasoma yi mata kutse acikin zuciyarta, hakanan kyakkyawar fuskarsa ke yawo acikin idanunta, tun rananda ta ganshi takejin wani baƙon yanayi adangane dashi, daga wani ɓangare na zuciyarta kuwa RAUNI ne da Tausayin rayuwarsu ita da SOORAJ, sai dai kuma sau da dama takanjinta cikin wani irin yanayi idan ta tuna da cewa har yanzun ita bakowa bace, sannan takanji babu daɗi idan ta tuna cewa itaɗin watace wacce bata

da gata, watace wacce bata da madafa,  hannu ta sanya ta share hawayen dake bin ƙuncinta. Jin tsayuwar na neman gajiar da itane yasa takoma kan gado ta kwanta, luf tayi tana tunanin halin rayuwa.   Yamma nafara gabatowa direct suka wuce asibiti.

Ƙarfe 5 daidai suka fito daga cikin asibitin tuni Abba da Ummu sun shige mota, Mas'oud ne ke gefen Sooraj wanda yake takawa ahankali sanye yake da farar button shirt marar nauyi, harma ana iya hango surar jikinshi, Ziyada ce ke biye dasu abaya hannunta ɗauke da food flask. Wata baƙar Benz suka nufa, da kansa ya buɗe gidan baya yashiga ya zauna. Ganin haka yasa Ziyada ta sulale ta nufi motarsu Abba,  dayake driver ne zai tuƙasu sai kawai ta buɗe murfin gefen mai zaman banza ta zauna.

Saida suka ɗau Hanya kafun Mas'oud ya saisaita gudun motar batare da ya juyo ba yace. "Ankama waƴanda suka kaimaka hari, amma kuma taurin kai yasanya sunƙi faɗan wanda ya sasu"

Sooraj da ke lafe jikin kujeran motar ya lumshe idanunsa, batare daya ɗago da kansa ba yace "Babu amfanin faɗansu ae"

Mamakine yakama Mas'oud harsai daya ɗan juyo ya kalli Sooraj ɗin.   "Meyasa?" yatambaya da mamaki.

"Saboda nasan kowa ya sasu!" yafaɗa ataƙaice domin bayason maganan tayi tsawo.

Shiru Mas'oud yayi tare da ɗan cije laɓɓansa, shikam har acikin ransa ya tsani wannan halin Na Sooraj daga anfara magana sai ya nuna ya gaji.   Saida suka ɗanyi nisa kaɗan kafun Mas'oud yace.  "Har yanzu bansan mekake nufi da Ziyada ba, menene ma'anar zamanta atare dakai? mekake tunanin su Ummu zasuji aransu idan suka san gaskian lamarin?"

Sai alokacin Sooraj ya ware idanunsa, shikansa saida yayi tunanin haka, amma duk yanda suka ɗauka zai bari ahakanne kawai.

Shirun da Yaji Sooraj ɗin yayi yasanya shima Mas'oud baisake cewa komai ba harsuka iso gaban tamfatsetsen gidan.   Suna shiga ko gama daidaita parking Mas'oud baiyiba Sooraj yasoma yunƙurin fita daga cikin motan.

Atare dukansu suka nufi babban falon gidan.   Direct Sooraj wajen wata ƙofa dake cikin falon ya nufa, koda yashiga samun kansa yayi acikin wani ɗan corridor, daga corridor'n straight wata ƙoface take facing mai tahowa.  tun daga corridorn har zuwa gaban ƙofar, ƙawace yake da farin haske da kuma wasu green and white flowers masu kyau.  Ahankali ya buɗe ƙofan ya tura kansa ciki, ganin komai dake cikin ɗakin nead yasanyashi maida ƙofar ya rufe.  Simple royal bed  golding colour ne acikin ɗakin, sai kuma wani tangamemen drawer me ɗauke da mabuɗai 10, gaba ɗaya jikin murafen drawern glass ne,  ɗakin babu wasu tarkace aciki amma duk da haka yayi kyau sosai, kayansa ya cire tare da buɗe drawer'n ya zaro wani light yellow towel

sabo ƙal ya ɗaura ajikinsa, kai tsaye ya wuce bathroom.    Aƙallla yaɗauki sama da 1 hour yana wanke jikinsa da kansa, harsai da yasoma jiwo ƙiraye ƙirayen sallan Magriba, kafun ya ɗauro alwala.    Koda yafito daga cikin bathroom ɗin gaba ɗaya jikinsa ajiƙe yake da ruwa, ɗan ƙaramin brown towel ne riƙe ahanunsa yana goge kansa,  ƙarasawa gaban dressing mirror yayi tare da jawo wani lotion ɗinsa mai ƙamshi yasoma shafawa, saida ya kammala kafun ya dubi kanshi amadubi,  duk da irin ciwon da yayi amma hakan baisanya jikinsa ya sauyaba, kallonsa yamayar kan murɗaɗɗun muscles ɗin hanunsa na dama, wasu irin murɗaɗɗun jijiyoyine suka fito raɗa raɗa ajikinsa,  numfashi mai zafi ya fesar daga bakinsa tare da ɗan lumshe idanunsa, jiyayi wasu abubuwa na yawo acikin brain ɗinsa, take jijiyoyin jikinsa suka sake fitowa gashin jikinsa kuwa lokaci guda suka soma miƙewa,  tamkar mai wani irin ciwo haka jikinsa ya soma rawa, cikin wani irin yanayi yasanya hanunsa ya daki mirror'n take ya tarwatse yayinda hanunsa kuwa take yasoma fidda jini domin mirrorn ya yankesa sosai. Dai dai lokacin Ziyada taturo ƙofar ɗakin tashigo hanunta ɗauke da tray. Shigowansa yayi daidai da juyowa yafuskanci bakin ƙofan, idanunsune yasarƙe acikin na juna amatuƙar tsorace tasaki tray ɗin dake hanunta tare da sulalewa awajen tana kallon cikin idanunsa da suka zama tamkar garwashin wuta.
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ!!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*
_{United we stand and succeed Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}_
*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*Wattpad*
fatymasardauna

#romance

*This Page Is Dedicated To You My Habibtie Niesher Jay. Love yhu Habibtie💘🔐*

*Chapter 25*

Cikin sauri tasoma tattara glass bowl ɗin daya tarwatse akan tiles ɗin, gaba ɗaya jikinta ɓari yake.  Baiko kalli inda take ba  ya juya ya koma toilet. Jiki asanyaye haka ta tattare wajen. Moper taɗauko tazo tasoma ƙoƙarin goge wajen da fruit salad ɗin ya ɓata, gashi gaba ɗaya glass bowl ɗin da fruit salad ɗin ke ciki ya tarwatse awajen.

Wanke hanunsa yayi acikin sink tare da ɗaukan wani ɗan ƙaramin towel ya goge gumin dake

fesowa ta goshinsa, atunaninsa zuwa yanzu bata cikin ɗakin don haka ya murɗa handle ɗin ƙofar toilet ɗin ya fito, ganinta a durƙushe tana tattare fasassun glasses yasan yashi saurin ɗauke kansa daga gareta, direct gaban closet ɗinsa ya nufa, wani Pencil Combat jeans black ya ciro sai kuma wata white button shirt, kallon agogo yayi yaga har lokacin sallan Magriba yaɗan gota, tsuka yaja ahankali tare da ɗan cizan laɓɓansa.
Gaba ɗaya jikinta ɓari yake, tsoro takeji kada yayi mata faɗa ko yace zaiyi mata wani abun. Jin takunsa na isowa gareta yasanya batare data kulaba ta sauƙe hanunta akan wani fashasshen kwalba, yana cakanta kuwa saiga jini, wani ƙara ta sake cike da ɗan tsoro, dubanta takai ga hanunta wanda har yaɗan fara fitarda jini, take tasoma jin wani irin raɗaɗi.    Sooraj dake tsaye agaban dressing mirror yana dressing hanunsa daya yanke, baiko waiwayo ya kalleta ba, yi yayima tamkar baiji ƙaran nata ba, yana kammala dressing ɗin, ya ɗauki kayansa ya wuce toilet.

Haka tacigaba da gyara wajen, duk da cewa hanunta nayi mata zogi amma haka  ta daure. Yana fitowa daga cikin toilet ɗin sassanyan ƙamshin turaren dake fita ajikin kayansa ya daki hancinta,  cikin takunsa na isa yaƙaraso  ta bayanta ya raɓa yafice daga cikin ɗakin batare da ko kallonta yayi ba.  Tanajin rufewar ƙofarsa, tasaki wata ƙatuwar ajiyar zuciya, sai alokacin ruwan hawayen da suka cika idanunta suka samu daman gangarowa.  Cikin mintuna ƙalilan ta gama gyara wajen, tattara fasassun glasses ɗin tayi tazubar a durstbin, daganan ta wuce ɗakinta duk raɗaɗi ya isheta.

Yana fita kaitsaye babban masallacin dake gefe da gidannasu kaɗan ya nufa, anan yayi sallan Magriba, haka ya zauna har aka ƙira sallan Isha.  Koda ya idar da sallan bai ko motsaba, istigfari yashiga yi acikin zuciyarsa, duk ƙoƙarinsa nason kawar da tunanin dake neman addabar  zuciyarsa abun yaci tura,  kansa ya jingina ajikin bango tare da lumshe idanunsa, numfashi yake fitarwa ahankali yayinda yake furta kalman  "Astagfirullah!" daga bakinsa ahankali.  Ahankali nutsuwa ke sauƙa ajikinsa, yayinda yaji damuwarsa na gushewa, sosai yaɗanji sanyi acikin zuciyarsa.   Ƙarfe 9 daidai yabaro cikin masallacin ya nufo gida.

Ziyada

Gaba ɗaya ɗan yankewan da tayi ya ɗaga mata hankali, sosai yake mata zafi da zogi,  fitowarta daga  toilet kenan tana ta faman hura iskan bakinta adaidai saitin wajen data yanke,   zama tayi akan gado, tare da jawo school bag ɗinta, gaba ɗaya zaman kaɗaici ya isheta sam batajin daɗin zaman da take yanzu burinta shine akoma makaranta.   Tajima tana dudduba littatafanta kafun daga bisani bacci ɓarawo yayi awun gaba da ita.

_SOORAJ_

Yana dawowa daga masallaci direct ɗakinsa ya wuce, gaban Computer ɗinsa ya ƙarasa tare da soma lallatsata, koda ya kunna wayarsa kuwa saƙon gaisuwane da kuma na jaje waƴanda abokai da ƴan uwa suka tara masa suka dinga shigowa, bai tsaya wani duba saƙon ba yamaida wayar ya ajiye,  har ƙarfe 11 yana kan computer.    Aɗan gajiye yaƙarasa gaban fridge, bottle

water ya ɗauko tare da ɓalle murfin, magungunan dake hanunsa ya watsa abakinsa tare da bin kansu da ruwa,  long jeans ɗin jikinsa ya cire yasanya wani 3 guater,  hanunsa yakai kan makunnin wutan ɗakin ya kashe take duhu ya mamaye gaba ɗaya ɗakin.  Kan lafiyayyen gadonsa ya hau tare da danna makunnin bedside lamp, take wani ɗan haske dark blue yabayyana acikin ɗakin.  Lumshe idanunsa yayi tare dajawo pillow yaɗaura kansa akai, wata ajiyar zuciya ya sauƙe tare da sanya hanu ya shafi ƙasan maranshi, wanda yakejinsa aɗan kumbure,  duk yanda zuciyarsa taso sanyashi dogon nazari yaƙi aminta da hakan, haka kuma yaƙi bawa brain ɗinsa daman yin tunani kamar yanda yasaba akoda yaushe,  dayake acikin magungunan dayasha akwai maganin dayakesa bacci sosai, hakan yasa acikin mintuna kaɗan bacci ya ɗaukesa.

Washe Gari.

Tuni tatashi tayi sallan asuba, ɗan madaidaicin ƙur'aninta ta ɗauka tashiga tilawan aƙur'ani, dayake ana koya musu amakaranta shiyasa tamai da hankalinta sosai, tana kammalawa ta wuce toilet donyin wanka.

Ahankali ta buɗe ƙofar bathroom ɗin tare da sako kanta, duk dacewa tasan ita kaɗaice acikin ɗakin, amma hakanan take jin kunyan fitowa da towel ajikinta, kamar wata marar gaskia haka ta rakuɓo ta fito, zama tayi akan stull ɗin mirror tare da ɗaukan body lotion ɗinta tashiga shafawa, tana gamawa ta murza powder akan fuskarta, wani peach colour oil lipstick ta goga akan lips ɗinta wanda yaƙara bayyana asalin kalan lips ɗinnata,  wata simple maroon colour Straight gown ta sanya ajikinta, duk da kasancewar rigan tana da ɗan faɗi amma hakan baihana hips ɗinta bayyana ba, ɗan kwalin rigan da yakasance tamkar gyale shita ɗauka ta yafa ajikinta, daidai lokacin aka turo ƙofar ɗakin aka shigo, da sauri ta waiga zuwa bakin ƙofan, idanunta ne ya sauƙa acikin na Ummu da sauri tayi ƙasa da kanta, tare daɗan durƙusawa, cike da ladabi tace da Ummu.  "Ina kwana!"  Fuska asake Ummu ta amsa mata da  "Lafiya lau kin tashi kenan?"

Kanta ta kaɗa alamar "Eh"

"To biyoni mushiga kitchine saboda yau mu zamuyi aiki kafun masu aiki su ƙaraso"

Babu musu tabi bayan Ummu suka fito daga cikin ɗakin, direct tamfatsetsen kitchine ɗin dake cikin babban falon suka nufa, kitchine ne da aka ƙawatashi sosai tamkar wani haɗaɗɗen falo haka kitchine ɗin yake, komai na cikinsa light green and milk colour ne.   gyaran su carrots da green beans Ummu ta bata, cikin mintuna ƙalilan ta kammala,  haka ta ɗebo  irish patatoes tashiga ferewa tana musu yankan chips, yayinda Ummu kuma ke kula da miyan egusin da zatayiwa Abba wanda zaici tuwo dashi, da taimakon Ummu Ziyada ta haɗa  liver and garlic sauce, sannan ta soya chips,   kasancewar Ummu tasan Sooraj daga fruits sai tea sune abincinsa yasanya dakanta ta haɗa masa fruit salad, Ziyada kuwa Ummu ne ta nuna mata yanda zata haɗa milk shake, haka kuma da taimakon Ummu ta samu tayi pepper soup ɗin cow meat,  tuwon semo miyan egusi wanda yaji kifi Ummu tayiwa Abba tare da Coconut juice  domin

Abba baicika shan drinks ɗin company ba.  Ziyada ce keta kai kawo tsakanin dinning area dakuma kitchine, tsab tagama jere duk abincin da sukayi akan dinning table,  komawa kitchine ɗin tayi ta haɗa gaba ɗaya kwanukan da suka ɓata tasoma wankewa.    Ummu naganinta taɗanyi murmushi tare da ƙarasowa gareta  "Wannan ba aikin ki bane kibarshi idan masu aiki sunzo zasu ƙarasa" Ummu tafaɗa cike da kulawa.
Ɗan murmushi Ziyada tayi cike da jin nauyin Ummun tace "Ummu kibari nima zan iya!"

Murmushi Ummu tayi haɗe da cewa "To Naji, amma dai yanzu lokacin cin abincine muje maza" Babu yanda ta iya haka ta tsame hanunta acikin wanke wanken tabi bayan Ummu.  Tanasanya ƙafarta acikin falon ƙamshin da ke matuƙar tafiya da imaninta wanda tasan mutum ɗaya ne tak me amfani dashi ya daki hancinta, lumshe idanunta tayi alokaci guda tare da buɗewa,  ƙoƙarin gyara mayafinta take har suka iso dinning arean,   idanunta ne suka  sauƙa akanshi sanye yake da riga da wando farare, sosai yayi wani irin kyau, gashin dake kwance akan fuskarsa sai sheƙi yake, idanunsa nakan iphone 11 pro max ɗinsa da alama gaba ɗaya hankalinsa na kan wayan. Hakanan taji wani irin abu yashiga dukan ƙirjinta amma saita daure tayi ƙasa da kanta. Kujera Ummu taja ta zauna tare da cewa "Ziyada yi serving ɗinmu"

Jiki asanyaye haka Ziyada tashiga serving ɗinsu,  ɗaukan glass bowl ɗin fruit salad ɗin da Ummu tace mata nashine tayi ta ajiye agabanshi, cikin sanyinta ta juya zata bar wajen.

"Ina kuma zaki?" muryan Ummu ya katseta.

"Uhumm dama ɗaki zankoma!" tafaɗa tana mai wasa da yatsun hanunta.

"Zauna idan kinci abinci saiki tafi ɗakin!" Ummu tafaɗi haka tana me jawo mata kujeran zama wacce take facing na Sooraj.
Sam musu ba al'adanta bane don haka kamar wacce aka cirewa laka ajiki haka ta zauna akan kujeran aɗaɗare,  hanunta har rawa yake alokacin data soma serving kanta, chips ta ɗiba ɗan kalan acikin plate sai liver sauce shima kaɗan. Milk shake dinne dai tasanya har rabin cup. Abba da Ummu tuni sunfara cin abincinsu amma banda ita da Sooraj,  ita kam wani iri haka takeji domin bata saba zama da manya ba, sam ita batasan wannan soyayyan ba, shikuwa Sooraj tunda yazauna ma bai ɗago kanshi ba screen ɗin wayarsa kawai yaketa shafawa, kamar wacce aka razana haka taɗauki fork tashiga tsakalan chips ɗin da ɗaya ɗaya tana kaiwa bakinta. Aƙalla yaɗauki sama da 10 minute yana latsa phone dinsa kafun ya ɗago, bowl din fruit salad ɗinsa yajawo ahankali yasanya spoon aciki, 2 spoon kawai yayi ya sake mayar dakansa ga wayarsa,  Ummu gaba ɗaya tana lura dashi, duk da tasan cewa bayida yawan cin abinci, amma yanda yanzun yaƙi maida hankali yasha fruid salad ɗin yasanya taji ba dadi acikin ranta, cike da kulawa ta ƙira sunanshi  "SOORAJ!"

Ahankali yaɗago kanshi ya kalleta batare dayace wani abuba.

Ɗan ɓata fuska Ummu tayi tare da cewa.   "Kasan dai me Dr. yace akanka ko? saboda haka yanzu lokacine da zakaci abinci sosai, rashin cin abincin shine zaisa kadingajin kanka kamar

baka da lafiya"

Ɗan yamutsa fuska yayi tare da kaɗa mata kansa alamar "Yaji"

Kansa yamaida ga bowl ɗin ya ɗeɓo fruid salad ɗin yakai bakinsa.    Abba daya kammala cin tuwonsa ya ɗago yana goge hanunsa da tissue. Sam babu wanda yayi zato saijin muryarsa sukayi yace.

"Sooraj Ina magananmu ta tsaya?"

Dummmm haka Sooraj yaji gabansa yafaɗi, har acikin ransa yama manta da maganan da sukayi da Abban.

Shirun da yayi yasa Abba ci gaba da cewa.  "Ayanzune zan matsamaka fiye da da akan maganan aurenka Sooraj, kaduba kai bakajin kunya ne ace har yanzu mahaifiyarka itace zata nunamaka abun daya dace?  kula dakai ayanzu ba haƙƙin mahaifiyarka bane, yakamata ne ace kana da mata domin kulawa da irin waƴannan abubuwan,  saboda haka ina mai tabbatar maka da tunkan nama abun dazaisa kaji babu daɗi ka nemo mata kakawomin ko acikin satinnan ne ni zan aura maka ita!"  Cikin maganganun Abba gaba ɗaya babu wasa, yana gama faɗan haka ya miƙe tsaye yabar wajen.    Gaba ɗaya tunanin Raj ne ya tsaya cak, sam baiyi tunanin Abbansa zai sake tada wannan maganan ba, musamman ma da yanzu bawai wani lafiyane ya isheshi ba, inama da Abba yasani dabaiyi maganan nan ba, domin kuwa gaba ɗaya ya sukurkutamasa tunani, duk wani ɗan annushuwan dayake ciki ya kau.

"Ina fata dai kaji abun da mahaifinka ya faɗa ma? kasan shi kakumasan abun da zai iya aikatawa saboda haka tunkan yazaɓama da kanshi kai kazaɓarwa kanka, don na tabbata wannan karon bazai maka da sauƙi ba!" Ummu tafaɗi haka itama tana me miƙewa tsaye, bata wani tsayaba tabi bayan mijinta, akabarsu su biyu akan dinning table ɗin.

Hakanan Ziyada taji murfin ƙirjinta na ƙoƙarin faɗawa.
 "Aure akeso yayi?" ta tambayi  kanta,  sam bata wani fahimci inda kalaman Iyayen Sooraj ɗin suka dosa ba, amma kuma da dukkan alama aure sukeso yayi, tsintar kanta tayi da kasa cigaba da tauna chips ɗin dake bakinta sai kawai ta haɗiyeshi.

Shikuwa Sooraj hannayensa yasanya ya rufe fuskarsa da tafukan hanunsa, wani numfashi me ɗumi ya fesar ta bakinsa, wani irin dokawa  ƙirjinsa keyi,  sam bayason yaji anyi masa maganan da zata alaƙantasa da mace, bayajin zaiyi aure a irin wannan lokacin, bayamajin akwai wata wacce zata soshi ayanda yake, koda ma wata ta soshi shibabu soyayya atsarinsa, baisan menene so ba, baitaɓayi ba baisan yazai fara ba.

Sam bazata iya jure zaman wajenba, don haka saɗaf saɗaf  tamiƙe tsaye tare da juyawa zata bar wajen.

"Waye sa'anki dazakibar masa ragowan dattinki anan?"

Husky voice ɗinsa yadaki dodon kunnenta wanda ya tilasta mata tsayawa, jikinta naɗan rawan tsoronsa ta juyo, plate ɗin data ci abinci tasoma ɗaukewa sannan ta haɗa dana su Ummu ta nufi kitchine, har yanzu bai sauƙe hannuwansa daga kan fuskarsa ba amma kuma komai take yana kallonta. Baitashi akan dinning arean ba harsaida ta tsabtace wajen ta goge, duk abun da takeyi atsorace takeyinsa, fatanta ɗaya kar tayi kuskure yayi mata masifa, tana tsaka da goge kan haɗaɗɗen royal table ɗin yatashi cikin tafiyarsa ta isa yanufi ɗakinsa. Tana ganin shigewarsa ɗaki, ta saki wata ƙatuwar ajiyar zuciya, tare da share hawayen dasuka silalo daga cikin idanunta.

28/May/2020
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ!!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*
_{United we stand and succeed;our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}_
*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
fatymasardauna

#romance

*Chapter 26*

Hanunta tasa da sauri ta goge hawayen daya sauƙo mata akan ƙuncinta, kitchine ta koma ta tare da cigaba da wanke wankenta......

RAJ
Tsaye yake agaban shower ruwa na dukan jikinsa, hannayensa duka biyu ya sanya ya dafe jikin bango, idanuwansa wanda suka sha ruwa sukayi jajur ya buɗe tare da furzar da ruwan dake bakinsa. Maganganun Abba gaba ɗaya sun gama dagula masa lissafi, ko tantama bayayi koda sun nemo zaɓinsu sun aura masa awannan karonma bazai iya jure zama da mace ba, dole zai saketa, sannan kuma dole ne zasuyi fushi dashi, ayanzu kam baya tunanin zai sake yarda alaƙa ba masa nauyin wata ƴa mace akansa, koda sau ɗayane yanason iyayenshi su

fahimcesa amma kuma hakan ya gagara,   kashe shower'n yayi tare da jawo towel ya ɗaura akan weast ɗinsa,  baidamu da yanda jikinsa ke ɗigan ruwa ba ya buɗe ƙofar bathroom ɗin ya fito,    idan yace zai iya baje damuwowin dake ranshi to tabbas ƙwaƙwalwa da zuciyarsa bazasu  iya ɗauka ba,   kaya ya sanya ajikinsa tare da ɗaukan car key ɗinsa yafice daga cikin ɗakin,   direct compound ɗin gidan ya nufa, wata baƙar 4matic ya buɗe yashiga tare dayi mata key, tun mai gadi baigama wangale gate ɗin da kyauba ya cilla hancin motarsa waje.

Tafiya yake amma gaba ɗaya hankali da tunaninsa suna wani waje daban, ababban ƙofar asibitin yayi parking,  yau bakamar ko yaushe ba, don bai shigar da motar tasa ciki ba kamar yanda ya saba.

Direct office ɗin Dr.Yunus  ya nufa, yana knocking aka bashi izinin shigowa,   kujera yaja ya zauna tare da miƙawa Dr.Yunus hannu sukayi musabaha, cike da fari'a  Dr.Yunus yace. "Yajikinnaka ina fata dai ankama wayƴanda suka aikata laifin?"

"Dasauƙi!" Sooraj yafaɗa aɗan gajarce kasancewar bayason zancen yayi tsawo.

Murmushi Dr.Yunus yayi domin sarai yasan halin Sooraj sai mutum ya shekara yana masa magana baitanka ba.

Gyara zama Dr. Yunus ya sakeyi tare da cewa "Result ɗinka yana ajiye tun after 1 week" Wata ƴar drawer dake jikin table Dr.Yunus ya jawo tare da zaro wata farar envelope.
Miƙawa Sooraj yayi tare da cewa   "Komai yananan daidai, nayi duk wani bincikena dazanyi Sooraj amma gaskia bangano wata sabuwar matsala ba, magungunan dana baka acan baya sune kawai zakana sha har abubuwa su daidaita!" Dr.Yunus yafaɗi haka cike dason kwantar da hankalin Sooraj.

Wani murmushin gefen baki wanda yafi kuka ciwo Sooraj yayi, shikaɗai yasan wani irin zafi zuciyarsa keyi masa awannan lokacin, karɓan takardan kawai yayi tare da sake bawa Dr. Yunus hanu sukayi musabaha, daganan yafice daga cikin office ɗin,  wani irin kallon tausayi Dr.Yunus keyiwa Sooraj, sosai matsalan Sooraj ɗin ke ɗaure masa kai, iya binciken duniya sunyi shida abokan aikinsa amma sam su basu iya gano matsalan Sooraj ba, hasalima komai nasa lafiya lau yake bashi da wata tawaya a halittar jikinsa. .

Tunda yafito daga cikin office ɗin Dr.Yunus yake ganin duhu a idanuwansa, cikin cijewa ya ƙarasa wajen da motarsa take, yana shiga ya kifa kansa ajikin steering motar tare da fesar da wani breath me ɗumi,  aƙalla yaɗauki kusan mintuna 9 ahaka batare dako motsi yayi ba, gaba ɗaya tunaninsa ya tsaya cak.

Da ƙyar ya iya ɗago kansa, idanuwansa tamkar jan garwashin wuta haka suka koma, Envelope ɗin da Dr.Yunus ya basa ya buɗe, tare da zaro wata ƴar farar takarda dake ciki, ahankali ya warwareta tare da sauƙe idanunsa akan  rubutun dake cikin takardan . Yana gama karanta abun dake cikinta ya duƙunƙuneta tare da rumtse idanunsa da ƙarfi.  Laɓɓan bakinsa

yaɗan ciza tare da  ɗauko wata lighter ya kunna, takardan yakawo jikin lighter'n take ta kama da wuta, sauƙe glass ɗin motar yayi ƙasa tare da cilla takardan waje, take takardan ta ƙone ƙurmus, key yayiwa motarshi tare da cillata kan titi yabar wajen....

Ziyada kuwa tana kammala wanke wankenta, ta shige  ɗaki bata kuma sake fitowa ba, duk da cewa zaman ɗakin bawani daɗi yakeyi mata ba amma kasancewar bata da abunyi yasanya ta gwammacewa kanta zama waje ɗaya.
***
After 3 days.
Tunda Abba yayiwa Sooraj maganan aure sai ya zamana Sooraj baya zaman gida kwata kwata, idan yafita tun safe bazai dawoba sai after Sallan Isha, kafunnan Abba yajima da dawowa suna tare da Ummu, sam bayason Abba yasake ɗago masa da wannan maganan domin magana ta gaskiya aure agareshi bamaiyiwuwa bane.

 Itakuwa Ziyada adaddafe haka take rayuwar cikin gidan duk dama Ummu na sake mata amma bawai wani sabawa sukayiba shiasa takejin kanta atakure, kallone kaɗai abun dake ɗebe mata kewa ayanzu, daga gefe guda kuwa  tana lissafin hutunsu wanda yanzu saura musu 1 week sukoma makaranta, har Allah Allah take lokacin yazo, duk da batasan menene makomarta a wajensu ba, batasaniba ko zasu koreta ko zasu barta...

5:15 pm.
Kwance yake akan makeken bed ɗinsa wanda yaji bedsheet na alfarma, dagashi sai long pencil jeans yayinda earpiece ke saƙale a kunnuwansa,  gaba ɗaya hankalinsa nakan laptop ɗinsa, Samsung Galaxy S20 ɗinsa ne tasoma ƙara alaman shigowan ƙira. Saida wayar takusa katsewa sannan ya zare earpiece ɗin dake  kunnensa, ganin sunan Abba nayawo akan screen ɗin wayar yasanyashi ɗaga wayar da gaggawa, yana kara wayar akan kunnensa. Abba dake tsaye cikin falonsa jin Sooraj ɗin ya ɗaga wayan yasanyashi cewa.
 "Kazo kasameni yanzu afalona!" ƙit yakashe wayan batare dayaji me Sooraj ɗin zaice ba.

Ahankali Sooraj yasauƙe wayan daga kunnensa tare da sauƙe ajiyar zuciya, rufe laptop ɗin yayi tare da zuro ƙafafunsa ƙasa, wata bruberry button shirt fara ya ɗauka ya sanya ajikinsa, bedroom slippers yasanya aƙafansa kana yafice daga cikin ɗakin.  Tun da ya doshi falon Abban yaji zuciyarsa na bugawa,  sam baison sakejin wani abu dazai ɗaga hankalinsa.

Zaune yasamu Abba akan kujera yana duba jaridan daily trust dake riƙe ahanunsa, zama yayi akan sofa tare da tanƙwashe ƙafafunsa.  "Sannu da hutawa" yace da Abba cikin nutsuwa.

Gyara zama Abba yayi tare da aje jaridan dake hanunsa. Kallon Sooraj ɗin yayi sosai tare da ɗanyin gyaran murya.   "Ina ka ajiye maganan da mukayi dakai? Shin kasamo wacce kakeso ɗin kokuwa?"  Abba yatambaya babu alaman wasa akan fuskarsa.

Ɗan shiru Sooraj yayi tare da haɗiye wani yawu me ɗaci da lokaci guda ya tsaya masa

amaƙoshi.  "Kayi haƙuri Abba, amma Bansamuba!"  yafaɗi haka cikin raunanniyar murya.

"Shikenan babu ma buƙatar kasamo da kanka,  Na auramaka  ƴaƴan abokaina basau ɗaya ba basau biyu ba kana sakosu babu wani babban dalili, to ayanzuma zan sake ɗaurama aure da ƴar abokina Alhaji Naseer, ina tabbatarmaka da cewa wannan shine naƙarshe, sannan kuma koda wasa idan ka sake kayi gigin sakinta wallahi! wallahi!! babuni babu kai, zan janye hanuna daga duk wani lamarinka, ai kai ba ƙaramin yaro bane kasan daidai kakumasan ba daidai ba, wannan umarni nake baka saika shirya inaso acikin satinnan kaje ka ganta, sannan kuma tana shekaran ƙarshe na kammala degree ɗinta, saboda haka da zaran tagama za a ɗaura muku aure, tashi kabani waje!!!" Abba yaƙare maganar murya akausashe.

Sooraj dake zaune wani irin jiri ne ke ɗibansa, tamkar sauƙan garwashi ajiki haka yaji sauƙan maganganun abba acikin kunnuwansa, take idanunsa suka sauya kala daga farare zuwa jajaye, wani irin ɗaci yakeji amaƙoshinsa, da ƙyar ya iya tashi yanufi hanyar fita daga falon, da kallo Abba yabisa har ya ɓacewa ganinsa, shikam har acikin ransa yasoma zargin ko aljana ce ta shafi Sooraj  ko kuma asiri aka mishi, saidai koma menene shidai yana kan ra'ayinsa na dole Sooraj sai yayi aure, domin aganinsa idan da akwai mace akusa dashi to ko bakomai zata rage masa kaɗaici.

Sooraj kuwa koda yabar part ɗin Abba kai tsaye garden yanufa, wani irin ƙunci yakeji azuciyarsa, jiyake kamar yaita tsala ihu kozai samu relief,  zama yayi akan wata beautiful chair tare da lumshe idanunsa, wani irin zafi zuciyarsa keyi masa ahankali yake ambaton sunan Allah acikin ransa lokaci guda yaɗanji zuciyarsa tayi sanyi,  sake lafewa acikin kujeran yayi tare da maida idanunsa ya kulle tamkar wanda yake bacci.

Ziyada ce ta fito daga part ɗinsu, hanunta ɗauke yake da wani bowl me kyau,  sanye take cikin riga da wando na Indian mai kama da pakistan, dayake kalan kayan blue ne shiyasa suka mata kyau sun karɓi white skin ɗinta sosai, ɗan kwalin kayan ta yafa daga kanta zuwa ƙirjinta. Kai tsaye take tafiya zuwa Inda Ummu tace taje ta ciro mata mango, zatayi mango juice.  Tana jefa ƙafanta acikin garden ɗin wani Irin sassanyan ƙamshi yadaki hancinta, wani irin ni'ima  ne ke tashi acikin garden ɗin, sanyine me daɗi yake ratsa ko ina najikinta,  baki buɗe haka take kallon komai dake cikin garden ɗin sosai wajen ya ƙawatu, ƙamshin kayan itatuwane kawai ke tashi. Cikin nutsuwa take tsinkan jajayen mango ɗin. Ahankali ya ware idanunsa ya sauƙesu akanta, lumshe idanunsa yayi tare da sake buɗewa, duk da cewa bayanta kawai yake iya gani amma yanayin yanda take motsa jikinta yasanyashi kasa ɗauke idanunsa akanta,  tana kammala tsinkan mango'n  tajuya daniyan barin wajen, batare data kulaba tayi tuntuɓe da wani ɗan itace take  bowl ɗin dake hanunta ya faɗi mangon ya watse. Bisa tsautsayi itama ta faɗi akan guiwowinta, rumtse idanunta tayi cike dajin zafi, ɗan cije laɓɓanta tayi tare da miƙewa tsaye bowl ɗin ta ɗauka tashiga bin Mangon da ya watse tana ɗauka da ɗaɗɗaya, tana maidawa cikin bowl,   kanta aƙasa yake hakan yasa sam bata lura da  akwai mutum awajen ba.  Batare data luraba taji tataka wani abu tamkar ƙafan mutum, tana ɗagowa sukayi ido huɗu dashi, wani irin faɗuwa gabanta yayi take ƙirjinta yashiga dukan uku uku,  ɗago idanunta dake ƙasa tayi take suka faɗa acikin nasa idanun, wani irin abu taji, wanda yataso tundaga ɗan yatsan ƙafarta har

zuwa kanta da jijiyoyin jikinta.  Pink lips ɗintane suka soma rawa da'alama magana takesonyi amma ya maƙale,  ahankali yayi ƙasa da rikitattun idanunsa, sauƙesu yayi  akan small lips ɗinta wanda suketa ɓari sukaɗai.

(Note editing🙏🏻kuyi haƙuri yau nashiga busy shiasa banyi muku update da wuri ba please kuyi manage!)

30/May/2020

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ!!!*

*Written By*
phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

#romance

(🌺I'm really proud of you my Wattpad fans, i felt happy with the way you are commenting and voting my work therefore I dedicate this page to you🌺)

*Chapter 27*

Kauda idanunsa gefe yayi tare da ɗauke duk wata annurin dake kan fuskarsa.  Ziyada dake tsaye tsaye still akansa  cikin wata sarƙaƙƙiyar murya tace.
"Kayi haƙuri....ban...kula bane!"

Bai juyo ya kalleta bama bare tasa ran zai tanka mata, saboda haka ta ɗanja da baya tare da nufar hanyar fita da ga garden ɗin, gaba ɗaya jikinta yayi sanyi wasu ruwan hawayene suka cika idanunta, itakam batasan me yasa tazama wawiya har haka ba, sam batasan meyasa dazaran abu yashiga tsakaninta dashi take saurin kuka ba, da wannan tunanin ta isa ga babban ƙofan da zai sadata da falon Ummu, hannayenta tasanya ta share hawayen dake kan fuskarta, sannan ta buɗe ƙofar tashiga.

Shikuwa Sooraj tunda yakawar da kansa gefe baisake koda ƙwaƙƙwaran motsi ba, lumshe beautiful eyes ɗinsa yayi tare da maida kansa jikin kujeran, daddaɗan iskan dake hurawa acikin

garden dinne ke ratsa ko ina na jikinsa, hakan yasa yaji zuciyarsa ta ƙarayin sanyi.

Zieyada kuwa atare da Ummu suka haɗa Mango juice, babban jug ɗin da mango juice ɗin ke ciki Ummu ta bata tace tasanya a fridge, koda tasanya mango juice ɗin acikin fridge kaitsaye ɗakinta ta wuce, faɗawa kan gado tayi tare da lumshe manya manyan idanunta, da sauri ta ware idanunta tare da tashi zaune, hannayenta tasanya duka biyu ta murza eyes ɗinta, wani irin ƙaton ajiyar zuciya ta sauƙe alokacin da ta fuskanci cewa gizo ne idanunta ke mata, bawai shiɗin bane, wani irin yaar taji ajikinta sakamakon tunowa da cikin kyawawan idanuwansa da tayi, tabbas idanunsa kaɗai sun isa rikita duk wata ƴa mace, matuƙar zata kallesu, wani irin sirrin kyau ne ke ƙunshe acikin idanunnasa, aduk randa tsautsayi yasanyata kallon cikin idanunsa ji take kamar zata suma, wasu abubuwane ke yawo ajikinta yayinda takejin kanta kamar wata wawiya, eye balls ɗinsa tamkar magnet ne acikin nata idanun dake matuƙar zautar da ita, wani irin murmushine ya bayyana akan fuskarta wanda bata san ma tayi ba, sakamakon tunawa da kyakkyawar fuskarsa da tayi.

"Yana da kyau sosai!!"

Tafaɗa abayyane cikin wata irin murya me sanyi. "Ko abacci ma kyau yakeyi, shi komai nasa me kyau ne!!!" Tasake faɗa tana me murza ƴan yatsun hanunta, itakanta batasan maganganun da take faɗa suna fitowa fili ba, gaba ɗaya ashagalce take, fararen ƙafafunta ta zuro ƙasa tare da tashi tsaye, direct wajen window ta nufa, ɗan yaye labulen window'n tayi tare da soma bin ko ina dake cikin compound ɗin gidan da kallo, idanunta ta tsayar asetin ƙofar shiga garden ɗin, dai dai lokacin yafito daga cikin garden ɗin hanunsa riƙe da wani green apple, tafiya yake kansa tsaye yayinda skin ɗinsa keta walwali kallo ɗaya zaka masa kasan hutu da kudi sun zauna masa, tundaga wajen da take tana iya hango yanda tarin suman dake kansa ke sheƙi, gashi ya kwanta luf luf tamkar sajen dake kwance akan fuskarsa, bata taɓa ganin wani irinsa ba, shi na dabanne ko acikin maza, hannunta takai ta dafa glass din dake jikin window'n, fuskarsa kawai take kallo, akullum tana mamakin yanda yake rayuwarsa babu annuri akan fuskarsa, koda yaushe haka yake baka taɓa ganin dariyarsa, kafun kaji maganarsa ma wahala ne, shi komai nasa is difference, Maganan aurensa ne ya faɗo mata lokaci guda ta marerece fuska tare da ɗan taɓe soft lips ɗinta. "Wace zata aureshi?" tambayar da tayiwa kanta kenan azuci, amma sam batasani ba har sautin maganan yafito fili. Soft lip ɗinta na ƙasa taɗan tsotsa tare da soma karyar da yatsun hanunta, idanunta ne sukayi raurau kamar wacce zatayi kuka, ɗago kanta tasakeyi da niyan kallonsa, amma kuma saitaga kome kama dashi babu awajen, sake labulen tayi tare dakomawa kan gado ta zauna. "Mene nawa? Meyasa nake tambayar kaina abubuwan da basu shafeni ba? No wannan ba halina bane kawai sharrin zuciya ne!" Tafaɗi haka cike da tuhuman kanta, domin sam tasan tunanin rayuwarsa ba huruminta bane. Remote taɗauka tare da kunna ɗan madaidaicin tv plasman dake ɗakin, tashar MBC Bollywood takamo inda tasamu suna nuna film ɗin Sushant Singh da Kriti Sanon wato Raabta, yanayin film din sosai yaɗauki hankalinta musamman yanda taga suna wata kalan rayuwa a daji, sam saita manta da tunanin komai ta bada hankalinta ga kallo.

_RAJ_

Koda yabar garden direct babban falon gidan ya nufa, babu kowa afalon kamar koda yaushe hakan yasa kaitsaye yawuce ɓangarensa, yana shiga ya murzawa ƙofarsa key, gaba ɗaya zaman gidan ya ishesa, ayanzu bayason damuwar kowa ta dameshi, saboda haka yaciro wani tablet dake jikin bedside drawer ɗinshi, ɓare maganin yayi ya jefa abakinsa sannan yabi da ruwa, toilet ya wuce ya ɗauro alwala domin alokacin har ansoma ƙiraye ƙirayen sallan Magriba, direct masallaci ya wuce, tunda yayi Sallah Magriba bai tashi ba har saida ya sallame isha yayi azkar, yana fitowa daga cikin masallacin yasoma jin jiri na ƙoƙarin kadashi, lokaci guda kansa yayi masa nauyi, idanunsa sukayi luhu luhu, cikin dauriya yake tafiya ahaka har ya isa gida, yana shiga cikin bedroom ɗinsa ya soma rage kayan jikinsa, dagashi sai long jeans haka ya faɗa kan royal bed ɗinsa tare da jawo pillow ya ɗaura kansa akai, wani irin duhu yake gani a idanunsa, har takai ma da ƙyar yake iya buɗesu mintuna kaɗan wani irin nannauyan bacci ya ɗaukesa, daga yanayin yanda yake baccin idan ka gani kasan bana lafiya ba....

Washegari.

Tun da safe Ummu da Ziyadah keta ƙoƙarin haɗa breakfast a kitchine kasancewar yau Abba zai koma KD, jirgin ƙarfe 9 zaibi shiasa Ummu keta ɗawainiya tanason yayi break kafun yatafi, don ita tace dawowarta ba yanzuba saboda Sooraj. Ba abun da Abba yakeso kamar Tuwo hakan yasa yauma Ummu tuwo takeyi masa da moringa soup wanda yaji cow meat da biscuit bone, ƙarfe takwas daidai suka kammala gaba ɗaya aikinsu, Ziyadah ce ta jere komai akan dinning table, Koda Ummu tagama serving ɗin Abba kujera taja ta zauna, har Abba yafara cin abincin ya ɗago ya kalli Ziyada wacce tayi shiru kamar me tunani. "Jeki ƙiramin yayanki" Abba yafaɗa yana me duban tsadadden agogon dake ɗaure a hanunsa, cike da ladabi tamiƙe tare da nufar inda zai sadata da ɗakinsa, duk da cewa ƙirjinta dukan uku uku yake, amma haka ta daure, tana tura kanta acikin corridor ɗin da direct zai kaika ɗakinsa ta shaƙi daddaɗan ƙamshinsa wanda yake matuƙar hautsina tunaninta, wani irin sanyi taji yana busata cikin sanyin jiki taƙarasa jikin ƙofar ɗakinnasa, hanunta na rawa tayi knocking amma shiru ba'a amsa taba, cike da tsoro tasakeyin wani knocking ɗin nanma shiru babu amsa, ɗan jim tayi tare da juyawa zata koma, tunani tayi idan takoma me zata faɗawa Abba tace tayi knocking ba a buɗeba ko me? hakan yasa tayi karambani'n murɗa handle ɗin ƙofar, kamar da wasa kuwa taji ƙofan ta buɗe, wani daddaɗan ƙamshi tare da sanyin AC ne suka daki fuskarta har saida ta lumshe idanunta. Ahankali taɗan kutsa kanta cikin ɗakin, kwance yake akan bed yayi irin kwanciyarnan ta ruf da ciki, dagashi sai dogon wando gaba ɗaya gadon a hargitse yake tamkar wanda akayi kokuwa akansa, kallonsa tayi tundaga ƙasa har sama, gaba ɗaya kwanciyanma baiyita a dai dai ba, domin kusan rabin ƙafafunsa suna lilo suba a sama ba suba a ƙasa ba, gangarjikinsa ne kawai ke kan gadon, idanunta ne suka sauƙa akan bayansa inda fresh white skin ɗinsa ke shining yana fidda ƙyallin zufa, mamakine yakamata ganin jikinsa na fidda gumi, domin kuwa sanyin ac ne keta tashi acikin ɗakin, hatta tiles ɗin dake malale aƙasan ɗakin yaɗauki sanyi sosai, sam takasa sanin bacci yake ko kuwa idanunsa biu, cikin yanayi naɗan tsoro ta ɗan tako zuwa tsakiyan ɗakin, muryarta akarye tace "Yaa..." kasa ƙarasawa tayi, ɗan cije laɓɓanta tayi tare da rumtse idanunta, gaba ɗaya jarumtarta ta tattaro tace "Ya--yah!" Jin shiru bai amsa ba yasanya tace "Dama Abbane yace naƙiraka!" shima dai shiru babu amsa hakan yasa taɗan matsa kusa dashi, jin zuciarta take kamar zata fashe saboda fargaba, da ace zai juyo ya kalleta

alokacin to tabbas abu me sauƙine ta sume masa awajen.   "Ya--Yah katashi!" Ta sake faɗa tana ɗan leƙa fuskarsa, domin yanzukam taga alamun cewa bacci yakeyi.   Ko motsi baiyiba balle tasaran zai bude idanunsa har yatashi kamar yanda take ɓuƙata,  cike da karanbani taɗan sanya hanu ta bugi katifan da yake  kai,  tun tana ɗan bugawa ahankali harta gaji taɗan buga da ƙarfi, still ko motsawa baiyi ba, hakan yasa tasa hanu tashiga jan bedsheet ɗin dayake kai cikin shagwaɓan da batasan ta iyaba tace.
"Please Ya--yah wake up!"   cikin bazata taga ya mirgino tare da juyowa hartana iya kallon fuskarsa saidai kuma bai buɗe idanunsa ba,  da sauri taɗauke idanunta daga kan faffaɗan chest ɗinshi,   cike da ƙosawa taɗan bubbuga ƙafafunta aƙasa murya agajiye tace "Nidai dan Allah katashi aikoni fa akayi!"   Bawai baitashi bane duk abubuwan da takeyi masa yana jinsune tamkar amafarki, sam ƙarfin maganin baccin da yasha baigama sakeshi ba, ko sallan asuba daƙyar ya iya tashi yayi nanma agida yayi baije masjid ba, ƙasa ƙasa yaɗan buɗe sexy eyes ɗinshi wanda sukayi masa matuƙar nauyi, dishi dishi haka yake ganinta hakan yasa ya maida idanunsa ya kulle, sam batama lura da cewar ya ɗan buɗe idanunsa ba, blanket ɗin dayake kai taja da ƙarfi waiko zai tashi amma sam ko sake motsawa baiyi ba,  hawayene suka cika idanunta sai kawai ta juya tabar masa ɗakin.  Tana shigowa cikin falon tasamu Abba da Ummu tsaye harsun kammala cin abincinsu.   "Ya haka naganki ke ɗaya ina Sooraj ɗin?" Ummu ta tambaya tana me ƙarewa Ziyada'n kallo, domin kuwa baƙaramin jimawa tayi aɗakin Sooraj ɗin ba.

Sunkuyar dakai ƙasa tayi cikin muryarta me sanyi tace. "Bacci yakeyi, tun ɗazu nake tashinsa kuma baitashi ba!"

"Bacci?" Ummu ta tambaya cike da mamaki.

Kai Ziyada ta ɗaga mata alamar "Eh"

"Badamuwa ku barshi idan yatashi zamuyi waya, yanzuma haka nakusa makara!" Abba yafaɗi haka yana me nufar hanyar barin falon, Ummu ce ta rufa masa baya, ita kuwa Ziyada  ɗakinta ta wuce domin kuwa lokacin da MBC Bollywood zasu fara haska series ɗin Ishqmeinmarjawan *(حب خادع)*  ya kusa kuma bataso tayi missing saboda sosai series ɗin keyi  mata dadɗi.

11:00 am daidai ya soma ware idanunsa ahankali har ya buɗesu  duka,  gani yayi kamar ɗakin na juya masa hakan yasa ya maida idanunsa ya rufe, mintuna uku tsakani yasake buɗewa, yanzu kam daidai yake ganin komai, jiyayi gaba ɗaya jikinsa yayi wani iri tamkar anyi masa duka, hannunsa yakai ya shafa tulin sumar dake kansa wanda yasha askin afro,   ƙafafunsa ya zuro ƙasa tare da miƙewa tsaye, hannu yasanya ya zuge zip ɗin wandon  dake jikinsa,  yana tafiya haka yacire wandon sannan ya buɗe wata ƴar glass drawer sabon white colour bathrobe na maza  ya ciro ya sanya ajikinsa, direct bathroom ya wuce,  wanka yayi sannan ya haɗa da brush,  yana fitowa ya jona handryer, dashi yayi amfani wajen busar da lallausan  gashin kansa,   sama sama yashafa mai ajikinsa,  wani oil and body perfume me daɗin ƙamshi ya shafa ajikinsa.   Kasancewar yau Jumma'a  yasanya shigar da zaiyi yauɗin ta da bance, duk da cewa shi baiwani damu da manyan kayaba amma time to time yana ɗan sanyawa,   wata

haɗaɗɗiyar getziner blue colour wacce kuɗinta ya haurawa  40k ya zaro daga cikin tarin kayansa wanda yawansu basu faɗuwa,  wani haɗaɗɗen half cover shoe me kalan blue wanda akawa samansa ado da ɗan ratsi ratsin golding ash  ya zaro daga ma adanan takalmansa, takalmine me kyaun gaske wanda aka sanya kuɗaɗe wajen sayansa, Hulan daya zaro ma ta musammance itama ajikinta akwai ratsi ratsin golding ash da blue,   Saida yagama kimtsa kansa cikin getziner'n wacce tasha ɗinkin half jumper, sosai yayi wani irin kyau me ɗaukar hankali, takalma ya zura aƙafafunsa sannan ya soma ƙoƙarin ɗaura agogon sa na companyn Gucci me tsadan gaske,  yana kammalawa ya sanya hula akansa,  baƙaramin kyau Sooraj yayiba acikin wannan shigan, wani irin ɗaukar hankali kwalliyartasa keyi, ga sajensa daya kwanta akan fuskarsa, juyawa yayi yaɗan kalli mirror, shikansa baƙaramin kyau yaga yayiwa kansa ba, musamman yanda kwarjininsa yasake bayyana afili, sosai ya fito a cikakken Namiji wanda ya amsa sunansa,  turarukansa ya ɗauka ya feshe jikinsa da su take ɗakin ya gauraye da sassayan ƙamshinsa mai sanya nutsuwa,    wayarsa yaɗauka yasanya acikin aljihunsa tare da ɗaukan key ɗin Black Range rover car ɗinsa,   cikin takunsa me ɗauke hankali yake tafiya Iya kyau yayishi har ya gaji   (Team RajZiyada please kuyi imagine  yanda Sooraj ɗinku ya haɗe.lol)

Ahankali take saƙƙowa daga kan step ɗin dake cikin falon, Plate ɗin da taci abincine riƙe ahanunta tafito daniyar zata kaisa kitchine,   ƙamshin dayake kashe mata jiki yake kuma sanyata acikin wani irin yanayi shine yafara dukan hancinta lokaci guda ya gauraya da numfashinta, saboda tsabar daɗin ƙamshin batasan sanda ta lumshe kyawawan idanunta ba, tana buɗesu kuwa idanunta suka sauƙa akan zallan kyawu da kwarjinin dake dosowa cikin falon, wani irin dokawa taji ƙirjinta yayi, take jikinta yasoma karkarwa kamar maijin sanyi batare data kulaba tayi missing step ɗaya take tatafi zata faɗi da sauri tariƙe ƙarfen dake gefen matattakalan plate ɗin hanunta kuwa faɗuwa yayi dayake plate ɗin  irin na cikin gift set ɗinnan ne tassss haka ƙaran fashewarsa ya cika falon,  jin ƙaran fashewan abu abayansa yasanya shi juyowa, ido huɗu sukayi shida ida,  kallon yanda plate ɗin ya tarwatse awajen yayi, baiko sake kallon gefen da take ba yasakai yafice daga cikin falon yana gyara zaman agogonshi, ita kuwa Ziyada tamkar wacce aka dasa haka ta kasa motsa koda ɗan yatsan ƙafanta ne,  wani irin ƙarya idanunta ke mata don har yanzu gani take tamkar yana wajen.

"Zieyadah!"

Ƙiran sunanta da Ummu tayi shiyayi sanadiyar sauƙar da idanunta ƙasa murya asanyaye tace "Na'am"

Kallon plate ɗin daya tarwatse aƙasa Ummu tayi cikin ɗan mamaki tace.
"Ya akayi haka ta faru?"

"Umm dama bankula bane shine yafaɗi!" Ziyada tafaɗa tana me ƙoƙarin maida ƙwallan dake cikin idanunta.

"Inadai baijimiki ciwo ba?" Ummu ta tambayeta cike da kulawa.

"Eh!" tasake faɗa murya araunane.

"Shikenan to kidai kula kada yamiki illa, ni zan fita bazan jimaba zan dawo ki kula sosai" Ummu tafaɗa tana me gyara zaman gyalen dake jikinta.

"Adawo lafiya" cewar Ziyadah tana me ɗan satan kallon Ummu wacce tasha ado da gwala gwalai masu tsadan gaske, itakam da badon ɗan zaman da tayi acikinsu ba to tabbas da zatace ba Ummu bace ta haifi Sooraj domin sam jikin Ummu bainuna hakan ba zallan kudi da jindaɗi haɗi da wayewa kawai jikin Ummu ya nuna.

Haka Zieyada ta gyara wajen amma gaba ɗaya tunaninta yana wani waje daban, daga wani ɓangare na zuciyarta kuwa daɗi takeji ranan monday zasu koma makaranta.

Sooraj kuwa yana fita haɗaɗɗiyar car ɗinsa ya shiga tare da bata wuta,   kai tsaye Central Mosque ya nufa domin samun sallan jumma'a, koda aka idar da sallan daga masallacin direct JABI LAKE yanufa don sunyi da Mas'oud zasu haɗu acan.

Vote
&🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*🌈Kainuwa Writers Association*

*Wattpad*
@fatymasardauna

#romance

*Chapter 28*

Inda yake zaune wani secret wajene me kyau da burgewa, wajen tamkar garden haka yake domin anƙawatasa da korayen furanni masu sanyin ƙamshi.
Zaune yake akan wata haɗaɗɗiyar chair wanda aka ƙawata tsakiyanta da wani haɗaɗɗen table me kyau, drinks ne kala kala ke jere asaman table ɗin,  gefe dashi Mas'oud ne ke sipping coconut juice,  yayinda Sooraj ke aikin latsa wayarsa, azahirin gaskia idan kaga yanda  gaba ɗaya attention dinsa  ke kan  wayan zakayi tunanin wani abu me amfani yake aiwatarwa,

saɓanin haka kuwa kwata kwata  hankalinsa ba ga wayar yake ba, idanunsa ne kawai ke kan wayan amma gaba ɗaya tunaninsa yayi nisa izuwa wani ɓangare na daban,  duk abun dayake Mas'oud na kula dashi, ɗan aje cup ɗin coconut juice ɗin yayi tare da duban Sooraj...

"Bazaka taɓa daina sakanka adamuwa ba matuƙar bazaka fito ka faɗa mana damuwarka ba, haka kuma bazaka warke daga ciwon dake damun zuciyarka ba matuƙar ba zaka amayar da abun dake cikinta ba, har yaushene zakana ɓoye matsalanka RAJ? taya kake tunanin zaka samu sassauci da kuma nutsuwar zuciya bayan bakanemi hakan ba? shin ni bankai na zama abokin da zaisan matsalarka bane RAJ? tun muna ƙanana muke abota me yasa har yanzu bankai jigon dayakai sanin sirrinka ba?"  Duka waƴannan tambayoyin Mas'oud yayiwa Sooraj alokaci ɗaya fuskarsa ɗauke da damuwa.

Ɗan numfasawa Sooraj yayi tare da ɗago kansa,  ɗan kallon Mas'oud yayi sannan ya kau da kansa gefe,  lips ɗinsa ya ciza tare dayin wani shu'umin murmushi, wanda shikaɗai yasan ma'anarsa, cikin husky voice dinsa yace.   "Babu wani wanda zai fahimci matsalata Mas'oud, idan nafaɗa maka matsalata ba lallai ka yarda ba,  idan nace maka bansan waneneni ba nasan bazaka taɓa yarda ba, wannan dalilin shiasa banason nayi sharing damuwata da kowa, saboda damuwata damuwata ce ni kaɗai!" cikin wani irin yanayi ya ƙare maganar tare da haɗiyan wani saliva me ɗaci da ya tsaya a maƙoshinsa.

Cike da mamaki haɗi da rashin fahimta Mas'oud yace "Banfahimci inda kalamanka suka dosa ba Sooraj, me hakan yake nufi?"

"Aure ne banaso Mas'oud, sam banason zama da kowace mace, nafison nayi rayuwata ahaka" ɗan tsagaitawa da maganan yayi tare da kallon kansa, daɗan ƙarfi ya cije laɓɓan bakinsa kana yaci gaba da cewa "Bazan taɓayiwa wata mace amfani amatsayin namiji ba, niba kamarka bane bakuma kamar sauran maza bane, inada rauni Mas'oud inada rauni wanda yake barazanar durƙushewar rayuwata, ita ƙaddara tana iya zuwa wa bawa aduk yanda baizata ba, ta ɓangarena haka tawa ƙaddaran take, amma banajin akwai wata wacce zata rayu dani ahaka, banajin zanyi wani farinciki.... "  Kasa ƙarasa maganan yayi sakamakon wani irin nauyi dayaji ƙirjinsa yayi,  bada kowani lokaci yacika yin magana me tsawoba, hakan yasa yanzu yakejin kansa tamkar zai faɗo ƙasa, yayinda yakejin tamkar ana hura masa wuta acikin ƙirjinsa.  Bottle water Mas'oud ya miƙo masa, babu musu ya amsa bai aje bottle water'n ba har saida ya tabbatar da babu wani sauran ruwa acikin goran, wani irin ajiyar zuciya mai ƙarfi ya sauƙe, ɗago idanunsa da suka soma rikiɗewa daga farare zuwa jajaye yayi ya kalli Mas'oud daya kafesa da idanu,    wani ɗan murmushi yayi tare da sanya hanu yashafi sajen dake kwance akan fuskarsa.

"Zan tafi, kada ka manta ranan monday muna da meeting" yanakaiwa nan azancensa ya miƙe tsaye kota bakin Mas'oud bai tsaya jiba yayi gaba, binsa  Mas'oud yayi da kallo har ya ɓacewa ganinsa, wani irin iska me zafi Mas'oud ya fesar tare da sanya hannuwansa ya dafe kansa,  sai ayanzu brain ɗinsa ke ƙoƙarin harhaɗo masa matsalolin Sooraj, batun yauba ya kamata ace yagano menene matsalan, tunanine barkatai suka shigo cikin brain ɗinsa, wasu abubuwa daya

tuno da kuma maganganun da sooraj yafaɗa masa yanzu sune suka taimaka wajen kawo masa haske daga duhun daya shiga, wani irin faɗuwa yaji gabansa yayi yayinda bugun numfashinsa ya soma fita da sauri sauri,  abayyane ya furta.
"Innalillahi wa'inna ilaihirraju'un!!"  kansa ya kifa ajikin table ɗin, take yaji ruwan hawaye naƙoƙarin cika idanunsa, da sauri ya yi ƙoƙarin maidasu, car key dinsa ya ɗauka, haka ya bar wajen jiki babu ƙwari.

Sooraj kuwa tafiya kaɗan yayi ya gangara gefen titi tare da yin parking din motar,  kansa yakifa akan steering motar tamkar me bacci, aƙalla yaɗauki sama da 30 minute awajen har saida yajisa ya fara zama normal sannan yasake ta da motar ya cillata kan titi.
***
Monday.

Kamar yanda duk wani ma'aikaci da student's  sukasani Monday ranace me mahimmanci agaresu, sannan kuma ranace da ko wani ɗalibi yakewa kansa shirin makaranta na musamman kasancewar ansha hutu harna tsawon kwana biu.

Ɓangaren Ziyada ma hakance takasance domin kuwa yau zasu koma makaranta inda zasu tafi S.S.2

Tun ƙarfe 5 da ta tashi tayi sallan asuba bata yarda takoma bacci ba,  ƙarfe shida da rabi daidai ta shiga toilet donyin wanka.

Wanka da brush tayi sannan ta fito ɗaure da towel ajikinta, zama tayi agaban mirror tare da ɗaukan body lotion  ɗinta ta shiga shafawa ajikinta,  normal green tea powder ta shafa akan fuskarta tare da goga wani man leɓe me kalan pitch,  eye black pencil taɗauka tagoga acikin idanunta, take idanunnata suka ƙara bayyana kyawu da girmansu,  tashi tayi daga gaban mirror'n tare da buɗe drawer tazaro gogaggun uniform ɗinta,  tsab tashirya kanta cikin riga da wando na uniform ɗinnata wanda yake matuƙar amsar jikinta, zama tayi akan bed tare da ɗaukan white socks ɗinta  ta zura a ƙafafunta, dogon gashin kanta ta kanannade tare da kamasa da ribbom, ɗan madaidaicin hijab ɗinta ta sanya,  ƙarasawa gaban mirror tayi tare da duban kyakkyawar fuskarta, ita kanta tasan tayi mugun sauyawa wani irin haske tare da kyau ne suke sake bayyana atattare da ita akullum kwanan duniya, sau da dama idan ta dubi kanta amadubi takan ga kamar ba itace Ziyadan ƙauye ba, kamar sauyata akayi, musamman ma yanzu da hips ɗinta suka ƙara cikowa shape ɗinsu yazama abun ɗaukar hankali, shiyasa bata taɓa yarda ta zauna haka batare data rufe jikinta ba, ita kanta yanzu tasan cewa cikar ƴan matancinta da bai bayyana ba ada, shine yake  bayyana yanzu, domin kuwa ayanzu babu wani abu daya rage na ƴanmatanci ajikinta da baifito ba, saidai kuma ita kaɗaice tasan haka kasancewar bata yarda kayan da take sawa su nuna hakan.

Tana kammala kimtsa kanta tajawo ƙatuwar school bag ɗinta ta aza akafaɗanta, har wani sanyi takeji aranta yau zataje taga ƙawayenta Nasmah da Shukrah sosai take kewarsu.

7:15 am  Ahankali take sauƙowa daga kan step ɗin yayinda ta kanannaɗe hannayenta acikin hijabinta.

Ummu ce zaune acikin katafaren falon, laptop na companyn apple ne aje agabanta da alama wani aiki takeyi, kasancewar har da wani ɗan madaidaicin farin glass dake sanye a idanunta.

Karasowa cikin falon Ziyada tayi cike da ladabi tarusuna tare da cewa.  "Barka da da safiya Ummu Ina kwana!"

Juyowa Ummu tayi fuskarta ɗauke da murmushi da "Lafiya" ta amsa mata sannan taƙara da cewa
"Har kinshirya da wuri haka?"

Murmushi tayi tare da ɗan kaɗa kanta alamar "Eh"

Agogo Ummu takalla taga babu wani sauran time hakan yasa tace da Ziyada ta ɗauki food flask ta sanya abinci aciki tatafi dashi,  hakan kuwa Ziyada tayi, koda tazo fita daga cikin falon tsaida ita Ummu tayi ta bata 500 tace tasaya chocolate,   cike da jin nauyi Ziyada ta girgiza kanta alamar bazata amsa ba.
Murmushi Ummu tayi ta tura mata kuɗin acikin jakanta sannan tahaura sama.   Fitowa tayi daga cikin falon tana ƙara gyara zaman school bag ɗinta wanda yake rataye kan kafaɗanta.    Kamalu driver ta tarar tsaye ajikin mota yana jiranta,  tafiya ta cigaba dayi tana me gyara igiyan jakar makarantarta.   Kansa tsaye yake tafiya yana me ƙoƙarin maida wayarsa daya amsa ƙira yanzu cikin aljihun wandonsa, babu wanda yakula da wani acikinsu, sam bata ankaraba saiji tayi ta buge mutum, kafun ta gama daidaita nutsuwarta ma tuni fitinannen ƙamshinsa ya gauraya da numfashinta, aɗan daburce taja baya,  chest ɗinsa daidai saitin inda kanta ya buga ya ɗan riƙe,   bakinta na rawa tace "Dan Allah kayi haƙuri bansan kana zuwa bane!"

Kallonta yayi daga ƙasanta har sama, yana kawowa  daidai  fuskarta yatarar da ƙwalla sun cika idanunta, ƙiris suke jira su gangaro.   Wani irin haushi da takaicinta ne suka cikasa, cikin wata murya me ɗauke da amo yace  "Are you insane?"

Ƙasa tayi da kanta aikuwa saiga hawaye kam sun ziraro kan kuncinta.    Wani baƙincikintane yasake kamasa, hannunsa yakai ya kamo haɓanta tare da ɗago fuskarta,  manya manyan idanunta ta zaro waje tana kallonsa,  bazato ba tsammani ya hankaɗata gefe yayi shigewarsa abunsa,  ƙiris yarage tafaɗi, wani irin wawan ajiyar zuciya ta sauƙe tare da ɗaukar school bag ɗinta data faɗi ƙasa ta nufi wajen Kamalu driver.

Tunda suka ɗauki hanyar makarantar take tunani, akan fuskarta kuwa hawayene caɓa caɓa, wasu na koran wasu.

"Me turetan da yayi yake nufi? wulaƙanci kenan kome?" abun da take ta tambayar kanta kenan.  Wata zuciyarta ce tace da ita "Baki da hankali Ziyada, dama irin waƴannan mutanen idan ba

alfarma ba mene zai haɗaki dasu? sam baki da daraja da kimar da zaki raɓesu"  Hannu takai kan fuskarta ta share hawayenta,  aranta taƙudiri aniyar zatayi karatu sosai itama ta zama wata, daganan saita fita daga cikin rayuwarsu baki ɗaya.  Da wannan tunanin azuciyarta har Kamalu driver ya ajiyeta acikin makarantar, tun bata gama fitowa daga cikin motar ba Nasmah ta taho da sauri ta rungumeta, wani irin daɗi Ziyada taji tuni ta manta da wata damuwa itama ta rungume Nasmah...

"I miss u so much my ƙawa!" Nasmah tafaɗa cike dajin daɗin ganin Ziyada.

"Miss you too!!" Ziyada itama tafaɗa tana murmushi, ƙarasowar Shukra yasa Ziyada sakin Nasma, ta rungume Shukra dukansu dariya suka sanya cike dajin daɗin ganin juna, suna maƙale da juna haka suka nufi wajen taron assembly, koda aka kammala assembly'n  direct sabon ajinsu suka nufa S.S 2A.   Kamar yanda suke a wancan ajin hakama suke a wannan ajin sit ɗinsu ɗaya, Ziyada ce ke tsakiya sai Nasma da Shukra dake gefenta.

Ƙarfe 10 am daidai  aka fito dasu break,   kai tsaye wajen da aka tanada na musamman doncin abincin ɗalibai suka nufa, soyayyen doya da chicken sauce din da Ziyada ta zo dashi shi suka fara ci kafun daga bisani suka ɗaura da snacks.

11:00 am

Mota ƙirar Jeeb ce baƙa tayi parking awajen da ake faka motoci dake cikin school ɗin,    Farouk wani irin ajiyar zuciya me sanyi ya sauƙe tare da lumshe sexy eyes ɗinsa, sai yanzu yaji sanyi acikin ransa da ya gansa acikin  makarantar,  zare key ɗin motar yayi tare da buɗe murfin motar ya fito, sanye yake da jumper na  shadda sky blue wanda taji aiki me kyau,  sanye yake da tsadaddiyar hulan zanna akansa wanda ta ƙarawa fuskarsa kyau, sosai yayi kyau sai fidda ƙamshi yake,  bayi da tantama akan inda zai sameta saboda haka direct office ɗin principal yanufa, koda yaje permission ya nema akan yanason ganin wata ɗaliba mesuna Ziyada Mansoor Mainasara, domin da wannan sunan akayi mata register. Da yake  principal ɗin ya sanshi, babu ɓata lokaci ya tura S.S 2A don aƙirata kasancewar a time ɗin sungama break harsun koma class.

Ba ƙaramin faɗuwa gaban ziyada yayiba jin wai ana ƙiranta daga office ɗin principal,  gaba ɗaya tunaninta ya tsaya cak, a iya saninta bata da wani wanda zaizo nemanta, haka ta nufi office ɗin principal ɗin zuciyarta cike da fargaba,  a corridor ɗin dazai sadata da office ɗin idanunta sukayi mata tozali dashi, wani irin duka taji ƙirjinta yayi sai kawai ta tsaya cak tare da sunkuyar da kanta ƙasa, murmushin daya bayyana cute dimples ɗinsa yayi tare da takowa zuwa gareta, wani irin kallo yakeyi mata, komai nata ya sauya tasakeyin kyau sannan taƙara girma duk dacewa ba jiki tayi ba amma tabbas kallo ɗaya zakayi mata kafahimci cewa ta ƙara girma.   Gaf da ita ya matso har yazama baifi saura taku ɗaya tsakaninsu ba.  "I miss you!!" yafaɗa cikin wata irin murya yana me kallon small lips ɗinta.

Murmushine ya bayyana akan kyakkyawar fuskarta, ahankali taɗago da fuskarta idanunsune

suka faɗa cikin na juna ƙasa tayi dakanta tana mai wasa da yatsun hanunta, sam bataji wani abuba da takalli cikin idanunsa, saɓanin Oga Sooraj da idan takalli cikin beauty eyes ɗinsa take rasa nutsuwarta.

Kallon yanda take lallanƙwasa yatsun hanunta yayi, yaɗan saki murmushi, jiyake kamar yajawo ta jikinsa ya bata tight hug, komai nata na musammanne babu abun dake burgesa atattare da ita kamar sanyinta.

"Muje mu zauna ko!" yafaɗa yana meyi mata nuni da wata bishiya wacce ƙasanta ke ɗauke da wani bench wanda akayi da cement. Bata iya musa masa ba saidai har yanzu kanta aƙasa yake, zama tayi akan bench ɗin tare da jawo hijab ɗinta ta ɗan rufe gefen fuskarta, shima akan bench ɗin ya zauna har ƙamshinsu na iya gauraya waje guda. "Nayi kewarki da yawa, bazan sake bari kiyimin nisa har haka ba, bansan da yaushene kika kama zuciata ba, please My cute babyy na ki juyo na kalli fuskarki!" yaƙare maganar cikin sanyin murya.

Har acikin ranta taji kalamannasa saidai tanaji kamar sunyi mata nauyi. Hannayenta tasanya taɗanja hijab ɗinta baya, tare da ɗago kanta ta kalleshi, shi ɗinma kallonta yake, murmushi ya sakarmata tare da ɗanyin ƙasa ƙasa da idanunsa, wani iri taji ajikinta hakan yasa itama taɗanyi masa murmushi. Cikin muryar shagwaɓa tace "Shine kaɗauko ni daga aji bayan kasan karatu zamuyi ko!"

"am sorry babyyyna inason ganinki sosai shiyasa."

Murmushi tayi tare daɗan satan kallonsa, Idanunsa ɗaya ya kashe mata hakan yasa ta cusa kanta acikin cinyoyinta tana sakin wani smile, agogon dake ɗaure a tsintsiyar hanunsa ya duba, time ɗin dazai koma office yakusa hakan yasa shi kamo hanunta, da sauri taɗago kanta ta dubeshi murmushi yayi mata tare da sake matsowa daf da ita, cikin wata irin murya me sanyi yace. "I love you!!!"

((( "Fatymasardauna kina mana rowan Sooraj" "Teemah sardauna bakya kyauta mana gaskiya bakya mana update da wuri" "Please me yasa yau bakiyi Sooraj ba?" "Haba teemah don Allah kina mana update akan lokaci" "Gaskiya typing ɗin da kike mana yana kaɗan please ki ƙara mana yawan page" Irin waƴannan ƙorafe ƙorafen kullum nake samu daga wajen wasunku, am really sorry bani da wani buri daya wuce nafaranta muku amma kuma lokaci yanamin jinkirin hakan, idan ta sonane kullum na baku update na Sooraj amma kuma hakan baya yiwuwa, please kunamin uzuri nima ba ason raina hakan ke faruwa ba, idan nace zanna muku typing kullum to kaina zaiyita min ciwo ne nasan kuma bazakuso hakan ba don Allah kuɗau uzurina, nasan kuna sona kuma kuna ƙaunar novels ɗina, nima kuma inasonku sosae sosae 💞)))

*Vote*🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
phatymasardauna

*Dedicated To My life (Sardauna)*

*Wattpad*
@fatymasardauna

#romance

*Chapter 29*

"I love you!!!"  ya faɗa slowly yana me murza yatsun hanunta dake cikin nasa.

Da sauri ta ɗago golding eyes ɗinta ta kallesa, wani irin abune taji yana yawo acikin jikinta,  sam batasan me yasa wani yanki na zuciyarta ke ƙoƙarin  accepting ɗinshi ba,  hannayenta dake cikin nashi ta soma ƙoƙarin zarewa, babu musu yasake hannun nata, sai dai kuma be janye mayun sexy eyes  ɗinsa daga kanta ba.    Murmushin daya bayyana kyawunta tayi tare da miƙewa tsaye,  batare da ta kalleshi ba tace  "Zan koma class"
Shima miƙewa tsaye yayi tare da ɗan sakin murmushin daya sanya dimples dinsa loɓawa,  wani farin envelope yazaro daga cikin aljihunsa, wanda aka ƙawata bayan envelope ɗin da zanen flowers masu sheƙi, gwanin burgewa, miƙa mata envelope ɗin yayi,    ɗago ɗara ɗaran idanunta tayi ta ɗan  kalleshi,  mumushi yayi mata kamar zai shige jikinta haka ya sake matsowa gaf da ita, yanayin idanunsa ne suka sauya, take taji wani sabon abu na sauƙa ajikinta.   "Pleaseee!!" yaja maganan tare da ɗan ƙanƙantar da idanunsa.   Adaburce tashiga kakkare jikinta, sam bata sabayin irin wannan kusancin da wani namiji ba, gaba ɗaya duk abun da Farouk keyi mata ganinsu take wasu daban, kowacce kalma da zata fito daga bakinsa jinta take tayi mata nauyi, takan rasa nutsuwarta idan taganshi akusa da ita sosai, domin wani irin faɗuwar gaba takeji, ganin irin mood ɗin data shiga yasanyashi sake kamo soft hand ɗinta, envelope ɗin ya ɗaura mata akan hanunta, tare da bin kyakkyawar fuskarta da ido,    sam batasan da yaushene kuma ya akayi taganta tana tafiya ba, sauri tashiga yi burinta ɗaya taganta acikin class, gaba ɗaya ma ta manta da cewa basuyi sallama ba.  Shikuwa Farouk wani killer smile ya sake bayan yaga shiganta cikin class, baisan me yasa ba hakanan yake losing control ɗinsa idan yana kusa da ita,   ayanda ya fahimce ta  yarinyace wacce take real innocent, batasan komai agame da soyayya ba, da wannan daman zaiyi amfani wajen koya mata sonsa, zai koya mata yanda zata sosa fiye da kowa, daga ƙarshe kuma zaiyi ƙoƙari wajen ganin ya sameta amatsayin Mallakinsa,  sosai yake sonta, sosai yake kuma son kasancewa tare da ita.  Da wannan tunanin ya ƙarasa wajen da yayi parking motarsa.

Kamar wacce aka jefo haka ta faɗo cikin class ɗin, ko izinin  shiga  ajin bata nema ba.    da yake a bencin gaba suke kuma malamin dake cikin class ɗin,  gaba ɗaya hankalinsa naga board yana rubutu, shiyasa bai kula da shigowanta ba harta zauna,    kallonta  Shukra da

Nasmah sukayi,  cikin ƙasa ƙasa da murya Nasma tace.  "I hope ba wani abun kikayi ba, naga jikinki duk yayi weak"

Sai alokacin taɗan soma dawowa sense ɗinta, murmushi ta ƙaƙalo tare da girgiza kanta alaman babu komae. Nasmah bata sake cewa komai ba ta maida hankalinta ga karatun da ake musu.

Duk abunda Malamin Chemistry ɗin ya koya musu ta bayan kunnen Zieyaderh yabi ya wuce, sam ko kaɗan hankali da tunaninta ba akansa suke ba, tunaninta yayi nisa ne izuwa wani waje daban, Farouk shine wanda yayi tsaye aranta.

"I love you!!!"
kalmar daya furta  mata shiketa dawowa  cikin tunaninta, lumshe beauty eyes ɗinta tayi tare da sakin wani murmushi wanda batasan da bayyanarsa ba,  hakanan taji wani sanyi aranta, sosai daɗin kalman ke ratsata,  kulawa shine abun da ta rasa tun tana ƙarama, kalmar Soyayya kalmace da babu wani wanda ya taɓa furta mata shi, hakan yasa takejin ayanzu tamkar wani kyautan farinciki Farouk ya bata,  duk da cewa  kai tsaye bazata iya tantance me takeji agame dashi ba, amma tabbas zuciya koya take tanason me kyautata mata,  tana a wannan tunaninne har malamin chemistry ɗin yafita batare da ta saniba, kasancewar period ɗinsa ya ƙare,  dafa ta da Shukra tayi shi yayi sanadiyar ɓacewan tunanin da take.

"Lafiyanki ƙalau kuwa Zieyaderh?"
Shukra ta tambaya tana me ƙarewa fuskar Zieyaderh'n kallo.

Board ta kalla tare da ɗan waiwayawa bayanta, cikin mamaki tace.
"Wae ina chemistry teacher'n ya fita ne?"

"Da ke zai tsaya jira?" Shukra ta bata amsa tana me harhaɗa text books ɗin dake watse saman desk ɗinta.

Murmushi kawai Zieyaderh tayi tare da duban Nasmah, cikin sakewa tace.
"Gaskiya ban fahimci abun daya koyarba please Nasmah taimaka min"

Dukansu tsaida abunda sukeyi sukayi tare da kallonta.

"Bazaki taɓa fahimta ba ae tunda anzuba miki kalaman love acikin brain ɗinki" Shukra tafaɗa tana me guntse dariyar dake ranta.

Hararanta Zieyaderh tayi tare da cewa "Love kuma?"

Dariya Nasmah da Shukra sukayi tare da tafawa,   kallonsu tayi kawai itama saitayi murmushi, jujjuya envelope ɗin dake  hanunta ta shiga yi.

"Lover gurl!" Shukra tafaɗa tana  dariya.

Kallonta Zieyaderh tayi, cikin yanayi na shagwaɓa tace "Allah Shukra banaso fa"  Dariya dukansu suka sanya,  envelope din dake hanunta ta soma ƙoƙarin buɗewa, duk suka zuba mata ido.

Wani golding colour neck chain ne me kyau da tsadar gaske ne ya bayyana acikin envelope ɗin.

"Wow!!" Nasma da Shukra suka haɗa baki wajen faɗa, da sauri Nasma ta karɓi envelope ɗin ta ciro chain ɗin,     saboda tsabar kyawun chain din har ɗauke musu ido yake.

Kallon Zieyaderh Nasmah tayi  tare da cewa   "Gaskiya guy ɗinnan ya haɗu, wannan chain ɗinfa na gold ne, zaikai 50k fa!"

"Wasa ma kike, zai iya kai 60k wannan neck chain din, gaskia guy ɗinnan ya iya bada gift" Shukra tafaɗa tana me jujjuya chain ɗin ahanunta.

Zaro idanu Zieyaderh tayi sakamakon jin kuɗin chain ɗin, cikin yanayi na tsoro tace.
"Zan maida masa gaskiya ni bazan karɓa ba"

Baki Nasma da Shukra suka sake suna kallonta,  cikin nuna mata batasan me takeyi ba Shukra tace "Zaki mayar masa fa kikace?"

"Eh, bazan iya sawa ba gaskiya" Zieyaderh tafaɗi haka har acikin azuciyarta.

Dariya suka sanya su duka biyun, cikin dariya Nasmah tace
"Allah har yanzun baki waye ba babe,  ae idan masoyinka ya maka kyauta baka maida masa."

Murmushi kawai Zieyaderh tayi kana ta kifa kanta akan desk, wani abune taji ya tsaya mata arai, har abada bazata taɓa manta matsayinta da kuma wacece itaba, sam bazata yaudari kanta ba,  tanajin su Nasmah nata yaba neck chain ɗin tayi musu shiru,, Shigowan Islamic teacher yasanya su yin shiru, tare da bada hankalinsu gareshi.   Gaba ɗaya wunin ranan Zieyaderh asukurkuce tayishi, abu biyune ke tsaye aranta,   ƙarfe 5 pm daidai aka kaɗa musu ƙararrawan tashi.  Amatuƙar gajiye takejin kanta, sama sama sukayi sallama dasu Nasmah, kana  tanufi inda Kamalu driver ke tsaye yana jiranta,  gidan baya ta buɗe ta shiga, duk da cewa tafi yawan zama agidan gaba, don  bata damu da zaman gidan baya ba.
Tunda suka ɗauki hanya ta maida hankalinta kan titi,  sanyin AC'n dake tashi acikin motar ne ya sanya tasomajin sanyi,   hakan yasa ta duƙunƙune jikinta.

Saida sukazo gaban tamfatsetsen gate ɗin gidan Kamalu driver ya danna horn,  take aka wangale masa gate ɗin gidan ya tura hancin motar ciki.

Wata Black colour jeep ce tayi parking a gefen gidan, wanda tun barowarsu makaranta take biye dasu batare da sunsan da hakan ba.   Murmushi Farouk yayi tare da sauƙe ajiyar zuciya,

key ya sake yiwa motar tare dayin reverse,  sai yanzu yakejin sanyi  aransa,  sam bada wasa yakeson Zieyaderh ba, so yake ya mallaketa, so yake ta soshi fiye da yanda zata so kowa, aransa ya gama yarda da shawaran da zuciyarsa ta basa, saboda haka da confidence ɗinsa ya juya yakoma inda ya fito.

Kamalu driver na gama daidaita parking, agajiye ta buɗe murfin motar ta fice,  school bag na riƙe ahanunta ta nufi  hanyar da zai sadata da babban falon gidan,    bakinta ɗauke da sallama ta shiga cikin falon, babu kowa afalon sai TV plasma wanda yaketa aiki shi kaɗai,  direct sama ta wuce, kamar zata wuce ɗakinta sai kuma ta ƙarasa gaban ɗakin Ummu tayi knocking, daga cikin ɗakin Ummu dake zaune tana karanta jarida tace  "Yes come in"

Tura ƙofar ɗakin tayi tashiga bakinta ɗauke da sallama, ganinta yasa Ummu taɗanyi murmushi.

"Barka da gida Ummu" Zieyaderh tafaɗa cikin ƙasa da kai.

"Yauwa Zieyaderh kindawo ko, ya school ɗin?"

"Alhamdulillah!" Zieyaderh tafaɗa still aɗan kunyace, domin har acikin zuciyarta tanajin girman Ummu.

"Masha Allah, to je kicire uniform ɗin akwai abinci a dinning" Cike da kulawa Ummu tafaɗi haka.

Miƙewa Zieyaderh tayi tare da cewa  "to"

Har ta fice daga cikin ɗakin Ummu bata daina kallonta ba, hakanan alkunyan Zieyaderh'n ke burgeta, sam baruwanta da rawan kai, komai nata acikin sanyi takeyinshi, tabbas zata sowa ɗanta Almustapha samun kyakkyawar yarinya kamar Zieyaderh, ta yanke hukunci aranta zata samu Mas'oud suyi magana, lallai tanason ganin iyayen Zieyaderh, don tanason nemawa ɗanta Almustapha auren Zieyaderh a wajensu,  tasan Almustapha bazai taɓa ƙin zaɓinta ba, musamman ma idan yaga Zieyaderh tasan dole zai sota, dama kuma shi bai da wata matsala bakaman SOORAJ ba wanda komai nasa aƙa'idance yake.

Zieyaderh kuwa tana shiga cikin ɗaki ta soma rage kayan jikinta,  towel ta ɗaura aƙirjinta tare da shigewa bathroom,  da ruwa me ɗan ɗumi tayi wanka, take taji gajiyan dake  nannaɗe a muscles ɗinta sun soma warwarewa,   Ko body lotion bata shafa ajikinta ba ta zura wata slim net gown red colour ajikinta, wanda take da guntun hannu, sosai rigan tayi mata kyau,  hasken fatanta yasake bayyana sosai, wani mayafi me shara shara ta ɗauka tayane kanta zuwa ƙirjinta dashi,    ko bedroom slippers bata sanya ba haka ta buɗe ƙofar ɗakin ta fice,  wani irin yunwane ke ƙwaƙulan cikinta,  kaitsaye dinning area ta nufa, food flask ne masu kyaun gaske jere a kan babban royal table ɗin,  kulan farko data buɗe white rice ne aciki wanda yaji carrot da piece, ɗayan kulan kuwa chicken soup ne wanda za aci shinkafan dashi, su kaɗai ma sun wadaceta hakan yasa bata bubbuɗe sauran food flask ɗin ba,   ɗiban abincin tayi ta sanya a plate, direct kitchine ta wuce don ɗaukan ruwa,   sam bata taɓa tunanin zata tarar da wani acikin kitchine

ɗinba kasancewar yanda taji gidan ya ɗauki shiru alamun banda Ummu da ita babu kowa acikin gidan,  bata damu da gyalenta daya zame daga kanta har yayi sanadiyar fito da tsefeffen gashin kanta ba, kasancewar gyalen yana da santsi shiyasa yaketa zamewa ajikinta.

Tanashiga kitchine ɗin taga baki ɗaya wutan kitchine ɗin akashe suke, abun da bata taɓa gani ba kenan, gashi garin yasoma yin duhu hakan yasa bakomai dake cikin kitchine ɗin take iya gani ba, dayake tasan wajen da makunnan wutan suke sai kawai ta ƙarisa ta kunna wutan, take haske ya mamaye gaba ɗaya kitchine ɗin, bata damu data waiga bayanta ba ta nufi wajen fridge,  buɗe murfin tayi ta ciro bottle water me ɗan sanyi.  Tana juyawa idanunta suka faɗa cikin nashi, take ta sake goran dake  hanunta ya faɗi ƙasa,  buɗe manya manyan idanunta tayi cike da mamaki taɗan kalleshi,   zaune yake akan saman wata ƴar madaidaiciyar drawer, dagashi sai long jeans ba shida ko riga ajikinsa, fresh naked skin ɗinsa sai shining take, wani cup ne riƙe ahanunsa wanda cikinsa ke ɗauke da black coffee, tun shigowarta cikin kitchine ɗin yake kallonta, harzuwa yanzu kuwa bai ɗauke idanunsa akanta ba,  wani irin bugawa taji heart ɗinta nayi amma saita ɗan daure, tsugunawa tayi ta ɗauki goran ruwan tare da miƙewa tsaye, gaba ɗaya a tsarge takejin kanta,      Ahankali ta juya ta nufi hanyar fita daga kitchine ɗin.

Cikin husky voice ɗinsa yace da ita.  "Zoki bani ruwa"

Cak ta tsaya da tafiyan da takeyi tare da juyowa taɗan saci kallonsa, har yanzu bai ɗauke idanunsa  akanta ba,  zuwa tayi ta buɗe firjin tare da ɗauko masa bottle water me sanyi, cikin yanayi naɗan rusunawa ta miƙa masa, idanunsa ne suka sauƙa akan ƙirjinta, da sauri yakawar da kansa gefe tare da taɓe baki, cikin rashin kulawa yace "Ajiye" agefe dashi ta ajiye, cikin sanyin jiki ta juya zata fice daga cikin kitchine ɗin.

"Waye kika ajiye da zai kashe miki wutan da kika kunna?"  ƴajefo mata tambayar yana me jujjuya spoon ɗin dake hanunsa.

Tsayawa tayi daga tafiyan da takeyi tare da juyowa,  jiki asanyaye ta ƙarasa ta kashe makunnin wutan,  tana fita daga cikin kitchine ɗin ta saki wani wawan ajiyan zuciya, tare da ɗaukan plate ɗin abincinta da sauri ta haura sama.    Shikuwa coffee ɗinsa ya cigaba da sha, sam duhun dake cikin kitchine ɗin bai damesa ba, sometimes yafison zama acikin duhu fiye da zama acikin haske.

Aƙasa ta zauna tare da tanƙwashe ƙafafunta, har yanzu ƙirjinta be daina bugawa da ƙarfi ba, hannu tasanya acikin plate ɗin, saidai takasa kai koda loma ɗaya ne na abincin cikin bakinta, gaba ɗaya tayi losing nutsuwarta, ganinsa da tayi yanzu ya matuƙar hautsina tunaninta, ba komai ke ruɗar da ita ba kamar zallan kyau da kwarjininsa, sosai takejin wani iri aduk sanda tayi gamo dashi,  lumshe  kyawawan idanunta tayi tare da jingina bayanta da jikin gado, shock ɗin da ta shiga lokacin da idanunsa ke yawo ajikinta tane, ya shiga yadawo cikin brain ɗinta.
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ!!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

*Chapter 30*

Haka ta daure ta cuccusa abincin wa cikinta zuciyarta cike da tarin tunani, tana kammalawa tayi sallan magriba, bayan tayi sallan isha ne tabi lafiyan gado, da yake agajiye takejin kanta take bacci ɓarawo ya ɗauketa.

_SOORAJ_

Yana gama sipping black coffee tea ɗinsa, ya aje cup ɗin tare da miƙewa tsaye ya fice daga cikin kitchine ɗin, direct ɗakinsa ya wuce, toilet yafara shiga yayi wanka sannan ya ɗauro alwala, wata blue t-shirt ya sanya kana ya wuce masallaci.
Bashi yadawo gidan ba sai ten pm dai dai, wanka ya sakeyi sannan yafito ɗaure da towel a weast ɗinshi, ɗan ƙaramin towel ya ɗauka agaban dressing mirror ya shiga goge kansa, duk da cewa bai shafa turare ba amma gaba ɗaya ƙamshin sabulun da yayi wanka dashi ya cika ɗakin, wani body lotion wanda baya kama jiki sosai ya shafa ajikinsa, turarensa me sanyin ƙamshi ya ɗauka tare da fesawa, cumb ya ɗauka ya taje kwantacciyar sajen dake kan fuskarsa, ɗan kallon kansa yayi amadubi lokaci guda kuma ya kawar da kansa gefe, pink lips ɗinsa ya ɗan ciza, wani tunanine yazo ransa hakan yasanyashi sakin murmushin daya bayyana zallan Kyawunsa, shi kansa baisan da yayi murmushin ba, direct gaban drawer ɗinsa ya nufa tare da zaro kayan dazai sa, riga da wando na black jeans ya sanya ajikinsa wanda sukayi matuƙar yi masa kyau, White kambas masu kyau yasanya aƙafafunsa, tare da ɗaura hulan white facing cap akansa, sosae da sosae yayi kyau harma baka iya tantance kammaninsa saboda yanda hulan ta ɓoye fuskarsa, wayoyinsa ya ɗauka tare da ɗaukan car key ɗinsa, yana fita daga cikin ɗakin ya murzawa ƙofar key tare da tura key din cikin aljihun wandonsa, koda ya fito ko ina dake cikin gidan ya ɗauki shiru, direct parking space ya nufa, mota ƙiran kia yashiga tare dayi mata key, koda ya iso bakin gate taradda Maigadi yayi yana ta zuba gyangyaɗi, wani silent horn ya danna, take maigadi yatashi a zabure, cikin daburcewa ya wangale masa gate ɗin, ba ɓata lokaci Sooraj ya cilla hancin motar sa waje, kasancewar dare ne hakan yasa babu wani hayaniya sosai akan tituna, tuƙi yake cike da nutsuwa yayinda ya saƙala earpiece akunnensa.
Duk da sanyin AC'n dake tashi acikin motar hakan bai hanasa sauƙe glass ɗin window ba, wani irin ni'imtaccen sanyine ke ratsa jikinsa wanda har ma yafi na AC daɗi.

TRANSCOP HILTON.

Wangale masa makeken gate ɗin akayi, asukwane ya tura hancin motarsa cikin ƙawataccen compound ɗin hotel ɗin,   ababban parking space ɗin hotel ɗin yayi parking motarsa.

Ahankali ya zuro da ƙafafunsa waje, cikin takunsa me ɗauke da nutsuwa haka ya nufi cikin hotel ɗin, direct babban ɗakin da zasu gudanar dawani important meeting ya nufa,  gaba ɗaya kowa da kowa sun hallara shi kaɗai kawai ake jira, kasancewar shine jagoran meeting ɗin shiyasa basu fara ba dole saida suka jira yazo,  aƙalla sun ɗauki sama da 1 hour suna tattauna maganganu wanda gaba ɗaya su yasu suke abunsu,  Sooraj kam maganarsa bata wuce "Eh" ko "A'a"    Ko kaɗan basu wani damuba domin dama acikinsu babu wanda baisan halinsa ba, 11:30 pm daidai suka kammala meeting ɗin, kowa ya kama gabansa,  koda ya baro Transcop Hilton baikoma gidansu ba, direct gidansa ya wuce kasancewar gobe zai koma bakin aikinsa na Bank.

Washegari.

Kamar koda yaushe 7:15 daidai take kammala shirinta na zuwa makaranta, yauma hakance ta kasance domin tuni ta shirya kanta cikin uniform ɗinta,  school bag ɗinta ta ɗauka agurguje tafice daga cikin ɗakin,  bata tarar da kowa acikin falonba gashi har 7:30 takusa sam kuma bataso tamakara,   buɗe ƙofar falon tayi ta fice,  Kamalu driver ta iske tsaye yana jiranta, tana shiga cikin motar yaja suka tafi.
***
Tun 7 daidai yagama shirya kansa cikin wani tsadadden maroon colour suit and white long sleeve shirt, sosai yayi kyau acikin suit ɗin, wani dark maroon toms  ƙiran company'n Italy yasanya aƙafafunsa,  sosai kwalliyan nasa ya sake ƙawata. Agogon rolex ne ɗaure a tsintsiyar hanunsa, gaba ɗaya gashin kansa sai shining yake yana ɗauke ido, saboda sosai yasha gyara,   kamar wanda akawa ɓarin turare ajiki haka yake tashin ƙamshi,  sabuwar   black car ɗinsa mercedes benz yashiga,  direct bank ɗinsu ya nufa,   tun fitowarsa daga cikin mota mutane keta kawo masa gaisuwa, sama sama yake amsasu yana wucewa,   koda yakai office ɗinsa ya samu komai nead, dama kowa yasan bayason ƙazanta shiyasa always ake tsabtace masa office ɗinsa, sosai yatarar da aiki na jiransa saboda haka tunda yaje bai wani huta ba aiki kawai yaketayi a computer.

_Zieyaderh_

Tun fitowansu break take jin kanta wani iri, ga wani amai da tashin zuciya dake damunta, haka dae tayi break adaddafe suka koma class, duk su Nasmah na lure da ita, saboda ko magana sosai yau din batayi,   ƙarfe 1 daidai aka fito dasu sallah, zuwa lokacin abun yasoma fin ƙarfin tunanin Zieyaderh, saboda ciwon sosai ya tsananta, gawani irin zazzaɓi daya rufeta, koda ta idar da sallah  cusa kanta tayi tsakankanun cinyoyinta ta saki  kuka me sauti, don bazata iya jurewa ba, sosai mararta ke murɗawa, gawani sabon ciwon ciki me tsananin azaba da takeji, ganin irin yanda take kuka yasa Nasma da Shukra kamata suka fice daga cikin masallacin, aƙasan wata bishiya suka zauna su dukansu, cike da kulawa hadɗi da damuwa Nasmah ta dubi

Shukhra wacce idanunta sukayi raurau alaman itama kuka takesonyi. "Ki kula da ita Shukhra banaje na faɗawa discipline master, nasan zai faɗawa principal!" kae kawai Shukhra ta iya kaɗa mata alamar taji, saboda itama zuciyarta cike take da rauni haɗi da tausayin halin da Zieyaderh ke ciki, don zuwa yanzu numfashinta har seizing yake kamar zai ɗauke,

Sauri Nasmah keyi don taga ta isa office ɗin discipline master, kamar daga sama taji anƙira sunanta.

Tana juyawa tayi tozali da Pharouk, da sauri taƙaraso gareshi, kallonta yayi daga sama har ƙasa, ganinta aɗan hargitse yasanyashi cewa.
"Lafiya kuwa naganki ahaka? Sannan kuma ina kuka shige tun ɗazun naketa nemanku?"

"Zieyaderh ce batada lafiya sosai, yanzuma office ɗin discipline master zanje!"

Sexy eyes ɗinsa yaɗan waro tare da cewa. "Tana ina? Meke damunta? Muje kinunamin inda take!"

Babu musu Nasmah ta juya shikuwa yabi bayanta.. Lokacin dayaga Zieyaderh na kuka baƙaramin tashi hankalinsa yayi ba. Shida kansa ya je office ɗin principal yasanar dashi cewa zai wuce da Zieyaderh asibiti, su Nasmah ne suka sata acikin motarsa sannan suma suka shiga, zuwa lokacin gaba ɗaya hankalinta yasoma gushewa. Da wani irin speed Pharouk kejan motar. A babban haraban asibitin yayi parking, zuwa lokacin bata da ƙarfin da zata iya ko da taka ƙafarta ne, batare da tunanin komai ba Pharouk ya sanya hannayensa duka biyu ya ɗagota zuwa jikinsa, tamkar ƴar baby haka ya ɗauketa yayi cikin asibitin da ita, duk dacewa baya cikin ishashshiyar nutsuwa amma duk da haka daya ɗagata saida yaji wani shock ajikinsa. Emergency aka wuce da ita, take aka shiga bata kulawa.

Nasma da Shukhra gaba ɗaya basa cikin nutsuwarsu, ganin haka yasanyashi lallaɓasu tare dace musu su koma makaranta shi zai kula da ita, babu yanda suka iya dole haka suka hau taxi suka koma makaranta, saidai kuma gaba ɗaya hankalinsu naga Zieyaderh har acikin ransu basason wani abu na cutarwa ya sameta.

Zama yayi akan wasu kujeru tare da sanya tafukan hannayensa ya rufe fuskarsa, numfashi yake fitarwa ahankali, wani irin feeling yakeji ajikinsa, daga wata ɓangare na zuciyarsa kuwa tunanin halin da take ciki yake, yana awannan yanayinne aka fito da ita daga emergency room ɗin, kwance take flat akan wani gado me ƙafafun taya, kaitsaye ɗakin hutu aka wuce da ita. Likitan da case ɗin ke hanunsa ne yace da Pharouk ya biyosa office.

Zama Pharouk yayi akan kujeran dake fuskantar na Doctor, cikin damuwa yace. "Yajikinnata?"

"Kada ka damu jikinta da sauƙi dama bawani babban ciwo bane, nace dama tana irin wannan ciwonne aduk sanda zatayi period ko kuma yanzune abun ya soma?" Doctor ya tambaya yana me ɗan rubuce rubuce ajikin wata fafar takarda.

Shiru Pharouk yayi cike da ɗaurewan kai, kwata kwata shi bai fahimci me Doctor'n yake nufi ba.

Ganin haka yasa Doctor ɗin gyara zama tare da duban Pharouk.

"Munyi mata alluran bacci, tana buƙatar hutu sosai, menstrual pain ne insha Allah idan tafarka zataji sauƙi,  saidai irin wannan ciwon baicika warkewa ba harsai mace tayi aure, wasu kuma yakan daina idan sun haihu, wasu kuma ko basuyi aure ba idan suka dace da magani yana iya dainawa, so amma nata yanada tsanani sosai gaskiya, yakamata akula, sannan  tarage yawan shan zaƙi, saboda shima yana ƙara ciwon sosai,  ga wannan magunguna ne da zaka nemo saboda idan tafarka tasha" Dr  Ya  faɗi haka yana me miƙawa Pharouk wata ƴar farar takarda. Karɓan takardan Pharouk yayi tare da yiwa Doctor'n godiya.

Koda yafito daga office ɗin Dr direct ɗakin da aka kwantar da ita ya nufa,   ahankali yaƙarasa gaban gadon da take kwance, gaba ɗaya gashin kanta ya watse akan pillow, yayinda kyakkyawar fuskarta tayi fayau, bakinta kuwa har ɗan bushewa yayi saboda wahalan da tasha, numfashi take fitarwa ahankali, kallon kyakkyawar fuskarta yayi tare da sanya hanu yashafi lallausan gashin kanta,   wani irin tausayi da soyayyarta ne suka sake dirarwa zuciyarsa, kallonta ya shigayi sosai, yaune karo na farko daya fara ganinta babu hijab,  ashe duk iya tunaninsa da yanda yake fasalta kyawunta azuciarsa tama wuce haka, idanunsa ne suka sauƙa akan ƙirjinta, wanda har ana iya  hango saman breast dinta, domin wuyan rigan yaɗanyi mata yawa kaɗan.  Lumshe idanunsa yayi tare da jan numfashi mai tsawo,  hanunsa ya zare daga cikin hair ɗinta tare da ɗan matsawa baya,  wani irin abu yakeji ajikinsa na musamman agame da ita,  kawar da kallonsa yayi daga gareta, domin kuwa idan ya yarjewa zuciyarsa yaci gaba da kallonta, to tabbas zai iya losing control  ɗinsa.  Jiki asanyaye yajuya yafita daga cikin ɗakin, azuciyarsa kuwa tattauna maganganun da Dr ya faɗa masa yakeyi.    Aƙaton pharmacy'n dake gefen asibitin ya saya magungunan, motarsa ya shiga  tare dayi mata key, inda ake saida fruits yanufa,  duk wani kayan fruit saida ya saya sannan kai tsaye yadawo asibitin.

Har zuwa wannan lokacin bata farka ba, zama yayi akusa da ita tare da zaro wayarsa daga cikin aljihunsa ya soma dannawa.

Jin kamar tana ƙoƙarin motsawa yasashi tashi da sauri yaƙaraso inda take, hanunsa yakai ya taɓa goshinta.    Daidai lokacin aka turo ƙofar ɗakin, waiwayawa yayi don atunaninsa likitane sai kuma yaga saɓanin tunaninsa, wani kyakkyawan farin gaye idanunsa suka gane masa, wanda yake sanye da maroon suit me tsananin kyau da tsada,  kallo ɗaya kayi masa zakasan ko wanene shi, matashin saurayi, maiji da kuɗi, ilimi, wayewa,ƙasaita, jinkai,  da kuma miskilanci, domin ko alaman annuri babu akan kyakkyawar fuskarsa, hannaye Pharouk yasanya acikin aljihun wandonsa tare da kafe wanda ke shigowa cikin ɗakin da ido.   Yanayin takunsa kaɗai ya isa sanar dakai cewa shiɗin wanine,   baigama shigowa cikin ɗakin ba, Doctor ya biyo bayansa.

"Tafarka ne?"
Dr Ya tambayi Pharouk yana me ƙoƙarin ƙarasawa gaban gadon.

"A'a" Pharouk yabasa amsa ataƙaice yana me kallon mutumin da shigowarsa ya tsaya masa amaƙoshi.

Babu wanda ya saurara acikinsu ya ƙarasa gaban gadon, kallon fuskarta yayi tare da dawo da kallonsa ga ƙirjinta,  rumtse idanunsa yayi tare da cije lips ɗinsa, lokaci guda yaji wani irin ɗaci amaƙoshinsa, hijab ɗinta dake gefe da ita ya ɗauka, hannayensa ya sanya ya tallafota tare da sanya mata hijabin, ransa na ƙuna haka yajawo hijab ɗin ya rufe mata ƙirjinta dake buɗe,  lokaci guda idanunsa  suka  sauya kala daga farare zuwa jajaye.  Juyowa yayi ya kalli Dr cikin lion voice ɗinsa yace "Inason kayi discharge ɗinta yanzu"

"Babu damuwa ae dama ba wani babban ciwo bane" Cewar Dr

Cikin rashin fahimta Pharouk yace.
"Saboda me za a sallameta bayan bataji sauƙi ba?"  yanayin yanda yayi maganan daɗan zafi yasanya, Dr sakin murmushi nuna masa SOORAJ dake tsaye ya haɗe fuska, yayi tare da cewa "Yayanta ne inaga yafiso subata kulawa agida ne"

Dummmm haka Pharouk yaji ƙirjinsa ya buga,  atare suka kalli juna shida Sooraj, wani irin kallo sukawa junansu mai ɗauke da tarin ma'anoni.  Wani killer smile Pharouk yayi tare da miƙawa Sooraj hanunsa cikin wata murya me amo yace "Am Pharouk"     Wani kallo Sooraj yayiwa Pharouk, daga ƙasa har samansa sannan yaɗan taɓe baki shima ya miƙa masa hannu suka gaisa, saidai da sauri Sooraj ya zare hanunsa daga cikin na Pharouk tare da kawar da kansa gefe, Murmushi Pharouk yayi tare da ƙarasawa gaban gadon, hannunsa yakai daniyar taɓa fuskarta, kafun hannunsa ya gama sauka akan fuskarta tuni Sooraj yayi masa wani irin riƙo wanda ya sanya Pharouk ɗagowa da sauri ya kallesa,   ido cikin ido haka suke kallon juna, kai Sooraj ya girgiza masa,  sannan ya ɗauke idanunsa daga kansa,  kallo Dr da yazama kamar wani statue agarin kallonsu yayi yace.

"Thank you Doctor"

Hannayensa duka biyu ya sanya ya ɗago Zieyaderh dake bacci, akafaɗansa ya ɗaurata tamkar ƙaraman yarinya ƴar shekara 3, ko kallon inda Pharouk yake baiyiba yafice daga cikin ɗakin.

Bin bayansa Pharouk yayi da kallo tare  da sakin murmushi. Azuciyarsa yace.
"SOORAJ!!! Yanzu aka soma wasan."

*Da Vote ɗinku kaɗai nake gane kunason labarinnan, ina godiya sosai masumin vote da comment Son So nake muku❤*

*Vote*
*Comment and share*

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ!!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

https://my.w.tt/7FVfmex8a7

*Chapter 31*

Yana fita daga cikin ɗakin direct hanyar dazai sadashi da compound ɗin asibitin ya nufa, baidamu da kallon da jama'a keyi masa ba. Yana isowa jikin motarsa ya buɗe gidan baya tare da kwantar da ita akan kujera, yana shiga yaja motar da wani irin speed yabar cikin asibitin, ransa amatuƙar ɓace yake wanda baisan dalili ba, hakanan yakejin wani ɗaci amaƙoshinsa. Yanayin yanda yake sharara gudu akan titi yasanyasa isowa gida cikin ɗan ƙanƙanin lokaci, ko jira agama buɗe masa gate ɗin gidan baiyiba ya tura hancin motar ciki.

Yana gama daidaita parking ya fito tare da buɗe gidan baya ya ɗauko ta, still akan shoulder ɗinsa yasake ɗaurata, wata hanya daban naga ya nufa ba wacce zata satadashi da babban falon dake cikin gidan ba, ajikin wata ƙofa naga ya tsaya tare da sanya key ya buɗe, ahankali yatura kofar ya shiga, wani ɗan corridor ne wanda gefe dashi wani haɗaɗɗen swimming pool ne wanda aka ƙawatasa, ruwan ciki gwanin ban sha'awa, sai kuma wasu ƴan tsirarun shukokin flowers da suka ƙara ƙawata kyawun wajen, wata ƙofar yasake buɗewa, wanda ya sadashi da ɗakin baccinsa, kasancewar bayan ƙofar shiga ɗakinsa wanda ke cikin babban falon gidan, akwai wata ƙofa ma wacce take ta bayan compound ɗin gidan. Ƙofar ya mayar ya rufe tare da murza mata key, ƙarasawa gaban makeken gadonsa yayi tare da birkito da ita ta dawo kan hannuwansa, cike da tsananin muguntan dake ransa yasaketa tafaɗa kan gadon da ƙarfi, atake ta saki wani ƙara tare da sakin wani marayan kuka, hannayensa ya harɗe akan ƙirjinsa, tare da tsayawa ƙyam yana kallonta, sam fuskarsa ko alaman wasa babu.
Agalabaice ta sanya hannayenta ta riƙe weast ɗinta dake ciwo kaman zai ɓalle, sam batama gama sanin awacce duniya take ba, kasancewar alluran baccin da akayi mata baigama saketa ba, azaban sakinta da ƙarfi da yayi akan gado ne yasanyata farkawa, ahankali idanunta suka ɗan soma washewa saidai duk da haka bata gani sosai, idanuntane suka sauƙa akan fuskarsa, adaburce taja jikinta baya, duk da cewa bata gama dawowa hayyacinta ba, amma hakan bai hanata tsorata data gansa ba, kukan da takeyi ta tsayar, tare da sanya white teeth ɗinta ta datse lips ɗinta, alaman wani waje nata nayi mata zafi.

Sooraj dake tsaye ya harɗe hannuwa ganin yanda take ciccije baki, yasanya cikin husky voice ɗinsa yace da ita "Tashi!"

Da sauri tasoma yunƙurin sauƙa daga kan gadon, tana aje ƙafafunta aƙasa, wani irin jiri ya ɗebeta tare da ƙoƙarin kada ita, da sauri tasanya hannayenta duka biyu ta dafe bango, siririn kuka tasaki marar sauti, don masifar tsoronsa takeji,   kallon jikinta yayi sannan ya kalli white bedsheet ɗin dake shimfuɗe kan bed ɗinsa, idanunsa yaɗan zaro tare dasanya hannu ya dafe goshinsa, aɗan harzuƙe yace.
"Bakida hankali ko? Ɗauka maza kije toilet kiwanke minshi yanzunnan, sannan kuma ki tabbatar da cewa yafita!!" yafaɗi maganar agadarance yana meyi mata nuni da bedsheet ɗin. Dubanta takai kan gadon, nan taga jini yaɗan ɓata tsakiyan bedsheet ɗin, wani irin faɗuwa gabanta yayi take taji wani masifaffen kunya ya rufeta. Kanta aƙasa ta sanya hannu tashiga jan bedsheet ɗin, duk da cewa dishi dishi idanunta suke gani sannan kuma babu wani ƙarfi ajikinta, hakan yasa komai takeyinshi cikin sanyi, ɗaukan bedsheet ɗin tayi tare da nufar wata ƙofa ta daban atunaninta nanne toilet, daga yanayin tafiyarta kaɗai ya isa sanar dakai cewa bata cikin hayyacinta, don har yanzu pain ɗin bai saketa ba.

Hannunsa yasanya ya damƙo ta, yanayin irin riƙon daya mata ba na wasaba ne, don har saida wani ƙashi dake cikin hannunta yayi ƙara, ƙafarsa yasanya ya daki ƙofar toilet ɗin, take ƙofar ta wangale, hankaɗata cikin toilet ɗin yayi tare da jawo ƙofar ya rufe.   Zama yayi akan wata kujera tare da ɗaukan laptop ɗinsa yashiga dannawa, gaba ɗaya wani irin takaicinta yakeji.

Itakuwa Zieyaderh rasa inda zata sanya bedsheet ɗin tayi, wani irin bacci tare da jiri ne ke fusganta har bata iya ganin gabanta sosai, wani bucket ta ɗauka tare da sanya bedsheet ɗin aciki, ruwa ta zuba acikin bucket ɗin sannan tajefa sabulu,  tsugunnawa tayi ta zubawa bucket ɗin ido, tama rasa ta ina zata fara, ganin tsayuwan ya isheta yasanya ta zauna daɓas aƙasan tiles tare da jingina bayanta da jikin bango, 5 minute kacal bacci ya ɗauketa awajen.

30 minute ya ɗauka azaune yana daddana laptop ɗinsa, kwata kwata shi yama manta da ita, ƙiran sallan magriba da akasomayi ne yasanyashi rufe laptop ɗin tare da miƙewa tsaye. Ahankali ya tura ƙofar toilet ɗin yashiga bakinsa ɗauke da addu'a.   Hannayen rigarsa yasoma naɗewa tare da ƙarasawa gaban sink. Alwala yayi yana cikin wanke ƙafarsa na hagu idanunsa suka sauƙa akanta, saida yaji wani irin faɗuwar gaba domin shi sam yama manta da ita,  cike da mamakin yanda tabaje tana sharar baccinta yashiga ƙare mata kallo, ga bucket agabanta sannan kuma ga bedsheet da sabulun wankansa nan acikin bucket ɗin, sabulun ya narke saboda yasha ruwa,  itakuwa baccinta take tana sauƙe ajiyar zuciya. hankalinta akwance.

Ƙafansa yaɗan sanya ya zungureta, ko motsi batayi ba,  wani murmushin da iyakansa leɓen baki yayi,  gaban babban bathtube ɗin wankansa ya ƙarasa, ruwan sanyi ya tara har saida yacika bathtube ɗin,  ƙarasowa gabanta yayi tare da ɗan durƙusawa ya ɗauketa,   kamar wata ƴar tsana haka ya jefata acikin bathtube ɗin,  aruɗe ta buɗe idanunta da sukayi luhu luhu sannan sukayi ja,  wani irin sanyine ke ratsata.  Juyawa yayi cikin halin ko inkula yafice daga

cikin toilet ɗin, cikin daurayi ta fito daga cikin bathtube ɗin, gaba ɗaya kayan jikinta sun jiƙe jaƙab,   ahankali take taka ƙafafunta da takejinsu kamar bazasu iya ɗaukanta ba.   Bazata iya jurewa azabobin dayake gana mata ba, ganin bakowa acikin ɗakin yasanya tanufi hanyar fita, saɗaf saɗaf take tafiya kamar munafuka,   ƙofar corridor ɗin ta buɗe ahankali, kanta tasako taɗan leƙa babban falon, kamar dai koda yaushe babu kowa acikin falon, da sauri ta fito ko tsaya rufe masa ƙofar batayi ba, daɗan sassarfa ta soma haura step ɗin dazai sadata da ɗakinta,   tana tafiya tana waigen ƙofar ɗakin Ummu, kamar ɓarauniya haka ta buɗe ƙofar ɗakinnata ahankali tana shiga ta kulleshi gam,  jiƙaƙƙun kayannata tasoma cirewa, sannan ta wuce bathroom. Adaddafe ta haɗawa kanta ruwan ɗumi, tayi wanka, har yanzu pain ɗin bai gama saketa ba, saima wani sabon fever daya sauƙa ajikinta,  pad ta ɗauka ta kimtsa kanta sannan ta sanya wata doguwar riga me ɗan nauyi, domin kuwa sosai takejin sanyi, duk da cewa akwai yunwa sosai acikinta amma bata damu da  neman abinciba, kan gado ta hau tare da jan blanket ta rufe gaba ɗaya jikinta, jikinta sai rawan sanyi yake, haka ta lumshe gajiyayyun idanunta da suketa ambaliya wajen fitar da hawaye.

Ganin har ƙarfe 7 Ummu bataji motsinta ba gashi yau bataga dawowanta ba yasanya hankalinta yaɗan tashi,  saboda haka tafito don dubata.

Ahankali Ummu tatura kofar ɗakin tashigo bakinta ɗauke da sallama,  ganin Zieyaderh nannaɗe acikin bargo yasanya Ummu ƙarasawa wajenta da sauri cike da kulawa tace.

"Zieyaderh lafiya kike kuwa?"

Zieyaderh da duk jikinta ke rawan sanyi, ta girgiza kanta cikin ciwo tace.
"Ummu zazzaɓine ke damuna!"

"Subahanallah shine kuma bakizo kin faɗamin ba? ba'a zama da ciwo ae, sam hakan ba kyau, kin maci abinci kuwa?" Ummu ta tambaya.

Kai Zieyaderh ta girgiza alaman.
"A'a"

Juyawa Ummu tayi tafice daga cikin ɗakin.

Mintuna kaɗan saiga  Ummu ta dawo hannunta ɗauke da plate da kuma cup ɗin tea, kan bedside drawer ta aje plate da cup ɗin, bargon da zieyaderh ke lulluɓe dashi Ummu taɗan yaye tare da miƙar da ita zaune, cup ɗin  tea ɗin Ummu ta bata, babu musu ta amsa,  ahankali takeshan tea ɗin,  sai da tasha kusan rabin cup ɗin, kafun Ummu ta amshi cup ɗin, plate ɗin soyayyen dankali da ƙwai wanda yaji sauce Ummu ta miƙo mata, nanma bata musaba ta amsa, ahankali takecin abincin duk batajin wani daɗin bakinta.   Pain reliever Ummu ta bata tasha, sannan tace da ita ta kwanta tayi bacci,  luf tayi akan gado tana maida numfashi ahankali, cikin wasu mintuna ƙalilan bacci ɓarawo yayi gaba da'ita.

Tunda Yafita sallan Magriba bashi yadawo gidanba sai 9 pm,  direct toilet ɗinsa ya wuce, wanka yayi yafito ɗaure da towel a weast ɗinshi, sama sama yashafa body lotion,  white trouser yasanya, tare da feshe jikinsa da turare me daɗin ƙamshi,  Luf yayi akan gadonsa tare da cusa kansa cikin pillow, sanyin AC ne ke ratsa naked skin ɗinsa, ahankali yake sauƙe ajiyar zuciya, ƙoƙarin faɗa da tunaninsa yake, sam bayason wani abu yasake damunsa,  a ƴan kwanakinnan yana yawan jin zuciyarsa nayi masa zafi, sam bayason ciwonsa yayi ƙarfin da harsai kowa ya gane yana ɗauke da ciwon zuciya, akullum yanaji ajikinsa bashi da wani sauran farinciki daya ragemai,   numfashi ya fitar ta bakinsa tare da lumshe idanunsa,  duk yanda zuciyarsa taso da yayi tunani yaƙi bata daman hakan, yajima sosai kafun yasamu bacci ya ɗaukesa.

Washegari.

7:00 am daidai yagama shirya kansa cikin navy blue suit,  Sosai yayi kyau sai tashin ƙamshi yake,   waya da key ɗin motarsa ne riƙe ahanunsa,  cikin nutsuwa yake takunsa har yakai bakin ƙofar da zai fitar dashi daga cikin falon. Muryar Ummu da yaji abayansa yasanyashi tsayawa, juyowa yayi cikin ɗan rusunawa yace.
"Good morning Maaa"

Murmushin daya bayyana tsananin kamanninsu dashi Ummu tayi tare da cewa
"Morning how are you?"

"Am fine!" ya amsa ataƙaice yana me gyara wrist watch ɗinsa.

"Kasanar da Mas'oud Zieyaderh batajin daɗi, sannan yau bazata samu zuwa school ba ya kamata asanar" Ummu tayi maganar tana me ƙoƙarin zama akan kujera.
Kansa kawai ya jinjina alamar yaji kana yafice daga cikin falon.

Sosai tasha bacci sai 10 tafarka, Alhamdulillah ta ɗanji sauƙin jikinta, saidai kuma duk da haka bakinta babu daɗi,   fitowarta daga wanka kenan, wani riga da sket ƴan kanti tasanya, sket ɗin irin rubber pencil ɗinnan ne yayinda rigan takasance me buɗaɗɗen kafaɗa, sosai kayan sukayi mata kyau ajiki,  rubber hijab tasanya ajikinta, sannan tanufi ƙasa,   ahankali take saƙƙowa daga kan steps ɗin, Ummu ce zaune afalon tasha ado cikin wani tsadadden lace maroon colour wanda yayi matuƙar amsar jikinta, gefe da ita wata matace wacce bazata wuce shekarun Ummun ba itama zaune ta caɓa ado, dagani basai anfaɗa ba kasan naira yazauna musu su dukansu.   Cikin ladabi taƙaraso tare da durƙusawa ta gaidasu, fuska ɗauke da murmushi Ummu ta shafa kan Zieyaderh'n tare da cewa

"Kintashi? har baccin ya isa kenan, to ga can break fast akan dinning"
Murmushi Zieyaderh tayi tare da miƙewa tsaye tanufi dinning area. Hajiya Munah dake zaune tabi Zieyaderh da kallo, ajiyar zuciya ta sauƙe tare da duban Ummu cikin yanayi naɗan mamaki tace.
"Hajiya Sulaimiyya ina kikasamo wannan kyakkyawar yarinyar kodai daga ƙasarku take ne?"

Murmushi Ummu tayi tare da cewa. "Ƙanwar Mas'oud ne abokin Sooraj, ai kindai san Mas'oud?"

Murmushi Hajiya Munah tayi tare da cewa "Ayya gaskiya balaifi yarinyar akwai hankali, uwa uba gata da kyau masha Allah!"

"Wannan halayyan nata shiyasa nakeson haɗata aure da Almustapha, nasan bazaiyi takaicin samunta amatsayin mata ba"  Cewar Ummu wacce ke sipping pineapple juice ahankali.

Murmushi Hajiya Munah tayi tare dacewa "Gaskiya kinyi tunani me kyau, amma ae zai fi kyau ki haɗata da Sooraj, don aganina yafi Almustapha buƙatar mace akusa dashi"

Aje glass cup ɗin hanunta Ummu tayi tare da duban Hajiya Munah, wani murmushi me ciwo Ummu tayi cikin wani irin yanayi tace "Saikace bakisan waye Sooraj ba Hajiya Munah? hmmm Sooraj ɗin da baibzauna da matan da suka amsa sunansu mata ba ma, mene zaiyi da ƴar wannan ta tsitsiyar yarinyar da duka duka shekarunta basu wuce 18 to 19 ba"

Ajiyar zuciya Hajiya Munah ta sauƙe tare da cewa "Allah ya kyauta"

Da  "Ameen" Ummu ta amsa daganan suka ci gaba da hiransu.

Zieyaderh kuwa zama tayi akan dinning tare da zubawa kanta pepper chicken soup, and chips, ahankali take tsakalan abincin don gaba ɗaya bawani daɗinsa takeji ba.   Koda ta kammala ɗakinta takoma magungunanta tasha kana ta kwanta, tashar Mbc  Action take kalla da haka har bacci ya ɗauketa.

Dayake magungunan da tasha suna da ƙarfi sosai hakan yasa ba ita ta tashiba sai wajen 5 na yamma, wanka tayi tare da sanya wata blue gown marar nauyi,  yunwa takeji sosai hakan yasa tashiga ƙoƙarin zura hijab ɗinta don sauƙa ƙasa, jin anturo ƙofar ɗakinne yasanyata waigawa da sauri, ido biyu sukayi da Ummu wacce fuskarta ke ɗauke da murmushi.

"Barka da yammaci Ummu" tafaɗa murya asanyaye.

"Yauwa, dama wai me gadine yanzun yashigo yace wai wani yana sallama dake awaje, shine nace ko kunyi da wani zaizo wajenki ne?"

Idanu Zieyaderh ta zaro, lokaci guda ƙirjinta yashiga wani irin bugu, bakinta narawa tace "Ni....ni...kuma?"

"Eh haka dai yace, yanaga kin tsorata? Maza kije kiga ko wayene bakyau kabar mutum yana jira!" Ummu nagama faɗan haka ta juya ta fice daga cikin ɗakin.

Tsorone ya kama Zieyaderh adaburce ta sanya hijab dinta,kana ta buɗe ƙofar ɗakin ta fice.

Bataga Ummu afaloba kai tsaye saita nufi hanyar waje.

Koda tafito compound ɗin gidan idanunta tashiga warewa ko zata hango wanda akace na nemanta.

Tun fitowarta daga cikin falon yake kallonta, sosai tayi masa kyau acikin hijab ɗin dake jikinta, ashe sosai uniform ke ɓoye kyawunta.     Kamar wanda akace tawaiga bayanta, hangosa tayi tsaye ajikin black car ɗinsa mercedes benz, sanye yake da riga da wando na bugaggiyar shadda Blue colour wanda tayi matuƙar yi masa kyau, mamakin ganinsane kwance acikin ranta amma saita sunkuyar da kanta ƙasa tare da nufar inda yake,  murmushine kwance akan fuskarsa yana me kallonta harta ƙaraso. Cikin siririyar muryarta tayi masa sallama.  Bai amsa sallamannata ba saima tsayawa kallonta da yayi, jin shiru bai amsa mata ba yasanya ta ɗago kanta ta dubeshi, idanunsune suka sarƙe cikin na juna, yanayin kallon daya mata yasanya ta sauƙar da idanunta ƙasa da sauri tana murmushi.   Kansa yaɗan sunkuyo yana leƙa fuskarta, ganin haka yasa tasanya tafukan hannunta ta rufe fuskarta da sauri.

"Jiya nakasa bacci saboda bansan wani hali kike ciki ba,  amma ganinki danayi yanzu yasa naji sanyi araina, basai ma kin faɗa ba nagane kinji sauƙi" Yafaɗi haka cike da tsantsar nuna kulawarsa gareta.

Har acikin ranta taji daɗin maganganunsa, domin tanada buƙatar kulawa sosae.

Ɗan matsowa kusa da ita yayi hartana iya jiyo sassanyan ƙamshin dake fita ajikinsa. Hannayensa yakai ya zame hannunta dake kan fuskarta.

Cikin wata irin sweetness voice yace "Kullum ƙara kyau kike, komai naki me kyaune, zanso kasancewa dake akoda yaushe sannan akowacce rana, please faɗamin kina sona?"  yaƙare maganar yana me juya idanunsa akan kyakkyawar fuskarta.

Lumshe kyawawan idanunta tayi sosae zuciyarta ke bugawa, batasan me zatace masa ba, sannan kalamansa sunyi mata nauyi sosai, shikaɗai ya lura da mota ƙiran black range rover dake shigowa cikin gidan, kasancewar ita tabawa ƙofar gate baya, sannan gaba ɗaya tunaninta yatafi izuwa wani wajen daban.    Ahankali taɗan buɗe idanunta tasaci kallonsa, abun da bata saniba shima kallonta yake sai kawai idanunsu ya sauƙa acikin na juna. Da sauri ta kawar da kanka gefe tare da sanya hijab ɗinta ta kare gefen fuskarta, idanunta ne suka sauƙa akan motar da ta shigo cikin gidan, wani irin masifaffen tsorone ya kamata take jikinta ya soma ɓari, lokaci guda jikinta yashiga fidda gumi,   yana gama daidaita parking ɗin motar yafito,  sanye yake da white t-shirt and  combat army jeans,  baƙaramin kyau yayi ba sosai kayan suka fitar da kwarjininsa.  Cikin isa yake takunsa yana me dosowa cikin gida, saidai abun mamaki bai ɗago kai ya kallesu ba, bawai kuma don baigansuba tun shigowansa idanunsa sukayi masa tozali dasu,    baya baya Zieyaderh keyi tana me ƙoƙarin ɓoyewa abayan Pharouk,  tuni hawayen tsoronsa sun cika idanunta. Yayinda shikuma yake daɗa kusanto inda suke, fuskarsa sam babu alaman wasa ko murmushi akanta.

*Vote*🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ!!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

#romance

*Chapter 32*

Cikin nutsuwa yake takunsa, tuni Zieyaderh ta koma bayan Pharouk ta ɓoye, rumtse idanunta tayi ƙam cike da fargaba. Kamshin turarensa da yacika hancinta ne yasanya jikinta ya soma rawa, saboda tasan zuwa yanzu yana gab dasu. Sam bai kallesuba balle yasa aransa cewa da gaske mutanene awajen, kansa tsaye ya wuce.

Aƙalla taɗauki kusan 5 minute ahaka, idanunta a rufe suke, jin shiru bataji motsin kowa ba yasanya tasoma buɗe idanunta ahankali, da beuty face ɗinsa tasomayin arba yayinda ya kafeta da sexy eyes ɗinsa, waro idanunta waje tayi tare da ɗanja da baya tashiga waige waige.

Murmushin daya bayyana dimples ɗinsa yayi, tare da ɗan kashe mata idanunsa ɗaya. "Tsoron me kikeyi haka? ba Brother ɗinki bane?"

Kanta ta sunkuyar ƙasa tare da sauƙe ajiyar zuciya, duk da bata ganshi awajenba amma amatuƙar tsorace take domin batasan wani hukunci bane zai biyo baya.

"Meyasa kikejin tsoronsa? Ya hanaki kula kowa ne? Waye shi awajenki? Please tell me karkimin ƙarya!" yafaɗi haka yana me gyara tsayuwarsa tare da kafeta da idanunsa....

Sallama ɗauke aƙasan maƙoshinsa yashiga cikin falon, kai tsaye ɗakinsa ya nufa.

"SOORAJ!" Ummu dake zaune acikin falon taƙira sunanshi.

Cak ya tsaya da tafiyan, ahankali ya ɗan juyo ya kalleta.

Fuskarta babu alaman wasa batare da ta kalleshi ba tace "Badai ka ɗauki maganganun da Abbanka yayi maka amatsayin wasa ba?"

Shiru yayi tare da sunkuyar da kansa ƙasa, baijin zai iya furta wata kalma awannan lokacin.

Sanin halinsa yasanya Ummu cigaba da cewa. "Kashiga hankalinka Sooraj, yakamata ace kasan mekakeyi, sai yaushene zaka fuskanci cewa ka girma? sai yaushe ne zaka nemawa kanka mutumci da daraja tahanyar yin aure? Ashe kafiso koda yaushe muta faɗa muna nanatawa duk akanka kai kaɗai? Idan kasake mahaifinka yayi mummunan fushi dakai to wallahi ba zakaga da kyau ba, sannan kuma gobe Almustapha zai dawo  ka tura mota a ɗaukosa!" Ummu tafaɗi maganganun fuskarta babu alaman wasa.

Kansa kawai ya jinjina alaman yaji, ko 1 second baiƙara ba ya juya ya shige ɗakinsa.

Da kallo Ummu tabisa, tarasa hali irin na sooraj wani kalan alfano gareshi,  ita tahaifesa amma batasan a ina yasamo wannan miskilancin nasa ba, sam itakam ba haka take ba.

Yana shiga cikin ɗakin ya murzawa ƙofarsa key,  kayan jikinsa ya shiga ragewa, towel ya ɗaura ya shige bathroom, ruwa ya sakarwa kansa tare da sanya hannunsa na dama ya dafe bango, lumshe kyawawan idanunsa yayi tare da sauƙe ajiyar zuciya, kansa ya ɗaga sama ruwa ya shiga dukan fuskarsa, saida numfashinsa yasoma barazanan ɗaukewa sannan ya sauƙar da kansa ƙasa, numfashi yashiga fitarwa akai akai, yana mejin zuciyarsa na bugawa da ƙarfi.

Ƙanƙance idanunsa yayi tare da lumshesu alokaci guda. "Zieyaderh!!" yaƙira sunanta in a cool voice ɗinsa.

Kanta ta ɗago tare da  ɗan satan kallonsa,  cikin muryarta me sanyi tace. "Na'am!"

"Inasonki!" Yafaɗa asanyaye yana me karyar da kansa gefe.

Kanta tajinjina tare da ɗan sakin murmushi, ƴan siraran laɓɓanta dake motsawa ahankali ya kalla.
Da alama maganace abakinta amma tanajin nauyin furtawa.

"Bakiji daɗin zuwana ba ko?"

Kanta ta girgiza alaman "A'a"

"To meyasa ba kya farinciki? Natafi ko kin gaji da ganina?" Ya tambaya yana me zura hannayensa acikin aljihun wandonsa.

Kanta ta girgiza cikin wani irin yanayi na shagwaɓa tace
"A'a nifa bance haka ba!"

Idanunsa ya lumshe har cikin ransa yaji salon shagwaɓan nata ya taɓasa,  cikin ƙasa da murya

yace "to faɗamin"

Tafukan hannayenta tasanya ta rufe fuskarta tana dariya.

"Pleaseeee mana baby faɗamin kina sona?"

Kasa jurewa tayi da sauri tajuya cikin yanayi na ɗan gudu gudu sauri sauri ta nufi cikin gida, murmushi Pharouk yayi tare da binta da kallo, wani irin sanyi yakeji acikin ransa, duk da cewa bata furta masa da bakinta ba, amma tabbas yasan bataƙinsa, don baiga ƙiyayyarsa acikin ƙwayan idanunta ba, motarsa ya buɗe ya shiga tare dayi mata key, mai gadi ne ya wangale masa gate, haka yabar cikin gidan zuciyarsa da tunani kala kala, gaba ɗaya ayar tambayarsa ya ɗigata ne akan SOORAJ.

Da ɗan guduntа tashigo cikin falon, tana rufe ƙofar ta saki wata ajiyar zuciya tare da sanya hannu ta dafe ƙirjinta, ƙoƙarin daidaita nutsuwarta tayi sannan takalli ɓangaren Sooraj, jin gabanta ya faɗi yasanya ta haura sama tana shiga cikin ɗakinta tafaɗa kan gado tare da lumshe idanunta, wani iri takeji azuciyarta, batasan dalilin da yasa takejin Pharouk awani ɓangare na zuciyarta ba, saidai kuma ako da yaushe kalamansa daɗi suke mata.

Luf yayi akan gadon tare da sake cusa kansa cikin pillow, gaba ɗaya ya rasa inda zai tsoma kansa yaji daɗi, ba yason yakai gayin abun dazai dameshi daga baya hakan yasa ya jure duk wata damuwarsa, sosai yakejin rauni azuciyarsa, musamman dangane da matsalarsa,,, yajima yana saƙawa da kuncewa acikin zuciyarsa kafun daga bisani bacci ɓarawo ya sace sa.

Washegari.

Alhamdulillah yau taji daɗin jikinta sosai hakan yasa ta shirya kanta tsab cikin shigar uniform ɗinta, hakanan takejin sanyi azuciyarta, ahankali take saƙƙowa daga kan step ɗin. Karan takun takalmanta yasanya shi ɗago da kansa, dai dai lokacin itama ta ɗago kanta, idanunsune ya sauƙa cikin na juna, da sauri tayi ƙasa da kanta, shima kansa ya kawar tare da ci gaba da sipping coffee ɗinsa.

Sumu sumu haka taƙarasa sauƙowa daga kan steps ɗin, ahankali take tafiya harta ƙaraso inda yake, cikin wata irin murya me sanyi tace "Ina kwana!"

Bai amsata ba hakan yasa taɗan ɗago kanta ta kalleshi, ganin kamar baisan tana wajenba yasanya ta soma wasa da yatsun hannunta tana me murzasu, cikin yanayi naɗan shagwaɓa tace "Ina kwana Ya...yah?"

A yanzu kam ɗago kansa yayi ya kalleta saidai haryanzu bai amsa mata ba, jiki asanyaye ta gyara zaman school bag ɗinta sannan tanufi hanyar fita daga cikin falon.

Kamalu driver tasamu tsaye ajikin mota, da sauri ta ƙarasa tare da buɗe gidan baya ta zauna,

tana ƙoƙarin aje school bag ɗinta, ya buɗe ƙofar motar ya shigo, ƙamshinsa take yacika ko ina dake cikin motar, mamakin shigowarsa cikin motar ne ɗauke akan fuskarta. School bag ɗinta ta rungume aƙirjinta tare da duƙunƙune jikinta waje ɗaya,  tunda suka ɗauki titi yake ta faan latsa wayarsa, gaba ɗaya kwarjininsa ya cika mata ido, musamman yau da yasha ado cikin white and black suit, sai ya zamana yaƙara kyau.   Aƙofar makarantar tasu Kamalu driver yayi parking motar, kamar marar gaskiya haka ta buɗe ƙofar motar tafice, ko taku uku batayiba taji ƙaran tashin motar, tana waiwayawa taga sunbar wajen, tana shiga cikin school ta haɗu dasu Nasmah, gaba ɗayansu hankalinsu atashe suke tambayarta yaya jikinta, sosai taji daɗin kulawarsu agareta da haka suka wuce class.

Ƙarfe Biyu daidai jirginsu ya sauƙa ababban airport ɗin dake cikin garin Abuja,   wani kyakkyawan saurayi wanda aƙalla bazai haura 29 years ba, shike sauƙowa daga kan matattakalan jirgin Sanye yake da riga da wando na jeans masu kyaun gaske,  kai tsaye baza'a ƙirasa da fari sol ba, sannan kuma shi ba baƙi bane, yana daɗan tsayi daidai misali sannan yana da faffaɗan jiki,  daga yanayin shigarsa kaɗai zai sanar maka da ɗan gaye ne, fuskarsa ɗauke take da murmushi,  Kamalu driver yana hangosa ya ƙarasa garesa da sauri cikin yanayi naɗan girmamawa yace "Ranka ya daɗe barka da zuwa"

Murmushi Alhmustapha yayi tare da bawa Kamalu driver hannu suka gaisa, cikin muryarsa yace "Yauwa Kamalu barka da aiki!"

Tunda suka baro airport ɗin Kamalu driver ke ta masa zuba, yayinda shikuma yawan maganartasa ba sosaiba saidai murmushi kawai da yakeyi.

Gyara zama Shukra tayi cikin kulawa tace "Me yasa zaki tauyewa kanki haƙƙi Zieyaderh?  indai kina sonsa kawai ki amsa masa, mene aibun Pharouk? Sam bashida wani aibu komai nasa mai kyau ne, inta ƙaicemiki babu wata ƴa mace da zataga Pharouk kuma ta ƙishi coz ba Namijin wasa bane"

Sunkuyar dakai Zieyaderh tayi tare daɗan ciza lips ɗinta,  "Bansan ya zanyiba Shukhra amma karki manta nafaɗa miki matsayina bai kai ace naso Pharouk ba, duk da bansan wanene shiba amma nasan ko sama zata haɗe da ƙasa yafini tsatso me kyau, da kuma gata, banason na tozarta rayuwata Shukhra!" taƙare maganar idanunta cike tab da ƙwalla.

Ajiyar zuciya Shukra tayi tare da sakin murmushi "Wannan ba hujja bane Zieyaderh, ana iya auren shegiyama wacce bata da uba, balle keda kike da uba, balallaine don bakisamu kulawan mahaifanki  yazamana kin tauyewa kanki haƙƙi ba, ke macece idan baki zaɓi mijin da zaizame miki garkuwa ba me kenan kikayi? Ki farka daga baccin da kike Zieyaderh akowacce ƙwanan duniya ƙara girma muke, ayanzune yakama musan dacewa muma matane sannan ayanzune yakamata mukau da wani shashanci da yarinya wanda ke cikin sense ɗinmu, yes nasani bamu da wasu shekaru masu yawa amma kuma babu wani abu na ƴan matanci ayanzu daya ɓoye kansa ajikinmu,  zamu mori damarmu ne kaɗai idan mukayi amfani dashi tun muna ƙanana, alokacin da muka girma kuwa bazamu taɓa morarta da kyauba, saboda alokacin bakowa ne

zaizo ya kallemu yace yana sonmu ba, ayanzu kuwa kowa so da sha'awarmu yake"  Ɗan tsagaitawa da maganar tayi tare da sanya hannunta ta dafa kafaɗan Zieyaderh.

"Ki amincewa Pharouk Zieyaderh, inada tabbacin Pharouk bazai taɓa nuna miki tsana tsangwama da kuma kyara ba!"

Wani irin ajiyar zuciya me ƙarfi Zieyaderh ta sauƙe, tabbas tasan abunda Shukhra ta faɗa gaskiya ne, saidai kuma tayaya zata furtawa Pharouk cewa tana sonshi? Idan har taso Pharouk menene matsayin tunanin Mr.helper dake kwance acikin zuciyarta? Da sauri takawar da wannan tunanin acikin zuciyarta.     Murmushi tayi cike da son samawa kanta ƙarfin guiwa  tace "Zan faɗa masa komai game dani Shukra, idan har zai soni ahaka to nima zan amasa masa, saɓanin haka kuwa shikenan zanjira wata ƙaddaran"

"Bazai taɓa gudunki ba Insha Allah!" cewar Shukra. Dariya suka sanya su dukansu.

5:10 pm  zaune take acikin motar gaba ɗaya tunaninta yayi nisa izuwa maganganun da sukayi da Shukhra,  sanyin AC'n dake tashi acikin motarne ya cakuɗa da daddaɗan ƙamshin turaren sa, duk da cewa baya cikin motar amma zaman dayayi acikin motar da safe yasanya har yanzu ƙamshinsa bai bar cikin motarba, hakan yasanya taji gaba ɗaya jikinta yayi wani iri, jingina bayanta tayi da jikin kujeran motar tare da lumshe idanunta, sosai ƙamshin yake jefata cikin wani irin yanayi. Sam batasan da cewa sun iso gidan ba    saida taji Kamalu driver ya tsaida motar. Jiki asanyaye take tafiya harta kawo ƙofar falon, tura ƙofar falon tayi ta shiga, da ƴar siririyar muryarta tayi sallama,  Amustapha dake tsaye acikin falon ya juyo ahankali yana me amsa mata sallaman, idanunsune ya sarƙe acikin na juna,  da mamaki akan fuskarsa ya shiga kallonta,   Itama kallonsa take,  "Almustapha" Muryar Ummu da suka ji yasa suka ɗauke idanunsu akan juna.
Ummu ce taƙaraso cikin falon fuskarta ɗauke da murmushi.

Kallon Zieyaderh tayi tare da cewa "Zieyaderh ga ɗana Almustapha"

Mamakine ya bayyana akan fuskar Zieyaderh amma saita share,cikin sakin fuska tare da murmushi taɗan rusuna tagaidashi, shima murmushinne akan fuskarsa ya amsa mata, har yanzu yana me dubanta don baigaji da kallonta ba. Harta haura steps bai ɗauke idanunsa akanta ba, Murmushi Ummu tayi sannan ta juya tafice daga cikin falon don dama fita zatayi.

Da ƙarfi ya buga table ɗin dake gabansa ransa amatuƙar ɓace yace  "Get out Aneesa!!"

Murmushi Aneesa tayi tare da juya idanunta dake cike da ruwan hawaye,  laɓɓanta ta ciza, "Bazan tafi ba RAJ Why kake kyarata? menene bani dashi? Kyau,Ilimi, dukiya, ko kuma me?" Ta tambayeshi hawaye suna mai sauƙa daga cikin idanunta.

Ransa amatuƙar ɓace yace "Kifitarmin a office!!!"

Murmushi mai ciwo Aneesa tayi cike da son ƙuntata masa tace "Baka sona saboda kai bakayarda da kanka bako? Hmmmm najima da sanin abunda kake ɓoyewa RAJ, najima da gane cewa kai Rago ne,  Kafito fili kafaɗamin cewa kai ba Namiji bane mana,  Ohhhhhh nagane kanajin kunyar sanar da duniya cewa kai wani marar amfanine ko, bansan meyasa ba duk da nasan cewa kai ba Namiji bane amma na liƙe maka, wallahi RAJ saika aure ni  koda......"
Wani irin bahagon mari SOORAJ ya sauƙe mata akan fuskarta wanda saida yagigita ta.  Bata gama dawowa cikin hayyacinta ba ya ɗamƙi wuyanta da ƙarfi, mannata yayi da jikin bango tare da sanya hannunsa da ƙarfi ya yaga rigan dake jikinta, dayake doguwar rigane ajikinta hakan yasa ya yagata har ƙasa, take surar jikinta ya bayyana,  idanunsane suka rikiɗe sukayi wani irin jaaa tamkar anwatsa masa barkono, lokaci guda jikinsa ya ɗauki ɓari tamkar wanda aka jonawa shocking.

"Ni ba Namiji bane ko? Yess niba Namiji bane, amma yanzu zanyi miki abun da wanda ba Namiji ba bazai taɓa iya yimiki shi ba" yana gama faɗan hakan ya wurgata saman table, tare da sanya hannu ya zare belt ɗin dake jikinsa.
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ!!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*WATTPAD*
@fatymasardauna

#romance

*This page is dedicated to my Brother HAMEED ALI (@Hameed29) I really ❤ You Brother*

*Chapter 33*

Wani irin jiri ne ke ɗibansa, duhu shine abun dake neman mamaye ganinsa,  jin duniyar yake gaba ɗaya tana juya mai, da ƙyar ya iya buɗe ƙofar ya fito hannunsa dafe da kansa.  Jefa ƙafafunsa kawai yakeyi batare da yana kula da inda yasa gaba ba,  da ƙyar ya iya kawo kansa wajen motarsa,  yana shiga yayi mata key.     Sam baya wani iya ganin gabansa da kyau, yanayin yanda gateman yaga yayo kansa da motar ne yasanya babu shiri da sauri ya buɗe masa gate, mamaki kwance akan fuskarsa na irin tuƙin gangancin da yaga yanayi.

Da wani irin speed yake tuƙa motar shikansa baisan wani irin gudu yakeyi ba,  babu babban abun tashin hankali da tsoratarwa kamar yanda ƙwayoyin idanunsa suka rikiɗe suka zama jajur dasu, gaba ɗaya jijiyoyin dake jikinsa duk sun tashi sunyi raɗo raɗo, mussamman forehead ɗinsa wanda jijiyoyi suka fito sukaɗi raɗa raɗa.   Irin gudun da yakeyi akan hanya ne, yasanya mutane da yawa ke kauce masa,  da ƙarfi ya daki gate ɗin gidan wanda don kansa saida ya

buɗe,   aguje mai gadi ya fito don kowa yaji irin dukan da akaiwa gate ɗin yasan ba lafiya ba. Da gudu yashigo cikin gidan kodamuwa da gaban motarsa da ya lotse baiyi ba.  Wani irin bahagon parking yayi.

Ummu da Almustapha ne suka miƙe atare sakamakon  jin yanda aka buga ƙofar falon da ƙarfi, waigawansu yayi daidai da shigowansa cikin  falon,  ƙirjin Ummu ne yashiga bugawa da sauri ganin yanda yake tafiya yana gauraya hanya tamkar wanda ke cikin  maye, sannan kuma ga hannunsa  dafe da  forehead ɗinsa.

"SOORAJ!" Ummu taƙira sunansa aɗan razane.

Bai waiwayo ba baikuma tsaya da tafiyan dayake ba kana kuma bai amsata ba, ya nufi hanyar da zata sadashi da ɗakinsa.

"RAJ!" Almustapha yaƙira sunansa,   kamar yanda bai amsa Ummu ba haka bai amsawa Almustapha ba, haka  ya buɗe ƙofar corridor ɗinsa ya shige.  Da sauri Ummu tarufa masa baya,  baifi saura taku uku tsakaninsu ba ya shige cikin ɗakinsa tare da murzawa kofar key, mamakine ya kashe Ummu hakan yasa ta tsaya cak, don tunda ta haifeshi bata taɓa ganinsa acikin irin wannan yanayin ba.

Ajikin ƙofar ya zame tare da sanya hannuwansa ya dafe kansa dake barazanan tarwatsewa. "Me yasa bazaka fito ka faɗawa duniya cewa kai ba Namiji bane?  RAGO!"   waƴannan kalaman suke ta yawo acikin brain ɗinsa suna me hautsina duk wani lissafin nutsuwarsa.   Idanunsa da suka kaɗa suka zama jajur ya buɗe tare da sauƙesu akan mirror, zumbur kamar wanda akawa allura haka ya tashi ahankali yashiga takawa har ya ƙarasa gaban mirror'n,  tsayawa yayi yana me kallon kansa, da sauri sauri yashiga cire rigan dake jikinsa, take murɗaɗɗen surar jikinsa da buɗaɗɗun muscles ɗinsa suka bayyana acikin madubin, 6 packs ɗin dake kwance raɗa raɗa akan cikinsa yakai hannu ya shafa,    ɗauke hannunsa daga cikinsa yayi ya taɓa fuskarsa da tayi jajur tsaɓan tsananin ɓacin rai da yake ciki.

"DA GASKE KAI BA NAMIJI BANE!!"
Zuciyarsa tafaɗa masa haka batare daya shiryawa jin hakanba, wani irin ihu yayi tare da sanya hannunsa ya naushi madubin, take ya tarwatse awajen,  hannunsa ne ya shiga ɗigar da jini amma ko ajikinsa,  wani ƙaton glass wanda yake kamar madubi ansanya rose aciki ya ɗaga tare da wurgi dashi,  ƙaran fashewan Glass ɗin take ya cika ɗakin,    tamkar wani zararre haka SOORAJ yaci gaba da wurgi da duk wani abun daya gani, gaba ɗaya ya watsar da kayan shafan dake kan mirror'n sa, kalmar da akace shiba Namiji bane, ita ce kawai keta yawo acikin brain ɗinsa, haka yakeji kamar zai haukace.

Hankalin Ummu ne yakai ƙololuwan tashi jin irin ƙaran fashewan abubuwa dake fitowa daga ɗakin Sooraj, Almustapha ne yaƙaraso da hanzari cike da mamaki yake kallon Ummu, hankalinsa atashe yace  "Meke damunsa ne haka?"

Hawayene kwance acikin idanun Ummu amma saitayi ƙoƙarin maidasu cike da damuwa tace "Almustapha bansani ba, kafun nazo ma ya rufe ƙofarsa, bantaɓa ganin Sooraj acikin irin wannan yanayin ba, bana fata acemin shaye shaye Sooraj yayi, domin sam ni ajinina ban haifi Mashayi ba, don Allah Almustapha kamasa magana ya buɗe ƙofarnan!" Duk yanda Ummu taso hana ƙwalla fitowa daga cikin idanunta saida suka fito.

Hankalin Almustapha amatuƙar tashe yashiga bubbuga ƙofan yana ƙiran sunan SOORAJ.

Ya soma fita daga hayyacinsa, gaba ɗaya ya birkita ɗakin, yayi watsi da komai. Jinine ke ɗiga ahanunsa sosai, gaba ɗaya ya ɓata ƙasan ɗakin da ɗigo ɗigon jini. Wani irin jiri ne ke ɗibansa, hakan yasanya shi faɗawa kan gado ya lumshe idanunsa, jiyake kamar duniyar zata kife tsabar tsananin ciwon da kansa ke masa.

Tun yanajin yanda Almustapha ke buga ƙofar har ya daina jin komai, sakamakon wani wahalallen bacci daya ɗaukesa.

Ummu kuwa ganin yaƙi buɗe ƙofan yasanya taje ta ɗauko spire key na ɗakinsa, Almustapha ne ya buɗe suka shigo atare, mamaki da tsorone ya bayyana akan fuskokinsu sakamakon yanda suka ga ɗakin ya sauya kammani, ga kuma ɗigo ɗigon jini akan tiles, kan gado Ummu ta kalla nan ta hangoshi yayi kwanciyar ruf da ciki, hannunsa kuwa duk jini ne wanda ya bushe.
Da sauri taƙarasa tare da sanya hannu ta taɓashi "Sooraj!!" Ta ƙira sunansa murya araunane, kana taɗan leƙa fuskarsa. Wani irin ajiyar zuciya ta sauƙe alokacin dataga bacci yake. Kallon Almustapha dake tsaye yayi shiru tayi, sannan tashiga ƙarewa ɗakin kallo, gaba ɗaya Sooraj ya hautsina komai, fasssun glasses da mirrors ne zube aƙasan ɗakin wanda idan baka kulaba tsab zasu raunata ka.

"Mutafi" tace da Almustapha tana me wucewa gaba, babu musu ya rufa mata baya.

Kallonta Almustapha yayi tsananin damuwa ne bayyane akan fuskarsa yace "Dama bashida lafiya ne Ummu? ko akwai wata damuwa ne?"

"Lafiyanshi ƙalau Almustapha ko da safe ma anan yayi breakfast, bansan mene yasameshi ba, ban taɓa ganinsa acikin irin wannan yanayin ba. Ko na ƙira Abbanku ne?"

Da sauri Almustapha yace "Karki ƙirashi Ummu, Isha Allah babu wata matsala maybe anɓata masa rai ne, kinsan Sooraj tun muna ƙanana bai iya ɓacin rai ba"

Ajiyar zuciya Ummu ta sauƙe sakamakon jin abun da Almustapha yace, tabbas SOORAJ bai iya ɓacin rai ba sam, idan ransa ya ɓaci to sai gyaran Allah. Daga nan bata sake cewa komai ba ta haura sama.

Zieyaderh ce zaune akan gado sanye take da dogon wando marar nauyi wanda yakasance rubber pencil, sai wata ƴar farar vest marar hannu, tayi shigarne saboda ana yanayi na zafi, jin

motsi kamar za'a shigo ɗakin, yasanya ta ɗaukar hijab ɗinta dake kusa da ita ta sanya da sauri, tana gama sanya Hijab ɗin taji ana knocking ƙofa, bedroom slippers ɗinta ta sanya kana ta nufi jikin ƙofan, tana buɗewa tayi arba da Ummu, ɗan matsawa baya tayi zatayi magana Ummu tarigata da cewa. "Kije ki kimtsawa Yayanki ɗakinsa, sannan kuma kiyi hankali wajen shiga ɗakin akwai fasassun kwalba zasu iya raunataki!" bata wani tsaya jin ta bakin Zieyaderh'n ba ta juya ta nufi ɗakinta, Mamakine yaɗan kama Zieyaderh musamman yanda taga damuwa kwance akan fuskar Ummu, sannan kuma Ummu bata taɓa cewa ta gyara masa ɗaki ba sai yau, da wannan tunanin acikin ranta ta sauƙo ƙasa kai tsaye ta nufi ɗakinsa, ko lura da Almustapha dake zaune acikin falon ba tayi ba.

Ahankali tatura ƙofar ɗakin ta shiga bakinta ɗauke da sallama, da fasassun glasses ɗin dake ƙasa tasomayin arba, baki buɗe take ƙarewa kowani kusurwa dake cikin ɗakin kallo, mamakin yanda aka hargitsa ɗakinne ya kamata, don kuwa ancire komai daga ma'ajinsa anyardashi ƙasa. Kallon Beedshet ɗin dake yashe aƙasa tayi sannan ta dawo da kallonta kan gado inda yake kwance, ƙirjinta ne taji yaɗan buga don ayanda taga ɗakin ahaukace batayi tsammanin ganin wani acikinsa ba. Idanunta ne suka sauƙa akan hannunsa wanda ke ɗauke da jini, wani irin tashi tsikar jikinta yayi, har saida ta ɗan ciza laɓɓanta. "Kenan shine yayi duk wannan abun?" tambayar da tayiwa kanta kenan tana me duban jinin dake jikin tiles ɗin. cikin takatsantsan ta ƙarasa gaban gadon tare da kafeshi da ido. "Meke damunshi? Bashi da lafiya ne?" zuciyarta ta tambayeta tambayar da bata da amsa. Ganin saƙawa da kuncewa ba nata bane yasanya ta ɗauki abun shara da packer tashiga tattara glasses ɗin, tana kammalawa ta ɗauko moper tayi mopping ɗin wajen, room freshner ta fesa acikin ɗakin take ko ina yaɗauki ƙamshi, kayan shafansa ta jere masa akan mirror sannan ta ninke bedsheet ɗin dake ƙasa ta ɗaurasa akan gado, saida ta maida komai dake cikin ɗakin nead kafun ta buɗe fridge ta ɗauko ruwa wanda bashi da sanyi sosai, audugan da ta gani acikin drawer ɗinsa ta ɗauko, ahankali taƙaraso jikin gadon tare da zama daɓas akan carpet ɗin daya kewaye gadon, dayake hannun nasa me ciwon ba'akan gadon yake ba hakan ya bata daman sanya hannunta ta kamo nasa hannun, ruwa ta ɗiga ajikin auduga sannan tashiga goge masa busashshen jinin dake hannunsa, ahankali takeyi kuma cikin nutsuwa gudun kada ta tashesa.
Ahankali yaɗan buɗe idanunsa da suka ƙanƙance, cute face ɗinta ya kalla da kuma small lips ɗinta, maida idanunsa yayi ya rufe yana mejin yanda take lallaɓa hannun nasa tamkar wanda aka bawa ajiyan ƙwai, sam batasan da cewa ya farka ba,domin gaba ɗaya tabada hankalinta ga aikin da takeyi, tas ta goge masa jini har ya zamana tana iya ganin yankewan da yayi, wani irin tausayinsa ne taji ya kamata, tasan dole idan ya farka sai ciwon yayi masa zafi, wata ƙila yanzu ma yanayi masa zafi, tunowa da haka yasanya taɗan sunkuyo da kanta, ahankali tashiga hura masa iskan bakinta adaidai kan ciwon, tayi hakanne saboda ta sama masa sauƙi, kasancewar idan taji ciwo in tana hurashi baya yi mata zafi, hakan yasa tashiga yi masa.

Wani irin sanyi yakeji na ratsa jikinsa, duk da cewa ciwon bayayi masa wani zafi sosai, amma hakan da tayi masa ya sanya ya samu relief, don har wani sabon bacci yaji yana fusgarsa, luf yasakeyi akan gadon tare da sake lumshe idanunsa. Sai yanzu yakejin ya dawo cikin sense ɗinsa, sai yanzu abubuwan da yayi ɗazu ke dawowa cikin brain ɗinsa, shiru yayi yana mejin

yanda zuciyarsa ke bugawa,  tabbas  SHI BA NAMIJI BANE  yau ya sake tabbatarwa kansa da hakan,  duk da cewa tuntuni yasan yana da rauni ta ɓangaren mu'amala da mace amma baiyi tunanin matsalartasa takai har haka ba,  bazai taɓa iya biyawa wata mace buƙatarta ba, sannan bazai taɓa iya alfahari da kanshi amatsayin cikakken Namiji ba,  baisan menene Sha'awa ba, bai taɓa jiba bai kuma san ya akeji ba, baisan ya Sex yake ba bai kuma san ya daɗi da rashinsa yake ba.  Tabbas shi gwanine akowani ɓangare amma awannan ɓangaren shi rago ne.  Zuwa yanzu ƙwaƙwalwarsa takusa daina aiki domin kuwa tunani na neman  illata ta, Meyasa bayajin Sha'awar mace? Me yasa bazai taɓa iya yin sex da mace ba? Me yasa bayajin wani abu na musamman ajikinsa dan gane da kowacce mace? Waƴannan tambayoyin sunjima suna barazanan tarwatsa zuciyarsa wajen neman amsarsu amma har yau baisamu amsan ba, hakan yasa ya rufe sirrinsa yabar abun amatsayin ƘADDARA me girma agareshi. Ajiyar zuciya me ƙarfi ya sauƙe, tare da rumtse idanunsa da ƙarfi, shi LOOSER ne, amma duk da haka  baya fatan ci gaba da zama looser akoda yaushe, saboda haka ayanzu baijin zai baiwa hawayen dake cikin idanunsa daman fitowa......

(Kowani bawa da irin ƙaddaransa, haka kuma kowani labari da irin yanda aka tsarashi, tabbas nasan nan gaba kaɗan zanzo wajen da bazai taɓa yi muku daɗi ba,  bakuma zanzo wajen ason raina bane ba, labarinne yazo ahaka, sai ansha gwagwarmaya, sai anfuskanci ƙalubale, sai kuma anjure ake kaiwa ga daɗi,   tabbas wasunku nasan bazasu iya juran wannnan wajenba, nasan ƙorafe ƙorafen ku zaita iskeni, nasan zakuyi challenge's ɗina,  wasunku zasu faɗamin magana mai daɗi, wasunku kuwa zanji saɓanin haka daga bakunansu, tun ayanzu ina fuskantar challenge's daga wajen  wasu, tabbas  nice me labari kuma nice me rubutu, idan asonane ako da yaushe nayi abun dazai faranta ranku, wannan shine kullum fata na, watarana inada important abun da zanyi amma haka nake squeesing nayi typing duk dan nafaranta muku, shin me zanji araina idan kuka jefeni da magana marar daɗi? kunaga zanji ƙarfin guiwa da farincikin sake yi muku wani fejin da zaku karanta? Tabbas nasan kuna ƙoƙari sosai sosai,musamman yanda kuke mini votes da comment, har acikin raina ku na dabanne My Wattpadians people, acikinku wasu ke faranta raina akuma cikinku wasu ke disturbing ɗina, amma nidai ina muku son so, nasan wasu mutane dagangan suke faɗan wata maganan duk dan su ɓata raina, amma babu damuwa dukanku ni inasonku.... Ni mutumce me ƙaunar duk wani maisona.... Please! Please!! Pleaseeeee!!! Idan kinsan nan gaba kaɗan zaki fito kiyi challenging ɗina akan labarinnan don Allah ki haƙura da karantawa wannan roƙo ne nayi muku masu challenge's ɗina.  Love You all and Son So My lovely fans❤*

*Vote and Comment*🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ!!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

#romance

*Chapter 34*

A hankali idanunta ke lumshewa da alama bacci takeji, amma kuma har izuwa wannan lokacin bata daina hura masa iskan dake bakinta ba.   Ahankali yake  fitar da numfashi, yana mejin sanyi na sauƙa acikin zuciyarsa, juyo da kansa ɓangaren da take yayi  tare da sauƙe gajiyayyun idanunsa akanta,   itama ɗago manya manyan idanunta tayi ta kalleshi, hakan yabawa idanunsu daman sarƙewa acikin na juna,  wani irin mimmiƙewa gashin dake jikinta sukayi, take tsikar jikinta ya shiga zubawa, tamkar wacce aka watsawa ruwan sanyi,  ba komai ya haifar mata da hakan ba kuwa, face arba da sexy eye balls ɗinsa da tayi,  wanda suke lumshewa ahankali tamkar na mejin bacci.  ƙasa tayi da idanunta, batare da ta sake hannunsa dake cikin nata ba, ƙofar ɗakin aka buɗe hakan yasa ta ɗago kanta da sauri ta kalli ƙofan, Almustapha ne ya shigo bakinsa ɗauke da sallama,  da sauri tatashi daga zaunen da take tare da sakin hannunsa ta koma gefe.   Ƙarasowa cikin ɗakin Almustapha yayi yana me ƙare mata kallo, cikin muryarsa me sanyi yace.  "Ya tashi ne?"

Kai kawai ta iya gyaɗa masa alamar "Eh" Raɓawa tayi tagefenshi ta fice daga cikin ɗakin. Binta yayi da kallo harta fice, ajiyar zuciya ya sauƙe tare da juyowa ya kalli Sooraj wanda ko motsawa baiyi ba.

"RAJ" Almustapha yaƙira sunanshi.

"Ummm!" Sooraj ya amsa masa akasalance yana meƙoƙarin tashi zaune.

Kallonsa Almustapha yayi sosai sai kawai yayi murmushi tare da cewa.   "Ya jikin naka?"

"Wani yace maka banida lafiya ne?" Sooraj ya faɗa yana me ƙoƙarin sauƙa daga kan gadon.

"No ni ne kawai nake tunanin baka da lafiya, ko dai mutanen naka ne suka motsa?" Almustapha ya tambaya yana me ƙoƙarin gimtse dariyan dake bakinsa.

Hararansa Sooraj yayi baice dashi komai ba ya nufi hanyar da zai sadashi da bathroom, sarai yasan iskancin Almustapha yawane dashi, yanzu idan ya tsaya yadinga ɓata ransa kenan.

Dariya Almustapha yayi tare da jawo laptop ɗin Sooraj ɗin yashiga amfani dashi.

Luf tayi akan gado tana me sauƙe ajiyar zuciya akai akai,  ƙwayan idanunsa ne keta yiwa nata idanun gizo,  lumshe idanunta tayi tare da sakeyin hugging pillow'n dake hannunta,  hancinta takai kan hannunta wanda tariƙeshi dashi, sosai hannunnata ke ƙamshinsa, wani irin kasalane

taji yana sauƙa mata,  tabbas ayanzu tayarda da cewa shiɗin na musammanne, kamar yanda komai da ya shafesa yake na musamman.

Tari yake sosai acikin toilet ɗin, wanda har hakan yaɗauki hankalin Almustapha dake zaune akan gado,  ɗan tsayawa yayi ajikin ƙofar toilet ɗin,  tare da cewa  "RAJ are you Okay?"  shiru baiji ya amsa masa ba, hakan yasa ya tura ƙofar bathroom ɗin,  da sauri ya ƙarasa wajen Sooraj dake tsaye agaban sink yana goge bakinsa da tissue.

Idanu Almustapha ya zaro tare da duban tissue ɗin dake hannun Sooraj hankalinsa amatuƙar tashe yace
"RAJ jinin mene wannan?"

Hararansa Sooraj yayi cike da ƙosawa yace
"Amma dai ban gayyatoka ba ko?"

Fuskar Almustapha babu alaman wasa ko tsokana yasake cewa. "RAJ jinin menene wannan? please tell me dama baka da lafiya sosai har haka ne?" Gaba ɗaya Almustapha ya ɗaga hankalinsa.

"Bakina ne ya fashe!" Sooraj yafaɗa ataƙaice yana me sanya ruwa ya shiga wanke bakinsa.

Kamar statue haka Almustapha ya tsaya yana kallon Sooraj, sam bai yarda da cewa wai bakinsa ne ya fashe ba, cikin yanayi me ɗauke da tsananin damuwa yace

"Shi kuma tarin da kake fa?"

"Uhhhhhh! am tired, please Mustapha leave me alone!!" Sooraj yafaɗi haka yana me dafe forehead ɗinsa, sam bayason irin wannnan tambayoyin da Almustapha keyi masa.

Jiki asanyaye Almustapha ya juya ya fice daga cikin toilet ɗin, saidai har cikin ransa yasan wannan jinin daya gani abakin Sooraj bana lafiya ba ne.

Almustapha na fita Sooraj ya sanya duka hannayensa ya riƙe weast ɗinshi,  iska ya fesar ta bakinsa tare da lumshe idanunsa, shikansa yasan bai taɓayin tari yaga jini ba sai yau,  sai alokacin ya tuna da cewa sam  bayashan maganinsa.  Wanka yayi kana ya ɗauro alwala, towel ɗaure a weast ɗinshi ya fito, black jeans and black t-shirt ya sanya, duk Almustapha na kallonshi, ganin zai fita baice dashi komai ba yasanya Almustapha tashi da sauri ya bishi, atare suka tafi masallaci.....

Saturday.

Kasancewar yau ba makaranta hakan yasanya tun tashinta tashige kitchine, zuwa yanzu ta iya

abubuwa da dama na dangane da girki,  saboda haka kafun Ummu ta sauƙo ma ta kammala kusan rabin aikin,  ɗauke da murmushi Ummu ta shigo cikin kitchine ɗin.

"Zieyaderh!" Ummu taƙira sunanta.

Barin aikin da takeyi tayi tare da juyowa, cikin ladabi tace " Ummu ina kwana"

"Lafiya lau"  Ummu ta amsa mata tana me ƙarasowa cikin kitchine ɗin.

Atare suka kammala aikin, kamar koda yaushe Zieyaderh ne ta jere duka abincin akan dinning,   Ƙamshin turarensa ne yafara sanar da ita zuwanshi, hakan yasa ta kasa ɗaga idanunta.  Shine agaba Almustapha na biye dashi abaya haka suka nufo wajen dinning ɗin, Ummu naganinsu tasaki murmushin jin daɗi.

"Morning Maaa!" Sooraj ya faɗa agajarce yana me ƙoƙarin zama akan kujera.

"Morning" Ummu ta amsa tana me ɗan shafa kansa.

Rungumeta Almustapha yayi tare da yimata kiss a forehead ɗinta cike da kulawa yace.
"Good Morning Ummuna!" Murmushi Ummu tayi tare da shima da shafa kansa  tace.
"Morning My Son"

Tana ɗago idanunta suka faɗa cikin na Almustapha hakan yasa ta saki murmushi tare da cewa "Ina kwana"

Murmushin shima yayi mata haɗe da cewa "Kintashi lafiya?"

"Lafiya" ta amsa tana me ƙoƙarin serving ɗinsu.
Ɗan satan kallon Sooraj tayi, taga gaba ɗaya hankalinsa nakan wayarsa, cikin sanyi tace.
"Yayah Ina kwana!"

Shiru yayi kamar bazai amsa ta ba sai kuma ya amsa mata da "Lafiya" acan  ƙasan maƙoshinsa.

Kamar yanda tasani kuma taga bashida wani abun sha daya wuce fruit salad, hakan yasa ta ajiye wani glass bowl wanda ke ɗauke da fruit salad  agabansa.

Serving ɗin kanta tayi sannan ta zauna, Ummu da Almustapha ne kawae keta hira, itakam dama mezatace acikin hirarsu, shikuwa SOORAJ dama kowa yasan ba magana yake ba....  Jin hirar su Ummu na damunsane yasanyashi miƙewa tsaye yabar wajen, da kallo Ummu tabisa har ya shige ɗakinsa.
Ahankali Zieyaderh itama tamiƙe tsaye don dama tuntuni ta ƙoshi da abincin, damar tashi kawai takejira.       Sunanta da Ummu taƙira yasanyata dakatawa daga yunƙurin barin wajen da takeyi.

"Zauna inason magana dake" Ummu tafaɗa tana me ƙokarin aje kofin tea din dake hannunta.

Ƙirjinta ne yashiga bugawa lokaci ɗaya taji gabanta ya faɗi, aɗaɗare ta koma ta zauna akan kujera,   miƙewa tsaye Almustapha yayi tare da ɗaukan kofin tea dinsa yabar wajen.

"Zieyaderh!" Ummu taƙira sunanta.

Bata iya amsawa ba saidai ɗago kai da tayi ta kalli Ummun jiki asanyaye.

Ummu bata wani damu da rashin amsawannata ba tace "Nayi magana da Mas'oud saidai abun da yafaɗamin akanki ya matuƙar girgizani, inaso kifaɗamin gaskiyar wacece ke? sannan kuma inason sanin ina mahaifanki suke da har zaki nesanta kanki dasu, karkimin ƙarya don banason ƙarya, Inajinki!" Ummu tafaɗi maganar tana me maida gaba ɗaya attention ɗinta ga Zieyaderh.

Ƙirjinta ne ya buga take idanunta suka cicciko da ƙwalla, bakinta na rawa tace.   "Banda mahaifiya tun ina ƙarama ta rasu, natashi agaban Mahaifina da kuma matarsa sam bansan wani abu waishi soyayya ba, kullum cikin ƙunci da kaɗaici nake rayuwa, babu wani wanda yadamu da farinciki ko jin daɗi na, bansan kowa daga cikin dangin mahaifiyata ba saboda naji Babana yace ita ba ƴar garinmu bace, ban kuma san inane garinsu ba,  tun ina ƙarama nayi sabo da wahalwahalun rayuwa, duk wani rashin gata ya ƙare akaina, sam babana bai ɗaukeni ƴa wacce ya haifa acikinsa ba,  bansan daɗin mahaifi ba" Kuka ta fashe dashi tare da kifa kanta ajikin table, saida tayi kuka sosai sannan ta ɗago kanta hawayenta ta share kana ta cigaba da bawa Ummu labarinta, kama daga kan zancen aurenta da tsoho ɗan dashe har izuwa yanzu da take tare dasu, durƙusawa tayi akan guiwowinta cikin kuka tace "Ummu ki gafarceni saboda ni Ya Mas'oud yayi miki ƙarya."

Hawaye ne suka cika idanun Ummu, tabbas yarinya ƙarama kamar Zieyaderh bai kamata ace an banzatar da ita har haka ba, ya kamata ne ace anbata kyakkyawan kulawa.
Kafaɗunta Ummu takama ta ɗagota cike da kulawa tashiga share mata hawayen dake kwaranya akan fuskarta.

"Ya isa daina kukan haka nan, naga kanki yayi datti ɗauko mayafinki muje shagon saloon!" Ummu tafaɗi haka cike da kulawa.

Jiki asanyaye haka Zieyaderh ta haura sama don ɗauko mayafinta. Da kallon tausayi Ummu tabi bayanta, bawani jimawa sosai sai gata ta dawo sanye da hijab ajikinta.

Ko amota shirune ya biyo baya tsakaninsu, dan kowa da abun dayake saƙawa acikin ransa. Ummu kam tuni tagama yanke shawaran abun dake ranta, wayarta ta ɗauka ta turawa Almustapha da Sooraj text akan tanason ganinsu, daga haka ta aje wayarta.

Sosai aka gyarawa Zieyaderh dogon gashinta, lokaci guda ya ɗauki ƙamshi da walwali, daga

shagon saloon Super market suka wuce, sosai Ummu ta sai mata kayan kwalliya dana sawa masu kyaun gaske, daganan suka ɗauko hanyar dawowa gida.

Tana sanya ƙafarta acikin falon idanunta suka sauƙa acikin na Almustapha wanda yasha kyau cikin baƙaƙen kaya. Da sauri tayi ƙasa da kanta, don har acikin ranta batajin daɗin irin kallon da yakeyi mata, kai tsaye ta haura sama nan tabar Ummu afalon.

Ummu na zama akan kujera Ya buɗe ƙofar ɗakinsa ya fito, sanye yake da army 3 guater jeans da kuma black t-shirt, fuskarsannan babu alaman farinciki ko sakewa akanta, haka yaƙaraso cikin falon, akan kujeran dake facing na Ummu ya zauna tare da ciro phone ɗinsa daga aljihun wandonsa yasoma dannawa.

Gyara zama Ummu tayi cikin yanayi na kulawa tace "Banƙiraku nan don na faɗa muku wasa ba"Kallon Almustapha tayi cikin kulawa taƙira sunanshi, da "Na'am ya amsa mata tare da ɗagowa ya kalleta.

"Nasan banice na haifeka ba, amma kuma kana mini biyayya tamkar yanda zakayiwa mahaifiyarka, haƙiƙa amatsayina na yar mahaifiyarka inada ƴancin dazan iya zartar da duk hukuncin da naso akanka,  kasani tamkar yanda nakeson ɗan cikina Sooraj kaima haka nake sonka,  saboda haka na zaɓa maka matar da zaka aura ina fatan bazaka watsamin ƙasa a ido ba?"

Murmushi Almustapha yayi tare da sanya hannuwansa ya kama na Ummu.  "Bazan taɓa iya bijirewa umarninkiba Ummu, ke uwace agareni saboda haka ina maraba da duk wani zaɓinki"

Murmushin jin daɗi Ummu tayi tare da sanya hannu ta shafa kansa cike da ƙaunarsa tace "Nagode sosai Almustapha Allah ya maka albarka!"

"Ameen Ummu, amma wace me sa'ace haka tayi gamdakatar ɗin samuna?" cike da zolaya yayi tambayar.
Dariya Ummu tayi tare da cewa "Kanason sani?"

"Sosaima" Almustapha yabata amsa cike da zaƙuwa.

Duk abunda suke yanajinsu yana kuma kallonsu, amma ko uhummm baice ba, azahirin gaskiya wayarsa yake dannawa abaɗini kuma gaba ɗaya hankalinsa na garesu.

"ZIEYADERH itace wacce na zaɓama kuma itace wacce zatayi daidai da rayuwarka!"

Maganar Ummu data faɗane yasanyashi ɗago da kansa ahankali ya kalleta..

"Zieyaderh!"Almustapha ya maimaita sunan abakinsa, kansa ya sunkuyar ƙasa fuska ɗauke da murmushi yace

"Na'amince!"

Tsaida duk wani abu da yakeyi yayi yana kallonsu, hakanan yaji tamkar ruwan jikinsa na ƙonewa.

(fever na damuna so banajin daɗin jikina please kuyi manage, wannan ma da ƙyar nayi muku, idan naji sauƙi gobe Insha Allah zakujini🙏🏼)
Naziphi Yarima:
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ!!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*WATTPAD*
fatymasarduna
#romance

*Chapter 35*

Sunkuyar da kansa ƙasa yayi tare da ɗan ciza laɓɓansa, idanunsa ya mayar kan wayansa, samun kansa yayi da kasa cigaba da amfani da wayan, ji yayi gaba ɗaya jikinsa yayi weak.

"SOORAJ!" Oummu taƙira sunansa.

Ɗago kansa yayi ya kalleta batare daya amsa mata ba, itama bata nemi amsawar nashi ba taci gaba da cewa "Kaji abun da muka tattauna akai, amma bakace komaiba, sannan kuma inaso na yaba maka game da namijin ƙoƙarin taimakon da kayiwa Zieyaderh, insha Allah, Allah Zai baka lada!" Oummu tafaɗi maganar tana murmushi.

Ko Uhumm baice ba, sai ma kallon Oummu'n daya keyi, ganin damuwarta dana Almustapha zasu kasheshi yasanyashi tashi gaba ɗaya yabar musu gidan.

Kwance take luf akan bed ɗinta, biscuit ne ahannunta tanaci da kaɗan kaɗan, turo ƙofar ɗakin da akayi ya sanyata tashi zaune da sauri, ganin Oummu yasanya tasakin murmushi tare da cewa "Barka da shigowa Oummu"

Murmushi Oummu tayi tare da zama akan wata kujera, cike da kulawa tace. "Magana nazo muyi dake Zieyaderh!"

Gaban Zieyaderh ne ya faɗi, amma saita dake tare da cewa "To"

Murmushi Oummu tayi tare da dafa kafaɗun Zieyaderh'n tace "Inaso kishirya ƙarshen wannan week ɗin zamuje ƙauyenku dan inason naga mahaifinki!"

Dummm haka ƙirjin Zieyaderh ya bada wani irin sauti, hawaye ne suka cika idanunta alokaci guda, bakinta na rawa tace "To!"
Murmushi Oummu tayi don tafahimci cewa tsoron zuwa ƙauyen Zieyaderh keyi, cikin son kwantar mata da hankali tace "Kar kisanya tsoro aranki idan munje bazan barki ahannunsu ba zandawo dake nan, kawai dai naga ya kamata ace mahaifanki susan inda kike ne!"

Ɓoyayyar ajiyar zuciya ta sauƙe tare da gyaɗa kanta kawai, alaman ta gamsu. Oummu na fita daga ɗakin. Zieyaderh ta fashe da kuka, sosai tayi kewar babanta, ko awani hali yake ciki Allah masani? duk da cewa bai nuna mata ƙauna ba, amma ita har gobe, akwai ƙaunarsa acikin jininta, saboda koba komai Uba Uba ne koda baikasance na gari ba.

MONDAY

Cikin yanayi naɗan sauri sauri yake tafiya, don 8 daidai jirginsu zai ɗaga zuwa garin Lagos. Sanye yake da black and white suit wanda suka matuƙar yi masa kyau, black cover shoe ne ƙiran kamfanin Gucci sanye aƙafansa me tsadan gaske. ƙamshi kawai yaketa zubawa, yayinda gashin kansa keta shinning na mayukan da aka shafa masa, yau kam masha Allah Yayi kyau har ya gaji da haɗuwa.

Manta biology text book ɗinta da tayi, yasanya ta taho cikin sauri don komawa ta ɗauka, sam bata kulaba saiji tayi sunyi karo da juna, wanda hakan yajawo zubewan documents ɗin dake hannunsa. Da sauri taja da baya ƙirjinta na bugu da ƙarfi, idanunsu ne suka faɗa cikin na juna, hakan yasanya taji tamkar an jona mata shocking, kallonta yayi sannan ya kalli ƙasa inda documents ɗinsa suka zube, da sauri ta durƙusa ƙasa hannunta har rawa yake wajen harhaɗa documents ɗin waje ɗaya. Agogon hannunsa ya kalla yaga 7:30 kuma sai ya biya ta office kafun ya wuce airport, gashi duk gani yake kamar bata sauri wajen tattara documents ɗin. Itakuwa bakomai ke cinta ba face tsoro hakan yasa gaba ɗaya bata sauri, ƙamshin mayen turarensa dake zautar da ita ne, ya daki hancinta sosai, hakan yasa ta ɗan ɗago da kanta, daidai lokacin shi kuma ya ɗan ranƙwafo don tattare documents ɗin, kanta ne ya bugi haɓanshi wanda hakan yasashi rumtse ido, ahankali yace "Auchhhh!!" dan ya ɗanji zafi sosai.
Sakin documents ɗin tayi tare da sanya hannuwanta ta rufe bakinta, wani sabon tsoro ne yasake kamata, baki na rawa tace "Kayi haƙuri Wallahi bansaniba ne!!"

Baikulata ba haka yasanya hannu ya shiga tattara papers ɗinsa da suka watse. ganin haka yasa itama tashiga tayasa tattarewa, gaba ɗaya ƙamshinsa ya jefata acikin wani irin yanayi, jin kanta take cikin wani baƙon yanayi, har wani iska ne ke shiga jikinta. Idanunta ne yakai kan wani papers da iska ke shirin kaɗasa wani wajen, da sauri takai hannunta zata kamo paper'n,

shima hannunsa yakai batare

da yayi zato ba yaji hannunsa ya sauƙa akan nata, atare sukaji wani shock da sauri yajanye hannunsa daga kan nata tare da ɗaukan paper'n ya miƙe tsaye, baijira komai ba ya nufi wajen motarsa wanda tuni dama driver na jiransa, yana shiga gidan baya driver yayiwa motar key suka fice daga cikin gidan.   Saida taji alamun fitansu sannan ta iya miƙewa tsaye daga tsugunnen da take,  batare da ta saniba wani murmushi ya bayyana akan fuskarta take kuma saiga hawaye sun ziraro daga cikin idanunta, Wallahi ko za akasheta bazata iya fassara abun da takeji dangane dashi ba, tausayi ne? rauni ne? Ita duk takasa ganewa, tasan koma menene tabbas abun da takeji akanshi na musammanne,  idanunsa kaɗai da ta kalla ya sanya taji wani iri ajikinta, tabbas da zata samu mai bata amsar abun da takeji dangane dashi da taso hakan fiye da komai, watarana idan tagansa sai taji kamar tasanya masa kuka, watarana kuwa jitake kamar taje da gudu ta shige jikinsa tayi kuka sosai, wataƙila hakan zai ɗan sama mata salaman abun dake ranta.    Sam tama manta da cewa text book zata ɗauko sai kawai ta koma tashiga mota.
Luf tayi ajikin kujeran motar,  ƙamshinsa da har yanzu takejinsa acikin hancinta shiyayi fatali da duk wata nutsuwarta, sam tarasa me yasa takejin ƙamshin nasa har yanzu duk da cewa baya tare da ita,  hannunta takai tashafi fuskarta, sai alokacin ta gano daga inda ƙamshin ke fitowa, sake kai hannunta kan hancinta tayi tare da shunshunawa, tabbas hannunta da ya taɓa ne ke ƙamshin, wani irin sanyi taji acikin zuciyarta, ɗaura hannun tayi akan fuskarta tare da lumshe idanu, ahaka har suka iso cikin school ɗin.  Yau kam tayi late duk da cewa bahaka tasoba, don sunada biology, kuma shine first period, bakuma taso tayi missing lecture ɗin biology ko kaɗan,
  ai kuwa tana zuwa bakin class ta iske malami aciki, da ƙyar ya barta tashiga cikin ajin, tana zama akan chair ta sauƙe ajiyar zuciya, hannu Nasmah tasanya ta ƙasa ta muntsineta akan cinyarta,   ƙasa ƙasa tayi dariya tare da rumtse ido alaman taji zafin muntsinin, hakan da tayi kuma sai ya tuna mata da MR.HELPER ɗinta, yanayin yanda ya rumtse idanunsa da kuma yanda yace "Auchhh!!" Baƙaramin kyau yanayin yayi masa ba, musamman yanda pink lips ɗinsa suka motsa abun saiya ɗauki hankalinta, sai ayanzu moment ɗin kedawowa cikin brain ɗinta da kyau, wani murmushi tasake tare da lumshe idanunta.
"Kenan shima yanajin zafi idan abu yasameshi?" A zuciyarta ta tambayi kanta, wani murmushin ta sakeyi alokacin da ta tuna da kyawun idanunsa, a iya tsawon rayuwarta itakam bataga irinsa ba, bata kuma tunanin zata taɓa ganin wani irinsa.    Ataƙaice dai  har biology teacher'n yafita, bata tsinci komai daga cikin darasin daya koyar ba,  gaba ɗaya hankali da tunaninta yau akan Mr.Helper yake.
Su Shukra da kansu yau sun fuskanci cewa tana cikin farinciki, don koda aka fita break zagewa tayi tayita zuba musu surutu.

7:59 AM

Gyara zama yayi tare da ɗaura sit belt ajikinsa, bayansa ya jingina ajikin luntsumemiyar kujeran dake cikin jirgin, 8:00 daidai jirginnasu ya ɗaga zuwa sararin samaniya,  tafin hannunsa yakai ya rufe fuskarsa, ko hakan zaisa yaɗan rage stress ɗin dayake ciki, ahankali yaji wani baƙon ƙamshi na ratsa cikin hancinsa yana me cakuɗa da numfashinsa, mamakine yakamasa don

sam baisan daga ina ƙamshin ke fitowa ba, ɗan waigawa bayansa yayi, dayake ɓangaren business class ne kowa sha'aninsa kawai yake, babu kowa kuma akusa dashi dasai yace na kusa dashine ke ƙamshin. Sake shunshuna hannunsa yayi, sai alokacin ya tabbatar da cewa tabbas hannunsa ne ke ƙamshin, bawani turarene me ƙarfi ba, irin dai turaren nanne da idan mutum yasa saima ka matso kusa dashi kafun kajiyo ƙamshin. "Itace!" yafaɗa in a silent voice ɗinsa, sake kai hannun kan hancinsa yayi tare da ɗan taɓe lips ɗinsa. Azuciyarsa yace.
"Su ƙamshi manya" Jarida ya ɗauka yashiga karantawa tare da watsar da duk wani tunani dake ransa.

Hadari ne sosai ya haɗu agarin kasancewar anacikin yanayi na damuna, 3:30 pm, fitowarsu sallan La'asar kenan.
Tana idar da sallan ta fito daga cikin masallacin, sosai take matuƙar son yanayi irin wan

nan, ahankali sanyin iska ke busa ko ina, hijab ɗinta iska keneman yayewa, da sauri tasanya hannuwanta ta kameshi ƙam ajikinta. Yanayin na fusgarta hakan yasa kai tsaye ta nufi wajen da garden ɗin makarantar yake.
Ƴan tsirarun ɗalibai ne awajen, kowa harkan gabansa kawai yake. Gefe da garden ɗin wasu kujeru ne masu kyaun gaske da aka tanada don zama, tana zama aka soma yayyafi hakan yasa tatashi da sauri don komawa cikin makaranta. Idanunta ne suka sauƙa akanshi, tsaye yake ya sanya duka hannuwansa acikin aljihun wandonsa, idanunsa ƙyam akanta fuskarsa ɗauke da beautiful smile, cike da mamakin ganinsa tasaki murmushi tare da sanya hannu ta kare kanta, kasancewar zuwa lokacin ruwa ya fara sauƙa kaɗan kaɗan. ganin haka yasanyashi takowa yazo gab da ita, cikin sexy voice ɗinsa yace.
"Kina tsoron ruwa ne?"
Murmushi tayi wanda har saida ya bayyana white teeth ɗinta, kanta ta kaɗa masa alamar "Eh" ruwane ya ɓarke me ƙarfin gaske hakan yasa lokaci guda ta ruɗe, shikansa ƙarfin ruwan yabasa mamaki, hannunta ya kama zuwa wani ɗan rumfa dake wajen, duk da shigarsu rumfar iya kawunansu kawai ruwan zai tare amma banda gangar jikinsu. Cikin yanayi na tsoro ta naɗe hannayenta akan ƙirjinta, kallonsa tayi da fuskarta dake jiƙe da ruwa. Murmushi yayi mata tare da ɗage mata giransa ɗaya, itama murmushin tayi masa tare da sake takure kanta waje ɗaya, don bawai sun tsirane daga ruwanba, har yanzu yana dukan jikinsu, tuni uniform ɗinta yajiƙe sunbi jikinta sun lafe, shikansa Pharouk gaba ɗaya ya jiƙe duk da cewa akwai denim Jacket ajikinsa hakan bai hanashi jiƙewa ba. bakinta har rawa yake saboda sanyi.
"Zieyaderh!" yaƙira sunanta akasalance.

Ɗago fuskarta tayi ta kalleshi, idanunsa ya sauƙe akan beautyful lips ɗinta wanda suka jiƙe suke kuma ɗigar da ruwa, wani irin tashi yaji tsikar jikinsa yayi, take lissafin kansa suka shiga kuncewa, wani irin saliva dake maƙale a maƙoshinsa ya haɗiya, sam bata ɗauke idanunta akansa ba, yanayin sanyin da take ji yasanyata lumshe idanunta tare da ɗan buɗewa alokaci guda, hakan da tayi baƙaramin kyau yaƙarawa face ɗinta ba, take yaji wani irin different feelings na sauƙa ajikinsa, ji yake kamar yajawota jikinsa ya bata professional kissing, amma mene sunansa idan yayi hakan? jingina bayansa yayi da jikin bango tare da lumshe idanunsa, bugun zuciyarsa ƙaruwa take, wani irin maganaɗisun sha'awarta ne ke fusgarsa, lokaci guda mood

ɗinsa ya sauya.  Cikin zaƙuwa da tsayuwan Zieyaderh ta juyo ta kalleshi acikin yanayinta na shagwaɓa tace "Am tired!!"  Ahankali ya buɗe idanunsa wanda sukai ja ya sauƙesu akanta, wani irin yarrr taji ajikinta sakamakon kallon cikin idanunsa da tayi,  batasan irin wannan yanayin ba hakan yasa ahankali tace  "Are you okay?"

Akasalance yayi murmushin daya bayyana dimples ɗinsa.
"Yes am okay!" yafaɗa yana me ƙare mata kallo,  murmushi tayi masa sannan ta juya tacigaba da kallon ruwa sam ta manta bata maida hannuwanta ƙirjinta ta kare baiyanar dasukayi ba, don saboda yanayin sanyin da ake ciki yasanya tsikar jikinta mimmiƙewa, hakan yasa nipples ɗinta ma suka miƙe tsaye, har idan kayi  mata kallon tsab zaka iya ganinsu.   Sauƙan idanunsa akan ƙirjinta baƙaramin gigita masa tunani yayi ba, take yaji tunaninsa ya tsaya cak, da sauri ya ɗauke idanunsa daga kanta tare da sanya baki ya cije laɓɓansa. (Nasan team RAJ, zasuce inama da ita da Sooraj ne😝)    Wani irin tsawa da aka buga ne ya matuƙar firgitata har batasan sanda ta dawo baya da sauri ba, sambata kula ba ta faɗa jikinsa, ƙamƙame jikinta tayi ƙaƙam tare da rumtse idanunta.   "Innalillahi" kawai take ambata acikin zuciyarta don ta tsorata,  ashe ba ita kaɗaice ke ambatan hakan ba harda Pharouk don alokacin da bayanta ya mannu da ƙirjinsa baƙaramin ruɗewa yayi ba, har numfashinsa saida yashiga seizing na ƴan wasu minutes.    Hanneyansa dake rawa yaɗaura akan shoulder ɗinta, hakanne ya bata damar dawowa cikin hankalinta, da sauri ta matsa gefe, cikin wani irin kunya ta jawo hijab ɗinta ta rufe fuskarta.  "Me na aikata haka?" ta tambayi kanta cike da nadama.

Matsowa yayi gab da ita tare da sanya hannu ya ɗ

ago haɓanta, hijabin ya ja baya fuskarta ya bayya, da sauri ta kulle idanunta don batajin zata iya haɗa idanu dashi.
Murmushi yayi mata ahankali ya sunkuyo da kansa daidai fuskarta,  kiss yayi mata a forehead ɗinta,  tare da kai bakinsa daidai saitin kunneta ahankali yace  "Ki kulamin da kanki!"  Yana gama faɗan haka ya juya acikin ruwan  ya tafi, yayi hakane saboda matuƙar ya ƙara some minutes awajen, zai iya hugging ɗinta.  (Chab lallai Pharouk yau zakasha zagi awajen ƴan team ɗin SOORAJ)

Buɗe idanunta tayi ahankali cike da fargaba da kuma tsoron abun daya mata, babu wani namiji daya taɓa yi mata kiss saishi, mekenan hakan yake nufi? ta tambayi kanta cike da mamaki, kallon bayansa tayi don zuwa yanzu yayi mata nisa, tafiya yake kamar baidamu da ruwan dake dukansa ba.

*SOORAJ*
Tsaye yake acikin wata baranda, dagashi sai wani white crazy jeans dake sanye ajikinsa, bashida ko riga sosai murɗaɗɗiyar surar jikinsa ta bayyana,  glass cup ne ahannunsa wanda ke ɗauke da ruwan inibi,   ruwa da iska ake sosai, amma ko kaɗan baijin wannan sanyin ajikinshi. Hakanan yakejin kansa cikin wani bad mood,  baikuma san dalilin hakan ba, tunanin dake maƙale azuciyarsa ayanzu yafi komai damunsa, meyasa yake ganinta acikin idanunsa? meyasa yakeji tamkar anrubuta wani abu daya shafeta acikin zuciyarsa?  yana da buƙatar sanin

meyakeji, da kuma dalilin dayasa yakejin hakan acikin rai da zuciyarsa.

Ahankali ƙarfin ruwan ke tsagaitawa, ganin haka yasa cikin sauri ta nufi farfajiyan makarantar, harda ɗan sassarfa take haɗawa wajen shigewa cikin ajinsu, Nasmah da Shukra dake tsaye bakin window sukayo wajenta da sauri cikin damuwa suka haɗa baki wajen tambayanta ina taje "Garden" ta basu amsa ataƙaice. Sunyi mamakin hakan amma sai kawai suka share suka cigaba da hiransu.

Ruwan na tsagaitawa aka tashesu ko 5 ma batayi ba, saboda sosai garin ya ɗau sanyi. Atare suka fito ita dasu Nasmah, daidai lokacin wata baƙar Car ƙiran Jeep ta kunno kai cikin makarantar, tsayawa sukayi a compound ɗin makarantar Zieyaderh na ta baza idanu ko zata hango Kamalu driver. Ƙasa yayi da glass ɗin motar tare da kafeta da idanunsa, ahankali ya danna horn, hakanne ya ɗauki hankalin ɗalibai da yawa har kowa yajuyo yana kallonsa, idanunta ne suka sauƙa akanshi, tsananin mamakine ya kamata, tabbas tasan ita yazo ɗauka, to ina Kamalu driver? ya ma akayi yasan antashesu? Duk bata dame amsa mata waƴannan tambayoyin, hakan yasa tayiwa su Nasmah sallama tanufi inda yake. Tana buɗe murfin motar wani sassanyan ƙamshin turare ya daki hancinta, saidai wannan turaren sam ba irin wanda yake gigita tunaninta bane. Ɗan satan kallonsa tayi tare da cewa "Ina wuni"

Bai amsa mata ba sai dai murmushi da ya bayyana akan fuskarsa. Har suka soma tafiya babu wanda yasake ce da ɗan uwansa wani abu, saidai kuma yana yawan satan kallonta lokaci zuwa lokaci, aranta mamakin yanda halinsu ya kusan zuwa ɗaya take. "Kenan su duka familyn su haka suke?" ta tambayi kanta azuci. "Uhmmm gwara wannan ma ae yana murmushi amma wancan Mr.Helper ɗin kam, ko murmushinsa bantaɓa gani ba" Ita kaɗai take magana da zuciyarta har suka iso gaban wani tafkeken mall.

(Najidaɗin addu'o'in ku agareni, nagode Allah yabar ƙauna💜
then Gaskia kunbani dariya😅 wae don nace nan gaba abun dazai faru acikin book ɗin bazai muku daɗi ba shine duk kuka ruɗe haka, hahhhhh ku kwantar da hankalinku wasa nake muku😝)

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ!!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*WATTPAD*
@fatymasardauna
#romance

*Chapter 36*

Agaban ƙaton mall ɗin yayi parking motar tare da dubanta, murmushi ɗauke akan fuskarsa yace  "Muje ki rakani sayayya"

Mamakine ya bayyana akan fuskarta, amma  sai ta share bata nuna ba, buɗe murfin motar tayi tare da fitowa waje.  Yana gaba tana biye dashi abaya,  haka suka nufi cikin ƙaton mall ɗin. Direct ɓangaren kayayyakin  mata suka nufa,   ita dai binsa kawai take, aranta  tana me mamakin ganin sun shigo wajen sayayyar mata,   ɗan juyowa yayi ya kalleta,  matsawa gefe yayi tare da yi mata nuni akan ta shige gaba. Kallonsa tayi alaman me hakan ke nufi.    "Muje mana ko bazaki tayani zaɓa bane, matata zan sayawa kuma agemate ɗinki ce, shiyasa nafiso ki zaɓa mata masu kyau!"  Ya faɗi maganar yana me jujjuya wata brown ɗin abaya dake hannunsa.  Murmushine ya bayyana akan  fuskarta.
"Kenan dama yana da mata?" tayiwa kanta tambayar cike da ɗan mamaki.   Jin cewar matarsa zai sayawa, yasanya duk wani abu da tagani idan ya mata kyau saita ɗauka, dogin riguna kala uku ta zaɓa masa masu kyaun gaske, wanda suke asalin ƴan dubai new designer.    Da ace tasan kuɗinsu da bata ɗauka ba, don kowanne kuɗinsa yakai 35k, kaya masu kyau ta zaɓa masa, duk wanda ta ɗauka sai yayi murmushi yace yayi, daga ɓangaren kayayyaki ɓangaren chocolates and sweets suka nufa,  wannan kam shida kansa ya ɗauka, sai ya duba wanda baida zaƙi sosai sannan yake sanyawa acikin basket ɗin dake hannunsa.
Koda suka kammala, cewa yayi tajirasa awajen da ake biyan kuɗi, komawa cikin mall ɗin yayi ya shiga dube duben ƴan abun da yake da buƙata.

Yana dawowa ya biya kuɗin, wani daga cikin yaran dake aiki awajenne ya kai musu kayan mota.

Ahankali yake murza steering motar, yana me gutsuran diary milk chocolate ɗin dake hannunsa, kallonta yayi tare da ɗan sakin murmushi  "Hummm" yafaɗa yana me miƙo mata chocolate ɗin alaman ta amsa.  Murmushi itama tayi masa tare da  kaɗa kanta alamar "A'a"

"Bafa kyauta bane, gutsura zakiyi ki bani!" ya faɗi haka yana me mayar da chocolate ɗin bakinsa.

Idanunta ta waro cike da mamaki, sai kuma abun yabata dariya wanda har hakan yasa ta dara, kallonta yayi tare da cewa "Kina mamaki ne? bazan iya baki duka bane shiyasa!"   Yayi maganan murmushi ɗauke akan fuskarsa.

"Nagode ma"  Tafaɗa tana me gimtse dariyan dake bakinta, gaba ɗaya yasata nishaɗi don yanayin yanda yayi abun sai yazama tamkar wani small babyyy.
Daga haka babu wanda yasake ce da ɗan uwansa wani abu har suka iso gida.    ƙoƙarin buɗe murfin motar take  muryarsa ya dakatar da ita, inda yake cewa tashiga da kayan da suka sayo ciki,   gidan baya inda aka sanya kayan ta buɗe tare da ciro ledodin ta wuce cikin gidan da su.

Bata samu kowa afalon ba hakan yasa kai tsaye ta wuce sama, tsayawa tayi ajikin ƙofar ɗakin Oummu tare dayin knocking. "Yes,Come in!" Oummu dake ciki ta bada amsa ataƙaice. Tura ƙofar tayi ta shiga bakinta ɗauke da sallama. "Oummu naganinta ta saki murmushi tare da cewa.
"Ƴan makaranta andawo kenan?"

Murmushi itama tayi cike da girmamawa tace "Eh nadawo, Oummu sannu da gida!"

"Waƴannan ledodinfa na menene?" Oummu ta tambaya fuska ɗauke da mamaki.

"Ummmm dama Ya Almustapha ne yace nashigo dashi ciki!" tafaɗa cikin sanyin murya tana me aje ledodin.

Murmushi kawai Oummu tayi tare da cewa "Aini nace yaje ya ɗaukoki, kasancewar naga anyi ruwa garin duk yaɗau ki sanyi, gashi Kamalu ma bayanan, ki cire uniform ɗin sai kici abinci ko!"

Kai ta kaɗa alamar "To" sannan ta juya ta fice daga cikin ɗakin.

Tana shiga ɗaki ta soma cire uniform ɗin, gaba ɗaya wani irin sanyi takeji, ruwan daya daketa baƙaramin shiga jikinta sanyinsa yayi ba, gashi harwani ciwo ciwo takejin kanta nayi. Da ruwan ɗumi tayi wanka kana ta sanya wata doguwar riga me kauri, rigan irin jallabiyannan ne na mata, amma tana da kauri sosai, sannan kuma haɗe take da hula, hulan ta sanya ta rufe kanta. Saida tayi sallan Magriba sannan ta buɗe ƙofar ɗakin ta fito don samawa cikinta abinci. Ahankali take sauƙowa daga kan matattakalan falon, tunkafun ta gama sauƙowa, ƙamshin turaren daya zame mata abunso ya daki hancinta, lumshe idanunta tayi tare da waresu alokaci guda, mamakine yakamata na rashin ganinsa afalon, don tasan tabbas indai taji ƙamshinsa to yana wajenne. Harta gama sauƙowa daga kan steps ɗin bata iske kowa acikin falon ba, kai tsaye kitchine ta wuce, kasancewar yau ba a haɗa abinci akan dinning ba. Fried cous cous and egg sauce aka dafa, kaɗan ta ɗiba don bata wani cika cin abinci da yawa ba, buɗe ɗayan food flask ɗin tayi, nan taga pepper soup ne na chicken's aciki, rufewa tayi don wannan ɗinma kaɗai ya isheta. fridge ta bude ta ɗauko ruwa, daidai lokacin Oummu tashigo cikin kitchine ɗin, ganin Zieyaderh a kitchine ɗin yasanya ta cewa.
"Yauwa Zieyaderh zoki kaiwa Sooraj coffee yana ɗakinsa"

Wani irin ƙululuuuuu haka ƴaƴan cikinta suka hautsina, ambatonsa ba ƙaramin faɗar mata da gaba yake yi ba, batasan mene dalili ba koda zancensa ake sai taji gabanta ya faɗi, ko kuma taji zuciyarta ta tsinke, ganinsa kuwa baƙaramin je fata acikin wani irin Yanayi yake ba. Bata gama idar da tunanin nata ba, Oummu ta miƙo mata wani tray me ɗan faɗi, wanda samansa ke ɗauke da kayan haɗin coffee da kuma ɗan madaidaicin cup me kyaun gaske, sai kuma small flask. "Idan kinje ki haɗa masa, ai dai kinga yanda na haɗa masa ranan ko?" Oummu ta tambaya tana me miƙa mata tray ɗin. Kamar wadda aka zarewa laka ajiki haka ta amshi tray ɗin tare da cewa "Eh nagani" Ficewa tayi daga cikin kitchine ɗin, yayinda zuciya da ƙirjinta keta bada wani irin sauti.

Dawowarsa daga Lagos kenan, dama baije don ya kwana ba,  socks ɗin dake ƙafansa ya cire sannan ya zare suit ɗin dake jikinsa, maɓallan long sleve ɗinsa yashiga cirewa,  yana kammalawa ya cire rigar tare da zare white singlet ɗin dake jikinsa, belt ɗin wandon shi ya zare yana me ƙoƙarin zame wandon ƙasa yaji ana knocking ƙofarsa, bai kula ba ya cigaba da cire kayansa, jin still ana knocking ɗinne yasanya shi ɗaukan wani 3 guater jeans ya sanya,  ko gama zuge zip ɗin wandon baiyi ba, ya nufi wajen ƙofar ransa aɓace, ko damuwa da yanda saman maranshi ta bayyana baiyi ba.  Itakuwa  Zieyaderh dake tsaye gaba ɗaya atsorace take, harta gama yanke shawaran cewa zata koma kawai tace da Oummu ƙofar a kulle take.  Da wani irin fushi ya buɗe ƙofar, idanunsu suka faɗa cikin na juna, kallonta yayi from head to toe sai kawai yasaki wata tsuka me sauti tare da komawa cikin ɗakin, ganin haka yasa jikinta ya shiga ƙyarma ba shiri ta bi bayansa, hannunta har rawa yake wajen aje tray ɗin, ƙoƙarin haɗa masa coffee ɗin take ya juyo tare da soma tahowa inda take, cak ta tsaya daga haɗa coffee ɗin da take,  tare da sunkuyar da kanta ƙasa, tabbas kunnuwanta  sautin takunsa suke jiye mata, wanda ke ɗauke da alaman cewa gareta yake zuwa, hakan yasa wani uban tsoro ya lalluɓeta, wanda har ya kaita ga kasa ɗaga kai ta kalleshi.  Taku biyu kacal ya rage atsakaninsu yace.
"Ke!!"

Da sauri ta ɗago kanta aɗan daburce tace "Umm!"  sake matsowa kusa da ita yayi wanda hakan yasa gaba ɗaya takusa ficewa hayyacinta, gab da ita yazo har suna iya jiyo hucin numfashin juna, sosai ta ruɗe sakamakon ganinsa agabanta, baƙaramin cika mata idanu yayi ba, gaba ɗaya ba ta iya ganin komai don yacika mata gaba da faffaɗan chest ɗinshi, haka ta zama wata ƴar cukula agabansa, gaba ɗaya jikinta ɓari yake.. Cikin wani irin husky voice ɗinsa yace. "Ke baki da hankali ko? Haka aka koyar dake  bugun ƙofa?"

Yanzu kam ba iya gangar jikinta bane  ke rawa,  harma da laɓɓan bakinta, cikin daburcewa tayi ƙasa da idanunta don bazata iya kallonsa ba, idanunta ne suka sauƙa akan waist ɗinshi wanda har saman mararsa ta bayyana, kasancewar har yanzu bai ƙarasa jan zip ɗin wandon nasa ba, wasu jijiyoyine kwance akan maran nasa wanda suka mimmiƙe, ga wani irin murɗewa da cikinsa yayi, da sauri ta rumtse idanunta, tana me ƙara ƙanƙame jikinta.  "Badake nake magana ba!!" Yafaɗa atsawace.  Baƙaramin tsorata ta wannan tsawan yayi ba, har batasan lokacin da ta ƙanƙame jikinta sosai ba, bakinta na rawa tace "Dan Allah kayi haƙuri, Allah Bazan sake ba!"

Kallon fuskarta yayi tare da ɗan cizan laɓɓansa, hannayensa ɗaure akan waist ɗinsa yace.
"Buɗe idanunki!"
Kasa buɗe idanunnata tayi saima rawan jiki data ƙara, tare da kullesu ƙam.

"I say open your eyes!!!" Yafaɗa murya akausashe.  Tun kafun ya gama idar da zancen, ta buɗe idanunta tare da sauƙesu akansa. Sarƙewar idanunsu waje guda yasanya idanunta sukayi wani irin juyawa, take suka wani irin lumshewa luuuuu  kamar  zata sume.  Cikin tsawa yace "Wallahi idan kika sumemin saina wanka miki mari stupid girl!!"  ae kuwa tamkar wanda ya watsawa ruwan sanyi saigata ta tsaya cak akan ƙafafunta,  tare da sake maida idanunta ta rufe, saidai ya kasheta amma tabbas bazata iya kallon cikin ƙwayan idanunsa ba, musamman ma ayau, idan

kuwa tace zata sake kallonsa to tabbas  sumewa zatayi koda kuwa kasheta zaiyi bayan ta farfaɗo.

Tsaki yayi tare da nuna mata hanyar ƙofa murya akausashe yace.  "Out!"

Ae kamar jira take haka ta tattari ƙasan riganta aguje ta fice, baki ya buɗe yana mamakin yanda tasa gudu kamar wacce aka turowa dodo.  "Wannan yarinyar anya tana da lafiya kuwa?" Tambayar daya yiwa kansa kenan cike da mamaki, ƙofarsa ya rufe tare da murza mata key, bathroom ya shige tare da sakarwa kansa shower.

Aguje ta haura steps ɗin dake cikin falon, tana kaiwa ɗakinta ta shige tare da rufo ƙafar, kan gado ta faɗa tare da lumshe idanunta, har yanzu jikinta baiwani gama daina ɓari ba,  saida ta ɗauki kusan  8  minute tana maida numfashi, kafun tasamu daman dawowa cikin nutsuwarta. Shiru tayi tare da cusa kanta acikin pillow, yau kam gaba ɗaya brain ɗinta ta cushe, yayinda tunaninta kuwa gaba ɗaya ya gudu.

Ruwan shower ne ke dukan lafiyayyar fatan jikinsa, yayinda hannunsa ɗaya ke dafe da bango, akasalance ya buɗe idanunsa, kasancewar yajima tsaye ruwa na dukansa, hakan yasa idanunnasa suka ɗanyi ja.  So yake ya goge wannan tunanin daga cikin ransa, so yake wannan idanun su fice daga cikin nasa idanun, so yake duk wani abu dake cikin zuciyarsa ya goge, baishirya ɗaukan wannan ƙalubalen ba, bakuma yajin zai shirya har abada,  hannu yasa ahankali ya kashe shower'n, tare da ɗaukan wani nead towel ya ɗaura akan waist ɗinshi. Haka ya fito daga cikin bathroom ɗin jikinsa na ɗigan ruwa,   wani ɗan ƙaramin towel ya ɗauka ya shiga goge jikinsa,  sama sama ya shafa mai ajikinsa, sannan ya sanya long jeans, shida kansa ya haɗa coffee ɗin yasha, jin ana ƙiraye ƙirayen sallan Isha ne yasanyashi miƙewa, wata farar rigar Dolce and Gabbana mai kamar na sanyi ya sanya, kasancewar ana yanayin sanyi hakan yasa ya jawo hulan  dake jikin rigan ya rufe kansa dashi.  Yana fitowa ya haɗu da Almustapha shima masallacin zaije saboda haka atare suka wuce.

Washegari.

Tun seven yagama shiryawa, wayarsa ya ɗauka tare da turawa shugaban makarantar text message, ko 4 minute ba ayiba saiga ƙiran shugaban makarantar ya shigo wayansa.  Fuska yaɗan taɓe sannan ya ɗaga wayar, bayan sun gaisa ne, Principal ɗin yace.
"Naga saƙonka amma banƙi ta taka ba, saidai bakowa muke bawa irin wannan uniform ɗin daka buƙata ba,  mukan bawa ire irenta ne yara da sukayi aure basu kammala school ɗinba, to idan zasu  ci gaba da zuwa shine muke basu, amma tunda haka ka keso babu damuwa"
Ajiyar zuciya ya sauƙe tare da cewa "Nagode, sannan kuma karka manta idan ansamu wani problem ka ƙirani, kamar yanda kaƙirani a wancan time ɗin da aka kaita hospital,  so ba matsala always zaka iya  nemana!"
"Okay dont mention" Principal  din ya faɗa tare da aje wayan.
Shima wayartasa ya aje tare da ɗaukan cover disigner shoe ɗinsa ya shiga sanyawa, iya kyau kam yayi sa, saidai kuma amma fuskar nan ahaɗe take babu alamar fari'a akanta.

Zaune suke su duka uku akan dinning ɗin, sanye take da kayan uniform ɗinta na riga da wando,  ahakali take tsakalan chips ɗin dake gabanta, gaba ɗaya batajin daɗin zama acikinsu don haryau ganinta take amatsayinta na bare. Gaba ɗayansu  ƙamshin turarensa ne ya cika hancinsu.    Cikin ƙasaitarsa yake tahowa hannunsa ɗauke da wata ƴar briefcase me kyau, kujera yaja ya zauna cikin ƙasan maƙoshi yace "Barka da safiya Oummu"    murmushi tayi masa tare da cewa "Barka, hope kunyi waya da commisioner?"
Kansa ya kaɗa mata alamar "Eh"

Mood ɗinta ne yaɗan sauya tare da cigaba da cewa "Ya faɗa maka cewa yarannan da suka harbeka sun faɗi wanda ya turosu ko? gaskiya nikam nashiga fargaba da tsoro,  indai har akan aikinka za a iya turowa akasheka, me kenan kake tunanin zai faru anan gaba? zasu iyayin komai!" ta ƙare maganar fuskarta cike da damuwa.

Kafun Yayi magana Almustapha yace "Nima nayi mamaki ƙwarai da akace wai MR.J.J  ne yaturo ayimaka hakan, wani irin tsananin gabane ke tsakaninka dashi ne wae? Meyake nema dakai ne,  tunfa sanda aka baka BM yakejin haushinka, gaskia yanzu kam baikamata mubarshi ba!"  ya ƙare maganar cikin yanayi naɗan ɓacin rae.

Aje mug ɗin dake hannunsa yayi tare da cewa "Its Okay, anyi arresting ɗinshi  jiya" yana gama faɗan haka ya miƙe tare da  ɗaukan tissue ya goge bakinsa, briefcase ɗinsa ya ɗauka ya fice, duka suka bishi da kallo, hakanan yake shi koda yaushe baiso ayi magana me tsawo dashi, sai kace marar gaskiya.

Ture plate ɗin abincin dake gabanta tayi tare da ɗaukan school bag ɗinta dake gefe ta rataya.

Zieyaderh Oummu taƙira sunanta, "Na'am" ta amsa asanyaye.  "karki manta inkin dawo ki sameni aɗakina kinsan gobene tafiyarmu"  "To" kawai tace sannan ta juya tafice daga cikin falon, tana fitowa compound ɗin gidan shikuma motarsa na fita daga cikin gidan,  mota tashiga ranta duk ba daɗi.
Ko amakaranta yau bata wani sake ba, bayan sundawo break ne aka turo wae principal na ƙiranta, saida gabanta yafaɗi amma haka ta daure taje, wata leda ya bata wanda ke ɗauke da wasu sabbin uniform har kala uku yace mata daga yau su zatana sanyawa. Sosai tayi mamaki amma sai bata nunaba ta amsa kawai ta fice, koda taje aji suka duba kayan, sket ne irin high waist ɗinnan wanda ƙasansa yake da faɗi, sai kuma wata ƴar rigar makaranta fitted da hijab ɗinta wanda idan tasa zai ɗan sauƙo mata kaɗan.   Mamakine ya kashesu su dukansu.  Shukra ce tace "Wannan fa kayan bakowa kesawa a school ɗinnan ba, kodai kinzama house wife ne bamusani ba?"   hararanta Zieyaderh tayi tare da turo baki gaba cikin takaici tace "Ni bawata house wife ɗin dana zama!" dariya suka sanya su dukansu, daga haka sukaci gaba da hiransu, kaɗan kaɗan take sa musu baki.   Har aka tashi sukuku  haka takejin kanta, koda ta koma gida ko falo bata sauƙo ba, haka ta ƙare kwanciyarta aɗaki...  Washegari   Saturday.     Ƙarfe 8 daidai ta kammala shiryawa cikin kayan da Oummu ta bata tace tasanya, riga da sket ne na tsadaddiyar atamfar Vlisco, wacce taji ɗinki, sket ɗin irin pieces ɗinnan ne yayinda rigan takasance fitted, sosai kayan suka amshi jikinta, kasancewar atamfar kalan Maroon gareta

hakan yasanya ta sanya maroon hijab ajikinta, sosai tayi kyau duk da cewa batayi wani kwalliya akan fuskarta ba, flat shoe ɗinta ta sanya tare da kallon kanta amadubi, ita kanta tasan tayiwa kanta kyau. Saida suka biya ta wani super market Oummu tayi sayayya sannan suka ɗauki hanyar zuwa KD inda acan ƙauyen su Zieyaderh yake. Ƙarfe 1 na rana daidai suka iso cikin ƙauyen nasu na Saminaka, tun daga lokacin ƙirjin Zieyaderh ke dukan uku uku, da ƙyar take iyayiwa Kamalu driver kwatance har suka iso ƙofar wahalallen gidansu, tun shigowarsu ƙauyen yara kebinsu yayinda manya kuwa ke bin haɗaɗɗiyar motarsu da kallo. Shawo kwanan Malam Garba kenan hannunsa ɗauke da wani buhu, turus haka yaja ya tsaya yana me bin motar daya gani fake aƙofar gidansa da kallo. Da sauri ya ƙarasa daidai lokacin kuma su dukansu suka fito daga cikin motar, koda zata shekara ɗari ne batanan bazai taɓa kasa gane jininsa ba, bakinsa abuɗe fuska ɗauke ɗa mamaki yake kallon Zieyaderh, itama kallonsa take lokaci guda hawaye suka wanke mata fuska, ji take kamar taje ta rungume Baban nata, amma kuma tanajin tsoro. "Ziyada!" yaƙira sunanta muryarsa na rawa. Kasa amsa masa tayi sai kawai ta fashe da kuka. Shima hawayene kwance acikin idanunsa. Kamar wadda aka wurgo daga sama haka Inna Ma'u tafito daga cikin gidanta, don tuni labari yakai mata cewa wata haɗaɗɗiyar mota fa faka aƙofar gidanta. Bakinta awangale taƙarasa gaban yarinyar da take kallonta kamar Zieyaderh, hannu tasa taɗan taɓa fuskar yarinyar dake kuka, "Laaaaa ha'ila wallahi itace, shegiyar gari kin gama gararanbanki kindawo ko?" Inna Ma'u tafaɗa tana me ƙarewa Zieyaderh kallo, mamaki kuwa aranta kamar zai kasheta. Ƙasa Zieyaderh tayi da kanta, Malam Garba shine wanda ya kama hannunta tare da duban Oummu dake tsaye yace.
"Hajiya kushigo daga ciki!" Babu musu Oummu ta bi bayansa yayinda yake riƙe da hannun Zieyaderh, aikuwa Inna Ma'u ma rufa musu baya tayi bayan ta tsaya ta gama ƙarewa motar da sukazo da ita kallo, harwani yawu ta haɗiya natsananin kwaɗayi dason abun duniya, musamman ma da ta hango ɗan ragowan lemun fanta dake gaban motar.

Gudu gudu sauri sauri haka taje ta ɗauko tabarma ta shumfuɗawa Oummu baki har kunne tace "Hajiyan Birni zauna mana!" Murmushi Oummu tayi tana me kallonta sannan ta zauna aranta tace "Kamar bayanzu tagama zagi ba" Malam Garba da kansa ya kawo musu ruwa, ita dai Zieyaderh laɓewa tayi abayan Oummu, don har cikin ranta tana jin tsoron abun dazai biyo baya.

Gyara zama Oummu tayi tare da ɗagawa baban Zieyaderh gaisuwa, amutumce ya amsa, kafun tasake wata magana Inna Ma'u tayi saurin cewa. "Mutanen Binni Sannu marabanki da zuwa Hajiya!" Still murmushi Oummu tayi tare da jinjina kanta alaman yauwa. Batare da ta bari kowa acikinsu yace wani abuba tace "Lallaima Zieyaderh wato dakika gudu kaina kikeso na aurawa tsoho ɗan dashen? ko kuwa kina tsammanin nida ubanki muna da kuɗin da zamu biyasa abun daya kashe ne, wallahi mudai kin cucemu akan guduwarki saida duk wani ɗan abun dana mallaka ya ƙare saboda ɗan dashe cewa yayi sai mun biyasa kudin daya kashe, kin cuceni kin cuci mahaifinki wallahi!!" Imma Ma'u tafaɗi haka tana me matse wasu munafukan hawayen ƙarya data ƙaƙalosu da ƙyar. Sake cewa tayi "Amma Allah ne zai mana sakayya, koda yake ma ai yanzu nasan kintara kuɗi sosai ko bakomai zan fanshe asarata" tana murmushi ta ƙare maganar. Oummu kam mamaki al'ajabi haɗi da tsoro al'amarin matar ya bata, wato dai ita ko agaban wayene bazata iya ɓoye maitanta ba. Cikin sauri tabuɗi baki zata

sake cewa wani Abu, da sauri Malam Garba yace "Ya isa haka Ma'u, dafari ya kamatane mufara sanin ina taje bawai irin waƴannan kalaman yakamata ayi mata ba" afusace Inna Ma'u tajuya zata faɗa masa baƙar magana sai kuma tatuna da wani abu tafasa. Saita fara yaƙen ƙarya tana me ƙarewa komai dake jikin Zieyaderh kallo.

Murmushin takaici Oummu tayi tare da kai dubanta ga Baban Zieyaderh, sannu ahankali tayi masa bayani akan cewa ɗantane ya tsinci Zieyaderh bawai yawon iskanci ta tafi ba. Ajiyar zuciya me ƙarfi Malam Garba ya sauƙe tare dayiwa Allah godiya daya sanya ƴarsa ta faɗa hannu na gari. Itakuwa Inna Ma'u afakaice take hararan Oummu aranta kuwa cewa tayi "Kuji ƙaryan banza, yo koma gaskiya ne wayasan abunda sukeyi dashi ɗannaki, kai banma yarda ba yanda yarinyarnan tayi ɓul ɓul da ita akwai abun da take aikatawa wata ƙilama cikine da ita" tana gama ƙimtsa zancen zucinta tayiwa Zieyaderh ƙuri, ba inda take kallo kamar cikinta, wai adole saita gano ko cikine da ita, burinta bai wuce taga tumbinnata yaɗan taso ba ta tabbatar da zarginta.

Godiya sosai Malam Garba ya shiga yiwa Oummu na irin riƙon amanar da tayiwa ƴarsa, don har acikin ransa yana me nadamar irin rashin kulawan daya nuna mata abaya, sannan kuma yana ƙaunar ƴarsa sosai, dan itace kaɗai jininsa aduniya, amma yazaiyi da sharri da kuma tsoron Inna Ma'u da yake, duk itace ummul aba'isin faruwar komai. Miƙewa yayi yace zaije ya samo musu fura. Aikuwa yana fita Inna Ma'u tace "Hajiyan birni ince dai ɗannaki daya tsinceta gidanki ya kawota ba gidansa ba?"

Mamakine ya kama Oummu cike da mamakin tambayar tace "Mekike nufi?" da sauri Inna Ma'u ta washe baki tare da cewa "A'a babu abun danake nufi kawai dai tambaya ne, ke Zieyaderh cire lufayan mana kisha iska" Tafaɗa cike da zaƙuwan son ganin yanda cikar halittan Zieyaderh'n ya koma, tayi rantsuwa matuƙar taga cikin Ziryaderh yaɗan tasa to wallahi saita cucesu maƙudan kuɗaɗe. (Chaii guys Inna Ma'u fa ta tsananta😆)

Kallon Oummu Zieyaderh tayi, idanu Oummu ta mata alaman karta cire mayafinta, aikuwa saita yi burus da maganan Inna Ma'u. Wani irin malolon baƙin cikine ya cika zuciyar Inna Ma'u, don sarai ta ga lokacin da Oummu tayiwa Zieyaderh'n idanu. Aranta tace "Wallahi ko zaku mutune saina laƙaba muku wani sharrin dasai kunbani kuɗi ƴan iska"

Babu jimawa Malam Garba ya dawo hannunsa ɗauke da ƙwaryan nono, babu wani ƙyama haka Oummu ta zage tasha nonon daganan tace da Malam Garba idan ba damuwa tanaso tayi magana dashi. "Magana kuma dashi kaɗai?" Inna Ma'u ta tambaya tana zare ido. Babu wanda ya kulata saima iso da Malam Garba yayiwa Oummu zuwa soro tayanda babu wanda zaiji abun da suka tattauna, cike da fahimtan juna Oummu tayi masa bayanin duk wani abu dake tafe da ita, har acikin ransa yayarda da matar da kuma kamalanta saboda haka atake ya amincewa buƙatarta baƙaramin daɗi Oummu taji ba, nan suka tsaida magana cewar zata turo manya don atsaida magana, inda shikuma yace ko babu wasu manya ya yarda da ita ya bawa Ɗanta Almustapha Auren Ƴarsa Zieyaderh, duk lokacin da suka shirya kawai suzo ayi biki.

(uhhhh guys kushiryafa kuna da biki😝)
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ!!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*WATTPAD*
@fatymasardauna
#romance

*This page is dedicated to you my dear @Zeety delight... heart you dear*

*Chapter 37*

Da tsananin farinciki ɗauke akan fuskar ko wannensu Oummu da Malam Garba suka shigo cikin gidan, Inna Ma'u na ganin hakan wani ƙaton baƙinciki ya ɗarsu azuciyarta, hakanan taji ajikinta cewa hanyar ƙaruwa suka tattauna, ae kuwa nan ta ƙudura aranta cewa Oummu na tafiya sai tayi maganin Malam Garba, yadae santa ae yakuma san wacece ita.

Kallon Zieyaderh Oummu tayi fuska ɗauke da murmushi tace "Inaga ya kamata ae ace mutafi tun yanzu, kada tafiyan dare ya kamamu"
Jin abun da Oummu tace yasanya ƙirjinta bugawa, ahankali ta ɗago idanunta tare da ɗan satan kallon mahaifinnata, cikin rashin sa'a tasamu shiɗinma kallonta yake, da sauri tayi ƙasa da kanta, murmushi yayi tare da cewa "Bakomai kuje Zieyaderh Allah Yakiyaye hanya ya tsare, nima inanan zuwa tunda yanzu nasamu adreshin inda kuke."
Wani irin sanyi ne Zieyaderh taji na ratsa zuciarta, sam batayi tunanin mahaifinta zai barta ta koma ba.

"Chab amma kuwa Garba kayi banzan hali, yanzun barinta zakayi ta koma, oh wato kaidai ba ka gaji da jin zagin da mutane ke mana agarinnan ba, karka manta fa duk akan ɓatanta sunanmu ya ɓaci, to babu inda zataje tananan tadawo kenan!" Inna Ma'u ta faɗa amasifance, don sam bata tsammaci haka ba.

"Haba Ma'u meyasa ne bazaki sanja ba, dan Allah Kibar yarinyarnan tayi tafiyarta, tafara karatu acan birni, tsayar mata da karatunta bashida wani amfani" Malam Garba yafaɗi haka cikin ɗan lallashi saboda yasan halin kayansa sarai ba mutumci.

Cike da kumfar baki Inna Ma'u tace "Dole kace haka mana saboda ƴar kace, ai dama ninasan banice na haifeta ba, kuma zaman birni kam wannan algungumar ƴar taka ta gama yinshi....."

Bata gama rufe bakinta ba taji sauƙar wani abu me ɗan nauyi akan cinyarta, idanu ta zaro lokaci guda tare da hadiye maganan dake bakinta, take yanayin fuskarta ya sauya daga ɓacin rai zuwa murmushi. "To Alhamdulillah, irin wanga farare bugun can babban birni, Hajiyan Birni Allah ya ƙara arziki!" Inna Ma'u tafaɗa bakinta har kunne, kuɗine masu yawa Oummu ta aje mata don rufe bakinta, ai kuwa lokaci guda sai ga bakinnata ya rufu . cike da nishaɗi tace.
"To yanzu sai yaushe zaku kuma dawowa?" yanayin yanda tayi maganan tana me ƙoƙarin cusa kuɗin cikin lalitantane yabasu daria amma sai suka gimtse, ɗauke da ɗan murmushi Oummu tace.
"Nan bada jimawa ba Insha Allah, Nangaba kaɗan kema nasan zaki kaimana ziyara!"

"Sosaima kuwa, kice ziyarori ma ba iyaka ziyara kaɗai ba, don fa basau ɗaya zanzo ba!!" Inna Ma'u tafaɗa cikin jin daɗi, dama ita abun duniya shine kanta.

Har wajen mota suka rakasu, bayan motar Oummu ta buɗe wanda ke shaƙe da kaya, Kamalu driver tasanya ya shiga ciro kayan yana kaiwa cikin gidansu Zieyaderh, kayan abincine kala kala da kuma wata leda dake ɗauke da kayan sawa, atamfofi da shadda irin na maza, godiya kam ba irin wanda baban Zieyaderh baiyi mata ba, duk da yanuna mata cewa kayan sunyi yawa, amma saitace masa ba komai, koda ta bashi kuɗi ƙin amsa yayi babu yanda batayi dashi ba amma haka yaƙi amsa, Inna Ma'u kuwa daɗine ya isheta, musamman ma ganin ana shigar da kayan abinci cikin gidanta. Haka su Zieyaderh suka baro cikin ƙauyen zuciarta cike da kewan babanta. Har bacci tayi a hanya kafun su iso, gaba ɗaya zaman mota ba daɗi ji take duk jikinta yayi mata wani iri.

Suna isa gida kowa ɗakinsa ya wuce, don gaba ɗayansu agajiye suke, da ruwan zafi tayi wanka kana tabi lafiyar gado.

Sunday.
Yawanci duk ranan weekend atare suke cin abinci akan dinning, tun 8 tatashi tayi wanka, riga da sket na 1million stones tasanya wanda suka amshi jikinta sosai, tayi kyau. Wani ɗan madaidaicin mayafi ta sanya ta rufe jikinta, a kitchine ta samu Oummu cike da ladabi ta gaida ta, fuska ɗauke da fari'a Oummu ta amsa mata, yauma kamar koda yaushe itace ta shirya gaba ɗaya abincin akan dinning. Ƙamshin turaren Almustapha daya shiga hancinta shi yasanyata ɗago da kai ta ɗan kalleshi, ƙasa tayi da kanta tare da gaidashi, amsa mata yayi yana me jan kujera ya zauna, sosai yau ɗin tayi masa kyau acikin shigarta, duk da cewa bai taɓa ganin kwalliya akan fuskarta ba amma gaskiya tana da kyau sosai.

Oummu da Almustapha ne suke taɓa hira kaɗan kaɗan yayinda ita kuma take serving ɗinsu, tunaninsa ne kwance aƙasan zuciyartaz hakanan taji wani iri da bataga ya fito ba, tunaninta ne ya katse sakamakon wani daddaɗan sanyin da taji yana ratsa jikinta, gefe guda kuma ni'imtaccen ƙamshinsa dake zautar da'ita ne yashiga cakuɗa da numfashinta.
Sanye yake da blue crazy jeans and Blue t-shirt mai kyau da tsada ƙiran company'n D&G, sosai yayi kyau kwarjininsa yasake bayyana, yayinda gashin kansa kuwa sai shinning yake, kujera yaja ya zauna, dakansa yayi serving kansa, wajen haɗa tea, ahankali yake sipping tea

ɗin yayinda kansa ke ƙasa, yau babu waya ahannunsa amma duk da haka yi yake kamar hankalinsa baya garesu, gaba ɗaya wajen ya ɗauki shiru, kowa abincinsa yakeci yayinda akabar mutane biyu daga cikinsu da saƙar zancen zuci, gaba ɗaya hankalinta yana garesa, so take ta ɗago idanunta ta kallesa amma fargaba ya hanata.
Tissue Oummu ta ɗauka ta goge bakinta tare da dubansu su dukansu, cikin nutsuwa tace "Ina da buƙatar hankulanku agareni dukanku!" Almustapha ne ya fara aje cokalin dake hannunsa tare da duban Oummu, itama Zieyaderh ɗago kanta tayi ahankali tana me kallon Oummu'n, shikam ko motsawa baiyiba, kana bai kuma daina shan tea ɗinsa ba.

Gyara zama Oummu tayi tare da cewa.
"Sooraj da Almustapha inaso nayi maganannan ne agabanku saboda ko ba komai kamar yayye kuke awajenta, sannan awajenta zataji maganar amatsayin sabuwace, saɓanin ku da kuka taɓa jinta" ɗan numfasawa tayi kana tace..
"Zieyaderh!"

Tun kafun ta kammala maganganun nata ƙirjin zieyaderh ke bugawa, asanyaye tace. "Na'am!"

Tashi Oummu tayi daga inda take zaune, tare da jawo wata kujera ta zauna gab da Zieyaderh'n, hannayen Zieyaderh Oummu ta kamo cike da son gamsar da ita tace.
"Haƙiƙa kowacce uwa tanaso ɗanta ko ƴarta su samu abokan zama na gari, burin kowacce uwa adunia shine ƴarta mace ta dace da mijin aure, haka ma kuma ɗanta namiji ya dace da macen aure, tamkar ƴa haka na ɗaukeki Zieyaderh, bazan taɓa son wani abu dazai cutar dake ba, bazan miki dole ba, saboda kema kina da ra'ayi kamar kowa, halayyanki da kuma irin nutsuwarki yasanya naji ina kwaɗayin da ki ƙara zama acikin zuri'ata, duk da cewa munatare dake ayanzu, amma anan gaba ba lallaine mukasance tare ba, dole watarana aure zai ɗaukeki ya nesantaki damu, bazanyi baƙinciki ba idan kika samu adalin miji daga wani waje na daban, amma zanfi so ace daga cikin zuri'ata kika samu wannan adalin mijin, ba daga wani waje daban ba, kamar yanda nace bazan miki dole ba, ba kuma umarni nake baki ba, saidai ganin ya cancanta yasanya ni yin tunanin haɗaki aure da ɗana Almustapha!"

Dummmmmm tamkar ankwaɗa mata katuwar guduma akan ƙirjinta haka taji, yayinda agefe guda kuwa taji sauƙan kalaman Oummu acikin kunnuwanta tamkar almara, wani irin abune taji ya sarƙemata maƙoshi, take tasoma tari har saida manya manyan idanunta suka rikiɗe daga farare zuwa jajaye, da sauri Oummu ta ɗauko ruwa ta bata, cikin ikon Allah tanasha tarin ya ɗan lafa, jingina bayanta tayi da jikin kujera tare dayin ƙasa da kanta, me Oummu ke faɗane? Kodai kunnuwanta ne basuji mata da kyau ba? Aure kuma da Almustapha? Waƴannan tambayoyin sune cike aranta, ganin komai take kamar ba da gaske ba. Dafa shoulder ɗinta Oummu tayi cike da kulawa tace "Karki taɓa cutar da kanki Zieyaderh, idan har kinaga hakan zai sa ki cutu to karki ɓoye ki sanardani, bazan taɓa miki dole ba, nayi hakanne kuma badon na cutar dake ba saidon ina kwaɗayin ganinki cikin zuri'ata, duk da nasan cewa banice na haifi Almustapha ba, amma inayi masa son da nake yiwa ɗana SOORAJ, kuma ina masa kwaɗayin zamowarki mata a garesa!!"

Hawayene suka cika idanun Zieyaderh, har takai ga sun soma sauƙa akan hannunta, wani irin bugawa zuciyarta keyi,  ita kanta batasan awani irin hali take ciki ayanzun ba, gaba ɗaya kalaman Oummu sunzama tamkar wani sinadari na bayyanar da raunin zuciyarta.

Ganin hawaye na ɗiga daga idanun Zieyaderh yasa Oummu cewa.
"Ya isa daina kukan, idan kingama cin abincin kije ki kwanta, komai ya wuce nafahimci halin dakike ciki!" tana gama faɗan haka ta miƙe tare da soma ƙoƙarin barin wajen.  Da sauri Zieyaderh ta riƙo hannun Oummu, cak Oummu ta tsaya tare da juyowa,   ɗago  manya manyan idanunta tayi bakinta na rawa tace.
"Kiyi haƙuri Oummu ba ina kukane saboda banason abunda kikazomin dashi ba,  nayarda ke uwace agareni, saboda haka NA AMINCE!" taƙare maganar ƙirjinta na mata wani irin suka, yayinda gaba ɗaya gabɓan jikinta sukayi weak, so take tafashe da kuka me sauti, so take ta kalli koda ɓangaren da yake ne kozataji sanyi, so take yace wani abu,  to amma metakeso yace ɗin, itama kanta batasani ba.
Cike da farinciki Oummu tashafa kanta cikin ƙaunar biyayya irin nata tace.
"Nagode sosai Zieyaderh nakuma ji daɗi da baki watsamin ƙasa a idona ba, haƙiƙa ke yarinyar kirkice, Insha Allahu Kuma zakiyi alfahari da wannan haɗin, kije ɗaki ki huta kinji!" Oummu ta ƙare maganar cike da lallashi. Babu musu kamar wacce ƙwai ya fashewa ajiki haka ta tashi daga zaunen da take, har yanzun bazata iya ɗaga idanunta ta kalli ko wanne daga cikinsu ba, cikin ƙwallan da suka sake cika idanunta ta haura sama daɗan sauri burinta taje tayi kuka kozataji sauƙi aranta.

Tunda suka fara maganar har kawo iyanzu bai koda ɗago kansa ya kallesu ba,  sannan baidaina abun daya keyi ba, da kaɗan kaɗan yake sipping tea ɗin da tsabar zafi har tiriri yake, hayaƙin dake fita acikin kofin tea ɗin shine ya sanya gaba ɗaya fuskarsa ta ɗanyi zufa, sam baijin wannan zafin shayin akan harshensa hasalima tamkar wanda yakeshan ruwan randa haka yaji test ɗin shayin ya sauya a bakinsa.

Kallon Oummu dake tsaye tana murmushi  Almustapha yayi jikinsa asanyaye yace
"Oummu kinaga kamar ba matsala kuwa?"   Still murmushi Oummu tayi tare da dafa shoulder ɗinsa cikin kulawa tace.
"Babu wata matsala Almustapha ka kwantar da hankalinka, kaidai ka shirya bikinka yakusa zuwa Insha Allah"  Tana gama  faɗan haka ta wuce zuwa ɗakinta.
Murmushi Almustapha yayi tare da sanya hannu ya dafa saitin zuciyarsa, har acikin ransa yaji wani irin farinciki,  da sauri yatashi ya nufi ɗakinsa sam yama manta da Sooraj dake zaune agefensa.

Shikaɗai ya rage zaune akan dinning ɗin, ahankali ya aje cup ɗin dake hannunsa, tare da ɗaukan tissue ya goge bakinsa,  miƙewa tsaye yayi kai tsaye ya wuce ɗakinsa,  yana shiga ya soma rage kayan jikinsa, baijin zai samu relief idan ba shower ya sakarwa kansa ba, bathroom ya shiga tare da kunna shower, tsayawa yayi saitin shower ɗin ruwa na dukan kai da jikinsa, ahankali yake fidda wani numfashi me zafi.

Tana rufe ƙofar ɗakinnata da gudu ta faɗa kan gado, kanta ta cusa acikin pillow tare da sakin kuka me sauti.  Sosai tayi kuka wanda ita kanta batasan na menene ba, batasan metakeji acikin zuciyarta ba, saidai tabbas tasan tanajin wani irin yanayi na babu daɗi,  ya zatayi idan bata amincewa Oummu ba, ko ba komai su ɗin sunkasance mutane masu tsananin karamci agareta,  idan har bata amince da maganan Oummu ba menene sunanta? BUTULU? tabbas Oummu tabata kulawa, sannan duk da batasan wacece itaba ta zauna da ita bata ƙyamaceta ba, shin saɓamata daidai ne? koma badon Oummu ba kodanshi ya cancanci tayiwa mahaifiyarsa biyayya, koba komai shiɗin wani ne na musamman awajenta, idan taƙi aminta da maganan mahaifiyarsa tabbas tasan bazaiji daɗi ba, amma kuma meyasa takejin wani abu dangane dashi? meyasa baice wani abuba alokacin?   "Mekikeso yace?" wata zuciar ta tambayeta, shiru tayi da kukan da take tare da soma sauƙe ajiyan zucia akai akai.

Kusan 30 minutes ya ɗauka ruwa na dukan jikinsa, da ƙyar ya iya kashe shower'n tare da ficewa daga cikin bathroom ɗin,  sauya shigarsa yayi zuwa wani white yard  wanda yaji ɗinkin half jumper da wando, sosai kayan sukayi masa kyau,  saidai rashin walwalan dake kan fuskarsa na yau ya zarce na kullum, ɗan makullin motarsa ya ɗauka tare da wayarsa kana yafice daga cikin ɗakin.
Tuƙa motar yake amma batare dayasan ina ya nufa ba,  ganin ya soma gajiyawa ne yasanyashi gangarawa gefen titi yayi parking ɗin motar, ahankali ya kifa kansa akan steering motar, shikansa baisan mene dalilinsa na tsayuwa awajen ba, baisan dalilin daya sanya yakejin kansa acikin wani irin bad mood ba,  mekenan? me hakan yake nufi? hakanan yaji kansa acikin damuwa, to amma abun tambayar shine damuwar tasa na menene? shikansa baisan akan mene yake damuwan ba,  dalilinsa na sanya kansa cikin damuwa yayi ƙaranci,   tabbas yanaji ajikinsa cewa idan har ya bari tunanin dake ƙwaƙwalwarsa yasamu mafaka acikin ƙirjinsa to tabbas zuciyarsa zata buga.
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*WATTPAD*
@fatymasardauna
#romance

*Chapter 38*

Ɗago kansa yayi daga jikin steering motar tare da sakin wani murmushi mai ɗauke da tarin ma'anoni,  agogon dake ɗaure a tsintsiyar hannunsa ya duba, ƙarfe 11 dae dae,  ɗan ƙaramin tsuka yayi tare da tada motar ya cillata kan titi.

Zieyaderh kuwa tana gama koke kokenta baccine ɓarawo ya saceta wanda sai yanzun ta tashi, ji tayi yanayinta ya sauya tamkar wata marar lafiya, bathroom tashiga tayo wanka, tare da dawowa ta zauna akan gado, tv ta ƙurawa ido amma azahirin gaskiya hankali da tunaninta ba ga tv'n yake ba, tunaninsa ya matsanta mata, lallai tana da buƙatar me fayayyace mata halin da take ciki, Shukra, itace wacce ta fara faɗo mata arai, tabbas tasan idan tasamu Shukra to zata fayyace mata komai, to amma idan Shukra ta bata amsar da zai hautsuna tunaninta fa? ajiyar zuciya ta sauke tare da soma ƙoƙarin shanye hawayen dake cikin idanunta, sam yau haka taji zaman gidan ya isheta, komai jinsa take ba daɗi.

Wuse zone 4

SOORAJ, zaune yake akan wata kujera dake kusa da haɗaɗɗen dinning table ɗin dake cikin falon, cup ɗin coffee ne agefensa yayinda yake signing ɗin wasu papers dake gabansa, Mas'oud ne ke zaune akan kujeran dake facing nasa, wayar dake hannunsa ya ajiye tare da kai dubansa ga Sooraj, cikin yanayi na ɗan damuwa yaƙira sunansa.

Batare daya tsaida aikin da yakeyi ba, batare kuma daya ɗago ba yace "Ummm"

Gyara zama Mas'oud yayi tare da cewa "Oummu tayimin magana akan auren Almustapha da Zieyaderh, sannan tace dani gobe Abba zaizo nakuma ce mata zan sameshi muyi magana, gaskiya RAJ nayanke shawaran zan sanar da Abba komai adangane da rashin lafiyanka!"

Aje pen ɗin hannunsa yayi tare da ɗago kansa ya dubi Mas'oud.

"Faɗa masa matsalata bashida wani amfani Mas'oud, kabari kawai badai aure suke so nayi ba, nashirya zanyi" Yafaɗi haka cikin halin ko inkula.

"Yin aurenka bashine mafita ba Sooraj samun lafiyanka shine abunso, ya zakayi da matar idan har baka samu lafiya ba?" Mas'oud ya tambaya cike da tsananin tausayinsa.

Murmushin gefen baki Sooraj yayi tare da ɗan cizan lips ɗinsa, adai dai wannan lokacin shikaɗai yasan me yakeji.

Ɗan numfasawa Mas'oud yayi tare da cewa "Amma RAJ auren Zieyaderh da Amustapha abun na damuna sosae!"

"Why?" Sooraj ya tambaya ataƙaice.

"Sooraj" Mas'oud yaƙira sunansa. Ɗago kai yayi ya kalli Mas'oud ɗin batare daya amsa ba, shima Mas'oud din kallonsa yake, tabbas shikam akwai abun daya jima yana hangowa acikin idanun SOORAJ, amma baitabbatar da abunba sai ayanzu, wani tarin tausayin Sooraj ɗinne yasake kamasa, haƙiƙa Sooraj baisan komaiba agame da so, shi mutum ne wanda yake

rayuwarsa shi kaɗai, baya sharing damuwarsa da kowa,  saboda haka ba lallai ya fuskanci cewa wani abu na damunshi ba, koda ma yafahimci hakan ba lallaine yasan menene abun ba. Kawar dakae gefe Sooraj yayi tare da miƙewa tsaye key ɗin motarsa ya ɗauka tare da cewa "Nagama signing papers ɗinnan, ka kula sai munyi waya!"

Kasa ce dashi wani abu Mas'oud yayi harya fice,  shikam Allah Yasani tausayin SOORAJ yake, tabbas yau ya hango damuwa me tarin yawa a cikin idanun SOORAJ.

Monday

Tun kafun 7 yau tagama shiryawanta, bata da wani buri wanda ya wuce taje ta sanar da Shukra damuwanta kozata ji sauƙi acikin zuciyarta, duk yanda Oummu taso ta tsaya tayi break ƙi tayi haka ta tafi makarantar da yunwa acikinta.

Shiru Shukra tayi tare da ɗan nazantar maganganun da suka fito daga bakin Zieyaderh.. "Bansan ya zanyi ba Shukra, bansan me yasa nakejin haka dangane dashi ba" Zieyaderh tafaɗa cikin yanayi na damuwa.

Murmushi Shukra tayi tare da dafa shoulder ɗinta,  gyara zama tayi tare da cewa "Zaki iya yarda da cewa kin kamu da son sa?"
Idanu Zieyaderh ta zaro waje tare da dafe ƙirjinta dake bugawa, cikin yanayi na tsoro tace "SO fa kikace Shukra?"

"Eh SO, karki yarda ki ƙaryata zuciyarki akan alamomin so da take gwada miki, tabbas Son shi kike Zieyaderh, don so ne kaɗai ke kawo waƴannan alamomin, idan ba so ba, me zae sanya dan kinganshi gabanki yana faɗuwa? me zaisa tunaninsa ya samu mafaka azuciyarki ba dare ba rana? Idan baso ba me zai sanya tsananin tausayinsa wanzuwa acikin ranki? Wannan duk alamomin SO ne Zieyaderh, hmmm bana faɗa miki SO ya wuce duk wani tunaninki yana zuwa da alamomi masu yawa, haƙiƙa sonda kike masa irin sane wanda yake sanya ciwo azuciya, kiyarda kawai sonshi yana daga cikin ƘADDARA'nki!"

Shiru Zieyaderh tayi tare da rumtse idanunta, tabbas bazata iya ƙaryata Shukra ba, domin itama zuciyarta ta gamsu da hakan... "Menene amfanin wannan son? menene amfanin son wanda baisan kanayi ba, meyasa zuciyata tayi mini haka, tabbas idan nasoshi na so kaina dayawa saboda ba ajina bane!" Zieyaderh ta faɗa murya araunane.

"So baruwanshi da aji ko rashinsa Zieyaderh, kiyi fata wata ƙila shima ya soki!" Shukra tafaɗa cikin son ƙarfafa mata guiwa.

"Soyayyata bata da amfani Shukra, saboda ɗan uwansa zan aura, wani riba zan samu idan naci gaba da sonsa Shukra?" hawaye har sun cika idanunta.

Ajiyar zuciya Shukra tayi tare da  cewa "Kicire sonsa azuciyarki Zieyaderh, haka shine samun

sauƙin kai da zuciyarki"

Hawayen dake cikin idanunta ne suka gangaro ahankali tasa hannu tashare,    "Nayarda inasonka, amma zan barwa zuciyata ita kaɗai, zan jure duk wani zafi da ƙunci, idan har soyayyarka zata zauna azuciata bazata fice ba, ko ba komai watarana ita zata tausheni" maganan da takeyi acikin zuciyarta kenan...   Haka taƙare gaba ɗaya wunin ranan cikin damuwa, sam walwalanta ya ragu babu wani jin daɗi atattare da ita. Koda aka tashi amakaranta data koma gida aɗaki ta zauna, ko abinci bata fito taci ba, damuwar SOYAYYARSA ne kwance aƙasan ranta.

Tun ɗazu yaketa juyi akan makeken gadonsa, shikansa baisan tunanin me yake ba, yasan ƙaddara tana iya sauyawa ako da yaushe amma baya fatan tasa ƙaddaran ta sake sauyawa, saboda zai iya jure komai amma banda sabon baƙon yanayin dayake samun kansa aciki kwana biyun nan,  yasani shi mai rauni ne ako da yaushe... Kansa ya cusa acikin pillow tare da sakin wani numfashi me zafi,  baitaɓajin ciwon ƙaddaransa ba sai ayanzu, yanaji ajikinsa cewa zuciyarsa nason wani abu, to amma metakeso? shine abun daya kasa sani, sau da dama yakanjinta awani ɓangare ne na zuciyarsa, amma asannu sannu sai yakejin gaba ɗaya ta mamaye zuciyarsa, kowani bugun numfashin da zaiyi da fargaba yake tafiya,  ada baisan wani damuwa da zafin zuciya ba, amma asannu yanzu duk ta dalilinta yasansu,   yana da buƙatar sanin me hakan yake nufi, baisan mezai kira abun ba, amma wani lokaci yakanji dama ace bai santa ba kwata kwata, yakanji inama da ace baizama silan taimakonta ba wataƙila da bata shigo rayuwarsa ba, akullum ji yake kamar an rubuta wani abu daya shafeta acikin ƙirjinsa, saidai babu wanda zai sanar dashi me hakan ke nufi.  Idanunsa da suka kaɗa sukai ja ya ware tare da ɗaukan wayansa ya turawa peter saƙo, akan yayi masa booking flight,    kallon agogo yayi yaga ƙarfe 7 na dare, ahankali ya sauƙo daga kan gadon tare da ƙarasawa gaban drawer ɗinsa, wata black trolly ya jawo tare da buɗe sip yashiga ɗebo kayansa yana zubawa acikin trolly'n, yagama sawa aransa cewa acikin waƴannan satuttukan bazaiyi zaman Nigeria ba....
***
Dariya sosai Yasmeen keyi wanda hakan ya matuƙar harzuƙa Aneesa, cikin yanayin fushi tace "Wallahi indai ina da rai bazan taɓa barin SOORAJ ba dole sai na koyardashi yanda zaiyi ya zama namijin gaske!"

Gimtse dariyan da takeyi Yasmeen tayi tare da cewa "Bakida hankali Aneesa, ko kin manta nice wadda nafara son SOORAJ acikin zuciyata?  Ke Sha'awar SOORAJ kawai kikeyi Aneesa nikuma ba iya sha'awaba sonsa nakeyi, bandamu ba don kince shiba Namiji bane, ni indai zanna ganinsa akusa dani akullum zan iya jurewa, please Aneesa kibarmin SOORAJ dan Allah Ina burin kasancewa dashi"

Tsuka Aneesa tayi tare da cewa "Duk da cewa shiɗin bashida amfani amma duk da haka inajin sha'awarsa, aranannan naso ace dagaske fyaɗe zaimin, tabbas nasan danaji daɗin da wata mace bata taɓajiba, don hakan ni awajena bazai zamanto fyaɗe ba, hmmm amma haka guy ɗinnan yatafi yabarni da yagaggen riga ko breast ɗina bai iya taɓawa ba!!" Aneesa taƙare maganar cikin yanayi na ƙufula.

Dariya Yasmeen tasakeyi tare da cewa "Bazan hanaki ba Aneesa, amma inaso ki sani bazan janye daga son SOORAJ danake ba saidai mu duka biyun Allah Yabawa me rabo sa'a"
***
Kasancewar Yau Abba zaidawo hakan yasa Oummu tun safe take ta shirye shiryen dawowarsa, tsaye take a kitchine tana ƙoƙarin harhaɗa abincin da tayi akan tray... Almustapha ne yashigo cikin kitchine din fuskarsa ɗauke da ɗan damuwa. Kallonsa Oummu tayi cike da mamakin ganin yanayinsa tace "Almustapha lapia kake kuwa?"

Murmushi yayi tare da cewa.
"Tsoro nakeji Oummu"

Shaye da mamaki Oummu tace "tsoron me?"
Ƙasa yayi da murya tare da cewa "Tsoron abun da muka shirya, nayi wani tunani, yakamata mugayawa RAJ gaskiya Oummu kinsan zuciyarsa, kar azo ayi abunnan kuma yace bayaso, sannan karkuma bayan anyi yazo yace zaiga laifina"

Murmushi Oummu tayi tare da cewa "Karka damu Almustapha, naɓoye hakanne bawai don wani abuba saidon inason wannan auren yafi waƴancan auren nasa ƙarko, jikina yajima da bani cewa awannan karon SOORAJ bazai saki matar da zan aura masa ba, kayi haƙuri Almustapha mucigaba da gudanar da shirinmu ayanda muka tsara!"

Murmushi Almustapha yayi tare da ɗaukan yankakken apple yakai bakinsa cikin yanayi na jin daɗi yace "Amma gaskiya Oummu kada asa lokacin bikinnan da yawa, don kinsan bazan iya jurewa ba watarana kada nayi abun dazai sanyashi gane plan ɗinmu!"

"Karka damu banajin bikinnan zai wuce 3 weeks saboda nima akwai abun danake hangowa, saidai kuma ita yarinyar ce bansan yazataji ba idan taji haƙiƙanin wanda ta aura."
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ!!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*WATTPAD*
@fatymasardauna
#romance

*Chapter 39*

Amatuƙar gajiye ta dawo daga makaranta, gaba ɗaya ƙafafunta ciwo suke, kasancewar yau ɗin kusan awa guda suka ɗauka tsaye acikin Lab, tana shiga cikin ɗaki tasoma rage kayan jikinta, wani white towel ta ɗaura aƙirjinta wanda ya kawo har kan santala santalan cinyoyinta, bathroom ta wuce kai tsaye, wanka tayi tare da ɗauro alwala. Wata pencil tightly skin gown tasanya wanda bayanta taƙasa yake aɗan tsage, sosai rigan tabi haɗaɗɗiyar surar jikinta ta lafe, wani ɗan madaidaicin hijab ta sanya ajikinta, kai tsaye tanufi ɗakin Oummu, tana knocking door ɗin, Oummu ta bata izinin shigowa, Zaune tasameta akan wata luntsumemiyar kujera dake cikin ɗakin, gabanta wasu takardune yayinda hannunta ke ɗauke da pen. Da murmushi akan fuskarta ta amsawa Zieyaderh gaisuwan da tayi mata, tare da ɗan zare farin glass ɗin dake sanye a idonta tana me cewa "Ya school ɗin?" "Alhamdulillah!" Zieyaderh ta amsa aɗan sanyaye, ƙatuwar leda wanda ke ɗauke da tambarin sunan wani super market Oummu ta miƙo mata tare da cewa. "Ungo amshi Kayan da kuka saya da Almustapha ne, ashe wai ke ya sayawa sai kimasa godiya"

Asanyaye takarɓi ledan dake shaƙe da kaya, cikin sanyin daya sake zama sabo agareta tace "Oummu kitayani godiya, nagode sosai!"
Murmushi Oummu tayi irin tasu ta manya tare da cewa "Ae kinfi kusa dashi ayanzu zai kyautu kiyi masa godiyan da kanki!"

Murmushi kawai tayi cike da kunya ta sadda kanta ƙasa tare da miƙewa tsaye, da ƙyar ta iya jan ledan don tana da nauyi, haka tafita daga cikin ɗakin tanajin wani iri acikin zuciyarta. Tana shiga ɗakinta ta Zazzage ledan akan gado, tabbas sayayyan da sukayi ita dashi ne, sam bata wani ji farinciki ba, juyawa tayi ta fice aɗakin don samawa kanta abun da zata ci, batajin cin wani abu hakan yasa ta tsiyayo fresh milk me sanyi, kanta aƙasa take haura step ɗin da zai sadata da samannasu, sam bata kula da cewa shima yana zuwa ba, haɗuwarsu waje ɗaya ne yasanya gaba ɗaya fresh milk ɗin ya zube masa ajiki, cikin tsautsayi cup ɗin ya faɗi ya tarwatse a wajen. Aɗan razane ta ɗago kanta ta kalleshi, daidai lokacin shima ya ɗago kyawawan idanunsa, idanunsune suka sauƙa acikin na juna, da sauri tayi baya kasancewar sunyi matuƙar kusa da juna, bisa tsautsayi ta aje ƙafanta akan fasassun glass, wani irin ƙara ta sake tare da rumtse idanunta ƙam, beautyful eyes ɗinsa yaɗan zaro waje tare da kallon ƙasa inda ƙafanta tuni har ya soma fidda jini. Karan da tayi shiya janyo hankalin Oummu, da sauri ta fito tare da ƙarasowa inda suke, cikin yanayi na damuwa tace
"Subahanallahi me ya faru?" cikin tsananin zafin dake ratsa har ƙwaƙwalwarta, ta buɗe idanunta da suka tara ruwan hawaye kana sukai ja, yunƙurin ɗaga ƙafanta ta somayi, amma zafin da takeji ya hanata, hakan yasa ta saki wani ɗan siririn ƙaran wahala, small pink lips ɗinsa ya ɗan ciza tare da raɓawa ta gefenta zai wuce. "SOORAJ me kayi mata ne?" cewar Oummu tana me ƙoƙarin kama ƙafan Zieyaderh don ta duba, fuska ɗauke da ɗan mamaki yasake ɗan waro Idanunsa alaman ni kuma mezan mata, kana ya taɓe lips ɗinsa.
"Subahanallah tayaya haka ta faru? Glass fa ta taka" Oummu tafaɗa tana me riƙe da ƙafan Zieyaderh, wanda har yanzu yake fidda jini, ƙarasowan Almustapha cikin falon kenan ya taraddasu atsaitsaye, da sauri ya ƙaraso garesu yana me cewa "Lafiya kuwa Oummu me ya faru?"

"Fasashshen glass ta taka, please zoka riƙemin ita naɗauko first aid box sai kayi mata treatment!" Oummu ta faɗa cike da tausayin halin da  Zieyaderh ke ciki.
Babu musu Almustapha ya haura kan step ɗin tare da sanya hannayensa duka biyu ya kama kafaɗun Zieyaderh, wanda hakan yasa harta ɗan kwanto cikin jikinsa.  Sauƙe hannayensa akan kafaɗunta, yayi daidai da bugawar zuciyarsa, da sauri ya rumtse idanunsa tare da dunƙule hannuwansa, lokaci ɗaya yaji wani irin jiri na neman kadashi, aɗan hanzarce ya juya cikin azama yabar falon.
Da taimakon Almustapha ta iya ɗingisawa zuwa kan kujera, sosai takejin zafi domin kuwa glasses ɗin sun ɗan caketa sosai,  Oummu ne ta dawo hannunta ɗauke da first aid box,  zama Almustapha yayi akan sofa tare da ɗaukan ƙafannata ya ɗaura akan wani ɗan madaidaicin stull,  da cotton yayi using wajen goge mata jinin da ya ɓata ƙafannta, hannunsa yasa ya kama ƙafan, cike da kulawa ya shiga dubawa ko akwai wata ɓoyayyar kwalba dake a
cikin ƙafar, ganin babu yasanyashi ɗaukan hydrogen  ya haɗa da auduga ahankali yake ɗan goga mata akan ciwon, kuka tasanya me sauti tare da rumtse idanunta, sosai takejin zafin hydrogen ɗin,  murmushi Almustapha yayi ganin yanda take kuka tana me cije baki,   cike da salon tsokana yace.
"Haba Bae da zafi ne?"

Tsaida kukannata tayi tare da buɗe jajayen idanunta, samun kanta tayi da murguɗa masa baki tare da yunƙurin zame ƙafarta daga hannunsa,  murmushin daya bayyana white teeth ɗinsa yayi tare da cewa "Am sorry ai nama gama!" Kallon Oummu tayi tare da ɗan marairaice fuska, Murmushi Oummu dake tsaye tana kallonsu tun ɗazu tayi, aranta kuwa cewa tayi  "Anya abun danayi kyautawa ne?"      "Idan baizama kyautawa ba to tabbas za a ƙirasa da son kai!" Wata zuciyarta ta bata amsa. Ajiyar zuciya ta sauƙe tare da cewa. "Allah shine shaidana nayi hakane don samun nutsuwa da salama azuciyar su dukan biyun, idan hakan bai yiwu ba kuwa to tabbas ko mai ya faru NI CE SANADI, sannan hakan zai zama kamar rashin adalci ne ga rayuwar ZIEYADERH!"    maganan da Almustapha ke matane ya sanyata dawowa daga tunanin da take, inda yake cewa
"Yakamata taje ta huta, daga nan zuwa da safe karta taka ƙafan muga idan babu wani matsala shikenan,  idan kuma mukaga ƙafar ta kumbura  sai muje hospital!" Ya ƙare maganar yana me ƙoƙarin rufe first aid box ɗin dake gabansa.

Da taimakon Oummu Zieyaderh ta iya ɗingisawa zuwa ɗaki,   adaddafe ta iya yin alwalan sallan magriba saboda zafi da ƙafan ke mata,  haka ta samu tayi sallah nanma saida dabara don dazaran ta shumfuɗe tafin ƙafanta aƙasa tofa zafi zai ratsa gangar jikinta.

Yana barin falon haka yaji zuciyarsa nayi masa wani iri, yanajin yanayinsa duk ba daɗi,  peter dake ta zaman jiransa tun ɗazu a waje yana ganinsa yataso da hanzari tare da buɗe masa murfin motar,  shiga cikin motar yayi ransa duk ajagule,   kallon agogonsa yayi yaga  5:50 am. Tsuka yaja tare da lumshe idanunsa da suka ɗan nuna alamun ɓacin rai acikinsu, 6 daidai jirginsu zai tashi amma gashi har yananeman yin late akan wannan stupid girl ɗin,  wani siririn tsuka yaja akaro na biyu, shikam ya lura kamar yanda take mashiririciya haka komanta ma yake, yayi imani haukane kaɗai yake wanzar da irin tsoron da yake ganinta aciki da zaran ta

ganshi.  Hakanan yakejinsa cikin ƙuncin rai, suna isowa airport ya buɗe murfin motar agurguje, da sauri peter ya miƙo masa wata ƴar black trolly wanda abubuwan amfaninsa ne ke ɗauke aciki. Amsa yayi kana yashiga can cikin airport ɗin, saida ya kammala komai kafun yataho agurguje ya shiga cikin jirgi don 5 minute kacal ya rage flight ɗin ya tashi.    Yana zama akan kujera ya sauƙe wani irin ajiyar zuciya tare da jingina bayansa da jikin kujeran,  sit belt ya ɗaura kana ya lumshe gajiyayyun idanunsa, kamar yanda jirginsu ya tashi zuwa sararin samaniya haka arai da zuciyarsa yake fatan ace damuwarsa tayi ƙaura daga gareshi,  awannan tafiyan yanason samawa zuciyarsa nutsuwa sosai,    musamman akan sabon cutar da  ta ɗauko mai wanda yakasa sanin gabansa balle bayansa.

Kwance take luf  akan gado yayinda  ta baza gaba ɗaya gashin kanta akan pillow,  duk da cewa anɗau wasu mintuna dajin ciwon nata amma har yanzu tanajin zafi, wannan zafin da takeji ajikinta shine zafin daya tafi har zuwa cikin zuciyarta, ko wani bugu ɗaya na zuciyarta yakan zo matane da wani sabon sauyin yanayi, akowanni daƙiƙa ji take soyayyarsa na hauhawa acikin zuciyarta,  sake gyara kwanciyarta tayi tare da lumshe idanunta.

SINGAPORE

Adaidai wannan lokacin shima ya gyara kwanciyarsa tare da lumshe kyawawan idanunsa,  ako wani bugun zuciyarsa ɗaya yana tafiyane da sauye sauyen tunani da yake samu daga ƙwaƙwalwarsa, hannunsa ya ɗaura adaidai saman mararsa tare da ware idanunsa, sauƙesu yayi akan haɗaɗɗen adon zanen dake kewaye saman ɗakin,   daga gefe guda kuwa ƙoyayen wutane keta aikinsu wajen bada kaloli masu ma'ana da ɗaukar hankali, domin duk bayan ko wani second kowanne daga cikinsu yake fidda wani irin diffrent colour na haske me kyau, daddaɗan sanyin garin da kuma iskan da ake shiya sanya yaji gaba ɗaya jikinsa yayi weak, sake gyara kwanciyarsa yayi akaro na sau ba adadi, burinsa bai wuce bacci ya ɗaukesa ba, don zuwa yanzu zuciarsa takai ƙololuwa wajen matsawa ƙwaƙwalwarsa da tunani, bayan haka kuma gashi akwai gajiya sosai atattare dashi, sauda dama yakan zurfafa tunaninsa akan rashin lafiyansa, saidai kuma yasan komai na Allah Ne sai idan yasone zai baka lafiya, saɓanin haka kuwa kowani irin magani zakasha kodako yana maganin cutar taka sai kaga baiyi maka komai ba, yana matuƙar buƙatar lafiyarsa ayanzu saboda yanaji ajikinsa cewa nan gaba kaɗan zai cire rai da rayuwa, da kuma samun ingantaccen farinciki, tabbas ƙaddaransa babbace amma zaici gaba da ɗaukanta ahaka har izuwa lokacin mutuwarsa.

Bayan tayi sallan asuba bacci tayi sosai hakan yasa ba itace ta farka ba sai after 8. aɗan zabure tatashi daga kwancen da take tare da sanya hannu ta murza idanunta,  ganin hasken rana ya bayyana raɗau ta window'n ɗakinne yasanyata zuro  ƙafafunta ƙasa da sauri,  agurguje tayi wanka tare dayin brush,  koda ta fito sama sama tashafa body lotion ɗinta,  sauri sauri tasanya kayan uniform don tasan zuwa yanzu tayi latti sosai,  zama tayi akan bed tare da jawo cover shoe ɗinta wanda yake na makaranta, ƙoƙarin sanyawa ta somayi,  ciwon dake cikin tafin ƙafanta ne yasoma yi mata ɗan zafi sakamakon safa data sanya, shikuma ciwon baison zafi, ɗan rumtse idanunta tayi tare da soma ƙoƙarin tura kafanta cikin takalmin.  Turo ƙofar ɗakin Oummu tayi bakinta ɗauke da sallama, ganin Oummu yasanyata sakin murmushi tare dayin ƙasa da kanta cikin girmamawa tace da Oummu
"Ina kwana!"

"Lafiya lau, kinsamu tashi kenan yanzu shigowana na biyu kenan, ya ƙafan naki?" Oummu ta tambaya cike da kulawa.

"Da sauƙi Oummu, saidai yana ɗanmin zafi amma basosai ba"

Kallonta Oummu tayi tare da cewa
"Yanaganki cikin uniform? halan dai baki san ƙarfe nawa bane yanzun ko, kuma ma ai bazaki iya jigilan zuwa school da wannan ciwon aƙafanki ba!" Oummu tafaɗa cike da kulawa

Cikin yanayi naɗan sanyi ta gyaɗa kanta, don bata da abun cewa.

Murmushi Oummu tayi tare da dafata cike da kulawa tace "To kizauna yau ba zuwa school don mahaifiyar Almustapha da kuma wasu daga cikin ƴan uwana sun taso musamman don zuwa ganin amaryarsu!" Oummu taƙare maganar tana murmushin jin daɗi.

Faɗuwar gaba da tsinkewar zuciyane suka ziyarceta alokaci guda, amma saita ɗan daure ɗago kanta tayi ta kalli Oummu, murmushi Oummu ta mata cike da son ƙarfafa mata guiwa tace "Karki damu kanki akan komai Zieyaderh,  ninan matsayin uwa nake awajenki idan kina da abun da kikeso ko abun da bakyaso duk ki sanar dani nikuma Insha Allah Zan sha re hawayenki,  nasan ƴan uwana dukansu masu fahimta ne,  so bakida wata matsala dasu nakuma san insha Allah Zaki samu ƙauna ta musamman daga garesu, karki damu kinji!" Oummu taƙare maganar cike da lallashi.

Kai Zieyaderh ta kaɗa mata alaman  "To"
Cike da jin daɗi Oummu tace "Yauwa ki saki jikinki, ki cire uniform ɗin zan turo akawomiki abinci, sannan kizauna cikin shiri don anjima zan turo meyin kwalliya tazo ta gyaramin ke"

Kasa cewa komai tayi har Oummu tafice daga cikin ɗakin, ɗan guntun murmushin dake kan fuskarta ne ya koma, take kuma saiga hawaye suna gangarowa daga cikin idanunta, da sauri ta sanya hannu ta share cike da tausayin kanta, haƙiƙa tasan duk wannan abubuwan suna faruwa ne kawai saboda tarasa abu ɗaya aduniyarta wannan abun kuwa bakomai bane face UWA MAHAIFIYA haƙiƙa duk wata Uwa haskece ga rayuwar ƴarta mace matuƙar itaɗin takasance UWA ta gari, UWA itace ginshiƙi sannan kuma farinciki arayuwar YAYANTA, hannu takuma kaiwa ta share hawayenta,  sakamakon knocking door ɗinta da taji anayi, tana buɗewa tayi kiciɓus da Nabila hannunta ɗauke da tray ɗin abinci, Nabila ɗaya daga cikin tarin ƴan aikin gidanne amma ita tana ɓangaren kitchine ne,  itace me share sharen kitchine da goge duk wani inda aka ɓata,  fuskarta ɗauke da ɗan murmushi ta amshi tray ɗin, yayinda Nabila ta juya ta koma, aje tray ɗin abincin tayi tare da soma bubbuɗe plates ɗin dake saman tray ɗin, plate ɗin farko soyayyan doya ne da egg sauce  agefe,  plate na biyu kuwa pepper soup ne na kayan ciki, ɗayan plate ɗin kuwa shawarma ne me zafi har turiri take,  duk acikin abu ukun babu cimarta, hakan yasa da ƙyar ma ta iya cin doyan, sannan ta haɗa da tea, kaɗan taci abincin ta ture gefe, bathroom tashiga ta wanke hannunta, tray ɗin ta ɗauka da niyan sauƙa ƙasa, aikuwa

3 steps kawai ta kawo sukayi kiciɓus da Oummu tare da wata ƴar budurwa dake bayanta, wacce aƙalla bazata haura 27 years ba,   murmushi Oummu tayi tare da duban budurwar  cikin sakin fuska tace
"To Bilkh gama ƴar tawa please kiyi mata irin wanda kika jima bakiyi ba!"
Murmushi wacce aka ƙira da sunan Bilkh tayi cikin hausarta me bada wani irin sauti tace
"Bakomai Hajiya Insha Allah zaki yaba da wannan aikin sosai!"

Murmushi Oummu takumayi tare da ƙwaɗawa  Nabila ƙira, dama dayake tana kusa hakan yasa tataho da sauri, tray ɗin dake hannun Zieyaderh Oummu ta amsa tare da miƙawa Nabila tace takai kitchine, duban Zieyaderh tayi cike da kulawa tace "Zieyaderh wannan itace Bilkh shahararriyar me kwalliya ce,  please ki bata haɗin kai, maza ki mata jagora zuwa ɗakin ki"

Murmushi Zieyaderh tayi tare da cewa "To" itadai har yanzu kanta akulle yake don batasan menene za a mata ba.   Suna shiga cikin ɗakin Bilkh ta baje ƙaton ƙaton akwatin meckup ɗinta wanda tazo da shi.  Kallon Zieyaderh tayi tare da ce mata taje tayi wanka, musu banata bane hakan yasa ta wuce toilet, wanka tasakeyi kana ta ɗauro babban towel ajikinta wanda bazai bayyana tsiraicinta ba, tana fitowa Bilkh ta zaunar da ita tare da fiddo da wani tsadadden mai daga cikin akwatin meckup ɗinta ta shiga shafa mata, ita Zieyaderh abunma mamaki ya bata don bataga amfanin shafa mata mai ba bayan itama tanada nata hannun, tana kammala shafa mata mai ɗinne ta zaro wata galleliyar atamfa wacce taji ɗinkin fitted gown me kyau, wanda yana daga cikin kayan da Oummu ta miƙo mata lokacin da Zieyaderh ke wanka,  miƙawa Zieyaderh rigan tayi tare da cewa tasanya,  amsa tayi tare da komawa bayan drawer ta laɓe anan tasanya rigan gudun kada Bilkh taga tsiraicinta, ita kuwa Bilkh abubuwan da zata buƙata taketa haɗawa,  sosai rigan ya zauna ɗas ajikin Zieyaderh baƙaramin kyau kuwa tayi ba, akan wata kujera Bilkh ta zaunar da ita, saida tayi mata duk wani abu daya kamata kafun cikin nutsuwa ta shiga tsantsarawa Zieyaderh meckup akan beauty and innocent face ɗinta.
Bawani lokaci sosai suka ɓata ba kasancewar ba wani meckup aka mata akan fuskar nata sosai ba, simple ne amma yayi kyau sosoi,  take tsananin kyawun Zieyaderh ya sake bayyana, tsantsara mata ɗaurin ɗankwali Bilkh tayi bayan ta nannaɗe mata dogon gashinta atsakiyan kanta,  wani haɗaɗɗen sari me kyau da tsada kalan ja Bilkh ta ɗauka,  miƙar da Zieyaderh tsaye tayi tare da soma nannaɗa mata sarin ajikinta, kasancewar atamfar dake jikinta baƙine me ratsin ja, hakan yasa baƙaramin matching yayi da material sarri ɗin ba.
"Wow!" Bilkh ta faɗa bayan ta gama nannaɗawa Zieyaderh sarri ɗin, ita kanta sosai kyawun Zieyaderh ya ɗauki hankalinta, haƙiƙa ita kanta tasan ta iya kwalliya wanda zai gyara mace ya me da mummuna kyakkyawa, amma awannan karon tana da tabbacin cewa ba kwalliyarce tayiwa Zieyaderh  kyau ba, ita Zieyaderh'n ce tayiwa kwalliyan kyau. Turaruka masu ƙamshi da tsada ta fesawa Zieyaderh wacce tazama so silent.  Shigowar Oummu cikin ɗakinne yasa duk suka kalleta. Fuska faɗaɗe da murmushi tace  "Masha Allah, lallai Bilkh aikinki yayi kyau!"

Murmushi Bilkh tayi tare da cewa
"Hajiya ita yarinyar takice me kyau!"
Murmushi me sauti Oummu tayi sannan taja hannun Zieyaderh suka fice daga cikin ɗakin, yayinda Bilkh kuma ta ɗauki wayarta ta soma latsawa.  Tun shigowansu cikin katafaren falon

Oummun dayake na musamman gaba ɗaya waƴanda suke cikin falon suka maida kallonsu gareta, matane su Uku zaune acikin falon kowacce idan ka ganta kamar ka latsa jini yafito tsabar fari da jin daɗi, kallo ɗaya zaka musu kafuskanci cewa manyan masu akwai ne.  Cike da fari'a ɗaya daga cikin matan wanda itace bata da yawan shekaru kamar na su Oummu ta tarbo su, hannun Zieyaderh wacce kanta ke ƙasa ta riƙe tana me cewa  "Masha Allah!" agaban sauran matan ta zaunar da Zieyaderh kan wani lallausan carpet.

Atare duka matan suka haɗa baki wajen cewa "Masha Allah!" don kowaccensu ta yaba da kyau da kuma ƙuruciyar Zieyaderh,  duk da bata ɗago kanta sun kalleta da kyau ba amma kunyanta kaɗai ya isa gamsar dasu. Cike da ladabi Zieyaderh ta gaidasu, dukansu suka amsa fuska asake cike dajin daɗi.  Oummu ce tace taje ta kawo musu drinks da kayan fruits, aikuwa babu musu Zieyaderh ta miƙe, cikin mintuna kaɗan ta cika musu gaba da kayan fruits da drinks wanda duk tanayin aikinne cikin nutsuwarta, ba laifi sukam sun gamsu da yanayin tarbiyan yarinyar sosai, fatansu ɗaya shine Allah yasa tazamo itace matar zama agareshi.  Koda ta kammala gabatar musu da komai ɗakinta ta koma tare da ƙarasawa gaban madubin ɗakin ta shiga duba irin kyawun da tayi, don zuwa lokacin Bilkh tama jima da tafiya. Wani irin murmushi me sanyi tayi tare da sanya hannu ta shafi fuskarta daketa fidda ƙyallin kyau hancinta kuwa sai shinning yake.

Gyara zama Hajiya Sauba tayi tare da duban ƴar uwarta cike da jin daɗi tace "Gaskiya Sulaimiyya na yaba da hankalin wannan yarinyar sosai Allah yabasu zaman lafiya!"

Da Ameen Oummu ta amsa tana murmushi.

"Nima kuwa na yaba ƙwarai Allah yasanya alkhairi, amma fa wani hanzari ba gudu ba Sulaimiyya  yakamata ace anyi bikinnan acikin watannan, saboda banga amfanin jinkirtawa ba" Cewar Aunty Laylerh.

"Wannan tunanin shine araina Aunty Laylerh, kuma Insha Allah zamusa auren nan bada jimawa ba, domin kuwa daren jiya maganan auren mukayi da Abbansa yakuma ce zasuje shida abokinsa har can garin su yarinyar!"

Murmushin jin daɗi su duka sukayi tare dayin addu'an Allah yatabbatar da alkhairi acikin auren.

(Chaiii wani gurmin sai  ranan da RAJ ɗinku yayi aure zai angwance😝  am so sorry jia banyi update ba naɗan shiga busy ne🙏🏼)

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*WATTPAD*
@fatymasardauna
#romance

*Chapter 40*

Hira Oummu da ƴan uwanta sukayi sosai inda suka cigaba da tsara yanda bikin zai kasance. Aunty Muhibbat wanda takasance itace ƙaramar cikinsu ta kalli Oummu tare da cewa "Ni aganina idan babu damuwa, zamanta ya dawo wajena saboda kinga ina tare da shuwa arab saboda haka ba ƙaramin gyara zata samu ba" murmushi Oummu tayi tare da cewa "Hakane amma aikinsan tana zuwa makaranta, duk da ma dai muntsara kan cewar awannan year din zata zana waec nd neco ɗinta"

Cike da jin daɗi Aunty Muhibbat tace "To Allah yasa ayi komai dai a sa'a" da "Ameen" suka amsa su dukansu, basu wani jima sosai ba suka kama hanyar tafiya bayan sun jibgewa Oummu tsarabobi masu yawa da suka kawowa surukarsu Zieyaderh.

Ɓangaren Zieyaderh kuwa jin kamar ta takura yasanya cikin nutsuwa ta shiga warware sari ɗin dake jikinta tare da aje sa gefe. Ajiyar zuciya ta sauƙe akaro na barkatai, tare da ɗan jingina kanta da saman gadon da take zaune akai, tunanine cike fal azuciyarta, turo ƙofar ɗakin da akayi ne yasanyata ɗago kanta ta kalli bakin ƙofan, Nabila ce tashigo cikin ɗakin cikin ɗan rusunawa tace "Hajiya tace ayi mata ƙiranki"
Murmushi Zieyaderh ta ɗanyi tare da ƙoƙarin miƙewa tsaye "Ganinan zuwa" tafaɗa tana me zura bedroom slippers aƙafanta. Kai tsaye ɗakin Oummu'n ta nufa, ɗan tsayawa tayi ajikin ƙofan tare dayin knocking. Sanin cewa itace yasa Oummu dake zaune akan gado ta bada izinin shigowa, da sallama ɗauke abakinta ta shigo tare da neman waje taɗan rusuna daga gefe.

Oummu da yawancin lokuta fuskarta baya rabo da murmushi yanzun ma murmushine ɗauke akan fuskarta, miƙowa Zieyaderh wata haɗaɗɗiyar ƴar jaka me kyau tayi, amsan jakan Zieyaderh tayi tana me kallon Oummu cike dason ƙarin bayani, "Kyautane daga surakanki, inafata zakiyi murna zakuma ki yaba da kyautar!" Oummu tafaɗa tana me ƙoƙarin manna farin glass akan idanunta.

Jitayi gaba ɗaya jikinta yayi sanyi sunkuyar dakanta ƙasa tayi asanyaye tace "Nagode sosai Oummu amma sai nake ga kamar kyautan sunyi yawa, duk dama banga menene aciki ba!"

Murmushi Oummu tayi tare da cewa "Bana tunanin kyautar tayi yawa kedai ki amsa kawai, gaba kuma idan kunsake haɗuwa sai ki musu godiya"

Cike da jin nauyin Oummu'n tasake yi mata godiya sannan tatashi ta wuce ɗakinta. Koda taje

zama tayi akan gado tare da buɗe jakar, wani ɗan box me kyau da burgewa taciro daga cikin jakan, tare da buɗewa, wani danƙareren agogon hannu na gwal ne ya bayyana acikin kyakkyawan box ɗin. agogone na mata me matuƙar ɗaukar hankali, kyawawan duwatsunsa sai ɗauke ido suke, sake fito da wani box ɗin tayi wanda har yamafi wancan ɗin girma, shi kuwa wani irin danƙareren sarƙa da ɗankunnen gwal ne acikinsa me kyaun gaske, sosai design ɗin sarƙan ya mata kyau, har batasan sanda ta saki lallausan murmushi akan fuskarta ba, ganin kyaututtukan nada yawane yasanyata zazzage jakan gaba ɗaya akan gado, nan tayi arba da wasu arebian gown masu kyaun gaske, tare da wasu kwalaben humra masu ƙamshi irin masu kama jiki ɗinnan, cike da jin daɗi ta tattara kayan ta maida cikin jaka, sosai kayan suka mata kyau saidai kuma tasan matsayinta baikai nanba, bai kamata ace amatsayinta na ƴar wanda ba kowa ba ayi mata irin wannan hidiman, shigowar Nabila cikin ɗakinne yasanya ta tsaida duk wani abu da take tana kallonta.

"Hajiya tace ashaida miki kina da baƙo awaje"

Ƙirjinta ne ya buga da ƙarfi yayinda taji gabanta ya ɗan faɗi cikin yanayi naɗan mamaki tace "Baƙo?"
Kai kawai Nabila ta iya kaɗa mata alamar "Eh" kasa cewa komae tayi har Nabila ta juya ta fice daga cikin ɗakin, Vail ɗinta me kyau da walwali ta sanya tarufe jikinta, cikin fargaban sanin ko waye haka ta buɗe ƙofar ɗakin ta fita, bata samu kowa afalon ba hakan yasa kaitsaye tanufi ƙofar da zai sadata da compound ɗin gidan.

Tsaye yake ajikin motarsa ƙirar jeep yasha kyau cikin shigarsa ta half jumper White and blue colour, yayinda ya kafa hular Zanna bukar mai adon blue akansa, haɗaɗɗen sajen dake kwance akan fuskarsa ne ya kwanta luf akan ƙuncinsa, yana ganinta yasaki murmushinsa mai kyau wanda har saida gefe da gefen kumatunsa suka loɓa, ganinsa baƙaramin faɗar mata da gaba yayi ba,take mood ɗinta ya sauya daga ƙwarin guiwa zuwa raunin zuciya, kanta ta sunkuyar ƙasa tare da kasa ƙarasowa inda yake, murmushi yayi ganin ta tsaya batare da ta ƙaraso garesa ba, ahankali yashiga takawa har zuwa inda take, daddaɗan ƙamshin turarensa ne yasanar mata da zuwansa, ahankali ta ɗan lumshe idanunta tare da buɗesu, kanta taɗan ɗago ta kallesa, idanunsune suka sarƙe acikin na juna kasancewar shiɗinma kallonta yake, kasa ɗauke idanunta daga kansa tayi saima wani irin marairaicewa da idanun nata suka yi, shiɗinma kallonta yakeyi da sexy eyes ɗinsa wanda suke wani irin lumshewa kaɗan kaɗan, cikin wata irin murya me sanyi yace "Anan zaki barni bazaki bani wajen zama ba?"

Kanta ta sunkuwar ƙasa tare da ɗanyin murmushi, kallonta tamayar ga wajen ɗan shaƙatawan dake cikin gidan wanda aka ƙawatashi da wasu kujeru guda huɗu masu kyau gaba ɗaya flowers sun zagaye wajen yayinda sukayiwa rumfar dake wajen ƙawanya, kallonsa tayi sannan tanufi wajen shima ya rufa mata baya. Akan ɗaya daga cikin kujerun ta zauna yayinda shima ya zauna akan kujeran dake facing nata. Ƙasa tayi da kanta tare da soma wasa da ƴan yatsun hannunta murya asanyaye tace. "Ina wuni!" murmushin daya bayyana dimples dinsa yayi batare daya amsa taba sai idanu daya zuba mata, sosai yau ɗin tayi masa kyau, don kokaɗan meckup ɗin dake kan beauty face ɗinta bai goge ba, jin shiru bai amsata bane yasanyata turo

bakinta gaba aɗan shagwaɓe tace "To ba gaisheka nake ba kuma kaƙi amsawa!" Murmushi yayi harsai da haƙwaransa suka bayyana. "To ae banji bane, please kiɗan ƙara ɗaya sainaji!" Yafaɗa cikin salon kwaikwayon maganarta. Idanunta ta ɗago kana taɗan watsa masa hararan wasa tare da ɗan murguɗa masa ƙaramin bakinta dayasha baby pink colour lipstick, lumshe idanunsa yayi tare da jingina bayansa da jikin kujeran, wani irin shauƙi ne ke shigansa, sosai yanda tayi da bakinta yayi masa kyau, cikin wani irin yanayi yace. "Kullum ƙara kyau kike, idan kina fushi kyau kike ƙarawa, idan kina murmushi kyau kike ƙarawa, haka ma idan kina gabana kyau kike ƙarawa, inajin kamar sonki acikin jinina yake Zieyaderh, ko sau ɗaya ne please ki amsa min cewa kina sona!" yaƙare maganar yana me kafeta da mayun idanunsa wanda suka ɗan sauya kala, gaba ɗaya jikinta yayi sanyi, kanta ta sunkuyar ƙasa tare da ɗan ciza laɓɓanta, ƙirjinta ne yake bugu da sauri, maganan aurenta da Almustapha ne yazo yayi tsaye aranta, tabbas tanajin wani abu na daban dangane da Pharouk, to amma bata da tabbacin cewa wannan abun soyayyace, koda ma acd sonsa take mecece amfanin soyayyar? yanzu burinta shine ta koyawa zuciyarta soyayyar Almustspha, dan sai da soyayya ne kaɗai zata iya kyautata masa azaman aurensu. Ɗago idanunta da sukayi raurau da hawaye tayi daniyar yiwa Pharouk magana, saidai tuni maganan nata ta maƙale sakamakon ldo biyu da sukayi da Almustapha dake tunkaro inda suke, ganin ta tsaida idanunta abayansa yasanyashi ɗan waigawa don ganin abunda take kallo, idanunsa ne suka sauƙa akan kyakkyawan saurayin dake zuwa garesu, kwata kwata bai wuce saura taku shida ya ƙaraso inda suke ba, tashi tsaye yayi yana me fuskantar saurayin, daidai lokacin Almustapha ya ƙaraso, dayake shi jan ajin nasa baya hanasa fari'a, hakan yasa bawani ɓata lokaci ya miƙawa Pharouk hannu don su gaisa, ganin haka yasa Pharouk ma bashi hannu suka gaisa, cike da kulawa Almustapha ya kalli Zieyaderh wanda kanta ke ƙasa, hakanan gabanta keta faɗuwa, cikin muryarsa me ɗauke da nutsuwa yace "Inason aron baƙon naki naɗan wasu mintuna, inafatan bazan takuraki ba?"

Wani iri taji yayinda wani irin nauyi da kunyarsa suka lulluɓeta alokaci guda, jikinta asanyaye ta miƙe tsaye tare da kaɗa kanta alaman "Babu komai" cikin nutsuwa haka tajuya tanufi cikin gida, ita kanta bazata iya tantance awani hali take ciki ba awannan lokacin. Kamar wanda ƙwai ya fashewa haka ta haura sama ko lura da Oummu dake tsaye a bakin kitchine batayi ba, Ajiyar zuciya Oummu ta sauƙe tare da duban hanyar da Zieyaderh'n tabi, wani irin fargabane taji ya kamata, sai yanzu takejin tsoron haɗin da tayi, musamman ma da taga yanayin da Zieyaderh'n tashiga ayanzu, shiru tayi tare da faɗawa wani sabon duniyar tunani.
Ita kuwa Zieyaderh tana shiga ɗaki ta rufo ƙofarta, samun kanta tayi da sulalewa ta zauna daɓas aƙasa, batare da ta ankara ba taji wasu hawaye masu ɗumi suna sauƙa akan ƙuncinta, tabbas wannan sabuwar ƙaddaran da ta tsinci kanta aciki tayi mata girma, ƘADDARA tana neman haɗa aurenta da Almustapha, sannan kuma agefe guda ga Pharouk da yake neman ta amsa masa soyayyarsa, ƘADDARA mafi girma awajenta kuwa itace soyayyar Mr.Helper, hannayenta tasanya ta share hawayenta, wata zuciya ce me bata ƙwarin guiwa akan ta yarda da duk wata ƙaddara da tazo mata me kyau ko akasin haka, samun kanta tayi da kwanciya luf akan gado, mintuna ƙalilan bacci ɓarawo ya saceta.

Pharouk. Gudu sosai yake sharawa akan babban titin gaba ɗaya hankali da tunaninsa baya jikinsa, maganganun da Almustapha ya faɗa masa suketa yi masa yawo acikin ƙwaƙwalwarsa,

da ƙarfi ya daki steering motar ransa amatuƙar ɓace yace
"Bazan taɓa zama looser akaro na biyu ba SOORAJ, awannan karon tabbas bazan bari kasake nasara akaina kamar lokutan baya ba, bazan taɓa bari ka auri Zieyaderh ba SOORAJ!!" wani irin murmushi yayi tare da cije laɓɓansa, ahankali yashiga rage gudun da yakeyi tare da ƙoƙarin samarwa kansa nutsuwa tahanyar aminta da shawaran da zuciyarsa ta basa.
***
Oummu ce ta shigo cikin haɗaɗɗen ɗakin wanda yake mallakin Mijinta ne, Abba dake tsaye yana sanya garen kayansa ya ɗan juyo tare da kallonta murmushi yayi mata tare da cewa "Saboda kawai ɗanki zaiyi aure shiyasa kika kasa zaune kika kasa tsaye ko Sulaimiyya!" yaƙare maganar cikin yanayi na ɗan tsokana.

Murmushine ya faɗaɗa akan fuskarta tare da cewa "Yanzuma ai nashigo ne nasanar dakai abokan tafiyanka sun iso"

Murmushi ya kumayi tare da cewa "Bake kaɗai kikejin farinciki aranki ba Sulaimiyya nima inaji, saidai kuma ata wani ɓangare na zuciyata ina ɗauke da fargaban abun da zaije ya zo"

"Insha Allah Alhajina babu wani abu da zaizo sai alkhairin Allah!" Tafaɗa cikin son ƙarfafa masa guiwa.
Yaji daɗin maganan nata sosai hakan yasa yayi murmushi, har wajen motarsa Oummu ta rakasa inda ya haɗu da manyan aminansa su Uku suka kama hanyar airport, kai tsaye suka wuce Kaduna, daga nan kuma zasu shige cikin motocinsu su wuce ƙauyen saminaka.

Itakuwa Zieyaderh gaba ɗaya wunin yau batajin daɗin jikinta, hakanan takejin kanta cikin ƙunci, wani irin kewa me taɓa zuciya takeji yana ratsa duk ilahirin jikinta, gaba ɗaya su Shukra sun lura da rashin walwalan da takeyi kwana biyu, yanzuma zaune suke su duka ukun akan wani ɗan dakali suna me shan iskan dake kaɗawa asararin samaniya. Cikin yanayi naɗan zolaya Nasmah tace "Amarya badai wai cin amarcin aka fara tun yanzu ba? naga gaba ɗaya duk kin rame, sometimes kuma kina cikin damuwa"
Hararanta Zieyaderh tayi tare daɗan murguɗa mata baki cikin yanayin ɓata fuska tace
"Ni ba amarya bace"
Dariya Nasma da Shukra suka sanya, wanda hakan yaƙara ƙular da ita. "Uhumm kigama zille zillenki yarinya wallahi sai mun fidda ankon bikin ki ehe, sannan kuma sai mun sha rawa koya kikace Besty" Shukra tafaɗa tana kallon Nasmah. "Ƙwarai kuwa" Nasmah tafaɗa tana me gimtse dariyanta. Cikin turo baki gaba Zieyaderh ta miƙe daga zaunen da take tare da nufar hanyar da zai sadata da class ɗinsu. Kallo su Nasmah suka bita dashi harta ɓacewa ganinsu, sannan suka sa dariya, har acikin ransu su mamakinta suke na yanda gaba ɗaya tabi ta takura kanta.

Acan Ƙauyen Saminaka kuwa Tuni Abba sun gana da Malam Garba baban Zieyaderh, inda yayi musu karɓa ta mutumci, babu laifi kuma sun yaba da halin karamcin daya nuna musu, nan suka zauna suna me sake fahimtan juna, sam su Abba bada wasa suka ɗauko maganan auren ba hakan yasa lokaci guda suka gama magana inda Malam Garba ya shaida musu cewa ya basu

auren ƴarsa Zieyaderh, Alhaji Maham ɗaya daga cikin aminan Abba shi ya ciro wasu kuɗi dake cikin aljihunsa inda ya miƙa amatsayin sadakin auren Zieyaderh, naira dubu ɗari ne cas, cewar da sukayi basason bikin ya ɗauki lokaci ne yasanya Malam Garba cewa suyi haƙuri suɗan bashi lokaci zuwa nan da kwana huɗu zai sanar dasu kowani lokaci ya yanke, shikuwa yayi hakanne don yanason tattaunawa da Zieyaderh akan batun auren, domin tun da aka fara batun auren baiji ta bakinta ba kuma itama tana da haƙƙi, cikin mutumta juna su Abba sukaiwa Malam Garba sallama inda suka kama hanyar dawowa cikin garin Kaduna.
..........

15 minute da tashinsu a school  kenan amma har zuwa yanzu Kamalu driver baizo ɗaukarta ba kamar yanda ya saba,  waige waige taɗan somayi wai kozata hangosa amma babu ko me kama dashi, gashi gaba ɗaya ƴan makarantar sun soma watsewa don tuni su Shukra ma sun tafi, ahankali take takawa harta isa bakin gate ɗin fita daga makarantar,   tsayawa tayi daga ɗan gefe kaɗan tana me ƙarewa motocin da keta hada hada awajen kallo,   wata haɗaɗɗiyar blue car wanda taji black tinteck ne ta tsaya adaidai gabanta,  kallon motar Zieyaderh tayi amma ganin bata iya ganin wanda ke cikin motar ya sanya ta ɗauke kanta gefe,tare da cigaba da kallon hanya, ahankali ya shiga zuge glass ɗin motar, fuskarsa ɗauke da murmushi yace "My ƴar kyakkyawan budurwata!"  jin muryarsa acikin kunnuwanta yasanya tayi saurin ɗagowa ta kalleshi, hakanan taji gabanta ya faɗi amma sai tasaki murmushi,  da hannu yayi mata alaman da ta taho, samun kanta tayi da kasa musa masa sai kawai taɗan ƙarasa jikin motar, daga ciki yasanya hannu ya buɗe mata murfin motar,  duk da cewa ƙirjinta na dukan uku uku haka ta daure tashiga cikin motar saidai bata rufe murfin motar ba,  kanta ta sunkuyar ƙasa tare da kama ƴan yatsunta tana wasa dasu, shikuwa Pharouk ajiyar zuciya ya sauƙe tare da ƙiran sunanta murya asanyaye. Jin yanda yaƙira sunannata yasanyata ɗago da kanta ta kalleshi, gani tayi gaba ɗaya murmushin dake kan fuskarsa ya kau, zuwa yanzu damuwane shumfuɗe akan fuskarta sa,  kasa ɗauke idanunta daga kansa tayi saidai kuma ba cikin idanunsa take kallo ba, tunowa da tayi cewa jiya tabarsu da Almustpha batare da tasan me Almustaphan ya faɗa masa ba yasanya taji gaba ɗaya jikinta yayi sanyi, jitayi idanunta naneman kawo ruwa, ahankali yasanya hannunsa ya ɗago haɓarta, hakan yasa suka jefa idanunsu cikin na juna, cikin wani irin yanayi me wuyar fassaruwa yace "Kinason aure'n?"  gabantane ya faɗi dajin tambayar tasa amma kuma saita samu kanta da kasa amsa masa,  fuskarsa yasake mareraicewa tare da cewa "Da gaske kenan aure za'a miki? me yasa kika amince da hakan? kinyarda arabani dake kenan ko?" yaƙare maganar yana me matuƙar nuna rauninsa akan fuskarsa.
Hawayen dake kwance acikin idanunta ne suka samu daman gangarowa batare da ta shiryawa hakan ba.     Ganin hawaye akan fuskarta ya sanyashi lumshe idanunsa tare da matso da fuskarsa gaf da tata har suna iya jiyo hucin numfashin juna, jin sauƙan numfashinsa akan fuskarta yasanya azabure tayi saurin buɗe idanunta , shima buɗe nasa idanun yayi wanda suka kaɗa sukai ja, wani irin kallo daya mata ne yasanya tayi saurin jan jikinta baya tare da ture hannunsa dake kan haɓan ta,  kuka ne yake neman cin ƙarfinta hakan yasa ta juya da sauri ta fita daga cikin motar, dai dai lokacin kuma motar da aka saba zuwa ɗaukanta dashi wanda kamalu driver ke ciki ya tsaya adai dai ƙofar shiga gate ɗin makarantar, da ɗan sassarfa taje ta buɗe murfin motar tare da faɗawa ciki kana ta jawo murfin ta rufe,  kanta ta cusa acikin cinyoyinta tare da sakin kuka me sauti, Ko bi takan Kamalu driver dake bata haƙurin rashin

zuwansa da wuri da yayi bata biba, kuka take sosai tana me kakkame jikinta, wani irin zafi zuciyarta ke mata, Me yasa har izuwa yau baice komai ba? me yasa ya hanata ganinsa har na tsawon kwana uku? tanajin zafi acikin rai da zuciyarta, safe, rana, dare, duk shine acikin rayuwarta me yasa takejin hakan? Kukanta taci gaba dayi wanda babu me rarrashi, zuwa yanzu harta soma jin haushin kanta, musamman yanda tamaida kanta wata wawiya akansa.

Ganin tashin motarsu yasanya Pharouk sakin wani murmushi wanda shikaɗai yasan ma'anarsa, key ɗin dake jikin motar yaɗan murza, tare da cilla motar tasa kan titi, yayiwa kansa alƙawarin matuƙar shine Pharouk to SOORAJ bazai taɓa samun Zieyaderh amatsayin mata ba.

SOORAJ
Ahankali yake matsowa jikinta yayinda takeja baya shi kuma yana me ƙara matsota, wani irin numfashi yake fitarwa me zafi, kasancewar takawo jikin bango hakan yasa ta tsaya cak, hakan kuma yayi daidai da ƙarasowarsa gareta, ganinsa adaf da ita yasanyata lumshe kyawawan idanunta tare da sakin wani sassanyar ajiyar zuciya, kyakkyawan fuskarta yake kallo yayinda idanunsa ke lumshewa ahankali hankali, numfashinsu ne ya cakuɗa dana juna, yayinda ƙamshin turarensu ya haɗe waje guda, hakan yasa wani irin ƙamshi mai daɗi ke fita ajikin kowannen su, fuskarsa ya manna da tata fuskar yayinda ya sauƙe hannayensa akan faffaɗan waist ɗinta, cikin wani irin yanayi ya ɗaura lips ɗinsa akan nata tare ɗan kama lip ɗinta na ƙasa ya ɗan tsotsa, wani irin abune yaji ya zirga masa har cikin tafin ƙafansa, sake kama lips ɗinnata yayi yashiga tsotsa ahankali yayinda yake fitar da wani irin numfashi, ahankali cikin rufewar ido yake ƙara tsotsan laɓɓanta, wanda hakan yasanya taɗan buɗe bakinta, ahankali ya tura bakinsa cikin nata yayinda harshenta ya faɗa cikin bakinsa, wani irin abu yaji yatsarga ajikinsa yayinda yaja wani irin numfashi tamkar wanda zai shiɗe, azabure ya farka daga baccin da yakeyi, tare da buɗe idanunsa da suka kaɗa sukai jajur, wani irin zufane ke ketowa ta jikinsa yayinda gaba ɗaya gashin jikinsa suka mimmiƙe, jijiyoyin jikinsa ne suka fito raɗa raɗa, tashi zaune yayi yana ne ƙoƙarin jawo numfashinsa dake ƙoƙarin ƙwacewa, yayinda yakejin tamkar ana buga masa guduma acikin kansa, wani irin ƙara yayi tare da dafe kansa wanda yakejin wani irin azababben ciwo acikinsa, hannayensa yasanya ya dafe kunnuwansa tare da rumtse idanunsa, duniyarce gaba ɗaya take juya masa.

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*WATTPAD*
@fatymasardauna
#romance

*Chapter 41*

Ahankali ya zuro da ƙafafunsa ƙasa,  tare da rumtse idanunsa wanda suka kaɗa sukai ja tamkar waƴanda aka watsawa garin barkono,  hannayensa ya sanya ya dafe kansa dake barazanan tarwatsewa, wani iri yakeji acikin kansa tamkar ana doka masa gudu ma, cikin ƙarfin halin daya aro ya dasawa kansa ya miƙe tsaye tare da soma binbango yana neman hanyar da zai sadasa da toilet,  zuwa yanzu ko gani sosai baya iyawa,  wani irin duhu ne ke neman mamaye ganinsa, sunan Allah Yashiga ambata acikin ransa yana me tafiya ahankali,  ƙafafunsa  ne sukayi masa nauyi, haka yakeji  tamkar an ɗaure masa su da kaca,  aninayen dake jere reras agaban rigarsa ya soma cirewa, tare da sanya hannunsa  ya kunna shower take ruwa yasoma zuba ajikinsa, duka hannayensa ya sanya ya dafe bango tare da rumtse kyawawan idanunsa, yayinda ruwa ke dukan naked skin ɗinsa, still ambaton Allah Yaketayi acikin ransa, ahankali yakejin nutsuwar daya rasa na dawo masa, yayinda yaji gaba ɗaya jikinsa yayi weak, zuciyarsa kuwa har yanzu fast fast haka take bugawa, sake lumshe idanunsa yayi tare da ɗan cizan laɓɓansa,  ko ka ɗan bayason tuno mafarkin da yayi wanda tunda yake bai taɓayin makamancin irin saba,  bayan hannunsa yasa yaɗan naushi bango tare da kashe shower'n, wani white towel ya ɗaura akan waist ɗinsa tare da ɗaukan wani ɗan ƙaramin towel yashiga goge jiƙaƙƙiyar suman kansa,  koda ya fito daga toilet ɗin, zama yayi akan dressing mirror tare da ɗaukan body lotion  ya shiga shafawa jikinsa,  yana gamawa ya feshe jikinsa da wani irin body spray me daɗin ƙamshi,  black pencil crazy jeans and white t-shirt ya sanya, kasancewar anyi ruwa sannan akwai sanyi sosai agarin yasanya shi ɗaura black leda jacket akan rigan,  wayoyinsa ƙiran Samsung galaxy  S20 da kuma iphone 11 pro max ya zura acikin aljihun jacket ɗin nasa, wasu irin combat shoe yasanya masu kyau da tsada, ahankali ya ƙarasa gaban mirror tare da ɗaukan facing cap white colour ya sanya akansa, baƙaramin kyau shigan yayi masa ba, yayinda sajen dake kwance akan fuskarsa keta shinning.  Farfumed ya fesa ajikinsa kana ya nufi hanyar fita daga ɗakin, ahankali yake sauƙowa daga kan haɗaɗɗen matattakalan da zai sadasa  da wani katafaren falo wanda yagaji da haɗuwa,  yana ƙarasowa cikin falon yanufi wajen wani haɗaɗen fridge wanda yake na glass, gaba ɗaya kana iya hango duk wani abu dake ciki, buɗe fridge ɗin yayi tare da zaro gwangwanin malt, ɓalle murfin yayi tare da kai bakinsa jikin gwangwanin,  8 minute kacal ya shanye gaba ɗaya malt ɗin, tare da wurga gwangwanin cikin dustbin. Cikin takun dake nuna tsantsar aji da kuma nuna cikakken zarransa na ɗa namiji, ya fito daga cikin ƙawataccen hotel ɗin, wanda anan yake da zama tunda yazo Singapore, hotel ne mai kyaun gaske don yana ɗaya daga cikin manyan hotels ɗin da akeji dasu a ƙasar Singapore,  tafiya yake da ƙafafunsa yayinda yashiga cikin  ƴan ƙasar yasaje dasu sak, kasancewar kalan fatarsu iri ɗayane danasa yasanya bazaka iya banbanceshi da suba, babu wani ɗaya acikinsu da zaice ya ɗarasa hasken fata,  wani ƙaton club yanufa inda maza masu aji ke zuwa, kowa dake cikin club ɗin harkan gabansa yake babu ruwan kowa da kowa, wasu suna shaƙatawane da ƴan matansu yayinda wasu keshan wine, wasu kuwa rawa kawai sukeyi,  kan wata kujera da take ita kaɗai ya zauna tare da zaro wayansa don yanaso yayi vedio call da Mas'oud,  ɗaya daga cikin masu aiki a club ɗinne ya tambayashi tsakanin Alcohol da wine wanne yake da buƙata. kansa ya girgiza tare da cewa ya basa drinks kawai, hakan kuwa akayi inda ma aikacin ya cika masa gabansa da drinks kala kala, nan ya maida hankalinsa ga wayarsa tare da dannawa Mas'oud ƙira.

Nigeria

Kasancewar Yau asabar babu makaranta hakan yasa bata tashi da wuri ba sai wajen 9, kasancewar yanzu sam bata aikin gidan Oummu ta ɗebi wadatattun ma'aikata wanda sukeyin girki da komai, fitowanta a wanka kenan zama tayi agaban mirror tare da shafa mai ajikinta, sama sama ta shafa powder akan fuskarta tare da ɗan goga man baki abakinta,  wata doguwar riga na black lace ta sanya, sosai rigan tayi mata kyau,  tsayawa tayi tana me kallon kanta a madubi,  ita kanta tasan tayi wata ƴar rama wanda bakowane zai gane hakan ba har sai  in wanda ya lura,  tana ƙoƙarin ɗaura ɗankwali  ne aka turo ƙofar ɗakin nata, murmushi ne ya bayyana akan fuskarta cikin yanayi na girmamawa tace "Barka da safiya Oummu!"

"Yauwa barka, fatan kintashi lafiya!" Oummu ta tambayeta cikin kulawa.

"Lafiya ta amsa tana me ƙoƙarin sunkuyar da kanta ƙasa.
"Masha Allah, to maza zo muje yau kina da babban baƙo yana falon Abbanku,  nasan da ace kinsan da zuwansa to tabbas da tun 7 zaki tashi" Oummu tafaɗa tana me ƙoƙarin kamo hannunta.  Jitayi gabanta ya faɗi, tsorone ya kamata don gaba ɗaya tunaninta ya bata cewa Pharouk ne ya kuma dawowa.  Haka tabi Oummu jikinta asanyaye,  suna sauƙa daga kan steps ɗin Oummu ta miƙo mata wani tray wanda samansa ke ɗauke da kayan fruits. "Ungo ki kai masa tun ɗazu ke yake jira yace yana sauri zai koma"
Jikinta na rawa haka ta amshi tray ɗin ta fice daga cikin falon, ƙirjinta na dukan uku uku haka ta nufi ɓangaren da zai sadata da  falon Abba.   Ahankali taturo ƙofar falon bakinta ɗauke da sallama ta kutsa kanta ciki,  tarwal idanunta suka sauƙa akansa, koda wasa bata taɓa tunanin ganinsa awannan lokacin ba, muryarta narawa tace "Baba!!"  murmushi Malam Garba yayi tare da yi mata alama da hannunsa akan taƙaraso, da sauri ta ƙaraso cikin falon tare da ƙarasowa gabansa ta aje tray ɗin, idanunta ne suka kawo ƙwalla cikin muryarta dake rawa tace "Baba sannu da zuwa!"
"Yauwa Zieyaderh sannu ya makarantar?"
"Alhamdulillah!" tafaɗa asanyaye tana me kallon mahaifinnata.
Ganin haka yasanyashi sakin murmushi tare da sanya hannu ya dafa kanta, cikin kulawa yace "Kina mamakin ganina ko Ziyaderh? karkiyi mamaki ni mahaifinki ne kuma ina ƙaunarki amatsayinki na tilon ƴata, haƙiƙa nasan banzama mai kyautawa agareki ba, duk irin abun da nayi miki banyi miki shi ason raina ba, nakuma ɗauki hakan amatsayin ƙaddara da babu wanda ya isa ya guje mata,  kiyi haƙuri ki yafemin Zieyaderh haƙiƙa na cutar da rayuwarki na bari kinyi rayuwa cikin wahala da rashin gata, nasan ban kyauta miki ba amatsayina na mahaifi agareki...."  Kuka tasanya me sauti tare da kifa kanta akan ƙafafunsa kana ta sanya hannayenta duka biyu ta rungume kafafun nasa, wani irin kuka takeyi mai ban tausayi yayinda agefe guda kuwa wani irin nutsuwa ke shiga zuciyarta.

"Nibakamin komai ba Baba, kaine zaka yafemin, duk da cewa bansamu ƙauna daga gareka ba, amma baka koyar dani tarbiyan banza ba, na saɓa tarbiyana na gudu na barka batare da neman izininka ba, kayi haƙuri Baba kayafemin!!" Tafaɗa tana kuka sosai.  Idanunsa ne suka cika tab da ƙwalla ahankali ya ɗago kafaɗunta cikin son ya rarrasheta yace "Nayafemiki Zieyaderh, najima da yafemiki Allah yayi miki albarka, kema kuma inaso kiyafemin haƙƙin ki

dake kaina wanda bansauƙe miki shi ba!"
Hawayen dake gudana akan fuskarta ta share tare da yin murmushi cikin jin daɗin ganinta gata gashi tace "Najima da yafe maka Baba!"
Murmushin jin daɗi shima yayi tare da shafa kanta cikin soyayya irin ta ɗa da uba yace "Allah Yamiki albarka!"   da "Ameen" ta amsa tana murmushin jin daɗi, kamar ba itace tagama kuka yanzu ba, tray ɗin da ta shigo dashi ta miƙo mai tare da cewa "Baba kasha fruit" Murmushi yayi tare da girgiza mata kansa cikin halin dattako irin nashi yace "A'a Zieyaderh naƙoshi, bakiga har abinci sun kawomin ba!" yafaɗa yana meyi mata nuni da kulolin dake jere saman table.  Cikin jin daɗi Zieyaderh tashiga bubbuɗe kulolin wanda aka shaƙe cikinsu da abinci na alfarma.  "Baba to ai bakaci ba!" tafaɗa aɗan shagwaɓe tana kallonsa. Murmushi yayi tare da cewa "Dawo kizauna kusa dani" cikin jin daɗin sabuwar kulawan da tasamu daga mahaifinnata ta dawo ta zauna akusa da ƙafafunsa.
"Zieyaderh" yaƙira sunanta cikin kulawa.
"Na'am" ta amsa masa tana me dubansa.

Gyara zamansa yayi tare da cewa "Nasan ko ada can baya ke me hankali ce da nutsuwa, sannan kuma ke yarinyace me biyayya, bansan ko akwai soyayya atsakaninki da wanda ake ƙoƙarin haɗaki aure dashi ba, amma haƙiƙa na amince da karamci da kuma mutumci irin na waƴannan mutanen, saidai kuma duk da haka bazan yi gaggawan yin gaban kaina ba, duk da cewa na amince musu batare danaji ta bakin ki ba, sannan sun kawo sadaki suna me neman asanya musu lokacin aure amma banyi musu na'am ba nadaice su bani nan da kwana huɗu, bazan hanaki abun da kikeso ba Zieyaderh, bakuma zan tilastaki yin abun da bakya so ba, idan har bakyason aurennan karkiji ɗar ko shakka ki sanar dani, nikuma zan maida musu da sadakin su zan kuma basu haƙuri"
Shiru tayi tare da sunne kanta ƙasa, wasa da hannayenta tashiga yi cikin sanyin daya zame mata sabo tace "Na'amince musu Baba!"
Murmushine ya faɗaɗa akan fuskarsa cike da tausayin ƴartasa yace "Allah yamiki albarka Zieyaderh, tashi kije idan yaso sai ki sanar da Ummantaku ni zan wuce!"   "To" tace dashi asanyaye kana ta miƙe tsaye tana cewa "Baba kaɗanci abincin ko kaɗanne dan Allah!" murmushi kawai yayi harta fice bai sake ceda da ita komai ba.  Zieyaderh kuwa tana fita daga cikin falon aɗan corridor ɗin dake barandar falon ta tsaya, bayanta ta jingina da jikin bango tare da sanya hannu ta sharce hawayen daya silalo kan ƙuncinta,  kanta ta girgiza tare da ɗan cije laɓɓanta, ita kaɗai tasan meke zuciyarta,wanda bazata kuma iya furtawa kowa ba,  gefen mayafinta tasanya ta goge idanunta sosai sannan ta nufi ɓangaren Oummu.  Afalo ta samu Oummu hakan yasa ta ɗan rusuna tare da gaya mata saƙon Baban nata, murmushi Oummu tayi tare da miƙewa tsaye mayafinta ta ɗauka kana tafice daga falon, Zieyaderh kuwa kitchine ta wuce inda ta haɗawa kanta tea, domin ayanda take batajin wani abu bayan tea zai iya samun gurbin zama acikinta.

Jin abun da Malam Garba yace yasanya Oummu yin murmushi, batakai ga cewa komai ba muryar Abba dake shigowa ya karaɗe cikin falon inda yake cewa "Karka damu Malam Garba ae danan dacan wajenku duk ɗayane awajen mu, kuma kamar yanda kuke iyaye awajenta, haka muma muke matsayin iyaye awajenta"

"Ƙwarai kuwa kuma insha Allah zata samu kyakkyawan kulawa awajenmu, idan kace takoma wajenka kafun bikin makarantar ta zai iya samun matsala, amma idan tananan baza a samu wani matsala ba muna shirye shiryen mu kuma tana zuwa makaranta!" cewar Oummu wacce sam batason Baban Zieyaderh'n ya kafe akan ta koma wajensu, so take tayiwa zieyaderh gyara na musamman, kana kuma tayi mata auren gata.
Ganin sun haƙiƙance ne yasanya Malam Garba, janye maganarsa na cewa yanason tafiya da Zieyaderh, dole tasa ya haƙura yayi musu bankwana bayan sunyi shawara da Abba sun kuma yanke lokacin biki nan da sati biyu masu zuwa,  duk yanda Malam Garba yaso ya shiga motar haya ya koma Abba ƙiyawa yayi nan ya kafe akan dole saidai driver ne zai maidashi gida, sam bayason jayayya dasu hakan yasashi amincewa bayan Oummu ta sanar dashi cewa acikin satin zasu kammala haɗa kayan lefensu  zakuma su kawo har ƙauyen Saminaka, sanin halin Inna Ma'u yasan ya Malam Garba cewa idan sunma haɗa lefen su barshi a wajensu idan yaso duk randa aka kai yarinya ɗakinta sai abata. Sosai su Oummu sukayi na'am da hakan don Oummu itama ganauce akan hali irin na Inna ma'u.
***  Sosai su Oummu suka ta da maganan bikin gadan gadan Inda Oummu ta bawa Aunty Muhibbat milions ɗin kuɗi wanda za a haɗo lefe dashi, musamman Aunty Muhibbat ta hau jirgi zuwa Dubai don acanne take da tabbacin samun ingantattun kaya masu kyau da nagarta, jin wannan auren suke tamkar shine aure na farko da  za'a farayi acikin family ɗinsu,  Zieyaderh kuwa ayƴan kwanakinnan sosai tashiga busy kasancewar sun fara test ɗin first time, kuma yanzune karatunnasu yake zafi sosai, hakan yasa gaba ɗaya hankalinta naga karatun ta, awannan karon so take tazo first class acikin ajinsu, inda suka sanya gasa su Ukun ko wacce burinta shine tazo first class,  yauma agajiye ta dawo daga makarantar inda tun shigowarta taga haraban gidan cike da motoci,  gyara zaman school bag ɗin dake rataye a kafaɗanta tayi kana ta tura ƙofar falon tashiga bakinta ɗauke da sallama.  Oummu da Aunty Muhibbat ta iske acikin falon sai kuma wayƴansu mata guda biyu, gaba ɗaya tsakiyan falon cike yake da wasu akwatuna masu tsananin kyaun gaske,  akwatuna ne har guda 24 inda kowani set shida yake ɗauke da nasa kalan, cike da girmamawa Zieyaderh ta rusuna tagaida Aunty Muhibbat, fuska ɗauke da murmushi Aunty Muhibbat ta amsa mata tare da tambayanta ya makaranta,
da "Alhamdulillah!" ta amsa mata, harta kusa haura step ɗin dazai sadata da ɗakinta muryar Oummu ya tsaida ta inda take cewa tashirya sannan ta zuba kayanta a akwati tazo zasu wuce gidan Hajiya Arabi da Aunty Muhibbat,  Hajiya Arabi wata matace wacce ta matuƙar iya gyara mace daga ciki har waje, ta iya gyaran amarya sosai hakan yasa duk wani wanda yakeji da kuɗi idan yatashi gyara ita yake nema, gyaranta yana da matuƙar tsada amma kuma yana da kyau sosai, hakan yasa Oummu ta narkamata  maƙudan  kuɗaɗe don ta gyara mata Zieyaderh.

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*WATTPAD*
@fatymasardauna
#romance

*Chapter 42*

Tana shiga cikin ɗakin tasoma rage kayan dake jikinta, wani mini pink towel ta ɗaura  kana ta wuce bathroom, cikin nutsuwa tayi wanka  tare da ɗauro alwala.   Kasancewar yanayin na yau ana ɗan zafi yasanya komai bata shafa ba ta zura wata  jallabiya irin ta mata wacce take da adon duwatsu haɗi da zanen beuty's followers agabanta, sosai rigan ta amshi jikinta kasancewar rigan nada kalan ja hakan yasa taƙara bayyana hasken fatarta, ɗan ƙaramin trolly ɗinta tajawo, sif ɗin kayanta ta buɗe ahankali tashiga  ɗiban kayan tana zubawa acikin trolly ɗin,  wani irin tunanine ke yawo aƙasan zuciyarta, hakanan taji batason barin gidan, duk da kasancewar acikin ƴan kwanin bata ko ganinsa bare jin labarinsa, wani irin kewane ke cinta azuciya,  tanaso taji wannan daddaɗan ƙamshin nasa mai ratsa zuciya, tanaso taga koda gilmawansa ne,  da tunani iri iri acikin ranta haka ta kammala haɗa ƴan kayanta wanda tasan zata buƙata,  gyalen jallabiyan ta yafa akai zuwa jikinta kasancewar yana da ɗan girma, ahankali take sauƙowa daga kan step hannunta riƙe da trolly da kuma school bag ɗinta dake rataye akan kafaɗunta.

Oummu naganinta tace.
"Yauwa kin kimtsa ko, kici abinci sai ku wuce"  da  "To" kawai ta amsa kana ta aje jakakkunan nata ta nufi dinning area, ɗaya daga cikin kujerun wajen taja ta zauna tare da ɗaukan plate tayi serving kanta,  ahankali take tsakuran abincin tana kaiwa bakinta, sam batajin test akan harshenta,  sama sama take jiyo hiran Oummu da Aunty Muhibbat inda duk maganan tasu akan auren nata ne sukeyi,  itakam har yanzu ganin abubuwa take kamar al'amara, don bata taɓa ganin aure irinnata ba, sam ta rasa awani matsaya take, don ita kanta takasa gane kanta, ahankali take ɗiban abinci acikin spoon tana kaiwa bakinta,  wani irin baƙon ƙamshin turaren daya shigo hancinta ne yasanyata ɗago kanta takalli cikin falon, idanunta ne suka sauƙa akan sa wanda shigowarsa cikin falon kenan shiɗinma kuma kallonta yakeyi, tarine ya sarƙeta yayinda abincin da takeci ya shaƙe maƙoshinta,  da sauri ya ƙaraso kan dinning ɗin tare da ɗaukan bottle water, ɓalle murfin yayi kana ya miƙo mata, da sauri ta amsa takai bakinta, saida tasha har kusan rabin goran sannan ta ajiye tare da sunkuyar da kanta ƙasa ahankali take maida numfashi don har idanunta saida suka sauya kala sukayi ja.
"Are you okay?" Almustapha wanda yasha ado cikin jan shadda ya tambayeta.
Kanta ta kaɗa masa alaman "Eh"
Murmushi yayi tare da ɗan ranƙwafowa gaf da ita cikin yin ƙasa da murya yace "Ehem ƴan mata kin ruɗe ne saboda kinga nayi miki kyau ko?"
Da sauri ta ɗago kanta ta kalleshi fuskarta ɗauke da mamakin jin maganarsa. Idanunsa ɗaya ya kashe mata tare da zura hannayensa cikin aljihun  wandonsa,  haɗa idanu da suka sakeyi yasanya ta murguɗa masa baki,  murmushine ya suɓuce masa tare da ɗan zaro idanunsa, ƙasa ƙasa yace "Ni kika murguɗawa baki ko, watarana zaki murguɗawa wanda zai cire bakin

gaba ɗaya" yafaɗi haka yana me ƙoƙarin komawa cikin falon, bayansa tabi da kallo harya ƙarasa kusa da Oummu ya zauna, miƙewa tayi itama tare da ƙarasowa cikin falon, dubanta Oummu tayi cikin kulawa tace "Harkin kammala?" murmushi tayi tare da ɗaga kanta alaman "Eh"
Miƙewa Aunty Muhibbat tayi tare da ɗaukan mayafinta cikin kulawa ta dubi Almustapha tare da cewa "Muje ka sauƙe mu ko!"
Trolly ɗinta ta ɗauka tare da kallon Oummu, itama Oummun kallonta takeyi murmushi tayi mata tare da cewa.
"Ki kwantar da hankalinki nima gobe zanzo insha Allah!"
asanyaye ta gyaɗa kanta alaman to.
Almustapha ne ya fara yin gaba, sai Aunty Muhibbat yayinda tarufa musu baya, har jikin motar Almustapha Oummu ta rakosu, inda Aunty Muhibbat tabuɗe gidan baya ta shiga, hakan yasa dole ta shiga gaba badon taso ba. Koda suka ɗauki hanya Almustapha da Aunty Muhibbat ne keta hiransu, ita kuwa shiru tayi tana kallon hanya.

Asokoro shine unguwar da Hajiya Arabi take, agaban wani tamfatsetsen gate Almustapha ya tsaida motar, nan Aunty Muhibbat tasoma ƙoƙarin buɗe murfin motar, jakanta ta ɗauka tare da kai dubanta ga Zieyaderh "Muje ko" tafaɗa tana me ƙoƙarin fita daga cikin motan.
buɗe murfin motar tayi itama tare da ɗaukan trolly bag ɗinta, atare suka shiga cikin gidan ita da Aunty Muhibbat, tundaga compound ɗin gidan sukejin tashin ƙamshi kamar wani wanda sukazo kamfanin turare, ƴan tsirarun ƴan mata ne ke zazzaune awata runfa dake compound ɗin. kowacce harkan gabanta takeyi, aunty muhibbat nagaba tana biye da ita abaya haka suka shiga cikin wani haɗaɗɗen falo, wata farar mata tamkar balarabiya akyau suka iske zaune acikin falon tana ganinsu ta saki murmushi tare dayi musu barka da zuwa.
ƙarasowa cikin falon sukayi Inda Aunty Muhibbat ta zauna akusa da matar itakuwa Zieyaderh akan sofa ta zauna tare da gaishe da Hajiya Arabi wacce ta kafeta da idanu. Fuska ɗauke da murmushi Hajiya Arabi ta amsa mata tare da duban Aunty Muhibbata tace "Tun ɗazu ae nake zuba idanun ganinku"
Murmushi Aunty Muhibbat tayi tare da cewa.
"Taje school ne yanzu dawowanta, dan Allah Arabi ki gyara mana ita da kyau kinsan amaryace irin tagaban goshinnan"
Dariya Hajiya Arabi tayi tare da cewa "Kada ki damu Muhibbat ina da tabbacin har tukuici saikun bani!"
Dariya Aunty Muhibbat tayi tare da miƙewa tsaye, zaman jakan dake rataye akan kafaɗanta ta gyara tare da cewa.
"Ni zan wuce sai munyi waya" duban Zieyaderh tayi tare da cewa "Ki kwantar da hankalinki nanma kamar gida yake, ki nutsu kuma amiki gyaran da kyau, idan kinje makaranta banda yawan yawo ki nutsu awaje ɗaya." kai Zieyaderh ta jinjina mata alaman to.
Ƙwala ƙiran wata mata Hajiya Arabi tayi nan wata ƴar dattijuwar mata taƙaraso cikin falon, nuna mata Zieyaderh Hajiya Arabi tayi tare da cewa ta kaita masauƙi na musamman domin tun yau da dare zasu fara aikinsu. "To" Matar tace tare da duban Zieyaderh tace "Muje ko" babu musu ta ɗauki trolly ɗinta tabi bayan matar yayinda Aunty Muhibbat kuwa suka fice daga falon ita da Hajiya Arabi.

Matarnan nagaba Zieyaderh na binta abaya haka suka nufi wani ɗaki,   koda suka shiga cikin ɗakin ɗakine mai girma wanda ke ɗauke da ƴan madaidaitan gado har guda uku masu kyau, sai kuma sif ɗin ajiye kaya da kuma dressing mirror, ƙasan ɗakin amalale yake da wani red carpet me kyau, idanunta ne ya sauƙa akan wasu kyawawan ƴan mata guda biyu wanda ko wacce ke zaune akan gadonta, wayoyinsu ne ahannunsu da alama chatting sukeyi.
Gadon dayake shine na ƙarshe Matarnan ta nunawa Zieyaderh tare da nuna mata inda zata ajiye akwatinta,  saida matar me suna Mama Ladi  ta gwada mata komai sannan tabar cikin ɗakin, haɗa idanu Zieyaderh tayi da ɗaya daga cikin ƴan matan, murmushi tayi mata tare da cewa "Sannu" itama Zieyaderh'n murmushi tayi tare da ɗaga mata kai alaman yauwa.
Trolly ɗinta ta ajiye tare da warware mayafin dake jikinta, kasancewar lokacin sallan magriba ya gabato anata ƙiraye ƙirayen sallah hakan yasanya ta shiga bathroom tare da ɗauro alwala. tana fitowa ta buɗe trolly ɗinta tare da zaro hijab ta sanya,  ɗaya daga cikin ƴan matan da ta samu acikin ɗakin me suna Humaira ne ta miƙo mata sallaya, godiya tayi kana ta shimfuɗa ta gabatar da salla, ba ita tatashi akan sallayan ba sai da ta gabatar da sallan Isha, tana ninke sallayan, Mama Ladi tashigo cikin ɗakin hannunta ɗauke da basket wanda cikinsa ke ɗauke da food flask, da kuma plates guda uku,   dubanta takai ga Zieyaderh inda tace "Idan kinci abinci Hajiya tace ki sameta a falo"  "To" kawai tace tare da cire hijab ɗin dake jikinta. Humaira ce ta jawo basket ɗin gabanta tare da ɗaukan plates ɗin tashiga zuba haɗaɗɗiyar coconut rice dake ɗaya daga cikin food flask ɗin da aka kawo, dubanta takai ga ƴar uwarta mai suna Nina cikin kulawa tace "Hajiyar chatting zakici abinci ne?"
Hankalin Nina nakan waya batare da ta ɗago ba tace
"Aa sai zuwa anjima"
Baki Humaira ta taɓe tare da zuba abincin acikin plates biyu  kana ta ɗaura musu pepper chicken akan coconut rice ɗin, miƙowa Zieyaderh plate ɗaya tayi tare da cewa "Sister ga abinci kici,  sunana Humaira waccar kuma cousin ɗina ce sunanta Nina, ke kuma fa ya sunanki?"
Murmushi Zieyaderh tayi aranta tace "Nasmah two" afili kuwa cewa tayi "Zieyaderh"
"Nice name!" Humaira tafaɗa tana me komawa kan bed ɗinta ta zauna, Zieyaderh kuwa kasancewar ba wani yunwa takeji sosai ba hakan yasa bata wani ci abincin da yawa ba, mayafinta ta ɗauka ta fice don amsa ƙiran Hajiya Arabi, a falo tasamu Hajiya Arabi, wani yellow'n towel Hajiya Arabi ta bata tace tacire kayanta, wani ɗan ɗaki ta shiga ta cire kayan nata tare da ɗaura towel ɗin, kasancewar towel ɗin nada girma hakan yasa ya sauƙo har zuwa kan guiwanta, wani irin kunya takeji amma babu yanda zatayi dole haka ta fita, wani ɗaki suka shiga me girma wanda keta ƙamshin kayansu humra da dai sauran kayan gyaran jiki, kujera Hajiya Arabi ta nuna mata zama tayi akai tare da miƙe ƙafafunta, wani kwalba me ɗauke da wani irin farin ruwa Hajiya Arabi ta ɗauko daga cikin wani glass, ƙarasowa gaban Zieyaderh tayi tare da buɗe kwalban ruwan cikin kwalban wanda ke da masifaffen ƙamshi ta shiga shafawa Zieyaderh agaba ɗaya jikinta har zuwa kan cinyoyinta, bayan ta gama ne tace da Zieyaderh tashafa akan ƙirjinta da kuma cikinta, hakan kuwa akayi ganin idanun Hajiya Arabi ba akanta yake ba yasanya ta zame towel ɗin tashafa akan ƙirjinta har zuwa kan lafaffen cikinta, tana gamawa Hajiya Arabi takuma shafa mata wani ruwa saidai shi kalansa yellow ne saɓanin wancan dayake white, shima balaifi yana da ƙamshi sosai,  bayan tagama shafa mata yellow'n ruwan ta ɗauko wani abu dake cikin wani ɗan bowl kaman kwaɓaɓɓen dulka tashiga shafa mata saidai wannan karon harda fuskanta aka shafa,    wani cup dake cike da wani irin abu kamar zuma

Hajiya Arabi ta miƙowa Zieyaderh tare da cewa tatashi tsaye tashanye, cikin ɗari ɗari Zieyaderh takai cup ɗin bakinta, amaimakon taji ɗaci saitaji abun nada ɗan zaƙi hakan yasa ta rufe idanunta ta shanyesa tas, tana aje kofin Hajiya Arabi ta ƙara miƙo mata wani shima nasa kalan da ban saidai kuma shi yana da bauri bakamar wancan ba, shima rufe idanunta tayi ta shanye, still tana ajiye kofin Hajiya Arabi ta miƙo mata wani ɗan kwalba wanda cikinsa ke ɗauke da wani abu kamar zuma saidai shi danƙonsa yazarje na zuma, haka Hajiya Arabi ta dinga ɗura mata abubuwa wani yayi mata dadi wani kuwa akasin haka, saida wannan kwaɓaɓɓen dulkan yayi 1 hour ajikinta sannan Hajiya Arabi ta haɗa mata wani ruwan wanka wanda aka cika turaren wanka acikinsa, koda tayi wanka wani irin tashin ƙamshi jikinta keyi, bacci takeji sosai hakan yasa agajiye ta nufi ɗakin su, Nina nanan tana ta aikin chat, yayinda Humaira kuwa ke waya, wata riga marar nauyi tasanya tare da kwanciya luf akan gado, idanunta ta lumshe tare da sauƙe ajiyar zuciya, ahankali kalaman soyayyan da Humaira ke faɗawa wanda take waya dashi ke shiga kunnenta, wani irin abune taji ya daki zuciyarta take heart ɗinta yasoma beating da sauri, sake lumshe idanunta tayi kana ta cusa kanta cikin pillow da haka bacci ya ɗauketa.
Washe gari tun 7 tagama shiryawa, tun kafun tasanya komai acikinta Hajiya Arabi ta bata tatacciyar madaran shanu wanda babu ko ɗigon mix acikinta, kamar yanda ta faɗa mata tace kada tasha azaune, atsaye tashanye gaba ɗaya madaran sannan taɗanci soyayyen dankalin da aka kawo musu amatsayin break fast, bakwai da rabi daidai Kamalu driver yazo don kaita makaranta. Gaba ɗaya yau bata je ko ina ba koda suka fita break basuje ko ina ba acikin aji sukayi ciye ciyensu, su Nasmah sai tsokananta suke wai tafara ƙamshin amarci. Koda aka tashesu Kamalu driver ne yazo ya maidata gidan Hajiya Arabi, tana cire uniform tayi wanka ko abinci bata ciba Hajiya Arabi ta miƙo mata wani tsumi, saida tasha wasu haɗin magunguna kusan kala uku sannan taci abinci, kasancewar agajiye take hakan yasa ta kwanta tare da ɗaukan littafin Agric Science ɗinta tana karantawa kasancewar gobe zasuyi test, Nina ce tashigo cikin ɗakin gaba ɗaya jikinta sanye da dulka, kallon Zieyaderh tayi tare da cewa "Hajiya tace kije kina da baƙuwa"
"To" kawai tace kana ta sauƙo daga kan gadon, sosai taji daɗi ganin Oummu da tayi, da sauri ta ƙarasa tare da rusunawa agaban Oummu'n cikin girmamawa tace "Oummu barka da zuwa"
Murmushi Oummu tayi tare da cewa "Yauwa Zieyaderh ya kwanan baƙunta?"
"Alhamdulillah ta amsa tana murmushi.
Daidai lokacin Hajiya Arabi ta fito daga cikin ɗakin ta, nan tazauna suka ɗan taɓa hira da Oummu, koda Oummu tazo tafiya har bakin mota Zieyaderh ta rakata, nan Oummu ta buɗe jakarta tafito da kwalin waya ƙirar iphone 9 plus, miƙawa Zieyaderh tayi tare da cewa "Kiriƙe wannan akwai sim card aciki kuma nayi miki setting komai, zanna ƙiranki muna gaisawa, idan kina da buƙatar wani abuma ki sanar dani"
Amsan wayar tayi tare da yiwa Oummu godiya, nan Oummu ta ɗora da cewa "Naƙira shugaban makarantarku munyi magana, kasancewar lokacin da zaku fara exam zai kama lokacin biki, saboda haka nasanar masa komai yakumace ba matsala za'asa wata ɗaliba tayi miki, ki kwantar da hankalinki, idan kina da damuwa ki sanar dani kinji!" Oummu taƙare maganar cike da lallashi.
Murmushi Zieyaderh tayi tare da cewa "Nagode sosai Oummu"

Saida taga tafiyansu Oummu'n sannan takoma cikin gida, zama tayi akan gadonta tare da buɗe

kwalin wayar, dalleliyar iphone 9 plus grey colour ne ta bayyana acikin kwalin, yayinda aƙasan kwalin aka shumfuɗe fararen ƴan dubu dubu wanda aƙalla zasu kai 8k, murmushi kawai tayi tare da ciro wayan kana ta maida kwalin ta rufe tasan Oummu tayi hakane saboda tasan idan ta bata kuɗin bazata amsa ba. Kasancewar komai arubuce yake kuma yanzu kanta awaye yake hakan yasa ta kunna wayar tare dayin downloading games ɗin da zasu ɗebe mata kewa. Koda tayi sallan Isha wajen Hajiya Arabi ta nufa, yau kam gyaran da akayi mata har ya zarce najiya, sai kusan wajen 10 sannan tayi bacci.

Wasa wasa yau kwananta 4 agidan Hajiya Arabi wani irin gyaran jiki ake mata na mussaman, acikin ƴan kwanakin huɗun jikinta ya soma sauyawa fatarta taƙarayin smooth yayinda face ɗinta ke shining, acikin kwanki huɗunan kullum da safe tatacciyar madaran shanun take fara sha kafun tayi break fast, wasu irin haɗaɗɗun magungana Hajiya Arabi ke bata, wanda har ƙarfinsu ya soma taɓa ta, don ayanzu takan yawan jin kanta acikin wani irin yanayi,, ɓangaren su Oummu kuwa shirye shiryen biki suke sosai hidima suka shiryawa bikin ba ɗan kaɗan ba.

*Singapore*

Kwance yake akan tangamemen gadonsa yayinda gaba ɗaya jikinsa ke lulluɓe da blanket, ahankali ya buɗe kyawawan idanunsa wanda suka kaɗa sukai ja, hannunsa yasanya ya dafe kansa dake masa masifar ciwo, yau kwanansa uku kenan yana fama da wani irin zazzafan zazzaɓi, da zaran yayi tari kuwa saidai yaga jini ta bakinsa na fita, wani irin ciwo yakeji sosai ajikinsa, yau kwanansa uku banda ruwa baisa komai acikinsa ba, ahankali yaɗan tashi tare da jingina bayansa da saman gadon, rumtse idanunsa yayi tare sanya hannunsa ya riƙe saitin heart ɗinsa dake beating da sauri, Numfashi me ɗumi ya fesar, sai kuma ga tari ya biyo baya farin handkerchief yasanya yashiga goge jinin dake fita daga bakinsa, tsabar zafin zazzaɓin dake jikinsa har karkarwa laɓɓan bakinsa keyi, cikin dakiya ya zuro da ƙafafunsa ƙasa, ahankali ya sauƙo daga kan gadon, sanye yake da long jeans black colour, kasancewar baisanya riga ba hakan yasa murɗaɗɗun muscles and 6 packs ɗinsa suka bayyana, cikin dauriya tare da aro jarumta ya nufi toilet, agaban sink ya tsaya tare da kunna fanfo ya wanke bakinsa, lumshe idanunsa yayi tare da kifa kansa da jikin bango.

(am so sorry jia banyi update ba kuyi haƙuri Wallahi nashiga busy ne, zanbiyaku bashin najia gobe Insha Allah.)

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*WATTPAD*
@fatymasardauna
#romance

*Chapter 43*

Juyi take tayi akan ɗan madaidaicin gadon, yayinda gaba ɗaya nutsuwarta ke neman yin ƙaura daga gareta, ahankali take buɗe idanunta har ta sauƙesu akan Nina wacce ke zaune akan gado tana faman lumshe idanunta, wayarta ƙiran iphone ne kare akan kunnenta, waya takeyi me ratsa zucia, kasancewar ɗakin ya ɗauki shiru, sannan ta ƙure volume ɗin wayan, hakan yasanya gaba ɗaya maganan da akeyi mata acikin wayan yake fitowa fili, kalaman soyayya saurayin nata ke zazzaga mata, yayinda gaba ɗaya maganganun nasu ya ƙare akan maganan aurensu da kuma ɗokin burinsu nason kasancewa tare daya kusa cika.
Ahankali ta janye idanuwanta daga kan Nina tare da ɗaura hannunta akan maranta dake yi mata ciwo, kusan kwana biyu kenan tanajin mararta na ɗaurewa, gawani irin baƙon yanayi da takejin kanta aciki, idanunta ta sake lumshewa tana mejin daddaɗan ƙamshin jikinta na cakuɗa da numfashinta, ita kanta yanzu ƙamshin da takeyi na matuƙar yi mata daɗi, gefe guda kuwa ga skin ɗinta daya ƙara kyau yayi santsi da laushi, zuwa yanzu rabin rayuwarta cike take da kewa, wani irin son ganinsa takeyi, akullum gizo idanunta keyi mata na ganinshi, bata taɓa mantawa da kyakkyawar fuskarsa, kyawawan idanunsa masu ɗaukar hankali, harma da kyakkyawan nagartarsa, komai nasa me kyau ne, tanason komai daya dangance sa,, ahankali wasu siraran hawaye suka gangaro daga cikin idanunta, kana suka biyo ta gefen ƙuncinta, ajiyar zuciya ta sauƙe tare da fesar da wani irin numfashi, bata iya seccond 1 batare da ta tunasa acikin ranta ba, da tarin tunaninsa acikin rai da zuciyarta bacci ɓarawo ya sace ta..

Yau ta kama saura sati guda aurensu, sosai take shan gyara awajen Hajiya Arabi, zuwa yanzu idan kaga Zieyaderh sai kasha mamakin irin kyaun da tayi, fatarta tayi smooth yayinda duk wata halitta ta cikar ƴa mace dake jikinta suka sake ciccikowa, fatarta takoma milk colour wato kalan madara, ita kanta tasan ayanzu kyawunta ya ƙara bayyana, kuma ayanzune takejin kanta cikakkiyar mace.

Shirin biki ake sosai yayinda Oummu ta kashe maƙudan kuɗaɗe wajen sayawa amarya kayan da zata sanya alokacin biki, gaba ɗaya ahalin Oummu da Abba cike suke da farinciki saboda auren, kowa ka gani acikin Familyn burinsa shine yaga anyi auren lafiya.
***
Cike da masifa Inna Ma'u ke duban Malam Garba, cikin tsananin Mamaki tace.
"Kasan mekace kuwa? aure fa kake cewa zakayiwa Zieyaderh!"

Kallonta Malam Garba yayi cikin nutsuwa yace. "Ƙwarai Aure zanyi mata kuma saura kwanaki shida aɗaura mata aure inaso kisan da haka, yanzu ma na faɗa miki ne saboda karkice ban kyauta miki ba"

"Kam bala'i lallai Malam kacika butulu, yanzu ni Ma'u ni zakayi wa butulci? Har kasa auren

ƴarka ka kuma karɓi kuɗin auren ka cinye batare da sanina ba? to wallahi bazai taɓa yiwuwa ba!" Cikin tsananin masifa Inna Ma'u ta faɗi haka.
Cikin nutsuwa Malam Garba yace "Ki kwantar da hankalinki Ma'u, auren Zieyaderh babu fashi Insha Allah za ayishi, yanzuma burina shine na saida gona ta don na saya mata ƴan abubuwan buƙata kama daga kan kayan ɗaki dadai sauransu"

Cikin mamaki Inna Ma'u tace "Gonarka kuma? Lallai ma Malam, akan auren wannan gantalalliyar yarinyarne har zakace zaka saida gonarka, to bazai taɓa yiwuwa ba!"

Kallonta kawai Malam Garba yayi tare da yin shiru, don acikin abun da yayi niyya babu wani wanda zai fasa, dole zai sauƙe haƙƙin Zieyaderh dake kansa amatsayinsa na uba.

Ganin yaƙi kulata yasanya tasa masa kukan munafurci  tare da cewa.
"Nagode ae saboda banice na haifi Zieyaderh ba shiyasa kakemin haka"
Shidai har yanzu idanu kawai ya zuba mata, don sarai yasan kukan munafurci takeyi, don ahalinta babu wani abu ɗaya wanda baisani ba, ganin da tayi cewa yaƙi kulata ne yasanya tasake taso da wani sabon borin inda tashiga haɗa kayanta wai lallai sai dai ya kaita birni ayi bikin da'ita.
Shidai ƙala baice mata ba baikuma sa aransa cewa zaikaita ba don yasan zuwanta bazai zama alkhairi ba.
***
Oummu ce zaune akan gado tana ta faman har haɗa kayan ɗinkin Zieyaderh wanda aka kawo mata ɗazun, Abba ne ya turo ƙofar ɗakin ya shigo, Oummu naganinsa ta saki murmushi tare da ƙarasowa garesa, murmushin dake kan fuskar nata ne yaɗan gushe, ganin yanayin yanda fuskar Abba ta sauya, alamun akwai damuwa.
Cikin kulawa tare da ƙaunar mijin nata ta kamo hannayensa, haɗe da dubansa tace
"Lafiya kuwa?"

Ajiyar zuciya  Abba yayi tare da kamo hannun Oummu suka zauna akan gado,  dubanta yayi tare da cewa.
"Sulaimiyya ina jin kamar Sooraj ba lafiya yake ba!"
Gaban Oummu ne ya faɗi take ta waro idanunta cikin yanayi na damuwa tace.
"Wani abu ya sameshi ne?"

Ajiyar zuciya yakuma sauƙewa tare da cewa. " Shine abun da bansaniba, amma ki kwantar da hankalinki nasan babu wani abu daya sameshi, kawai dai  nine danakejin kamar bayacikin halin lafiya"
Cikin tsananin damuwa Oummu tace "Yace maka zaidawo ne?"
"Eh yace zai dawo jibi"
Ajiyar zuciya ta sauƙe tare da cewa.
"Allah yadawo dashi lafiya"  da "Ameen" Abba ya amsa kana yace da Oummu takawo masa ruwa yasha.

Yau yakama saura kwana huɗu biki inda yaune kuma su Zieyaderh suka fara zana jarabawarsu na first term, wanda kuma ita bata samu daman zuwa ba, saidai kamar yanda Oummu ta faɗa ansamo wata ɗaliba ta musamman tana zana mata jarrabawar.
Ɓangaren gyaran jikinta kuwa komai yana tafiya daidai, dok sosai gyaran da akayi mata ya bayyana ajikinta, duk inda ta zauna saita raba tsaraban ƙamshi, baƙaramin sauyi takeji ajikinta ba, lokaci ɗaya ta zama wata babbar yarinya kuma cikakkiyar mace.
Kayanta take haɗawa acikin trolly ɗinta, kasancewar yau zata koma gida don sun kammala duk wani gyare gyaren su, wasu ingantattun magunguna haɗi da turaruka Hajiya Arabi ta bata, sannan musamman ta bata wasu turaruka kala biyu tace kada tayi amfani dasu sai bayan anɗaura auren tana shafasu idan zata kwanta, godiya tayi mata sosai, kana tayiwa su Nina da kuma Humaira sallama, kasancewar su ba aranar zasu tafi ba sai washe gari, inda suɗinma dukansu aure zasuyi, exchenging phone number sukayi, daganan ta ɗauki trollynta tafice daga cikin ɗakin. Cikin nutsuwa tafito compound ɗin gidan tafiya takeyi me ɗaukar hankali yayinda take ta walwali tamkar wata tauraruwa.
duk atunaninta Kamalu ne zaizo ɗaukarta amma saitaga saɓanin haka don Almustapha ta tarar tsaye ajikin mota yana jiranta, tun fitowarta da yayi mata kallo ɗaya ya kau da kansa gefe, baƙaramin kyau da cika ta ƙara ba hakan yasa bazai iya jure kallonta ba, daddaɗan ƙamshin turarenta ne yafara kawowa hancinsa ziyara hakan ne yabashi daman gane cewa taƙaraso garesa, cikin zazzaƙan muryarta tace dashi.
"Ina wuni"
Kansa ya ɗago tare da sakin murmushi cikin kulawa yace "Lapia lau amaryata!"
Ƙasa ƙasa ta hararesa tare da murgaɗa masa baki, dariya kawai yayi kana ya karɓi jakan hannunta, gidan baya ya buɗe ya ajiye jakannata , zagayawa yayi yashiga ɓangaren driver ita kuma tashiga gefen me zaman banza, tafiya suke babu wanda yace da ɗan uwansa wani abu, gaba ɗaya hankalinta naga wayanta inda take chatting da Shukra wanda ketayi mata tsiya, shikuwa Almustapha gudu kawai yaketa shararawa akan babban titin, sosai ƙamshinta ke taɓasa hakanne ma yasanya yaketa sauri don yakaita gida, gudun kada daddaɗan ƙamshinta ya hautsina masa lissafi. Ababban haraban gidan yayi parking motar, kamar dama jira take da sauri ta buɗe murfin motar ta fita, trolly ɗinta ta ɗauka kana ta shige cikin gida. Mutane tasamu sosai acikin babban falon na Oummu, kasancewar sunyi nisa acikin hidiman da sukeyi yasanya saɗaf saɗaf ta haye sama, batare da kowa ya ganta ba, kaitsaye ɗakin Oummu ta nufa, da sallama ɗauke abakinta ta shiga cikin ɗakin nan ta iske Oummu da Aunty Muhibbat da kuma Aunty Laylerh, cike da girmamawa ta gaidasu, cikin so da ƙauna suka amsa mata, inda dukansu suka yaba da gyaran Hajiya Arabi don sosai Zieyaderh taƙara kyau, daga ɗakin Oummu ɗakinta ta wuce, nan ta rage kayan jikinta ta kwanta wayarta ta ɗauka ta shiga IG kasancewar yana ɗebe mata kewa sosai.

Washegari.
Yau takama thursday kuma yaune za'a gudanar da henna day, tun safe gidan yake ɗinke da ƴan uwan Oummu dana Abba, yayinda aka ɗauko ƙwararrun masu zanen lalle daga maiduguri wanda zasuyiwa Amarya Zieyaderh zanen lalle na musamman, su Nasmah da Shukra ma sunzo wanda bayan sungama zana exam ɗinsu na yau ɗinne suka biyo ta gidan, zuwansu yasanya damuwan da take ciki yaɗan gushe, don sun ɗebe mata kewa sosai, har kusan ƙarfe 3

na yammaci sannan aka gamawa Amarya Zieyaderh zanen lallenta wanda ya matuƙar yiwa fatarta kyau, kasancewarta fara sosai hakan yasa jan lallen ya kama farar fatar jikinta ya zauna raɗau har wani maroon colour yayi,   masha Allah Zieyaderh tazama tamkar wata sarauniya banda walwali ba abun da takeyi,  sai wajen ƙarfe 6 na yammaci sannan su Shukra suka soma shirin tafiya gida, Oummu da kanta tasanya Kamalu driver ya maida kowaccensu gida.

Friday.
 Tun ƙarfe 6 Aunty Muhibbat ta tasheta inda tanayin breakfast suka wuce shagon saloon, gyaran gashi akayi mata mai kyau, daganan wani ƙaton mall suka wuce, Aunty Muhibbat ne tayi sayayya sannan suka dawo gida, kasancewar yau da yamma ƙarfe 4 za a gudanar da walima. Tun ƙarfe 2 Bilkh tazo don shirya amarya,  kafun ƙarfe uku tuni Bilkh ta tsantsara mata kwalliya akan fuskarta,  Aunty Muhibbat da kanta ta shiryata cikin wani irin tsadadden lace mai kalan fari da ratsin sky blue, wanda yaji ɗinkin riga da sket 12 pieces, sosai lace ɗin ya amshi jikinta, wani haɗaɗɗen sky blue material sari Aunty Muhibbat ta naɗa mata akan kayan, wanda yaƙara bayyana kyawun kwalliyan nata, daga kan ɗan kunne zuwa dan ƙareren sarƙan dake wuyanta har izuwa awarwaro da zoben hannunta gaba ki ɗaya na gold ne, masha Allah Amarya Zieyaderh kam taji kyau harma tagaji da haɗuwa, kowa ya ganta sai yayi santin kyawun da tayi, haka Bilkh da Aunty Muhibbat suka dinga ɗaukarta hotuna, Bilkh kuwa har ma da vedio tayi mata ta ɗaura akan shafinta na Instagram.  Ƙarfe huɗu daidai aka soma ƙoƙarin tafiya da ita wajen walima, adai dai lokacin su Nasmah suka ƙaraso sun sha kyau ita da Shukra inda sukayi ado cikin wasu tsadaddun dogayen riguna masu kyau.   Tsala tsalan motoci aka tanada na musamman don zuwa walima, cikin wata haɗaɗɗiyar mota ƙiran ferarri aka sanya amarya ita da su Shukra tare da Aunty Muhibbat.  Ajere motocin da suka cimma guda talatin kebin dogon titin suna tafiya cikin nutsuwa ahaka har suka ƙarasa babban katafaren hall ɗin da za'a gudanar da waliman, Aunty Muhibbat da Shukra ne suka riƙo amarya aka shigo da ita cikin taron jama'an, nan fa kowa yafara ambatan masha Allah, don dayawansu basu san amaryar ba sai aranan, kowa ya yaba da tsananin kyawunta.
Walima aka gabatar mai rai da lafiya yayinda aka gudanar da wa'azi mai ratsa jiki da zuciya akan zaman aure, sosai wa'azin ya ratsa zuciyar Zieyaderh har batasan sanda hawaye suka fito daga cikin idanunta ba, wanda ita kanta batasan mene dalilin fitar hawayen ba, anci ansha sosai awajen waliman yayinda aka raba kyaututtuka, duk wanda yazo waliman sai da yasamu kyautar Sallaya da kuma al'ƙur'ani izu sittin,  bayan an kammala walima ne kuma aka shiga ɗaukan hoto,   abu dai yayi daɗi saidai ace masha.
 Tun ahanyar dawowansu gida wani irin zazzaɓi ya rufe Zieyaderh, wanda har saida Aunty Muhibbat ta lura da hakan,  koda suka koma gida Aunty Muhibbat da kanta ta haɗa mata ruwan wanka,  tana fitowa awanka ta zura wata riga marar nauyi, sallah tayi sannan ta kwanta bayan tasha maganin da Aunty Muhibbat takawo mata, lulluɓa tayi da blanket tare da matse jikinta waje ɗaya.

6:00 pm daidai jirginsu ya sauka ababban airport ɗin dake cikin garin abuja Nnmdi Azikwe International Airport.
Ahankali yake sauƙowa daga kan matattakalan jirgin, sanye yake  da white pencil  jeans and white t-shirt,  sai kuma wata jibgegiyar rigan sanyi daya ɗaura akan rigannasa wanda take da

kalan maroon,  white facing cap ne akansa wanda hakan yasanya ba a iya ganin fuskarsa sosai,   yana gama sauƙowa daga kan step ɗin cikin sauri Kamalu driver ya ƙaraso tare da karɓan ƴar ƙaraman jakan dake hannunsa, tare da yi masa sannu da dawowa..    Kaitsaye gidansa ya wuce, don bayason kowa yasan da dawowarsa,  yana shiga cikin tamfatsetsen ɗakinsa ya kashe wuta, tare da cire kayan jikinsa dogon wandonsa kawai ya bari, kwanciya yayi luf akan gadonsa tare da lulluɓa da blanket, awahalce yake maida numfashi yana me ƙara takure kansa waje ɗaya, sannu ahankali zafin zazzaɓin dake jikinsa ke ƙara hauhawa.

1:00 am daidai awannan lokacin cikin kaso 90 na mutane suna bacci, kasancewar dare yakasance mahutar bawa, saidai saɓanin haka ne yakasance daga ɓangarenta  don kuwa sam bacci yƙi zuwa idanunta awannan dare, kuka take ƙasa ƙasa hadda sheshsheƙa wanda hakan ya haifarmata da ciwon kai, zafin zazzaɓin jikintane ya ƙara hawa hakan yasa gaba ɗaya jikinta ya ɗauki masassara, kuka take sosai, wani irin faɗuwar gaba takeji na musamman idan ta tuna da cewa gobe za'a ɗaura mata aure, tanaji ajikinta tamkar wani abu zai faru da ita. Haka takwana acikin matsanancin zazzaɓi da ciwon kai sai wajen ƙarfe huɗu na asuba sannan tasamu bacci ɓarawo ya ɗauketa.

Wayewar garin yau yakasance rana ta musamman awajen ahalin Sooraj don kuwa yau tun safe suke cike da farin ciki, yayinda gidan kota ina ke cike  da ƴan uwa da kuma abokan arziki. Ƙarfe takwas daidai tasoma yunƙurin buɗe gajiyayyun idanunta ahankali, har yanzu akwai zazzaɓi ajikinta, cikin dauriya ta jingina bayanta da saman gadon tare da rumtse idanunta, Aunty Muhibbat ce taturo ƙofar ɗakin  tashigo, ganin Zieyaderh'n da tayi azaune yasa ta ƙaraso da sauri cikeda kulawa tace.
 "Kintashi ya jikin naki?"

"Da sauƙi!" tafaɗa asanyaye tana me karyar da kanta gefe,   Hannu Aunty Muhibbat takai ta taɓa wuyanta, zafi zau taji hakan yasa tace "Subahanallahi har yanzu zazzaɓin bai sauƙa ba, muje kiyi wanka sai kiyi break kisha magani!"
Da taimakon Aunty Muhibbat ta sauƙo daga kan gadon, har toilet Aunty Muhibbat ta kaita tare da haɗa mata ruwan wanka.

9:30 am tuni ƙofar gidan ya ɗinke da mutane manya manyan ƴan siyasa da masu muƙami harma da masu sarauta da ƴan kasuwa, kowa kagani fuskarsa ɗauke take da murmushi, Abba wanda yake cikin tawagarsa kallo ɗaya zakayi masa kafahimci cewa yana cikin farinciki,  can na hango Almustapha wanda yasha ado cikin wata blue ɗin shadda riga da wando tare da babban riga, sosai yayi kyau shima fuskarsa ƙunshe take da murmushi, duk bayan minti ɗaya yake kai dubansa zuwa ga agogon dake ɗaure a tsintsiyar hannunsa.

Cikin tsananin damuwa Mas'oud ke kallon SOORAJ wanda ke zaune agaban dressing mirror yana shafawa jikinsa mai, zallan damuwa Mas'oud ya hango kwance akan fuskar Sooraj, ajiyar zuciya ya sauƙe tare da duban agogon dake ɗaure a tsintsiyar hannunsa 9:40 cikin ɗan zaƙuwa yace "9:40 fa RAJ kayi sauri kada mu makara"
Harara Sooraj ya watsa masa tare da cewa "Bayan ka matsamin akan cewa saina bika yanzu

kuma mene zaka dameni"
Murmushi kawai Mas'oud yayi tare da cewa "Naji koma me kayi sauri."
Baki Sooraj ya buɗe daniyar yin magana sai kuma tari ya sarƙesa da sauri yasanya handkerchief ya toshe bakinsa gudun kada Mas'oud ya ji sautin tarin har ya lura da jinin dake fita daga bakinsa,  ganin kamar hankalin Mas'oud baya garesa hakan yasa ya goge bakinsa tare da komawa toilet ya wanke bakinsa, da kallo kawai Mas'oud ya bisa don yaga sanda Sooraj yayi saurin goge jinin dake fita a bakinsa, yanasane yayi kamar baigani ba, wani irin tausayin abokinnasa ne yasake lulluɓe zuciyarsa.
Cikin dauriya da danne ciwon dayakeji yasanya tsadaddiyar shaddan da Mas'oud ya kawo masa, riga da wando ne ɗinkin half jumper, sai kuma gare wanda yasha aiki sosai,  yana gama sanya kayan ya zura baƙaƙen takalmansa na kamfanin gucci aƙafansa wanda suke da matuƙar tsada,  hulansa mai ratsin white and blue yasanya, kasancewar shaddan jikinsa white ce aikinta kuma ya kasance blue, sosai da sosai yayi kyau, yayinda gold wrist watch ɗinsa keta shinning yana ɗauke ido, baƙaramin kyau Sooraj yayi ba, duk da cewa ciwon dake cinsa arai yaɗan bayyana rama kaɗan ajikinsa, saidai kuma ya ƙara fari sosai, sannan kuma ƙawataccen sajen dake kwance akan fuskarsa ya ƙara kwantawa luf akan fuskarsa, Mas'oud da kansa saida ya yaba irin kyawun da Sooraj yayi,  wayoyinsa ya ɗauka ya zuba acikin aljihun rigarsa, batare dayacewa Mas'oud ƙalaba ya murɗa handle ɗin ƙofar ya fita. Ganin haka yasanya Mas'oud  rufa masa baya.
Cikin wata haɗaɗɗiyar motar SOORAJ ƙiran Buggati suka nufi unguwar Maitama inda anan za'a ɗaura auren.

Haɗaɗɗiyar motartasu ce ta ƙaraso ƙofar gidan yayinda ta ratsa cikin yawan jama'an dake cike a wajen, Mas'oud ne ya fara buɗe murfin motar ya fita, yayinda Kamalu wanda shike driving motar ya zagayo da sauri ya buɗewa Sooraj ƙofar motar, yana fitowa kallo ya dawo kansa domin sosai yayi kyau.  Sam baidamu da kallon da jama'an wajen keyi masa ba,  yanufi inda Abbansa yake, kan wata lallausan darduma ya zauna, fuskarsa ɗauke da mamaki yake bin ƴan tsirarun abokansa da yagani awajen da kallo,  Mas'oud ne ya zauna akusa dashi tare da dafashi, ɗago da kansa yayi ya kalli Mas'oud, murmushi Mas'oud yayi masa tare da kashe masa ido, sanin iskancin Mas'oud nada yawa yasanyashi kawar da kansa gefe, yanayin hayaniyan da akeyi awajen yasanya har aka gama ɗaurin auren baisani ba, wayarsa dake ta faman ruri ya ciro daga aljihunsa, baikai gayin picking call ɗinba yaji ana shelan cewa an ɗaura auren *SOORAJ MANSOOR MAINASARA da Amaryarsa ZIEYADERH ABUBAKAR* akan sadaki naira dubu ɗari.
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

Sooraj !!!
Written By
Phatymasardauna
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*WATTPAD*
@fatymasardauna
#romance

*Chapter 44*

Ahankali ta buɗe idanunta da sukayi mata matuƙar nauyi ta sauƙesu akan Aunty Muhibbat.
Cikin tsananin kulawa Aunty Muhibbat tace "Sannu Zieyaderh tashi kisa kaya sai muje asibiti ko, naji jikin naki yayi zafi sosai!"
Oummu ce tashigo cikin ɗakin fuskarta ɗauke da damuwa, ƙarasowa gaban gadon da Zieyaderh'n ke kwance tayi cike da tausayin Zieyaderh'n tasanya hannunta ta taɓa wuyanta, jin zafi zau ajikinta, yasanya Oummu cikin damuwa sosai tace "Muhibbat sanya mata kaya naƙira Dr.Bashir yana hanya!"

"To" kawai Aunty Muhibbat tace tare da ɗauko wani lallausan arebian gown wanda aka tsara ado me ɗaukar hankali ajikinsa, miƙawa Zieyaderh rigan tayi tare da cewa ta sanya, cikin ɗan kuzarin daya rage mata tasanya rigan wanda yabi gaba ɗaya surar jikinta ya lafe, komawa tayi ta kwanta tana me maida numfashi ahankali, jin kanta take kamar zai rabe biyu.
Blanket Aunty Muhibbat ta rufa mata, inda tabi bayan Oummu suka fice daga cikin ɗakin.

Wani irin shock ne yaji ya kama gaba ɗaya illahirin jikinsa, take yaji komai ya tsaya masa cak, yayinda maganan maroƙin ke ƙara yawo acikin kunnuwansa yana me hautsina ƙwaƙwalwa da tunaninsa, dummmm haka yaji acikin kunnuwansa yayinda yaji tamkar an buga masa guduma atsakar kansa, tunani gami da nutsuwarsa ne suka ɗauke gaba ɗaya, haka yazama tamkar wani statue, cikin tsananin farinciki da jin daɗi Mas'oud ya dafa kafaɗunsa tare da cewa.
"Ina matuƙar tayaka murna da farincikin samun Zieyaderh amatsayin mata, Allah ya tayaka riƙo!" Mas'oud ya faɗi maganar yana me ɗan bubbuga kafaɗan SOORAJ wanda har yanzu ya kasa ƙyafta koda idanunsa ne, fuska ɗauke da tsananin farinciki Almustapha ya ƙaraso inda Sooraj din ke zaune, hug ya basa tare da cewa.
"Happy Married life my brother, am very happy to day!"
Sai alokacin Sooraj ya motsa idanunsa inda yakeyiwa Almustapha wani irin kallo me ɗauke da tarin tambayoyi haɗi da ma'anoni daban daban.
Ƴan tsirarun abokansa da suka samu daman halartar ɗaurin auren ne suka ƙaraso inda yake, kowanne daga cikinsu bakinsa ɗauke da fatan alkhairi, shidai SOORAJ tamkar wani gunki haka yake binsu da idanu, wani irin gumi ne ke tsatstsafowa ta goshinsa, lokaci guda jikinsa ya soma karkarwa tamkar wanda aka watsawa ruwan sanyi, lura da hakanne yasanya Mas'oud kamo hannunsa suka fice daga cikin taron jama'an dake wajen, kai tsaye mota Mas'oud ya nufa dashi inda ya buɗe gidan baya ya tura Sooraj ɗin aciki kana yamaida murfin ya rufe.

Da ƙarfi ya rumtse idanunsa yana mejin zuciyarsa na bugawa da ƙarfi kamar zata faso ƙirjinshi, wani irin sarawa kansa keyi, yayinda numfashinsa ke seizing yana me ƙoƙarin ɗaukewa, hannunsa yakai kan ƙirjinsa dake masa wani irin ƙuna, idanunsa ne suka kaɗa sukai jajur, da ƙyar ya iya haɗiye wani yawu me ɗaci wanda ya tsaya amaƙoshinsa,  jiyake kamar ana watsa masa ruwan zafi akan fatarsa, yanajin kamar yata kurma ihu ko zai samu nutsuwa da salama acikin zuciyarsa,  jingina bayansa yayi da jikin kujeran motar tare da cije laɓɓansa, idanunsa da suka kaɗa sukai ja kamar  garwashin wuta ya lumshe tare da sanya hannuwansa duka biyu ya toshe kunnuwansa dake ta faman amsa masa amo.

Cikin mintunan  da basu wuce 20 ba Dr.Basheer yasamu daman ƙarasowa cikin gidan, kai tsaye Aunty Muhibbat ce tayi masa jagora zuwa ɗakin Zieyaderh, saboda Oummu na fama da jama'arta.
Akan bedsite Dr.Bashir ya zauna tare da ciro kayan aikinsa ya soma kwada yanayin jikinnata, yana kammalawa ya haɗa wasu allurai guda biyu wanda zaiyi mata, drip ya shiga ƙoƙarin ɗaura mata  don ya lura sosai take buƙatan ruwa,   ganin manyan alluran dayake ƙoƙarin yi mata ne yasanya ta rumtse idanunta, cikin fitar hayyaci tare da sambatu irin na zafin zazzaɓi daya sauƙar mata lokaci guda tace.  "Banason Allura, wayyo Yaya kazo kafaɗa masa banason allura, banason komai kai kawai nakeso!"
Baki buɗe Aunty Muhibbat ta kalli Dr.Bashir,
murmushi Dr.Bashir yayi mata tare da girgiza kansa cikin nutsuwa yace.  "Karki damu zafin zazzaɓi ne yasanyata haka amma nanda 1 hour insha Allah zata ji sauƙi!"
Kuka Zieyaderh keyi sosai haka Dr.Bashir yayi mata allura, har ya gama yi mata alluran kuwa bata daina kuka ba,   tun baigama haɗa kayan aikinsa ba wani irin fitinannen bacci ya soma fusgar ta,  kasancewar manyan allurai yayi mata masu ƙarfi hakan yasa dole zasu sata bacci, lumshe idanunta wanda sukayi luhu luhu tayi, gaba ɗaya yanayin idanunnata sun sauya, yayinda suka koma kamar na wata wacce ke cikin tsananin maye.
Wata farar takarda Dr.Bashir yabawa Aunty Muhibbat inda yace anemamata magungunan idan tatashi sai abata tasha insha Allah Zata warke, godiya Aunty Muhibbat tayi masa inda daganan yayi musu sallama ya tafi, mintuna 5 kacal da tafiyan Dr.Bashir nannauyan bacci ya ɗauki Zieyaderh, ganin haka yasa Aunty Muhibbat gyara mata kwanciya tare da rufa mata blanket, rage mata gusun a.c tayi  kana ta jawo mata ƙofar ɗakin  ta fice,   koda ta gayawa Oummu yanda sukayi da Dr.Bashir ƙiran Almustapha Oummu tayi tabashi takardan tare da gaya masa halin da Zieyaderh'n ke ciki.
Idanu Almustapha ya zaro waje cikin damuwa yace "Badai aurenta da SOORAJ ne matsalan ba?"

Kai Oummu ta girgiza masa tare da cewa "Bashi bane, don har yanzun bata sani ba, tunjiya dai take fama da zazzaɓin"

Ajiyar zuciya ya sauƙe tare da cewa.
"Allah ya bata lafiya"
Da  "Ameen" su duka suka amsa kana ya fice don siyawa Zieyaderh magani.

Acan  waje kuwa sannu ahankali jama'a keta watsewa inda kowa ke kama gabansa, Alhaji Mansur ne ya dubi Malam Garba wanda yazo ɗaurin auren dashi da ƴan tsirarun abokansa, cikin kulawa yayi musu iso zuwa cikin katafaren falonsa, shidai Malam Garba gaba ɗaya jinsa yake wani iri, burinsa shine yayi ido huɗu da angon ƴartasa don ya damƙa masa amanarta, saidai kuma yawan jama'an dake wajen yasanya sam baiga angon ba yadaiji wasu nacewa angon yanacikin mota amma dai bai ganshi ba.

Mas'oud ne ya buɗe murfin motar ya shigo, saidai ba inda Sooraj ke zaune yashiga ba ɓangaren driver ya shiga tare da yiwa motar key,    tunda ya sunkuyar da kansa ƙasa bai ɗagoba harkawo yanzu da suka kawo cikin katafaren gidannasa. Mas'oud na gama daidaita parking motar ya juyo da kallonsa ga Sooraj  baikai ga cewa Komai ba,  Sooraj ya buɗe murfin motar ya fita, sam bayako iya ganin gabansa da kyau hakan yasa yake ta gauraya hanya tamkar wanda ke cikin maye, kamar kububuwa haka ya wuce zuwa ɗakinsa dake sama, yana shiga yasoma kiciniyar cire babban rigan dake jikinsa, ƙarasawa gaban tangamemen glass mirror ɗin dake cikin ɗakin yayi, duban kansa da yayi acikin mirror ɗinne yasanyashi jin wani irin ɗaci amaƙoshinsa, cikin wani irin zafin nama haɗi da ƙunci, damuwa, da takaici yasanya hannunsa ya daki mirror'n, take mirror'n ya tarwatse, yayinda hannunsa kuwa yashiga zub da jini,  cikin wani irin tururin ɓacin rai dake damunsa yasanya hannunsa gaba ɗaya yayi watsi da gaba ɗaya kayan shafan dake jere reras agaban mirror'n, wani irin ƙara yasanya tare da soma buga kansa ajikin bango, daidai lokacin Mas'oud ya ƙaraso cikin ɗakin,  ganin abun da Sooraj ɗin ke aikatawa, sannan ga kuma hannunsa dake zubar da jini,  yasanya Mas'oud ƙarasowa cikin ɗakin da sauri, cikin tsananin tashin hankali yace.
"Sooraj ka......"

"Shut up Mas'oud!!!" Sooraj yafaɗa atsawace wanda har saida Mas'oud yaɗan tsorata, cikin tsananin ɓacin ran dake cinsa azuciya yace.
"Mekuka aikata kenan Mas'oud? Nace me kuka aikata!!" Kunsan abun da kukayi kuwa?" Azafafe ya shaƙe wuyan rigar Mas'oud cikin wata irin murya me amo, wanda tunda Mas'oud ɗin yake baisan cewa Sooraj  na da'ita ba yace.
  "Why do you do this to me? mehakan da kukayi yake nufi? You already know my problem Mas'oud!  you know dat i am not a complete man, meyasa kuka zaɓi cutar da ita? bazan zauna da ita ba Mas'oud! bazan Zauna da ita ba!!"
Gaba ɗaya cikin ficewar hayyaci SOORAJ ke faɗan maganganun.
Tsananin damuwa ne ya bayyana akan fuskar Mas'oud cikin son kwantarwa da Sooraj  hankali yace.
"Kadawo cikin hankalinka Sooraj, kai musulmi ne kasan ƙaddara kuma tana iya sauyawa ako da yaushe, sannan kyakkyawa takan iya zama mummuna,  mummuna kuma takan iya zama kyakkyawa, dan Allah Sooraj kada ka aikata abun da zuciyarka ke shirya maka,  nasan matsalanka Sooraj nasani amma nasan bazaka taɓa tabbata ahaka ba, nayarda dacewa wannan auren rufin asirine agareka dan Allah RAJ ka tausashi zuciyarka, kadawo cikin nutsuwarka!"
Mas'oud ya faɗi haka idanunsa cike tab da  ƙwalla, tabbas ya hango tsananin damuwa da

tashin hankali akan fuskar SOORAJ, amma basu da wani zaɓi, tunda Allah ya riga da yayi nasa.

Iska SOORAj ya fesar ta bakinsa tare da rumtse jajayen idanunsa, wani irin azababben ciwon kai yakeji, yayinda yakejin gaba ɗaya duniyar na juya masa,   ahankali ya taka tare da ƙarasawa gaban bedsite ɗinsa, cikin zaƙuwa ya buɗe drawer'n  bedsite ɗin, wata kwalba ya ciro wanda cikinta ke ɗauke da magani,  cikin rufewar ido ya ɓalle  murfin kwalban tare da kafa bakin kwalban acikin nasa bakin,  arazane Mas'oud yayo kansa daniyar hanasa shan maganin, amma kafun yaƙaraso tuni Sooraj ya shanye maganin tas, cikin zafin nama Mas'oud ya ƙwace kwalban maganin daga hannun Sooraj cikin nuna damuwa yace.
"Please calm down RAJ, dan Allah ka nutsu kada kayiwa kanka illa!"

Kan gado ya faɗa tare da rumtse idanunsa, jiyake kamar zuciyarsa zata fashe, wasu baƙin abubuwane ke ziyartan tunaninsa,   akusa dashi Mas'oud ya zauna tare da sanya hannayensa ya rufe fuskarsa, sosai damuwar abokinnasa ke damunsa, musamman yau da yaga gaba ɗaya RAJ ɗin ya fita a hayyacinsa, sai yakeji inama da ba'a haɗa baki dashi wajen ɓoyewa SOORAJ auren ba.
Tarin da Sooraj ɗin keyine yasanya Mas'oud juyowa ya kallesa, wani irin guda gudan jini dayaga yana fita abakin Sooraj ɗinne yasanyashi zaro idanunsa cikin tsananin kaɗuwa yace.
"RAJ dan Allah kada kayiwa kanka illa!"
Wani farin handkerchief yasanya ya goge jinin dake  fita abakin sa, cikin ƙarfin hali ya sauƙo daga kan gadon,  toilet ya nufa yana shiga ya wanke bakinsa tare da watsawa fuskarsa ruwa, wani irin dishi dishi yake gani yayinda  jiri ke neman kadashi, adaddafe yafito daga toilet ɗin, zuwa lokacin  baya  ko iya ganin gabansa, hayyacinsa ne ke neman barin jikinsa, kan gadonsa ya faɗa, lokaci guda idanunsa suka rufe ruf..

Ganin haka yasanya Mas'oud lulluɓa masa blanket, wayarsa ya ciro ya dannawa Dr.Waleey likitan Sooraj ɗin ƙira, bayanin komai yayi masa, nan Dr.Waleey yace gashinan zuwa, mintuna kaɗan saiga  Dr.Waleey  yaƙaraso gidan, duƙufa yayi sosai akan Sooraj ɗin wajen gano matsalarsa,  ganin cewa maganin da Sooraj ɗin yasha yana da illa sosai ne yasanyashi yi masa wata allura wanda zata sauƙaƙawa jikinsa wajen gusar da duk wata wahala,
  kallon Mas'oud Dr.Waleey yayi cikin kulawa yace.
" Wani abu ya ɓata masa rai ne?"
Ajiyar zuciya Mas'oud yayi tare da jinjina kansa alamar.
"Eh"

Cikin tausayawa Dr.Waleey yace.
"Ciwonsa yayi worse yakamata kuna kiyaye ɓacin rai ko wani abu da zai na taɓa zuciyarsa, sannan yana da buƙatar kulawa ta musamman"
ajiyar zuciya ya sauƙe haɗe da cigaba da cewa.
"Ina tsananin tausayin Sooraj Mas'oud, saboda Allah ya haɗasa da ƙaddarori masu girma, saidai ina masa fatan samun sauƙi akoda yaushe"
Wasu magunguna ya ciro daga cikin jakarsa kana ya miƙawa Mas'oud, cikin kulawa yace. "Idan

yatashi katabbatar yasha waƴannan magungunan zasu taimaka sosai!"
Kai Mas'oud ya jinjina tare da yiwa Dr.Waleey godiya daga haka sukayi sallama, zama Mas'oud yayi akan wata lallausan kujera dake cikin ɗakin tare da kai dubansa ga Sooraj wanda ke kwance kamar gawa, wani irin hawayene suka cika idanun Mas'oud har suka samu daman gangarowa, bayansa ya jingina da jikin kujera tare da lumshe idanunsa.

Ahankali idanunta ke buɗewa harta gama waresu tas, tashi zaune tayi tare da kai dubanta ga cannula'n dake ɗaure a tsintsiyar hannunta, bayanta ta jingina da jikin gadon da take kwance, ahankali hayaniyan jama'an da suka cika gidan ke ratsawa cikin kunnuwanta, sake lumshe idanunta tayi yayinda wasu siraran hawaye suka samu daman gangarowa daga cikin idanunta, hannunta takai ta dafe saitin zuciyarta dakeyi mata zafi, daidai lokacin aka turo ƙofar ɗakin nata, da sauri tasanya bayan hannunta ta share hawayen nata,
Oummu da Aunty Laylerh ne suka shigo cikin ɗakin, ganinta azaune yasanya murmushi bayyana akan fuskarsu,
cike da kulawa Oummu tace "Sannu Zieyaderh kintashi ya jikin?"
Cikin sassanyar muryarta wacce ke ɗauke da zallan damuwa tace "Da sauƙi!"
Aunty Laylerh ne ta zauna akan gadon tare da ɗan taɓa jikin Zieyaderh'n cikin kulawa tace "Masha Allah zafin jikin ya sauƙa, yanzu me kikeji ajikin naki?"

Ita kanta bazata iya tantance me takejiba saboda ciwon ba ajikinta yake ba azuciyarta yake, rashin sanin abun da zatace yasanya kawai ta nuna kanta, cikin kulawa Aunty Laylerh tace "Sannu ko"
Duban Oummu tayi tare da cewa, takawowa Zieyaderh'n tea me kauri da abinci idan taci sai tasha magani, hakan kuwa akayi Oummu da kanta ta haɗa mata tea da kuma pepper chicken, Aunty Laylerh da kanta tasanya Zieyaderh agaba akan cewa lalle dole sai tasha tea din, duk da cewa batajin daɗin bakinta haka dole ta daure taɗansha tea ɗin kaɗan, koda ta nuna ta ƙoshi Aunty Laylerh da kanta tashiga bata naman abaki, da ƙyar ta iya cin kaɗan ta kauda kanta gefe alaman ta ƙoshi,

shigowar Aunty Muhibbat cikin ɗakinne yasanya Aunty Laylerh cewa takai Zieyaderh'n tasakeyin wanka daganan sai a shiryata tunda dai sunga jikinnata daɗan sauƙi, wani irin ingantaccen ruwa wanda yaji haɗaɗɗen turaren wanka Aunty Muhibbat ta haɗa mata, ahankali take takawa saboda gaba ɗaya jikinta ba ƙarfi, toilet ɗin ta shiga tare da zare rigar jikinta, dayake ruwan nada ɗan ɗumi hakan yasa ta kwanta lif acikinsa, wani irin ajiyar zuciya ta sauƙe tana mejin wani sabon yanayi nashiga jikinta, cikin rashin kuzari haɗi da kasala tayi wankan inda gaba ɗaya jikinta yasake gaurayewa da daddaɗan ƙamshi, alwalan sallan Azahar tayi kana fito daga cikin toilet ɗin, cikin ɗan kuzarin daya rage mata yayi sallah inda Oummu ta taturo Bilkh don ta gyarata. Kasancewar bata wani jin daɗi yasanya Bilkh yi mata light meckup, hakan kuwa baƙaramin fito da kyawunta yayi ba, wani haɗaɗɗen lace wanda yaji ɗinkin doguwar riga fitted gown tasanya, sosai leshin ya amshi jikinta kasancewar lace ɗin nada kalan ja, hakan yasa Bilkh ta naɗa mata ƙaton white vail ajikinta mai adon jan duwatsu, sosai tayi kyau, saidai ƴar rama kaɗan data bayyana ajikinta, yanayin yanda bilkh ta naɗa mata mayafinne yasanya yaɗan rufe rabin fuskarta kaɗan, Aunty Muhibbat ce tariƙota suka fice daga cikin ɗakin,

kaitsaye ɗakin Oummu suka nufa,  Oummu ce ita kaɗai zaune akan gado, akusa da ƙafan Oummu Aunty Muhibbat ta ajiyeta kana ta juya ta fice daga cikin ɗakin,   cikin nutsuwa Oummu ta ɗago Zieyaderh kana ta kawota kusa da ita, cikin tsananin kulawa tace.
"Cikar mutumcin ko wacce ƴa mace shine aure, haka kuma duk wata ƴa mace tana sanin ƙima da darajar kanta ne aduk lokacin da tayi aure, kamar yanda kika sani yau anɗaura miki aure saboda haka  kin tashi daga sunan budurwa kin zama matar aure" ɗan numfasawa Oummu tayi tare da kamo hannuwan Zieyaderh cike da tausayawa tace
"Kigafarceni Zieyaderh, haƙiƙa ban aikata haka daniyar son zuciya ba, nayi hakane saboda inganta rayuwarku ku duka biyun, nakumayi hakanne amatsayina na uwa mai son cigaban ƴaƴanta,  bansan yazakiji ba amma yazama dole na faɗa miki"  sake hannun Zieyaderh'n tayi tare da sanya hannu ta ɗan ɗage mayafin dake kan Zieyaderh'n,  hakan yasanya Zieyaderh taɗan ɗago ta kalleta, cikin kulawa Oummu tace.

"Anɗaura aurenki yau saidai kuma bada Almustapha aka ɗaura ba, kamar yanda kike tunani, nasan zakiji abun wani iri amma ƙaddara ta riga fata!"

Ɗago idanunta dake cike da mamaki tayi ta kalli Oummu,  hannunta Oummu tasake kamawa cikin son kwantar mata da hankali tace
"Ƙwarai bada Almustapha aka ɗaura miki aure ba, dan Allah Zieyaderh kiyi haƙuri ki karɓi wannan ƙaddaran!"

Kan Zieyaderh ne ya ɗaure sosai don sam takasa fahimtan inda kalaman Oummu suka dosa, cikin sarƙewar murya tace "Oummu Nayarda da ƙaddara me kyau da kuma akasinta"
Ajiyar zuciya Oummu ta sauƙe tare da dafa shoulder ɗinta,  cikin rauni tace
"Yana da buƙatarki acikin rayuwarsa, haƙiƙa nasan SOORAJ yana da damuwa yana kuma da buƙatar mai magance masa wannan damuwan,  kiyi haƙuri ki karɓeshi amatsayin mijinki!"
Azabure Zieyaderh ta matsa baya tare da zaro idanunta cikin wani irin kaɗuwa ta soma jijjiga kanta yayinda gaba ɗaya jikinta ya ɗauki rawa, jin sauƙan kalaman Oummun tayi tamkar sauƙan  aradu acikin kunnuwanta,  ganin yanda ta firgice yasanya Oummu kamo hannuwanta cikin sanyin murya tace "Nasan zakiji ba daɗi, sannan nasan bamu kyauta miki ba amma ya zamuyi ki ɗauka wannan tsarin Allah ne bana muba, dan Allah Zieyaderh ki riƙi aurennan amatsayin ƙaddaranki"
tuni idanun Oummu sun cicciko da ƙwalla.   Rungume Oummu Zieyaderh tayi tare da sakin wani irin fitinannen kuka, kuka sosai takeyi yayinda gaba ɗaya jikinta ke karkarawa, jin Oummun takeyi kamar uwa mahaifiya agareta, cikin kuka  tace "Kidaina roƙona Oummu ke uwace agareni kodawa kika haɗani bazan gujeba, bazan bijiremiki ba Oummu bazan taɓa gujewa hukuncinki agareni ba!!"
ta faɗi maganar tana me sakin sheshheƙan kuka, wasu irin hawayene suka sauƙo daga cikin idanun Oummu tabbas saiyanzu taƙara tabbatar da cewa batayiwa ɗan nata zaɓen tumun dare ba, wani irin ƙwarin guiwa da farincikin samun Zieyaderh amatsayi suruka da tayi tasanya hannunta akan bayan Zieyaderh dake kuka ahankali take shafa mata bayannata tare da cewa.
"Nagode sosai Zieyaderh Allah yayi miki albarka!"
Zaunar da Zieyaderh'n tayi akan gadonta tare da soma ƙoƙarin share mata hawayen dake

gudana akan fuskarta, cikin so da ƙaunarta tace "Ya isa haka kwanta ki huta kada ciwon kai ya kama ki!"  a irin halin da take ciki batajin zata iyayiwa Oummu musu,luf ta kwanta akan gadon Oummu'n tare da cusa kanta acikin pillow, Oummu ce tafita aɗakin don amsa ƙiran wayan da akeyi mata, tanajin ficewar Oummu aɗakin tasaki wani sabon kuka mai tsuma zuciya kuka takeyi sosai wanda har saida numfashinta yasoma ƙoƙarin ɗaukewa,   gaba ɗaya tunani da nutsuwa sun gudu daga gareta, jin motsin kamar za a bude ƙofar ɗakin ne yasanyata haɗiye kukanta tare da rufe idanunta, yanayin yanda zuciyarta ke bugawa yasanya ta sake cusa kanta acikin pillow'n, ajiyar zuciya da numfashi take ta sauƙewa ahankali, cikin ɗan ƙanƙanin lokaci bacci ɓarawo yayi gaba da ita.

Tunda ya kwanta bai tashiba sai ƙarfe 4, da wani irin zazzafan zazzaɓi ya buɗe idanunsa yayinda yakejin gaba ɗaya komai na duniya bayayi masa daɗi, lumshe rinannun jajayen idanunsa yayi tare da ɗan yunƙurawa, cikin ɗan kuzarin daya rage masa ya zuro da ƙafafunsa ƙasa,   koda ya miƙe tsaye wani luuuu haka yaji  tamkar wanda zai faɗi, adaddafe ya nufi bathroom ɗinsa. Shower ya kunna tare da sanya hannunsa gaba ɗaya ya dafe bango, lumshe idanunsa yayi tare da sakin ajiyar zuciya, sauƙan ruwan shower ɗin akansa ba ƙaramin nutsuwa ya samar masa ba,  sake gyara tsayuwarsa yayi still hannayensa dafe da bango ya lumshe kwawawan idanunsa, sannu ahankali komai ke dawowa cikin ƙwaƙwalwarsa, sai yanzu yakejin nutsuwar yin tunani,   wani irin saliva me ɗaci ya haɗiya amaƙoshinsa,   tabbas ƘADDARA tayi masa sauyi irin wanda bai zata ba, kusan minti 20 ya ɗauka agaban shower'n ruwa na dukan pure skin ɗinsa, jikinsa ya janye kana ya kashe shower'n, gaban sink ya ƙarasa tare da ɗauro alwala.
Cikin wani tsadadden getzner blue colour ya shirya kansa, wanda yaji ɗinkin half jumper,  sosai kayan sukayiwa jikinsa kyau,  sallaya ya shumfuɗa inda ya gabatar da sallan La'asar, wanda baisamu daman yiba sakamakon bacci da yake.  Wayoyinsa ya tura acikin aljihun wandonsa, ɗan jim yayi tare da jingina bayansa da jikin bango, wani irin sarawa kansa keyi masa yayinda zazzaɓi ke ƙara cin ƙarfin jikinsa, idanunsa da ako yaushe suke farare ƙal  sai gashi yau gaba ɗaya sun sauya kala sun koma launin ja,  key ɗin motarsa ya ɗauka inda ya murɗa handle ɗin ƙofar ya fice,  mercedes ɗinsa ya buɗe ya shiga, kansa ya kifa ajikin steering motar tare da fesar da wani irin numfashi, wayarsa ce takawo haske alaman shigowar saƙo, ganin sunan Oummu yasanyashi shiga cikin saƙon.   _"Kozo cikin gaggawa inason ganinka!"_  shine abun da aka rubuta acikin saƙon,
Murza key ɗin motar yayi tare dayin reverse, maigadi ne ya wangale masa gate ya tura hancin motar tasa waje.
Gudu sosai yakeyi akan titin wanda shikansa baisan dacewa gudu yakeyi ba domin gaba ɗaya nutsuwarsa bata jikinsa, gawani irin ciwon kai dake addabarsa kamar kansa zai rabe gida biyu haka yakeji.

Tashinta kenan daga baccin da tayi, wani sabon zazzaɓine yasake rufeta saidai na yanzu baikai na ɗazu ba, hakan kuma yana da nasaba da kukan da tasha ta ƙoshi, Aunty Muhibbat ce ta tursasata akan cewa taje bathroom ɗin Oummu tayi wanka tazo ashiryata don anjima da dare za'a damƙata ga Mijinta, badon tasoma haka Aunty Muhibbat tasata agaba harcikin toilet suka shiga ta haɗa mata ruwan wanka, cikin rashin kuzari tayi wanka yayinda ta ɗaura wani farin

towel ajikinta, kwata kwata iya cinyarta towel ɗin ya tsaya,  hannunta tasa ta dafe kanta sakamakon tunowa da cewa tabar kayanta akan gadon Oummu, sannan kunya bazai barta tafita da wannan ɗan ƙaramin towel ɗin ba.

Daga waje yayi parking motarsa inda yashiga cikin gidannasu da ƙafafunsa dayake magriba ta kawo kai sannan gaba ɗaya mutanen da suka zo bikin suna ɗayan ɓangaren dake cikin gidannasu hakan yasa kai tsaye ya wuce ɓangaren Oummu ganin bai ganta afalo bane yasanyashi haurawa sama kaitsaye.
Ahankali taɗan buɗe ƙofar ban ɗakin ta leƙo kanta, ganin babu kowa acikin ɗakinne yasanyata fitowa cikin sauri batare da ta tsaya goge ƙafanta dake ɗigan ruwa ba,
yana zuwa  ya ɗaura hannunsa akan handle  ɗin ƙofar tare da turata ciki, daidai lokacin ita kuma ta kawo tsakiyan ɗakin jin motsin taɓa ƙofa yasanya ta juyo arazane bisa tsautsayi ruwan dake ƙafanta ya gogi tiles take tsantsin tiles ɗin ya ɗebeta wani irin ƙara ta sake yayinda towel ɗin dake jikinta ya zame  yayi ƙasa.

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*WATTPAD*
@fatymasardauna
#romance

*Chapter 45*

Wani irin ƙara ta sake yayinda towel ɗin jikinta ya zame ya faɗi ƙasa,  cikin tsautsayi ƙafanta ya bugi jikin gado, suuuuu haka tatafi zata faɗi, cikin abun da baiwuce 1 second ba ya ƙaraso cikin ɗakin,  da sauri yaƙarasa tare da sanya duka hannayensa biyu ya tarota, inda ya zube ƙasa kan guiwowinsa,  cikin tsananin tsautsayin dake jansa ya sauƙe idanunsa akan naked pure white breast ɗinta, da sauri ya rumtse idanunsa yayinda lokaci guda yaji tamkar andoka masa guduma atsakiyar kansa,  gaba ɗaya jikinsa ne ya soma ɓari,
Ita kuwa Zieyaderh tamkar wata matacciya haka gaba ɗaya jikinta ya sandare, yayinda ta kulle idanunta ƙaƙam,  cikin tsananin tsoron  dake ɗawainiya da zuciyarta hadɗ da fusgewar numfashi ta ɗan buɗe idanunta kaɗan, wani irin ƙara tasake  sakamakon ganin fuskarsa da tayi, cikin tsananin ruɗewa hadɗ da zabura ta tashi daga jikinsa,
aruɗe ta soma ƙoƙarin neman towel ɗinta daya faɗi, don  suturce jikinta, irin yanayin ruɗewan da tayi yasanya takasa ganin towel ɗin, wanda kuma yashe yake agabanta,  cikin hanzari ta jawo blanket ɗin dake kan gadon na Oummu ta rufe gaba ɗaya jikinta dashi,  zamewa ƙasa tayi

tare da sakin wani irin marayan kuka wanda ke ɗauke da tsananin takaici da kuma haushin kanta, wata fitinanniyar kunyace gaba ɗaya ta rufeta.

Jin diran sautin kukanta da yayi acikin kunnuwansa, yasanyashi miƙewa daga durƙuson dayayi, cikin dauriya dason kawar da zazzafan ciwon kan daya kawo maza cafka lokaci guda, ya juya tare da nufan hanyar barin ɗakin.
Kasancewar har yanzu idanunsa arufe suke, hakan yasanya sam baikula da Oummu da kuma Aunty Muhibbat dake ƙoƙarin shigowa cikin ɗakin ba,
jin cewa yayi karo da mutum ne yasanyashi saurin buɗe idanunsa, nan ya sauƙe su akan fuskar Oummu dake tsaye tana kallonsa, kansa ya sunkuyar ƙasa tare da raɓawa ta gefenta zai wuce, cike da mamakin yanda idanunsa sukai jajur Oummu tace.
"Kajirani a falon ƙasa".

Kansa kawai ya jinjina mata alaman. "To"
Ahankali yashiga taka matattakalan da zai sadasa da falon ƙasan.

Oummu kuwa dubanta takai ga Aunty Muhibbat, gane abun da Oummun ke nufi yasanya Aunty Muhibbat murɗa handle ɗin ƙofar ɗakin ta shiga da sauri, don ta duba Zieyaderh wacce sautin kukanta ke ratsa kunnuwansu.
Oummu kuwa juyawa tayi tare da fasa shiga ɗakin, kaitsaye tanufi matattakala don sauƙa ƙasa.

Da auri Aunty Muhibbat ta ƙaraso inda Zieyaderh'n ke zaune, yayinda ta takure jikinta waje ɗaya acikin blanket tana kuka.
Kallon towel ɗin dake ƙasa Aunty Muhibbat tayi tare da sakin murmushi, cikin kulawa ta zauna akan gado tare da sanya hannu ta dafa kafaɗa Zieyaderh.

"Jikinne har yanzu?" ta tambaya tana me ƙoƙarin jawota ta zaunar da ita akan gadon Oummu.

Jin muryar Aunty Muhibbat acikin kunnuwanta, yasanyata sake ɓoye kanta acikin blanket, tare da ƙara sautin kukanta.

Still murmushi Aunty Muhibbat tayi cikin rarrashi tace.
"Kukan ya isa haka, ko so kike kanki yayi miki ciwo? maza tashi ki sa kayanki kinji, ko SOORAJ yayi miki wani abune?" Aunty Muhibbat ta tambaya.

Cikin sheshsheƙan kuka tagirgiza kanta alaman.
"A'a"

Murmushi Aunty Muhibbat tayi tare da cewa.
"To tashi kisa kayanki, ko so kike kowa yazo yana ganinki ba kaya?"

Cikin nutsuwa Oummu ta kai dubanta garesa, murya asanyaye ta ƙira sunanshi.

Amsa mata kawai yayi batare daya ɗago kansa ya dubeta ba.

Cikin kulawa ta gyara zamanta tare da cewa.
"Duk da wannan bashine karo na farko da muka fara yi maka aure ba, amma inaso kasancewa wannan auren daban yake da sauran,  bandamu ba koda zakaji cewa hakan da mukayi rashin kyautawa ne agareka, saidai inason kasan cewa  ban taɓajin ina yimaka sha'awar rayuwar aure da wata mace ba kamar Zieyaderh,
kamar yanda kaine ka kawota kakuma riƙeta tunkan musan da ita, ayanzuma haka nakeso kacigaba da  riƙeta,  kai ba ƙaramin yaro bane Sooraj,  kamar yanda na gargaɗeka abaya akan sakin aure, to awannan karon ma zan gargaɗeka, Wallahi! Wallahi!! Sooraj idan har ka saki yarinyar nan Zieyaderh kamar yanda kake sakin sauran matan da muke aura ma to tabbas saina tsinemaka!!"

Amatuƙar razane Sooraj yaɗago kansa da idanunsa wanda sukayi jajur ya kalli mahaifiyar tasa, gani yayi  sam babu alamar wasa akan fuskarta,   sake gyara zama Oummu tayi tare da cewa.

"Kada kaɗauki maganata amazaunin wasa,  idan kuma kace bahaka ba lallai zan shayar dakai ruwan mamaki"
Miƙewa tsaye tayi tare da ɗan soma tattakawa har takai  bakin steps  taɗan  tsaya tare da juyowa, dubansa tayi kana tace.

"Bazan baka ƴar mutane katafi da ita gidanka ba, dole anan zaku zauna, saboda haka anjima za'a kai maka amaryarka, cikin part ɗinka dake gidannan,  sannan kuma Wallahi idan ka cutar da ita ban yafe maka ba!"   Tana gama faɗin haka ta juya tare da soma haura  steps ɗin.

Ahankali Sooraj yaɗago idanunsa wanda suka zama tamkar garwashin wuta yabi bayan mahaifiyar tasa da  kallo, ajiyar zuciya mai ƙarfi ya sauƙe tare da lumshe kyawawan idanunsa, jiki asaluɓe haka ya tashi ya bar cikin falon.

Wani irin haɗaɗɗen lace purpule colour mai taushi wanda yaji ɗinkin riga da sket ta sanya, sosai kayan ya zauna ɗas ajikinta, inda farar fatarta ta sake bayyana acikin purpule colour lace ɗin, tsayawa ajikin madubi tayi tare da duban kanta, wani irin kunyane ya kamata sakamakon ganin yanda gaba ɗaya rabin ƙirjinta ya bayyana ta saman wuyar rigar, rumtse idanunta tayi ayayinda taji tsikar jikinta na tashi, sakamakon tunowa da yanda hannayensa suka sauƙa akan naked skin ɗinta da tayi, da sauri ta sanya hannu ta rufe fuskarta, wani irin haushi da kunyan kanta takeji,  turo ƙofar ɗakin da akayine ya sanyata shiga cikin nutsuwarta.

Aunty Muhibbat da Bilkh ne suka shigo, ganin yanda tsadadden leshin ya zauna ajikin Zieyaderh yayi mata kyau, yasanya Aunty Muhibbat sakin murmushi tare da cewa.
"Masha Allah!"

Zama tayi akan stull ɗin mirror yayinda Bilkh tashiga aikin tsantsara mata kwalliya akan

kyakkyawan fuskarta, duk da  cewa bawani  uban kwalliya sosai akayi mata ba, amma sosai tayi kyau,  ɗauri mai kyau Bilkh tayi mata tare da yafa mata wani  babban mayafi ajikinta wanda yake purpule colour marar nauyi,   sosai Zieyaderh tayi kyau irin mai ɗaukar hankalin nan, yayinda oil lipstick ɗin da aka shafa mata akan lips ɗinta keta shinning.

Sooraj kuwa yana fita daga cikin falon na Oummu kai tsaye gaba ɗaya gidan ya bari inda ya wuce night club, can yaje suka haɗe da Mas'oud.

Ƙarfe 8 daidai Aunty Muhibbat ta kamo hannun Zieyaderh inda ta ƙarasa da ita har gaban Oummu da ke zaune akan kujera.

Hannun Zieyaderh  Oummu ta kamo  cike da ƙaunar biyayya irin na yarinyar tace.
"Haƙiƙa kamar ƴata dana haifa ta cikina haka nakejinki Zieyaderh, saboda haka zanyi miki duk wani abu irin wanda uwa mahaifiya keyiwa ƴarta".

Ɗan numfasawa Oummu tayi haɗe da cigaba da cewa.

"Idan akace miki zaman aure ba'ana nufin zaman wasa bane, zaman aure bayana nufin zamane da zaki zauna kiyi abun da kikeso ko kuma kiyi duk abun da kikaga dama ba, aduk sanda mace tayi aure to tana zaune ne aƙarƙashin mijinta akuma ƙasan ikonsa, haƙiƙa aure wani babban sinadarin rufin asirine ga kowacce ƴa mace, aure yana ƙarawa mace ƙima da daraja sosai,  sannan kuma idan kikaji ance miki zaman aure bawai yana nufin kullum zaman daɗi akeyi ba, kamar yanda harshe da haƙori suke saɓawa awasu lokutan haka ma mata da miji ke saɓawa, wani lokaci harma fiye da haka, saboda haka dole saikinyi haƙuri kin kuma jure daɗi da rashinsa kafun zaman aurenki yayi kyau, sannanne kuma zakici riba,  Mijinki tamkar Uba yake agareki saboda haka koda wasa karkiyi ƙoƙarin taka maganarsa, idan yace kiyi koda bakyaso kiyi matuƙar bai saɓawa addini ba, kada ki taɓa tunanin ɗaga muryarki sama akan ta mijinki, sannan kada kitaɓa sanya masa baki idan yana magana, mace tagari mai nutsuwa,hankali, da kuma ilimi bata taɓa ɗaga muryarta sama akan muryar mijinta, sannan kuma bata taɓa tanka masa idan yana magana harsai ya gama,  sannan macen da tasan kanta itace macen da ako yaushe take tausasa zuciyar mijinta, idan yana fushi ta rarrashesa, idan tayi masa laifi ta basa haƙuri, haka kuma koda shine yayi mata laifi amma idanunsa suka rufe yake ganin kamar laifinta ne takan kwantar da kanta ƙasa ta bashi haƙuri,   zanji daɗi matuƙa idan kika zamo mace tagari acikin gidan aurenki"
Ajiyar zuciya Oummu ta sauƙe tare da dafa kafaɗan Zieyaderh wacce ke aikin zubar da hawaye, cikin kulawa ta sake cewa.

"Nasan babu soyayya atsakaninki da Sooraj amma har acikin raina ina fata da kwaɗayin ganin ɗorewar zamanku,  kada kice don bakyasonshi zaki ƙuntata masa, haka kuma kada kice don baya sonki zaki ƙuntata masa, kada kice don bakwason juna komai ya umarceki da yi bazakiyi ba, kisani dun wani abu dazakiyi masa wanda yakasance ba daidai ba to Allah Bazai barki ba

saiya kamaki  da laifi, sannan mala'iku zasu rubutamiki zunubi akan duk abun da kika aikata masa wanda yake ba daidai ba, kiyi haƙuri kizauna dashi da daɗi ko babu, sannan kiriƙe muku sirrinku koda wasa kada kitaɓa barin wani yaji sirrinku, kizama mai haƙuri akullum akuma koda yaushe insha Allah Allah Zai zama gatanki ako ina!"

Kuka me ƙarfine ya ƙwacewa Zieyaderh hakan yasa ta kifa kanta ajikin Oummu tashiga rera kukanta, itama Oummu hawayene suka cika idanunta amma saita shanye tare da sakin murmushi, hannu tasanya ta ɗago Zieyaderh  tare da share mata hawaye, cikin son ƙarfafa mata guiwa tace.
"Allah yamiki Albarka kema yabaki ƴaƴa masu biyayya!"

Aunty Muhibbat ce tazo ta kama Zieyaderh  inda kai tsaye suka wuce ɓangaren SOORAJ wanda aka sake ƙawatasa aka kuma zuba masa sababbin kayan funitures masu kyau da burgewa komai dake cikin falon kalan pitch and milk colour ne, sosai falon yayi kyau,  daga gefe guda kuwa one bedroom ne kaɗai acikin falon wanda shima aka ƙawata cikinsa da furnitures light pink da fari,  sosai komai yayi kyau, akan haɗaɗɗen gadon dayaji lallausan katifa Aunty Muhibbat ta zaunar da ita,  inda ta sanya mayafi ta rufe mata gaɓa ɗaya jikinta,     nan itama tayi mata ɗan taƙaitaccen nasiha,  cikin dabara tace mata zataje ta ɗauko wayarta tana zuwa, kai kawai Zieyaderh  ta iya jinjina mata alaman to.
 Aunty Muhibbat na fita daga cikin ɗakin ta saki murmushi, don wayo kawai tayiwa Zieyaderh babu wani wayarta da zata je ɗaukowa, tafaɗi hakane kawai don tabarta tatafi cikin salama.

9:00 pm

Tun tana jiran dawowan Aunty Muhibbat harta gaji, sannu ahankali takejin wani irin bacci na fusgarta, yayinda agefe guda kuwa takejin wani amai da tashin zuciya na taso mata, wani irin luuuuu haka takejin kanta kamar wanda jiri ke shirin kaiwa ƙasa, lumshe idanunta tayi tama mejin wani abu me  ɗumi daya  fito ajikinta, da sauri ta yaye mayafinta tare da saƙƙowa daga kan gadon, banɗaki ta nufa, inda tana shiga ta sauƙe wani irin ajiyar zuciya don babu makawa tasan cewa period ɗinta ne yazo, mamakine ya cikata ganin cewa wannan karon mara da cikinta basuyi mata ciwo kamar yanda suka saba yi mata  aduk lokacin zuwan period ɗinta ba, tsabtace jikinta tayi tafito zuciyarta ɗauke da fargaba, don sam batasan yanda za'ayi ta samu pad ta sanya ajikinta ba,  tana fitowa daga cikin toilet ɗin ta jingina bayanta da jikin bango, idanunta ne ya sauƙa akan ƙatuwar trolly ɗinta, wani irin ajiyar zuciya ta sauƙe tare da ƙarasawa gaban trolly ɗin, tana zuge zip ɗin jakan tazaro pad ɗinta tare da komawa cikin bathroom ɗin da sauri,  tsabtace jikinta tayi tare da dawowa ta zauna aɗan bakin  gadon, takure jikinta waje  ɗaya tayi tare da lumshe idanunta,   cikin ƴan mintunan da basu wuce 15 ba bacci ɓarawo ya ɗauketa..

11:00 pm.
Dai dai motarsa tashigo cikin harabar gidan, yana gama daidaita parking ɗin motar a parking lot, ya buɗe murfin motar  ya fito tare da sawa motar tasa key, ahankali yake tafiya har ya shigo cikin babban falon gidan,  duhune gaba ɗaya ya mamaye falon yayinda ko ina ya ɗauki shiru,

kaitsaye ƙofar da zata sadashi da ɓangarensa ya buɗe ya shiga,  direct bedroom ya nufa, ahankali ya tura ƙofar ɗakin ya shiga, yana shiga ya maida kofan ya rufe tare da murza mata key,  yana juyowa idanunsa suka sauƙa akanta, kwance take tana bacci abaki bakin gado yayinda ta duƙunƙune jikinta waje ɗaya, dagani kai kasan bata shiryawa baccin ba ya ɗauketa, wani irin duka ƙirjinsa yayi ahankali ya lumshe idanunsa tare da jingina bayansa da jikin ƙofar ɗakin,   wata irin ƙatuwar ajiyar zuciya ya sauƙe  tare da ware idanunsa ahankali ya kuma sauƙesu akanta, sam yama manta da batun kawota ɗakinsa da Oummu tayi masa ɗazun, sama da minti goma ya ɗauka yana kallon yanda ta nannaɗe jikinta waje ɗaya, sake lumshe idanunsa wanda sukai ja yayi tare da ɗan cizon laɓɓansa, sam baiso ace ƙaddaransa ta shafeta ba, sai yanzu yafahimci dalilin dayasa wasu lokuta takan tsaya masa azuciyarsa,  saiyanzu kuma yagane cewa zanen ƙaddaranta ne shumfuɗe azuciyarsa,  maganganun da Oummu tayi masa ɗazunne suka shiga dawowa cikin kunnensa filla filla,  ahankali ya raba bayansa da jikin ƙofan tare da ƙarasowa cikin ɗakin, kayan jikinsa ya soma ragewa yayinda ya cire rigar dake jikinsa, bathroom ya wuce inda ya sakarwa kansa shower, yajima atsaye ruwa na dukan jikinsa, ahankali wata irin nutsuwa ke sauƙar masa,  yana gama wankan yayi alwala kana ya fito daga cikin toilet ɗin,   kaitsaye gaban ƙaton sif ɗin kayansa ya nufa, wani dogon wandon jeans ya sanya, tare da barin murɗaɗɗiyar surar jikinsa awaje batare daya sanya riga ba,  wani farin towel ya ɗauka yashiga goge kansa dake jiƙe da ruwa, yana kammalawa ya feshe gaba ɗaya jikinsa da daddaɗan turarensa mai sanya nutsuwa,    kashe gaba ɗaya makunnan wutan ɗakin yayi, kan wata doguwar kujera dake cikin ɗakin ya nufa, kwanciya irinta ruf da ciki yayi tare da sauƙe ajiyar zuciya,  gajiyayyun idanunsa ya lumshe yana me fitar da numfashi ahankali, kasancewar amatuƙar gajiye yake hakan yasa mintuna ƙalilan bacci ya ɗaukesa.

2:00 pm sosai take ta faman juyi akan gadon hannunta dafe da mararta dake tsananin ciwo, tamkar acikin mafarki haka takejin wani irin azababben ciwon mara na damunta, cikin tsananin wahala ta buɗe idanunta wanda lokaci ɗaya suka ƙanƙance saboda tsabar wahala,   wani ɗan ƙara tasake sakamakon wani irin murɗawa da mararta tayi, lokaci guda ciwon ya tsananta fiye da wanda takeji acikin bacci, duk da sanyin ac'n da yacika gaba ɗaya ɗakin hakan bai hana jikinta fitar da gumin wahala ba, cikin matuƙar tsoro daya kamata da kuma zafin ciwo tasaki wani irin kuka, sosai jikinta ke karkarwa gashi ɗakin gaba ɗaya gauraye yake da duhu, wani irin murɗawa da mararta tayine yasanyata yin wani irin juyi,  haka tafaɗo har ƙasa da ga kan gadon, wani irin sabon kuka tasanya yayinda ta dafe mararta da takejinta kamar zata tarwatse.

Ahankali sautin sheshsheƙan kuka ke ratsa cikin kunnuwansa, tun yanajin abun kamar amafarki har ya soma jiyosu raɗau acikin kunnuwansa, ahankali ya ware idanunsa dake cike da bacci, shiru yayi yana mejin sautin kukan nata na ratsa ko ina dake cikin ɗakin, cikin ɓacin rai ya rumtse idanunsa, sam shikam baisani ba ko aljanune da ita wanda ke sata kuka tsakiyan dare, don wannan bashine karo na farko da kukanta ke tashinsa abacci ba, cikin takaici yagyara kwanciyarsa tare da maida idanunsa ya rufe.
Ita kuwa Zieyaderh ciwon mararne ke sake cin ƙarfinta hakan yasa taci gaba da rera kukanta cikin fitar hayyaci,   duk yanda yaso ya manta da ita yayi baccinsa hakan ya faskara domin kuwa jin kukannata yake har acikin ƙahon zuciyarsa,  tsuka yayi tare da buɗe idanunsa, hannunsa yakai saman kujeran dayake kai, wani ɗan madanni ya danna take wani blue ɗin

haske ya gauraye ɗakin,  idanunsa  ya sauƙe akanta, har yanzu kwance take aƙasa tana ta murƙususu, gaba ɗaya ta birkita kanta,  tuni ɗan kwalin dake kanta ya kama gabansa,  ahankali ya aje ƙafafunsa aƙasa tare da miƙewa tsaye, cikin takunsa mai ɗauke da nutsuwa ya ƙarasa gareta,  tsayawa yayi akanta yana me kallon yanda take kuka tsakaninta da Allah hannunta dafe da mararta, ahankali yaɗan sunkuyo cikin ƙosawa daji kukan nata yace.
"Waike bakida lokacin yin kukane sai tsakiyar dare? zaki tashi daga ƙasannan ne ko saina ɓaɓɓala miki waƴannan siraran ƙafafunnaki?"

Cikin tsananin ciwon dake addabarta taji muryarsa na ratsa kunnuwanta, saidai ko kaɗan taba fahimci abun dayake faɗa ba, don zuwa yanzu tafara fita hayyacinta,   ganin yanda taketa faman neman shigewa ƙarƙashin gado yasanyashi sanya hannayensa ya riƙe waist ɗinsa, idanunsa ya tsura mata tare da ɗan cije laɓɓansa,  itakuwa Zieyaderh sam batasan metakeyi ba, hakan yasa taketa ƙara shigewa cikin lungun gadon tana sakin wani irin gurnanin kuka, ahankali ya durƙusa agabanta tare da sanya hannunsa ya kamo arm ɗinta,  jin shi akusa da ita yasanyata kai hannunta ta kamo damtsen hannunsa cikin tsananin azaban da takeji tashiga yaƙushinsa akan murɗaɗɗun muscles ɗinsa,  rumtse idanunsa yayi yana mejin zafin yanda take yaƙushin fatar jikinsa,  hannayensa yakai ya tattara gaba ɗaya gashinta dake watse kan tiles, ɗagota jikinsa yayi tare da matseta aƙirjinsa, saboda ya lura sosai zafin ciwon ke ƙoƙarin gusar da nutsuwarta, duk da cewa bata cikin hayyacinta amma hakan baihanata sauƙe ajiyar zuciya ba alokacin da taji sauƙar kanta acikin ƙirjinsa,kuka take sosai tana ƙara shigewa jikinsa, yayinda tasake riƙesa ƙamƙam tana me jujjuya kanta acikin faffaɗan ƙirjinsa, wani iri yakeji acikin zuciyarsa, sam bayason jin kukanta, cikin dauriya da jarumtar daya arowa kansa yakai hannunsa dake rawa kan bayanta, ahankali ya ɗanyi ƙasa da zip ɗin rigar dake jikinta, still hannunsa na rawa haka ya taɓa naked skin ɗinta,  rumtse idanunsa yayi ƙam kana yasoma yawo da hannun nasa akan fatar bayanta, ahankali yake shafa skin ɗinta,  sama da mintuna 20 suka ɗauka ahaka harzuwa wannan lokacin baidaina shafa fatar bayanta ba, sannan kuma harzuwa wannan lokacin bai buɗe idanunsa da suke kulle ƙam ba,  ahankali sautin kukannata ke raguwa sai sheshsheƙanta dake tashi kaɗan kaɗan,  kukannata ne ya ɗauke gaba ɗaya alokacin da tasamu relief daga menstrual pain ɗin dake damunta, cikin tsananin galabaita da tayi,  ta ƙara gyara kwanciyarta akan faffaɗan jikinsa, karo nafarko kenan arayuwarta data fara ajiye kanta acikin ƙirjin wani ɗa namiji, haka shima karo nafarko arayuwarsa daya fara ajiye wata mace acikin jikinsa,   sannu ahankali numfashinta ya daidaita yayinda wani irin bacci me daɗin gaske yasoma ƙoƙarin fusganta,   hucin numfashinta dake sauƙa akan ƙirjinsa shine abundaya sanyashi buɗe idanunsa ahankali,  wata irin ajiyar zuciya ya sauƙe tare da ɗan matsawa ya jingina bayansa da jikin gado inda ya tanƙwashe ƙafafunsa, ahankali yasoma ƙoƙarin cireta daga jikinsa, cikin magagin baccinta da baiyi nisa ba tabuɗe baki tare da sakin wani sabon kuka, duk wannan abun da takeyi sam bata cikin nutsuwarta don batasan metakeyi ba, sake ƙanƙamesa tayi ƙam tare da cusa fuskarta acikin ƙirjinsa hartakai tausassun laɓɓanta na gogan kan nipple ɗinsa,   lumshe idanunsa yayi tare da ɗan jingina kansa da gadon, wani irin sarawa yakejin kansa nayi masa, yayinda yakejin wani irin bacci na fusgar idanunsa,     sannu ahankali gaba ɗaya jikinta ya jiƙe da wani irin gumi, duk da cewa sanyin ac ya wadata ɗakin, cikin yanayi na gajiyawa  haɗi da bacci ya sanya hannayensa yaƙarisa zuge mata zip ɗin rigar dake jikinta, kansa ya ɗaura adaidai kafaɗanta wanda hakan yasata sauƙe wani irin ajiyar

zuciya badon komai ba saidon sauƙar  da lallausan sajen sa da yayi akan fatar wuyanta, ahankali yake hura mata iskan  bakinsa akan wuyanta,  sakamakon haka wani irin sanyi ne  taji na ratsa gaba ɗaya ilahirin jikinta, sannu ahankali jikinta ya sake alaman baccinta yayi nisa, yanda numfashinta ke sauƙa akan chest ɗinsa yasanya shi lumshe idanunsa wanda suke cike da bacci, 10 minute kacal bacci ɓarawo ya ɗaukesa yana me zaune akan ƙafafunsa yayinda ita kuma Zieyaderh ke kwance ajikinsa.

(Naji wasu sunacewa har yanzun waisu basusan mene ke damun SOORAJ ba, nayi mamaki ƙwarai don dai nasan tun a pages ɗin baya da suka wuce nafaɗi matsalarsa,  nafaɗi matsalan RAJ ne acikin hikima tayanda duk wanda yake nazartan labarin to cikin sauƙi zai iya gano menene matsalarsa,  amma wasu sam sun kasa fahimta,  to kamar yanda kukeson ji shine SOORAJ namijine amma bashida cikakikkiyar lafiya idan nace bashida cikakkiyar lafiya bawai ina nufin fever ko headache ne ke damunsa ba, a'a  ina nufin shiba cikakken namiji bane kamar yanda wasu maza suke, sam shi bayajin sha'awa kamar yanda wasu daga cikin mutane keji, haka kuma bashi da ingantaccen lafiyar da zai iyayin sex da mace, saura kuma wasu suƙara cemin  basu san mene matsalan SOORAJ ba🙄)

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*WATTPAD*
@fatymasardauna
#romance

*Chapter 45*

Wani irin ƙara ta sake yayinda towel ɗin jikinta ya zame ya faɗi ƙasa,  cikin tsautsayi ƙafanta ya bugi jikin gado, suuuuu haka tatafi zata faɗi, cikin abun da baiwuce 1 second ba ya ƙaraso cikin ɗakin,  da sauri yaƙarasa tare da sanya duka hannayensa biyu ya tarota, inda ya zube ƙasa kan guiwowinsa,  cikin tsananin tsautsayin dake jansa ya sauƙe idanunsa akan naked pure white breast ɗinta, da sauri ya rumtse idanunsa yayinda lokaci guda yaji tamkar andoka masa guduma atsakiyar kansa,  gaba ɗaya jikinsa ne ya soma ɓari,
Ita kuwa Zieyaderh tamkar wata matacciya haka gaba ɗaya jikinta ya sandare, yayinda ta kulle idanunta ƙaƙam,  cikin tsananin tsoron  dake ɗawainiya da zuciyarta hadi da fusgewar numfashi ta ɗan buɗe idanunta kaɗan, wani irin ƙara tasake  sakamakon ganin fuskarsa da tayi, cikin tsananin ruɗewa hadi da zabura ta tashi daga jikinsa,

aruɗe ta soma ƙoƙarin neman towel ɗinta daya faɗi, don suturce jikinta, irin yanayin ruɗewan da tayi yasanya takasa ganin towel ɗin, wanda kuma yashe yake agabanta, cikin hanzari ta jawo blanket ɗin dake kan gadon na Oummu ta rufe gaba ɗaya jikinta dashi, zamewa ƙasa tayi tare da sakin wani irin marayan kuka wanda ke ɗauke da tsananin takaici da kuma haushin kanta, wata fitinanniyar kunyace gaba ɗaya ta rufeta.

Jin diran sautin kukanta da yayi acikin kunnuwansa, yasanyashi miƙewa daga durƙuson dayayi, cikin dauriya dason kawar da zazzafan ciwon kan daya kawo maza cafka lokaci guda, ya juya tare da nufan hanyar barin ɗakin.
Kasancewar har yanzu idanunsa arufe suke, hakan yasanya sam baikula da Oummu da kuma Aunty Muhibbat dake ƙoƙarin shigowa cikin ɗakin ba,
jin cewa yayi karo da mutum ne yasanyashi saurin buɗe idanunsa, nan ya sauƙe su akan fuskar Oummu dake tsaye tana kallonsa, kansa ya sunkuyar ƙasa tare da raɓawa ta gefenta zai wuce, cike da mamakin yanda idanunsa sukai jajur Oummu tace.
"Kajirani a falon ƙasa".

Kansa kawai ya jinjina mata alaman. "To"
Ahankali yashiga taka matattakalan da zai sadasa da falon ƙasan.

Oummu kuwa dubanta takai ga Aunty Muhibbat, gane abun da Oummun ke nufi yasanya Aunty Muhibbat murɗa handle ɗin ƙofar ɗakin ta shiga da sauri, don ta duba Zieyaderh wacce sautin kukanta ke ratsa kunnuwansu.
Oummu kuwa juyawa tayi tare da fasa shiga ɗakin, kaitsaye tanufi matattakala don sauƙa ƙasa.

Da auri Aunty Muhibbat ta ƙaraso inda Zieyaderh'n ke zaune, yayinda ta takure jikinta waje ɗaya acikin blanket tana kuka.
Kallon towel ɗin dake ƙasa Aunty Muhibbat tayi tare da sakin murmushi, cikin kulawa ta zauna akan gado tare da sanya hannu ta dafa kafaɗa Zieyaderh.

"Jikinne har yanzu?" ta tambaya tana me ƙoƙarin jawota ta zaunar da ita akan gadon Oummu.

Jin muryar Aunty Muhibbat acikin kunnuwanta, yasanyata sake ɓoye kanta acikin blanket, tare da ƙara sautin kukanta.

Still murmushi Aunty Muhibbat tayi cikin rarrashi tace.
"Kukan ya isa haka, ko so kike kanki yayi miki ciwo? maza tashi ki sa kayanki kinji, ko SOORAJ yayi miki wani abune?" Aunty Muhibbat ta tambaya.

Cikin sheshsheƙan kuka tagirgiza kanta alaman.
"A'a"

Murmushi Aunty Muhibbat tayi tare da cewa.
"To tashi kisa kayanki, ko so kike kowa yazo yana ganinki ba kaya?"

Cikin nutsuwa Oummu ta kai dubanta garesa, murya asanyaye ta ƙira sunanshi.
Amsa mata kawai yayi batare daya ɗago kansa ya dubeta ba.

Cikin kulawa ta gyara zamanta tare da cewa.
"Duk da wannan bashine karo na farko da muka fara yi maka aure ba, amma inaso kasancewa wannan auren daban yake da sauran, bandamu ba koda zakaji cewa hakan da mukayi rashin kyautawa ne agareka, saidai inason kasan cewa ban taɓajin ina yimaka sha'awar rayuwar aure da wata mace ba kamar Zieyaderh,
kamar yanda kaine ka kawota kakuma riƙeta tunkan musan da ita, ayanzuma haka nakeso kacigaba da riƙeta, kai ba ƙaramin yaro bane Sooraj, kamar yanda na gargaɗeka abaya akan sakin aure, to awannan karon ma zan gargaɗeka, Wallahi! Wallahi!! Sooraj idan har ka saki yarinyar nan Zieyaderh kamar yanda kake sakin sauran matan da muke aura ma to tabbas saina tsinemaka!!"

Amatuƙar razane Sooraj yaɗago kansa da idanunsa wanda sukayi jajur ya kalli mahaifiyar tasa, gani yayi sam babu alamar wasa akan fuskarta, sake gyara zama Oummu tayi tare da cewa.

"Kada kaɗauki maganata amazaunin wasa, idan kuma kace bahaka ba lallai zan shayar dakai ruwan mamaki"
Miƙewa tsaye tayi tare da ɗan soma tattakawa har takai bakin steps taɗan tsaya tare da juyowa, dubansa tayi kana tace.

"Bazan baka ƴar mutane katafi da ita gidanka ba, dole anan zaku zauna, saboda haka anjima za'a kai maka amaryarka, cikin part ɗinka dake gidannan, sannan kuma Wallahi idan ka cutar da ita ban yafe maka ba!" Tana gama faɗin haka ta juya tare da soma haura steps ɗin.

Ahankali Sooraj yaɗago idanunsa wanda suka zama tamkar garwashin wuta yabi bayan mahaifiyar tasa da kallo, ajiyar zuciya mai ƙarfi ya sauƙe tare da lumshe kyawawan idanunsa, jiki asaluɓe haka ya tashi ya bar cikin falon.

Wani irin haɗaɗɗen lace purpule colour mai taushi wanda yaji ɗinkin riga da sket ta sanya, sosai kayan ya zauna ɗas ajikinta, inda farar fatarta ta sake bayyana acikin purpule colour lace ɗin, tsayawa ajikin madubi tayi tare da duban kanta, wani irin kunyane ya kamata sakamakon ganin yanda gaba ɗaya rabin ƙirjinta ya bayyana ta saman wuyar rigar, rumtse idanunta tayi ayayinda taji tsikar jikinta na tashi, sakamakon tunowa da yanda hannayensa suka sauƙa akan naked skin ɗinta da tayi, da sauri ta sanya hannu ta rufe fuskarta, wani irin haushi da kunyan kanta takeji, turo ƙofar ɗakin da akayine ya sanyata shiga cikin nutsuwarta.

Aunty Muhibbat da Bilkh ne suka shigo, ganin yanda tsadadden leshin ya zauna ajikin Zieyaderh yayi mata kyau, yasanya Aunty Muhibbat sakin murmushi tare da cewa.

"Masha Allah!"

Zama tayi akan stull ɗin mirror yayinda Bilkh tashiga aikin tsantsara mata kwalliya akan kyakkyawan fuskarta, duk da cewa bawani uban kwalliya sosai akayi mata ba, amma sosai tayi kyau, ɗauri mai kyau Bilkh tayi mata tare da yafa mata wani babban mayafi ajikinta wanda yake purpule colour marar nauyi, sosai Zieyaderh tayi kyau irin mai ɗaukar hankalin nan, yayinda oil lipstick ɗin da aka shafa mata akan lips ɗinta keta shinning.

Sooraj kuwa yana fita daga cikin falon na Oummu kai tsaye gaba ɗaya gidan ya bari inda ya wuce night club, can yaje suka haɗe da Mas'oud.

Ƙarfe 8 daidai Aunty Muhibbat ta kamo hannun Zieyaderh inda ta ƙarasa da ita har gaban Oummu da ke zaune akan kujera.

Hannun Zieyaderh Oummu ta kamo cike da ƙaunar biyayya irin na yarinyar tace.
"Haƙiƙa kamar ƴata dana haifa ta cikina haka nakejinki Zieyaderh, saboda haka zanyi miki duk wani abu irin wanda uwa mahaifiya keyiwa ƴarta".

Ɗan numfasawa Oummu tayi haɗe da cigaba da cewa.

"Idan akace miki zaman aure ba'ana nufin zaman wasa bane, zaman aure bayana nufin zamane da zaki zauna kiyi abun da kikeso ko kuma kiyi duk abun da kikaga dama ba, aduk sanda mace tayi aure to tana zaune ne aƙarƙashin mijinta akuma ƙasan ikonsa, haƙiƙa aure wani babban sinadarin rufin asirine ga kowacce ƴa mace, aure yana ƙarawa mace ƙima da daraja sosai, sannan kuma idan kikaji ance miki zaman aure bawai yana nufin kullum zaman daɗi akeyi ba, kamar yanda harshe da haƙori suke saɓawa awasu lokutan haka ma mata da miji ke saɓawa, wani lokaci harma fiye da haka, saboda haka dole saikinyi haƙuri kin kuma jure daɗi da rashinsa kafun zaman aurenki yayi kyau, sannanne kuma zakici riba, Mijinki tamkar Uba yake agareki saboda haka koda wasa karkiyi ƙoƙarin taka maganarsa, idan yace kiyi koda bakyaso kiyi matuƙar bai saɓawa addini ba, kada ki taɓa tunanin ɗaga muryarki sama akan ta mijinki, sannan kada kitaɓa sanya masa baki idan yana magana, mace tagari mai nutsuwa,hankali, da kuma ilimi bata taɓa ɗaga muryarta sama akan muryar mijinta, sannan kuma bata taɓa tanka masa idan yana magana harsai ya gama, sannan macen da tasan kanta itace macen da ako yaushe take tausasa zuciyar mijinta, idan yana fushi ta rarrashesa, idan tayi masa laifi ta basa haƙuri, haka kuma koda shine yayi mata laifi amma idanunsa suka rufe yake ganin kamar laifinta ne takan kwantar da kanta ƙasa ta bashi haƙuri, zanji daɗi matuƙa idan kika zamo mace tagari acikin gidan aurenki"
Ajiyar zuciya Oummu ta sauƙe tare da dafa kafaɗan Zieyaderh wacce ke aikin zubar da hawaye, cikin kulawa ta sake cewa.

"Nasan babu soyayya atsakaninki da Sooraj amma har acikin raina ina fata da kwaɗayin ganin

ɗorewar zamanku,  kada kice don bakyasonshi zaki ƙuntata masa, haka kuma kada kice don baya sonki zaki ƙuntata masa, kada kice don bakwason juna komai ya umarceki da yi bazakiyi ba, kisani dun wani abu dazakiyi masa wanda yakasance ba daidai ba to Allah Bazai barki ba saiya kamaki  da laifi, sannan mala'iku zasu rubutamiki zunubi akan duk abun da kika aikata masa wanda yake ba daidai ba, kiyi haƙuri kizauna dashi da daɗi ko babu, sannan kiriƙe muku sirrinku koda wasa kada kitaɓa barin wani yaji sirrinku, kizama mai haƙuri akullum akuma koda yaushe insha Allah Allah Zai zama gatanki ako ina!"

Kuka me ƙarfine ya ƙwacewa Zieyaderh hakan yasa ta kifa kanta ajikin Oummu tashiga rera kukanta, itama Oummu hawayene suka cika idanunta amma saita shanye tare da sakin murmushi, hannu tasanya ta ɗago Zieyaderh  tare da share mata hawaye, cikin son ƙarfafa mata guiwa tace.
"Allah yamiki Albarka kema yabaki ƴaƴa masu biyayya!"

Aunty Muhibbat ce tazo ta kama Zieyaderh  inda kai tsaye suka wuce ɓangaren SOORAJ wanda aka sake ƙawatasa aka kuma zuba masa sababbin kayan funitures masu kyau da burgewa komai dake cikin falon kalan pitch and milk colour ne, sosai falon yayi kyau,  daga gefe guda kuwa one bedroom ne kaɗai acikin falon wanda shima aka ƙawata cikinsa da furnitures light pink da fari,  sosai komai yayi kyau, akan haɗaɗɗen gadon dayaji lallausan katifa Aunty Muhibbat ta zaunar da ita,  inda ta sanya mayafi ta rufe mata gaɓa ɗaya jikinta,     nan itama tayi mata ɗan taƙaitaccen nasiha,  cikin dabara tace mata zataje ta ɗauko wayarta tana zuwa, kai kawai Zieyaderh  ta iya jinjina mata alaman to.
 Aunty Muhibbat na fita daga cikin ɗakin ta saki murmushi, don wayo kawai tayiwa Zieyaderh babu wani wayarta da zata je ɗaukowa, tafaɗi hakane kawai don tabarta tatafi cikin salama.

9:00 pm

Tun tana jiran dawowan Aunty Muhibbat harta gaji, sannu ahankali takejin wani irin bacci na fusgarta, yayinda agefe guda kuwa takejin wani amai da tashin zuciya na taso mata, wani irin luuuuu haka takejin kanta kamar wanda jiri ke shirin kaiwa ƙasa, lumshe idanunta tayi tama mejin wani abu me  ɗumi daya  fito ajikinta, da sauri ta yaye mayafinta tare da saƙƙowa daga kan gadon, banɗaki ta nufa, inda tana shiga ta sauƙe wani irin ajiyar zuciya don babu makawa tasan cewa period ɗinta ne yazo, mamakine ya cikata ganin cewa wannan karon mara da cikinta basuyi mata ciwo kamar yanda suka saba yi mata  aduk lokacin zuwan period ɗinta ba, tsabtace jikinta tayi tafito zuciyarta ɗauke da fargaba, don sam batasan yanda za'ayi ta samu pad ta sanya ajikinta ba,  tana fitowa daga cikin toilet ɗin ta jingina bayanta da jikin bango, idanunta ne ya sauƙa akan ƙatuwar trolly ɗinta, wani irin ajiyar zuciya ta sauƙe tare da ƙarasawa gaban trolly ɗin, tana zuge zip ɗin jakan tazaro pad ɗinta tare da komawa cikin bathroom ɗin da sauri,  tsabtace jikinta tayi tare da dawowa ta zauna aɗan bakin  gadon, takure jikinta waje  ɗaya tayi tare da lumshe idanunta,   cikin ƴan mintunan da basu wuce 15 ba bacci ɓarawo ya ɗauketa..

11:00 pm.

Dai dai motarsa tashigo cikin harabar gidan, yana gama daidaita parking ɗin motar a parking lot, ya buɗe murfin motar ya fito tare da sawa motar tasa key, ahankali yake tafiya har ya shigo cikin babban falon gidan, duhune gaba ɗaya ya mamaye falon yayinda ko ina ya ɗauki shiru, kaitsaye ƙofar da zata sadashi da ɓangarensa ya buɗe ya shiga, direct bedroom ya nufa, ahankali ya tura ƙofar ɗakin ya shiga, yana shiga ya maida kofan ya rufe tare da murza mata key, yana juyowa idanunsa suka sauƙa akanta, kwance take tana bacci abaki bakin gado yayinda ta duƙunƙune jikinta waje ɗaya, dagani kai kasan bata shiryawa baccin ba ya ɗauketa, wani irin duka ƙirjinsa yayi ahankali ya lumshe idanunsa tare da jingina bayansa da jikin ƙofar ɗakin, wata irin ƙatuwar ajiyar zuciya ya sauƙe tare da ware idanunsa ahankali ya kuma sauƙesu akanta, sam yama manta da batun kawota ɗakinsa da Oummu tayi masa ɗazun, sama da minti goma ya ɗauka yana kallon yanda ta nannaɗe jikinta waje ɗaya, sake lumshe idanunsa wanda sukai ja yayi tare da ɗan cizon laɓɓansa, sam baiso ace ƙaddaransa ta shafeta ba, sai yanzu yafahimci dalilin dayasa wasu lokuta takan tsaya masa azuciyarsa, saiyanzu kuma yagane cewa zanen ƙaddaranta ne shumfuɗe azuciyarsa, maganganun da Oummu tayi masa ɗazunne suka shiga dawowa cikin kunnensa filla filla, ahankali ya raba bayansa da jikin ƙofan tare da ƙarasowa cikin ɗakin, kayan jikinsa ya soma ragewa yayinda ya cire rigar dake jikinsa, bathroom ya wuce inda ya sakarwa kansa shower, yajima atsaye ruwa na dukan jikinsa, ahankali wata irin nutsuwa ke sauƙar masa, yana gama wankan yayi alwala kana ya fito daga cikin toilet ɗin, kaitsaye gaban ƙaton sif ɗin kayansa ya nufa, wani dogon wandon jeans ya sanya, tare da barin murɗaɗɗiyar surar jikinsa awaje batare daya sanya riga ba, wani farin towel ya ɗauka yashiga goge kansa dake jiƙe da ruwa, yana kammalawa ya feshe gaba ɗaya jikinsa da daddaɗan turarensa mai sanya nutsuwa, kashe gaba ɗaya makunnan wutan ɗakin yayi, kan wata doguwar kujera dake cikin ɗakin ya nufa, kwanciya irinta ruf da ciki yayi tare da sauƙe ajiyar zuciya, gajiyayyun idanunsa ya lumshe yana me fitar da numfashi ahankali, kasancewar amatuƙar gajiye yake hakan yasa mintuna ƙalilan bacci ya ɗaukesa.

2:00 pm sosai take ta faman juyi akan gadon hannunta dafe da mararta dake tsananin ciwo, tamkar acikin mafarki haka takejin wani irin azababben ciwon mara na damunta, cikin tsananin wahala ta buɗe idanunta wanda lokaci ɗaya suka ƙanƙance saboda tsabar wahala, wani ɗan ƙara tasake sakamakon wani irin murɗawa da mararta tayi, lokaci guda ciwon ya tsananta fiye da wanda takeji acikin bacci, duk da sanyin ac'n da yacika gaba ɗaya ɗakin hakan bai hana jikinta fitar da gumin wahala ba, cikin matuƙar tsoro daya kamata da kuma zafin ciwo tasaki wani irin kuka, sosai jikinta ke karkarwa gashi ɗakin gaba ɗaya gauraye yake da duhu, wani irin murɗawa da mararta tayine yasanyata yin wani irin juyi, haka tafaɗo har ƙasa da ga kan gadon, wani irin sabon kuka tasanya yayinda ta dafe mararta da takejinta kamar zata tarwatse.

Ahankali sautin sheshsheƙan kuka ke ratsa cikin kunnuwansa, tun yanajin abun kamar amafarki har ya soma jiyosu raɗau acikin kunnuwansa, ahankali ya ware idanunsa dake cike da bacci, shiru yayi yana mejin sautin kukan nata na ratsa ko ina dake cikin ɗakin, cikin ɓacin rai ya rumtse idanunsa, sam shikam baisani ba ko aljanune da ita wanda ke sata kuka tsakiyan dare, don wannan bashine karo na farko da kukanta ke tashinsa abacci ba, cikin takaici yagyara kwanciyarsa tare da maida idanunsa ya rufe.
Ita kuwa Zieyaderh ciwon mararne ke sake cin ƙarfinta hakan yasa taci gaba da rera kukanta

cikin fitar hayyaci,   duk yanda yaso ya manta da ita yayi baccinsa hakan ya faskara domin kuwa jin kukannata yake har acikin ƙahon zuciyarsa,  tsuka yayi tare da buɗe idanunsa, hannunsa yakai saman kujeran dayake kai, wani ɗan madanni ya danna take wani blue ɗin haske ya gauraye ɗakin,  idanunsa  ya sauƙe akanta, har yanzu kwance take aƙasa tana ta murƙususu, gaba ɗaya ta birkita kanta,  tuni ɗan kwalin dake kanta ya kama gabansa,  ahankali ya aje ƙafafunsa aƙasa tare da miƙewa tsaye, cikin takunsa mai ɗauke da nutsuwa ya ƙarasa gareta,  tsayawa yayi akanta yana me kallon yanda take kuka tsakaninta da Allah hannunta dafe da mararta, ahankali yaɗan sunkuyo cikin ƙosawa daji kukan nata yace.
"Waike bakida lokacin yin kukane sai tsakiyar dare? zaki tashi daga ƙasannan ne ko saina ɓaɓɓala miki waƴannan siraran ƙafafunnaki?"

Cikin tsananin ciwon dake addabarta taji muryarsa na ratsa kunnuwanta, saidai ko kaɗan taba fahimci abun dayake faɗa ba, don zuwa yanzu tafara fita hayyacinta,   ganin yanda taketa faman neman shigewa ƙarƙashin gado yasanyashi sanya hannayensa ya riƙe waist ɗinsa, idanunsa ya tsura mata tare da ɗan cije laɓɓansa,  itakuwa Zieyaderh sam batasan metakeyi ba, hakan yasa taketa ƙara shigewa cikin lungun gadon tana sakin wani irin gurnanin kuka, ahankali ya durƙusa agabanta tare da sanya hannunsa ya kamo arm ɗinta,  jin shi akusa da ita yasanyata kai hannunta ta kamo damtsen hannunsa cikin tsananin azaban da takeji tashiga yaƙushinsa akan murɗaɗɗun muscles ɗinsa,  rumtse idanunsa yayi yana mejin zafin yanda take yaƙushin fatar jikinsa,  hannayensa yakai ya tattara gaba ɗaya gashinta dake watse kan tiles, ɗagota jikinsa yayi tare da matseta aƙirjinsa, saboda ya lura sosai zafin ciwon ke ƙoƙarin gusar da nutsuwarta, duk da cewa bata cikin hayyacinta amma hakan baihanata sauƙe ajiyar zuciya ba alokacin da taji sauƙar kanta acikin ƙirjinsa,kuka take sosai tana ƙara shigewa jikinsa, yayinda tasake riƙesa ƙamƙam tana me jujjuya kanta acikin faffaɗan ƙirjinsa, wani iri yakeji acikin zuciyarsa, sam bayason jin kukanta, cikin dauriya da jarumtar daya arowa kansa yakai hannunsa dake rawa kan bayanta, ahankali ya ɗanyi ƙasa da zip ɗin rigar dake jikinta, still hannunsa na rawa haka ya taɓa naked skin ɗinta,  rumtse idanunsa yayi ƙam kana yasoma yawo da hannun nasa akan fatar bayanta, ahankali yake shafa skin ɗinta,  sama da mintuna 20 suka ɗauka ahaka harzuwa wannan lokacin baidaina shafa fatar bayanta ba, sannan kuma harzuwa wannan lokacin bai buɗe idanunsa da suke kulle ƙam ba,  ahankali sautin kukannata ke raguwa sai sheshsheƙanta dake tashi kaɗan kaɗan,  kukannata ne ya ɗauke gaba ɗaya alokacin da tasamu relief daga menstrual pain ɗin dake damunta, cikin tsananin galabaita da tayi,  ta ƙara gyara kwanciyarta akan faffaɗan jikinsa, karo nafarko kenan arayuwarta data fara ajiye kanta acikin ƙirjin wani ɗa namiji, haka shima karo nafarko arayuwarsa daya fara ajiye wata mace acikin jikinsa,   sannu ahankali numfashinta ya daidaita yayinda wani irin bacci me daɗin gaske yasoma ƙoƙarin fusganta,   hucin numfashinta dake sauƙa akan ƙirjinsa shine abundaya sanyashi buɗe idanunsa ahankali,  wata irin ajiyar zuciya ya sauƙe tare da ɗan matsawa ya jingina bayansa da jikin gado inda ya tanƙwashe ƙafafunsa, ahankali yasoma ƙoƙarin cireta daga jikinsa, cikin magagin baccinta da baiyi nisa ba tabuɗe baki tare da sakin wani sabon kuka, duk wannan abun da takeyi sam bata cikin nutsuwarta don batasan metakeyi ba, sake ƙanƙamesa tayi ƙam tare da cusa fuskarta acikin ƙirjinsa hartakai tausassun laɓɓanta na gogan kan nipple ɗinsa,   lumshe idanunsa yayi tare da ɗan jingina kansa da gadon, wani irin sarawa yakejin kansa nayi masa, yayinda yakejin wani irin bacci na fusgar idanunsa,     sannu

ahankali gaba ɗaya jikinta ya jiƙe da wani irin gumi, duk da cewa sanyin ac ya wadata ɗakin, cikin yanayi na gajiyawa  hadi da bacci ya sanya hannayensa yaƙarisa zuge mata zip ɗin rigar dake jikinta, kansa ya ɗaura adaidai kafaɗanta wanda hakan yasata sauƙe wani irin ajiyar zuciya badon komai ba saidon sauƙar  da lallausan sajen sa da yayi akan fatar wuyanta, ahankali yake hura mata iskan  bakinsa akan wuyanta,  sakamakon haka wani irin sanyi ne  taji na ratsa gaba ɗaya ilahirin jikinta, sannu ahankali jikinta ya sake alaman baccinta yayi nisa, yanda numfashinta ke sauƙa akan chest ɗinsa yasanya shi lumshe idanunsa wanda suke cike da bacci, 10 minute kacal bacci ɓarawo ya ɗaukesa yana me zaune akan ƙafafunsa yayinda ita kuma Zieyaderh ke kwance ajikinsa.

(Naji wasu sunacewa har yanzun waisu basusan mene ke damun SOORAJ ba, nayi mamaki ƙwarai don dai nasan tun a pages ɗin baya da suka wuce nafaɗi matsalarsa,  nafaɗi matsalan RAJ ne acikin hikima tayanda duk wanda yake nazartan labarin to cikin sauƙi zai iya gano menene matsalarsa,  amma wasu sam sun kasa fahimta,  to kamar yanda kukeson ji shine SOORAJ namijine amma bashida cikakikkiyar lafiya idan nace bashida cikakkiyar lafiya bawai ina nufin fever ko headache ne ke damunsa ba, a'a  ina nufin shiba cikakken namiji bane kamar yanda wasu maza suke, sam shi bayajin sha'awa kamar yanda wasu daga cikin mutane keji, haka kuma bashi da ingantaccen lafiyar da zai iyayin sex da mace, saura kuma wasu suƙara cemin  basu san mene matsalan SOORAJ ba🙄)
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*WATTPAD*
@fatymasardauna
#romance

*Chapter 46*

Sannu ahankali ƙiran sallan assalatu da akeyi ya ratsa cikin kunnuwansa,  ahankali ya ware manyan idanunsa, ajiyar zuciya mai ƙarfi ya sauƙe,  tare da ɗan cije laɓɓansa sakamakon yanda yaji ƙafafaunsa sun ƙage waje guda, hakan ya faru ne kuma saboda jimawa da sukayi anannaɗe,   ƙasa ya ɗanyi da idanunsa tare da duban fuskarta, baccinta takeyi cikin kwanciyar hankali da natsuwa, yayinda take ta faman sauƙe ajiyar zuciya akai akai,  saurin ɗauke idanunsa wanda suka sauƙa akan breast ɗinta yayi,  tare da ɗan yunƙurawa ya tashi da ita ajikinsa.
Ahankali ya shumfuɗeta akan gado,  tare da juyawa ya nufi hanyar bathroom.

Zip ɗin wandon jeans ɗin dake jikinsa ya zuge, tare da zame wandon nasa yayi ƙasa, daidaita tsayuwarsa yayi agaban shower, tare da ɗan murɗa makunnin shower'n, sassanyar ruwan dake fitowa acikin shower'n ne ke dukan jikinsa, sannu ahankali yakejin wani irin sanyi na ratsa gaba ɗaya jikinsa, cikin nutsuwa yayi wanka tare da ɗauro alwala, farar bathrobe ya sanya ajikinsa kana yafito daga cikin toilet ɗin.
Kaitsaye gaban sif ɗin kayansa ya nufa, wani black jeans tare da white long sleeve shirt yasanya, kana ya fesa turarensa mai daɗin ƙamshi, wani ƙaton darduma ya shumfuɗa aƙasa, inda ya gabatar da sallah raka' biyu, yana idarwa yaji ana ƙiran sallan Asuba a masallaci, shafa addu'an da yakeyi yayi tare miƙewa tsaye, har yakai bakin ƙofar fita daga cikin ɗakin, sai kuma yaɗan tsaya tare da juyowa ya kalli inda take, haryanzu baccinta take sha cikin kwanciyar hankali, handle ɗin ƙofar ya murɗa kana ya fice daga cikin ɗakin.

7:30 am.
Ahankali take buɗe idanunta wanda sukai nauyi kana kuma sukai ja, sake ɗan lumshe idanun nata tayi sakamakon sihirtaccen ƙamshinsa daya samu daman kawowa hancinta ziyara, ahankali tatashi zaune daga kan gadon, ɗakin tasoma bi da kallo, kana ta sauƙe wani irin ajiyar zuciya, ahankali ta zuro da ƙafafunta ƙasa, wanda suka sha jan lalle gwanin ban sha'awa, direct inda trolly ɗinta yake ta nufa, zuge zip ɗin jakar tayi tare da fito da wata maroon ɗin abaya gown mai kyau wanda aka ƙawata jikinta da adon ƙyalƙyali, cikin sauri ta shige toilet.
Tsayawa tayi tana me ƙarewa haɗaɗɗen toilet ɗin kallo, komai dake cikinsa nead, sosai aka ƙawata toilet ɗin, gaba ɗaya toilet ɗin ƙamshi yake, ahankali ta ƙarasa jikin wani glass wanda aka jere kyawawan bathrobe da kuma towels acikinsu, rigar dake hannunta ta ajiye tare da zage zip ɗin rigar, ɗaya daga cikin towel ɗin ta ɗauko ƙoƙarin ɗaurawa ajikinta take, daddaɗan ƙamshinsa mai sanya nutsuwa ne ya daki hancinta, jingina bayanta tayi da jikin bango tare da lumshe idanunta, sosai ƙamshin nasa ke kashe mata jiki, ɗaura towel ɗin tayi ajikinta tare da ƙarasawa gaban bathtube ta haɗawa kanta ruwan wanka, cikin nutsuwa tayi wanka inda ta zura abaya gown ajikinta, sosai rigar tayi mata kyau ta kuma amshi jikinta, ahankali ta murɗa handle ɗin ƙofar bathroom ɗin tafito, kaitsaye dressing mirror ta nufa, tsadaddun kayan shafansa ne suka cika gaban mirror'n, gwanin ban sha'awa, hannunta takai ta ɗauki wani kyakkyawan kwalban turarensa dake kan mirror'n, jujjuya kwalban turaren tayi ahannunta tare da sauƙe ajiyar zuciya, nannaɗe dogon gashinta tayi tare da sanya ribbom tayi parking gashin atsakiyar kanta, nan tashiga kimtsa kan gadon, duk dama nead yake bai wani ɓaci sosai ba, saida ta gyara komai dake cikin ɗakin, kana ta wuce toilet ta wankesa tsab, zama tayi akan gado haɗe da jingina bayanta da jikin gadon, lumshe kyawawan idanunta tayi sannu ahankali wasu daga cikin abubuwan da suka faru atsakaninsu jiya da dare suka soma dawo mata, tabbas Ƙaddara tayi mata sauyi, Ƙaddara ta canza duk wani tunaninta, wasu irin sanyayyun hawayene suka samu damar gangarowa daga cikin idanunta, kwanciya tayi akan gadon tare da cusa kanta cikin pillow ta saki wani irin marayan kuka,
tayaya zata fara koyawa kanta zama dashi? wani abu takeji na daban acikin rai da zuciyarta dangane dashi.

Tunda yafita sallan asuba bashi yadawo gidan ba sai 8:30.

Ahankali ya tura  ƙofar ɗakin yashiga,   Zieyaderh wacce take fidda sheshsheƙan kuka tana jin motsinsa tayi shiru tare da sake ɓoye fuskarta acikin pillow, hakanan wani ɗan banzan tsoronsa ya shiga zuciyarta, ko ƙaunar haɗa idanu dashi batasonyi ayanzu.

Sam baidamu da cewar waidon tana ɗakin bazaiyi abun da yakeso ba, hasalima  ko inda take baikalla ba,  tundaga bakin ƙofar ɗakin yashiga ɓalle maɓallan rigarsa, zuge zip ɗin wandonsa yayi tare da cire rigar jikinsa, cikin takunsa dake amsa amo yanufi gaban sif ɗin kayansa, tamkar ƙirjinta zai fito waje haka takeji saboda tsoro,  sake duƙunƙune jikinta tayi tare da ɗauke numfashinta  tayi luf akan gadon kamar wacce ke bacci, ƙasa yayi da wandon jeans ɗinnasa, tare da cire wandon gaba ɗaya daga jikinsa, wani white towel ya ɗaura akan waist ɗinsa,  kai tsaye ya wuce bathroom, tanajin motsin rufe ƙofarsa,  tasaki wata kyakkyawar ajiyar zuciya.

Ruwan wanka ya haɗawa kansa acikin bathtube inda ya cika turaren wanka aciki,  kwanciya yayi luf acikin bathtube ɗin yana me sauƙe ajiyar zuciya, sosai yakejin wani irin bacci na fusgarsa, wanka yayi kana yafito daga cikin toilet din, ƙamshin sabulunsa ne gaba ɗaya ya cika ɗakin,  wanda hakan ya narkar da zuciyar Zieyaderh dake kwance,  cikin nutsuwa ya gama shafa body lotion ɗinsa, men crazy t-shirt black colour tare da pencil crazy jeans shima black colour yasanya, sosai kayan suka fito da natural white skin ɗinsa, suka kuma yi masa kyau matuƙa,   Duk abunda yakeyi tanajin motsinsa, amma saboda tsoro  takasa koda kyakkyawan motsine.
 Yana gama kimtsa kansa ya nufi kan lallausan doguwar kujeran da ayanzu ta zame masa gado,  kwanciya yayi akanta yana me fitar da wani irin numfashi,  idanunsa ya ɗan lumshe tare da buɗesu ya sauƙesu akanta, ahankali yake bin jikinta da kallo, harya kawo idanunsa kan fararen ƙafafunta wanda aka ƙawatasu da zanen jan lalle, cikin nutsuwa yake kallon zanen lallen dake ƙafafunnata tamkar mai nazartar wani abu, azahirin gaskiya kuwa idanunsa ne kawai kekallon zanen, dan sam ƙwaƙwalwarsa ba zanen take kallo ba,  ayanzu damuwarsa tafi ta da yawa, yakanji kamar zuciyarsa zata tarwatse, sannan yakanji kamar ana buga masa guduma atsakar kansa, musamman aduk sanda ya tuno da cewa ita din matsayin mata take agaresa, yazaiyi da haƙƙin ta dake rataye a wuyansa? tayaya zai zama cikakken namijin da zai iya maidata cikakkiyar mace?  kwarai ya sani bazata iya ɗaukar rauni da damuwarsa ba.

Ajiyar zuciya ya sauƙe tare da lumshe idanunsa, inama da ace Kaddara bata zamo silar haɗuwarsu ba, ya tabbata da duk haka bata faru ba, inama da ace wani namijin daban kaddara ta zaɓa mata ba shiba, tayaya zai fara fuskantarta da matsalarsa?  lumshe idanunsa wanda suka soma sanja launi daga fari zuwa ja yayi tare da sakin zazzafar ajiyar zuciya, mintuna goma kacal da kwanciyarsa bacci ɓarawo ya saceshi.

Ahankali taɗan buɗe idanunta, sam  babu wani ƙwaƙƙwaran motsi dake tashi acikin ɗakin, sai sautin ƙaran ac da kuma sautin  numfashinsa dake fita ahankali, ɗan juyo da fuskarta tayi ta fuskanci inda yake kwance,  ajiyar zuciya ta sauƙe ganin cewa yayi bacci,  zuro da ƙafafunta ƙasa tayi tare da miƙewa tsaye, cikin takun sanɗa tanufi hanyar fita daga cikin ɗakin,  murɗa handle ɗin ƙofar tayi ahankali kana ta fice.

Tana samun kanta acikin ƙawataccen falon nasa, tasaki wata irin narkakkiyar ajiyar zuciya, daidaita nutsuwarta tayi tare da zame ɗan kwalin dake kanta ta yafa bisa jikinta, duk da cewa tana matuƙar jin kunyan Ummi ayanzu, amma tanaga zama da Ummi'n zaifiyi mata daɗi akan tazauna shiru cikin miskilancinsa.
Bakinta ɗauke da sallama haka ta kutsa kanta cikin falon Oummu'n, zaune Oummu take akan kujera, yayinda Aunty Muhibbat kuwa ke kan dinning area tana haɗa abinci acikin basket.
Ganin Zieyaderh  yasa  Oummu faɗaɗa fari'arta.
Cikin ladabi haɗi da girmamawa Zieyaderh tayi ƙasa da kanta tare da durƙusawa har ƙasa tagaida Oummu'n,  fuska ɗauke da murmushi haɗe daso da kuma ƙauna Oummu ta jawota, tare da zaunar da ita akan kujeran da take.
Cikin kulawa Oummu ta tambayeta jikinta.
"Dasauƙi."
Tabawa Oummu'n amsa murya asanyaye,  ƙarasowar Aunty Muhibbat wajen yasanyata sauƙowa daga kan kujeran cikin girmamawa tagaida Aunty Muhibbat ɗin.
Fuska asake Aunty Muhibbat ta amsa mata tare da cewa.
 "Yanzu nake shirin kai muko break fast, sai kuma gaki kin fito, wa yace miki amarya tana zuwa gaisuwa? ae saidai azo agaisheta."

Mumushi Zieyaderh tayi cike dajin kunya tayi kasa da kanta, basket din abincin Aunty Muhibbata tamiƙo mata tare da cewa.
 "Idan kina buƙatar wani abu waya kawai zakinayi amma kizauna aɓangarenki kinji, nan ɓangaren Oummu ne  saboda haka sai angayyaceku kafun kuzo!." Cikin sigar wasa Aunty Muhibbat taƙarishe maganan.
Wani irin kunyane yasake rufe Zieyaderh, Oummu kuwa murmushi kawai tayi, karɓan basket ɗin tayi inda tamiƙe asanyaye ta nufi ƙofar dazai sadata da ɓangaren nasu,
da kallo Aunty Muhibbat ta rakata, aranta tana me ƙissima abubuwa da yawa, hakanan jikinta yafara bata wani abu dangane da SOORAJ, duk da cewa tunanin nata yayi gaggawa, amma dai tabbas zuciyarta nayi mata wani zargin na daban, lumshe idanunta tayi aranta tana cewa.
"Ya Allah Kasa kada tunanina ya zama gaskiya."

Hira suka shiga ɗan taɓawa kaɗan kaɗan ita da Oummu.

Itakuwa Zieyaderh tana shiga falon nasu  aje basket ɗin tayi, inda ta zauna akan ɗaya daga cikin royal chairs ɗin da suka ƙawata tsakiyar falon,  kasancewar bata wani jin yunwa sosai hakan yasanya bataci abincin ba, idanunta ne suka sauƙa akan wani haɗaɗɗen hotonsa wanda ke saƙale ajikin bango,  sosai hoton yayi kyau yayinda aka sirrantashi cikin wani glass mai tsada, ahankali tashiga takawa harta ƙarasa inda hoton yake,  idanunta ta tsurawa hoton tare da sakin wani murmushi,  ahoton sanye yake da army jeans black and black t shirt, yayinda yasanya wasu kyawawan combat shoe suma kalan baƙaƙe aƙafansa, yanayin tsayuwar da yayi acikin hoton, yasanya shi  yin kyau sosai, murmushi taƙarayi tare da kai hannunta daidai saitin bakinsa, sosai murmushin dake ɗauke akan fuskarsa ta ƙara bayyana tsantsar kyawunsa.
 "Kafi kyau idan kana murmush!."
Tafaɗi maganar acikin zuciyarta, sai dai abun da bata sani ba shine maganartata tafito fili,

ahankali tasanya hannunta ta shafo kan kyakkyawar fuskarsa,  aranta tace.
"Kai ɗin na dabanne! babu wani ɗa namiji dazai gwada maka komai, koba kyauba kana da abun da sauran maza basu dashi."
Lumshe kyawawan idanunta tayi tare da ɗan matsawa daga jikin hoton,  juyowan da zatayi idanunta suka faɗa cikin nasa idanun,  ƙirjinta ne taji yaɗan buga,  cikin yanayi na ɗanjin kunya tayi ƙasa da kanta, shima ɗauke idanunsa daga kanta yayi tare da  raɓawa ta gefenta ya wuce, ƙasa ƙasa tabi sa da kallo harya fice daga cikin falon, sosai yayi kyau cikin ssbuwar shigar daya kuma sauyawa, lumshe idanunta tayi tare da komawa cikin falon ta zauna, luf tayi akan kujera tana mejin wani irin tsananin shauƙi na ratsa gaba ɗaya jikinta, wani irin abu takeji ajikinta wanda batasan dame zata ƙirasa ba, tanajin gaba ɗaya tsikar jikinta na mimmiƙewa, haka tayita juyi akan kujera daga ƙarshe  bacci ya ɗauketa batare da ta shiryawa hakan ba.

Gyara zama Mas'oud yayi tare da duban Sooraj wanda ya sunkuyar da kansa ƙasa,  ɗago idanunsa yayi ya kalli Dr.Waleey, cikin yanayin dake nuna damuwa akan fuskarsa yace.
 "Idan har kuma kun gazo gano matsalar RAJ, hakan nanufin kenan  sihiri ne ko  kuna shafan aljanu."

Murmushi Dr.Waleey yayi tare da girgiza kansa,  cikin son kwantar musu da hankali yace.

"Sam ba asiri bane bakuma shafar aljanu bane kamar yanda kayi tunani, sau dayawa Allah kan jarrabi bawansa ta ɓangarori daban daban, wata jarrabawar abayyane take wata kuwa takan zuwa aɓoye, sannan acikin gaba ɗaya mutanen duniya babu wani wanda ya isa ya gujewa ƙaddararsa, me kyu ko akasinta, Ƙarfin ikon Allah ya wuce tunani, tayanda zai iya jarrabanka da komai,  haƙiƙa Allah na jarraban bawansa da jarabawa mafi girma, sau dayawa kuma idan Allah ya jarrabi bawa da jarrabawa mafi muni sai  hankalin wasu daga cikin mutane ya gushe, har ta kaisu ga mantawa da ƙarfin ikon Allah, Idanunsu kan rufewa,  sukan dage akan cewa asiri akaiwa mutum, bayan kuma babu wani wanda yayi masa asiri jarrabawace kawai daga Allah!."
Ɗan numfasawa yayi tare da shafa sumar kansa, kallon Sooraj yayi da kyau, cikin tsananin tausayin Sooraj ɗin da yakeji yaci gaba da cewa.

"Haƙiƙa kai ɗin maitawakkaline, sannan kuma kana da ƙarfin imanin riƙo da ƙaddara, tabbas jarabawar da Allah ya ɗaura maka mai matuƙar girmace, bakowani Namiji bane zai iya juran rufe sirrinshi tare da fawwalawa Allah Lamuransa kamar yanda  kayi ba,  Baka da matsalan komai Sooraj, kuma kaima watarana Insha Allah zaka zama cikakken Namiji mai lafiya, watarana kai da kanka zakayi mamakin kanka, Insha Allahu bazaka taɓa tabbata ahaka ba!."
Dr.Waleey yakai ƙarshen zancen cikin tausasa murya.

Ajiyar zuciya Mas'oud yayi cikin sanyi yace da Dr.Waleey
 "Tayaya?"

Still murmushi Dr.Waleey yayi, zamansa ya gyara da kyau, tare da gyara zaman glass ɗin dake idonsa.

"Tabbas zai iya zama cikakken namiji kuma lafiyarsa zata iya dawowa ako da yaushe,  zai iya samun sauƙi idan har ya kawar da duk wani tunani tahanyar sarrafa matarsa koda ko bayajin daɗi."
 Shiru yayi kana yacigaba da cewa.
"Kusanci da mace zai iya daidaita komai, sannan yawan raɓan mace zai iya rage masa kaso 30 acikin 100 na matsalar dayake tattare da ita."
Sake kallon Sooraj da haryanzu kansa ke ƙasa yayi cikin lallami yace.
"Ka gwada jarrabawa Sooraj, domin lafiyarka abun buƙatace agareka, Namiji baya taɓa zama ingarma kuma jajirtacce, harsai yakasance yana iya biyawa matarsa buƙata, haƙiƙa nasan cewa kaiɗin gwarzone, saidai kuma irin wannan rashin lafiyan taka zata iya haifar da babban matsala arayuwarka, idan ka gwada za a dace insha Allah, matsalace da ka soma jinta ajikinka tun shekatu 8 da suka wuce,  bada ita aka haifeka ba saboda haka zaka iya, watarana kuma zakayi mamaki."

Lumshe idanu Mas'oud yayi tare da buɗesu alokaci guda,  kallon Dr.Waleey yayi tare da basa hannu sukayi musabaha, cikin ɗan sukunin da ya samu acikin ransa najin cewa aminisa zai samu lafiya yace.
 "Mungode sosai doctor!."

Nan sukayiwa Dr.Waleey sallama, shidai Sooraj ƙala baice daga bakinsa ba har suka bar cikin asibitin,  hasalima wani irin abune  yaji ya toshe masa maƙoshi.
Tunda suka shiga mota babu wanda yace da ɗan uwansa wani abu, agaban tangamemen gate ɗin gidansu Sooraj ɗin, Mas'oud yayi parking motar.

Ajiyar zuciya ya sauƙe tare da kallon Sooraj wanda yajingina bayansa da jikin kujeran motar.

Cikin kulawa Mas'oud ya ƙira sunansa.
"RAJ!."
Ɗago idanunsa wanda suka ɗan soma sanja launi Sooraj yayi ya kallesa.

Idanu Mas'oud yaɗan lumshe cikin son samawa Sooraj ɗin nutsuwa yace.
"Tabbas nayarda, kamar yanda Dr.Waleey yace idan ka jarraba zaka iya, please RAJ ka jarraba."

Murmushin dayafi kuka ciwo ne ya bayyana akan fuskar Sooraj, cikin cool voice ɗinsa yace.

"Ƙaddara itace wacce tarigayi fata Mas'oud, kamar yanda Dr.Waleey ya faɗa hakane, ƙaddarata tana da girma sosai,  banso shigowarta cikin rayuwata ba Mas'oud, saboda nafi kowa sanin menene illata,  bazan amfaneta dakomai ba, sannan aurena yazama laluri agareta, aurena zai kashe mata ƙuruciyarta zai kuma kashe mata lokacinta, anayin aure ne don aji daɗi akuma raya sunna, bazan taɓa iya jiyar da ita wannan daɗin ba Mas'oud, saboda ina ɗauke da Nakasa."
Ɗan tsagaitawa yayi da maganan, still murmushi yayi tare da lumshe idanunsa, cikin sanyin murya yace.

"Kasan yanda nakeji akanta kuwa Mas'oud?  Bansan daliliba amma kowani bugun zuciyata da tunaninta yake tafiya, Inajinta awani ɓangare na jikina, tayaya zan cutar da yarinya ƙarama kamarta? duk wata mace indai bata kasance marar lafiya ba tabbas nasan tana buƙatar Namiji akusa da ita, Ni nakasance saɓanin tunanin mutane, bazan amfaneta ba." Ajiyar zuciya ya sauƙe tare da ɗan cije laɓɓansa, yanzun kam sosai rauni ya bayyana akan kyakkyawar fuskarsa, tunda yake bai taɓajin ciwo da ɗacin rashin kasancewarsa lafiyayyen namiji ba sai yau, dama irin wannan ranan yaketa gudu, shiyasa ya keɓe rayuwarsa daga sha'anin mata, irin wannan raunin yake gujewa kansa shiyasa ya nesanta kansa da soyayya, gashi duk iyaka gudunsa ranar ta riskesa,  ɗago idanunsa yayi ya kalli Mas'oud wanda ƙwalla suka cika idanunsa tab, murmushin daya sanya hawayen dake cikin idanunsa gangarowa  yayi tare da cewa.

"Zanyi abun daya dace Mas'oud!."

Yana kaiwa nan azancensa ya buɗe murfin motar ya fito, Da kallo Mas'oud ya bisa harya buɗe tangamemen gate ɗin gidannasu ya shige, hawayen dake cikin idanun Mas'oud ne suka samu daman gangarowa waje, wani irin tausayin abokinnasa yakeji, cikin sanyin jiki yaja motarsa yabar ƙofar gidan.

Tsaye take agaban dressing mirror, wani haɗaɗɗen humra wanda Hajiya Arabi ta bata, take shafawa ajikinta, gaba ɗaya ko ina dake cikin ɗakin ya cika da ƙamshin humra'n nata, gaba ɗaya ta shagala da abun da takeyi,  sanye take da bathrobe pink colour ajikinta, wanda ya tsaya iyaka cinyarta,   kunce igiyan bathrobe ɗin tayi tare da ɗan zamesa ya sauƙa zuwa kan ƙugunta,  humra tashiga shafawa akan ƙirjinta har zuwa kan kafaɗunta,  sam ta manta da cewa ma aɗakinsa take, gaba ɗaya ta saki jiki, daga gefe guda na zuciyarta kuwa,  mamakin ɗaukewan period ɗinta take, don yau kwata kwata kwanansa ɗaya amma ya ɗauke, baikuma taɓa yi mata haka ba,     ahankali ya murɗa handle ɗin ƙofar ɗakin ya shiga,  tsaye yayi ajikin ƙofar yana me ƙare mata kallo tundaga sama har ƙasa, santala santalan legs ɗinta dake ta shinning ya kalla, kana ya sauƙe idanunsa akan bayanta wanda ya matuƙar fidda shape ɗin gefe da gefen cikinta, yayinda fatar bayan nata ke shinning  tana fidda wani irin ƙyalli, lumshe idanunsa yayi  ahankali ya soma takowa zuwa gareta,  sam batasan da shigowarsa cikin ɗakin ba, gaba ɗaya hankalinta yayi nisa wajen rufe kwalban humran dake hannunta, taku ɗaya ne kacal ya rage atsakaninsu, tsayawa yayi, yayinda sosai ƙamshin da jikinta ke fitarwa yayi masa daɗi,  ɗan lumshe idanunsa yayi, hannunsa dake rawa yakai kan fresh skin ɗin dake tsakiyar bayanta.

Azabure Pharouk yayi wurgi da laptop ɗin dake hannunsa, wani irin tuƙuƙin baƙinciki da ɓacin rai ne suka cika idanunsa har suke neman rufe ganinsa, jikinsa ne ya ɗauki rawa tamkar mazari, cikin ƙunan zuciya yafara sambatu lokaci guda kuma yasaki wata mahaukaciyar dariya mai cike da ƙeta,  abayyane yace.

"Aure ko, hmmm lallai kuwa mu dukanmu zamu rasata,  aurenta da kayi bashike nuna cewa ka

mallaketa ba SOORAJ! tabbas kashiryawa rashinta daga yau zuwa sauran ranaku masu zuwa."

(kuyi haƙuri two days bana baku updated da wuri, insha Allah yanzu zannayin ƙoƙarin baku update akai akai saboda inason nima na ƙare labarin soon!)

*Vote*
*and*
*Comment*

fatymasardauna

*Vote*
*and*
*comment*

fatymasardauna
*Vote*
*and*
*comment*

fatymasardauna
*Vote*
*And*
*Comment*

fatymasardauna
Dedicated To My Life (Sardauna)
WATTPAD
fatymasardauna
romance
Chapter 44

Maimaitawarda marokinzaiyi karaf akunnen sooraj wata mummunarfaduwargaba sooraj yaji saikumayasauke nannauyar ajiyar zuciya yasakiwani kayaceccen murmushi wandashikansa baisan ma anar yinsaba yadaiji tamkar ansaukemasa wanidutsene akan kirjinsa.......................✍️nagajizanhutakuyi godiya kunji

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My life Sardauna*

*Wattpad*
@fatymasardauna
#hearttouching

*Chapter 48*

Wani irin zazzafan numfashi ya fesar, tare da sake kamo labb'anta na ƙasa yaɗan tsosa, numfashinsa ne yasoma ƙoƙarin sarƙewa, yayinda ƙirjinsa ke dukan uku uku, gaba ɗaya jikinsa ya ɗauki rawa, haka yakejin kansa na sarawa.

Wasu irin zafafan hawaye ne suka cika idanunta, ayayinda suke gangarawo izuwa gefen fuskarta, wani abu takeji na musamman acikin jikinta,
jitake kamar zata shiɗe, yayinda wasu irin baƙin abubuwawa ke yawo acikin sassan jikinta, tanajin kamar zata zauce.
Hannunsa ya ɗaura adaidai saitin zip ɗin rigar dake jikinta, ahankali yayi ƙasa da zip ɗin rigar, sauƙan da lallausan tafin hannunsa sukayi, akan lallausan skin ɗinta ne, yasanyata sauƙe wata irin ajiyar zucia me karfi, sake ƙara shigewa cikin jikinsa tayi, yayinda daddaɗan ƙamshin turaren sa ke ƙara hura mata wutar sha'awar dake damunta, sannu ahankali, ɗumin bakinta yasanyashi jin wani iri ajikinsa, sake lumshe idanunsa yayi, cikin wani irin yanayin dake fusgarsa, yashiga sucking tongue ɗinta ahankali.
Wani irin sabon abune ke tasowa Zieyaderh, wanda yasanya har takejin kamar numfashinta na koƙarin ƙwacewa, bakomai ya haifar mata da hakan ba kuwa face yanda tausassun lips ɗinsa ke kokari wajen sarrafa tongue ɗinta, wani abune ke tsarga mata har cikin tafin ƙafarta, kamar yanda take ƙoƙarin fusgo numfashinta, wanda ke ƙoƙarin ƙwacewa, hakannne shima ya kasance a bangarensa, lokaci guda idanunsa suka cika da wasu irin k'walla, ahankali yasoma janye bakinsa daga cikin nata, wani irin numfashi mai zafi ya fesar, alokacin dayake zare bakinsa daga cikin nata, sake ɗagota jikinsa yayi, fuskarsa yakawo daidai saitin tata fuskar, bakinsa dake ɗauke da danshin saliva, yakai kan forehead ɗinta inda ya manna mata wani zazzafan kiss,
wanda taji sanyinsa har cikin jikinta, forehead ɗinsu ya haɗe waje guda, wasu irin zafafan hawaye ne suka sauƙo daga cikin idanunta, sosai yaƙara mata wutar sha'awa, saidai kuma awannan karon ba iya zallan sha'awa bane ke damunta, wani irin azabebben ciwon ƙaunarsa ne ke motsa ta, sam bazata iya jure zafin ciwon So da kuma na sha'awa ba.

Ahankali ya bud'e idanunsa wanda suka kaɗa sukai wani irin ja, innocent face ɗinta ya kalla,

kana  ƙasa ƙasa ya kalli yanda kyawawan laɓɓanta suka jiƙe da yawun bakinsa har wani shinning suke,  ahankali yakai bakinsa daidai saitin idanunta, batare da ta tsammata ba, kawai saijin sauƙan bakinsa tayi akan idanunta, inda ahankali ya shiga tsotse hawayen dake maƙale cikin eye lashes ɗinta, wani irin yaarr! haka taji ajikinta, lokaci daya jikinta ya sake, ahankali yake yawo da harshensa akan fuskarta ta, cikin wani irin tsananin tausayinta daya rufesa, yashiga ƙoƙarin danne yanayin dayakeji, kansa ne ke barazanan tarwatsewa, yayinda yake masa wani irin masifaffen ciwo,  ahankali ya ɗaura laɓɓansa adaidai gefen bakinta, har takai ga yana iya kamo leɓen bakinta na ƙasa, harshensa yasanya rabi acikin bakinta rabi kuwa na bisa harshenta, cikin nutsuwa yake ɗan goga harshen nasa akan lips ɗinta,  duka hannayensa yasanya akan kafaɗunta, cikin dauriya yayi ƙasa da rigan jikinta,  yayinda yasanya duka hannayensa,  akan skin ɗin bayanta yana shafawa, bazata iya jurewa ba, hakan dayakeyi mata tamkar wuta yake ƙara kunna mata, jitake kamar yana  tada mata da wani abu acikin jikinta,  bazata iya haƙurin jure rashin daddaɗan saliva ɗinsa abakinta ba, wani irin garɗi takeji acikin saliva dinnasa  wanda hakan yasanya takejin kamar zata zauce,  cikin tsananin shagwaɓa haɗi da ciwon dake nuƙurƙusanta, ta sanya laɓɓanta duka biyu inda ta riƙe tongue ɗinsa,  idanunta sun rufe bataji bata gani, gaba ɗaya ta birkice,  yayinda tsikar jikinta suka mimmiƙe,  ahankali irin na wacce bata taɓa ba,  taɗan tsotsi tongue ɗin nasa, sauƙan tausassun laɓɓanta akan harshensa ne,  yasanya tsikar jikinsa mimmiƙewa, kana kuma jijiyoyin jikinsa suka fito sukayi raɗa raɗa,   lokaci guda yaji mararsa ta  daure,  daga gefe guda kuwa kansane ke barazanar tarwatsewa, lokaci d'aya wani irin zazzafan zazzaɓi ya rufesa,  cikin dauriya da ƙarfin hali yaɗan janyeta daga jikinsa, hannayensa yasanya ya kama duka shoulder ɗinta, jin yanda hannunsa daya riƙeta yaɗauki zafi zau yasanyata buɗe idanunta  wanda suka d'an rage girma,   gani tayi ya rumtse idanunsa, yayinda yake ta aikin jujjuya kansa, da'alama sosae kannasa keyi masa ciwo, tsorone ya kamata,  hakan yasanya takai hannunta, inda  ta taɓa jikinsa, zafi zau haka taji tamkar  garwashin wuta,   cikin wata irin raunanniyar murya tak'ira sunansa, inda tace.

"Ya....ya!."

Idanunsa wanda suka kaɗa sukai ja,  kana  kuma suka cika da ƙwalla ya ɗan bud'e,  ahankali ya kalli cikin idanunta, saurin sadda kanta ƙasa tayi don bazata iya juran kallon yanda cikin idanunsa suka koma ba, infact ma bazata iya jure ganin cikin idanunsa  Wanda suke d'auke da ƙwalla ba, cikin wani irin tsananin tausayinta dake cin zuciyarsa yasanya hannayensa duka biyu yajawota jikinsa,   hannayensa yasake maidawa kan bayanta ahankali ya kai bakinsa saitin kunnenta, cikin wani irin rikicewa da yayi yatura harshensa cikin kunnenta, ahankali yake yawo da harshen nasa acikin kunnen nata,  kana yana me shafa fatar bayanta slowly, ƙasa yayi da ita inda ya kwantar da ita kana shima ya kwanta agefenta, sake matso da ita jikinsa yayi ahankali yake ƙara tura harshensa cikin kunnenta, wani irin ajiyar zuciya take sauƙewa akai akai,   gefe guda kuwa hawayen dake fita daga cikin idanunta ne,  ke sauƙa akan dantsen hannunsa,  sosai hakan da yakeyi mata ya zautar da ita, gaba daya tafara manta duniyar da take, sake shigewa cikin jikinsa tayi,  tana me cusa kanta acikin ƙirjinsa, ji take kamar ta koma cikin jikinsa saboda yanda daddaɗan ƙamshinsa keyi mata daɗi,  sama da mintuna 15 ya ɗauka yanayi mata haka, zuwa yanzu ko kyakkyawan motsi batayi, sosai zafin zazzaɓin jikinsa ke ƙara turarata, sannu ahankali sanyin jikinta yaɗan soma ratsa nashi jikin, cikin son samawa kansa sauƙi daga

tsananin ciwon dayakeji ya ƙara matseta ajikinsa,   atare suke fitarda wani irin zazzafan numfashi,  hannunsa dake rawa ya ɗaura adaidai kan lafeffen cikinta wanda yake kamar zai haɗe da bayanta,  yanayin yanda yake shafa fatar cikin nata ne yasanyata sakin jikinta, ahankali sheshsheƙan kukanta ke tashi,  jin yanda take fitar da sheshsheƙa ne yasanyashi kamo laɓɓanta, ahankali yashiga tsotsa yana me sake matseta acikin jikinsa, kamar yanda bazai iya faɗan tsananin azaban dayakeji acikin jikin nasa ba, haka bazai iya tantance mai yakeji cikin zuciarsa awannan lokacin ba,  tamkar lollipop haka yake tsotsan lips ɗinta, atare suke sauƙe ajiar zucia, hannayenta tasanya akan faffaɗan bayansa, ƙa ƙam ta rungumesa tare da lumshe idanunta,   cikin yanayin yanda yake sucking lips ɗinta,  yasanyata jin wani irin bacci na fusgarta,  ganin kamar tayi bacci yasanyashi soma ƙoƙarin zare bakinsa daga cikin nata, wani sabon kukan shagwaɓa ta saka masa, sam bayason kukanta hakan yasa yaƙara kamo harshenta yana sucking ahankali, lokaci k'ank'ani bacci  ya ɗauketa,  hawayen da suka cika cikin idanunsa ne suka samu daman gangarowa, ahankali hawayennasa ke ɗiga bisa kan kyakkyawar fuskarta, sake hugging ɗinta yayi tight, wani irin tausayinta ne ke ɗawainiya da zuciyarsa,  bai taɓajin zafin ƙaddaransa sosai har haka ba, sai  yanzu daya kasa bata abun da takeso daga gareshi, haƙiƙa baicancanci zama miji agareta ba, yana da rauni, wanda kuma raunin zai iya shafar rayuwarta, wata irin wahalalliyar ajiyar zuciya ya sauƙe, daga gefe kuwa har yanzu jikinsa ɗauke yake da zazzafan zazzaɓi, yayinda yakejin wani irin abu ya riƙe masa waist ɗinsa, sosai yakejin azaba acikin jikinsa, saidai kuma duk da yanda yakejin wahala ajikinsa, baikai ya zuciyarsa dake barazanar tarwatsewa ba,  yanayin yanda numfashinta ke sauƙa akan wuyansa, shi ya sanyashi  lumshe idanunsa, cikin wasu y'an mintuna ƙalilan bacci ya ɗaukesa, haka sukayi bacci lips ɗinsu haɗe dana juna,yayinda bugun zuciyarsu ke tafiya atare.

6:00 am.
Ahankali yaɗan ware idanunsa wanda suka ƙanƙance saboda bacci,   tarwal ya gama buɗe idanun nasa inda ya sauƙesu akan kyakkyawar fuskarta, sosai ya kura mata kyawawan idanunsa,  zara zaran eye lashes ɗinta wanda ke ɗauke da busassun hawaye ya kalla, kana yagangaro da kallonsa harzuwa kan ƴan ƙananan laɓɓanta, wanda cikin yanayi na bacci ta ɗan buɗesu batare da ta sani ba, hannunsa yakai kan kyakkyawar fuskarta inda ya haɗe mata laɓɓan nata waje guda, ahankali ya zare jikinsa daga cikin nata, ƙafafunsa ya zuro ƙasa kana ya miƙe tsaye daga kan gadon, kaitsaye bathroom ya wuce,  shower ya sakarwa kansa inda zuciyarsa ke cunkushe da tarin tunani kala kala,  aƙagauce yayi wanka tare da ɗauro alwala, koda ya fito daga cikin toilet ɗin wata jallabia yasanya tare da shumfuɗa sallaya ya tada sallah, koda ya idar da salla'n, sosai yayi addu'o'i kana yashafa, miƙewa yayi cikin nutsuwa ya ƙarasa gaban sif ɗin kayansa,   ɓangaren da suit's ɗinsa suke ya ɓuɗe, wata haɗaɗɗiyar black shinning suit ya ciro  tare da wata white long sleeve,  koda ya sanya kayan sosai sukayi masa kyau, yayinda suka fitar da cikakken kamanninsa na ma'aikacin  banki, sosai yayi kyau, inda yasanya wasu tsadaddun takalma toms aƙafafunsa,  cumb ya ɗauka inda yashiga gyara kyakkyawan sajen dake ƙarawa farar fatarsa kyau,   turarensa mai daɗin ƙamshi ya fesa, take ƙamshin nasa ya cika gaba ɗaya ɗakin,     wata ƴar madaidaiciyar briefcase ya riƙe ahannunsa, cikin takunsa mai ɗauke da nutsuwa, ya ƙarasa jikin ƙofar fita daga cikin ɗakin, har yakai hannunnsa kan handle ɗin ƙofar saikuma yaɗan tsaya, idan da ason zuciyarsa ne shine  juyawa ya kalleta,

saidai kuma yanajiyewa kansa abun dazai faru dashi nan gaba, bahaka yake ba sam, bakuma yaso ya zama haka, saboda ita arayuwarsa karo na farko daya zubda hawayensa, saboda ita kaɗai yafarajin tsanan kansa da rayuwa, saboda ita kaɗai ya bari akaron farko rauninsa ya bayyana, inda ya zubar da ƙwalla sanadin lalurarsa, sam bayason sakeyin wannan ganganci.
Murɗa handle ɗin ƙofar yayi yafice,  cikin isa yake takunsa har ya kawo compound ɗin gidan, motarsa ƙiran range rover black colour ya shiga, maigadi ne ya wangale masa gate ɗin gidan, shi kuma ya tura hancin motartasa waje.

7:00 am.
Daidai alarm ɗin dake gefen gadon wanda batasan waya saitashi ba yasoma ƙara kamar zaicire kunnen mai sauraro, wannan ƙaran alarm ɗinne yasanyata buɗe idanunta,  ahankali taɗan buɗe idanun nata tare da yunƙurawa ta tashi zaune, kallonta takai ga window'n ɗakin, nan taga gari gaba ɗaya yayi haske, bayanta ta jingina da saman gadon, cikin gajiyawa da jin ƙaran alarm ɗin tasanya hannunta ta kashe,  dogon gashinta da yake a hautsine ta haɗa waje ɗaya, lumshe idanunta tayi, yayinda take shaƙan daddad'an ƙamshin da ɗakin ke fitarwa, lokaci guda moment ɗinsu na daren jiya yashiga dawowa cikin ƙwaƙwalwarta, wani irin mimmiƙewa tsikokin jikinta sukayi, yayinda takejin wani irin yaaarrr acikin jikinta,  kamar yanda bazata taɓa iya mantawa da kanta ba, haka tayi imani bazata taɓa iya mantawa da moment ɗinsu na daren jiya ba, sake lumshe idanunta tayi musamman tuno yanda yake tsotsan harshenta slowly da tayi,  wani irin ɗanɗano na musamman yawun bakinsa ke ɗauke dashi, laɓɓanta taɗan ciza ahankali don kuwa haryanzu tanajin marar nata nayi mata ciwo kaɗan kaɗan, cikin rashin kuzari ta sauƙo daga kan gadon, kayan jikinta ta cire,  inda ta ɗaura wani sky blue towel aƙirjinta, wanda ya tsaya zuwa kan santala santalan cinyoyinta farare ƙal ƙal, wanda ɗigon tabo ɗaya babu akan shinning skin ɗin nata mai tsananin taushin gaske.  Ruwa me ɗan ɗumi ta haɗawa kanta, inda dashi tayi wanka, bayan tayi wankanne ta ɗauro alwala, sam bataji dadɗin makaran da tayi ba,  wata simple women gown ta zura ajikinta inda ta sanya hijab,  sallah tayi, tana idarwa taɗanyi azkar kana ta mik'e.
Wani irin fitinannen yunwa takeji na ƙwaƙulan cikinta, kasancewar rabonta da abinci tun jiya da yamma,  ɗaure dogon gashin kanta tayi batare da ta sanya ɗan kwaliba ta fita zuwa falo, ko ina ta kutsa kanta saitaji wannan fitinannen ƙamshin nasa na neman ruguza mata zuciya, ita tarasa wannan wani irin turarene wanda ajikinsa kawai takejin irin ƙamshin.
Kaitsaye kitchine ɗin dake cikin falon ta nufa,  duk da kasancewar tanajin yunwa, amma batajin cewa wani abu na abinci zaisamu mazauni acikin cikinta, tea ta haɗa kana ta dawo falo ta zauna, tanƙwashe ƙafafunta tayi yayinda ahankali take sipping tea ɗin, wayarta wanda tunjiya take aje kan table ɗin dake tsakiyar falon ne, takawo haske, lokaci guda kuma sassanyar muryan mawaƙinnan  Atif Aslam tasoma tashi acikin wayar alaman shigowar k'ira, ɗan yunƙurawa tayi ta ɗauki wayar.
"Shukra" Shine sunan dake yawo akan screen ɗin wayar, cikin hanzari ta ɗaga ƙiran tare da karawa akan kunnenta,  kafun tace wani abu Shukra tayi saurin cewa.
"Amarya bakya laifi koda kuwa ace kin ciji ango!."

Ɗan ƙaramin bakinta taturo gaba cikin yanayinta me ɗauke da sanyi tace.
"Bakida wani abun da zakicemin ae Shukra, yanzu ƙin zuwa da kukayi keda Nasmah kun

kyauta kenan?."
Dariya Shukra tayi, cikin yanayi na tsokana tace.
"Rufa mana asiri mu mutu agida maza sukaimu ba mata ba, mu ƴan gidan zuwa, me zamuzo muyi miki keda kike ƙarɓan special lecture awajen Mr.Handsome ɗinki, mukan ae dai kuma saita waya!."

Tsuka Zieyaderh tayi cikin ƙosawa da tsokanan da Shukran keyi mata tace.
"Nifa banason iskanci Shukra, ƴar iska kawai."

Dariya sosai Shukra da Nasmah wacce kejin duk maganganun Zieyaderh'n suka sanya, jin dariyar Nasmah yasanya Zieyaderh sake ɓata fuska, ahasale tace.

"Kun maidani mahaukaciya ko?."

Ɗan gumtse dariyannasu sukayi, cikin salon tsokana Nasmah tace.

"Sorry ƙawata, ya tsamin jiki, nasan fushi kikeyi damu, am so sorry idan muka haɗe a school zamu taushi zuciyarki."
Shukra ne ta caɓe da cewa.
"Inafatan dai kina gwada masa irin wannan salon shagwaɓan naki, dannasan idan kina gwada masa ko aiki bazaina fita ba."
Gyara zamanta tayi cikin zaƙuwa tace.
"Dan Allah ƙawata faɗamin aure da daɗi ko? hmmm nima Inatsananin son aure, gaskiya bazan iya jurewa ace harsai na ƙare secondary school ba, seriously na ƙosa nima nazama cikakkiyar mace."
Shukra tafaɗi maganan dayake har cikin zuciyarta hakane, duk da kasancewar basu da wani shekaru masu yawa, amma tagamsu da cewa yin aure tun mace nada yarintarta yafi komai daɗi, sannan kuma maza da yawa sunfi sha'awar ƙananan yara kamarsu, badon komai ba saidan suna da daɗin zama, ita yarinya aduk yanda ka koyar da ita haka zaku tafi, bata da wani buri kaman ganinta tare da mijinta tana zuba masa shagwaɓa da sakalci, yayinda shikuma zaizama tamkar soko akanta, sam ita bazatayi wannan dogon karatun awaje kamar yanda wasu keyi batare da tayi aure ba, saboda yawanci hakan najawo matsala sosai ga rayuwar ƴa mace, saboda awannan lokacin da kayi zurfi cikin karatu bakowane zaiji sha'awar aurenka ba, sannan kuma ba lallaine kasamu irin mijin da kake muradi ba.

Hararan wayan Zieyaderh tayi tamkar suna ganinta, cikin gajiya da tsokanar tasu tace.
"Allah yashiryaki Shukra,nikam yanzu kinfi ƙarfina."

Fari da ido Shukra tayi tare da cewa.
"Naƙirane dama na tuna miki cewa next week zamu koma school, so sauran bayanin sai mun haɗu a school, nasan zuwa yanzu kin ƙara fresh, hope baki manta islamic lecture'n da akayi ranan a school ba?."

Kunyane ya rufe Zieyaderh, cikin ƙosawa tace.
"Allah yashiryaki Shukra, bazaki taɓa sanjawa ba."

Dariya suka saka atare, inda sukayi sallama akan cewa sai sun haɗu a school din.

Awannan rana haka Zieyaderh taƙare zamanta agidan ita kaɗai.

Dare nayi tana idar da sallan isha kuwa bacci ya ɗauketa anan falo kan kujera, yauma baidawo gidanba sai ƙarfe 9, ganinta kwance afalo yasanyashi wucewa ɗaki kai tsaye, wanka yayi inda yashirya kansa cikin ƙananun kaya marassa nauyi, kwanciya yayi akan gado tare da jawo blanket ya rufe jikinsa, da tunani kala kala acikin ransa, haka bacci ya ɗaukesa.

Yauma kamar jiya tun 6:00 am yafice daga cikin gidan, haka ya wuceta kwance afalo tanata sharar bacci, koda ta tashi taganta kwance afalon baƙaramin mamaki tayi ba, nan tatuna da cewa baccine ya ɗauketa jiyan batare data shiryawa hakan ba, kaitsaye bedroom ta nufa, sannu ahankali take ƙarewa cikin ɗakin kallo, komai dake ciki nead, da dukkan alama dai babu wani wanda ya kwana acikinsa, cikin zuciyarta tace.
"Kenan baidawo ba? ko yayi tafiya ne?."
Sanin bata dame amsa mata tambayoyin nata, yasanya ta wuce toilet, wanka tayi, yauma dai ta makara hakan yasa ta ɗauro alwala tazo ta gabatar da sallah.
****
Wasa wasa yau kwananta 6 bata sashi acikin idanunta ba, kullum batajin motsinsa, batasanin fitansa ba kuma tasanin dawowarsa, daga gefe guda kuwa wani irin masifaffen kewarsa ne ke ɗawainiya da zuciyarta, sosai takejin wani abu na daban akansa, sannan kuma aduk sanda ta tuna da moment ɗinsu na ranan, saitaji wani irin feeling ya taso mata, sosai take buƙatan hakan daga garesa, sau ɗaya tak yashayar da ita yawun bakinsa, amma gaba ɗaya hakan ya zautar da ita.

Zaune take jigum akan gado, wata sleeping gown ne ajikinta me kalan light pink, sosai rigan tayi mata ɗas ajiki, wani ɗan madaidaicin hijab ta ɗaura akan rigan, baccine cike a idanunta, amma haka take ƙoƙarin shanyewa, kasancewar gobe ne zasu koma school hakan yasa tun da yamma tagama kimtsa duk wani abu da zata buƙata, tuni har gugan uniform ɗinta tayi, kasancewar tagaji da zaman gidan, yasanya har Allah Allah take gobe tayi.
Yau ta ƙuɗurta aranta cewa bazata taɓa yin bacci ba harsai ta ganshi, takuma sanardashi maganan komawarsu makaranta gobe,don sunyi waya da Oummu, inda Oummu dakanta tace tasanar da shiɗin cewa gobene komawarsu school, saboda yanzu dole saida izininsa za take zuwa school ɗin.

Sama da mintuna talatin taɗauka zaune akan gadon har bacci yaɗan ɗauketa batare da ta shiryawa hakan ba.
10 pm daidai ya shigo cikin gidan, yana shiga cikin ɗakin yasoma rage kayan jikinsa batare daya kula inda take ba, towel ya ɗaura akan waist ɗinshi inda ya nufi bathroom, kwana biyunnan baƙaramin azabtuwa yakeyi ba, sosai yakejin zafi azuciyarsa, shikansa yanajin kamar

yana hora zuciyarsa da horo mafi girma, baisan meyasa abun dayakeji ajikinsa ke ƙara yawaita kullum ba, ƙaran ruwan dake tashi daga cikin toilet ɗinne yayi sanadiar buɗe idanunta, Ajiyar zucia ta sauƙe, tare da ɗan langwaɓar da kanta gefe, fargaba ne aranta don batasan daya zata fuskancesa da maganan ba.

Baiwani jima cikin toilet ɗin ba, yafito, farar bathrube ne ajikinsa, gaba ɗaya kansa jiƙe yake da ruwa, kaitsaye gaban mirror yanufa, da wani ɗan ƙaramin towel ya goge jikakkiyar sumar kansa. yana gama tsane ruwan ya tako ahankali ya zauna abakin gadon, wani ɗan madaidaicin table yajawo gabansa, inda ya ɗaura laptop ɗinsa akai, cikin nutsuwa yashiga ajiye wasu bayanai cikin Email ɗinsa.

Ahankali taɗan sauƙo daga kan gadon, kanta aƙasa ta tako har zuwa inda yake, samun kanta tayi da durƙusawa agabansa tare dayin ƙasa da kanta, cikin rashin sanin madafa tasoma murza ƴan yatsun hannunta, bugun zuciyarsa data tsananta ne yasanyashi gane cewa tana kusa dashi, lumshe idanunsa yayi batare daya buɗe ba yace. "Menene?."
Kaman dama shitake jira, gyara zamanta tayi cikin nutsuwa haɗi da yarintar dake ɗawainiya da ita tace...
"Dama...umm dama gobe hutun mu na school zai ƙare, shine Oummu tace na gaya maka."

Shiru yayi tare da ɗan juyowa ya sauƙe shanyayyun idanunsa akanta, jin yayi shiru ne yasanyata ɗan cije laɓɓanta, ahankali ta ɗago fararen idanunta aniyarta shine taɗan saci kallonsa, karab idanun ta suka sauƙa cikin nasa idanun, ganin yanda idanunsu suka sarƙe cikin najuna ne, yasanyata ɗan lumshe idanunta, kana takuma buɗesu alokaci guda, cikin wani irin yanayin da ƙwayan idanunnasa suka shigar da ita taɗan kwaɓe fuska kamar wacce ke sonyin kuka, ahankali take motsa bakinta kamar wacce takeson faɗan wani abu, karo na farko kenan arayuwarsa dayaji don kansa yana sha'awan yin kissing ɗin bakinta, sannu ahankali yakejin gargasan jikinsa na buɗewa, lumshe idanunsa yayi don bazai iya jurewa abun dayakeji ba, can ƙasan maƙoshi yace.
"Naji kije ki kwanta."
Jin maganarsa yasanya taji zuciyarta tayi mata sanyi, ahankali tatashi ta koma kan gadon, nannaɗewa tayi acikin lallausan blanket ɗin dake ta tashin ƙamshinsa, cikin wani irin shauƙi ta cusa kanta acikin pillow, ahankali take sauƙe ajiyar zuciya akai akai, ta rantse aduniya itakam bataga wani kyakkyawa mai kyawawan idanu tamkarshi ba, shi komai nasa na musammanne, magana ma yanayinta ne kawai alokacin dayaga dama, zuciyarta cunkushe da tunaninsa haka tayi bacci.

Shikuwa SOORAJ duk yanda yaso cigaba da aikin nasa kasawa yayi, don wani irin baƙon al'amarine ke ziyartar gaba ɗaya gangar jikinsa, akasalance ya rufe laptop ɗin tare da miƙewa tsaye, ahankali ya karasa gaban sif d'in kayansa, wani 3 guater jeans ya sanya, yayinda Kai tsaye ya nufi kan doguwar kujeran dake cikin dakin, kwanciya yayi tare da lumshe idanunsa, kasancewar adan gajiye yake yasanya baiwani jimaba bacci b'arawo ya d'aukesa.

Duk sammakon tashi da ta buga, Saida ta samu yarigayeta tashi, don ko da ta tashi daga

baccin tsaraban k'amshinsa kawai ya barmata, cikin tsanaki tayi wanka, tana idar da sallah ta dauki sassanyan body lotion dinta Mai dadin kamshi tashiga shafawa ajikinta, sama sama ta shafa powder, wani dan pink lipstick ta goga akan labbanta, kamar yanda take ko yaushe bata cika  kwalliya ba, hakama yanzun batayi wani kwalliya ba, dogon sket high waist, and long sleeve ta sanya, Wanda sune suke mazaunin kayan uniform dinta,   tubke dogon gashin kanta tayi inda ta zura Dan madaidaicin hijab din makarantar tata, Wanda tsayinsa ya kawo harkan cikinta, katuwar school bag dinta ta rataya bisa kafadanta, agurguje haka tafita daga cikin dakin don kuwa lokacin har bakwai da rabi tayi, kamar da can baya yau dinma Kamalu driver ne ya kaita makarantar, sosai sukayi murnan ganin juna ita dasu Shukra,  ba ita tasamu daman karyawa ba, Saida suka fita break, sosai yau din taji dadin makarantar saboda koba komai ya kore mata kadaici.

5 daidai aka tashesu atare suka jero tare da su Shukra, tafe suke suna hira harsuka iso babban compound din makarantar,  tuni driver'n Nasmah yazo daukarta saboda haka tayi musu sallama tatafi, tana tafiya kuwa saiga driver'n gidan su Shukra shima yazo daukarta, haka suka watse sukabar Zieyaderh ita kadai, agogon dake daure atsintsiyar hannunta takalla 5:16 pm,  fuska tadan kwabe tana me sake ware idanunta wai ko zata hango Kamalu, sannu ahankali hadaddiyar motar da takawo Kai cikin makarantar ta karaso gareta,  agefe da ita kad'an motar wacce tasha tintect ta faka,  bude murfin motar yayi tare da zuro da k'afafunsa k'asa,  sannu ahankali ya fito gaba dayansa daga cikin motar, Sanye yake da k'ananan Kaya, yayinda ya manna sun glass akan idanunsa,   Sam Bata kalli gefen da yake ba, cigaba tayi da duddubawa ko zata hango Kamalu driver, amma abun mamaki ko irin motarsu Bata hango ba.

Wani irin bak'on k'amshin da yaziyarci hancinta shiya Sanya tadan waiga bayanta, donjin daga Ina k'amshin ke fitowa, sauke idanunsa akanta yayi daidai da bugawar zuciyarta, lokaci guda kirjinta yayi wani irin tsalle kamar zai fad'o, cikin tsananin mamakin ganinsa tadan zaro idanunta waje,
wani irin kawataccen murmushi yayi mata, cikin takunsa ya karaso gab da ita,  tsakanin su bai wuce saura taku daya ba ya tsaya tare da  lumshe munafukan idanunsa, sun glass din ya zare daga kan idanunsa, inda ya waresu tas akanta, wani irin kallo, Mai dauke da tsananin shauki ya bita dashi, cikin kwantar da murya yace.

"I missed you so much babe, ganinki ya fiye min komai ayanzu, I Love you so so much!"
Pharouk Yakare maganan Yana me byyana zallan shaukin dake ransa afili, kanta ta sunkuyar kasa, samun kanta tayi da kasa ce masa komai, batare da zato ko tsammani ba taji ya kamo hannuwanta, arazane ta d'ago kanta ta dubeshi, kansa ya langwabar gefe cikin salo irin nasa yace.
"Bazan iya jure rashinki ba, duk da nasan cewa anyi Miki Dole wajen aura masa ke, Inasonki Zieyaderh, burina shine kasancewa dake, please Kar kice Zaki rabu Dani, karkice zaki k'i aminta Dani, Inasonki!."
yakare maganar Yana me kokarin murza Yan yatsun hannunta, gaba daya ta rude tana kokarin zare hannunta, Amma rikon da yayi mata bana wasa bane.
Daidai lokacin wata hadaddiyar mota Kiran 4matic takawo Kai cikin makarantar, gaba daya fiye

da Rabin daliban makarantar kowa ya kama gabansa, Yan tsirarune kawai suka rage, irinsu Zieyaderh da ba'azo daukarsu da wurine ba.
Ahankali yayi parking motar inda dagowan da zaiyi idanunsa suka Masa mummunan gani, ganin daya sanya kirjinsa wani irin dokawa, ganin daya sanyashi Jin wani irin d'aci amak'oshinsa, ganin daya sanyashi jin wani irin jiri yayinda wani irin tari ya taso masa, har takai numfashinsa na kokarin carkewa.

(Bani da bakin da zan baku hakuri bisa jinkirin yi muku update dana samu, wallahi wani babban uzurine ya rikeni, ina fatan zakumin uzuri, insha Allah gobe zan baku page 49 sannan zanyi kokarin Yi muku typing kullum insha Allah, saboda nikaina nakosa nayi ending labarin.... Son So nake muku my fans Dina...)
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ!!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life Sardauna*

*Wattpad*
@fatymasardauna
#love

*Chapter 49*

Idanunsa ne  suka kad'a sukai ja,  lokaci guda gargasan dake kwance  ajikinsa suka mimmik'e, idanunsa ya rumtse,  yana  mejin wani irin abu da ya taho ya tokare mak'oshinsa.
Cikin yanayi na tsoro ta shiga girgiza kanta,  da k'arfi ta fusge hannunta dake cikin nasa, hawayene suka shiga gangarowa daga kan fuskarta,  cikin sauri ta juya da niyar barin wajen, idanunta ne suka sauk'a akansa, inda yake zaune cikin motarsa yana kallonsu, wani irin bugawa k'irjinta yayi, take wani irin mummunan fad'uwar gaba ya rusketa, wasu sabbin hawayene suka kwaranyo daga cikin idanunta,  zuwa kan fuskarta.

Wani  k'awataccen murmushi Pharouk yasake,  tare da d'an satan kallon SOORAJ wanda ke zaune acikin motarsa,  inda ya d'auke kae yayi kamar ma baigansuba,  murmushin mugunta Pharouk yayi, yana mejin wani irin sanyi na ratsa zuciarsa,  komai da gangan yayi, don kawai ya k'untata zuciyar SOORAJ d'in,  yanasane da Zuwan SOORAJ d'in shiyasama ya rik'o hannayenta,  duk da cewa sha'awar da yakeyi mata nada yawa, amma kuma awani b'angare na zuciyarsa yanajin soyayyarta,  hannunsa yakai da niyar sake tab'a hijab d'inta, saidai yayi rashin sa'a don kuwa tuni tasoma tafiya, hannayensa ya zura cikin aljihun wandonsa inda ya k'urawa bayanta ido,   tsoro fargaba sune abun da suka cika zuciyarta, cikin yanayin sanyin da jikinta

yayi ta k'araso jikin motar,  cikin tsoro ta bud'e murfin motar,  Sassanyan k'amshin turarensa da ya bugi hancinta ne yasanya tsikar jikinta mimmik'ewa, cikin rashin kuzari ta shiga cikin motar, kafunma tayi yunk'urin daidaita zamanta yafigi motar da wani irin speed,  kan Pharouk dake tsaye yayi da motar, ihu Zieyaderh tasanya tare da rumtse idanunta, don taga dagaske kan Pharouk d'in ya nufa,  saida yakawo gaf da Pharouk d'in sannan ya taka wani irin birki Wanda yasanya harsaida kanta ya bugu da gaban motar,   Ido cikin ido suke kallon juna shida Pharouk d'in,  wani irin kallo Wanda ke k'unshe da zallan gargadi SOORAJ ya watsawa Pharouk, tare saying wani irin reverse, murza steering mota yayi,  cikin wani irin speed yanufi hanyar fita daga cikin makarantar yayinda ya bud'awa Pharouk k'ura, daga kan jikinsa harzuwa kan fuskarsa,  da gudu masu gadin gate d'in makarantar suka mammatsa gefe, sakamakon ganin yanda motar tayo kansu.

Da k'arfi Pharouk ya rumtse idanunsa,  yana mejin wani irin bak'in ciki na ratsa zuciyarsa, kallon jikinsa yayi,  gaba d'aya kayan jikinnasa sun b'aci da k'ura,  ransa ne ya b'aci,   saidai kuma tunawa dayayi cewa ya isar da sak'on da yakeso na bak'in ciki azuciyar SOORAJ, yasanyashi jin sanyi a ransa, haka yashiga motarsa yabar makarantar, zuciarsa na k'issima masa abubuwa da yawa.

Sosai ta tsorata da irin gudun da yake shararawa akan babban titin, cikin rufewar ido yake tuk'i, gaba d'aya jikinsa rawa yake, matsanancin b'acin rai ne kwance akan kyakkyawar fuskarsa, sosai zuciyarsa ke tafasa, wani irin d'aci yakeji amak'oshinsa,  idanunsane suka sake kadawa sukai ja,  yayinda jijiyoyin dake kansa suka mimmik'e  inda suka fito sukayi rud'u rud'u.

Sam bayako iya ganin gabansa da kyau, dayawan motoci ke kauce masa ahanya, don kuwa kowa yaga irin tuk'in da yakeyi yasan bana lafiya ba.

Wani irin mahaukacin horn yake dannawa kamar zai dage unguwar bak'i d'aya,  da wani irin hanzari maigadi ya wangale masa gate d'in gidan,  dan shi kansa ya tsorata da irin yanda maigidannasa ke danna horn kamar zai tashi sama.

Dagudu yatura hancin motar ciki,  wani mahaukacin parking yayi,  inda ko second d'aya bai k'ara acikin motar ba ya bud'e murfin motar ya fice,  wasu sabbin hawayene suka silalo daga cikin idanunta, sosai tahango matsanancin fushi akan fuskarsa , jikinta amatuk'ar sanayaye ta bud'e murfin motar ta fito.

Koda yashiga falon kaitsaye bedroom ya wuce, yana shiga ya bugo k'ofar da k'arfi, cikin yanayinta me d'auke da sanyi tashigo cikin falon, ganin bata gansa acikin falon bane yasanyata zubewa akan sofa,  idanunta wanda har yanzu ke tsiyayar hawaye ta lumshe.

Akan gado ya zauna tare da sanya duka hannuwansa biu ya dafe kansa da yakejin kamar zai tarwatse,  sosai zuciyarsa keyi masa zafi,  rumtse idanunsa ya kuma yi da k'arfi, sakamakon tuna wa da yanda yaga hannuwansu sarke cikin na juna,
Jikinsa ne ya d'auki rawa sosai cikin tsananin b'acin rai yayi wurgi da bedside lamb din dake

gefen gadon,   wani mak'ak'i ne kedamun zuciyarsa,  baitaba jin zafi irin haka ba,  baisan wannan bak'on Al'amarin ba, saboda haka bazai iya jurewa ba,    wani irin tari  ne ya sarke mak'oshinsa,  sosai yake tarin ba k'akk'autawa, cikin yanayin gajiyawa daya dan soma shiga, ya d'auki wani farin handkerchief, inda yashiga goge jinin dake fita ta bakinsa, saboda tsabar tsananin b'acin rai har wani d'aci yakeji a mak'oshinsa.
Ahankali taturo kofar dakin tashigo,  idanunta ne suka sauk'a akansa, cikin firgici ta zazzaro idanunta waje, sosai jinin da tagani abakinsa ya razana ta,  d'ago kansa yayi inda idanunsa suka sa'uka acikin nata,  afusace ya tashi daga zaunen da yake, ya nufota, yana k'arasowa ya damk'i hannunta,  ransa amatuk'ar bace ya bugi k'ofar d'akin, har saida ta bud'e, da k'arfi ya hankad'ata waje tare da jawo kofar d'akin ya rufe,  kana ya murzawa kofar key,   wani irin bugewa kanta yayi da jikin kujera asakamakon wurgota da yayi,   kuka ta sake mai sauti, inda lokaci guda jikinta ya d'auki rawa, bata tab'a ganinsa acikin irin wannan yanayin ba, sosai yanayin idanunsa suka tsorata ta,  kanta ta cusa atsakankanun cinyoyinta,  kuka take sosai tare da matse jikinta waje daya.

Cikin yanayin b'acin ran dayake ciki ya bud'e k'ofar bath room ya shige, sosai zuciyarsa ke tafasa hakanne yasanyashi kunna shower, tare da tsayawa ruwa na dukan
jikinsa, ak'alla ya d'auki kusan sama da mintuna talatin yana tsaye ruwa na dukan jikinsa, har yanzu zuciyarsa tafasa take,  daya kulle idanunsa su kawai yake gani,  yanajin kamar ana caccaka masa wuka akan kahon zuciyarsa, da k'yar ya iya kashe shower'n,  farin bathrube ya sanya ajikinsa, haka ya fito daga cikin toilet d'in zuciyarsa duk ba dad'i, ko tsayawa goge jikinsa baiyi ba, ya zura wani dogon trouser ha'e da wata farar long sleeve marar nauyi,   zama yayi akan bedside tare da sanya hannuwansa ya dafe kansa dake masa ciwo,  Sam bayajin dadin jikinsa,, rumtse idanunsa yayi da k'arfi, ahankali sautin kukanta ke shiga cikin kunnuwansa, labb'ansa yadan ciza da k'arfi,
sam bayason kukanta, jin kukanta daidai yake da d'iga masa narkakkiyar dalma akan fatar jikinsa, zai iya jure komai amma banda kukanta,   hannayensa yasanya ya toshe gaba d'aya kunnuwansa, mekenan? Me hakan yake nufi? ganinta da Pharouk yasanyashi jin wani irin rad'ad'i acikin zuciya da gaba d'aya ilahirin jikinsa, yanajin wani irin abu me d'aci ya toshe masa mak'oshi,    idan har hakan dayaji akanta shine abun da ake Kira KISHI, to tabbas yana matsanancin kishinta,  Inda KISHI kuma akwai SO,  duk da cewa baisan menene SO ba, haka baisan tayaya zai misalta abun da ya keji a zuciyarsa ba, ajiyar zuciya ya sauke, tare da jingina bayansa da jikin bango, Ya yarda yana mata wani irin TSANANIN SO,  baisan yaushe kuma da yaya hakan ya kasance ba,  amma tabbas yayarda cewa yana cikin magagin Soyayya.

Kuka take sosai tana fidda sheshsheka,  bazata tab'a iya jure fushinsa agareta ba,  babban abun daya daga hankalinta shine jinin da taga yana fita daga bakinsa, bataso ace sanadinta ya shiga wani hali,  taya zata fahimtar dashi cewa hakan da ya faru ba laifinta bane?  yaza'ayi ya fahimceta, k'ara sautin kukanta tayi tare da matse jikinta ajikin kujera.

Abu wasa wasa har dare ya rufa SOORAJ bai bud'e kofar dakin ba, ko sallan magriba da isha ma duk cikin dakin yayi,  itakuwa Zieyaderh sai kitchine ta shiga tayi alwala,  inda ta gabatar da salla, akan tattausan chanies carpet din dake malale tsakiyan falon,  koda ta idar da sallan isha

kwanciya tayi akan carpet din tare da dukunkune jikinta waje d'aya , wani irin azababben sanyi ne ke shiga jikinta, kasancewar garin akwai hadari sosai shiyasa ko ina ya dauki sanyi, sannan has wata sassanyar iska me dadi da ke hurawa, tana a duk'un kune taji sauk'an ruwan sama. shaaa kamar da bakin k'warya, sake matse jikinta waje d'aya tayi tare da cusa kanta cikin hijabin makarantar dake jikinta, sannu ahankali sautin sheshshekan kukanta ke tashi.

Ahankali ya zuro da kafafunsa kasa daga kan gadon, idanunsa ya sauke kan hadadden agogon dake sakale jikin bangon dakin, 10:30 pm daidai har zuwa lokacin kuma ruwa ake sosai da sosai, dan lumshe idanunsa yayi aransa yanajin wani dan zafi zafi, mikewa tsaye yayi inda ya karasa jikin kofar dakin, hannunsa ya daura akan handle din kofar tare da murza key d'in dake jiki, bude kofar yayi ya fito, tsaye yayi ajikin kofan yana me kallon yanda ta takure Jikinta waje d'aya da'alama sanyi takeji sosai, wani irin tausayinta ne ya cika zuciyarsa, ahankali ya tako zuwa tsakiyan falon, hannunsa yakai jikin makunnin wutan falon ya kashe, karasowa inda take yayi Dan sunkuyo wa yayi tare da sanya hannuwansa ya dagota jikinsa, kaitsaye daki ya nufa da'ita, akan lallausan gadon ya shumfudeta, cikin nutsuwa ya shiga Karena kyakkyawar fuskarta wanda yake dauke da bushashshen hawaye kallo, bacci take amma kallo d'aya zakayi mata kafuskanci cewa batacikin yanayi me dadi, tunowa da yanda yaga Pharouk rike da hannunta ne yasanyashi rumtse idanunsa, wani irin masifafffen kishinta yakeji, tabbas idan bacirewa Pharouk hannayensa yayi ba bazai taba jin sanyi acikin zuciarsa ba, wani irin tsanar Pharouk yakeji na Kara ruruwa acikin zuciarsa.

Cikin yanayin baccinta tajiyo daddadan kamshinsa na gauraya da numfashinta, ahankali ta bude idanunta Wanda suka kankance, idanunsu ne suka sarke cikin na juna, wani irin bak'on abune ke ratsa jiki da jijiyoyinsu, cikin yanayi na shagwab'a ta kwab'e fuska sai kuma ga hawaye na gangara agefen fuskarta, bakinta dake d'an rawa ta bud'e, so take tace dashi wani abu amma takasa, sai Kawai ta fashe da kuka mai sauti, hannunsa ya daura akan labb'an bakinsa, dan lumshe idanunsa yayi asanyaye yace. "Shiiiii!!!."
Had'iye kukan nata tayi, cikin matsanancin rauni ta Kalli kyakkyawar fuskarsa.
Hannayensa yasanya ya tallafo bayanta, ahankali ya zare hijab d'in dake jikinta, hannu yakai jikin makunnin wutan d'akin ya kashe, inda bedside lamb kawai ya bari akunne, ahankali ya d'aura hannunsa ajikinta, aninayen dake jere reras agaban long sleeve d'in dake jikinta yasoma b'allewa har saida ya b'allesu gaba d'aya, take cikakkiyar suran k'irjinta ya bayyana, cikin nutsuwa ya zare rigar daga jikinta gaba d'aya, kok'arin kare breast d'inta tasomayi, nan ya sake tallafo bayanta Wanda hakan
yabawa tudun breast d'inta daman sauk'a akan naked chest d'insa, kasancewar dama babu riga ajikinsa, atare suka sauk'e wani irin ajiyar zuciya mai k'arfi, wani irin abune yaji yatsarga tun daga kansa har zuwa tafin k'afarsa, sosai sauk'an naked breast d'inta akan chest d'insa ya birkita masa lissafi, cikin wani irin yanayi mai wuyar fassaruwa ya d'aura bakinsa akan nata, atare numfashinsu yakusan d'aukewa sakamakon yanda wani irin d'umi ya ratsa gaba d'aya cikin jikinsu, sauk'an bakinsa acikin nata shiyasanyata shid'ewa, take gaba d'aya tsikan jikinta suka mik'e, cikin wani irin bakon yanayin daya samu kansa ciki yake tsotsan harshenta Wanda yakejinsa kamar sweet, yanda nipples d'inta ke gogan nasa ne yasanyashi jin kansa acikin wata duniya ta daban, wani irin numfashi yake fitarwa mai d'auke da sautuka Kala Kala, harshensa

ya tura
cikin bakinta inda yayi amfani da labbansa wajen kamo lips d'inta ya basu wani irin hot socking, ya k'udurta aransa cewa yau zai mai da'ita cikakkiyar mace, k'asa yayi da hannunsa inda ya sauk'e su akan mararta Wanda take a shafe, yawo da hannun nasa yasomayi akan lafaffen cikinta, sannu ahankali yake k'ok'arin kai hannunsa kan tsayayyun breast d'inta.

(Am sorry to say wani uzuri yatasomin Wanda yasanya zan d'an bar online na d'an wasu kwanaki maybe nayi 3 to 4days maybe kuma nawuce haka, so kud'an yi hak'uri Dan Allah Insha Allah dana dawo zan d'aura daga inda na tsaya. )

*Vote*
*and*
*comments*

fatymasardauna

*Vote*
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ !!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life Sardauna*

*Wattpad*
@fatymasardauna
#fantasy

*(Wannan fejin baki ɗayansa sadaukarwace agareku masoya littafin SOORAJ!!! haƙiƙa kun ƙaunaci book ɗin nan sosai da sosai shiasa na baku kyautar wannan fejin saboda ina ƙaunar ganinku cikin nishaɗi, duk wata mai karanta wannan littafin nawa, wato SOORAJ!!! to tasani /kasani, wannan fejin sadaukarwane agareki/ka.)*

*Chapter 50*

Lumshe idanunsa yayi wanda suka tashi daga farare suka koma launin ja, atare suke fitar da wani irin numfashi, kamar yanda gangar jiki da ƙirjinsu ke haɗe waje ɗaya haka ma zuciyoyinsu ke bugawa atare cikin nutsuwa, sosai ɗakin ya ɗauki shiru babu abun dake tashi cikinsa, sai ƙaran A.C da kuma sautin yanda breath ɗinsu ke fita, idanunsa yasake lumshewa tare da sake mannata ajikinsa, sosai ɗumin jikinta ke sanyawa yanajin wani irin abu na musamman ajikinsa.

jikinsa rawa yake, haka kuma zuciarsa bugu take, cike yake da tsantsar tsoro, haɗi da fargaba, baisan me zai biyo baya ba,  bai taɓa yiba, baisan ya akeyi ba, saidai kuma ina zaikai haƙƙinta dake kansa?

Idanunsa wanda suka cika da ƙwalla ya ɗan buɗe ahankali, cikin nutsuwa ya zare bakinsa daga cikin nata,  inda  ya sauƙe ganinsa akan baby innocent face ɗinta,    ahankali take fitar da wani irin wahalallen numfashi,  sam bazata iya tantance yanayin da take ciki ba,  sosai takejin wani abu na yawo ajikinta,  gaba ɗaya ya hargitsa mata lissafi, wani irin abu me ɗumi ne ke fita daga ƙasanta,  tabbas idan ya barta haka bazata iya jurewa ba, ya kaita wani mataki wanda tunda take aduniyarta bata taɓa zuwa ba,   takai ƙololuwa, saidai kuma har yanzu batasan me ɗaya take buƙata daga garesa ba, kiss, romance, sex, duk acikinsu takasa tantance wanne take muradi.
Ahankali ta buɗe idanunta wanda suke cike tab  da mayen sha'awa, sauƙe ganinta tayi akan pitch colour lips ɗinsa, wanda suke ɗauke da  danshin saliva asamansu,  idanunta na sauƙa acikin nasa idon tayi saurin lumshe su, don sam bazata iya jure ganin cikin idanunsa ba, domin tamkar magnet haka  idanun nasa suka zame mata, dazaran ta kallesu kuwa feeling ɗinta ne ke ƙaruwa,   wani irin yawu ya haɗiya amaƙoshinsa,  ahankali ya sauƙe idanunsa akan breast ɗinta,  sosai yaji tsikar jikinsa sun tashi, yayinda yaji wani irin abu na ratsa  tsakar kai har zuwa tafin ƙafansa, jijiyoyin kansa ne suka mimmiƙe,   awajen jikinsa haka yakeji tamkar ana watsa masa ruwan sanyi, acan cikin jikinsa kuwa wani irin zafi yakeji, tamkar wanda ake gasa sa, lumshe idanunsa yayi tare da yin ƙasa da kansa zuwa wuyanta,  still hannunsa na dafe da tsakiyan bayanta, sauƙe tausassun laɓɓansa yayi akan fresh neck skin ɗinta,  wani irin sabon mood tasamu kanta aciki alokacin da taji sauƙan laɓɓansa akan fatar wuyanta,  cikin nutsuwa yasanya harshensa haɗi da laɓɓansa yana lasar fatar wuyanta, wanda hakan yabawa lallausan sajen dake kwance gefe da gefen fuskarsa daman gogan ƙasan haɓanta, sosai hakan ke ƙara zautar da ita, sannu ahankali yake yawo da hannunsa akan naked skin ɗinta,   ƙasa yayi da kansa zuwa daidai ƙirjinta, ahankali yasanya harshensa yaɗan yi sucking saman ƙirjinta, wani irin yarrr haka taji ajikinta, lokaci ɗaya ta fidda wani irin numfashi tare da sake shigewa cikin jikinsa,  ƙasa sosai ya ƙarayi da kansa inda ya ɗaura bakinsa adaidai tsakiyar cikinta, slowly yake wasa da harshensa akan fatar cikin nata, sosai tafara fita hayyacinta, wani iri takeji acikin jikinta, kan nipples ɗinta ne suƙa mimmiƙe, kaɗan kaɗan  sukeyi mata ƙaiƙayi,  burinta shine taji sauƙan hannunsa akan breast ɗinta, amma kuma ko kaɗan baiyi ƙoƙarin yin hakan ba, yanayin yanda yake murza jikinta,  yasanya ta cusa hannunta acikin tulin gashin kansa, sosai tsikar jikinta ke miƙewa,  idanunsa ya lumshe ahankali yake yin sama da kansa, yayinda lallausan gashin jikinsa ke gogar fatarta,  harshensa ya sanya adaidai tsakiyan ƙirjinta, ahankali yake wasa da harshensa awajen,   yanzu kam takai yanayi irin na zautuwa, bazata iya jure salonsa ba, kuka mai sanyi ta sake,  awahalce ya ɗago da kansa inda ya haɗe bakinsu waje ɗaya, sauƙar hannunsa akan breast ɗinta, shi yasanya numfashinta ɗaukewa cak, yayinda yatafi hutu naɗan wani lokaci, hakan ya farune kuma badon komai ba saidan baƙon yanayin da tasamu kanta aciki, wanda yazarce ko wani yanayi daɗi awajenta, cikin sanyi yakeshan bakinta yayinda yake murza breast ɗinta slowly,   ɗayan hannunsa ya sanya yacire gaba ɗaya rigan dake jikinta,   zama yayi akan gadon tare da tanƙwashe ƙafafunsa, ɗagota yayi inda ya zaunar da ita akan cinyoyinsa ya zamana suna fuskantar juna,   gashin kansa yake ɗan goga mata

akan wuyanta, cikin nutsuwa yasanya harshensa akan saman breast ɗinta, sannu sannu harya kawo kan pink nipples ɗinta, harshensa yasanya yana gogan nipple ɗinnata yayinda kuma yake goga mata lallausan gashin kansa awuyanta, sheshsheƙan kuka haɗi da wani zazzafan numfashi take fitarwa ahankali, sauƙe hannayensa yayi akan faffaɗan waist ɗinta, cikin nutsuwa ya kwantar da ita akan gadon tare da yi mata rumfa da faffaɗan ƙirjinsa, idanunta wanda suka ƙanƙance ta buɗe tare da ɗan kallonsa, shi ɗinma kallonta yakeyi cikin wani irin yanayi, hannunsa yasanya ahankali yaɗan matsar da gashin kanta wanda yaɗan rufe mata gefen fuskarta kaɗan, wani irin saƙo suke turawa ta cikin idanun junansu, kansa ya ɗaura agefen wuyanta tare da zura harshensa acikin kunnenta, hannunsa yakai kan saman maranta yana shafawa ahankali, idanunta ta rumtse tare da sanya hannuwanta takama damatsan hannunsa, ahankali take girgiza kanta tana fitar da wani irin numfashi dake nuna cewa tajima da shiɗewa, cigaba da shafa saman marar nata yayi, kana yana me ƙara sucking cikin ear ɗinta, jin yanda numfashinta ke fita da sauri, ga kuma ƙirjinta dake bugun uku uku ne yasanyashi zare harshensa daga cikin kunnenta, sannu ahankali yake bin kowani gaɓa dake jikinta da kiss, santala santalan legs ɗinta ya ke shafawa ahankali, ƙafarta na dama ya ɗago tare da sanya yatsun ƙafar nata acikin bakinsa, ahankali yake tsotsan yatsun nata yana shafa Ƙafarta, luf tayi akan gadon tana sauƙe ajiyar zucia, sosai takejin daɗin yanda yake sucking yatsun ƙafar nata, har wani irin baccine taji na ƙoƙarin fusgarta, saidai kuma abun da taji yana ƙoƙarin yi matane, yasanyata ware idanunta da sauri, ƙoƙarin tashi zaune take, da sauri yasanya hannunsa ya maidata kwance, rumfa yayi mata da faffaɗan chest ɗinshi, cikin nutsuwa ya ɗaura laɓɓansa akan nata, ahankali yake tsotsan lips ɗinta, yayinda yasanya hannunsa guda ɗaya yana shafa jikinta, hakan da yayi matane yasanyata shagala harta fara manta wa da duniyar da take.

Ƙam ya runtse idanunsa, saboda yanajin kansa na duka kamar zai tarwatse, ƙirji da zuciyarsa kuwa bugawa suke da sauri sauri kamar zasu fito waje, da ace wani zai san me yakeji awannan lokacin to tabbas daya tausaya masa, inama da ace idan yabarta haka babu haƙƙinta akansa, tabbas da zai barta saboda samawa kansa nutsuwa.

Cikin wani irin yanayi ya buɗe gaba ɗaya jikinta, gudun kada tasakar masa kuka yasanyashi sake haɗe bakinsu waje ɗaya, hannayensa ya sanya duka biyu ya tallafi bayanta, gaba ɗaya jikinsa rawa yake, haka laɓɓan bakinsa keta karkarwa kamar wani mejin sanyi.
Rumtse idanunsa yayi cikin son daure bugun da zuciyarsa keyi yanemi hanyar shiga cikin jikinta.
Wani irin ƙara tasake tare da sakin wani irin fitinannen kuka alokaci guda, cikin sauri ya maida bakinsa cikin nata, sosai wani irin zazzafan zazzaɓi ya sauƙowa jikinsa amma duk da haka bai fasa abunda yakeyi ba, kuka take sosai tana me ƙoƙarin ƙwace jikinta daga nashi amma sam yakasa bata daman hakan, infact shi yama fita, fita cikin nutsuwarsa, jin yanda mararsa ke bala'in yi masa ciwone yasanyashi ɗaura hannunsa akan bakinta ya toshe mata bakin gudun kada ihunta yayi affecting ɗinsa, da gaba ɗaya ƙarfinsa yaje mata, wani irin razanannen ƙara tasaki alokacin da taji wani irin raɗaɗi da azaba na ratsa gaba ɗaya jiki da ƙwaƙwalwarta, wanda tunda take aduniya bata taɓa jin irinsa ba, wani ƙaran ta kuma saki saidai ayanzu ba ita kaɗaice tayi ƙaran ba hardashi kansa wanda nasa ƙaran ma yafi nata amsa amo, cikin tsananin

azaban da takeji ta damƙi hannuwansa tare da soma yaƙushin fatarsa, sosai take kuka kamar ranta zaifita, hannu bibbiyu haka tasa take dukan chest ɗinsa tana kuka mai taɓa zuciya, baisan awace duniya yake ba, baisan taya zai fara fassara halin dayake ciki ba, shikansa baisan tayaya hakan tafaru ba,  tunda yake adunia baitaɓa jin koda makamancin abun da yakeji ayanzu ba, jiyake kansa na juyawa, gaba ɗaya gaɓɓan jikinsa sun amsa wani irin ɓaƙon yanayi daya ziyarcesu,  so yake ya farka daga nannauyan baccin da yake, ko da zai iya tantance duniyar da yake ciki,  idanunsa ne suka rufe ruf tamkar makaho wanda baya gani, cikin tsananin azabtuwa da kuma irin shiɗewan da yayi ya ɗaura bakinsa akan laɓɓanta,  kwata kwata bayacikin hayyacinsa hakan yasa azafafe yake sucking lips ɗinta,  sosai take neman sumewa saboda tsabar tsananin azaban dayake gana mata, musamman  laɓɓanta dayake tsotsa kamar zai fincikesu daga kan fuskarta.

Azauce yakai bakinsa daidai saitin kunnenta, sosai yake sucking ɗinta yana fitar da wani irin breath mai ɗauke da wani  sauti, sam bakinsa ya kasa rufewa  wasu irin maganganu yake faɗa wanda shikansa baisan me yake cewa ba balle kuma ita,  sosai ɗumin dake cikin jikinta ke azabtar dashi, wani irin horo yake basa na musamman, haka kuma wannan ɗumin shiya kaisa ga wata dunia wanda baisan akwaita ba kwata kwata, wani irin abu yakeji acikin jikinta wanda ke ƙara zautar dashi yana kuma fitar dashi hayyacinsa. Da ƙarfi sosai yayi hugging ɗinta yana me ƙara shigewa can cikin jikinta,  zuwa yanzu kam sam bata iya motsawa bare harma ta sarrafa gangar jikinta,  hatta numfashi ta baki take iya fitarwa, hawaye kuwa sai ambaliya suke suna gangara ta gefen ƙuncinta, raɗaɗi da zafi kuwa har cikin ƙwaƙwalwarta takeji,  tun tana iya buɗe idanunta har takai ga sun rufe ruf, ko ina dake jikinta haka ya saki, tuni ta cire rai da rayuwa don ko da wasa bataga alamar cewa SOORAJ zai barta tarayu ba....

30 minute.

Ahankali yake sakin wani irin nishi mai ƙarfi, alokacin da yakejin wani irin abu na musamman na game gaba ɗaya jikinsa,  aje faffaɗan chest ɗinsa yayi akan ƙirjita, tare da  lumshe idanunsa, wasu irin zafafan hawaye ne suka kwaranyo daga cikin idanunsa, zafi zau haka jikinsa ya ɗauka tamkar wuta,  bakinsa yakai daidai saitin kunnenta, cikin muryarsa dake  rawa alaman kuka nason cin ƙarfinsa yace.
"Am sorry,  am so sorry MY SUNSHINE am really sorry!! i don't mean to hurt you, please forgive me!!!."
Ya faɗa, gaba ɗaya muryarsa tayi rauni, sosai hawaye ke fita daga cikin idanunsa, cikin tsananin zazzaɓin daya rufesa yaƙara hugging ɗinta sosai ajikinsa, kansa ya ɗaura bisa wuyanta,  ahankali hawayen dake cikin idanunsa ke sauƙa akan fatar wuyanta,      zafin zazzaɓin dake jikinsa, da kuma yanda hawayensa ke sauƙa akan wuyanta yasanyata ɗan buɗe gajiyayyun idanunta, wanda suka rine sukai jajur dasu, tsabar kukan da tayi yasanya suka ƙanƙance kana kuma suka kumbura, fuskarta kuwa saida tayi jajur saboda kuka da kuma azabar daya jiyar da ita, jin yanda yake ƙara shigewa jikinta yasanyata maida idanunta ta rufe ahankali, sosai itama jikinta ya ɗauƙi zafi gawani ciwon kai me tsanani da ya rufeta, har tanajin bazata iya ɗaga kanta ba,  ɗago da kansa yayi ya kalleta, wani irin masifaffen tausayinta ne ya cika zuciyarsa, take yaji wasu sabin hawaye sun cika idanunsa,  tazama ta musamman

agareshi, itace mace tafarko aduniarsa, itace mace tafarko da ta maidashi cikakken namiji, itace mace tafarko data bashi kyautan budurci, itace mace tafarko da ya fara sani matsayin ƴa mace adunia, itace mace tafarko wacce daɗin jikinta ya zautar dashi yakuma fitar dashi daga hayyacinsa, itace mace ta farko da tajiyar dashi wani daɗi wanda baisan da irinsa ba adunia, itace mace ta musamman agareshi, tazama HASKE acikin rayuwarsa, tabbas yayarda cewa anrubuta ƙaddaran kowannensu acikin zuciyoyinsu,  ahankali ya ƙara matso da fuskarsa gaf da tata, cikin wani irin yanayi ya kama lip ɗinta na ƙasa yashiga tsotsa kamar yasamu candy sweet, awahalce ta buɗe idanunta wanda suke cike tab da ƙwalla ta kalleshi, shiɗinma kallonta yayi atare suka lumshe idanunsu dake cike da ƙwalla, cikin wata irin zazzafan soyayyarta dake neman fasa masa zuciya ya haɗe bakinsu waje ɗaya.

*Vote*
*and*
*comments*
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ!!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*Wattpad*
@fatymasardauna
#truelove

*(Wannan fajin baki ɗayansa kyautane agareku Members ɗin waƴannan groups  masu albarka.
(1) SOORAJ FANS GROUP*
*(2)SOORAJ FANS BY N.Y*
*(3) ZEETY NOVELS (A-Z)  Kuji daɗinku ku more wannan fejin nakune saima kun ga dama wasu su karanta😝 fatymasardauna nayi muku SON SO)*

*Chapter 51*

Sannu ahankali hawayen dake silalowa daga cikin idanunta, ke  sauƙa akan hannunsa wanda ke tallafe da gefen ƙuncinta, yana bata wani professional kiss akan lips ɗinta,   ɗan zame jikinsa daga nata yayi,  cike da tsananin tausayinta ya  ɗago kansa inda ya kalli beauty face ɗinta, tabbas yasan bai aikata daidai agareta ba,  sosai ya hango tsananin wahalan da ya bata akan fuskarta,   ɗagata yayi tare da mirginawa gefenta ya kwanta irin kwanciyar nan ta rub da ciki, ahankali yake sauƙe wata irin nannuyar ajiyar zuciya, yayinda numfashinsa ke fita cikin sanyi, lumshe idanunsa yayi, take wasu sabin hawaye suka gangaro daga cikin su, wannan rana

tazame masa rana ta musamman acikin gaba ɗaya ranakun rayuwarsa, zai iya mantawa da komai amma banda wannan rana'n, a rana irin tayau ya fara gamsuwa cewar shima Namijine kamar kowa, sannan akuma wannan rana da daren yaji wani abu, wanda bai taɓa jin irinsa ba iyaka tsawon rayuwarsa, Muradi, Buri, Fata, da kuma farin cikin zuciya duk ya mallaka acikin wannan daren, sake lumshe idanunsa yayi tare da ɗan takure jikinsa waje ɗaya, wani irin zazzafan zazzaɓi ne ke damunsa, har takai ga teeth ɗinsa ma rawa suke, kowanne na gogan juna, kansa kuwa ciwo yakeyi masa sosai kamar zai rabe biyu, sosai yake buƙatar agaji saidai kuma amma duk da yanda yake buƙatar taimako, ya kula cewa ita tafishi buƙata, domin kuwa duk yanda jikinsa yakai ga ɗaukan zafi baikai nata ba, don daga inda yake kwance yana iya jiyo hucin zafin zazzaɓin dake jikinta, cikin dauriya haɗi da jarumta ya tashi zaune daga kan gadon, hannuwansa yasanya duka biyu ya ɗan tallafota jikinsa, cike da kulawa ya ɗaura kanta akan faffaɗan chest ɗinsa inda yasanya hannuwansa ya rungumota sosai, lumshe idanunsa yayi tare da cusa fuskarsa cikin lallausan gashin kanta, sosai yake shaƙan ni'imtaccen ƙamshin da gashin kannata ke fitarwa.

Jinta acikin ƙirjinsa yasanya hawayen da suka cika idanunta, samun daman gangarowa, sosai jikinta ke ɓari, zuciyarta kuwa da ƙarfi take bugawa, wani irin masifaffen tsoronsa ne ke ƙara ratsa gaba ɗaya sassan jikinta, ko sau ɗaya bata son tuna azaban da taji alokacin da yake ƙoƙarin ratsawa cikin jikinta, tanaji inama da ace zata iya yin kuka mai sauti, tabbas da tayi ko zataji sassauci na daga zafin da takeji acikin jikinta, abubuwane suka haɗe mata ga zafin rabata da virgin ɗinta da yayi ga kuma zafin zazzaɓi da ciwon kan da suka sauƙar mata lokaci guda, sam jikinta babu ƙarfi ko ƴar yatsanta bata iya motsawa da kyau, komai na jikinta ciwo yakeyi.

Hannunsa yasanya ya kwantar da ita, cikin dauriya dason shanye ciwon dayakeji acikin jikinsa ya sauƙo daga kan gadon, kaitsaye bathroom ya nufa, yana shiga cikin bathroom ɗin ya tsaya tare da ɗanyin jigum, baisan me zaiyi mata wanda zai ɗan samamata relief daga ciwon da takeji ba, shi baisan komai ba, baikuma san tayaya zai fara ba, jingina bayansa da jikin ƙofar bathroom ɗin yayi, kana yaɗan lumshe gajiyayyun idanunsa, wanda kallo ɗaya zaka musu ka karanto ciwon dake cin jikinsa acikinsu, don har wani lumshewa suke su kaɗai, dabaran haɗa mata hot water ne yazo mishi, hakan yasa cikin mintuna ƙalilan ya cika babban bathtube ɗin dake cikin toilet ɗin da ruwa, buɗe ƙofar bathroom ɗin yayi ya fito, kaitsaye inda gadon yake ya nufa, cikin tausayawa ya sanya duka hannayensa biyu ya ɗagota zuwa jikinsa, kamar wata ƴar tsana haka ya nufi hanyar bathroom ɗin da'ita, ita kuwa har zuwa yanzu idanunta akulle suke ƙam, don ko buɗesu wahala suke mata,
cikin nutsuwa ya ƙarasa da ita gaban bathtube ɗin, ahankali ya ajiyeta cikin ruwan zafin, wani irin ƙara ta sake tare da yunƙurowa zata fita daga cikin bathtube ɗin, da sauri ya riƙeta, cikin marairaice fuska yace.
"Am sorry please!."
Sai alokacin tasamu daman sakin kuka me sauti, nan tashiga rera kuka tanajin wani irin sabon zafi da raɗaɗi na ratsa gaba ɗaya jikinta, don kuwa shigarta cikin ruwan zafin yasanya taji kamar garin barkono aka watsa mata cikin privet part ɗinta, kuka take sosai tana me ƙoƙarin ƙwace kanta daga riƙon da yayi mata amma sam yaƙi bata daman hakan, idanunsa ne suka cika da ƙwalla, tausayinta yakeji sosai, sam baisan haka yake ba da baije mata ahaka ba, baiyi

tunanin cewa zai iya ba shiyasa ya rufe idanunsa ya shigeta da ƙarfi, tabbas yasan dole zataji zafi, amma shikansa awannan lokacin baya cikin hayyacinsa, yasani bai kamata ace ya bata wahala har haka ba, musamman idan aka dubi shekarunta, ganin tana ƙoƙarin yi masa tijara ne yasanyashi faɗawa cikin bathtube ɗin wankan,  inda ya kama duka hannayenta ya riƙe, faffaɗan ƙirjinsa ya ɗaura akan breast ɗinta,  wanda suma saboda tsabar wahalan da suka sha awajensa saida suka sauya kala daga farare zuwa ja, kan nipples ɗinta kuwa haka yayi ja sannan sosai yakeyi mata zafi,   jin yanda ya danneta ya kumayi mata rumfa da faffaɗan chest ɗinsa yasanya numfashinta ya soma seizing,  tsoronta ɗaya shine karyace zai kumayin wani abu da ita, don tanaji ajikinta cewa takai matakin da daya ƙara mutuwa zatayi, kansa ya ɗaura akan wuyanta tare da lumshe idanunsa, jin ya sakar mata nauyinsa yasanya ta kwantawa acikin ruwan tare da ƙara kulle idanunta gam,  sannu ahankali ɗumin ruwan ke ratsa jikinsu su duka, har yakai ga ya huce,  jin haka yasanyashi ɗagata caɗak, inda ya zubar da wannan ruwan ya ƙara zuba wani mai ɗumi sosai acikin bathtube ɗin, ɗaukanta ya ƙarayi suka faɗa cikin bathtube ɗin,  jin wani sabon zafi yasanyata sake sakin kuka, cikin aro jarumta da kuma ɗan kuzarin da tasamu ayanzu shiganta ruwan zafin, tashiga dukan faffaɗan ƙirjinsa, kuka takeyi sosai wanda yake ɗauke da zallan shagwaɓa haɗi da zafin zazzaɓi, sam baiyi yunƙurin hanata dukan jikinsa ba, saima matseta da yayi sosai, kana ya ƙura mata ido, itakuwa zagewa tayi da ɗan iya kuzarinta ta shiga dukansa, ita adole  hakan da takeyi sosai take dukan jikinsa, shikuwa sam bama yajin zafin dukan, ji yake kamar ma shafa sa kawai takeyi.
Haka ta dingayi masa rikici da kukan  shagwaɓa,  lokaci ɗaya ta rikice masa tadawo kamar ƙaramar yarinya ƴar shekara 3,  saida ya tabbatar da cewa zafin ruwan ya gasa jikinta sosai kafun ya fita daga cikin bathtube ɗin, gaban shower ya ƙarasa inda ya sakarwa kansa ruwa, yayinda ita kuma yabarta kwance acikin bathtube tana faman shashsheƙan kuka mai ɗauke da zafin zazzaɓi.
Yana gama wanka ya sanya wata fara ƙal ɗin bathrobe ajikinsa, tare da ɗaure igiyoyin bathrobe ɗin akan cikinsa,  gaban  bathtube ɗin yaƙarasa,  mamakine ya kamasa ganin da yayi cewa tuni tafara bacci acikin ruwan,  wani haɗaɗɗen murmushin  daya bayyana zallan kyawun fuskarsa yayi, cikin kulawa ya ɗagota daga cikin bathtube ɗin,  kuka tasaka masa tare da soma yi masa wani irin sambatu, da'alama zazzaɓin nata ƙaruwa yakeyi,  da ƙyar ya iya yi mata wanka, kasancewar ganinta haka naked na hautsina tunaninsa sosai,  tana kuka haka ya ɗaura mata wani baby yellow towel ajikinta, ɗaukarta yayi ajikinsa suka fice daga cikin toilet ɗin,  koda suka fito daga cikin bathroom ɗin, batare daya sauƙeta ƙasa ba, ya jawo stool ɗin mirror kana ya zauna akai, cikin kulawa yasake rungumeta aƙirjinsa,  handryer ɗinsa ya jona ajikin socket, ɗagota yayi inda yazaunar da ita bisa cinyarsa,  hannayensa ya sanya duka biyu ya kama waist ɗinta,  kukan shagwaɓa tasakamai cikin wani irin yanayi ta turo ɗan ƙaramin bakinta gaba, cikin yanayi na shagwaɓa da kuka kuka tace.
"Nidai banaso ka ƙyaleni, zafi nakeji sosai, please kayi haƙuri bazan ƙara yi maka kuka cikin dare ba tunda baka so, dan Allah amma kada ka ƙaramin kajiiii! pleaseeee!!." taja maganan tana sakin sheshsheƙan kuka.
Lumshe idanunsa yayi tare da ɗan dafe daidai saitin heart ɗinsa dake bugawa.
Kallon ƴanda ƴan ƙananan laɓɓanta ke mamul mamul  yayi. da alama wasu magana suke faɗa wanda baya fitowa fili, idanunsa yasake ɗan lumshewa cikin wata irin unique voice ɗinsa yace.
"Am so  sorry bazan ƙara ba kinji, da zafi sosai ko?."

Ɗan ƙaramin bakinta tasake turowa gaba cikin sheshsheƙan kuka ta gyaɗa masa kai alamar "Eh."

Hannayensa yasanya ya tallafi gefen fuskarta cikin tsananin kulawa ya manna mata kiss adaidai forehead ɗinta, cikin wata irin kasalalliyar murya yace.
"I promise you bazan ƙara yi miki da zafi ba!."

Handryer ɗin ya ɗauka cikin lallami da dabara yashiga busar mata da jiƙaƙƙen gashin kanta, sai bori takeyi masa tana zizzillewa zata sauƙa daga jikinsa, saida ya riƙeta dagaske tukun sannan yasamu ya busar mata da gashin kannata, ajiyeta yayi akan stool ɗin mirror'n, nan fa ta sake sakar masa kuka kamar wata yarinya meshan nono, hannayensa yasanya yaɗan dafe kansa, harwani irin duhu duhu yake gani acikin idanunsa saboda tsabar yanda kansa ke bala'in yi masa ciwo, sannan gashi kukanta sosai yake ɗaga hankalinsa, kallon bedsheet ɗin dake shumfuɗe akan gadon nasu yayi, gani yayi gaba ɗaya tsakiyan bedsheet ɗin yayi staining, hannayensa ya ɗaura akan waist ɗinsa, iska ya furzar ta bakinsa, lallai shikam yau yajawa kansa, ashe dama haka disvirgin ɗin mace keda ɗan iskan wahala? komai ya caɓe masa, ga ciwon da yakeji ga kuma kukanta dake damunsa, janye bedsheet ɗin yayi daga kan gadon inda ya buɗe drawer ya ciro wani sabon bedsheet ɗin, nan ya shumfuɗa akan gadon, bathrobe ɗin jikinsa ya cire inda ya sanya wani dogon black crazy jeans, still tana zaune akan stool ɗin tana matsar ƙwalla haɗi da wasu irin sambatu marassa kan gado, first aid box ɗinsa ya ɗauko inda ya ciro wani paracetamol, guda biyu ya ɓalla yasha, inda ya ɓalli wasu guda biyun ya dunƙule acikin tafin hannunsa, ɗayan hannun nasa ɗauke da goran ruwa ya ƙaraso inda take, sungumarta yayi inda ya ƙarasa kan gado da ita, zama yayi tare da ɗaurata akan cinyarsa, hannunsa yasanya ahankali yana shafa bayanta, bakinsa yakai daidai saitin kunnenta cikin husky voice ɗinsa mai kama da raɗa yace.
"Kinaso na baki chocolate kici?."
cikin yanayin zafin zazzaɓin da take ciki ta gyaɗa masa kanta alamar "Eh."
Murmushin daya bayyana tsantsar kyawunsa yayi, cikin yin ƙasa da murya yace.
"Yauwa good girl haaaa buɗe bakinki na samiki akwai daɗi sosai."
ashagwaɓe ta ɗan bude ɗan ƙaramin bakinta, murmushi yayi tare da cewa. "To idan nasamiki kada ki tauna haɗiyewa kawai zakiyi kinji ko." still kae ta ƙara gyaɗa masa alamar to, maganin dake dunƙule cikin hannunsa ya tura mata acikin baki, tare da ɗaura mata goran ruwa akan bakinta, wani irin ɗaci ne taji ya game gaba ɗaya maƙoshinta, aƙoƙarinta nason dawo da maganin daya zuba mata acikin bakinnata ne, batare da ta shirya ba maganin ya wuce can cikin maƙoshinta, babu shiri ta haɗiye, kuka tasakar masa tare da cusa kanta cikin ƙirjinsa cikin yanayin shagwaɓa ta cijesa akan fresh skin ɗinsa, lumshe idanunsa yayi tare da sakin murmushi, sosai yaji zafin cizon nata, ɗan cije lips ɗinsa yayi tare da kai hannunsa ya kashe gaba ɗaya hasken ƙwan wutan dake ɗakin, bedside lamp ya kunna inda yaɗan haska ɗakin kaɗan, kwantar da ita yayi akan gadon, yana ƙoƙarin miƙewa tsaye, ta riƙe masa hannu tare da sa masa kuka, lumshe idanunsa yayi tare da sauƙe wata irin ajiyar zuciya, kwanciya yayi akusa da ita tare da sanya hannunsa ya warware towel ɗin dake jikinta, lallausan blanket ɗin dake kan gadon yajawo tare da rufe musu jikinsu, hannunsa ya ɗaura akan cikinta kana ya

jawota jikinsa,   daddaɗan ƙamshinsa daya bugi hancinta ne, yasanyata ƙara shigewa cikin jikinsa, yayinda ta cusa fuskarta acikin ƙirjinsa,  tana me ƙara shaƙan ƙamshin nasa dake sauƙar mata da nutsuwa haɗi da zallan kasala, duka hannayensa yasanya ya tallafi tsakiyan bayanta, sake hugging ɗinta yayi, inda ya ɗaura haɓansa akanta tare da lumshe idanunsa, sosai yakeson ƙamshin da fatar jikinta keyi, yakanji wani irin abu na Musamman aduk sanda yaji tattausan fatar jikinta ta gogi nashi, sihirtaccen ƙamshin daya kama jikinta shine abun da yafi so, yanason ƙamshin sosai, yana kuma so ako da yaushe ya zamana ƙamshin na ziyartan hancinsa,  sake maƙalewa acikin jikinsa tayi, bakinta taɗan buɗe ahankali cikin sanyi ta manna laɓɓanta akan fatan ƙirjinsa, saida ya lumshe idanunsa saboda yanda abun ya shigesa sosai, ahankali yake yawo da hannunsa akan naked skin ɗinta, daɗin hakan da tajine yasanyata sakin jikinta gaba ɗaya,   lumshe idanunsa yayi tare da sakin wani irin nunfashi mai sauti,  yanayin yanda breast da nipples ɗinta ke gogan chest ɗinsa ne yasanyashi kasa jurewa, harshensa ya tura acikin kunnenta, ahankali yake yawo da harshen nasa acikin kunnenta, kana yana me hura mata daddaɗan iskan bakinsa acikin kunnen nata kaɗan kaɗan.
Cikin mintuna ƙalilan wani irin daddaɗan bacci ya ɗauketa, jin yanda numfashinta ke sauƙa akan wuyansa yasanyashi sakin ajiyar zuciya,  hannunsa ɗaya ya tura cikin lallausan gashin kanta yana shafawa ahankali,  lallai wannan Baƙon Yanayi ne awajensa, tabbas yayarda rayuwa tana iya juyawa ako da yaushe, sannan ƙaddara na sauyawa, yanzu ko anjima, sannan buwaya irin ta Ubangiji ta gagari misali,  yayarda cewa ƙunci baya taɓa tabbata acikin rayuwar ɗan adam, haka ma bako yaushe ne zaka zama cikin farinciki ba, ya aminta cewa gaba ɗaya rayuwa cike take da ƙalubale haɗi da  ƘADDARA me kyau ko akasinta, tana iya zuwawa kowani bawa, cuta da sauƙi duk na ALLAH Ne, sannan kuma ba acire rai da rabo, komai yana ga Allah.
Shizai baka alokacin dayaso shine kuma zai hanaka alokacin da yaso, Baya hanaka kuma wai don bayasonka, haka kuma baya baka waidon yanuna maka cewa yafi sonka, Yana bawa wanda yasone kuma ya hana wanda yaso alokacin da yaso, babu wanda yafi wani awajensa sai mai tsoronsa wanda kuma yake bauta masa da gaskiya,  sannan komai yana da lokacinsa.
Wasu irin raunannun hawayene suka gangaro daga cikin idanunsa,  sosai yakeyiwa Allah godiya acikin zuciyarsa, yakasance tsawon shekaru yana ɗauke da cuta, baisan menene sha'awa ba, baisan menene so ba, baiwani san cikakken farinciki ba, yayi rayuwa shi kaɗai, ya shanye tarin damuwa acikinsa shi kaɗai, tsawon shekaru yana fama da ƙuncin zuciya haɗi da ciwo, amma sai gashi yau RANA ƊAYA  Allah Ya sauƙaƙa al'amuransa, Tabbas ALLAH Shikaɗai ya kamata a bautawa saboda ƙarfin iko da buwayarsa ya zarce duk wani mai tunani.
Sake hugging ɗinta yayi tare da lumshe idanunsa, duk da cewa zafin jikinnasu baiwani sauƙa ba amma dai yaɗanji sauƙi bakamar ɗazu ba, cikin mintuna ƙalilan wani bacci wanda bai taɓayin irinsa ba ya ɗaukesa.

7:00 am daidai alarm ɗin dake ɗaure bisa kan bedside ɗin gadon yasoma ƙara,  sannu ahankali ƙaran alarm ɗin ke ratsa cikin kunnuwansa,  ahankali ya buɗe idanunsa inda ya sauƙesu akan kyakkyawar fuskarta wanda take gab da tasa fuskar, hannunsa yakai  ya kashe alarm ɗin,  ɗan janye jikinsa daga nata yayi tare da tashi zaune, idanunsa yakai jikin window'n ɗakin, nan yaga tuni haske ya bayyana ta jikin window'n alaman Safiya tayi, hannunsa yasanya ya dafe goshinsa, sam baiso ya makara ba, ajiyar zuciya ya sauƙe cikin zuciyarsa yace. "Me yasa aduk sanda takwana ajikina saina makara?."

ita flat, bakinsa ya ɗaura akan cikinta inda ya shiga bata wasu mahaukatan kiss, gaba ɗaya ya ruɗe, jikinsa har rawa yake,  zazzafan groaning yake sakewa, sake ɗagota yayi inda ya ɗaurata akan cinyansa,  kansa ya tura cikin wuyanta sosai yake sucking skin ɗinta kamar wanda ya samu sweet. Daidaita jikinsu yayi tare da lumshe idanunsa.
Itama rumtse idanunta tayi da ƙarfi tare da buɗe bakinta so take tayi ihu, ganin haka yasa da sauri ya haɗe bakinsu waje ɗaya, yayinda yasa hannayensa ya sake hugging ɗinta, cikin zaucewa haɗe  da fitar hayyaci, ya zare bakinsa daga cikin nata inda yasaki wani irin groaning mai ƙarfin gaske.
Alokacinne tasamu daman fashewa da wani irin kuka,  wanda ya bayyana tsananin zafi da raɗaɗin da takeji, wani ihun takuma sakewa alokacin da yake ƙoƙarin ratsa cikin jikinta, gaba ɗaya jikinta ya ɗauki rawa, wani irin masifaffen tsoron sane ya cika ranta,  gefe guda kuwa ga wani zafi na Musamman da ke ziyartar brain ɗinta.
Ya zauce yakuma fita cikin hankalinsa, idanunsa gaba ɗaya sun rufe, haka yakejin wani irin daɗi na ratsa gaba ɗaya jikinsa,   sosai yasake zaunar da ita ajikinsa, inda yashiga bata lafiyattun kiss kamar wani wanda zai cinyeta haka yakeyi,  sam tanemi bakin kuka ta rasa, saboda ya sanya laɓɓansa duka biyu ya rufe bakinnata, zazzafan numfashi kawai yake sake mata akan fuskarta,   zafin da takeji ne yasanyata sanya haƙoranta ta ciji lips ɗinsa, ɗan ƙaramin ƙara yayi tare da sake shigewa jikinta,  kuka ta fashe dashi, tare da sanya hannunwanta duka biyu ta yaƙushi fatan jikinsa da ƙarfi, amma ko gizau kamar wanda ta yagi dutse,  sake matseta yayi yana sakin wani zazzafan numfashi mai haɗe da groaning, wanda ke bayyana tsananin shauƙin dayake ciki,   kukan da takeyi ne yasanyashi ɗan tsagaitawa ɗago idanunsa wanda basa gani sosai yayi ya kalleta, ahankali ya kwantar da ita tare da yi mata rumfa da faffaɗan ƙirjinsa, fuskarsa ya kusanto daidai da nata,  cikin wani irin yanayin da yake jin kansa aciki ya tura lips ɗinsa cikin bakinta, harshenta yakamo inda yasoma yi mata wani irin suck, kana ya ɗaura hannunsa akan ƙirjinta,
Tuni sheshsheƙan kukanta ya ɗauke, samun kanta tayi acikin wata irin duniya ta daban, wanda daɗinta ya zarce misali.
Kwanciya yayi akanta, ahankali yake ratsa cikin jikinta, wani irin abune ke ratsa gaba ɗaya jikinsu su duka biyun, daga wani ɓangare zafi takeji, saidai kuma amma daɗin da takeji yafi zafin yawa, sannan alokaci guda abun ke sarrafawa ƙwaƙwalwarsu, inda atake brain ɗinsu ke watsawa gangar jikinsu, yanayin da suke samun kansu aciki, wanda har yasa RAJ yakasa controlling kansa.
Sake shigewa cikin jikinta yayi lokaci guda yasaki wani irin groaning, me ɗauke da amo, take kuma saiga wasu irin hawaye masu zafin gaske sun silalo daga cikin idanunsa,  sosai ɗumin cikin jikinta ke neman mantar dashi sunansa, da kuma wayeshi, harma da duniyar da yake, sam yakasa controlling kansa,  ahankali  ya zura harshensa cikin kunnenta, yanayin yanda yake sarrafa harshensa acikin kunnen nata yasata ƙara sakar masa jikinta, bazatace batajin zafi ba, saidai wannan zafin tafe yake da wani irin sinadari mai wahalar fassaruwa, ita kanta ayanzu takasa tantance me takeji, saidai tayi imani wani abu wanda ƙarfinsa ke iya zautar da tunani yana nema ya rinjayi zafin da takeji ajikinta.
Sosai a'l'amarin na Sooraj yasoma fin ƙarfinta,  ita kanta bazata iya tantance wani irin groaning yakeyi ba,saboda tunda take aduniya bata taɓajin groaning irin wanda yakeyi ba, yanayin abu kamar zautacce.

Numfashinta ne yasoma ƙoƙarin ɗaukewa gaba ɗaya, alokacin da ya soma sucking ɗinta, bazata iya jurewa ba, tanajin kamar kanta zai fashe, bazata iya jure yanda yake tsotse cikin jikinta ba, tanajin kamar zata shiɗe, hakanne yasa ta sakar masa kuka irin na fitar hayyaci, sam kukanta baisa yadaina abun da yakeyi ba, itakuwa Zieyaderh da gaske ta shiɗe, saboda da ƙyar take iya fusgo numfashinta, bata taɓayi ba, batasan ya daɗin abun yake ba, saboda haka brain ɗinta baikai ɗaukan wannan daɗin da yakeson jiyar da ita ba, ahankali ya ɗan janye bakinsa, sake shigewa cikin jikinta yayi, hakan kuwa yayi daidai da ɗaukewar numfashinta, take komai najikinta ya daina motsi, haka idanunta suka rufe ruf, bayacikin hayyacinsa, ba kuma ya tare da nutsuwarsa, saboda haka baisan da cewa tadaina motsi ba,
Shikansa bai iya tantance wanene shiba sai aranan, koda wasa bai taɓa tunanin ƙarfin lafiyar daya samu har takai haka ba.

Cikin matsanancin shiɗewa haɗi da zaucewan da yayi ya kwanto gaba ɗaya jikinta, sosai jikinsa ke rawa, bakinsa ya ɗaura adaidai saitin kunnenta, cikin wani irin yanayi dake bayyanar da fitar hayyacinsa a fili, ya sakar mata wani irin zazzafan numfashi haɗi da nishi, hugging ɗinta yayi sosai tare da ƙara shigewa cikin jikinta, wasu irin kiss yake yi mata, wanda da ace tana cikin hankalinta babu abun dazai hanata zaucewa, dan kuwa adaidai wannan lokacin duk wani zafi da takeji sai ya kau. Kwantar da kansa yayi akan wuyanta tare da lumshe idanunsa, still wasu hawaye ne suka fito daga cikin idanunsa, inda suka sauƙa akan skin ɗinta.
Ajiyar zuciya yake sauƙewa akai akai, tare da ƙara shigewa cikin jikinta kamar wani ƙaramin yaro.
Jikinsa gaba ɗaya rawa yake, babban blanket ɗin dake aje gefen gadon ya jawo tare da rufa musu ya rufe gaba ɗaya jikinsu, sam yamanta dacewa itaɗin ƙaramar yarinya ce, hakan yasa yasake mata gaba ɗaya nauyinsa akan jikinta, bakomai ke zautar dashi agame da ita ba kamar fitinannen ƙamshin turarenta, sosai yakeson ƙamshin, har idan yanajin ƙamshin jiyake ajikinsa kamar yayita sucking skin ɗinta.
Aƙalla 15 minute ya ɗauka yana huce gajiyar da yayi ajikinta, ɗago kansa yayi ahankali ya kalleta, ƙirjinsa ne ya buga da ƙarfi, sai alokacin ya lura da cewa babu alamar fitar numfashi atattare da ita ba, atsorace yakai hannunsa kan hancinta, shiru haka yaji babu alaman tana shaƙan numfashi, hannunsa yasanya ya dafe forehead ɗinsa, cikin ruɗewa yace.
"Oh My God." da sauri ya yaye blanket ɗin inda ya ɗauketa yasata cikin jikinsa, kaitsaye ya nufi toilet da ita.
Tana ajikinsa ya haɗa musu ruwa acikin jakuzzie mai matsanancin ƙamshi, yana rungume da ita haka ya shiga cikin babban jakuzzien ya kwanta, wani irin ƙatuwar ajiyar zuciya ta sauƙe alokacin da ɗumin ruwan ya gama kama jikinta, take numfashinta ya daidaita, ahankali ta buɗe idanunta wanda sukayi luhu luhu dasu, cikin 2 second gaba ɗaya abun daya faru ya dawo cikin brain ɗinta, azabure ta yunƙura zata tashi, cikin hanzari ya riƙo waist ɗinta.
Idanunta taɗan waro tana masa kallon tsoro.
Cikin yanayin haɗe fuska, wanda idan yayi yake ƙarawa fuskarsa kyau yace.
"Shall we?"

Da sauri ta girgiza kanta tare da fashewa da kukan shagwaɓa, murya na rawa tace.

"No!."
Murmushin gefen baki yayi tare da ɗage mata giransa ɗaya, sosai yanda ya hango tsoro akan fuskarta ya bashi dariya, saidai kuma yin dariya sakaka bata ɗaya daga cikin ɗabi'unsa, yafi ganewa murmushi, murmushin ma ba ko yaushe ba.
Jawota jikinsa yayi tare da kwantar da ita akan faffaɗan chest ɗinsa, ahankali yake typing bayanta, kasancewar ruwan nada ɗan ɗumi sannan gefe guda kuwa ga yanda yake shafa bayanta, yasa hakan sosai keyi mata daɗi, luf ta kwanta ajikinsa, tun tana fitarda sheshsheƙan kuka har wani irin kasala da bacci suka kawo mata ziyara.
Shima lumshe idanunsa yayi tare da ɗaura kansa bisa kafaɗanta, sama da mintuna 15 suka ɗauka ahaka, tuni wani bacci mai daɗi ya ɗauketa, sai ajiyar zuciya kawai take sauƙewa, tana me fitar da numfashi slowly.
Ahankali yaɗan zameta daga jikinsa, jingina bayanta da jikin jakuzzie'n yayi, tare da fita acikin jakuzzie'n, wanka yayi, kana ya tasheta itama tayi, sai shagwaɓa kawai take ta zuba masa, shidai idanu kawai ya zuba mata, don sam baya taɓa gajiya da kallonta, akasalance tajawo wani towel ta ɗaura ajikinta, Cikin yanayi na shagwaɓa haɗi da magagin baccin dake fusgarta, tasoma tafiya ahankali aƙoƙarinta nason fita daga cikin toilet ɗin batare da tayi aune ba, ta buga kanta ajikin bango, ɗan ƙara ta sake tare da sakin kuka, zip ɗin wandonsa ya zuge, tare da ƙarasowa gareta ɗagota yayi zuwa jikinsa inda ya buɗe ƙofar bathroom ɗin ya fice.
Kwantar da ita yayi akan gado tare da ƙarasawa gaban drawer, wata light purpule nighty gown ya zaro wanda gaba ɗayan jikinta ya kasance net ne, ɗagota yayi daga kwancen da take tare da sanya mata rigan ajikinta, maida ita yayi ya kwantar kamar ƴar ƙaramar yarinya tare da rufa mata blanket, zama yayi agefen gadon tare da jawo laptop ɗinsa yaci gaba da aikinsa, yayinda hakanan yakejin wani irin nishaɗi cikin ransa.
Sama da awa ɗaya ya ɗauka yana danna laptop ɗin kafun daga bisani ya rufe laptop ɗin, light off yayi na hasken ɗakin tare da hawowa kan gadon, tuni bacci yayi mata daɗi har takai ga nighty gown ɗinnata ya tattare gefe, yayinda santala santalan cinyoyinta suka bayyana, hannunsa yakai jikinta inda ahankali ya zare rigar, kwanciya yayi tare da jawota jikinsa, ya rufe gaba ɗaya jikinsu da blanket, daddaɗan ɗumin jikinta ne ke ratsa nasa jikin, hakan yasa yaƙara hugging ɗinta sosai, sakamakon haɗewar da ƙirjinsu yayi waje ɗaya, yasanya har cikin jikinsa yakejin wani irin feeling nataso mai, itama acikin bacci tajita cikin daddaɗan jikinsa, take taƙara shige masa tana me sake maƙalewa ajikinsa, kiss yayi mata akan forehead ɗinta, kana ya lumshe idanunsa, jin soyayyarta yake na ratsa jini da jijiyansa, wani irin zazzafan ƙaunarta yakeji, baisan yaushe ne kuma tayaya yafara sonta ba, saidai yayi imani cewa itace mahaɗin rayuwarsa, sannan itaɗin kamar numfashine agaresa, duk randa yakasance babu ita to tabbas babu numfashinsa.
Cikin mintuna ƙalilan wani daddaɗan bacci ya ɗaukesa.

Ƙiran sallan asuban fari akan kunnuwansa, ahankali ya buɗe idanunsa, inda ya sauƙesu akanta, baccinta take sosai yayinda ta ɓoye fuskarta acikin ƙirjinsa, ɗan janye jikinsa yayi tare da ƙara gyara mata kwanciya, ahankali ya zuro da ƙafafunsa ƙasa daga kan gadon, kaitsaye bathroom ya wuce inda yasakarwa kansa shower, yana gama wanka ya ɗauro alwala.
Koda ya fito wani long jeans ya sanya, tare da ɗaura wata black t-shirt akai, turarensa mai sanyin ƙamshi ya fesa, ahankali ya murɗa handle ɗin ƙofar ya fice, kaitsaye ya nufi masallaci.

6:00 am daidai alarm ɗin dake gefen gadon yasoma ƙara, akasalance ta buɗe idanunta tare dakai hannunta takashe alarm ɗin, tashi tayi zaune tare dakai dubanta makwancinsa, ganin babushi yasanyata lumshe idanunta, ahankali sassanyan ƙamshinsa dake tashi ajikinta ke shiga hancinta, nighty gown ɗinta dake gefe tajawo ta sanya, sam bacci bai isheta ba, gawani uban ciwo da jikinta keyi, saida tayi wanka kafun ta ɗauro alawala, koda ta fito wata brown ɗin jallabiya irin ta mata ta sanya, hijab ta ɗaura akai kana ta tada sallah, koda ta idar da sallan bata tashi akan sallayan ba saida tayi azkar, komawa kan gadon tayi ta duƙunƙune tare da rufawa kanta blanket, har yanzu kalmarnan ta
"I love you!" Da ya furta mata nayi mata yawo acikin ƙwaƙwalwarta, lumshe idanunta tayi tana mejin sabon ƙaunarsa na ratsa jiki da jininta, sannu ahankali moment ɗinsu na daren jiya ke dawowa cikin brain ɗinta, haka ta dinga sauƙe ajiyar zuciya akai akai, ko cikakkun mintuna goma batayi da kwanciya ba bacci ɓarawo ya ɗauketa.

Tunda yafita baidawo gidan ba sai 7:00 am daidai, yana shiga cikin ɗazin cikin hanzari ya nufi bathroom wanka yayi, kana yafito jikinsa duk danshin ruwa, towel yaɗauka yashiga goge jikinsa, koda ya gama body lotion ɗinsa ya shafa, cumb yasanya ya taje lallausan tarin gashin kansa, lallausan sajen dake kwance akan fuskarsa kuwa dama koda yaushe akwance take luf, ga wani irin shinning da take, kasancewar bakaɗan ba ake kashe mata kuɗi, wajen sayen mayukan da zasu gyarata.
Body spray ya fesa ajikinsa inda ya ƙarasa gaban makeken sif din da yake ajiye duk wani suit ɗinsa, wani haɗaɗɗen suit black colour ya ciro, wandon irin pencil ɗinnan ne, sai kuma long sleeve ɗin ciki da ta kasance fara ƙal, ƙarasawa gaban mirror yayi inda ya ɗaura black colour necktie awuyansa, koda ya ɗaura black suit akan long sleeve ɗin sosai yayi kyau, wasu tsadaddun takalma ƙiran company'n Italy toms ya sanya aƙafafunsa, sosai yayi kyau, tare da ƙara wani kwarjini da burgewa, komai na jikinsa shinning yake, kama daga kan suit ɗinsa harzuwa kan lallausan gashin kansa.
Ahankali ya taka zuwa jikin gadon, hannunsa yasanya yaɗan yaye blanket ɗin da ta rufe jikinta dashi.
Sunkuyo da kansa yayi inda ya bata wani kyakkyawan kiss akan forehead ɗinta, hannunsa yasa yaɗan shafi gefen fuskarta, sake jawo blanket ɗin yayi ya rufe mata jikinta, jakar laptop ɗinsa dake kan bedside ya ɗauka, cikin takunsa mai ɗauke da nutsuwa ya murɗa handle ɗin ƙofar ɗakin ya fice.
Cikin nutsuwa ya fito daga part ɗin nasu yana me duba tsadadden wrist watch ɗin dake ɗaure a tsintsiyar hannunsa.
Sam baikula da Oummu dake zaune cikin falon ba, har yakai bakin ƙofar fita daga cikin falon, Oummu taƙira sunanshi cikin sanyin murya.
Tsayawa yayi da tafiyan tare da ɗan juyowa ya dube ta.
Cikin kulawa Oummu tace.
"Harkayi warkewan da zaka fara fita wajen aiki? jiya jiyannan fa aka sallamoka daga asibiti, ai dai kabari ka huta."
Fuska yaɗan kwaɓe tare da cije laɓɓansa, akasalance yace.
"Am okay."

Murmushi kawai Oummu tayi domin tasan yayi hakanne don kawai ya katse maganan da takeyi, duk da cewa ita ta haifesa amma har yau tana mamakin halin miskilancinsa, tarasa wani irin murɗaɗɗen mutum ne shi, magana ma wahala takeyi masa.
Ganin yana ƙoƙarin fita daga cikin parlour'n ne yasanya tayi saurin cewa.
"Ya maganan makarantar Zieyaderh? kafasan yanzu ne yakamata ace tabada himma akan karatunta, saboda yanzu suke S.S ,  yanzune kuma karatun nasu yaɗau zafi."

Ɗan jim yayi tare da lumshe idanunsa, hannunsa ɗaya ya zura acikin aljihun wandonsa, cikin halinshi na rashin sabawa da yawan magana yace.
"Bazata sake zuwaba nacireta."
Idanu Oummu tazaro tare da cewa.
"Kacireta kuma?"
Kansa ya gyaɗa mata alamar "Eh."
duban agogon hannunsa yayi tare da cewa.
"Lesson teacher zaizo yana koya mata agida, then zatayi WAEC examination s S.S 2."
Ɗan jinkirtawa da maganan yayi kana yace.
"Zan sama mata addmission a Nile University."

Ajiyar zuciya Oummu ta sauƙe tare da cewa.
"Amma Sooraj me zai hana ka...."
Da sauri yasake kwaɓe fuska, kamar wani ƙaramin yaro wajen sakalci yace.
"Oummu pleaseeeee!!..." Yaƙare maganan yana meyi mata nuni da agogon hannunsa.
Tun kan tasake cewa wani abu ya fice daga cikin falon.
Murmushi kawai Oummu tayi tare da komawa kan kujera ta zauna,  aranta tana tunanin halin ɗan nata, shi komai bayaso, bayaso ayi masa magana mai tsawo, haka kuma bayaso shima yayi,  saidai har aƙasan zuciyarta tana cike da farinciki, musaman ma yanzu da ta hango zallan kwanciyar hankali hadî da jin daɗi acikin ƙwayan idanunsa, wanda dama tsawon shekaru haka take fata.
***
Sauri sauri haka take zura kaya ajikinta, cikin ɗoki da zaƙuwan son ganin fuskar mahaifinta da akace mata yazo,  tana gama zura doguwar rigan data ɗauko ta zura hijab, da sauri tasanya flat shoe aƙafanta,  Kana tafice daga cikin ɗakin.  kaitsaye BQ ta nufa, da sallama ɗauke abakinta ta ƙarasa cikin babban falon, nan ta iske Babanta, dakuma Inna Ma'u, hadî da Oummu dake zaune can gefe dasu, yayinda aka cika musu gabansu da kayayyakin ciye ciye dasu drinks, fuskarta ɗauke da tsananin farinciki taƙarasa wajen mahaifin nata, har ƙasa ta durƙusa tagaishesa, inda ya amsa mata fuskarsa ɗauke da fari'a, shima sosai yaji daɗin ganin ƴartasa, nan tagaishe da Inna Ma'u wacce keta tsuru tsuru da ido.
amaimakon Inna Ma'u ta amsa sai kawai tasaki kuka, baki Zieyaderh da Oummu suka buɗe suna kallon ikon Allah. Cikin sheshsheƙan kuka tace..
"Dan Allah Zieyaderh kiyafemin, haƙiƙa nasan na cutar da rayuwarki, haka kuma ban kyauta miki ba, saidai kuma nayi nadama dan Allah kiyi haƙuri!."  Takare maganan tanajan majina.
Murmushi Zieyaderh tayi tare da cewa.
"Bakomai Inna Ma'u, ni dama ban riƙeki da komai ba, kuma na yafe miki."

Cikin jin daɗi Inna Ma'u tace.
"Nagode Allah yayi miki albarka.
Nan Zieyaderh ta dubi mahaifinta inda tace.
"Baba ka ɗansha koda ruwane mana."
Ae ma kafun yai yunƙurin cewa wani abu, tuni Inna Ma'u tajawo bowl ɗin dake cike da apples ta ɗau ɗaya tare da kaiwa bakinta, bata gama tauna nabakinnata ba taƙara gabzan wani, hannu tasa tajawo wani babban bowl dake cike da dambun nama, nanfa ta dumbula tare da kaiwa bakinta, (Like Amjad ƙawata, lokacin da tazo gidana kwaɗayin nama. Lol)
Murmushi kawai Zieyaderh tayi tare da girgiza kanta, cikin ranta tace tabbas mai hali baya fasa halinsa.

Oummu kuwa dariya Inna Ma'un ta bata, hakanan sha'anin na Inna Ma'u ke bata dariya, miƙewa tsaye tayi tafice daga cikin falon, tayi hakanne kuma don barinsu su tattauna.
Oummu na fita Zieyaderh ta matso kusa da mahaifinta, cikin yanayinta daya sauya taɗan karyar da wuyanta gefe, murya araunane tace.
"Kayi haƙuri da tambayar da zanyi maka Baba, tun ada naso nasani saidai bansamu fuska ko daman da zan tambayeka ba."
Murmushi mahaifinnata yayi tare da shafa kanta, cikin kulawa yace.
"Ki tambayeni duk kan wani abu da kikeson tambaya zan baki amsa matuƙar nasani."
Kanta ta sunkuyar ƙasa take wasu siraran hawaye suka kwaranyo daga cikin idanunta, araunane tace.
"Su waye dangin MAHAIFIYATA ? inson saninsu Baba, Inason sanin meyasa sukayi watsi da ƴar uwarsu, sannan kuma sukayi watsi dani, shin me mahaifiyata ta aikata musu haka da ta cancanci yin watsi da ita da sukayi?."🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ!!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*Wattpad*
@fatymasardauna
#romance

*Chapter 55*

Ajiyar zuciya ya sauƙe tare da duban ƴar tasa, tabbas ko kaɗan bayason tuna irin tsananin wulaƙancin da dangin Maryama sukayi masa, wato dangin mahaifiyarta kenan, sun tozartashi, sun kuma wulaƙantashi duk dan kawai saboda bashi da kuɗi.
Cikin sanyin murya yace.
"Dangin mahaifiyarki ba suƙita don komai ba saidan aurena da tayi, mahaifiyarki tasoni duk da

kasancewata talaka,  takasance itaɗin kyakkyawar mace ce, don kuwa ko acikin sauran ƴan uwanta na shuwa arab, samun mai kyau kamarta sai an tona, asali mahaifiyarki ƴar garin Maiduguri ce, sannan takasance cikakkiyar shuwa arab,  awannan lokacin shuwa arab basa yarda su auri kowani namiji sai inyakasance daga cikin danginsu ya fito, idan kuwa har takai ga wani bare zasu aura tofa sai ya tabbata cewa shi ɗin mai kuɗine na gaske,    kamar yanda kika sani talaka baya zama akoda yaushe yana cikin fafutukan neman na kansa, sannan yakan iya tsallakawa yabar garinsa ya tafi wata duniya ta daban domin samun abun da zai rufawa kansa asiri, hakanne takasance agareni, inda nayi ƙaura daga garina na tsallaka zuwa garin Maiduguri dan nanemo kuɗi, zuwana Maiduguri shi ya haɗani da mahaifiyarki, inda soyayya mai ƙarfi tashiga tsakaninmu, ko kaɗan bata ƙyamaceni wai dan ina matsayin talaka ba, tana sona fiye da yanda nakesonta, hakan yasa bata sauraran kowa idan bani ba, koda gidansu suka nemi aurar da ita saita bayyana musu kan cewar tana da wanda takeso, sunyi baƙinciki sosai saboda sun so ta auri tsatsonsu, koda sukace takowani su ganni, sai batayi ƙasa a guiwa ba wajen sanar dani, zuciyata cike da fargaba haka na shirya don zuwa gidansu,  sam iyayenta da ƴan uwanta basu taɓa kawowa cewa da talaka take soyayya ba, saboda su atunaninsu wani hamshaƙin mai arziki zata kawo musu, ko kusa basu kawo cewa kamar yanda take da kyau zata iya tsayawa sauraran talaka kamarni ba, haka naje gidansu zuciyata cike da fargaba, koda suka ganni sun cika da baƙinciki haɗi da takaici, nanfa sukayi rantsuwa akan cewa ko mutuwa zatayi bazasu taɓa yarda ta aureni ba,  sunƙirani da maƙasƙanci, mafataucin talaka, sunƙirani da baƙauye, kuma marar ilimi, saboda kwata kwata ni banyi karatun boko ba, saidai kuma bankasance jahili ba saboda nayi karatun islama, dayawan mutane sukan ɗaukan mutum jahili don kawai baiyi karatun boko ba, bayan azahirance kuwa babu jahili sama da wanda baiyi karatun addininsa ba, ko kuma wanda yayi sani ya kuma take sanin,  haka suka ƙaremin cin mutumci da cin fuska, suka kuma gargaɗeni dana fita daga cikin rayuwar ƴarsu,
soyayyar da Maryama mahaifiyarki kemin tana da matuƙar yawa Zieyaderh, haka take wuni take kwana tana kuka, sannan takan hana cikinta abinci, ta kuma hana kanta sukuni duk dan saboda soyayyata, burinta shine iyayenta da ƴan uwanta su aminta ta aureni, sam sukuma idanunsu ya rufe, basaji aransu cewa zasu bari ta aureni, abu kamar wasa haka ta dinga rashin lafiya,  damuwa sukayi mata yawa, sosai tashiga halin tashin hankali,  ganin abun nata yayi tsamari ne yasanya suka ɗauki mummunan fushi da ita, mahaifinta da kansa ya zauna yace mata, tunda ta dage dole saini zata aura shikenan taje ta aureni amma tasani bada sa yawun bakinsa ba, saidai taje can wata uwa duniya aɗaura mana aure, sannan kuma daga ranan da aka ɗaura mata aure dani tasani babushi babu ita, komai yafaru da ita kada tazo masa gida, haka ma ƴan uwanta kowa yace babushi babu ita,  giyar soyayya dake ruɗan zuciyarta yasa tace ta amince, saboda ita dai burinta aduniya bai wuce zama dani ba,  haka tana kuka ta baro ƴan uwanta,  anan cikin garin na Maiduguri mukaje wani masallaci inda nasanarwa da limamin masallacin kaf abun da ke faruwa,  sam limamin baiyi ƙasa aguiwa ba yatara jama'arsa inda yace nabiya sadaki, nan nabada sadakin aurenta naira dubu goma shabiyar aka ɗaura mana aure, tabbas limamin yayi hakane saboda yana gudun mu faɗa halaka, saboda mafi akasarin masoyan da suka tsinci kawunansu a irin wannan yanayi,  sukan faɗawa cikin halaka aduk sanda akace an hanasu auren juna, baya ga kuma suna matuƙar son juna.
Haka aka ɗaura mana aure nida mahaifiyarki inda kaitsaye na wuce da ita ɗan ɗakin dana kama wanda ciki nake kwana, kwananmu biyar a Maiduguri naji gaba ɗaya bazan iya zaman

garin ba, hakan yasa natattara ƴan abubuwana, muka taho garinmu Saminaka kenan,  tundaga kan neman auren mahaifiyarki har kama daga kan auren mu babu wani mutum ɗaya a dangina dana faɗawa, koda muka dawo Saminaka iyaye da ƴan uwana suka ganta nakuma gabatar da ita amatsayin mata, shikenan kuma tashin hankali yasoma, tsantsar tsana dangina ke nuna mata, babu ma kamar ya mahaifiyata,  sam basa sonta, acewarsu wai ita kaɗo ce baikamata ina cikakken fulani naje na auro musu ita ba,  auren ma kuma wai ni nayi gaban kaina, haka muke rayuwa watarana daɗi watarana akasin haka, awajena kaɗai Maryama kesamun soyayya, kowa bayasonta, ƴan uwana kyararta suke, har takai ga tsoron shiga cikinsu take, ahaka muka shafe shekaru huɗu da ita, acikin waƴannan shekarun babu wani ɗan uwanta guda ɗaya daya nemi sanin inda muke, sau dayawa nakan isketa tana kuka wanda na tabbata kukan nan na kewar ƴan uwanta ne takeyi, saboda akwai shaƙuwa mai kyau atsakanin su, wanda kuma ƙaddararren aurena da tayi ne ya raba hakan,  tsana da tsangwaman da ƴan uwana keyi mata ya ƙarune alokacin da muka shafe shekaru huɗu   sukaga babu alaman ciki atattare da'ita, nanfa bakin kowa akanta yake kowa sai yana ce mata juya,  sam mutane sukan manta cewa haihuwa da rashinta duk na Allah Ne, sannan Allah Yakan iya tawayan bawa ta kowani fanni, dayawan mutane ƙarancin ilimi da tunani kesa suyin gorin haihuwa, sun manta  ita haihuwa Allah Kan bawa wanda yasone ya kuma hana wanda yaso, hakan kuma bawai yana nuni da cewa Allah Ya hanaka don baya sonka bane, wataƙila hanakan dayayi shine mafi alkhairi agareka, kuma dama shi Allah Baya hana bawa abu dan haka kawai, saidai idan abun ya kasance ba alkhairi bane agareka, kuma komai na duniya yana da lokaci, sannan ƙaddara tana yawo akan kowa,  bayan munshafe shekara huɗu da ƴan watanni Allah Ya azurtamu da samun ƙaruwa, tahanyar bawa Maryama ciki, nayi farinciki sosai, duk da kasancewar awannan lokacin inacikin wani hali na takurar rayuwa, ma'ana talauci yayimin  tsanani, munzauna da mahaifiyarki lafiya koda sau ɗaya bata taɓa ɗaga muryarta akan tawa ba, munyi zaman daɗi da ita, takasance mace me tsananin biyayya da haƙuri, kana takasance me kyakkyawar zuciya, da kuma kyawawan halayya, takanci duk wani abun dana kawo mata komai rashin daɗinsa, aduk sanda bansamo ba kuwa takanyi haƙuri taɗanyi ƴan dabarbarunta wajen ganin tasama mana abun da zamuci,  sosai tasha wahala wajen rainon cikin da ke jikinta, kusan kullum bata da lafiya, amma haka take jurewa."

Ɗan numfasawa yayi tare da sanya hannu ya dafe kansa, zuciyarsa cike take da tsananin danasanin da yayi, haƙiƙa yabiyewa son zuciya, da ruɗin shaiɗan wanda yakaisa ya baro, ci gaba yayi da cewa.

"Cikin Maryama nada wata 5  nawayi gari da wani irin hali, wanda har kawo yau bansan meyasa halina ya canza ba, saidai nasan cewa hakan ma yana ɗaya daga cikin Ƙaddarata, hakanan nakejin wani irin masifaffen son ƙara aure ya shigeni, har takai ga inaji ajikina cewa idan banƙara aure ba hankalina bazai taɓa kwanciya ba,  wallahi nayi rantsuwa Maryama bata taɓa ƙuntatamin ba, hasali tanayimini biyayyya, sam kuma batacancanci zama da kishiya ba, amma saboda hali irin namu na maza hakanan naji ina sha'awar zama da mata biyu, duk da kasancewar bani da kuɗi, saidai dama ance ƙarin aure ajininmu yake mu maza, koda ana zaune lafiya, ko ana tashin hankali idan mukaso sai munyi,  haka naje na jajiɓowa kaina auren Ma'u,  babu wani fargaba bare ɗar haka nazo na tunkari Maryama da batun ƙarin aurena, ko da sau ɗaya banji tausayin halin da zata shiga ba, gashi lokacin da ciki ajikinta, sannan bata da kowa wanda ya wuce ni, akaina tabaro iyaye da danginta, ta zaɓeni sama da kowa, halacci take

buƙata agareni akullum bawai butulci ba, amma kuma saidai me zuciyar ɗan adam bata da ƙashi, idanuna sun rufe ƙarin aure kawai nasa agaba, hakan yasa nadaina bata wani ingantacciyar kulawa, ƴan uwana kuwa dama basonta sukeba, jin batun ƙarin aurena kuwa yasa suka cika da murna, nan fa suke ta yada mata haibaici, ita dai haka take rayuwarta sam bata tanka musu, koda damuwa yayi mata yawa, saidai ta roƙi Allah Sassauci ko kuwa tashiga ɗaki ta ɓoye kanta tayi kuka, daga bisani kuwa tayi murmushi ta share hawayenta, saboda tasan ƙunci baya taɓa dauwama acikin rayuwar ɗan adam, dole watarana sauƙi zaizo.
Anyi bikina da Ma'u lafiya lafiya, inda na gina mata ɗakinta na laka agefen na Maryama, satin Ma'u ɗaya agidana ta fara bayyana wasu halaye, sannan lokaci ɗaya yazamana inajin mugun shakkanta, idan tace eh bana iya cewa a'a, haka take juyani son ranta, saikuma taga dama nake kula Maryama.
Akwana atashi cikin Maryama ya cika wata tara da sati biyu cif, awata rana ta jumma'a ne nakuda ya tashi mata, rashin kuɗi yasa ta haihu agida, cikin iko da jin ƙai irin na Ubangiji kuwa ta haihu lafiya, inda ta haifo ƴarta mace, wannan ƴar bakowa bace face ke Zieyaderh, haka Maryam tayi jegonta cikin rashin jin daɗi, don kwata kwata nadaina kulawa da ita, saudayawa takan sa kanta aɗaki tayi kuka sosai, sanja halina danayi yasa gaba ɗaya ta rame ta fita hayyacinta, nikuwa ko ajikina, haka nake rayuwa ta da Ma'u, inda komai take buƙata inayi mata, tsananin son zuciya irin tawa yasa na manta da halaccin Maryama agareni.
Haka rayuwa take tafiya babu dadi, aɓangaren Maryama don ma saina ga dama nake shiga ɗakinta, haka take rainonki cikin so da ƙauna, sannu ahankali kike ƙara girma, yayinda kammanninki da Maryama ke ƙara bayyana, harma takai ga kinaso ki ɗarata fari da kyau, sam namanta da wani haƙƙinku ko nauyinku dake kaina, rayuwata kawai nake gaba gaɗi, ɓangaren Ma'u kuwa kullum ƙara ganin ƙimarta nake, yayinda ita kuma takemin duk wani abun da taga dama, tun kina ƙanƙanuwa ban baku kulawa keda mahaifiyarki ba, bansan meyasa zuciyata tazama butulu akan halaccin da mahaifiyarki tayimin ba."
Hawayen da suka cika idanunsa yayi ƙoƙarin shanyewa tare da cewa.
"Har mahaifiyata ta rasu batazama mai ƙaunar Maryama ba, haka ƴan uwana suka dinga rasuwa da ɗai ɗaya, akwana atashi asaran me rai, haka Maryama ta rasu ban zama mai kyautatawa agareta ba, sannan ko bayan rasuwarta da ƴan uwanta suka zo, sun nuna tsantsar tsana akaina saboda acewarsu talauci da zaman ƙuncine yayi ajalinta, inda suka barmini ke don sunce ke jininace sukuma bazasu karɓi jinina ba, har kawo yau kuwa basu sake nemanki ba, bankuma ƙara jin labarinsu ba, saidai akwai yayan mahaifiyarki Alhaji Ahmad Rufa'e wanda yake cikakken ɗan kasuwa, kana kuma babban ɗan siyasa, shine ma wani lokaci nake ganin fostan sa, amma bayan haka har kawo yau babu wata alaƙa dake tsakanina dasu."

Hawayen dake tsiyaya bisa kan fuskarta ta sharce, tabbas taji ƙaunar dangin mahaifiyarta ya shigeta, saidai kuma sam abun da sukayi basu kyauta ba, baikamata ace sunyi watsi dasu har haka akan wani ɗan dalili nasu ba.
Duban mahaifinnata tayi cikin sanyin Murya tace.
"Amma Baba baikamata ace donsu sunƙi nemanmu mu muƙi nemansu ba, inasonsu Baba inason naje garesu, naji gaba ɗaya naƙosa don naga ƴan uwan mahaifiyata, tabbas nasan zuwa wannan lokacin sunyi nadama, marar amfani."
Murmushi Baban nata yayi tare da kai dubansa ga Inna Ma'u wacce keta gabzan apple, duk

labarinnasu da sukeyi tanajinsu, amma dake kayan kwaɗayine agabanta, yasa komai da hankali garesu batayi ba, don koda ma tamai da hankali itace zataji kunya, don sam bata aikata alkhairi ba.
Girgiza kai baban yayi tare da duban ƴartasa yace.
"Kitambayi Mijinki idan ya baki izini, sai nayi miki jagora harzuwa garin na Maiduguri!."
Murmushi kawai tayi tare dayin ƙasa da kanta.
Sam su baban nata basu wani jima sosai ba suka tafi, dama sunzone dan su dubata, haka Oummu ta haɗa Inna Ma'u da kayan tsaraba Niƙi niƙi, amma sam haka Baban Zieyaderh ya hanata amsa, haka suka kama hanya zuciyar Inna Ma'u acunkushe sam bataso hanata karɓan alkhairin da Oummu tayi mata da yayi ba, ita aganinta kawai yana mata baƙin cikine,don ita dama asontane shine yabarta ta kwana, saboda ko kaɗan bata gaji da cin kayan daɗin da aka narka musu ba,  tabbas itakam Allah Yaga zuciarta tana tsananin son kuɗi, da kayan ƙyale ƙyalen dunia, haka dai tayita surutanta ƙasa ƙasa, kana tana wurgawa Malam Garba'n harara, can ƙasan ranta tace ɗan baƙin ciki.
***
Kwata kwata jikin Pharouk yaƙi daɗi, kasancewar yasamu wani irin mummunan buguwa acikin kansa, sakamakon haɗarin da sukayi, wanda shine sanadiyar komai,  sanadin mummunan buguwan daya samu hakan yasanya koda ya farfaɗo zai dinga yawan ciwon kai  matsananci, yanzu haka likitoti suna iyaka ƙokarinsu wajen ganin sunshawo kan matsalan nasa, tsoronsu ɗaya shine kada abun ya shafi  brain ɗinsa, inda suka dage tuƙuru wajen yi masa aiki.

Yau amatuƙar gajiye ya dawo gidan kasancewar kwana biu yatarawa kansa aiki sosai a office, sannan ga ciwonsa dake matuƙar yi masa zafi, yana ƙarasowa cikin bathroom ɗin, ya aje briefcase ɗin dake hannunsa tare da sanya hannuwansa duka biu ya kama waist ɗinsa, sosai ya ƙarewa ɗakin kallo ganin babu ita babu alamunta, ahankali yashiga rage kayan jikinsa, inda ya buɗe drawer ɗinsa tare da zaro wani sabon blue ɗin towel,   ɗaura towel ɗin yayi akan waist dinshi, tare da nufar toilet, tsayawa yayi agaban shower tare da sakarwa kansa ruwa,  saida yaji gajiyan jikinsa yaɗan soma warwarewa kafun  ya kashe shower'n,  wani ɗan ƙaramin towel ya ɗauka, yana me tsane ruwan dake kansa.
Koda yafito daga cikin toilet ɗin sama sama ya shafa body lotion ajikinsa, kallon ƙaton agogon dake saƙale  jikin bangon ɗakin yayi, 8:00 pm daidai, drawer ɗinsa ya buɗe tare da ciro wani tree quater jeans ya sanya, da body spray ɗinsa me daɗin ƙamshi ya feshe jikinsa,  wani ɗan ƙaramin set na glass wanda aka matuƙar ƙawatasa ya buɗe, wani ɗan box mai kyau ya ɗauko tare da buɗewa, wata ƴar siririyar chain ne ta bayyana cikin ɗan ƙaramin akwatin irin ta maza, sosai sarƙan keda azaban kyau, duk da cewa siririyace kuma ta maza ne amma tana da kyau sosai,  akan kakkauran wuyansa yasanya sarƙan,  inda ya ƙarasa gaban ɗan madaidaicin fridge din dake cikin ɗakin,  kwalin fresh milk ya ɗauko, tare da bootle water wanda baida sanyi sosai, tablets ɗinsa ya ɗauko tare da ɓare kowanne ya zuba acikin bakinsa, kana yabi da ruwa, ɗaukan fresh milk ɗin yayi tare da ƙarasawa gaban gadon ya zauna, tunda ya ɗaura bakin goran fresh milk ɗin abakinsa bai cire ba, har saida yashanye sa tas, cikin durstbin ya wurga kwalin tare da shigewa bathroom ya wanko bakinsa, kasancewar yayi sallan isha tun kafun shigowarsa hakan yasa kaitsaye ya nufi kan gado, kwanciya yayi luf akan gadon tare da lumshe idanunsa, sosai yakejin gajiya ajikinsa hakan yasa bacci ke fusgarsa.

Zieyaderh kuwa tun da tayi sallan magriba tatafi ɓangaren Oummu, inda acan tasamu wata ƴar aminiyar Oummun tazo, nan Oummu tasa ƴar budurwan mai suna Zainab, ta zanawa Zieyadern jan lalle ayatsunta na hannu, domin kuwa Zainab ɗin ta iya sosae.
yanzuma can cikin ɗakin Oummun take tana shirya mata kayanta acikin trolly, don Oummun tasanar da ita cewa zata koma Kaduna yayinda su kuma zasu koma gidansu, sam Zieyaderh bataji daɗin hakan ba, saboda batason rabuwa da Oummu, Oummu ce tashigo cikin ɗakin fuskarta ɗauke da murmushi, duban Zieyaderh  tayi  haɗi da cewa.
"Shirya kayan ya isa hakanan ae dai ba yanzu bane tafiyan, yakamata ki ɗan sarara ki huta, kuma ma naga dare yayi, ya kamata kije ki kwanta, dan inama tunanin yajima da dawowa."

Kunyane ya rufeta jin abunda Oummun ta faɗa, hakan yasa tayi ƙasa da kanta, ahankali take wasa da ƴan watsunta wanda sukasha jan lalle, cikin sanyin murya tace da Oummun "Saida safe."
Fuska ɗauke da murmushi Oummu ta sa mata tare da binta da kallo harta fice,  sosai takejin ƙaunar Zieyaderh'n acikin ranta.

Tun shigowarta cikin ƙawataccen falon tasamu tsaraban ƙamshinsa, hakanne ya tabbatar mata da cewa ya dawo, ahankali tatura ƙofar ɗakin tashiga bakinta ɗauke da sallama, dashi idanunta suka fara tozali inda yake kwance yayi irin kwanciyarnan ta rub da ciki,yayinda yasanya hannunsa ɗaya ya dafe mararsa, da dukkan alama bacci yake,  ahankali taƙaraso cikin ɗakin, idanu ta zuba masa, inda take ƙarewa naked fresh white skin ɗinsa kallo,  sosai komai nasa ya haɗu, idanunta ta sauƙe akan faffaɗan bayansa wanda keta shinning batare dako ɗigon zufa akan skin ɗin nasa ba,  ƙarasowa jikin gadon tayi tare da zuba masa ido, ganin ya kwanta akan hannunsa mai ciwo ne yasanyata ɗan rumtse idanunta,  ahankali takai hannunta daniyar taɓa sa, da sauri kuma ta janye hannunta tare da juyawa cikin sauri ta nufi hanyar   toilet, tana shiga tasoma rage kayan jikinta, wanka tayi tare da ɗauro towel ajikinta, sanin cewa yana bacci yasanya ta  fitowa da towel ɗin ɗaure ajikinta babu ko ɗar,  gaban mirror taƙarasa, kasancewar ana ɗan yanayi na zafi yasanya bata shafa mai ajikinta ba, body spray ɗinta  mai daɗin ƙamshi kawai ta fesa, kaitsaye gaban drawer ta nufa, wata ƴar ƙaraman sleeping dress tasanya, wanda take iyakanta cinya, gaba ɗaya rigan showing take, ganin dare ne yasa bata wani da muba, kwalban turaren da Hajiya Arabi ta haɗota dashi ta ɗauka takuma shafawa ajikinta, sosai ƙamshin turaren ya cika ɗakin,
Cikin nutsuwa ta taka harzuwa kan kan gadon, zama tayi abakin gadon tare da kai dubanta garesa, zuwa yanzu ya gyara kwanciyarsa inda yake fuskantar sama,  idanu ta zuba masa tana me kallon  kyakkyawar fuskarsa haɗi da lallausan sajensa, sauƙe idanunta tayi akan golding chain ɗin dake wuyansa sosai yayi mata kyau, hakan yasa taɗan saki murmushi,  cigaba tayi da kallon kyakkyawar fuskarsa, ahankali takai hannunta kan fuskarsa, so take ta shafa lallausan sajen dake kwance akan fuskarsa,  lumshe idanunta tayi alokacin da hannunta ya sauƙa akan tattausan sajen nasa, bazato ba tsammani taji yasanya hannunsa inda ya riƙe nata hannun, da sauri taɗan zaro idanunta waje, don kuwa koda wasa batai tsammanin idanunsa biyu ba, ahankali ya buɗe lumsassun idanunsa, ya sauƙesu akanta, wani irin yarrr taji ajikinta sakamakon wani irin fitinannen kallo daya jefata dashi,  lumshe idanunta tayi ahankali tare da

buɗewa,  cikin nutsuwa ya jawota jikinsa inda ta faɗa kan chest ɗinsa,  cikin wani irin yanayi yake ƙarewa kyakkyawar fuskarta kallo, wani irin kallo me matuƙar kashe jiki yakeyi mata, hakan yasa sam bazata iya jure ganin cikin ƙwayar idanunsa ba, domin kuwa wani irin maganaɗisun ƙaunarsane ke fusgarta, ahankali ya ɗago hannunta, kallon yatsunta da suka sha jan lalle yayi, cikin nutsuwa ya tura ɗan yatsun nata abakinsa, lumshe idanunsa yayi yayinda yasa harshe da laɓɓansa duka biu yana tsotsansu ahankali, wani irin matsanancin daɗi ne ke ratsa jikinta, sosai ɗumin bakinsa dake sauƙa akan yatsun nata, suka sanya taji gaba ɗaya jikinta yayi weak,  cikin wani irin yanayi yasake jawota jikinsa, bakinsa ya ɗaura adaidai saitin kunnenta, cikin unique voice dinsa mai sanya bacci yace.
"I MISS YOU!."

(Kuyi haƙuri yau ina azumi shiasa bansamu nayi muku editing ba)
🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SOORAJ!!!*

*Written By*
Phatymasardauna

*Dedicated To My Life (Sardauna)*

*Wattpad*
@fatymasardauna
#romance

*Chapter 56*

Ajiyar zuciya ya sauƙe tare da duban ƴar tasa,  tabbas ko kaɗan bayason tuna irin tsananin wulaƙancin da dangin Maryama sukayi masa, wato dangin mahaifiyarta kenan, sun tozartashi, sun kuma wulaƙantashi duk dan kawai saboda  bashi da kuɗi.
Cikin sanyin murya yace.
"Dangin mahaifiyarki ba suƙita don komai ba saidan aurena da tayi,  mahaifiyarki tasoni duk da kasancewata talaka,  takasance itaɗin kyakkyawar mace ce, don kuwa ko acikin sauran ƴan uwanta na shuwa arab, samun mai kyau kamarta sai an tona, asali mahaifiyarki ƴar garin Maiduguri ce, sannan takasance cikakkiyar shuwa arab,  awannan lokacin shuwa arab basa yarda su auri kowani namiji sai inyakasance daga cikin danginsu ya fito, idan kuwa har takai ga wani bare zasu aura tofa sai ya tabbata cewa shi ɗin mai kuɗine na gaske,    kamar yanda kika sani talaka baya zama akoda yaushe yana cikin fafutukan neman na kansa, sannan yakan iya tsallakawa yabar garinsa ya tafi wata duniya ta daban domin samun abun da zai rufawa kansa asiri, hakanne takasance agareni, inda nayi ƙaura daga garina na tsallaka zuwa garin Maiduguri dan nanemo kuɗi, zuwana Maiduguri shi ya haɗani da mahaifiyarki, inda soyayya mai ƙarfi tashiga tsakaninmu, ko kaɗan bata ƙyamaceni wai dan ina matsayin talaka ba, tana sona fiye da yanda nakesonta, hakan yasa bata saurararan kowa idan bani ba, koda gidansu suka nemi

aurar da ita saita bayyana musu kan cewar tana da wanda takeso, sunyi baƙinciki sosai saboda sun so ta auri tsatsonsu, koda sukace takowani su ganni, sai batayi ƙasa a guiwa ba wajen sanar dani, zuciyata cike da fargaba haka na shirya don zuwa gidansu,  sam iyayenta da ƴan uwanta basu taɓa kawowa cewa da talaka take soyayya ba, saboda su atunaninsu wani hamshaƙin mai arziki zata kawo musu, ko kusa basu kawo cewa kamar yanda take da kyau zata iya tsayawa sauraran talaka kamarni ba, haka naje gidansu zuciyata cike da fargaba, koda suka ganni sun cika da baƙinciki hadi da takaici, nanfa sukayi rantsuwa akan cewa ko mutuwa zatayi bazasu taɓa yarda ta aureni ba,  sunƙirani da maƙasƙanci, mafataucin talaka, sunƙirani da baƙauye, kuma marar ilimi, saboda kwata kwata ni banyi karatun boko ba, saidai kuma bankasance jahili ba saboda nayi karatun islama, dayawan mutane sukan ɗaukan mutum jahili don kawai baiyi karatun boko ba, bayan azahirance kuwa babu jahili sama da wanda baiyi karatun addininsa ba, ko kuma wanda yayi sani ya kuma take sanin,  haka suka ƙaremin cin mutumci da cin fuska, suka kuma gargaɗeni dana fita daga cikin rayuwar ƴarsu,
soyayyar da Maryama mahaifiyarki kemin tana da matuƙar yawa Zieyaderh, haka take wuni take kwana tana kuka, sannan takan hana cikinta abinci, ta kuma hana kanta sukuni duk dan saboda soyayyata, burinta shine iyayenta da ƴan uwanta su aminta ta aureni, sam sukuma idanunsu ya rufe, basaji aransu cewa zasu bari ta aureni, abu kamar wasa haka ta dinga rashin lafiya,  damuwa sukayi mata yawa, sosai tashiga halin tashin hankali,  ganin abun nata yayi tsamari ne yasanya suka ɗauki mummunan fushi da ita, mahaifinta da kansa ya zauna yace mata, tunda ta dage dole saini zata aura shikenan taje ta aureni amma tasani bada sa yawun bakinsa ba, saidai taje can wata uwa duniya aɗaura mana aure, sannan kuma daga ranan da aka ɗaura mata aure dani tasani babushi babu ita, komai yafaru da ita kada tazo masa gida, haka ma ƴan uwanta kowa yace babushi babu ita,  giyar soyayya dake ruɗan zuciyarta yasa tace ta amince, saboda ita dai burinta aduniya bai wuce zama dani ba,  haka tana kuka ta baro ƴan uwanta,  anan cikin garin na Maiduguri mukaje wani masallaci inda nasanarwa da limamin masallacin kaf abun da ke faruwa,  sam limamin baiyi ƙasa aguiwa ba yatara jama'arsa inda yace nabiya sadaki, nan nabada sadakin aurenta naira dubu goma shabiyar aka ɗaura mana aure, tabbas limamin yayi hakane saboda yana gudun mu faɗa halaka, saboda mafi akasarin masoyan da suka tsinci kawunansu a irin wannan yanayi,  sukan faɗawa cikin halaka aduk sanda akace an hanasu auren juna, baya ga kuma suna matuƙar son juna.
Haka aka ɗaura mana aure nida mahaifiyarki inda kaitsaye na wuce da ita ɗan ɗakin dana kama wanda ciki nake kwana, kwananmu biyar a Maiduguri naji gaba ɗaya bazan iya zaman garin ba, hakan yasa natattara ƴan abubuwana, muka taho garinmu Saminaka kenan,  tundaga kan neman auren mahaifiyarki har kama daga kan auren mu babu wani mutum ɗaya a dangina dana faɗawa, koda muka dawo Saminaka iyaye da ƴan uwana suka ganta nakuma gabatar da ita amatsayin mata, shikenan kuma tashin hankali yasoma, tsantsar tsana dangina ke nuna mata, babu ma kamar ya mahaifiyata,  sam basa sonta, acewarsu wai ita kaɗo ce baikamata ina cikakken fulani naje na auro musu ita ba,  auren ma kuma wai ni nayi gaban kaina, haka muke rayuwa watarana daɗi watarana akasin haka, awajena kaɗai Maryama kesamun soyayya, kowa bayasonta, ƴan uwana kyararta suke, har takai ga tsoron shiga cikinsu take, ahaka muka shafe shekaru huɗu da ita, acikin waƴannan shekarun babu wani ɗan uwanta guda ɗaya daya nemi sanin inda muke, sau dayawa nakan isketa tana kuka wanda na tabbata kukan nan na kewar ƴan uwanta ne takeyi, saboda akwai shaƙuwa mai kyau atsakanin su, wanda kuma

ƙaddararren aurena da tayi ne ya raba hakan,  tsana da tsangwaman da ƴan uwana keyi mata ya ƙarune alokacin da muka shafe shekaru huɗu   sukaga babu alaman ciki atattare da'ita, nanfa bakin kowa akanta yake kowa sai yana ce mata juya,  sam mutane sukan manta cewa haihuwa da rashinta duk na Allah Ne, sannan Allah Yakan iya tawayan bawa ta kowani fanni, dayawan mutane ƙarancin ilimi da tunani kesa suyin gorin haihuwa, sun manta  ita haihuwa Allah Kan bawa wanda yasone ya kuma hana wanda yaso, hakan kuma bawai yana nuni da cewa Allah Ya hanaka don baya sonka bane, wataƙila hanakan dayayi shine mafi alkhairi agareka, kuma dama shi Allah Baya hana bawa abu dan haka kawai, saidai idan abun ya kasance ba alkhairi bane agareka, kuma komai na duniya yana da lokaci, sannan ƙaddara tana yawo akan kowa,  bayan munshafe shekara huɗu da ƴan watanni Allah Ya azurtamu da samun ƙaruwa, tahanyar bawa Maryama ciki, nayi farinciki sosai, duk da kasancewar awannan lokacin inacikin wani hali na takurar rayuwa, ma'ana talauci yayimin  tsanani, munzauna da mahaifiyarki lafiya koda sau ɗaya bata taɓa ɗaga muryarta akan tawa ba, munyi zaman daɗi da ita, takasance mace me tsananin biyayya da haƙuri, kana takasance me kyakkyawar zuciya, da kuma kyawawan halayya, takanci duk wani abun dana kawo mata komai rashin daɗinsa, aduk sanda bansamo ba kuwa takanyi haƙuri taɗanyi ƴan dabarbarunta wajen ganin tasama mana abun da zamuci,  sosai tasha wahala wajen rainon cikin da ke jikinta, kusan kullum bata da lafiya, amma haka take jurewa."

Ɗan numfasawa yayi tare da sanya hannu ya dafe kansa, zuciyarsa cike take da tsananin danasanin da yayi, hakiƙa yabiyewa son zuciya, da ruɗin shaiɗan wanda yakaisa ya baro, ci gaba yayi da cewa.

"Cikin Maryama nada wata 5  nawayi gari da wani irin hali, wanda har kawo yau bansan meyasa halina ya canza ba, saidai nasan cewa hakan ma yana ɗaya daga cikin Ƙaddarata, hakanan nakejin wani irin masifaffen son ƙara aure ya shigeni, har takai ga inaji ajikina cewa idan banƙara aure ba hankalina bazai taɓa kwanciya ba,  wallahi nayi rantsuwa Maryama bata taɓa ƙuntatamin ba, hasali tanayimini biyayyya, sam kuma batacancanci zama da kishiya ba, amma saboda hali irin namu na maza hakanan naji ina sha'awar zama da mata biyu, duk da kasancewar bani da kuɗi, saidai dama ance ƙarin aure ajininmu yake mu maza, koda ana zaune lafiya, ko ana tashin hankali idan mukaso sai munyi,  haka naje na jajiɓowa kaina auren Ma'u,  babu wani fargaba bare ɗar haka nazo na tunkari Maryama da batun ƙarin aurena, ko da sau ɗaya banji tausayin halin da zata shiga ba, gashi lokacin da ciki ajikinta, sannan bata da kowa wanda ya wuce ni, akaina tabaro iyaye da danginta, ta zaɓeni sama da kowa, halacci take buƙata agareni akullum bawai butulci ba, amma kuma saidai me zuciyar ɗan adam bata da ƙashi, idanuna sun rufe ƙarin aure kawai nasa agaba, hakan yasa nadaina bata wani ingantacciyar kulawa,  ƴan uwana kuwa dama basonta sukeba, jin batun ƙarin aurena kuwa yasa suka cika da murna, nan fa suke ta yada mata haibaici, ita dai haka take rayuwarta sam bata tanka musu,  koda damuwa yayi mata yawa, saidai ta roƙi Allah Sassauci ko kuwa tashiga ɗaki ta ɓoye kanta tayi kuka, daga bisani kuwa tayi murmushi ta share hawayenta, saboda tasan ƙunci baya taɓa dauwama acikin rayuwar ɗan adam, dole watarana sauƙi zaizo.

Anyi bikina da Ma'u lafiya lafiya, inda na gina mata ɗakinta na laka agefen na Maryama,  satin Ma'u ɗaya agidana ta fara bayyana wasu halaye, sannan lokaci ɗaya yazamana inajin mugun shakkanta, idan tace eh bana iya cewa a'a, haka take juyani son ranta, saikuma taga dama nake kula Maryama.

Akwana atashi cikin Maryama ya cika wata tara da sati biyu cif, awata rana ta jumma'a ne nakuda ya tashi mata, rashin kuɗi yasa ta haihu agida, cikin iko da jin ƙai irin na Ubangiji kuwa ta haihu lafiya, inda ta haifo ƴarta mace,  wannan ƴar bakowa bace face ke Zieyaderh, haka Maryam tayi jegonta cikin rashin jin daɗi, don kwata kwata nadaina kulawa da ita, saudayawa takan sa kanta aɗaki tayi kuka sosai,    sanja halina danayi yasa gaba ɗaya ta rame ta fita hayyacinta, nikuwa ko ajikina, haka nake rayuwa ta da Ma'u, inda komai take buƙata inayi mata, tsananin son zuciya irin tawa yasa na manta da halaccin Maryama agareni.
Haka rayuwa take tafiya babu dadi, aɓangaren Maryama don ma saina ga dama nake shiga ɗakinta, haka take rainonki cikin so da ƙauna, sannu ahankali kike ƙara girma, yayinda kammanninki da Maryama ke ƙara bayyana, harma takai ga kinaso ki ɗarata fari da kyau,   sam namanta da wani haƙƙinku ko nauyinku dake kaina, rayuwata kawai nake gaba gaɗi, ɓangaren Ma'u kuwa kullum ƙara ganin ƙimarta nake, yayinda ita kuma takemin duk wani abun da taga dama,  tun kina ƙanƙanuwa ban baku kulawa keda mahaifiyarki ba, bansan meyasa zuciyata tazama butulu akan halaccin da mahaifiyarki tayimin ba."
Hawayen da suka cika idanunsa yayi ƙoƙarin shanyewa tare da cewa.
"Har mahaifiyata  ta rasu batazama mai ƙaunar Maryama ba, haka ƴan uwana suka dinga rasuwa da ɗai ɗaya,   akwana atashi asaran me rai, haka Maryama ta rasu ban zama mai kyautatawa agareta ba, sannan ko bayan rasuwarta da ƴan uwanta suka zo, sun nuna tsantsar tsana akaina saboda acewarsu talauci da zaman ƙuncine yayi ajalinta, inda suka barmini ke don sunce ke jininace sukuma bazasu karɓi jinina ba, har kawo yau kuwa basu sake nemanki ba, bankuma ƙara jin labarinsu ba, saidai akwai yayan mahaifiyarki Alhaji Ahmad Rufa'e wanda yake cikakken ɗan kasuwa, kana kuma babban  ɗan siyasa, shine ma wani lokaci nake ganin fostan sa, amma bayan haka har kawo yau babu wata alaƙa dake tsakanina dasu."

Hawayen dake tsiyaya bisa kan fuskarta ta sharce, tabbas taji ƙaunar dangin mahaifiyarta ya shigeta, saidai kuma sam abun da sukayi basu kyauta ba, baikamata ace sunyi watsi dasu har haka akan wani ɗan dalili nasu ba.
Duban mahaifinnata tayi cikin sanyin Murya tace.
"Amma Baba baikamata ace donsu sunƙi nemanmu mu muƙi nemansu ba, inasonsu Baba inason naje garesu, naji gaba ɗaya naƙosa don naga ƴan uwan mahaifiyata, tabbas nasan zuwa wannan lokacin sunyi nadama, marar amfani."
Murmushi Baban nata yayi tare da kai dubansa ga Inna Ma'u wacce keta gabzan apple, duk labarinnasu da sukeyi tanajinsu, amma dake kayan kwaɗayine agabanta, yasa komai da hankali garesu batayi ba, don koda ma tamai da hankali itace zataji kunya, don sam bata aikata alkhairi ba.
Girgiza kai baban yayi tare da duban ƴartasa yace.
"Kitambayi Mijinki idan ya baki izini, sai nayi miki jagora harzuwa garin na Maiduguri!."
Murmushi kawai tayi tare dayin ƙasa da kanta.
Sam su baban nata basu wani jima sosai ba suka tafi, dama sunzone dan su dubata, haka Oummu ta haɗa Inna Ma'u da kayan tsaraba Niƙi niƙi, amma sam haka Baban Zieyaderh ya hanata amsa, haka suka kama hanya zuciyar Inna Ma'u acunkushe sam bataso hanata karɓan alkhairin da Oummu tayi mata da yayi ba, ita aganinta kawai yana mata baƙin cikine,don ita dama asontane shine yabarta ta kwana, saboda ko kaɗan bata gaji da cin kayan daɗin da aka

narka musu ba,  tabbas itakam Allah Yaga zuciarta tana tsananin son kuɗi, da kayan ƙyale ƙyalen dunia, haka dai tayita surutanta ƙasa ƙasa, kana tana wurgawa Malam Garba'n harara, can ƙasan ranta tace ɗan baƙin ciki.
***
Kwata kwata jikin Pharouk yaƙi daɗi, kasancewar yasamu wani irin mummunan buguwa acikin kansa, sakamakon haɗarin da sukayi, wanda shine sanadiyar komai,  sanadin mummunan buguwan daya samu hakan yasanya koda ya farfaɗo zai dinga yawan ciwon kai  matsananci, yanzu haka likitoti suna iyaka ƙokarinsu wajen ganin sunshawo kan matsalan nasa, tsoronsu ɗaya shine kada abun ya shafi  brain ɗinsa, inda suka dage tuƙuru wajen yi masa aiki.

